🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

NA SAKE ZUWA DA SABON TSARI, SABUWAR TAFIYA, SABON AL.AMARI........ NI CE YAR MUTAN NIGER NA KAWO MAKU SABON NVL DINA WANDA A KASATA NAKE MAI TAKEN *BAK'A CE* bak'a ce na dauke da darusan rayuwa, dole ya nishadantar, ya baku mamaki, ya saka ku tunani..... *BAK'A CE* zai zo da kadan daga cikin al.adun yarena *BUZANCI* da kuma *TUBANCI* ..........ku biyo ni ku sha labarin *BAK'A CE*

TALLAH TALLAH TALLAH

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

1️⃣

*WANI YANKI NE CAN WAJEN AGADEZ CIKIN JAMHURIYAR NIGER mai sunna TIMIYA*, inda buzaye ne ke rayuwa a garin indai ka ga bakuwar fata to lale bako ne ya zo kuma juyawa zai yi ,
A kauyen nan basu da ruwan pampo sai fan take, wuta bata kai can ba ,
Gari ne mai tarin ni.ima , albarkar noma garake , sannan mota bata shiga domin can cikin sahara ne sai dai a hau rakumi a samu a shiga cikin Timiya

Yan mata ne laye su hudu,
Cikin ukun nan kowace ta kala tamkar ka lasheta dan kyau da daukan hankali sun sha digo digonsu na buzaye da katanga , sai daya a gefensu wace kanta ke sade kasa jikinta na dan rawa rawa hanayenta kawai ake ganni bakin kirin da yafen mayafinta na turkudi (tufafin buzaye )
```

Shigowa wani datijo ya yi yana dan dukawa dan tsayi ne da shi, da hannunsa yake yiwa mutanen dake bayansa nuni da su shigo domin bashida hausar kirki a bakinsa
Yana dago kansa ya hangota a cikinsu, ya juyo da dan sauri ya ga mazan nan har sun zauna
Rai bace ya nufi dakinsu wajen uwar yaran wato matarsa yana zuwa ya daga hannunsa ya dungurewa yar datijuwar kai ransa bace cikin yaren buzanci ya ce" ban hane ki turo min da wannan bakar yar taki ba? Na aurar da yaya hudu saura uku na cire wannan bakar a yayana, na sha fada maki ni a danginmu ba baki aman kika tashi kika haifo min baka? Na yi na yi ki fada min gaskiyar waye ubanta kin ce ni? Kuma dan bakin ciki an samu elhazawa masu son auren yaren kin tunkudo (turo) mini da ita ko?

Bata ce komai ba sai sada kai da ta yi, har ya gama babatunsa ya juya

Yana komawa ya damki hannunta ya jata kiiiii suna shiga ya hankadata ta tafi tagataga ta duke nan kusa da gadon karagar mahaifiyarta kanta sade, ya aibatata sosai kafin ya juya ya koma wajen bakinsa

Kanta sade hawaye ya ziraro mata, ta dago a hankali ta kali mahaifiyarta da idannuwanta ke rufe ruf tana jin yanda zuciyarta ke suya
Murya a raunane ta ce" *ANNA* (wato mama)

Bata bude idannuwanta ba, bata amsata ba
Ta dan jima a haka kafin take mikewa ta dage rufar da ta yi tana kallon mahaifiyarta da wani irin yannayi, a gaskiya a jikin wannan matashiyar budurwa banda idannuwanta ba wani abu mai hasken fari domin kuwa tana da baki ga kuma tufafinta mai rinar da fata ne wato turkudi
Mamanta ta dago ta bude ido a karo na farko, murya shake cikin yaren buzanci ta ce" kal ki ce komi, ki yi hakuri kawai

A hankali ta juya dan ruwa gidan baba tsoho....

Ku biyo ni garina, *TIMIYA* domin a Niger nake.... ......taku har kulun YAR MUTAN NIGERSAJIDA

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

2️⃣

A hankali take tafiya tana dan rabewa, da ta hango gugun yara sai ta labe har sai sun fice idan kuwa wasa ne suke dole sai dai ta canza hanya domin irin wulakancin da mahaifinta da wasu a cikin yan uwanta ya sanya har jama.ar garin ke wulakantata suma suna dubanta daban cikinsu....

A hankali ta karyo kwanar runfar baba tsoho

Sanda take dan karasawa domin bata son haduwa da almajiransa tun bama Ali ba wanda ya so hada shi da ita ya ci mata mutunci yayi mata kwakwaran kashedi na koda wasa kar ta yarda ta nuna tana son sa domin shi dama ya shigo garin Timiya ne dan ya samu buzuwa fara ya aura..to tun daga lokacin sauran almajiran ke tsokanarta suna fadin ta Aliyu *BAK'A*

zaune yake cikin bukarsa, rawani ne a fuskarsa kwaurin hannun sa da na kafarsa ake gani , hakan zai nuna maka tsohon mutun ne, domin fatarsa du ta yi yaba haka gashin dake kwaurinsa du sun yi fari sol sol da su

Waje daya kawai yake kallo, a zuciyarsa kuwa ya afka tunanin yau ina ta yi? Ya aka yi bata zo ta dauki karatu da safe ba? Bata da kawa, bata da wani mai rabata a jikinsa, mahaifiyarta kanta bata mugun sake mata dan tana tsananin tsoron mijinta a kan yarinyar
Shi kam yana cike da zulunmin abinda ya sa bata zo ba

A hankali ta daga kasarin dakin ta yi masa salama

Murmushi ne ya subuce masa yana kallonta kafin ya amsa salamarta

karasawa ta yi tana dan tatare tataren dakin ta kai dubanta wajensa, cike da kaunar tsohon
```

sannan idan tana tare da shi takan ji ta wani iri, bata jin tsoronsa sai soyayarsa, tsohon shi ne kawai mai yi mata murmushi a duniya,
Dan murmushi ta sakar masa ta ce" SOFO (wato tsoho)

Shima murmushin ya yi, ya dan nunota da yatsarsa,

Ta karasa ta duka kasa ta ce" ta gode (gaisuwa kennan)

Turkudin kanta ya shafa a hankali kafin ya ce" Alharasssss

Mikewa ta yi ta gama tatare masa dakin ta dauko tsintsiyar kabar da ta yi da kanta dan share dakins ta shashare ko.ina ta dan dage kasarin ta dauki tulun ruwansa ta fice

Murmushi ya yi, ya bi ta da kallo....a kasan zuciyarsa ya ayanna" Allah ya nuna min farin cikin ki kafin na koma gareshi

Tafe take da tulunta cikin nutsuwa, tana zuwa ta duka wajen diban ruwan , wani dan kewaye ne aka yi shi ba rijiya ba, shi ba teku ba  shi dai ruwan ana jayo masu shi ne, sannan kalar ruwan jajajir ne sai kanshin laka , akoy ruwa masu kyau sai dai idan ta yarda ta je wajen sai dai ta dawo ba ruwan ba tulun domin du yawancin yan matan garin can suke zuwa dibo ruwa su kuwa sun ki jinnin ganninta a wajen

Sai da ta cika tulun ta mike ta gyara bakin zaninta da kyau ta daga ta dora saman kanta

Yanda ta bar shi zaune haka ta dawo ta tarar da shi
Ta nemi wajen Tulun ta ajiye tana dubansa cikin yaren buzanci ta ce" baka gajiya da kallon waje guda?

Bai bata amsa ba sai mika mata allonta da yayi yana nuna mata wajen zama

A hankali ta zauna ya ci gaba da koya mata karatu wanda sosai ta nisa kuma shine malaminta tunda ta san shi
Suna gama karatun ya ce" menene tambayarki ta yau?

Ta yi tsai tana kallonsa, can ta nisa ta ce" sofo, shin mutun mai bakar fata laifi ya yi aka halice shi baki?

Da sauri ya kallota, ganni ya yi kanta a sade, tana faman murza hannayenta .....yarinyar akoy zurfin ciki sosai aman wani lokacin sai ta fadi dan abinda ke ranta domin tana gannin abubuwa masu firgitarwa a rayuwarta

Hannunsa ya daga, murya a sanyaye ya ce" ko daya mutun baki da fari du daya ne a wajen Allah

Dara daran fararan idannuwanta ta dago ta sauke kan nasa da sukai dan ja sannan du sun yi yaba irin na tsohon mutun, hawayen da ya taru a idannuwanta ta yi iya kokarinta ta mayar da su , daga haka bata kara komai ba, bata bari ta yu kuka ba ta mike tsam ta fice ba tare da ta kara kalma daya ba

Ajiyar zuciya ya sauke, yana tir da halayen Agali, Agali bashi da hankali da tunani, dan kawai Allah ya yi yarinya an haifeta bak'a cikin y'ayanka sai ta zama abin kyama abin kyankyami abin wulakantawa? Ita ta halici kanta ne?

Ta jima tana tafiya kafin ta karaso gidan iya mai siyar da nono

Har kasa ta duka tana gaisheta

Iya ta amsata kafin take cewa" kin ga nonon nan yana yi min wuya, ban san me yasa idan kin dauka cinikinki baya fice dala dari da ashirin .....sai dai ki maido mini shi haka du an motsa shi sannan in baki salama ni kam yau ki yi hakuri na sararma masu zuwa gida sara, kinga daman tausayin ki yake saka ni na baki dan ki samu dan kudin kashewa

Kanta a kasa ta ce" ki yi Hakuri iya, zan kara kaimi wajen siyarwan ki zuba min kadan yanda zan iya siyarwa

Kanta ta girgiza ta mike ta dauki kwarya ta zuba mata nono dan madaidaici ta mika mata, ita Allah yana ganni dan tana jin tausayin yarinyar ne aman tana da masu siyan nononta a hannu a hannu domin shannunta suna da yawa

Dauka ta yi ta fice a gidan, tana tafe tana jin wata irin juwa na daukanta, bata karya ba, bata ci komai ba sai yanzu ta tuna
Ajiyar zuciya ta sauke ta samu gu ta dan rakube ta daga kanta sama ta afka tunani

Mu je zuwa ci kin labarin *BAK'A CE*

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

3️⃣

Suna tafiya ya shigo dakin,
Yanda ya barta tunda ya dungure mata kai haka ya tarar da ita
Ransa bace ya nunota da yatsarsa ya ce" ke,

A hankali ta dago kanta ta sauke kansa tana kallon sa

Y.ayana biyu sun samu miji yan albarkana

Wani abu ta hadiye a makogwaronta, a hankali ta ce" wannan karon wa ka siyarwa yaran?

Da mamaki yake kallon ta, mayar masa da magana ne ta yi? Shi?
Da izgili ya karasa kusa da ita ya nunata ya ce" ke balagazar mace, ke har kin isa ki dube ni ki fda min cewar ni ina siyar da yara? A me kika dauke ni kennan? Matsiyaci? To bara na tuna maki a gidannan daidai da sansannin ( tabar buzaye) da zaki gumtsa sai kin taba tawa ba zaki iya siya ba dan bakya saye bakya saidawa zaune kike dabar ta.kar duwawu komai sai an yi maki,
To yaranna sun samu mazaje sun yi min kyakyawan tayi! Kuma na fada maki idan har na aurar da yaran nan gaba daya ki kuka da kanki ke da yarki dan kuwa ba zai yiwu ya kasance ina ciyar da yar da ban yarda cewa tawa bace bama

Har ya gama bata kara tofawa ba , ya juya ya fice a dakin

A hankali ta zauna kusa da mahaifiyarsu, itama farinta har daukan ido yake,
Hannunta ta kamo ta rike gam ta ce" zan so ki fada mana tarihinmu kafin muma mu tafi kamar su aunty a daina jin labarin mu, ba labari ba aike ba wani motsi.....Allah kadai ya san halin da suke ciki idan suna raye! Ba yace auren wata biyu kawai zan yi, idan na cika wata biyu na kwaso masa kudade na dawo ko ya sake ni ko bai sake ni ba sarki zai hana shi shigowa garin
```

........ ki daure ki fada mana tarihin rayuwarmu Anna (mama)
Su waye mu?
Ina ne asalin asalin mu?
Su waye dangin mu?
Bamu da kowa ne sai mu da ku?
Idan muna da mai ya sa ba wanda ya taba zuwa inda muke? Ina son sani ANNA

Jajayen idannuwanta ta sauke kan *Gaishat*, wai ita nan mai damar ce domin ita bata hantarar Bak'A, sannan tana kamanta bin iyayen su ba kamar sauran ba
Kwace hannunta ta yi ta hade rai ta yi mata nuni da kofa

Ta san kan zancen dan haka ta mike ta fice daga dakin

Kallonta yake tunda ya kirayeta ta zo turakarsa tana zuwa ta tube du wani abin da sunnansa sutura a jikinta, ta tsaya masa a gabansa wato gashi ka yi ka gama na koma

Kansa ya girgiza kafin yake tsareta da idonsa, ya juyar da kansa ya kuma kallota
Can ya ce" Nadia, haka zamu yi ta rayuwa? Ke ba zaki taba saukowa ki bani kulawar da nake bukata ba?

Saurin zubewa ta yi kasa ta ce" ka yi hakuri Uban gidana, ban san zan bata ranka ba kar ka hada ni da Ba (Aba)

Idannuwansa ya lumshe, a gaskiya Allah ya jarabe shi da matsanancin son yarinyar,
Yarinyar ce ko a cikin bugaje (buzaye) ta fita daban, ta hadu iya haduwa ko ba wanka Nadia mai kyau ce, dalilin haka ya amshi tayin aurenta da Ba dinta ya yi masa bisa sharudan kawar da ido da toshe kunnuwa kan karansa da za.a kawo a cikin garin kan yanda yana tafiyar da rayuwar gidansa, aman ya kasa samun nutsuwa da ita........ya kasance komai zatai masa tana yi ne dan tsoro ba dan soyaya ba

A hankali ya dagota ya jata zuwa ainahin turakar domin yanda yake kwakwarta shi kansa mamaki yake, yanzu dai shekara biyar da aurensu bayanta ma ya kara auren mace biyu ya saki gudar aman har yanzu ta kasa fice masa a rai a kulun yana mai jin zumudin kasancewa da ita.....aman ita ta kasa kontar da hankalinta ko dan matsayinsa na sarkin garin ta murza mulkinta aa tana rabe rabe ne a gidan mijinta
Nadia kennan babar yar *BA*

Ke kin san nawa ne million daya? Jika dari dari har goma fa, an ce Gaishat har million goma sha hudu mutumin ya bada kudin aurenta,

Ke ki rufe min bakin ki, ke fa haka birge ki yake ko? Kina ganni yanda yake aurar da yayan nasa daga sun tafi shikennan ba labari, kudin ya zo bai yi masa anfannin komai ba, daga an kwana

biyu ya kashe sai kuma ya fara harin wata a cikin y'ayan nasa, ai sun kusa karewa zamu ga kuma idan wada ya tsanar zai yi shelar ya siyar

Mahaifiyarsu da ta shigo da Buzu (salaya) a hannunta ta kale su ta ce" ke Amina, ki tashi maza ku je ku yi sallah, wannan maganar kun cika yinta bayan kun san ya zama abin gasa a garin nan, sai kun jaza min abinda ya fi karfina ko? Kuma da hakan bata faruwa da ku dan Ba din ku bai yarda da hakan ba, ku kun fi kowa sanni gidajen da basa haka basu fi a kirga a garinnan ba aman zaku zauna mamakin kwaya daya? Kowa ya yi da kyau kai nasa! Ku mike ku bace min a wajen nan kar ku yarda maganar nan naku ta yi tsayi ya zo ya tsige mu baki daya domin ku kun san waye shi !

Sumui sumui suka fice dan zuwa yin alwallah su gabatar da sallah

Sai yama sosai ta kamo hanyar gida,
Tana tafe ne tana dan jin dadin yannayin garin domin sanyin yama ya fara busawa sosai ita kuwa gwanar son sanyi ce sosai
Ba ita ta kai gidan iya mai nono ba sai kusan magariba, ta kai mata cinikin inda iyar ta bata dala ashirin da biyar ta yi godiya ta mike
Har ta kusa fita iya ta kirayeta ta dawo
Ta ce" kin ga , ga abinci nan ki dauka ki ci mana ni na ci na rage, sauran ki yi min halin naki sai na tabatar kina kyankyamina ne na san irin matakin da zan dauka

Fanata ce ta fito daga daki, kmar kulun cikin mahaukacin gayu mai gigitar da jama.ar garin
....Fanata dai y'a ce a wajen yar uwar iya wace ke aure a cikin garin agadez, mahaifin fanata Babarbare ne shi ya sa sunnanta ya fita daban ,
A da fannata ta kasance ita ba fara kar  ba ita ba baka ba duda mahaifiyarta farar buzuwa ce,
Aman kasancewarta a can cikin birni, da taraya da kawaye ya saka take shafa mai wanda ya mugun karbarta ta yi fari kar kar kar harma ta fi maman nata farin,
Fannata akoy kyau ga iya daukan wanka
Tana son garin timiya a rayuwarta domin gari ne mai cike da ni.ima

Tunda ta fito take kallonta da mamaki,
Dubanta ta mayar wajen Iya ta ce" iya, yarinyar nan mai maki tallah ce ta girma haka?

Iya ta ce" eh ita dai ce

Fannata ta yatsina fuska ta ce" to aman har yanzu sunnan da ake kiran nata da shi ne? Wato *BAK'A*?

iya ta amsata da kai

Fannata ta kallo wajenta ta kuma kallon iya ta ce" menene sunnanta na gaskiya ne ita wai?

Iya ta kalli Bak'a, ta kalli Fannata, ta ce" sunnan Hajia ne da ita, karfi da yaji Ba dinta ya mayar da sunnanta Bak'a har ake mata kiranye da haka

Da mamaki Fannata ta karasa kusa da ita tana kallonta,
Yarinyar fa nata wani tsararan kyau, boyeyen kyau, duda mugun bakinta ga bakin turkudi na bugajen kauye🙈🤣, ga dati da take fama da shi, aman ita tana hango wani al.amari a tatare da yarinyar, to aman me zai hana ta shafa mai itama? A sanninta ba bakon lamari bane buzu farinma ya shafa mai, kai ba buzu ba yanzu abin ya zama larabawama mai suke karawa shi yasa zaka gan su wani farfarfar da su sunna daukan ido, ba sai dan duniya ke shafa mai a duniyarmu ba, mun dauki mai mun mayar da shi abin kmgyaran fata, ra.ayi ne shafa shi idan ka shafa ba mai yi maka kallon dan duniya a karkarar mu

Abimcinta take ci kanta a sade tana ji yanda Fannata ke aikin tambaya a kanta, tsoro take kar a je mugun kyankyaminta kamar yanda mutanen garin ke yi ya saka take son sannin ko ita wacece dan ta kara samun damar ci mata mutunci, hakan ya sa take sauri dan ta gama cin abincinta ta kara gaba , so take ta siyarwa SOFO goro na dala biyar, ta  saka dala goma asusun da take tarawa dan ta bawa Ba ko ya daina tsanarta, Gomar kuwa itama ta ci wani abin

*AGAISHAT*
ta ji sunnanta a sama sama yana yawo, sunnanta na gaskiya aka kiraya,
Da dan sauri ta dago sukai ido hudu da Fannata,
Fannata ce ta kirayi sunnanta na ainahi ba bak'a ba.............

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---
```

4️⃣

A hankali ta kai idannuwanta kan Fannata dake kara matsowa kusa da ita

A hankali fannata ta saka hannunta ta dago na Agaishat, kallon hannun take tana jujuyawa, fannata ta fahimci bayan bakinta na halitarta da Allah ya yi, akoy tarin dati ga kuma karin bakin turkudi,

Da sauri Ta janye hannunta tana kokarin mikewa daga cin abincin cike da tsoron menene kuma Fannata ke taba mata hannu?

Fannata ta ce" kin ga, ba abinda zan maki

Kallonta take da mamaki domin da hausa radau Fannata ta yi magana bayan Agaishat kadan kadan take jin hausar itama baba Tsoho ke dan koya mata dan abinda ya iya, yakan ce ba.a san gobe me zatai ba

Goshinta ta dafe ta kalli wajen iya ta ga sai faman gyara Sansanninta take(tabar buzaye), tana dan kukulewa da zare tana ajiyewa gefe tana yin kulin kadago kadago (dala biyar biyar )

Kurumci Fannata ta shiga yiwa Agaishat,
Ta yi mata nuni da hannayenta da fuskarta gaba daya,
Ta yi saurin taba ruwa ta nuna mata alamar bata wanka  ne?

Agaishat ta shiga faman saka tsohon takalminta na soso tana faman guduwa domin ta saka a kasan zuciyarta wannan abin zai kare ne a wulakanci da tozarci

*WaRDUGU*

Ta fada tana mai daga murya kamar zata kaiwa gabjejen mutumin dake tsaye a gabanta duka,

Ta kuma cewa" WaRDUGU Odon jidu anna indahan yuna yugusnan gwa ( tun kana yaro yake fama da kai)

Kansa ya dafe, ya kai dubansa kan agogon hannunsa, kallota ya yi ya yatsina fuska, can ya ce "Ayya (wato mama), Ayya inda medi mundu tam (wato mama ke rigimarki ta yi maki yawa)

Hannunta ta dora a goshinta ta shiga kai kawo, kai take tana kawowa, can ta dauki wani ihu ihu tamkar tana buda, ta je ta dawo ta je ta dawo, ta kallo shi cikin yaren hausarta da bata fita da kyau  ta ce"  shikennan rayuwar bariki (gayu) ta lalata min kai, shikennan na zama uwar da ina fadi ba.a saurarena, ko nima zaka kula zazafar gabar da ni ne kamar yanda ka kula da Abbanka (mahaifi)?

Hannayensa ya jimke ya daki garu da su, kafin yake juyowa wajen mahaifiyarsa,
Taku ya yi zuwa gabanta kafin yake sada kansa, shima cikin yaren hausar sai dai tashi ta fi dan goguwa ya ce" Ayya ba dai saboda wajen wannan bugudin (tsofo) ne kike daga hankalinki harda hada kanki kike min da wannan Bugudin (wato mahaifinsa)?

Kanta ta kawar ta ki bashi amsa hakan ya sa ya mike ya fito daga falon

Yana fitowa ya nufi wani dankareran mashin *ROUTIER* jibga jigban nan masu shegen tsada domin daga million daya abinda ya kai har million shida ne, kuma mashin ne ba mota ba...gudunsu ma daban yake da kananun mashin

Bakin gilas dinsa ya fitar ya saka ya tayar da mashin din ya yi masa wani irin ja wanda kana ganni tamkar dambe ake da mai jan da mashin din domin mugun karfi ne da shi ga kyau

Hangame gate mai gadi yayi don kar ya jawa kansa bali wajen Wardugu

Yana fitowa daga  anguwa *Plateau* a birnin Niamey ya nufi *Francophoni*  inda gidansa yake

Yana karasawa shima tuni an hangame kofar ya shige da gudun tsiya ya silala wani waje da nan ne ma.ajiyar abinda ya shafi mashin da motoci

Dira yayi ya juya da sauri sauri ya shiga hawa matatakalar bangarensa domin bangare daban daban ne da matarsa mai sunna *GALayn*

Wata yar karamar carte ce ya dora mai dauke da hotonsa ya dora daidai wani detecteur ya bada dan kara titeeee kofar ta bude
Caicaicaicaicaicaicai wash, gidan tubawa kamshi, wayo gidan batube ni.ima, bale mai auren gimbiya hajiar hajia, sarkin tsafta, sarkin ado, kwaliya ba dai a nuna mata ba, ta kasance cikin kamshi wanda indai kai ka ce zaka kwaikwaya sai dai ka tashi da mura (gaisuwa yar baba)

Sanyi mai hade da kamshi ne ya buso shi, sanyi mai sanyaya zuciya
Terrace din dakin fara kal kal kal haka take daukan ido ta sha guga,
Tafka tafkan salon ( kujeru) ne irin na zamani masu kalar fari kal kal sai dan coussin kananuwa sosai su kuwa masu kalar baki kamar yanda mauquette  (capet)

Rido (wato labulaye) yen dakin suma kalar fari ne, sai dai farin ba kar ba kamar yanda kujerun suke , shi ya fi ruwa da kalar peinture  (colern) dakin, shima an saka abinnan na daure labule baki wanda kana ganninsa ka san ba karamin kudi bane dakin ba wani tarkace aman komai ka kai dubanka ka san karshe ne sannan ya bada kala ta mamaki,

Nan ya yada zango, ya daga kansa sama ,
Iska ya furzar yana jin yanda takalmin matarsa ke tahowa kwaskwaskwaskwas
Kamshin da take fitarwa shima na daban ne, ta shafa turaruka har ta gaji,

Tunda ta fito take kallon yannayin fuskarsa, a cikin ranta ta ayanna" wani masifafe kuma ya hargitsa min yannayin miji?

Bata yi kasa da gwuiwa ba ta karaso kusa da shi ta daga damatsunnan hannayensa ta shiga masaging a hankali tana kara kallon yannayinsa

Murya can kasa ya ce" *ADIBIRA* (Matata)

Tsai ta yi tana kallonsa kafin ta ce" qu'est-ce qui ne va pas  mon Bb? (Me ke  faruwa  Baby?)

Kansa ya kawar gefe kafin ya janye hannunta a hankali ya mike ya nufi uwar dakansa

Bakinta ta tabe, Galayn akoy saurin fushi, mace ce iya mace aman bata tunnanin zata tsaya tana wani bibiyar namiji ko waye shi balatanna wardugu? Wardugu zuma ne ga zaki ga halbi, wardugu ko a cikin tubawa tsoronsa ake, mutumin da idan ransa ya baci idan bai samu ya damki mutun ba yake suma? Mutumin da ya wawuri ogansa ya daga sama ya nana da kasa ogan nasa bama na niger ba domin a niger ba marichal, bako ne da kowa ke tsoro yana shayi, gardama kadan ta hada su General Wardugu ya daga shi ya nana shi kasa a gaban yaransa da kuma yaran general, wannan abin ya jaza masa da mukaminsa da komai shugaban kasa ya tsaya kai da fata aka tura shi daji can wajen mali sai da ya yi wata hudu ya sauko, aman maimakun abin ya yi sauki sai kara gaba da yayi, mutumin dake gaba tukura da mahaifinsa , fada yayi gwa da gwa cewa abansa ya kiyayi hanyarsa kan laifin da ya boyewa kansa sai shi sai mahaifiyarsa suka sani, ita a wa zata tsaya ta bi bayan wardugu da idan ransa a bace ka bashi hakuri yake hucewa kanka? Du irin yanda yake ikirarin shi yanzu ba ruwansa da fada da mutun na gugar jiki karya ne ! Ka yarda ka yi  gigin kai masa wargin baya ce masa komai ya ciro daya daga cikin wukaken dake jikinsa ya burma maka idan ya so a kashe shi, Wardugu nada zuciya ta ainahin tubawa....

Mu je zuwa labarin *BAK'A CE*

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

5️⃣

Mikewa Galyn ta yi ta fice itama ta bi ta babar kofar danma ya san ta yi tafiyarta ta je ta kara bada turaren ruwa a jikinta ta fito ta je wajen da kys din motoci suke ta dauki guda ba tare da ta tsaya zabe ba domin kuwa kaf ciki manya ne

Tana fitowa ta shige motar ta tayar ta fice abinta wajen auren kanwar kawarta tana mai duba carte dinta ta bank dan ta tsaya ta ciro yayan banki na kari a wajen wasa....
Wannan kennan

Ya yi kai kawo ya fi a kirga, ya dafe kansa yana tunanin irin nacin mamansa kan abu, ita yanzu dan wani tsoho can daban zata dame shi kan sai ya kaita, shi ya san wani bai isa ya bashi lafiya ba aman har fadi take shi ya taimake shi yana yaro, an dai dudura masa itatuwa haka kawai za.a kashe masa kwayoyin jiki

Tsaki ya ja mai karfi, ya mike ya shiga cire kayan jikinsa masu nauyi ya rage masa culotte kawai Da dan gudugudu yake kara taka matatakalar benen bangarensa har ya karasa bangaren da piscine dinsa take
```

Ba tare da wani tsaye tsaye ba ya fada cikin ruwan nan ya shiga iyo tamkar wani kifi yana kai yana kawowa ba wani alamun gajiyawa a tatare da shi

Ba ita ta kai gidansu ba sai can dare har wajen karfe tara abinka da jeji shiru garin sai kukan tsuntsaye sai jefi jefin samari da yan mata ana tadi domin sukan kai har goma suna tadinsu

A hankali ta shige gidan nasu ta samu ta leka kanta
Fitilar kwai a kunne, sai dai tana jiyo minsharin Abansu dan haka a hankali ta kutsa ta nufi dakinsu yan matan gidan

Mahaifiyarta ta gani zaune saman abin sallah, da alama ita take jira duba da irin yanda ta tsareta da ido

Jiki a sanyaye ta karasa kusa da ita kanta duke ta ce" ANNA

Bata amsata ba sai kureta da ta yi da kallo,

Ta jima duken nan, aman bata mike ba domin ta san wani abu guda da mahaifiyarta keda na buzaye tamkar wata yar gidan sarauta koda yake du buzuwa ko buzu haka ne dadaya ne basu da shi wanda mutane ke jifansu da sun cika *Ashak* ,

Can kamar ba zatai magana ba ta ce" kin ga, ko wani hali zaki shiga, ko wace rayuwa zaki fuskanta *AGAISHAT*, ki guji sabawa mahalicin ki, ki rike mutuncin ki , ki ci gaba da hakuri watarana sai labari

Kanta take gyadawa, kuma wani dadi ta ji har cikin ranta, ko ba komai ta san a duniya bayan baba Sofo Annartama bata kyamatarta, tana kawar da kai a lamuranta ne dan gudun fitina, irin yanda Abanta ke binta da shari kwararo kwararo ya sa mutanen garima haka, ba mai kulata da daraja, ko magana za.ai mata ba.a mata ita a mutunce, ya kasance ko gaishe da mutun ta yo sai ya yi mata yatsina domin Abanta bai barta haka ba har shari ya yiwa annarta kan cewa ko dai wajen baba Sofo take zagayawa gannin irin yanda ya damu da ita ?
Wannan wutar kafin ta mutu sai da aka sha tashin hankali, baba tsoho ya yi kuka sosai aman bai daina kula Bak'a ba domin tana da mutunci yarinyar, shi Allah bai azurtashi da yin auren bama domin bashi da lafia ko ya yi ba anfani hakan ya sa yake jin yarinyar tamkar yar da ya haifa, itama tana mutunta shi tamkar mahaifinta

Mamanta na gama fadar haka ta yi shiru kanta itana a saden tamkar tana gaban sarakuwarta

A hankali ta mike ta nufi dakin su

Tana zuwa ta tarar du sun yi baci abinsu dan haka ta dauro alwallah ta shige ciki ta tayar da

sallah ta shiga ramuwar wa.inda batai ba , tana so du rintsi ta ringa samun gurin sallah sai dai tana tsoron mutane da kwagirar su, yanzu za.a wulakantata dan haka take bari idan ta zi gida sai ta yi wanda bata samu ta yi ba

Tun karfe takwas na safe Aba ya fice bayan ya canza rawaninsa daga baki zuwa maroon turkudi sabo fil, ya sayi tufafi ya sayi rawanininka harda waya, ya fito sabo kudi sun fado shikennan a haka zai fada su tamkar wuta shima ya dankaro aure daga an cinye kudin shikennan ta gudu abinta

Bai jima sosai a wajen ba ya dawo,
Daidai lokacin Anna na fitar da dawar masararsa a ruwa wace ra jika dan tana son yin garin tuwo

Bai yi mata magana ba ya zarce dakinta dake baban daki idan ka cire nasa a gidan, daman dakuna uku ne, da nasa da na Anna da na yan matan gidan
Bai yi wata wata ba ya shiga kwasar kayanta yana kaiwa dakin yan matan yana jibgewa gefe guda,
Ba wanda ya tanka shi ko ya yi mamakin lamarinsa domin sun san halinsa, haka yake du idan zai yi aure dakin mahaifiyar su yake fitar da ita ya hadeta da su ya kawo amarya, bama zai barta a dakinta ba sai dai ya hade su ya kawo amarya su sha shagalinsu ba wanda ya isa ya yi magana yanzu zai cici masa uwa ko waye

Ko kallo bai isheta ba, don ta daukarwa kanta alkawarin in dai ba mutunci ne lamarinsa toh ba zatana kai kanta yana wulakantata ba gaban yayanta.
Sai da ya gama fitar da komai kafin yake fita ya shigo da magini
Sosai aka gyara dakin ya yi tas da shi

Tare suka fita , sun jima sosai kAfin yake dawowa
Wannan karon kuwa masu shigo da kaya ne

Mariama dake wanke fuskarta bayan ta shafa kurkum ta yi tsai tana bin kayan da kallo,
A gaskiya siyayar idan ka yita a kauyen ka isa ne, tun daga gado har kayan abinci na gayu ya kwaso abinsa sai dai abin haushin babu rabonsu a ciki na amarya ne, domin idan ka auri jar buzuwa ko duniya zaka kai gidansu nasu ne ba za.ai mata komai ba sai dai a kawo maka ita daga ita sai butarta (a kauye fa kar a ce inji sajida🤣)

Sai da suka gama kawo kayan tsaf Mariama ta je faban mahaifinta ta tsaya masa kerere a gabansa, somin kuwa in dai haihuwar rashin mutunci ne ya haifa Mariama ta isa ta iya tsayaya tamkar mahaifinta

Ido tar cikin nasa da yaran buzanci ta ce" Aba ya haka? Na ga ka fara kwaso kaya alamun aure zaka yi? Ya baka fitar da mu ba? Baka ba anna kudin siyayar kayanmu ba?

Kun san wasu iyayen sun fi son yaya masu tsayayar nan, domin Aba yana dan shayin lamarin yar tasa domin a yanda yake gani tama fi shi rashin mutunci dan haka ya dan gyara rawaninsa irin zai yi magana ya ce" wani siyaya kuma? A sanina cikakiyar buzuwa ba.a yi mata kayan daki?

Ta yatsina bakinta ta ce" sai kuma cikakiyar buzuwa ana yi mata sutura

Karya ne Mariama, ya fada yana matsowa kamar zai doke ta, ya ce" ku ne yayan zamani kuke zuwar mana da abubuwan da suke neman fin karfin tunanin mu, ko uwarki haka aka bani ita, haka ake kai ku daga ku sai turkudin amarci da buta, kudin auren ku kuwa mu iyayen ku ke siyan maku kadara mu ajiye maku a nan wanda idan kun waiwaya zaku ji dadin su

Wani malalacin murmushi ta saki tana kallonsa

Ya ci gaba da fadin" ke da kin ga minister ne ya turo a nemi aurenki, ya saya maki komai, sannan ke da auren wata shida ne zaki yi ki kwashe komai ki dawo mini mu more da kudi?

Tar ta kara saka idannuwanta cikin nasa kafib take juyowa ta ga mahaifiyarta ta fara daka dawar da ta wanke ta baza a rana ta sha iska tana so ta mayar da ita gari kennan , ta kuma kai dubanta wajen yayarta *BAK'A* dake ta dirzar wankin yan matan gidan harda na su kanenta ita dai burinta idan sun tashi su bata konce, ta kuma kallon mahaifinta dake kokarin shi dole sai ya yi mata wayo, wai wani harda cewa wai ya siyar masu kadara, shi? Kudin aurwnsu bai taba wata a hannunsa ba komin yawansu zai kashe su  ne ya dawo talakansa marar mutunci, yan yatsunta biyu ta hade ta yi tap tap da su suka bada dan sauti kafin ta ce" ka kirga kudi, ina so ka bawa Anna kudi har million shida a cikin kudin da ka karba na auren mu domin na sani cinikinmu kake tamkar abin siyarwa baka amsan kasa da goma, ka bamu shida mu je birni tare da Anna mu siyo kaya mu dawo idan baka yi haka ba zan shiga duniya na saka ka a matsala kai da wanda ya kawo kudin aurena, ka san ni horonka ce

Yana tsaye bami bude har ta fice a gidan, kallonsa ya dawo wajen Anna, da sauri ya karaso ya ce" kina jinta kika yi tamkar baki gani bayan kin san tana jin nauyin zuciyarki? Ko ke kika kitsa mata a taru a cuce ni? Har million shida? Ai kudin sun kusa karewa idan na baku haka!

Bata bashi amsa ba ta ci gaba da dakanta , nan ya juya wajen Agaishat ya ga shi take kallo

Ke dan ubanki daina kallona da wasu tula tulan idannuwanki masu kama da na mayu, shegiya da aka kwaso cikin ki a waje aka yayaba min, dan bakin jini ko almajiri na yiwa tayi guduwa yake, zan zo in kwakwale miki idannuwan nan in baki a hannayen ki ki je ki kaiwa tsohon dan iskan nan da kike zuwa kina wuni wajen shi wama ya san ko me yake maki a bukar nan

Da sauri Annan ta juyo wajen shi, ta kai dubanta wajen Agaishat da ta sada kanta jikinta na bari, tausayin yarinyar ya kara dirar mata, nan ta kara gane shi ya sa idan ta fice take cika dare dan kar ta hadu da mutumin dake mahaifinta aman ya zamo makiyinta , ta rasa da wata kalma

zata kirayi mutumin dake miji a gareta, ta san ya yi karatu, sai dai son kudinsa ya fi imaninsa yawa

A hankali ta ce" ki je kawai zan idasa maki aikin

Da sauri ta ajiye wankin ta warware mayafinta na bakin turkudi butubutu da shi ta yane jikinta gaba daya ta fice har tana hardewa tana waiwayen gidan nasa

Bakin wata bishiyar mangwaro ta zauna ta fashe da wani matsanancin kuka mai karfin gaske

Ku mu je a labarin Bak'a ce na sajida

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

6️⃣
```

Kuka take tana murza goshinta a kan cinyarta dake lulube da turkudi, hawayen nan ya jika turkudin ya yayakune sannan ya gogun mata a fuska ya kara rinar da fuskar ya kasance wani waje ya fi wani wajen duhu sosai fuskar du ta yi jirwayi da ita

Sai da ta ci kukanta har kanta ya fara ciwo kafin take yin shiru, mangwaron nan ta kuma kallo gannin du ya yi jajajir ya nuna ya saka ta mike ta gyara zaninta da kyau ta kama kokarin hawa , Da kyar ta hau bakibakin ta kamo wa.inda ke kusa ta tsintsinka ta diro ta zauna nan tana gogewa da hannunta sai kuma ta sha abinta, yau bama zata iya zuwa wajen tsoho ba ta san yana da ruwa goronsa kuwa ta kai masa gobe sai ta yi safiya ta je wajen shi

Wardugu, yanzu yanzu?

Kansa ya dafe ya ce" Ayya ko kin fasa tafiyar ne?

Da sauri ta mike ta nufi dakinta tana dafe kanta, yaron nan akoy kagauta , bashi da hakuri yanzu in ba rigima ba a kai tsayen nan ya zo yace su yi tafiyar da a yanda ake bata labari garin can cikin jeji ne? Aman ba komai irin yanda take mafarkin mutumin nan abin ya tsaye mata a rai, tana tune sun yi da shi idan yaro ya samu lafiya sai ta bashi salama da abinda ya sawaka sai dai ta zo tana yiwa Wardugu magani da magungunnan aka tashe su daga garin aka maido su Capital tun daga shi bata kara ganninsa ba domin ta neme shi sosai, sai kwanan nan take jin lanarin yanzu tsufa ya kama shi sosai baya yawo yana garinsa na haihuwa harma an fada mata sunnan garin , tana son sauke nauyi domin kuwa tun daga kan maganin wajensa Allah ya aminta wardugu bai kuma Huka ba sai tana gannin haki ne ta je ta sauke ba wanda ya san gawar fari

Nade ta fito da lifaya mai ruwan ja da kyalkyalin zaiba, lifayar sai baza kanshi take , Ayya ta kwana biyu a duniya aman karshe ce, akoy iya ado da sannin hakin turare, idan ka ganta sai ta birge ka gata da saka zinare tamkar ba da kudi take siya ba, danta ya bata damar murza mulkin da ta ga dama

Tafiyar manya ba.a kwasan tufafi, mai aikinta baturiya ce ta fito da wata yar valise (yar akwati) yar karama wace a ciki ta saka du wani abin bukatarta ta nufi kofa dan kaiwa cikin mota

Gaba ya yi yana amsa waya da aminiyarsa, kawarsa, wace du duniya itace babar kawarsa sai wa.inda ba za.a rasa ba, itace basa fada, ta iya tafiyar da lamarinsa ta iya zama da shi , sannan

du irin yanda ya ki jinnin jajayen buzaye ita wannan baya iya kyamatarta , ba.a shaifar mutun aman shi zai bigi kirji da halayen *ALHINAYETT*

Kana nufin yanzu yanzu? Bama zan yi maku bankwana ba?

Wardugu ya ce" Alhinayettt bafa wani jimawa zamu yi ba, ke dai ki yi mana adu.a
Yana fadin haka daidai yana zama cikin motar Hilux tamkar wani daki tana fa fadin waje,

Sai fa ya gama wayar ya dubo AYYA da ta tsura masa ido

Kallonta yake da alamar mamakin kallon domin irin kallon nan ne na tsare mutun idan ya yi karya

Bakinta ta dan turo ta ce" kuma ka ce ba budurwarka bace, mutunci ne bakwa wata soyaya da ita,

Murmushi ya yi do.in daman ya saka a ransa wannan ne, ya dan sasauto ya riko hannunta ya ce" Anna, aa, Alhinayett aminiyata ce, wace bani da amini ko aminiyar da ta kai ta

Yatsina fuska ta yi ta ce" karyar banza wai aminci mace da namiji ? Ai ba shi sai idan soyaya ake

Kawar da kansa ya yi ya ce" kin ce a lokacin da ya baki magungunnan da aka dura min ma tsofo ne, kuma har yanzu kina da tabacin yana raye? Ni din ma fa na jima a duniya

Murmushi ta saki ta mika hannayenta masu saye da zobunnan zinariya ta dankwashe masa kansa dan ta san yana so ta yi zuciya ne ita kuwa ba zata yi ba, halayensa tana gannin sai dai ta fada masa domin tun bai san kansa take tafe da shi ba

Sun Dauki hanyar airport dan  zuwa garin Agadez daga nan kuma ya nemi abinda zai kai su garin da suka nufa

Mali yaro ne ke wasa a wajen auren kawar Walyn ,
Tunda ta shigo wajen wasan yake kofata da kiran General wande, Walyn kin fice yaro (Matar general),
Tunda ta nemi wajen da tana iya gannin kowa kowa na iya ganninta ta hakimce ta dauki kafa daya ta dora saman daya, ta karkace kadan ya kasance dankareriyar sarkarta ta zinari ta fito sosai, ta dora hannunta guda saman cinyarta awarwarayenta ma suka fito radau da su, takan dan saki dan murmushi hakoran makarta su bayanna, ta dan juya ta kuma juyar da kanta tana karewa mata da yan matan wajen kallo tana auna su daya bayan daya,
Kari ake masa na hauka aman hankalinsa du ya karkata kanta, ya sani ne udan ta zuge bakin

wannan jakar nata mai shegen kyau sai ya yi kwasa, jakar a yashe take kusa da kafarta tamkar ba komai na anfani ciki bayan kuwa a cikinta kudane da dankara dankaran wayoyinta na kece raini

A haka har aka fito daga salar isha.i bata mike ta je ta yi sallar ba suna zaune sun zagaye mawakin da yakan silalewa ya bar yaransa da basu san ciwon kansu suma ba ya je ya gabatar da sallah ya dawo ya dora daga inda ya tsaya

Wannan dawowar da ya yi bai zame ko.ina ba sai gabanta domin ya lura yau yan mulkin ne, yan na isan ne, tana son nuna bambanci tsakaninta da sautan matan wajen,
Yana zuwa ya shiga kodata, yana waketa, yana wake jarumtar mijinta

Kanta ya fashe , ya yi gingirigin
Ai kuwa ta dauki jakar nan ta yage bakinta ta shiga zuba masa masu aku wato jika goma goma tana dangalar masa tana yi irin bata san ciwonsu ba sai da ta karar da jimki biyu wajen ya cika da ihu wata kawarta guda na daukanta vidio dan ta tura mata
A wannan rana an jima ana wasa wanda Walyn bata bar wajen wasan nan ba sai da aka gama sai da ta ga karyar ko wace yar karya kafin take mikewa ta dauki jakarta kawayenta masu mata fada suka biyo bayanta har sai da ta shige dankareriyar bakar motarta bayan ta wankesu suma da kudi ta tayar ta halba bakin titi a lokacin har karfe goma sha daya ta buga na dare

Garin niamey capital ta niger du wanda ya taba shigota ya san gari ne dake baje ta ko.ina da polisai
Basa wasa kame suke tun karfin su, in dai ka kuskura ka taka doka toh fa zasu damke ka ne ba sasauci

Tukinta take cikin nutsuwa,
Danja ce ta tsayar da ita bakin inda polisai shida ke tsaye suna duba takardun mota na mashin, da kuma takardar shedan kai wanene
Hankalinta konce take jira danja ta saki domin ta san sun san number motar general ko sun kurbi giyar bera ba zasu tunkareta ba koda kuwa ta taka dokar domin ta tsira tunda ta hau motar *DOKA* gabadaya

Kwonkwonkwon karar kwonkwasa motarta,
Da mamaki ta dubi wajen
Wani saurayin police ne fuskarsa daure tamau ba alamun wasa a tatare da shi

Da yannayin rashin mutunci ta sauke gilashin motar ta sauke masa idannuwanta masu nuni da baka da wayo

Shima fuska a daure ya ce" madame vous etes en état d'arrestation, veillez sortir calmement nous nous occuperont  de la voiture (Madame mun kama ki  ki fito cikin nutsuwa zamu kula da motar)

Da mamaki take yi masa kallon sakarai, baki bude ta nuno shi da yatsarta ta ce" kai aman kai sabo ne ko? Waye kai? Ka san ko wacece ni?

Sadowa ya yi sosai ya saka idannuwansa cikin nata ya ce" eh mun san ko ke wacece, umarnin mijinki ne in dai kika kai karfe bakwai a gari du wanda ya hadu da ke ya kai ki cel ki kwana da safe karfe goma a sake ki daidai gari ya cika kuma a rubuta a jarida!

Dum dum dum take jin maganar tamkar saukar aradu, quoi? (What), ita? A cel? Prison! Ita Walyn? Wardugu wardugu ta fada tun karfinta tana dukan sitiyarin motar ta .........

Ohk

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

7️⃣
```

Ita Wardugu xai yiwa wannan wulakancin? Ta kwana a cikin kaso, batai sata batai komai ba? Dan kawai ta cika dare?

Wayarta ta warta a cikin jakarta ta shiga laluben numbersa wace ta sam zata same shi

Ta yi kira ya fi a kirga daidai lokacin polisawan sun zagayeta tamkar dai ta yi wani gagarumin laifi

Hanjaki kwonce ya daga domin lokacin yana hakimce kan gadon hotel din da ya sauka ita Ayya tana can gidan sarkin Agadez matarsa uwar gidan ce kawarta ta kusa sosai, shi kuwa ya ki sauka a nan ya je hotel , bayan ya gama harkar kasuwancinsa ne kiran Walyn ya shigo wayarsa, domin Wardugu na sana.a.o.i ya san dadin nema , yakan ce ba dole ya nema ba shi mai Ayya da Walyn

Murya irin ta yan duniya ya ce" adibinira (wato matata ) (readers kar ku manta a wannan nvel yare hudu ne, buzanci, tubanci, french da kuma hausa )

Murya ta sasauta tana tura hannunta cikin kannanuwan kitson da ta sha domin dai tubawa basa wasa da kitso ta ce"  Haba mijina ya haka wannan tsatsauran hukuncin?

Murmushi ya yi jin yanda ta sasauto, kennan dai sai yanzu ta nufi gida ko? Muryarsa yanda take ya ce" hukuncin ya yi tsauri ne? Ko bai kai daidai da laifinki ba?

Idannuwanta ta lunshe tana jinsa har cikin ranta ta ce" matarka guda a prison? Ko laifi na yi ina tunanin na fi karfin nan sai dai ka hukunta ni a gida a dakin mu a saman gadon barcin mu ka rungumeni ka matseni ka haukatani da lamuranka , na san ina cika dare kuma baka so aman mutun ai ajizi ne, ka yi mini uzuri Wardugu

Murmushi mai sauti ya sakar mata, ya ce" bara dai mu gwada wannan idan ya so na dawo daga tafiar da baki tsaya kin ji ina zan je me zan je yi ba zamu yi magana

Fashe masa ta yi da kukan kisa , ta ci gaba da lalaba shi dan ya yarda ya yi masu magana su sakar mata hanya ta karasa gida dare na yi

Lumfashi ya sauke ya ce" ki bani daya daga cikin su

Cike da murna ta mikawa wanda ya fi kusa da ita tana zabga masa harara

Yana kara wayar ya kame yana sara masa tamkar yana gabansa

Murya a kausashe ya ce" wasu sutura ne a jikin matata?

Murya a ladafce ya ce" aa oga, mu mun isa mu kali matarka? Bamu kala ba bamu san irin

suturar jikinta ba

A ransa ya ayana han, kafin yake cewa" idan ta ki ta fito ku zauna da ita a nan har safiya ta yi , har karfe goma sha biyu na rana kowa ya kasance ya ganta, sannan ku gayaci jarida ku bada cikaken labarin abinda ya faru, kar ku taba jikinta aman bata wahala, ka rike wayarta a hannunka sai goben ka bata! Sannan kar ku nuna mata wasa idan ta so kawo maku tsayaya ku tsoratata da bindiga

Da " a vos ordres ya amsa kafin yake katse layin ya saka a aljihun rigarsa

Wa ya ga zafi biyu 🤣

Karfe uku ne fa na dare aman ji kake gam gam gam ana dukan yar kofar gidan nasa

Da sauri *Tibillal* wato mahaifiyar su Agaishat mata a wajen *ALGABIT* mahaifin su Gaishat ta zabura ta kai dubanta wajen *AGAISHAT* dake zaune tsuru tun bugawar farko ta fara tana kallon kofar shigowar su

Mayafinta ta ja da kyau ta fito ta nufi dakin mijin nata

Tana zuwa ta tarar da shi a kwonce tamkar mai baci bayan ya farka ya yi tsuru daga kwoncen yana tsoron mikewa ma

Girgiza kafafuwansa ta fara ta ce" Algabit, Algabitt, ka tashi ana ta buga gidan nan

Hannunsa ya saka ya bige nata ya ce" naki na tashin, bayan a gari an san na amshi kudin auren yaranna , in na bude wani mugu ne fa? Koma waye ya yi hakurin safe mana aman a wannan tsofon daren? Ba zan bude ba!

Gannin ya tashi sai balbaleta yake da fadan da hujojinsa na karya ta mike ta nufi kofar wanda ya saka ya hantsilo ya rarumi wukarsa ya ja tunga yana fadin" kar ki bude mana, koma waye a daren nan ba bakon alkhairi bane!

Janye sakatar ta yi ta bude kofar,

Fado mata ta yi a jiki tana kuka, jikinta du sai rawa yake, ga sanyin garin aman wata yar ficiciyar riga ce a jikinta, mutumin da ya kawota a rakumi ne ya ce" na ga gidan zan dawo da safe a bani salamata!

Da tashin hankali Anna ta janyota cikin gidan tana ta kokarin kara dagota tana duba fuskarta

dake da balshe ko.ina a tsannanin tashin hankali ta ce" *FATIMATA* fatimata , fatimata

Gaba daya mutanen gidan suka fito jin muryar Anna cikin tashin hankali

Da sauri Algabitt ya karaso ya janyota ya ce" Ke Fatimata, meye haka? Daga ina kike? Ya haka a tsiyace jiki a lalace? Ina mijin naki yake????

Dago kumburanrun idannuwanta ta yi ta sauke su kansa, da haushi haushi ta budi baki tun karfinta ta ce"""" Aba, sai na kashe shi, kuma ko zaka kashe ni sai na hana ka kara bada kannuna a irin auren da ka yi mini!

Idannuwa ya zaro ya daga wukar nan nasa ya. Nufota ya saro daidai ita sai aka yi rashin sa.a Anna ta saka hannunta ta tare wukar ta yi mata muguwar sara a gefen hannunta ta yanketa sosai nan da nan jini ya bale

Ihu yayan suka kwasa, da sauri mariama ta karbe wukar ta yi jifa da ita ta hayayako masa da mugun bacin rai da nuni da zata iya aikata komai ta ce" ka je, kar jini ya biya jini!

Juyawa ya yi da sauri yana mamakin Kaf yayansa idan ya yi magana a da jiki na bari suke aikata abinda yake so aman kwanakin nan yana haduwa da hari kala kala da wajaje daban daban a cikin yayansa bale Mariama yarinyar na da zuciya ........

Labari bak'a ce labari ne kirkirare bisa lamarin da ba kirkirare ba, labarin yana tafiya ne bisa gaskiyar lamarin abinda ke faruwa , tabas na shiga kuma sai na fada......ku mu je zuwa a labarim bak'a ce in sha Allah

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

8️⃣

Yana fita Bak'a ta cire daurin dake kanta ta daure hannun mamansu da fan kwalin du suka zauna jigum jigum suna kallon Fatimata

A hankali ta dora kanta kan cinyar mamansu da take jin zuciyarta na yi mata nauyi sosai ta ce" a ranar da aka dora ni saman Amale (Rakumi) daga ni sai mata hudun da suka zo a matsayin fagin mijin da aka aura mini muka tafi

Mun shiga garin agadez daga nan muka dauki hanya muke tafia tamkar ba zamu tsaya ba
Sai da muka je Damagaran daga nan muke mike muka dauki hanyar kano
Muna zuwa kanno muka kwana guda muka dauki motar asuba suwa Abuja

Tafiyarmu tamkar ba zata kare ba, tsakanina da su ido ne su basa jin yarena nima bana jin nasu ya kasance muna tafiyar kurame ne sai dai abinda na lura da shi tamkar masu jin haushina domin ko abinci zasu bani sai dai su wulo mini su fadi wata kalma sannan su yi mini nuni da in ci

Ba mu mu isa garin nan ba sai da safe domin da mukai dare muka tsaya muka waye a wani garin kafin mu karasa

Gida ne tafkeke, ya tsaru, ya hadu iya haduwa
Muna zuwa kowace ta yi tafiyarta aka barni a wani tankamemen falo ina zaune ni guda

Ban jima sosai ba na fara gannin wasu mata masu kyau suma kowace ta sha kwaliya sai baza kamshi take sun fifito sun layu saman kujera gefe da gefena hakan ya saka na takure waje
```

guda

Ba.a jima ba wanda aka aura min da sunan mijina ya fito ashe yana cikin dakin du zaman nan da na yi ya zo ya zauna saman kujerar dake kallon tamu ya dora kafa daya kan daya
Walahi Anna mutumin sam ba annuri a tare da shi, mumuna ne, garjejen kato ne fuskarsa ba anuri ba fara.a ba haske ko kadan a nan ya kuna taba domin ba sigari bace taba ce ya kuna ya shiga ja wace nan take wajen ya garwaye da warin kwaya
Wasu maza ne suka fara shigowa, suka zauna suma inda suke hangen mu da kyau abin mamaki matan nan sai su ringa mukewa daya bayan daya su jujuya gaban mutanen nan wasu har su dakan masu duwawu su mamatsa a gabanmu a gaban kowa shi kuwa yana hakimce idan mace ta yi maka sai su hau ciniki cikin jarshen turanci a dauki mace a tafi da ita kwana wato Bariki
Nan wani yace wannan fa? Wato ni domin sun ga sabuwa ce a wajen

Da sauri na mike domin nunoni ya yi kafin yake yin maganar, koda ban ji me yace ba idannuwana sun nuna mini abubuwan da suka faru na ga komai na gane komai

Magana ya yi masu wace ban san me yake nufi ba suka gama kasuwancinsu ya cashi kudinsa sosai kafin suke tafiya

Sai da ya gama shaye shayensa ya taso kusa da ni sosai da muryar mashayi ya ce" ke fa sai na yi maki filafila dan kuwa an caje ni kudi kafin a bani ke kuma dan iskanci aka kawo ki daga ke sai wannan bakin kayan

Tashi ki tube

Da mamaki nake kallon shi, in tube, wai ina ne nan? Me hakan ke nufi? Matan nan su waye? In tube haka kai tsaye ai ko matarka ce ni koda mun saba da sannin juna fitsara ne gatsal ka kale ni ka ce mini tube

Mikewa na yi da yarena na rufe ido na shiga zazaga fitsara ina son sannin inda ya nufa

Ta yi shiru tana sauke ajiyar zuciya kafin take kara sakin wani kukan mai karfi ta ce" Anna matan nan da suka fita bayan ya amshi kudaden karuwanci da zasu fita su kwana da karti ashe gaba dayan su suna zaune a matsayin matansa mace har bakwai ni ta takwas cikinsu ba daya ta yarwa sannan ba daya da ta san hanyar gidansu
A wannan ranar da katsa ya dake ni kafin yake zuwarmini da wata irin sufa yayi anfani da ni ba imani yana gamawa ya wawatsa kafafuwana ya goge gaba daya najasar nan ya shafe a fuskarsa harda jini jinin nan ya side hannayen nasa ya fice
Anna a wannan ranar.kafin gari ya waye sau tara yana zuwar mini

Mariama ce ta dauko kwan fitilar sosai ta haska wajen kafafuwan Fatimata, ruwa ne ke yawo wanda ya saka Mariama cewa" Anna ruwan nan kuma na menene?

Fatimata ta ce" fitsarina ne ba ruwa ba, haka fitsari ke zubar mini bama na sannin yana binna

Anna ta fashe da wani irin kuka kafin ta ture kan Fatimata ta mike ta yi dakin yaren da sauri hannayenta duka biyu saman kanta, *YoYo, YoYon fitsari Fatimata ke yi*!

A wannan rana yanda suka ga rana haka suka ga dare inda suka cure gaba dayansu waje guda ba mai yiwa yar uwarta magana sai dai suna bin juna da ido , nan Mariama ta mike ta dauko wata leda baka baba ta shinfida ta dauko zani ta shinfida ta kallo yan uwanta ta ce" ke fatimata taso ki kwonta saman nan, ke Agaishat(Bak'a) tafi wajen Anna, kuma ku taso mu kwonta dare na tafiya kar safiya ta yi mana a nan

A hankali ta samu ta lalaba ta hau, suma du suka samu waje suka kwonkwonta ba dan zasu samu yin bacin ba, sun dai yi zuru ne domin Fatimata bata gama basu labarin irin ukubar da ta sha ba aka ga fitsari na binta hakan kuwa ya tayarwa da Annar hankali bata ma tsaya ta ji sauran zancen ba

Anna ce duke kanta kasa ta kai sujada tana ta sheka kuka ta ce" ALLAH ka san wacece ni, kai ka halice ni, ya Allah ina cikin jarabawarka tun daga yannayin aurena har zuwa yau, na rasa me ke daure da ni da wannan mutumin ainahi Allahna idan ba a cikin sallah ba bana iya tuna wacece ni, menene tarihina, ina da yan uwa ko haka nake ni daya? Bana son a yi min maganar ko wa ya kawo min zancen zan nuna bacin raina ne, Allah yayana, ka bayannar sauran, wa.inda basu da lafia ya Allah ka basu lafia, wa.inda yake niyar aurarwa dan samun abin duniya Idan da alkhairi a cikin auren ka tabatarda, idan kuwa ba alkhairi bane Allah kai ka yi shi ka hana, ka hana ya Allah Allah sannan ka yaye min duhun dake cinkushe min ganina

Ta jima tana kai kukanta wajen Allah kafin take mikewa ta yi tahiya ta salamce ta dora adu.a tana ta yawaita istigfari domin ba abinda ke saurin yaye kunci irinta

Da safe tana tashi ta dauki sansani (tabar buzaye) a cikin nata ta matsa a bakinta ta yane jikinta ta buga safiya ta fice a gidan

Zugum suke ba mai yiwa dan uwansa magana har wajen karfe tara Anna bata dawo ba, Aba daman tun cikin daren nan ya fice basu san ina ya kwana ba sannan bai dawo ba, sun zubawa sarautar Allah ido ne kawai

A hankali Bak'a ta kali gorin tsofo, ta mayar ta kule a harshen zaninta a ranta take ayanna bawan Allah ko a wani hali yake? Ko an dauko masa ruwa? Tabas yana cikin damuwar rashin ganninta yau har za.a kwana biyu, sai dai ba zata iya fita ta bar gidansu a wannan halin ba, a hankali ta rike goron ta ce" sofo ina nan lafiata klau, ka ga na saya maka goro ma kar ka damu ina nan tafe wajenka

..........inna Anna ta tafi?????

Gyara kimtsi, mai zamani dan sarki jikan sarki, Buzu jinnin sarauta, yaro mai zamani, taka lafia bijimin sarki, taka lafiya gagara gasa, kai ne na uku baban Rabatima, ka shigo a hankali yarima, taka sanu sanu sarkina

,
Kirarin da jakadiya ke yi masa kennan tunda ya tunkaro dakin mahaifiyarsa,
dan dakatawa ya yi har ta yi gyaran murya kafin yake saka kai da salama a bakinsa

Dago kanta ta yi tana murmushi ta amsa shi, a hankali ya karasa yana wata irin tafiya idan ya daga kafa daya kafin ya daga dayar sai ya jima

Dukawa ya yi har kasa kansa kasa ya ce" ta gode Anna, ta gode Amy (Wato mahaifiyar Wardugu aminiyar matar sarki....da Amy suke kiranta bisa umarnin mahaifiyarsu,)

Murmushi take sakar masa kafin ta ce" oh son tashi mana, amynka ce fa ko dan ka daina zuwa wajena ne?

Yana murmushi ya mike ya zauna saman kushin dake wajen cikin nustuwa suka shiga gaisawa da harsen freinsh domin ita ce kawai yaren da zasu yi su jima suna hira cikib gane abinda suke fadawa juna

Dan jim ya biyo baya kafin yake cewa " Amy ya labarin Oga ne? Na yi na yi ya siyar min da wata mota aman da yake yan rigimar a kansa cewa yayi aa motar ba ta yara bace, ki ji fa Amy

Dariya suka saka gaba dayansu, Ayya ta ce" Wardugu, Wardugu baya jin magana Aghali, sai hakuri da murdaden halayen Wardugu

Mahaifiyar Aghali matar sarki ta ce" Kawata, wai ina labarin aban Wardugu ne? Ni kam ina mamakin lamarinku, kawai daga wannan dan laifin?

Ayya ta dago tana kallonta, a ranta ta ayanna ban ga laifinki ba, ku baku dauki haka a matsayin laifi ba,
A fili kuwa ta ce" manta

Murmushi Mahaifiyar Aghali ta yi, Ayya akoy mulki  wannan da gidan sarauta take da an ji jiki domin mace ce mai mulki da isa, ga jan aji, da yake an dauko hirar da bata so daga haka ta katse hirar ta mike tana yi masu salama dan tana son shiga ciki ta kirayi number Wardugu rabonta da shi tunfa suka karaso jiya ba shi ba labarinsa

...........rashin Comment ne kawai zai saka ni daukan matakin siyar da novel din nan ko na tsayar da shi, 😊

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

9️⃣

Ayya na zuwa dakin da aka sauketa zauna ta jinginar da bayanta jikin kujera ta daga kanta sama,
Ta jima tana tunani, kafin take sauke ajiyar Zuciya a fili ta ce " *MARAHUT*, ina ka shiga? Ka san komai ka tarwatsa rayuwarmu, Marahut ina tausaya maka sai dai mutuncina darajata ba zan yarda ka zubda mini ba! Ka zabi wancen rayuwar ko? Ba komai ka je sannu duniya zata koya maka hankali,

Ranta ne ta ji yana suya, yama aka yi ta tabo mata wannan mikin, ta sani da gangan ta tuno mata da maganar domin ta fi kowa sannin abinda ya faru, ita kadai sai Wardugu suka san takamaimai abinda ya faru aman zatana tuno mata da shi , ita so take sai ta yi hakuri bata san ta rufe babinsa ba kuma ko da jaraba sai ya saketa dan bata fatan idan ta mutu ya kasance shine alwalin gawarta (Toh fa😳 tubawa akoy zuciya)

Aghali, dan me ba zaka kara aure ba? Matanka biyu yarka daya mace sai matan daki , ko a cikinsu har yanzu ba wace ta samu ciki bayan ina kula da irin zubin da ake maka ana canzawa
```

du wace ta kwana biyu, ko dai baka zuwa inda suken da gaske? Domin na ji kishin kishin cewar wannan matar taka ta shanye min kai,
Mahaifiyar magajin sarki ce ke fada kan ya ki karo aure bayan tana son ya tara yaya

Murmushi ya yi ya ce " zan kara aure, ki kwontar da hankalinki,

Ajiyar zuciya ta sauke kafin take miko masa yar akwati tana murmushi ta ce" ka ga Amynka ta kawowa wannan mumunar ( wato yarsa jikarta)

Hannu ya saka ya bude ya gani, sarka ne da yan kunaye na zinari masu kyau sosai kirar yara, murmushi ya yi ya ce" zata je ta gaisheta sannan ta yi godiya........ wannan kennan

Sai da ta bude lulubarta suka ga mace ce bayan ta fada masu ita mahaifiyar Gaishat ce , suka je suka shaidawa sarki ya bada izinin a shigar da ita bangaren Gaishat din yana mamakin zuwanta da fadawa zuciyarsa ba lafia ba domin shekara kusan takwas da aurensu bata taba takowa ko aiko da kannen Gaishat din ba duda tana yarta ta fari, itama bata wani zuwa gidan du ta takura rayuwarta da tsoronsa ta mayar da kanta ta daki duda kuwa irin yanda yake daukaka martabarta fiye da iyayen yayansa

Tana shiga dakin ta nemi waje nan kasa ta zauna ta sada kanta , da kujeru da komai aman ta fi fanewa zama a kasan nan

Da sauri ta fito jin sakon Sarki wai mamanta ce ta zo
Tana fitowa ta karaso da gudu ta riko hannayenta a rikice ta ce" Anna lafia? Anna wa ya mutu? Anna na shiga uku me yake damunki? Anna me ke faruwa? Me aka maki Anna? Anna.....

Shiiiiit anna ta fada tana dora yatsarta saman leben Gaishat, itama tana kare mata kallo, yarinyar bata wani karu ba a jikinta na da, sai dan girma daga fuska da ta kara, duda jikinta bai nuna alamar wahala ba aman tana da rama, kanta daure ,
Kunyar Gaishat din ta ji ta kamata, dole ta rikice domin bata taba zuwa alkhairi ko tashin hankali ba, itace ma ke yin kokari idan ta san Abansu baya gari ta leko a tsaitsaye ta koma shima ba wani zantawa suke sai dai su bi junna da ita
Tunani ta afka shin fada mata zata yi ko kawai ta yi shiru ta juya

A hankali Gaishat ta dago habar mamanta, dara daran idannuwanta na gado ta saka cikin nata ta ce" Anna, me ke damunki? Ki fada mani kin ji? In sha Allah ko bani da maganin damuwarki zan taya ki da adu.a

Anna ta sauke ajiyar zuciya ta ce" Gaishat, Algabitt ne....ya samarwa su Mariama mazajen aure wa.inda bama a niger din suke ba, kin san bani da labari tghmass ita a niger din ma aka bayar da ita, jiya Fatimata ta dawo, mariama fatimata ta kamu da cutar rashin rike fitsari , kin san ba

maganinsa a kauye sai asibiti, baki ga fatimata ba, ta dawo wata iri,
Ga irin tsanar Agaishat (BAK'A) , ya sako yarinyar a gaba tamkar ya kasheta dan ya san gardawan da yake zuwa da su dan zaben mata ba zasu zabeta ba, shi ya sa nake kara barinta da datinta, mai yiwuwa ita ta tsira daga muguwar rayuwar da yake saka mini yaya

Shiru ta yi kanta sade tana gursheken kuka daga ita har Gaishat din,

Ajiyar zuciya Gaishat ta sauke ta ce" Anna zan zo gidan kin ji? Sai mu samo abinda ya samu mu samu shiga asibitin

Ido Anna ta zaro ta ce" ta yaya zaki fita Gaishat?

Gaishat ta yi murmushi ta ce" Anna, ki daina damuwa da damuwata, ni na dorawa kaina, tabas Aba ya yi auren dole da mutumin da bana so, mai mulkin garina aman shi mutumen jira yake in nuna bukatata a wani abin jiki na rawa yake yi min ko menene , bana tunanin fita zata zama damuwa tsakanina da shi

Anna ta sauke ajiyar zuciya, ta dago habar Gaishat ta ce" me ya sa toh ba zaki kyautata masa ki kontar da hankalinki ba? Shekarunnan ba fa kwanaki bane, ya ci ace kin zubar da komai kun fuskanci juna, ke Allah ya taimake ki kina cikin konciyar hankali kar ki bijirewa Allah mana

Gaishat ta sauke ajiyar zuciya tana kallon Anna na kara nade jikinta da fuskarta wato dai tafia zata yi, ita ba zata ki su dawama a nan suna hira da mahaifiyarta ba

Tana ji tana gani Anna ta yi mata salama ta fice a gidan tana fatan kar ta hadu da wani a kusan gidan yarta ta fari , haka kawai take jin kunyar haka .......

Da dare, bayan ya gama salama da kowa ya nufo dakin mai motsa zuciyarsa, ya sani ne ta san sarai itace da shi aman taga damar ya tarar da ta rufe kofarta

Ga mamakinsa yana taba kofar ya tarar da ita a bude,
Turawa ya yi a hankali ya shiga da salama a bakinsa

Kanta ta dago duda tana jin kunya , ta yi kokari ta amsa salamarsa cikin nutsuwa tana dubansa

Da sauri ya karasa inda take zaune, da alama har wanka ta yi, na menene? Taba jikinta ya fara yi hankalinsa a dan tashe ya ce" GAISHAT baki da lafia ne? Me ke damun ki?

Dan bakinta ta turo, kafin take dauke hannun nasa ta kara turo bakin, murya a matukar kasalance ta ce" me ya sa ka zabi aurena ta hanyar baiwa Abanna damar ya ci gaba da tafka tsiya a cikin garinka?

Dakatawa ya yi, ya yi tsai yana kallonta, a hankali ya rungumeta a jikinsa ya ce" ba dai za.a yafe min ba du irin hakurin da nake bayarwa? Ki gane dan adam nake mai cike da izgili da sabo a doron kasa,

Ajiyar zuciya ta sauke ta ce" ina so ka bar ni na je gida

Da sauri ya zabura ya cikata yana kallonta, muryarsa na rawa rawa ya ce" zaki tafi ki barni kennan? Yau kin fitar abinda ke cikinki shine zaki yi nesa da ni? Me yasa ba zaki yi mini adalci ba? Ina sane da du ranar da zan zo gare ki sai kin sha madaciya dan kar ki haihu da ni, na so daukan mataki a kanki aman bana iyawa Gaishat, ki yi mini adalci mana

Dora dan yatsarta ta yi saman lebensa jajaji abinka da jan buzu ruwan sarauta ko na kauye dawisu ne, ta ce" zama da kai yanzu na fara, ina son zuwa gidanmu ne dan kanwata ba lafia, muna son kaita asibiti, ka bani dama da ikon da zan yi bajinta a lamarin

Ajiyar zuciya ya sauke, ya rungumeta sosai har kamar ta yi ihun zafi, ya mikar da ita yana kallonta ya shiga warware lafayar da ta yane jikinta yanai mata kallon maita, haka ya idasa shigar da ita uwar dakanta cike da zumudi, wa ya isa in ba ita ba? Ita kadai yake tardowa har dakinta, hajia Gaishat mai sarkin garin *TIMIYA*

Kamar yanda ya yi alkawari haka ya bayar da rakumi har goma, ya bata kudi masu yawa ya lamunce mata zuwa gari dan kai kanwarta asibiti inda gari ya dauka ana ta lale lale gimbiya ta karbi soyayar sarkinsu, abinka da kauye har yar salah aka yi ta murnar hakan ...................

🐪🐪🐪 *BAK'A CE*🐪🐪🐪

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---
```

11

........Niamey.......

Gidan Wardugu

Kawata, dan Allah wai da gadke kike? Gaki ga yan kaso wa.inda suka aikata mugun laifi? Gaskiya oga ya san kan mugunta

Walyn ta ja tsaki ta ce" ke, a dakin nan a nan suke fitsari, mata sai kawai ki ga an dage buje an tsirara fitsari a tsaye, basa kunya basa kyankyamin wajen , kai gaskiya Wardugu ni da shi akoy tashin hankali, ba ni ya wulakanta ba, walahi sai na rama!

Me zaki yi masa? Wardugu ne fa? Kin manta waye shi? Ko mu da muke gari bama rayuwa da shi mun san waye shi, koda kina kema jinnin tubawa ba lale ki iya da rigimarsa ba, ya hada abubuwa da yawa ne, kin ga shine da daya kwalin kwal a wajen iyayensa, shine Wardugu mai sunnan rikitatu a cikin ku, shi ne Batube, kuma shi ne Soja! Wardugu kakarfa, tsayaye, isashe, hamshakin......

Ke meye haka? Walyn ta fada tana kallon kawar tata,
Ta ce" ya zaki tsaya kina koda min miji sai kace wata mai son min miji? Toh bara ki ji mu a yarenmu ba.a yiwa mace kishiya sai ta cika wa.adin yin hakan, duka duka shekarana biyu da aure da mijina, ko na kai shekarun da yana iya kara wata Wardugu haramiyar wata mace ce a nan duniya, ban ki ba lahira idan ya dace da aljanna!

Murmushi ta yi tana kallonta ta ce" dadina da ke saurin hawa , toh yi hakuri ni ban kai abin can ba ..........

Bakinta ta tabe ta ci gaba da shafa cream dinta kan kurajen cizon sauron da suka yi mata cin balaki a cikin cel din nan, rabonta da ta saka kafarta kofa tunda abin nan ya faru, gashi ta rasa Wardugu a waya kwata kwata, !

Dogo ne fari kar, datijo ne christa sunansa Docter Lucien, kwararen likitan mata kennan wanda ya karanci abin kuma ya lakanta,

Allah ya taimaki su Anna sun samu gannin Docter Lucien a dasha kuma tausayin irin ciwon da ya gani bayan ya sha fada ya karbe su ya shirya shiga tiyata da ita a washe gari wanda cikin ikon Allah sai da ya dauki awa shida kafin yake fitowa daga dakin tiyatar da ita shi ya hada zufa hakama masu kama masa wanda ba.a jima sosai ba aka gurgurota a gadon mararsa lafia aka kaita dakin da ake kontar da masu yoyon fitsari

Jigum suke zaune suna mamakin wai asibiti ce haka, su kam tunda suka shigo garin a tsorace suke da yannayin tsarin gari, gini ne kala daban daban bene kai kasa na cin kudin masu kudin birni ....

A hankali ta shiga bukar tana dube dube kafin take kallo shi, a kwonce yake , idannuwansa a rufe kamar marar lafia

Da sauri ta karasa ta ce " Sofo?

Firgigit ya buda idannuwansa ya sauke saman kanta,

Kokarin tashi yake wanda da kyar abin tsufa ya samu ya zauna yana kallonta, murya na rawa irin ta tsufa ya ce" ina kika shiga? AGAISHAT zuciyata ta rikice na rashin gannin ki, na damu na kasa baci, kin ji har zazabi nake dan bana ganninki yata, ina kika je kwana biyu? Kin san ke nake gani ina jin dadi, kece mai daukana tamkar mahaifi, zo zo na ji me akai maki? Wa ya taba min ke ?

Karasawa ta yi tana sakar masa murmushi ta kamo hannunsa ta damka masa goron da ta siyo masa tun wancen ranar, murya a nitse ta ce" mun fuskanci matsaloli ne a gida Sofo, aman yanzu alhamdulilah mun gode Allah, Su Anna sun tafi birni Sofo, muma watarana zamu je? Zaka tafi da ni nima na ga birni?

Ajiyar zuciya ya yi jin ba abinda ya sameta na tashin hankali, ya lalubo karfen gurza goronsa ya mika mata ta mike ta darwaye ta dawo ta raba goron hudu ta maida hankali ta gurje masa shi tas ta mika masa ai kuwa ya hambuda yana tsotsa yana dan juya kai irin ya ji dadin goron

Can ya ce" Birni garuruwa,
A birnima akoy garin da dadi ne da shi sannan akoy wanda sam ba zaka so rayuwa ciki ba indai

kai din bako ne
Birni tana tatare da abubuwan firgitarwa, murane sun yiwa abin hawa irin mashin mota yarda, sun yarda da su suna halaka su

Tagumi ta yi ta ce" suna halaka su kamar yaya?

Ido ya dan zaro ya ce" zaki ga dan birni idan zai yi tafiyar da ba wata nisa ba, ba jeji ba, ba abin tsoro a hanya ba, dan tsabar sangarta da son jiki sai ya dare abin hawa abinsa ya tafi a dan kankanin lokaci in abin ya zo da karar kwana sai ya juyeka tamkar tuwon masara nan zigib ka mace shikennan sai kiyama

Murmushi ta yi ta ce" toh ba kace ajali na tarda mutun du inda yake ba? Mutuwa ai kai ka fada min ba.a gudunta kuma ba.a boye mata, kuna Anna ta ce ita mutuwa lokaci ne idan lokacinka ya yi ba tsumi ba dabara zata daukeka ne ko waye kai ko me kake , kai ka ce min mutuwa mai yanke kauna, takan raba da da uwa, miji da mata, kuma kace min kowani bawa da ajalinsa a duniya

Tsofo yama ta murmushi yana dan barin jikin nan na tsofafi ya dungure kanta ya ce" haka ne Agaishat, Mutuwa gaskiya ce, Allah ya sa mu cika da imani
Ta amsa da amin...., ta ci gaba da fadin " ka ce a birni suna da wata kalar madara banda irin wannan tamu ta rakumi ko shanu? Ina so idan ka je birni ka kawo mini in kaiwa Anna ta sha ta ji itama

Kansa ya girgiza kawai, domin ya lura yau du labari ne a kunshe a bakin Agaishat, wai shi zuwa birni, shi da a yanzu salarma baya iya zuwa masalaci kafafuwa sun kiya, ga tsufa me zai je nema birni? Sai dai idan har kadarar makwoncinsa a can wannan kuwa ya san ko ta wani hali Allah zai kai shi..............

Dago kanta ta yi ta ce " ka san me?

Ya gorgiza kai alamar aa

Ta ce" wankana sau biyu, su Mariama sun bani kaya suka saka na yi wanka

Murmushi yake na jin dadi, bai taba yarda a duniya Allah na hada jinnin mutun da mutun haka kawai sai a kan yar yarinyar nan,
Jinta yake tamkar jinninsa, sonta yake har bargonsa, baya son damuwarta, fatansa Allah ya bata miji na gari komai talaucinsa domin ba zata kasa ratuwa da talaka ba, a hakan rayuwarta ta ginu, gidansu ba laifi su ba talakawanan tukuf bane domin dadaya ne gidajensu ke zagaye a garin aman ita rayuwarta irin ta yayan talakawan nan tukuf ce masu wadatar zuciya,

Tana ta zubar ta mike ta shiga dan totona dakin kamar yanda ta saba dan dudubawa da kyau ta kashe kunama, domin kunamu na cikin kasa bakaken nan wa.inda idan sukai cizo in ba.a yi gagawar shan magani ba dafin na saurin kashe mutun , sune a cikin kasar garin kamar me, yan garin sun iya rayuwa da su, domin sun san inda zasu same su sun iya kashe su tamkar yanda ake kashe cirnaku,
Ta samu ta kashe wajen hudu ta cilar waje ta dauku tulu ta ce" sai na dawo

Hannu ya daga mata yana murmushi ya ce" Allah ya tsare ki

Yana kallonta har ta fice , ya samu kansa da zirarar hawaye, ya ce" ya Allah baka barin wani dan wani ya ji dadi, Allah ka sa , ka yarda, ka aminta , ka bani ikon gannin ta shiga hannu mai kyau kafin na koma gareka .......

*Niamey*

Kan Anna kasa take tafiya domin bata son gannin irin yanda mutanen ke cuwa cuwa, a can kauye shiru ne, ba hayaniya , ba komai, sannan mutanen basu fi a kirga ba, hakan ya sa du idan ta fito daga dakin da Fatimata take koda dan ta leka ta ga safiya ce rana ne ko dare ne? Sai ta rikice

Ji ta yi ta ci karo da mutun, da sauri ta dago dan bayar da hakuri sai dai me, gani ta yi ya zaro idannuwansa yana kallonta, a hankali ya nunota da yatsarsa sai dai wani abin ya ce masa Haba docter, haba docter, wacen koda jikin manyanta ya kamata ba zata koma haka ba, kuma ita batuba ce ba buzuwa ba, wannan kuwa buzuwa ce ta sha bakaken kayanta, kai bama zai yiwu ace ita bace,

Da sauri ya ce" yi hakuri baiwar Allah

Bata san ta ina ta iya hausa ba, bata san ya aka yi ta ce" Ba komai yi hakuri kaima

Gaba ya yi yana dan waiwayenta, shi dai rabinsa da wancen dama familynta tunda aka hana masa aurenta, tun suna saurayi da budurwa, muryar wancen da wannan ba daya ba, sannan kai ka daina tunani kan matar nan mai yiwuwa matar aure ce
Da sauri ya kawar da maganar a ransa ya nufi office dinsa yana dafe kansa a fili ya furta" ya dace na ajiye aikin nan, na jima ina fama har jikin tsufa ya zo....

Tunda ta koma dakin ta yi shiru tana tunani,

Gaishat ce ta salame sallah ta juyo tana kallon maman nata ta ce" Anna me ke damunki ne??

Anna ta dan yi jim ta dago ta ce" wani yare na yi yanzu Gaishat, wanni mutun na kade ya min yare na bashi amsa tartar tamkar na iya yaren

Da mamaki Gaishat ta taso ta zauna kusa da ita ta ce" me kuka ce?????????

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

1️⃣2️⃣

Cikin yaren buzanci Anna ta maimaita mata abinda suka ce

Da mamaki take kara kallon Anna ta ce" kuma baki san sunnan yaren ba?

Anna ta girgiza kai, da yannayin damuwa a fuskarta ta ce" ban sani ba, kuma da dukan alama ba yaren faransanci bane domin likita ya yi ta yinsa a gabana ba wani fahimta nake ba, sannan ba yaren nan da muke ji wajen masu siyar da abinci a garinnan bane wato Zabarmanci, wannan yaren shima daban yake

Gaishat ta mike tana kallon ledar fitsarin fatimata ta ga bata cika ba ta ce" Anna, ko mu koma wajen mutumen ku kara yin yaren? Anna ko haka na da nasaba da asalinki?
```

Nan da nan Anna ta ji ranta ya baci, asalinta? Kennan dai yayanta ba zasu daina daga mata hankali da wannan kalmar ba, rai a bace ta ce" ina ruwanki da asalina Gaishat? Ina ruwanki? Tana gama fada ta fice a dakin don ji take zuciyarta sai tukuki take mata na bacin rai

Da kallo Gaishat ta rakata, haka ne, komai irin dadin da kake ciki da Annarsu in dai ka yi gigin neman sannin wacece ita? Zata fatatakeka ne ko waye kai komai kusancinka da ita,
Ajiyar zuciya ta sauke ta karasa kusa da Fatimata da yanzu masha Allah sosai take samun sauki dinkinta ana kula da ita sosai, likitan karshe ne , du niger ta wannan fannin da shi muke takama!

A yannayin nishadi ta fito a gidansu, Abanta ya santalo Amarya yar bariki, irin a nuna masa ana son yayansa har Bak'A bata kyamata tana bata abinci bayan ya cashewa maryama kudaden da ta yi rantsuwar ba za.a shiga da matar ba sai ya bada su ......Algabitt dai na rakashewa fa amarya , yayansa na gefe suna rayuwarsu , inda bak'a ta dan samu inci na kwana biyu a gidansu domin bashi da lokacin wulakantata yana malake da amarya yan uwanta kuwa sosai suka dan sasauta mata tsanar da sukai mata

Yar waka take da yaren buzanci tana saka sunnanta a ciki, fadi take" ni bak'a yau wa zai so ni?
Bak'a nake wa zai rabe ni?
Yar bak'a haka ne sunana!
Dala biyar babu mai kaunata,
Ta yi dariya ta ce" ni ko a baiwa an rasa mai siyana a kauye da birni,
Agaishat kij cika muni....ta fadawa kanta sai kuma ta yi murmushi tana girgiza kai kawai

Algabittt, yar firit din yarinyar da ya auro ta furta kai tsaye

Shi kuwa da yake saman gadon karagarsa ya yi dadaya ya kallota ya amsata da um?

Tasowa ta yi tana juyi uwa bishiya ta karaso tana nuna masa gidan manta na shafawa ta ce" ka san yanzu muma a kauye mun yi ido, yarinyar nan jikanyar mai siyar da fura nake kawance da ita, ita na baiwa kudina ta siyo min wannan man,
Na ga fatar Agaishat ta dameka, baka son yarinyar dan bakinta, ni kuwa na hango kyakyawar yarinya ce ta karshe kawai bakin ne ya yi mata yawa, dan haka ga shawara wace in dai ka yarda ka takurata ta yi a hankali zata dawo farar mace itama mu siyar mu samu kudinmu mu yi tafiyarmu birni mu je mu rakashe mu hau mota mu saka gilashi mu dangwali kaji

Wata zabura ya yi daga konce yana kallonta, irin maganar ta fara shigarsa, ya fara aminta da shawarar amaryar tasa

Kara jujuya masa ido ta yi ta mika masa ta ce" ka ga bude ka gani, ai dai ka san wannan uban farin da na kara ba nawa bane wanda har kake son samun irina ............. ka yi mini ciki na haifa maka mai kyau ko? To sai fa wannan, ka bada na je na kai mata a siyo mata ta shashafa ka ga yanda bak'arka zata dawo yar dagwasssssss

Murmushi ya sakar mata ya jawota jikinsa ya ce" na yarda, in dai ta dawo fara sai in baki ki kai a siyo dan ubanta sai ta shafa ko bata so

Dan ture shi ta yi tana jin haushi a ranta, dan jaraba sai ya kama ya jajagulata shi ba wani nisa yake yi da lamarin ba du ya hargitsa mata tunani ya barta, haba ta yi aure ta bar jarumin maza saurayinta, aman yau sai ta gayato sho gidan nan

Dan dukan kirjinsa ta yi ta ce" ina so wani dan uwana ya zo mu wuni tare yau Algabiiiiitttttt
Ta fada tana jan sunnan

Da ido ya tsareta, wai itama nan ta iya bariki, murmushi ya yi, shi dai burinsa ta dauki ciki fa? Ina ruwansa inma 2a zqi dane mata ruwan ciki, shi dai in ta yi cikin ta haifar masa kace komin jaraba ya rike abinsa ko a shekara goma ne ya saida ya kara kama daloli, shi kam haihuwar yaya mata ta yi masa rana ( wani abu zai baku mamaki a lamarin nan, irin yanda Algabitt baya kishin matarsa? To bara ku ji readers , ban ce duka buzaye ba, ba zan ce duka ba domin mahaifina buzu ne dan tsananin kulle da yake yiwa matansa ko gidan mutuwa da ta shafi gidansu zasu je shi ke kai su da kansa ba direba ba kuma ya tsaya su fito rufrufruf uwa matan ninja baka gannin komai na jikinsa ko.ina a rufe ruf ba damar ganninsu komai kusancinka da su, sai dai kuma akoy buzayen da basu san darajar matansu ba, sam basa kishin matansu, sai su ga matarsu kwonce saman bed da kato su fice abinsu ko a kwalar rigarsu, baya hana suma in an jima su taketa abinsu doki ce dan haka suke zaune da ita ba wani abin ba! Gaskiya ce a fadeta🤷🏻‍♀️)

Murmushi Algabit ya yi mata ya matsota sosai cikin yannayin rada ya ce" ke , kar ki damu da fada mini fan yan uwanki maza zasu zo, in dai zaki zauna da ni ki haifa mini mata masu kyau? To na baki dama!

Ai kuwa da murna ta rungumeshi ta shiga bashi kulawa daidai daukar hankalin tsufansa 🤦‍♀️
Wannan kennan
...............................................

A hankali ya jona wayar abinda zai dafa masa ruwan zafin dan ya kada madara ya sha

Komawa ya yi jikin bed ya zauna ya shiga karanta messages din Walyn, daya bayan daya,
Na farkon farkon du yannayin ranta a bace ne, harda baya jin kunyar a ce matarsa guda ta kwana a cell? Toh garin niamey ya dauka, ita yanzu kunyar zuwa auren da zata hadu da mata

take, a jejefeta da habaici ya nuna ita ba kowa bace a fadin duniya

Sai daga baya kuma ta fara nuna wai ina ya je ne? Ya haka zai yi tafiya bai yi mata salama ba? Ina ya tafi?

Sai daga karshe ta sauko sosai ta yi ta turo masa alamun kuka da nuna ta yi missing dinsa yana ina ne? Tana son ganninsa ta yi missing dinsa

Murmushi ya yi a fili ya ce" Hajia Walyn matar Wardugu, Walyn mai zamani,

Girgiza kai ya yi, kai shi kansa ya sani da ace wani saunan namiji ne da tuni Walyn sai yanda ta yi da shi, kuma ba boka ba malan!

Wayarsa ya kunna wace take kiransa, ya cireta a liste noire (Black list) ya kwonta yana sauraron ruwan zafin na karar ya dafu aman ya yi masa banza, tunani yake, wai shi shugaban revel zai yiwa haka? Ya fada masa gashinnan zuwa aman ya ki zuwa? Har ya je ya yi ta zaman jiransa wai sai daga baya ya yi masa message  cewa ba zai samu zuwa ba,? Ya sani sarai waye shi aman ai shima ya san waye shi! In ba dan tsufansa ba da sai ta tafka masa ashar din da zai gigita!

Wayarsa ce ta shiga kara , irin kukan bindiga ratatatttatatatatatattatatatatatatattatatatatatatatatatatatatat

Muka hannunsa ya yi ya dauko yana karanta sunnan mai kiran

Sai da ta tsinke aka sake kira kafin ya daga bai yi magana ba

Oga, bako ne muka yi, ahi kadai yake tafe cikin duhun nan, ya zo ta hanyar boye , ragar wajen nan ta shaida zuwansa domin ta kama masa hannun shine ya fito yana fada

Kai waye ya zo? Wardugu ya katse shi da kakausar murya

Murya na rawa ya ce" Shugaban Revel!

Wardugu ya lumshe idannuwansa, a nitse ya ce" ku shigo da shi fallon farko, ku juya

Da toh suka amsa suna masu mamakin mai gidansu, yana nufin daga shi sai shi zai ganna da wannan hatsabibin mutumen?  Lale Wardugu bashi da tsoro, baya dar, baya tsoron uban kowa!

Kwonciyarsa ya yi bayan ya ji wa ke jiransa,

Can cikin tunaninsa wayar ta kuma daukan kuka,

Da haushi haushi ya mike ya daga da kakausar muryar nasa ya ce" Hello!

Wardu.........ta fada cikin sanyin murya

Tsai ya yi bai amsata ba

Kuka ta fashe da shi ta ce" tu me manque (i miss you)

Ajiyar zuciya ya sauke a takaice ya ce" ki bi Nuger airlines gobe ina Agadez hotel din sojoji ki sauka nan ko bana nan ki je dakina

Yana gama fada ya kashe kiran yana shafa gefen fuskarsa da sajensa

DOGON wando ya dora saman gajeran ya saka riga fara kar ta ririke damatsunansa ya fito ya nufi fallon da aka sauke bakon dare (🤣)

Yana zuwa ya shigo kai tsaye,

Mutumen dake zaune ya sha rawani ya hakimce cikin shiga ta kamala mai daukaka darajar dan adam ya dago ya tsaida kallonsa kan Wardugu, a tarihin rayuwarsa dole ya sako wannan yaro, domin shi ne mutun na uku da ya ajiye shi jira
Murya a kausashe ya ce" Wardugu ba.a tsayar da ni jira

Shima Wardugu kai tsaye ya ce" *Rhissa agbula* ba.a ajiyeni jira!

Murmushi Rhissa ya yi, ya mike tsaye suka gaisa irin gaisuwar musulunci suka baiwa juna hannu suna yiwa juna salama

Wardugu ya ce" ya zaka zo wajena ni daya bayan ka san ya dace a tatauna da kai a bainar nasi kowa na da magana da kai harda mai zuwa da maganar shugaban kasarka

Rhissa ya ce" shugaban kasarka dai, ka san ni ba nawa ba! Sannan ni kaima da na aminta ganninka dan na fafata da kai na yarda tsaurin kanka zai je da nawa, bana musanyar yawu da matsoraci, ba.a daukana a tv haka kyauta sai kace wani sakarai!

Wardugu ya girgiza kai ya ce" ya ake ciki? Wa ke son tayarwa kasata hankali? Ina suke? Menene abubuwan yakinsu? Ana jitajitar kune kuka dawo bayan kun daina aiki a niger kace niger ta yi maka kadan sata yanzu? Me yasa ake samun gawarwakin bayin Allah a gidajensu? Masu aikata min haka baki ne! Da sun san idan na damke su zasuna kururuwar na kashe su da abinda nake masu da basu shiga gonata ba!

Wardugu ya karasa yana dukan table din glass din dake falon ya yi wani jijiga aman bai fashe ba domin irin wannan mai masifar karkon ne, sai bindiga mai tsini ke tarwatsa shi

Rhissa ya mike tsaye ya ce" ba ni bane, kuma ba yarana bane, abinda ya sa na tsayar da hankalina kennan har na baro aikina na garzayo dan ganawa da kai! Kar ka shiga yaki da ni ba ni bane! Na yi bincike tsageru ne, kan harkar siyasa ne, kuma na ga makwoncinsu, suna cancanza waje ne ina son sannin tsarin canza wajen nasu, Wardugu nima sai na yi maka maganninsu

Wardugu ya girgiza kai ya ce.....

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

1️⃣3️⃣

Wardugu ya girgiza kai ya ce" ka taba gannin na nemi agaji? Kokowa ai ya dace mutun yayi abinsa! Ka bani hanya kawai ka barni da sauran ai na san tsarin tsagerancin yan tsagera, idan ka yi yaki a kambacina kana so gobe su afko su aikata abinda ya fi haka? Domin sun san ba zan iya tarbansu ba? Aa ba dai Wardugu ba
```

Haka tataunawar Wardugu da Rhissa ta kare, kowa na ji da kansa da kuma ikirarin kansa, Rhissa ya san abu guda Wardugu ba wai cika  baki yake ba, yana fadin abinda zai iya aikatawa ne, ya san da in dai suka yarda ya ci masu kamar yanda ya fada ne sai sun gwamace mutuwarsu da rayuwarsu a hannunsa, Wardugu ya ga damar ya fitar da su jeji su fuskanci juna wanda hakan kuwa ba zai gyara su ba!

Wannan kennan

Bayan kwana biyu .......AMERICA

Docteur Mu.azam ne ke zaune yana dadana computer,
Can ya dago kansa ya duba time,
A hankali ya ajiye ya mike ya nufi bayi ya sakarwa kansa ruwa
Yana fitowa ya dauki kayansa ya saka ya saka vest dinsa ya dauki agogonsa ya daura ya fito fallonsa dan madaidaici ba wani tarkace sai kujeru da dan table da tv tankamemiya, sai hoton wasu fararan mutane mata da miji ga dukan alamu suna murmushi a hoto
Kamar yanda ya saba zuwa ya yi ganan hoton ya tsaya ya ce" Abi, amy asalamu alaikum, yauma na tashi lafia, sai dai har yanzu ya kasa hakuri ya daina fushi da ni, gashi aiki ya taso min a kasarsa banda shi da mahaifiyarsa da mahaifinsa da suka dauke ni tamkar dan cikinsu bani da kowa,
Zan kuma gwada kiransa ku taya ni da adu.a daga inda kuke, ina mai kara yi maku adu.ar Allah ya sa kuna cikin Aljannah

Shi kadai ya tsaya ya yi zubarsa kafin yake zuwa wajen wayarsa ya zauna yana dan murmushi ya shiga doka kira

Yana kallon wayar na haske ya ki dagawa, Walyn ce ta fito daga wanka ta zo ta mike abinta saman lafiyayan bed din hotel din itama tana duba saman screnn din dan gannin wa ke kiransa yake sharewa haka?

Murmushi ta yi ta juya abinta ta shiga neman baci a kasan zuciyarta tana ayanna toh fa da shima yana gaba bare ni?

Can dai ya daga ya saka a  handsfree

Soja kake

Ya fada yana danne dariyar farin cikin ya daga kiransa

Murya ciki ciki ya ce" Docter kake, kuma dan rainin hankali kake

Murmushi ya yi ya ce" baka hakuri ne? Baka mantuwa ne???

Wardugu ya kawar da kansa ya ce" haka, ka san ba nine na watsa taron aurena ranar aurena dan wani gudiri nawa na shirme daga shiga ka ga amarya kafin a daura aure zaka fito ka watsa taro? Kai mahaukaci ne! Mu.azam baka da nutsuwa

Mu.azam ya bushe da dariya ya ce" Wardugu, abinda ya sa na tsalako fararan fatar, na yi doguwar tafiya niger ba dan ina son na samu *BAK'A* bane?, ni bak'ar mace nake so, ita ce ra.ayina, ita nake son zaman aure da ita! Kar ka manta ni likitan mata ne, idan ka ga na kuke abu kaima ka gwada abokina

Tsaki wardugu ya ja ya ce" kiran na menene?

Mu.azam ya kuma yin dariya ya ce" kai ka dena jin haushina mana, ai ni ban shaki mahaifin matana ba

Da sauri wardugu ya kai dubansa wajen Walyn wace ke kwonce, ta ji sarai dan haka ta yi saurin mikewa tana kallonsa,
Fuska ya hade idannuwansa cikin nata ya ce" eh haka ne na shake shi, domin a lokacin ban san mahaifinta bane, kuma na tarar da shi ya zabgawa mamanta mari , idona ya rufe ban tsaya wata wata ba na shake shi, kai dan ubanka sai yanzu ka tina?????

Ajiyar zuciya ta sauke, tana tine da ranar .....dalilin wannan action din da yayi na ta haukace kansa, wardugu jarabar duniya....komawa ta yi ta kwonta ta ja bargo tana rufe jikinta

Wardugu ya fice a dakin , yana fita ya ce" Mu.azam??

Mu.azam ya amsa da na.am?

Wardugu ya ce" kana son kashe min aure ne? Tana jinka fa

Mu.azam bai ji dadi ba aman ya ya iya har ta ji, dan tsam ya yi kafin cikin yannayin mamaki ya ce" Wardugu yamzu tsareka ake idan zaka amsa waya ko me? Lale dole na auri batuba

Kai banza ka nutsu ka ji!!

Mu.azam ya yi murmushi ya ce" dadina da soja zagi, ni dai ka fadawa Ayyata in sha Allah ina nan ina faman gama abinda nake zan shigo Niger, ka san bani da masauki sai kusa da ita dan ita ta iya kula da cikina, zan zo ba zan dawo ba sai na samu macen aure na kuma gama abindq zai kawo ni

Wardugu ya ji dadin haka dan haka ya amsa shi da murnar hakan

Satin su wardugu hudu a garin Agadez yana faman aikinsa wanda tun Anna na fada har ta kawo ido ta zuba masa, gashi ta yi ta yi aminiyarta ta barta ta koma wani wajen ta kiya ta ki fir sai ma fada da ta dauka cewar masarautar ai girma ne da ita, ba ita ba ko baki ta kawo suna da wajen zama har lokacin da suke so a masarautar Agadez

A yau suke saka ran komawa bayan ya fada masu su kiyaye, ya basu magungunna, ya kafa masu sharuda kan lafiar Fatimata,
Jirgin da ya kawo su an basu takarda dan haka suka kai aka saka su a layin wa.inda zai mayar garin agadez bisa jagorancin docter Fannata

Sun sauka lafia inda Fatimata ke dan takawa a hankali daga nan suka nemi abin hawa dan karasawa Timiya............

Timiya.....me aka kwaba? Me aka yi me ba.a yi ba? Me ake cikin yi? Timiya gari mai abin mamaki, Timiya garin bak'a,

Duka na kawo wuka a yanka Algabitt ya yi mata bisa taki shafa man da ya fitar da kudi ya saya, Rai bace ya ce" sai na tsine maki in dai baki shafa man nan ba

Cikin kuka ta ce" Aba, ka yi hakuri ka ji? Bana son canza kalar fatana ka yi hakuri Abanna

Ni ban haifeki ba, ke ba abin alfaharinki bane yau har na yi hakuri na dube ki na nemi intaki aman ki butulce min? Uban wa ke hure maki kune ne ni?

Aba ba kyau, ba kyau, mu ji tsoron Allah

Hannu ya saka ya dake bakinta ya ce" ki rufe mini bakinkin nan mai bakin jaraba! Ke sai kin shafa

Kokarin shaketa yake dan ya shafa mata Mariama ta fito da gudu tana ihu tana nuna dakinsu

Dakatawa ya yi yana binta da kallon meye ke kuwa

Hankali tashe ta ce" Ashta ce, ashta ce, tun da ta ce maka in dai ka yi mata auren nan sai dai a kai gawarta kai kuwa kace sai me ba dai ka daura mata auren ba? Ita ce gata can sai wani abu take daga baya ta fasa motsi

Fancakalar da Bak'a ya yi, shi da amaryarsa suka nufi dakin da gudu

Daidai wannan lokacin Su Anna da sukai doguwar tafiya suka shigo gidan da salama bayan su Dogarai ne da suka tarbo gimbiyarsu wace sarki yake hakimce yana ji tamkar ya zo ya tarbi abinsa

Jin kururuwa ya saka gaban Anna ya yanke ya yi wani irin faduwa, cak ta tsaya tana sauraron magangannun dake tashi, ihun kuka yayanta biyu suke inda Bak'a ke jingine jikin garu ta daga hannunta ta dora saman kanta ta yi tamkar status tana kallon kofar dqkin nasu ,
Muryar amaryar Algabiitt ce ta tashi ta ce" ta kashe kanta, ta kashe kanta

Wani irin luuuuu Anna ta yi wanda ba wanda ya ganta sai faduwarta da aka ji , nan mutanen gidan suka ankara da dawowarsu wanda nan da nan gidan kai dama anguwar ta cika da dukan jama.a ana ta daga maganar, tabas Ashata ta rasu, ta rasu ne da bakin ciki, tana da ciwon zuciya ne wanda ya yi mata tashin kai tsaye, wanda amaryar Algabitt ta yi kazafin ta kashe kanta,

Tashin hankali!

Mota ce katuwa irin ta sojoji, direba mai iya janta kawai ya dauka kai tsaye suka karasa gidan Sarki

Ayya na zaune tana gyara akaifunta labari ya zo mata cewar ta fito su tafi

Mikewa ta yi fa hanzari tana murnar yau kam Allah ya sa ,

Tafia suke cikin mota, Walyn na zaune tunda ta cewa Ayya ina kwana bata kara magana ba sai shanshan kamshi take domin da yar tsamarsu da Ayya, gani take Ayya ke zige mata miji yana wulakantata

Tafia ce suka yi mai tsayi, cikin jeji ne sosai kafin suke shigewa sahara gaba da baya

Wani kara motar take a cikin kasar nan tana cin tafiyar wace kana ganni ka san karfi ne ke aiki

Duda a cikin mota suke aman sun yi budu budu da su domin kura sosai ke tashi sanadiyar gudun da suke a motar da kuma kasa

A hankali ya ratsa yar gadar da ta kai mutun cikin kauyen, wato *TIMIYA*.............

YA RAYUWAR ANNA?
ALGABITTTT FA?
BAK'A?????

SU WARDUGU DA AYYA DA WALYN ME YA KAWO SU TIMIYA??????? MU JE ZUWA ........................................................na yi imanin da ba dan Allah na sakawa bawa hakuri da dangana a zuciyarsa a lokacin da ya rasa wani mutun mafi kusanci da shi da Anna ta samu tabuwar hankali ga wannan lamari na mijinta, kar ku manta na fada ba labarin mutun na dauko ba aa labarin abinda ke faruwa ne, (YA FARU!)......

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

1️⃣4️⃣

Bayan sun shiga garin timiya mutane suka ringa gudu suna kururuwa, wasu na fadawa gidajensu wasun kuwa na nufa gidan sarki wasu kuwa na kokarin neman hanyar da zata fitar da su daga garin ta barauniyar hanyoyi domin dai garin ba wani rufe yake ba

Da mamaki suke kallon reaction din mutanen, Warsugu da sojan dake jansu ne kawai basu yi
```

mamaki sosai ba duba da yannayin garin motar lafia dai bata shiga sai ta sojoji ko kuwa motar mugayen mutane masu zuwa su kai hargitsi su kashe mutane

Kallonsa ya maida wajen Ayya wace ta dafe habarta ta wara idannuwanta tana mamakin nan yake mutumen kuwa? Aman gudun me suke?

Labari ya kaiwa sarki a yar fadarsa,
Tabas gabansa ya fadi da jin wannan lamari, ba a taba ba, mota har nan bata fara shiga ba, Mikewa ya yi da dukan kokarinsa ya tatara karfinsa inda dogarawa suka shiga kabara sunai masa kallon jarumi mai tausayin talakawansa da kuma kallon marigayi

Du a bayansa suke inda yake daga kafafuwansa da kyar yana kara tunkarar motar, gannin motar ta sojoji ce hankalinda ya kara tashi, domin dai shi ya san motar tunda yana shiga gari kai gaisuwa fada, kai harma ya tafi kasa mai tsarki, me ya kawo motar sojawa Timiya? Shine tambayar da yake yiwa kansa,
To ko dai sojojin ne a cikin motar ko kuwa mugayen mutane domin idan sun kai hari ai suna karbe motocin sojawan

Wardugu ne ya bude gefen da yake zaune ya karbe hannunsa daga rikon da walyn ta yi masa ya diro daga cikin motar tsaye kan kafafuwansa
Jibgi, dankari, in ba wardugu ba zaka shiga kauye sai ka je da wando tree Carter?  Sai rigar sojawa irin body din nan damatsunnan hannayensa a fili, yar karamar bindiga marar karan sautin harbi ce a kugunsa inda ya rufeta da wannan rigar ta jikinsa ya saka belt kalar kayan sojojin ya daure tam abinsa
Kansa sanye da hula baka kalar wandon sai takalminsa sandal wanda ya daura abinsa
Sun karbe shi, sun amshi jikinsa, sun kawata shi
Taku ya shiga yi da karfin jiki ya nufi Sarki da ya ja ya tsaya jikinsa na bari, ta faru ta kare, jita jitar Ashta kanwar matarsa ta kashe kanta wani ya kai birni an zo kama sirikinsa, mutuwar yau har kwana takwassss tabas wani ya kai, shikennan Alghabiittttt ya bani domin a hoto kuma a tv a birni Yana gannin wannan mutumen, an ce shugaban sojoji ne, shi da kansa ya zo kama algabiit? Algabitt ya ji haushin rayuwarsa, tunanin da Sarki ke yi kennan inda ya daskare da tare da bugun zuciyar ko wani taku na Wardugu dan nufo shi (🤦‍♀️ in ba kauyanci irin na sarki ba, a rasa mai zuwa kama Algabiit karamin kwaro sai Wardugu? Za dai ka san waye shugaban sojojin nan hangensa kake!)

Yannayin shigarsa ta tabatarwa da Wardugu shi ne magabacin garin, dama irin haka idan an zo sarkin gari ko mai garin gari ko kuwa tsageran gari wanda ya gagari uban kowa ke zuwa ya tarbi mutanen, in da karar kwana a kansu ake farawa

Salama ya yiwa sarkin yana mika masa hannu sannan tar yana kallonsa ido cikin ido

Jiki na bari Sarki ya karbi gaisuwarsa yana tambayarsa hanya da zarcewa da magana kamar haka" mai gida, na san ba auren iri ka zo nema a wannan jeji namu ba? Koma wa ka zo

kamawa ka yi hakuri, a yi mana sasauci kar a kashe mu, a kama iya mutumen a tafi, ni kaina inada kankannan yara da mata, idan aka tsame masu ni wa zai ji da su?

Da mamaki Wardugu ke kallonsa , aman da yake Wardugu dan duniya ne sai ya ce" Kai, baka san Allah baya barin wani dan wani ya ji dadi ba?

Ai kuwa gaba daya sarki ya haukace, jiki na bari ya saki kuka ya duka kasa ya rike kafafuwan wardugu ya shiga magiya

Ayya dake cikin mota ta dake lebenta na kasa ta kali sojan nan ta ce" ka karasa da mu, na san wardugu wani lamarin ya shiga na tsawatar masa tun kafin abin ya birge shi

Walyn ce ta juyo da sauri ta kalli Ayya, a ranta ta ayanna wai ta tsawatar masa, sai son ta nuna ita kadai ta isa ta juya shi, ta ja tsaki a ranta a fili kuwa ta ce" Hum tana tabe bakinta sosai

Sojan ne ya juyo ya ce" Hajia, ki yi hakuri, nan ya ce na ja na tsaya idan na matsa bai bani umarni ba ni da shi ne

Da haushi haushi ta shiga bude motar wanda sojan bai ankara ba har sai da ya ji ta bude ya juyo da  sauri , har ta sauke kafarta guda ta ga Wardugun ya dawo da saurinsa gefen da take

Yana zuwa ya ja ya tsara mata ya ce" Ayya maman Wardugu, kece ikon mai sanya Wardugu cire wando ta kai, Ayyana kar ki yi fushi kin ji? Koma motar mu karasa sai ki yi masa tambayar ai sarkinsu ne

Da mamaki ta saki baki tana kallonsa, sarkinsu? Aman me ya saka shi kuka da dukawa ya kama kafar wardugu?

Dan murmushi ya yi bayan ya saka mata lafayarta ciki ya rufe ya bada umarnin su karasa inda sarki yake

Suna karasawa Ayya ta bude tana shirin fitowa sarkin na karasowa ya dan risina yana gaisheta,

Ayya ta kalli wardugu ya dan sakar mata murmushi

Kai ta girgiza ta sauka sosai ta gaishe da sarkin kafin take fada masa abinda ya kawo su

Wata ajiyar zuciya ya sauke a bayane, ya ce" A garinnan Sofo mai bada magani kwaya daya mukeda, ya sufa sosai, gidansa da dan nisa da kasuwarnan sai mun shiga gari sosai

Ayya ta amsawa sarki da ba damuwa su je

A cikin motar nan sarki ya shiga inda yake dan hangen Wardugu ta madubi lokaci zuwa lokaci, ya yarda da ake cewa sarkin sojojin fa masifafe ne , bashi da dar, in ba rashin tsoro ba du irin yanda ake tsoron abzinawa da asiri shi a gabansa sai dai ma shi sarkin ya ji gabansa ya fadi maimakun na wardugun ya fadi, lale yaron ya sha ya jiku ya tada kai , rabonsa da kuka tunda aka zo masa da sakon Gaishat ta tafi baban birnin niger inda ya yi tunanin shikenan ta gudu me ta bar shi.....(wani lamarin dan gyara nvl dina ne fa, sarkin abzin ba wasa walahi🤣🤣)

Basu zame ko.ina ba sai anguwar baba Sofo

Suna tsayawa mutane suka cika wajen, tunda sun ga sarkinsu a tare da mutanen ai shikenan sai suka sakin jikinsu da su harma ake matsowa a shafa motar sai a kwala ihu da yaren buzanci a ce" nima na taba, mota mota a garinmu, mota har gidanmu,

Du ja sukai a lokacin da mutanen ciki suka fito gaba dayansu, suna masu binsu da kallo, girma da yannayin tsarin halitar wardugu ta basu mamaki, suna da mutane dogaye sosai sai dai ba masu fafadan kirji da manyan damatsuna haka ba, sai kuma matan dake tare da mutumen da dayen sojan, kun san dai Ayya gwadar ado ce, bale Walyn farar mace alkyabar mata, walyn farar batuba ce tas tas tas, Ayya ce ma baka domin Ayya baka ce mahaifin wardugu ne farin batube shima tas tas tas , sai sojan dake saye da kayan sojoji komai harda bindigarsa da katon takalmin nan nasu da komai sai muzurai yake

Sarki ne ya amsa gaisuwarsu kafin yake kai dubansa bukar Sofo,
Bukar kanta ta tsufa du ta zuzube sai abinda ba za.a rasa ba, ga dati sosai a dan nesa da wajen domin an yi rasuwa baka bata samu zuwa ta share masa ta gyara masa ba,
Ruwa kawai take zuwa ta dauko masa ta koma

Nuna masu wajen ya yi bayan ya samu ya shiga ya tarar yana zaune saman buzunsa da carbinsa yana ja ya kurawa waje guda ido yana ta istighfari(Allah ka bamu nitsatsen tsufa in muna da rai wanda zai kara kusanta mu da kai ya Allah)

Gaishe shi ya yi ya juya inda sofo ke bin kofar da kallon mamaki, me ya kawo Sarki har wajena? Kuma hayaniyar me nake ji haka?

Ku shigo;

Sarki ya fada yana dubansu

wardugu ya ce" anya kuwa? Me zai hana ya fito???

Ayya ta kallo shi ta ce" Wardug.....
Da sauri ya yi gaba ya fara nufar yar bukar sofon a ransa yana ayyana ai idan Ayya ta nadaka toh fa tana yi da kai

Shishiga sukai banda sojan nan,
Walyn na saka kanta ta yi baya tana kakarin amai da coshe hanci, a fili ta furta" kai ina , ba zan iya ba!

Ayya ta karasa a hankali kusan tsofon dake zaune ya zuba masu ido gaba dayansu yana mai binsu da kallo, ko gezau bai yi ba daga zaman da yake sannan yana jan carbinsa cikin nutsuwa
A hankali ya amsa salamar Ayya da ta nufo shi cikin nutsuwa ta tsugunna dan nesa da shi aman suna facing din juna

A hankali ta ce" lokaci mai tafiyar da abubuwa, lokaci mai bayanna abubuwa, lokaci mai rarabe abubuwa,
Baba tsufa ya zo haka? Allah ya sa mu cika da kyau da imani

Murmushi ya yi na gano wacece ita, tabas ya ganeta, idan ba zai manta ba shekaru sun kai talatin da suka shude ya sha kai mata magannin athsma na yaronta da bai fi shekara hudu a lokacin ba tana karbar masa aman ya ki karbar komai da sharadin sai yaro ya samu lafia

Murya na rawa baba tsoho ya ce" y'ata ke ce a garin timiya? Ya jikin yaronki? Na koma ban same ku ba sai na yi adu.ar Allah ya sa ya warke

Ayya da murna ta janyo hannun Wardugu dake tsaye kikam ta ce" baba ai gashi, kana ganni soja ne, cikin ikon Allah magannin nan mun ji dadinsa, nima a raina kake, na nemeka Allah bai yi ba, kwanan nan na yawaita mafarkinka, a sifarka ta da hakan ya daga hankalina na saka aka nemo min inda kake, shi ne na zo na yi godiya sannan na yi salama kamar yanda na dauki alkawari,

Baba na murmushi yana kallon wardugu wanda shima zuwa lokacin ya risina, yana kallon tsohon yana kidaya shekarunsa a ransa, ya yi imanin a kadan ya linkasa uku da rabi,

Baba ya maido kallonsa wajenta, kafin yake bin dakin da yake zaune da kallo, ya yi murmushi bai ce komai ba

Ayya ta ce" Baba ka yi magana mana,

Baba ya dago yana dubanta ya ce" kaya y'ata, ki dubi dakin da nake ciki a zaune a yanzu, me ya rage min? Me zan yi da arziki? Kyakyawan karshe kawai nake nema, shekaruna dari da ashirin da uku a duniya a hasashe mai yiwuwa na fi,

Kallonsa kawai suke suna masu adu.a a ransu, adu.a suke da Allah ya datar da su da irin tsufan nan, wanda zaka yi ram da kai da carbinka,

Jikin ayya ya yi sanyi sosai , a hankali ta zauna a kasar dake dakin tana kallonsa, murya a

sanyaye ta ce" haka ne baba, Allah ya sa mu cika da imani......
Aman na so na yi maka wani abin da zai faranta maka, da zaka aminta ma da mun tafi da kai mun kula da kai

Baba tsofo da kansa ke kasa cikin rawaninsa ya dago yana kare masu kallo, ya yi imanin wannan matar da muguwa ce da bata bi bayan alkawarin da ta yiwa talaka futuk kamarsa domin ta san bai isa ja da ita ba domin zamani ya zama mai abu shi ne sarki, shi ya isa shi ke da magana ya dora doka, aman du ta manta ta tako ta ci gari da gari, ta ratso sahara du dan ta yi masa godiya sannan ta cika alkawarin da ta dauka,? Sannan ya san ba yar yankan kai bace domin ba da kansu suke nema ba kawo masu ake har gida, shi kam ji yayi gaba daya ya samu nutsuwa a zuciyarsa da shawarar sa,
Murya a sanyaye ya ce" tabas ina da bukata mau girma baiwar Allah, sai dai ban san ta inda zan fara ba, banma san ko za.a dace ba,

Hankalinta ta maida kansa ta ce" Mecece ita?????????????........

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

1️⃣5️⃣

Baba cikin yannayin damuwa ya ce" me zai hana na baki auren y'a?
```

A nitse ayya ta ce" Auren Ya baba?

Baba tsoho ya ce" eh, domin shi kawai zan nema a bada yarinyar dindindin ,

Aman baba wace yarinya ce wannan??

Baba ya sauke ajiyar zuciya ya ce" yarinya ce mai tarbiya mai ladabi da biyaya, yarinya ce mai nutsuwa, bata da kwaramniya, inda aka ajiyeta ta zauna kennan sai an ce ta tashi, yarinyar nan ina jinta a raina tamkar yar da na haifa, a kulun damuwana na mutu na barta a wannan hali, tana cikin halin matsi dan kawai Allah ya yita *BAK'A*  sai dai ni murnar hakan nake domin fatarta ya sa har ta kai warhaka sai dai har yanzu bata samu mijin da zai aureta ba a kauye ta girma sosai shekarunta goma sha takwas a duniya ,

Jim Ayya ta yi tana kallonsa, kafin take cewa " me dinka ce Baba?

Baba tsofo ya kalli Sarki dake kallonsa shima cike da rausayawa, da wani ne duda tsufanda in dai yana iya magana yana gane wasu abubuwan da gudu zai karbe makuden kudin da aka baza masa, sai dai shi bawan Allah ta yarinyar fake tare da shi tun tana yar shekara shida a duniya yake, irin tunanin da iyaye zasu kwana su tashi da shi na gannin yayansu sun samu mijin aure mai nagarta wanda zai kula da yayansu, toh haka baba tsofo yake kasancewa, du motsinsa itace a ransa, tambayar kansa yake ina? Ta yaya? Wanene wanda zai rike masa Agaishat mudin ranta cikin mutuntawa da kauna? Ya hanga ya hango bai samu ba, har almajirinsa ya tuntuba aman ya watsa masa kasa a ido, hakan ya saka shi dukufa wajen kai kukansa wajen Allah, yana rokonsa da ya bili masa da hanya ta inda baya zato baya tsamani, ya bilo masa da hanyar da zata zamo alkhairi gareta,,,,

Sarki ya ce" kanwar matana ce, Sunnanta *AGAISHAT*

Kana nufin farar  buzuwa?  Ayya ta tambaya

Sarki ya ce" buzuwar ce tabas, sai dai ita wannan Bak'ar buzuwa ce,

Ayya ta kai dubanta wajen Baba Tsofo da ya yi kododo yana kallonsu, kallonta ta maida wajen Wardugu dake tsaye ya tsareta da ido yana jiran jin me zata ce,? Ya san halin mamansa, ya san Ayya da daukarwa kai, !

Murya a sanyaye ta ce" Wardugggggggg..........

Fuskarsa a hade ya ce" Lalalalala,
Daga haka ya tamke fuska yana kallon su

Ajiyar zuciya ta sauke tana kallon kasa ta afka tunani (Tabas a al.adar Tubawa ba.a yiwa namiji auren dole, bake Wardugu, sannan idan namiji ya yi aure sai matarsa ta yi haihuwa kamar uku zuwa hudu kafin ya yi mata kishiya idan kuwa bata haihun ba sai ta dauki shekaru kafin ya yi mata kishiya, wannan haka ne ba ja, haka al.adar garin yake, ) Ayya ta kuma kallon su, ya zata yi?

A hankali ta ce" baba, wannan yaron shi daya Allah ya bani a duniya,
Sannan bai jima da yin aure ba,
Ban ki ba, ina so idan da hali a bani yarinyar a matsayin yar rikona, yar amanata, in sha Allah zata ci abinda na ci ta kwonta a makwoncin da na kwonta ko wani iri ne, kafata kafarta Har Allah ya bata miji, zan yi dukan abinda ake yiwa ko wace y'a na kaita gidan miji sannan zan bi dukan lamuranta a gidan miji mudin raina

Baba tsoho ya jima yana nazarin maganarta, baya shakun za.a bada AGaishat in dai sarki ya yi magana, damuwar shi ne: Agaishat zata so bin bakin fuska duda irin matsin da take ciki? Gida fa gida ne, sannan mahaifiyarta zata yarda da radin kanta a rabata da yarinyarta budurwa ba da wani dalilin aure ba ko dangi na jini haka kawai a tafi da ita tare da mutanen da bata sani ba? Ko wannan karon ma isar za.a nuna mata a kuma kwace mata *Y'A*?

Duda haka baba ya kai dubansa wajen sarki,

Irin kallon da baba ke yi masa sai da ya saka ya ji kunya, ya ce" abinda za.a yi, zamu kama baba a je da shi da ku baki daya ga mahaifiyar yarinya da mahaifinta, du yanda hali ya kama zuwa ya fi aike

Sun lamunce da hakan inda Wardugu ya kama baba a hankali ya mikar da shi sarki ya kama masa suka fito yana dan dingisa kafarsa har suka karasa wajen motar inda sojan nan ya bude wardugu ya daga baba a hankali ya saka shi gidan gaba sarki ya shiga suka shishige gaba dayansu Walyn da binsa da kallon meye kuma haka? Shima kallon Ayya dai yake,

Basu zame ko.ina ba sai kofar gidan Algabiitt

...................... .................

Anna, ki yi hakuri haka kin ji? Ki daina damuwarnan kin ji Anna?
Agaishat ta fada tana miko mata gurasa ta kasa da aka kawo sadaka gidan mutuwar

Anna ta lumshe idannuwanta bata karba ba ta bude tana kara bin yayan nata da kallo,
Mutuwar nan da aka yi bai saka Algabiitt ya yi sanyi a lamuransa ba, ya sako Agaishat gaba dole sai ta yi shafe shafe itama ya samo mata miji kamar yan uwanta tamkar damuwarsa ta yi

auren ne,
Yarinyar bata isa ta wulga ba sai ya dura mata zagi
Ya hana a yi zaman makoki sai yayanta dake zagaye da ita
Amarya kuwa idan yau wannan ya zo ta ce dan uwanta ne , gobe sai wancen ya zo ta ce kaninta ne, ta mayar da gidan filin kawo kwartayenta ba tare da wani dar ba domin mai gidan ya bata lamuni....

Anna murya a shake ta ce" bana so ya kashe mini wani cikin ku,

Mariama ta juyo fuska du ta yi mata ja abin kuka ta ce" to ki biyo mu mu bar masa gidan mana, dan mi ba zaki bi mu mu yi tafiarmu ba? Kin san abinda ke daure mu a nan ke ce,

Hankalinta tashe ta ce" a duk lokacin da kuka ambata mini abubuwan nan biyu asalina da barin Algabiit bara ku ji na fada maku yau abinda nake ji! Ji nake tamkar lumfashina zai tsaya idan na ji an ce na bar inda Algabiit yake in dai ba da yawunsa ba, ji nake zan fada halaka, ji nake duniyara shi ne, ji nake in ba inda yake ba ba ni! Wani duhu ke rufe mini ido kaina ya dauki nauyi idan na takura sai na tuno wacece ni? Nakan fada damuwa mai tsanani juwa ta ringa dibana du idan aka yi maganar dangina, kun ji damuwata

Suke suke kallonta, Agaishat (Bak'a) kanta na saman cinyar Gaishat, Mariama na zaune gefensu,  Fatimata na jingine da garu tana facing dinsu,
Jiki a sanyaye Fatimata ta ce" me ke damunki haka Anna? Wannan ba soyaya bace,

Mariama ta kallota ta ce" wace soyaya? Ai koda an yita a baya a yanzu Ya kasheta da kansa, Me ke damun Annarmu?

GAISHAT ta buda baki zatai magana sai ga Algabiit bugum ya fado dakin yana dan dudukewa dan tsayi

Direct ya zarce gurin Anna bakinsa na rawa ya ce" sai dai su tafi da ke da tsinaniyar yar ki! Ba wanda zai kama ni, ba abinda na yi!

Da sauri ta mike tana dafe kirjinta, tsinaniyar yarki ke mata yawo a kwakwaluwa, wacece kuma? Me aka yi? Su wa zasu tafi da su?

Bata kai ga tambaya ba ya duko ya dago Bak'a da gashinta ya mikar da ita,
Yawun bakinsa ya tatara mai cike da warin Sansani ya tofa mata a fuska ya ce" ga dan iskan tsohon da kike wuni wajensa tare da sojoji, to ki sani sai dai su kama uwarki

Janyeta Anna ta yi da karfi sannan ta yo fallon nasu da sauri dan jin lafia?

Gaba daya yayan nata suka biyota inda Algabitt ya labe yana leke yana kuma sauraron abinda ake fadi

Da kallo Anna ke bin su, sukai mata salama suka shiga gaisar da ita da yaren buzanci,
Ayya ta kalli wardugu dake karewa kowa na wajen kallo, ta ce" ban san bama da wani yare zamu tatauna da ita da alama buzanci kawai take ji

Anna dake tsaye ta ji komai abinda aka fada da yaren da ba zata ce ga sunansa ba, kuma ba yaren da suka yi da likitan nan a asibiti bane..........................................

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

1️⃣6️⃣

Bata kai ga magana ba dogarai ke sanar da shigowar sarki falon sirikan nasa , daman da baba tsoho ma shi ke fasara tsakaninsu domin ba komai yake ganewa ba shi kuwa sarki ya zauna da tubawa

Tunda ya shigo Anna ta sada kanta dan kunyar siriki, shima du a wani takure yake inda Gaishat ke binsa da kallo tana tambayar kanta me ya kawo shi ko bakinsa ne?
```

Gyaran murya ya yi ya ce" Anna, ina fatan kin san baba tsoho, wanda Agaishat ke zuwa wajensa babanta kennan

Daga inda yake ya daga murya da irin abin haushi haushi ya ce" ya zata manta kwartanta uban yarta? Ai ni dama na san dubunki sai ta cika munafuka, yau dai ga zance zai bude

Da wani irin yannayi Wardugu ya kai dubansa daga inda ake maganar, wa ke magana ta rashin da.a haka? Shine abinda yake tambayar kansa din wardugu na jin yaren buzanci kai bama buzanci kadai ba wardugu irin mutanen nan ne masu kwakwaluwar kwashe yaren da ba nasu ba, yana jin yaruruka da dama, hakan ya bashi damar jin abinda ake fada harma wanda Algabiit ke aikowa daga daka

Sarki ya girgiza kansa kawai, ya san wanene Algabiit farin sani, kuma fa ya san harma gudumuwarsa wajen Algabiit ya tsula tsiya a garin   aman ba komai zai dauki mataki ne tun kafin ya saka a tarwatsa su baki daya

Anna da ta kasa hada ido da shi ta gyada kanta, ya zata kasa gane mutun mai daraja a idannuwanta? Wannan mutumin ko dan tsufansa a girmama shi aman Algabiit ke aiko masa da zagi haka? Ta yi imanin ba ita ba ko Algabiit din baba tsoho ya haife shi

Bak'a kuwa tunda ta kyala ido ta ga baba tsoho ta samu ta rakube jikinsa tana dan jefo masa tambayoyi a hankali da alamun tsegumi
Hannunsa ya saka ya dungure mata kanta yana murmushi, a ransa ya ayyana idan kika tafi,....nishadina, murmushina, zai tafi da ke
Sarki ya ci gaba da fadin" wadinnan mutanen da kike ganni, wannan baiwar Allahm mahaifiyar wannan bawan Allahn ce, sannan ta taso tun daga garin da kuka kai Fatimata rashin lafia ta zo Agadez daga nan sun dauki hanya sun zo garin nan dan neman baba sofo da ya baiwa dan nata maganin huka tun yana yaro bisa alkawarin idan an samu lafia sai ta bashi abinda ya samu Toh Sai aka tashe su Allah bai yi sun kara haduwa ba, tun daga lokacin take nemansa domin mutun ce mai son cika alkawari abin na tsaye a ranta sai yau Allah ya yi

Dan numfasawa ya yi, ya ci gaba" kin ga, ba a niger ba, ko a kasar waje masu fada a ji ne, Sun zowa Baba sofo da alkhairi na mamaki sai dai abin mamaki baba ya ce sam shi yanzu ba ta abin duniya yake ba, ya yafe sai dai damuwarsa *AGAISHAT CE*
Anna ta dago da sauri ta ce " AGAISHAT?

Sarki ya ce" kwarai kuwa, Baba ya nemi alfarmar.....................................................gaba daya sarki ya kwashe yanda suka yi baba da su Wardugu ya fadawa Anna dake zaune kanta na kallon kasa sauran yayanta na zagaye da ita Bak'a kuwa na jikin Baba sofo

Da sauri Bak'a ta dago ta kai dubanta wajen Anna da Sarki, ta maida dubanta wajen baba Sofo, Baba Tsoho ya yi gyaran murya ya ce" shakuwa, da tunani ya hana ni sakun nutsuwa Annar Agaishat, na sani bani da ikon zartar da hukunci kanta domin ban haifeta ba sannan ni ba wani

shakikikin dan uwa ba
A duniya adu.ata biyu ce, Allah ya sa in gama da duniya lafia Aljanna ta zamo makomata , fatan Allah ya nuna min ta zama mutun mai cikaken inci, ta samu nutsuwar zuciya , ta samu zama itama mutun,
Anna Agaishat ta yaya hakan zai faru? A timiya mu duka bamu fi kirgo da yatsu ba, nan da kike ganina har limamin garinnnan na nemi alfarmar ya aure man ita mana aman ya nuna aa ba zai iya ba
Almajirina ma ya kiye min,
Gashi yau da gobe sai Allah, Agaishat girma take, mu kuwa gajiyawa muke kara yi,
Idan ta fito daga nan ina ta fada? Me ta ci? Ya ta yi ta samu Allah ne masanin gaibu, ni kam a matsayina da wanda take zuwa wajensa sannan ta daukeni tamkar uba nakan yi mata nasiha, nakan tsoratar da ita, nakan nuna mata karara rayuwa da abinda Allah ya bani ikon sani
Annar yara , Ba zan tirsasa maki ba, ba zan saka ki daukan abinda zaki yi ta nisawa zuciya bata da tabas, aman ina so ki yi tunanin gaba da bayan lamarin, in da hali ki dauki Agaishat ki baiwa wannan mata riko da zuciya daya, ki yi kyakyawan zato, ki saka a ranki alkhairi ne sannan ki bi da adu.a, na yi imanin koda mugaye ne Allah zai saka mata kaunar yarinyar shari ya juye wa khairi

Wardugu ya yatsina fuska ya dubi Ayya dake zaune tana kallon su, da yaren tubanci ya ce" Ayya, yarinyar nan fa wannan mahaifiyarta ce , kuma ina jin shegiya ce shi ya sa wancen yake zazaginta haka! Ayya me ya sa suke faman rabuwa da yarinyar? Ayya

Wardugu ya isheka haka , Ayya ta fada tana zaro masa idannuwanta, murya a kausashe ta ce" baka lura da abinda ke faruwa ne?

Ba zato ba tsamani muryar Anna, cikin yaren Tubanci ta ce" ba shegiya bace, wannan da ka gani ya shige daki ya labe shine ubanta, yana kyamatarta ne dan ta zo duniya *BAK'AR FATA*

Da mamaki du suke kallonta,
Ayya ta taso ta karasa kusa da ita, hannunta ta kamo tana kallonta ta ce" batuba ce ke?????

Anna ta lumshe idannuwanta sai ga hawaye sharsharshar ta dan jijiga hannun Ayya ta ce" ban sani ba, ban san ko mecece ni ba,

Damko hannun Ayya ta yi da dan karfi ta saka idannuwanta cikin nata ta ce" ban san ko dan ina jin yarenki ba? Sai kawai nake ji zan iya sadaukar da y'ata wa ke, zaki rike mini yarinya da gaskiya?

Ayya ta ji gabanta ya dan fadi, matar na tare da wani banban lamari, Ayyan ta jijiga hannayenta itama tana kallonta ta ce" mudin raina

Algabiit dake ciki sai zaro ido yake, ya shiga ukunsa, ya aka yi Anna bata manta yaren nan ba? Aman abinda ya yi mata *Harta sunnanta ta manta*!  Domin kafin ya lulo timiya da ita sai da ya

tabata ta iya yarensa, ta iya saka kaya irin nasu, ta iya yan dabi.unsu, shigewa ya yi ciki ya zauna jikinsa na dan rawa rawa

Anna ta lumshe idannuwanta, ta ce" thank you,

Wardugu dake tsaye ya kalo su , Inglish kuma? Inglish ta yi?
Hai san ya karasa shigowa dakin da kyau ba sai da ya karasa, inda shigowarsa ya saka du yan matan suka tsaya kallonsa da mamaki, Bak'a kuwa ta lafe da tsoro jikin baba tsoho jikinta du yayi wani sanyi tana son fahimtar maganar tafiya da wa wai ake? Ina ai ita ba inda zata, ba zata bi wasu mutanen da bata sani ba bata taba gani ba ta je a kasheta, ya zata iya tafia ta bar yan uwanta da annarta da baba Sofo? Wa zai ringa kawo masa ruwa? Wa zai ringa saya masa gogo yana gurza masa a karfen gurje goro? Wa zai ringa koya mata karatu? Wa zai ringa ce mata itama mutun ce dan tana baka Haka Allah yake son ganninta ?

Wardugu yana karasowa ya dan duka yana kallon Anna ya ce" di u speak Inglish?

Anna ta dago ta kale shi, ta amsa masa da kanta, a ranta tana nanata inglish? Wani yare ne shi kuwa? Ba irin wanda suke yi da matar bane kennan?

Wardugu da mamaki ya ce" ya aka yi kika iya inglish? A ina kika koya? Wa ya koya maki? Daga wani gari kika zo?

Anna da kanta ya fara sarawa ta dafe kanta da sauri , muryarta ya fara rawa rawa ta ce" i...i...i don't know ! Ta fashe da kuka tana rungume hannayenta da sauri Gaishat ta karasa tana rungumo Annarsu itama tana kukan za.a kuma raba su da yar uwarsu? Domin ta sani ne , a yanda anna ke jin zafin irin abubuwan da ake yiwa Agaishat , a yanda aba ya tasota a gaba da man bleating kan sai ta shafa ya yi kudinta itama , anna na neman koma waye ta bashi aurenta ta tafi ta huta, ta gwamace ta tafi ta auri koma waye da aba ya yi kudinta itama kar a je ta fada irin rayuwar da fatimata ta fada ko ma wace ta fi ta

Sai da Anna ta yi kuka mai isarta, suba bata hakuri kafin take share hawayenta ta yafito Bak'a sake kukan yan uwanta da mamanta na kuka

A hankali ta taso ta nufo Anna

Tunda ta taso suka sauke idannuwansu kanta
Wardugu ya tsura mata ido, a ransa ya ayyana " Eh lale baka ce, tana da baki sosai da kuma kazanta, a rayuwar kauye dole su tsangwameta domin gari ne mai bambace bambance

Kawar da kansa ya yi, jikinsa ya yi sanyi da lamarin uwar yarinyar, tabas akoy bamban al.amari a tatare da ita, da farko ya so ya cakula abin, ya kasance an watse su yi tafiarsu ba tare da Ayya ta kwaso masu wani jangom din ba, sai dai ina yanda matar ta yi yarensa tar tar tamkar

nata, sannan ta shiga turanci tamkar yarenta shima, kuma ta furta bata san bama sunnan yaririkan da ta yi, harma ta shiga wani yannayi dan za.a takurata da tambayoyi ya saka shi yin sanyi, a hankali ya furta" sai na san su waye ku!

Anna ta kamo hannunta ta zaunar da ita daf da daf, ta dago fuskarta, abinda bata taba yi ba irin kusancin nan da yar tata, tana so ta yi tana mugun tsoro da kunya

Murya a raunane ta ce" Agaishat, Ina son ki

Da sauri Agaishat ta kara kallonta,

Anna ta sakar mata murmushi ta ce" sosai, ina son ki, kuma ina so ki samu canjin rayuwa, bana so ki kare a haka bana so ki kare a ciki duhun rayuwa

Gaishat ta ce" Anna, Anna

Anna ta kallota ta ce" menen Gaishat? Kar na raba ku da yar uwarku?
Na san muna cikin jimamin mutuwa, muna cikin rudu, aman ku kun fi kowa sannin rayuwar da muke , mutanen nan na tafia in dai ba da ita ba na yi imanin ba zai barta ba tunda ya saka wannan lamarin a ransa sai ya aikata
Da wa zai hadata? Ina zata fada? Mai yiwuwa idan aka tsilira da ita wani wajen koda ta so guduwa ishrwa ta kasheta a hanya,

Agaishat ta fashe da kuka jikinta ya kwashi rawa ta ce" Anna aa, aa Anna, kar ki bada ni haka Anna, ku kadai na sani Anna, kar ki raba ni da ku, kar ki yi mini haka Anna, ki barni ina ganninki har in mutu, ki barni ina gannin baba Sofona ina kai masa ruwa yana kiya mini karatu, ni ba ruwana Aba ya yi ta dukan nawa ba komi Anna in dai ina ganninki ina gannin yan uwanna ina gannin Baba Sofo ya isheni Anna, kar ki rabani da abinda nakeda a duniya wato ku........

To jama.a ya zama kwashe ne? ............m

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

1️⃣7️⃣

Anna zuciyarta ta yi mugun karyewa
Hawaye yana shatatar mata muryarta na rawa ta ce " Agaishat, ki yi hakuri ki bi su, ba mugaye bane

Agaishat ta buda idannuwanta da kyau ta ce" kina da tabacin ba mugaye bane? Kina da tabacin su din mutanen kirki ne??

Jikin Annan ya yi sanyi ta sada kanta
Gaishat dake hawaye itama ta matso ta dafa hannun Agaishat ta ce" Agaishat....

Anna ta dago ta ce" bani da tabacin halayensu, ba zan ce su din mutanen kirki bane kuma ba zan fadi akasin hakan ba
Agaishat, ni da na haike ki, ni da na yi rainon cikinki, na haife ki , tunda kika ji na ce ki je, toh ki je din kawai....ba zaki fahimci girman maganana ba sai ranar da Allah ya nuna maki kin haihu, soyayar dake tsakanina da ke na iya cewa ki je to ki yarda da na yi imani na barwa Allah komai ne, a nan kike ko a wani wajen dama shi ya halice ki, ko wace rayuwa zaki fuskanta shi ya kadaro maki, ni ban isa na hana ko na saka ba sai dai na yi ta kai kukana wajensa ina neman jin sanyi daga wajensa

Agaishat ta rintse idannuwanta, ita bama bin nasu ba, wannan mutumen da suke tare wanda yake tsaye tunda suka zo wanda fuskarsa bata ga saki ko tausayi a tatare da ita ba, shi take tsoro, in dai mugaye ne ta san shine mai yanka mutanen domin wannan da gani shine bamban mugun

Algabiit dake daka sai sintiri yake, haka zata tafi? Ba.a bashi komai na kudin tafia da ita ba? Koda ba yarsa bace ai shi yake ciyar da ita tunda aka haifeta, ya isa a yi shawara da shi sannan a biya shi! Sai dai yana ganin yanda wardugu ya diro daga motar nan ya nufosu, tun a lokacin
```

ya fara sakin fitsari domin shi yama yi tunanin an zo kashe shi ne, ba zai fita gaban wannan mutumin mai kwarjini ya yi wani abin ba, aman ta yarda ta bada Bak'a haka zata gane bata da wayo!

Bak'a na ji tana ganni, tana gurzan kuka mahaifanta da rai ba babu ba, ba aure ba ba dangi ba aka fitar da ita tana waiwayen Anna da ta koma da sauri ta shige bayi ta rufe ta shiga rizgar kuka, aka shiga da ita cikin motar da bata taba gani da idannuwanta bama bale ta shiga,
Tana ji tana ganni matar nan ta shiga ta riko hannunta tana dan murzawa Alamar rarashi
Tana kallon baba Sofo har aka sako shi motar shima kafin da kyar sai da Wardugu ya yiwa Walyn tsawa ta shiga motar wai karni take ji na bak'a, ya shiga suka tayar tana ji tana ganni aka bar anguwarsu gidansu yara sai bin bayan motar suke suna ihun murna sun ga mota manya sai daga hannu suke har sai ta bace da ganninsu aka je kofat baba sofo aka tsaya suka sauke shi Agaishat ta kara rikicewa gannin da gaske sun bar baba Sofo wanda ya tsaya yana daga mata hannu idannuwansa sun kara kodewa alamun kuka yake na zuci sai dai ya fi farin cikin hakan da zamanta a garin

Haka suka dauki hanya ba tare da sun huta ba ko sun sha ruwan garin ba suka dibi hanyar komawa garin Agadez

Kukan take tana fadin"" Anna, Sofo, Anna, sofo

Walyn ta ja tsaki ta ciro ecouteurs dinta ta saka a kune, Wardugu dake gaba ya rufe idannuwansa a tunaninsa zata gaji ta yi shiru ne aman ina sai kara boda Agaishat ke yi Ayya na tausarta tana bata hakuri da tubanci bata san ta dan iya hausa ba ita kuwa bata iya buzanci ba

Juyowa ya yi, da yaren buzanci ya ce" Ke ki rufe mini baki a nan tun kafin na saukeki na yi maki dukan tsiya, shiiit bakin nan naki ya mini shiru ko na ciro maki shi a hannunki

Wa ya ga hadiya, Agaishat hadiye kukanta ta yi, tana zaro ido tana kallonsu daya bayan daya tana sauke ajiyar zuciya,
Ayya tana magana tana yi mata nuni da ta yi hakuri ta yi shiru ta daina kuka

A hankali Agaishat ke ajiyar zuciya sannan ta damke hannun Ayya wace ke rike da nata itama, tana kallonta, a nan ita kadai ta dan hangi laushi a tare da ita

Tafiya suke suna ratsa sahara har suka baro suka debi titi,
Agasihat ko dis ba baci a tare da ita sai kallon titin da take , tsoro fal ranta haka idannuwanta suka nuna, mamaki take dama Shukoki na gudu? Domin yanda motar ke gudu sai take gannin suma shukokin gudu suke tun karfinsu

Walyn dake takure tana sakin numfashi sama sama ta shiga yinkurin amai tana kakari

Ayya ta kai dubanta wajenta da mamaki, lale walyn bata da mutunci, yanzu du irin yanda ta

fafeshe su da turare tana jan tsaki kuma ta kai amai zata yi dan warin Yarinyar da suka dauko
Ta girgiza kai kawai ko ci kanki bata ce da ita ba

Wardugu dake zaune a ransa ya ayanna Walyn bata son zaman lafia, in dai Ayya ce ta isheki ba abinda ya dame ni!

Ba su su karasa cikin gari ba sai can wajen karfe goma na dare
Abinka da agadez ma ba wani banban gari sosai bane sai ya kasance shiru garin sai yan mata da samari wasu na tafe a kafa wasu a mota wasu a mashin suna dan yawansu na yau da kulun wasu sun nufi gidan rawa, wasu sun tafi gidan cin abinci, wasu suna yawatawa dan shan iskan gari kuma suna hirarsu

Idan ta juya can sai ta juyo nan, kallo take irin na kauyawa sosai jikinta kuwa har zuwa wannan lokacin bata saki ba, sai dai ta rakube jikin Ayya wace take kara rike hannunta dan ta saki jikinta Direct gidan Sarki aka kai su Ayya, har ciki suka shiga da motar suka sauke su Ayya Walyn sai sauke ajiyar zuciya take ta rabu da alkakai

Har sun juya motar Wardugu ya ce" tsaya

Sojan ya ja ya tsaya ,
Wardugu ya juyo wajen Walyn ya ce" sauka ki kwana wajen Ayya

Walyn ta dago da sauri daga kakabe kakaben jikinta ta zaro ido ta ce" me me ka ce?

Wardugu ya tsareta da wani kallo na kar ki raina min wayo

Walyn ta ce" aman Wardugu , wani irin na sauka na kwana a wajen Ayya bayan ga mijina wajenka na sauka kayana a wajenka komaina na tare da kai? Yama zaka raba ni da kai ka hada ni shakar iska daya da wannan mumunar yarinyar mai siffar aljannu

Yatsina fuska ya yi, a ransa ya ce wai siffar aljannu, ko a ina ta san aljannun ita? A fili kuwa ya ce" Haka na yi ra.ayi

Walyn ta ce" Wardugu kar ka yi min haka, me na maka? Kar ka yi min irin horon nan!

Wardugu ya kalli sojan nan ya ce" sauka mu je

Sojan dai bai ce komai ba ya bude ta fita da bindigarsa yana kallon ikon Allah
Wardugu ma ya fito ya rufe ya tafi wajen sojan ya fara tafiya, sojan ya waiwaya ya ga a yanda suka ajiye motar a bakin hanya, bayan wannan matarsa a ciki, sannan tsakanin fadar da hotel din sojojin akoy tazara, kuma idan mutun ya tunkaro wajen haka kai tsaye daga bakin karfe goma na dare ordre da aka baiwa sojojin shine harbi ba ji ba gani in dai ba a mota ko wani abinda yake malakinsu ba wanda da ya tunkaro wajen akoy adadin odar da aka ce su yi dan

shaida su ne wada kowace safiya ake canzawa
Shi dai biye yake da shi da sauri yana hadawa da fan gudugudu suna tafiya har suka fita daga gidan suka dauki hanya (🤔 sisi kika ce zaki iya da wardugu ko?🤣)

Walyn wani ihu ta saki a daidai lokacin da ta fahimci wardugu bara mata ya yi motar gaba daya ya tafi a kafa da ya je da ita, Wardugu ita yake wulakantawa? Toh ita kuwa ba zata shiga wajen wannan uwar tasa da wannan yarinyar mai karnin jini ba! Sai dai ta kwana a motar!
Haka ta takure a motar nan ta ki kunna hasken waya dan a gaskiya tsoro take ta kunna waya wani abin ya lura da mutun tun bama dare da ya tsala maguna suka fara kukan jarirai ba,

Kawata, tsakaninki da Allah ke haka rayuwarki wata irin mace ce bahaguma? Yanzu yarinyar nan da kika kwaso kin san asalinta ne?

Ayya ta yi murmushi tana kallon kawarta aminiyarta matar sarki, ta ce" mamanta ta iya tubanci

Anna matar sarki ta dafe kai ta ce" dan ta iya tubanci sai me? Dan ta iya yarenki shikennan sai ki wani kwaso yarta? Kin ce a gidansu kuka daukota

Ayya ta ce" ki gane kawata, lamarin mahaifiyar yarinyar da yarinyar ne akoy sarkakiya, wai kawai dan kalar fatarta shikenan take fuskantar tsangwama, ita kuwa uwar sai kawai ki ji tana yare kuma wai tace itama bata san sunnan yaren ba, kuma ni na yi haka ne dan cika alkawarin bawan Allahnan, baki ga yanda ya tsufa ba aman haka yake nisa lamarinta,

Anna matar sarki ta dafe kanta da hannunta dake cike da zobunnan zinari ta kalota ta ce" ai idan kin lura yanzu wannan matsakar ta zama ruwan dare, a kauye suna kin bakar fata tare da jahilci a birni suna kiyaye bakar mace dan dogon buri irin nasu sannan suna hakan ne da dabara, kina ganni daidaiya zaki ga a yanzu mutun ya tashi ya dauko bakar mace, sai ki ji suna fadin Allah ya basu farar mace koda maya ce, banza idan ta cinye su fa?

Ayya ta dora kafarta daya saman daya tana ajiye tufar da ta gutsura ta ce" ba ko.ina ba, ban ki maganarki ba aman nima nace maki ba ko.ina ba,
Du macen da kika ga ana yi mata duban marar kyau ko anai mata wani gani gani ina mai tabatar maki ita ta saki kanta,
Mace du muninta idan ta iya wanka ta iya kula da jikinta ta iya kwaliya daidai da yannayinta sai ta kara da adu.a kawai
Sannan ita bakar mace da kike ganni baiwa ne da ita, bakar mace tana da kwarjini, bakar mace nada juriya a kowani fani, bakar mace na da kyau mai fuzga, idan bakar mace ta sakar maki tsararen murmushi zaki hangi haske ne a tatare da ita, ke kawata zaki sha mamakin yar amanata in sha Allah

Anna matar sarki ta yi murmushi tana jujuya kanta ta ce" oho dai, kina kare bakar fata dan kina

da ita bayan taki mai kyau ce, na rantse maki ko ni na samu taki ina so domin bakinki mai kyau ne, ba gashi ba Wardugu ya samu dan bakinki da farin mahaifinsa sai ya samu kalar fatar nan ta yan ethiopia baki ga yanda fatarsu take ba? To aman wannan yarinyar kina ganni da akace wanka ta saka kuka aman kika biye mata wai kika rakata ta yi baci a haka? Anya kuwa zaki iya wani gyarata?

Ayya ta ce " ki saka ido kawai.....

Sojan nan tafiya dai yake aman ba karamin gajiya ke tatare da shi ba, sai ya ga Wardugu daga kafa kawai yake yana jefawa yana kara kutsawa cikin duhun garin suna ta sauki su karasa hotel din
Ba su su karasa ba sai kusan sha biyu na dare,
Suna karasawa Wardugu ya saka kai kai tsaye ya nufi shiga wajen da idan ka shigo harbi ne zai salamo maka ....................

Kadan ne ku yi maneji😍😍😍😍

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

1️⃣8️⃣
```

*Godiya ta tabata ga Allah sarkin sarauta ubangijin talikai, godiya mai dumbin yawa gareku da adu.a Allah ya saka da alkhairi ya biya ....*

*Khadijat tawa ta grup BAK'A CE* wannan page din naki ne

Ja sojan ya yi ya tsaya bai san lokacin da ya ce " Oga, zone interdite ce fa

Wardugu ya juyo yana kallonsa, ya yi murmushi ya ce " tsoro kake ka mutu sergent?

Kansa ya dan shafa yana kallo  Wardugu,
wardugu ya kara cewa" mutuwa fa ko kana kan gadonka sai ta daukeka sergent ba gwara mu tunkareta ba?

Kara kwalalo idannuwansa ya yi yana kallon wardugu

Wardugu ya matso ya dafa kafadarsa ya yi murmushi ya ce" mu je ......

Haka suka kutsa gaban Sergen din nan tamkar ya bale ya fado dan tsoro,
Sai dai ga mamakinsa sai ya ga sun kama wata yar raga a nan Wardugu ya bude ya shige
Shima shiga ya yi yana ta waige waige yana biye da wardugu nan ya hango ashe har sun shiga balbalin hotel din sun fice hatsarin

Wara wawar ajiyar zuciya ya sauke yana biye da wardugu
Wardugu ya rage sauri ya dan rage sautin muryarsa ya ce" nima bana so na yi mutuwar bindiga fa Sergen, ina so na mutu cikin nutsuwa kai da zabi gareni in mutu ina sallah kuma ranar juma.a,
Aman kawai yau ranar asabar gatsai gatsai sai mu tarbi mutuwa? Da juma.a ne ma,

Ya dan yi murmushi ya yi gaba ya barshi nan tsaye yana murmushin shima, kai ogansa idan ya yi wani abin tamkar ba shi ba, wai shifa a nan wasa ya yi masa da rai🤔

Tun fa wuri ta farka daga bacin da ya saceta, sai dai ta ki motsawa tun a jiya da aka sauketa saman gado ta yi baci ta kasa ta sauko kasa ta kwonta saman farin tls din ta rufa da mayafinta na turkudi tana kallon yanda pankar sama ke juyawa har baci ya dauke, a yanzuma ta farka tun da wuri tana son tashi sai dai tsoro take hakan ya sa ta yi kuri da abin mamaki a fuskarta tana kallon pankar nan, mamaki take menene? Ya aka yi bai daina gudu haka ba? A gaban idannuwanta aka kunna , tunda ya dauki gudu bata ga ya tsaya ba, ita tsoroma take ya yo kasa

kasa ya kasheta

Ayya ce ta bude dakin ta shigo da salama a bakinta

Firgigit Bak'a ta tashi ta zauna jikinta jikin garu tana bin Ayya da kallo

Ayya ta yi tsam itama tana karantarta, a kasa ta kwana du sanyin nan na kasa, sannan da alama bata yi sallah ba

Dukawa ta yi kusa da ita tana kallon yanda take jan mayafinta tana lulubawa a jikinta, Murya a sake ta ce" kin yi sallah?

Da ido kawai Agaishat ke bin Ayya domin bata san me take fada da yaren tubanci ba

Ayya ta yi dabara ta kamo hannun Agaishat ta mikar da ita ta jata suka nufi bayi

Suna shiga Ayya ta dauki butar karfen dake wajen ta kunna ruwa mai dumi dumi ta cika mata ta nuna mata wajen da zata iya dukawa domin ta san ba wani gane lamarin wc zarai ba tukunnan dai, ta yi mata nuni da ta yi dagara ta yi alwallah ta yi sallah , ta yi mata nuni da har rana ta fito

Da kai Agaishat ta amsata tana kallo sai da ta fita ta duka ta yi fitsari nan inda aka nuna mata ta wanke jikinta ta mike ta yi alwallah tana jin dadin yanda ruwan keda dumidumi

Tana gamawa ta fito ta ga salaya aman ba kowa a wajen dan haka ta hau ta tayar da sallah ta yi abinta cikin nutsuwa kamar yanda Baba tsofo ya koya mata

Tana gamawa ta zauna ta hade kanta da gwuiwarta tana zubar da hawaye, tunani take ya Anna ta tashi? Ya yan uwanta? Ya baba sofo? Wa zai kai masa ruwa? Wa zai gurza masa goro? . .....

Buda kofar aka yi aka kuma shigowa ,
Wannan karon matar sarki ce da wata baiwa buzuwa da kuma Ayya

Ayya ta kali matar sarkin ta ce" so nake a fada mata ina so ta yi wanka ta shirya mu tafi garinmu domin Wardugu yace jirgin karfe daya zamu bi

Matar sarki ta yi murmushi har yanzu tana mamakin daukarwa kai irin na aminiyarta, ita da ko hausar juna basu iya ba
Ta kali baiwar nan cikin isa da dakewa ta fada mata abinda zata fadawa Agaishat wace tunda matar sarkin ta fara fadi take kallonta daga zaunen da take tana fahimtar yarenta

Kafin ma baiwar ta fadi Agaishat ta kallo Ayya, a hargitse ta ce" ina zamu tafi kuma? Kar ki kaini

wani wajen  kin ji? Ki barni a nan ma

Tana fada ne tana dan nufo su Ayya dake tsaye

Baiwar ta yi saurin tareta , da yaren buzanci ta ce" ki tsaya nan, kin san ina ne kike a nan? Kina garin agadez, a garin agadezma kina masautar agadez, a masarautar agadez ma gaki gaban matar sarki uwar gida sarautar mata,
Ki koma baya ki cika umarninta

Rakubewa Agaishat ta yi tana kallonsu, ta shiga ukunta, ya zata yi? Matar sarki kuma? Ko sarkin garinsu talaka bai isa ya yiwa matarsa ko yayansa wargi ba bale na garin Agadez

Kanta a sade ta ce" zan yi wankan

Ayya dake tsaye ta karaso kisanta tana kamo kafadunta ta kallo aminiyarta ta ce" me ta ce mata? Sai nake gannin kamar ta tsorata? Kar ta tsorata min yarinya fa kar ta rikitata

Anna dariya ma kawai yannayin Bak'a ke bata, ta fadawa Ayya abinda aka yi

Ayya ta dafe kanta ta zabgawa matar nan harara ta ce" ku tafi abinku tunda dai ba zaku tausasa ba, idan ita sarauniyarta ce ke ni ai aminiyata ce, bana son irin yanda kike nunawa kan yarinyar nan, kina manta mutun ce itama ?

Anna ta yatsina fuskarta ta ce" kin ga bara na je na ga in an kawo kayan da kika ce kina so, gaskiya ki yi hakuri ba zan iya wannan faman ba

Ayya na kallo Anna ta juya baiwarta ta bi bayanta suka tafi

Zaunar da Bak'a ta yi gefen gado wace ta takure waje guda, ta juya ta fauko wayarta ta zauna ta danna kira

Ana dagawa ta ce" kana ina?

Amsawa ya yi da" gani gefen aghali muna ratauna wata magana

To ka bari ka zo yanzu yanzu nan bangaren da aka saukeni ina ciki ina jiranka

Da toh ya amsa ya mike yana cewa Aghali ina zuwa

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na            *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

19

Shiga ya yi ya zarce dakin Ayya ya tarar bata nan sai ya fito ya shiga dayan dakin, daman falo ne mai daki biyu,

Yana shiga ya tarar da ita tsaye , Bak'a kuwa zaune inda ta ajiyeta

Karasawa ya yi yana tambayar lafia?

Ta amsa shi cikin kulawa ta tambayeshi kwannan iyalinshi
Ya yi murmushi dan ya san Walyn bata zo nan ba kennan wajen matar sarki ta je?

Ayya ta ce" Wardugu, zo ka yi mana fasara da y'ata ka ji? Ina son yi mata magana yanda zata fahimta aman ban lamunce maka ka rikita min ita ba ka ji?

Da mamaki yake kallonta, daman shine dalilin kiran nasa? Kai? Yanzu Ayya ya zata yi idan baya nan toh?

Kai kawai ya dan girgiza ya karasa inda Agaishat ta kara rakubewa jikinta ya fara rawa ta nuna alamar tsoronsa take ji

Ayya ta ce" Wardugu ka yi wani abin mana, ka ga tsoronka take ji, bana so dan Allah

Wardugu ya sauke ajiyar zuciya ya kali Ayya ya kara kallonta, uwa uwa hummm
```

Karasawa ya yi ya dan rage tsayinsa yana kallon yarinyar, kokari ya yi ya saisaita maganarsa ya ce" me ke damun ki?

Kallonsa take ita kuwa, irin kallon nan na kana jiran gannin me za.ai maka

Wardugu ya dan rontse idannuwansa ya bude ya ce" kin ga, mu fa ba mayu bame, ba mugaye bane kamar yanda kike tunani, mamanki tace mu zo da ke, idan kika kwontar da hankalinki kika nutsu sai ina kai ki kina gaishe da mamanki, kinga dai yanda kuka yi da ita ko so kike a mayar da ke ne??

Tsam ta yi tana kallonsa bata bashi amsa ba

Ayya ta matso ta ce" me kake ce mata?

Wardugu ya kali Ayya ya ce" ba komai

Ayya ta ce" to ka ce mata ta tashi ta shiga ta yi wanka , ko na yi mata da kaina ma

Ido Warsugu ya zaro, sai kuma ya basar, ya kaleta sosai ya ce" kin ce Sofo na koya maki karatu ko?

Kai Agaishat ta shiga daga mai

Ya ce" yawa, kuma sofo ya fada maki tsafta na cikin adini? Sai mai tsafta zai shiga aljannah fa

Agaishat ta kara gyada masa kai,

Ya fara jin haushin gyadegyadan kan nan, aman Ayya na wajen ta kasa ta tsare, ya tausasa murya ya ce" toh ki tashi ki shiga bayi, Ayya ta nuna maki kayan wanka ki yi wanka sosai kin ji?

Kai ta kuma gyada masa ta mike tana kallon Ayya, tunda ta ji yace za yana kaita wajen Annarta zata gwada yi masu biyaya ......

Ayya da jin dadi ta rakata bayin ta kuna mata ruwa masu dumi sosai ta bata sabulu da soso sababi, ta bude bruch da maclean ta mika mata ta yi mata nuni da yanda zata yi ,
Har ta juya ta dawo tana nunawa ta ce" ki cuta jikinki lungu lungu sannan ki wanke tafin kafafuwanki kin ji

Kai Agaishat ke gyadawa har Ayya ta gama ta fice

A hankali ta tube kayan jikinta, ta yi tsaye gaban ruwan tana kallon yanda yake zuba
Da tsoro tsoro ta tara hannunta ta janye, ta kuma tara ta janye hardai ta yarda da ruwa ne ke

zubowa kuma ba zai konata ba

A hankaki ta shiga tana bismillah a ranta ta yi tsaye ruwan ya shiga kwararun mata a jikinta tun daga kanta dake da kitso kwaya daya tal har jikinta

Sai da ya gama dukanta ta dauki sabulun ta shiga gogawa a jikin soson tana jin yanda kamshinsa ke tashi tana jin dadin kamshin
A hankali ta shiga cuda fuskarta da soson nan ta cudeta da kyau ta darwaye kafin ta shiga wanke wuyanta sosai da bayan kunnayenta da cikin kunnen ta gangaro hamatarta kamar yanda Ayya ta nuna mata ta daga ta kama dirza ta yi kasa ta wanke jikinta sosai ta bi ruwan nan ya shiga darwaye mata kumfar da har ta zama baka dan tsabar datin dake jikinta, tana kallo ruwan na bin yar magudadar ruwa yana tafiya
Ta koma ta darwaye soson ta kara yin yanda ta yi , ta shiga saba sabulun a tufkeken gashinta na buzuwar usul  ruwan nan na dareaye mata,
Abinka da tufkeken gashi wani wajen ya wanku sama sama aman cikin kam da datinsa daskare, haka Agaishat ta yi ta wanka tana sakewa tana jin kanta wani sakayau tana kara balbaluwa a cikin ruwan nan tana jin dadinsa abinka da ba sabanba ta wanke tafin kafafuwanta da abinda Ayya ta nuna mata nanma ta ga dati sai fita yake , har yatsarta ta saka ta debo datin tana kallo da gaske dati ne ta wanke da sabulu tana daga kanta sama ruwan na shiga idannuwanta yana kara ratsa gashinta da jelar ta sako tana yawo du idan ta juya kan

Fitowa ta yi ta dauki kayanta wa.inda sai a lokacin ta ji suna wani irin bugawa da ta rabu da datin jikinta, har ta shiga tunanin ko ta wanke? Sai wani abin yace mata idan kika wanke ki saka me kuma? Mayar da kayan ta yi ta fito ba tare da ta kashe panpan ba domin bata iya ba

Ayya dake zaune tana jiranta domin Wardugu ya tafi abinsa , ta mike tana fadin" eyah Agaishat ki cire kayan nan mana

Agaishat ta yi kasakai tana kallonta

Ayya ta dafe kai ta ce" wani yare kika iya

Agaishat kin iya frencais? Angalais? Ko hausa?

Agaishat dake kallon Ayya ta ce" Ayya, hausa kadan kadan

Ayya cikin itama dan yaren hausar nata ta ce" ouf , mun samu na gaisuwa, ki fida kayan nan ki canza wasu kin ji

Agaishat ta gyada kanta tana kallon wa.inda Ayya ta nuna mata, sannan ta juyo dan gannin a gaban Ayyan zata saka sai ta ga Ayya ta nufi kofa abinta

Ajiyar zuciya ta sauke ta tube kayan ta dauko wa.inda aka ajiye mata

Tsayawa ta yi tana kallon doguwar rigar abaya baka wace bata san ina ne gabanta ko bayanta ba sai dogon wando wanda ta daga tana ta jujuyawa irin na maza ta ayanna a ranta sai dai ba irin na mazan garinmu ba domin wandunnansu tamkar buhu........
Da daurin kirjinta tana tsayen nan Ayya ta dawo ta ga bata saka kayan ba

Nufota ta yi ta ce" aa ya baki saka ba?

Agaishat ta mika mata ta ce" Anna ban iya ba

Ayya ta yi murmushi ta shiga nuna mata ta juya ta saka wandon da kyar domin ya yiwa jikinta kadan duda fadinsa da yanda kuma yake jayuwa,
Ta dora rigar ta kule yar igiyar dake ciki

Ayya ta juyo tana kallonta, ba laifi kayan sun amsheta sai dai sam wankan nan bai yiwa ayya ba , gani take bata wanku ba da saura duda yanda du wani jirwayi na turkudi da fari fat din nan ya fita

Mai ta miko mata ta shafa , ta miko mata turare ta tayata shafawa

Agaishat bata san tana sakin murmushi ba sai da ta waiga wajen madubi

A hankali ta taka ta karasa, hannunta ta mika ta taba madubin tana kallon kanta, a hankali ta juyo wajen Ayya ta ce" na gode Anna

Ayya ta karaso da dan kalabin rigar ta kama kanta da bai karasa bushewa ba ta saka mata ribom ta daure mata sannan ta nada mata dan kwalin ya zagaye fuskarta

Kwali ta dauko ta nuna mata da ta shafa , Agaishat ta ce bata iya ba , hakan ya sa Ayya ta saka mata idonta ya fara ruwa ruwa abin rashin sabo Ayya tace ta jure karta murje ta kuwa juren

Abin maskara ta dauka ta fitar da shi ta saka wani mouchoir (kyale) ta goge bakin jikin tas tas, ta dauki jagira mai ruwan baka ta gogoga a jikin abin ta samu ta caje girar bak'a,  girar ta kwonta tsaf a inda ya kamata ba kamar da farko yanda take wawatse ba

Ayya ta juyata wajen madubin ta ce" Agaishat, Tsafta, kwaliya, ya zama wajibi ga macen da ta san ciwon kanta, ki rike wanka , ki kasance mai tsafta kin ji??

Kai Agaishat ta daga tana kallon kanta da mamaki, tamkar ba ita ba, ta sawaya hancinta ya wani tafi zuwat, wai a nan Ayya bata gamsu da wankan ba jira take dai su karasa Niamey ta dauki lamarin a hannunta..........

Karfe sha biyu da minti arbadin suka fito daga masarauta suka nufi aeroport, ita dai Ayya bata

san yanda wardugu ya yi ya samawa Agaishat waje ba bata tambaye shi ba

Sauran minti biyar suka karasa, suna zaune Ayya na kallonsa yanda ransa ke bace, bata ga Walyn ba bata tambayi inda take ba domin ba wani shiga lamarin juna suke ba, bata san zuwanta ba sai da ta ganta daga ina kwana wani abin bai kara shiga tsakaninsu ba sannan dan yanzu bata ganta ba itama ba zata wani tambayi inda take ba , Allah ya basu zaman lafia ita da mijinta ba abinda ya shafeta da zamansu haka kuma ba zata shiga dan wani gyara ba!

Ba.a jima ba suka mike domin an fara kiraye kirayen sunnaye,
Ita dai agaishat tunda aka haliceta bata taba gannin jirgin bama bale wai har ta shigeshi
Ta dai bi bayan Ayya da ta kama hannunta ta shiga nuna mata yanda zata taka matatakalar ta hau suka hau tare tana kara rike Ayya da kyau dan kar ta fadi har suka shiga
Kallon tsarin cikin jirgin take a ranta ta ayanna ba irin na mota ba ,
Nan Ayya ta tsaya sai da Wardugu ya shige kusan madubin domin sam ya hannata zama a nan in dai tafiar jirgi zata yi, ita dai sai dai ta yi murmushi kawai irin yanda yaron nata ke sonta ke kokarin kareta har mamakinsa take ,
Yana shiga sai ta saka Agaishat ta shige tsakiya , shi kam bai yi magana ba domin ransa a kololuwar bace yake, wai Walyn ta bi jirgin damagaran gobe ta bi na niamey ta karasa, shi zata nunawa zuciya ko? Han......

Ayya ma ta zauna ta ja ceinture ta sakawa Agaishat sannan itama ta saka bayan ta kashe babar wayarta ta android

Ba.a jima ba aka shiga fadin a daura ceinture a kashe waya da yarurukanmu na niger da kuma french da inglish duka , bayan an gama jirgin ya fara tafiya wace suuuuuuuuuuuuuuuuuuuuuuuuuu ne saman doguwar hanyarsa har ya zo wajen hatsarin wato tashi da saukar jirgi ba,

Cikin adu.a a bakin Ayya

Nan fa ake yinta domin abin tashin jirgin nan, kun san ko wanda ya saba sai ya ji cikinsa ya yi kasa bale wanda shigarsa ce ta fari kuma sha.af Ayya ta sha.afa da fada mata abinda kan iya zuwa sannan tace da ita tashi zasu yi sama, ita kuwa a kauye baba sofo ya taba gaya mata akoy harda wani abin mai tashi sama a birni sunnansa jirgi ,

Ai gaba daya ta shiga jijiga ta damki cinyar wardugu dake gefenta na dama ta damko ta ayya ta bude baki ta........

🤣🤣🤣🤣 ku taro su kauyawa a birni🤣😂😂😂😂😂

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

20

Ido Wardugu ya zaro, ya kai kallonsa kan hannunta wanda ke dauke da dogayen akaifu domin ba wani cire su take son yi ba sai baba sofo ya sakata gaba take yanke akaifunta sai tace nai ai susa take da su,
Wardugu bai gama tantance meye haka ba ya ji wani irin ihun da ya yi barazanar tarwatsa masa dodon kunne,
A tare suka juyo wajenta shi da Ayya ......

Ayya cikin yannayin tashin hankali da yaren tubanci ta ce " Wardugu Wardugu tsoro ne take ji na manta ban fada mata ba, kuma ban riketa ba , mai yiwuwa bata taba ganninsa bama bale ta shiga;

Bak'a da jikinta ke bari gaba daya ta kwalallo idannuwanta, daurin dan kwalin nata ya kunce , hawaye tuni sun kama zarya, ihu kawai take tana ambatan innalilahi wa.ina ilaihi raj.une!

Mutanen dake kusa da su harma wa.inda ke dan nesa da su ne hankalinsu ya fara tashi du aka fara jiyowa wajen su Ayyar da ayyar tambaya da alamun tsoron a fuskokin su....
Daga can kofar masu kula da passenger wata mata mai kulawa da bukatun passenger ta fito da
```

sauri da dan sket dinta, ta sha kwaliya, tana dan sauri tana fadin kowa ya zauna kowa ya kwontar da hankalinsa ba komai bane , sannan tana nufo wajen su wardugu;

Hannunsa ya daga na dama ya shafa sumarsa, a kasan zuciyarsa ayannawa yake wannan wani irin tashin hankali ne?  Shi Wardugu da girmansa da irin yanda duniya ta san shi, shine za.a yiwa taro da yar kauyen nan! Merde! merde! merde!

Juyowa ya yi wajenta, hannunsa na hagu dake kusa da ita ya saka ya janyota jikinsa, ya sakata a jikinsa da hannun nasa ya karkata fuskarta gefen hannunsa na dama , ya saka hannun nasa na damar ya yiwa bakin nata mai ihu wata damka ...ai kuwa shiru kake ji ba ihu ba di kira da salamcewa sai dan mutsu mutsu wanda shima da ya kara riketa sai laf tamkar ta lafe ne a jikinsa. (WARDUGU kan keta)

Tambaya matar nan take lafia ? Me ke faruwa??

Wardugu gannin bakuwa ce yar amerika, sai ya ciro carte dinsa da hannun hagu dinsa ya nuna mata mai shaidar ko shi waye, sannan da lebensa ya yi mata nuni da mahaukaciya ce kar ta wani damu........🤔

Ai kuwa ta shiga bada hakuri da iya yi, ta juya ta koma.
 Ayya sai faman ya cika yarinya take aman ya tsareta da ido ya ki yin maganama;

Nauyin da ya ji ta yi ne ya saka shi sasauta rikon, ba.a wani dauki lokaci ba Agaishat ta yi baci sai kace wata  baby, bacin tsoro da tashin hankali, bacin wahala, gashi daman daren jiya ba wani bacin kirki ta yi ba dan tsoro da zulumi,  sai ajiyar zuciya take saukewa du ta goge hawayenta a jikin rigar wardugu.
A hankali wardugu yake kokarin kwontar da ita jikin kujerarta, Ayya ta zabga masa harara ta jinginar da Agaishat a jikinta tana kara tabata dan tabatarwa in ba suma ta yi ba.

Murmushi Wardugu ya yiwa mahaifiyarsa na alamun bada hakuri kafin ya jingina yana duba agogon hannunsa domin tafiar idan Allah ya yarda ba wata mai tsayi bace a jirgi tsakannin Agadez da Niamey.

Allah ya sauke su lafia, Wardugu da kansa ya tuka motar da ya je da ita ya ajiye aeroport ,
Bai zame ko.ina ba sai gidan Ayya.

Suna zuwa Ayya ta yi hamdallah ta kamo Hannun Bak'a wace ke kallo da baki da hanci da ido gaba daya

Fitar da ita ta yi ta ce" mu tafi yar gidan Ayyarta

A hankali ta fito itama kamar yanda Ayya ta koya mata ta bi bayan Ayya tana waiwayen Wardugu da ya fitar da kafarsa guda waje yana ta faman yamutsa gashin kansa, wayarsa ya

ciro yar karama ya dannawa abokinsa kira wato docter DOCTER MU.AZAM

Yana dagawa ya ce" Ranka ya dade oga *Wardugu Marahut*

Wardugu ya ja tsaki ya ce" Mu.azam ni za ka yiwa rashin mutunci? Yaushe ka fara karya?

Mu.azam ya yi shiru, ......tamkarma ya kashe kiran.

Wardugu ya duba ya ga kiran na tafia, ya kara karawa a kunnensa ya ce" kai!

Mu.azam ya sauke ajiyar zuciya ya ce" abokina, ka yi hakuri ka ji? Jikina ne ya tashi aman yau nake fita asibiti in sha Allah da na huta sai na kamo hanya.

Wardugu da ya gama jin abinda ya fada, cikin mutuwar jikin da bai san ko na meye ba ya ce" me ke damun ka ne harda kwonciya hopital? (HOSPITAL)

Mu.azam dake kallon karin ruwan da aka saka masa ya lumshe idannuwansa, jiki a mace ya ce" idan Allah ya kawo ni zan fada maka koma menene,

Wardugu ya sauke ajiyar zuciya, bai bashi amsa ba ya katse kiran ya rufo motar ya tayar dan ya samu ya karasa gidansa ya huta

..........................

TIMIYA

Rana ce, karfe biyu na rana ne, aman da dan lulumi kamar yanda garin ya saba,
A kasan innuwa suke zaune su uku suna yamutsa garin kwakwi da mai da yaji da manda (gishiri),
Fatimata ce mai kwadawar, Ayya na yiwa maryama susa a kanta

Mariama ce ta dago ta ce" Fatimata kar ki hade yajin nan duka ki ware min a robar nan kuma kar ki zuba mai iya shi din sai mandan ya isa kin ji?

Fatimata ta amsata da kai, Ayya dake mata susa kuwa a ranta take tambayar kanta Mariama ko ta daina cin yaji ne? Kai ina Mariama da yaji ai akoy amana.

Fatimata na gama warewa, Maryama ta mike ta dauki dankwalinta ta daura, ta dauki robar ta nufi wajen tulun Anna kwaya biyu dake cike da ruwa ta dauki guda ta dora saman kanta ta kama hanyar fita,
Kallonta suke da mamaki, Fatimata ta ce" Mariama ina zaki tafi kuma? Ki bari mu ci mana.

Mariama ta juyo ta ce" ki ware min nawa, zan je wajen Sofon nan na Agaishat na dubo shi ne,

Murmushin da Anna ta jima bata yi ba ta saki, sanyi ta ji a ranta daman tana ta tunaninsa halin da yake ciki mutumen kirki

Mariama oga kennan, Mariama ba daukan raina,
Bata zame ko.ina ba sai majalisar mahaifinta,
Tana zuwa ta mika masa hannu ba alamar wasa ta ce" kudi nake so Aba,

Bakinsa ya yatsina, Mariama fa ta fara isarsa da wannan ya bata ya batan, tunda ya karbi kudin aurenta take tatikarsa, idan ya nuna ba zai bada ba kuwa a ji su,
Rai bace ya saka hannunsa a aljihun rigarsa ya ciro dala dari ya mika mata a ransa yana adu.ar Allah ya sa ta karba kar ta ce ta yi mata kadan!

Karba ta yi ta maida tulunta da robar saman kanta ta juya ta nufi gidan mai goro....
Nan ta sayi goro har na dala Ashirin, ta sayi man zafi na ciwon jiki ta sayi yar tsintsiya, dauka ta yi ta nufi runfar baba Sofo.

Tana zuwa ta yi salama har sau biyu kafin take jiyo muryarsa can kasa yana amsawa;
Shiga ta yi tana wara idannuwanta dan ganni da kyau domin ta biyo rana idannuwan nata duhu suke ganni.

Yana kwonce fuskarsa na dubinta, ya takure ya kara yamutsewa da cazbaharsa yana ja kuwa,

Bata yi masa magana ba ta karasa inda ta ga tulun ta jawo ta fitar da shi ta wanke shi tas ta juye ruwan nan na cikin tulun Anna,

Ledojin da suka shihigo da kararuwa ta tatare ta fitar kafin take juyowa ta shiga share bukar inda baba sofo ya samu ya zauna yana binta da kallo da mamaki a kasan zuciyarsa; wannan ai yayar Agaishat ce, mai fadan nan, ikon Allah kawai yake fadi a kasan zuciyarsa.

Tana gamawa ta dauko robar abincin ta debo ruwa ta dawo ta darwaye hannunta ta zauna, ruwan nan ta kara yayafawa garin dan ya kara yin laushi sosai, tana yi bata ko kallonsa dan ta yi imanin ya tsareta da ido ne,............
Sai da ta kai bakinta ta ji idan mutun yace tsotsama zai yi tsaf zai tsotse abinsa ta dago da dubanta a hankali ta kai wajen baba Sofon dake kallonta ta ce"""

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

2️⃣1️⃣

Ta ce" ga abinci, ina magurjinka?

Hannunsa dake dan rawa ya saka ya fitar da magurjin ya mika mata yana kallonta dai, Mikewa ta yi ta wanko magurjin da goron, sannan ta dauko wata yar roba mai marfi da ta amso wajen mai siyar da goro ta kara darwayeta itama, ta dawo ta zauna ta saka yar farar leda a kasan abin gurzawar ta shiga gurza goron nan manya har uku;

Robar ya saka hannunsa ya janyo, bismillah ya yi har zai fara ci maganar Bak'a ta dawo masa inda take cewa < ka ringa wanke hannunka Sofo, ka ga jiki na iya daukan dati mai yawa banda ciki ka ji sofona? >

Dubansa ya kai wajen Mariama, a hankali ya ce" Mariama?

Dagowa ta yi tana dubansa bata amsa ba,

Baba tsoho ya ce" ina kwana,

Mariama ta kifta idannuwanta ba wani dar ta ce" Lafia, still tana kallonsa

Murmushi ya yi ya yi mata nuni da kofin ruwan dake hannunta sannan ya nuna mata hannayensa.

Tasowa ta yi ta karasa, dukawa ta yi ta kamo hannun nasa ta wanke masa da kanta sannan ta
```

kuma ciko kofin ta ajiye masa ta koma ta ci gaba da gurza goron ba tare da ta furta masa kalma daya ba.

A hankali baba ya fara cin garin nan, yana ci yana dan kallon yannayin Mariama, Mariama ikon Allah, Mariama mai albarka,
A hankali ya ce" nima ina jin rashinta sosai,

Mariama ta dago kanta ta zuba masa ido, murya a cinkushe ta ce" dan me ka rabata da danginta?

Sai da baba Tsoho ya hadiye wanda yake dan tsotsa a hankali ya dan kurbi ruwa ya ce" dan ta rayu cikin nutsuwa, ta samu inci kafin ta yi kaura zuwa lahira

Mariama ta ce" a wajen danginta, a kusa da mahaifiyarta ta fi samun inci Sofo!

Idannuwansa ya dan lumshe kafin yake budewa ya ce" ta yaya? Ta hanyar ta kare rayuwarta a bakin titi? Ita ko arzikin mazan zamanin ta kasa samu idan sun shigo gari da gari dan jar fatar yayanmu ne da gashi da kyau! Ba ruwansu da tarbiya, usuli , da halaya! Burinsu shine au samu iri mai kyau ....bayan su kansu idan suka kalli kansu a madubi zasu gane cewa a da ba haka Allah ya halice su ba, kwonci tashi kuma fatarsu sai ta dawo irin tawa idan Allah ya nufa masu tsayin rai ne,

Su da ka hadata da su din kana da tabacin a inda zasu kaita ba.a kyamar bakar fata? Mariama ta maido masa da amsa du a hargitse da yannayin bacin rai tamkar a lokacin ne za.a tafi da Bak'a,

Baba tsofo ya ce" birni da kike ji ana fadi, wata duniya ce a cikib duniyarmu mai cike da abubuwan al.ajabi,
A birni mutane basu da lokacin dan kina da fata baka ko dan kina da muni ya kasance du idan kin zo waje za.ana kwagirar ki ko a hantare ki! Sannan birnu cike take da mutanen da kwakwaluwarki ba zata iya hasaso maki ba, idan wani ya tsana wani zai so.......Mariama, ku yi hakuri.

Kanta ta mayar ta ci gaba da aikinta, tana gamawa ta ware masa wanda zai ci a lokacin sannan ta zuba masa sauran ta kai kusa da dardumarsa ta ajiye masa ta ajiye tsintsiyar a gefe, ta fitar da sauran canjin kudin ta ajiye saman dardumar ta dauki robar Anna da tulunta ta juya,
Har ta fita ta dawo ta duka kusa da shi kanta a kasa da yaren buzancinta ta ce" ta kasance abokiyar fadana, wace idan na tashi itace kanwata ita nake cin zali, takan kwaso kayana ta wanke min, idan dare ya yi can tsakiyar dare in na je juyawa sai in jita nanake da jikina, sai in rungumeta sosai a jikina ita da marigayiya, sai gashi lokaci guda a cikin kwana goma na rasa su! su duka biyu, ita wace ta rasu ina binta da adu.a baba  wace kuwa take raye inai mata adu.a sannan zan yi iya yina dan gannin na kyautatawa wa.inda take so take kyautatawa, haushinku nake ji ku duka har Annar!

Tana gama fada ta mike ta yi gaba abinta .

Baba sofo ya yi murmushi har cikin ransa ya ji dadin haka, ashe dai Mariama na tare da ikon allah, Mariama kennan Allah ya sa ranar da zaki hadu da yar uwarki ki bini da adu.a koda na mutu.

NIAMEY

Doguwar riga fara kar ce a jikinta mai siririn hannu aman tsayinta har kasa, irin mai laushin nan ce bata da kwaliya ko das ta tafi ne ta bi tsarin halitar jikinta,
Kamshi take bazawa du inda ta gota sai fai fuskarta ta cabe da hawaye tana biye da shi,
Murya a raunane ta ce" WARDUGU, nice ya dace na yi fushi irin yanda ka wulakantani, ka banzatar da ni a cikin duhu a garin da ba nawa ba , a garin da na je dominka, ka fice ka barni, sannan da safe da ka dawo ko ka kali motar da ka bar ni a ciki, ka yi tafiarka wajen mamanka ni kuwa ko oho! Shine dan na tafi zaka dauki zafi da ni haka?

Wardugu da ya gama saka mabalin rigarsa ya juyo ya kare mata kallo, a ransa ya ayyana """rainin hankali kennan, ta dawo daga tafiarta wace ta isa da kanta , shine aka sha karamar riga aka sha wankan turare aka zo ni ga maye ga mai jira aka kawo min na karbe ko?

Murmushi ya sakar mata kafin yake binta da wani mugun kallo irin na rainin nan, ya dauki yar karamar wayarsa ya bar ta chating din nan ya dauki ky din mota domin garin da hadari hadari baya son ruwa ya foke shi yau, ya fice ba tare da ya furta mata ci kanki ba;

Da kallo ta bi shi kafin take zama bakin bed din tana shafe idannuwanta, bakinta ta zumburo a fili ta furta" zaka sauko ne, haka kawai ka wani hada ni shakar numfashin wannan uwar taka harda wata karin malatin? Naki din wardugu! Na ki na shirya da mamanka duda baka tambaye ni ba na san hakan kake so sai dai ni a gaskiya ba zan iya jure mulkinta ba sai kaceatar wani sarki dan tana uwar General! ........hum

Wardugu bai zame ko.ina ba sai aeroport, yana zuwa ya ajiye motarsa ya shige ta wajen sojojin dake tsaron kofar bayan sun sara masa ya shige ciki ya haye wajen tarban baki

Bai kai ga karasawa ba ya ji muryarsa ya ce" mek (men),

Juyowa ya yi, arba ya yi da amininsa, abokinsa, Mu.azam zaune saman kujera, gilas a idannuwansa ya saka costume kafarsa sanye da takalmi sau ciki baki sai sheki take.....sai dai abinda bai masa ba irin yanda ya rame
Yana kallonsa har ya karaso inda Mu.azam ya mike tsaye yana murmushi ya bude hannayensa

irin ya zo ya rungume shi ,

Ido Wardugu ya zaro ya nuno shi da yatsa ya ce" kai ko?

Mu.azam ya saki dariya yana kara kure Wardugu da kallon yaushe rabo ya mika masa hannu ya ce" Asalamu alaika amini

Wardugu ya karbi musabaharsa yana mai furta" amen wa.alaika salam amini,

Murmushi suka yi kafin suke gaisuwar larabawa,
Wardugu ya yatsina fuska ya ce" kai dai ka cika naci, gaisuwar nan ta wani runguma ba wani sonta nake ba aman sai ka wani damki mutun kato da kai!

Mu.azam ya bushe da dariya yana biye da shi inda soja guda ya karbi jakar Mu.azam dake hannun wardugu ya shiga ja har wajen mota ya bude ya saka masu ya juya bakin aikinsa,

Wardugu ke jan motar yana dan kallon Mu.azam jifa jifa, a kasan zuciyarsa yana tare da damuwa na abubuwan da ya gani a tatare da Mu.azam wannan zuwan, ya rage magana, ya rage fara.a, ga dan cazbi a hannunsa yana dan dadanawa, ga rama da ya tafka ta mamaki sai dai fatarsa ta gyaru ta yi fresh aman ba alamun yana jin dadin rayuwa.....

Haka har suka karasa gidan Ayya wada rabonsa da gidan kwana hudu kennan tunda ya kawo su bai samu aiki ya barshi ya zo ba , aman ita Ayyar ta ue har wajen aikin ta amshi carte dinsa ta banki wai zasu je shopping ita da sabuwar yarta, ya yi murmushi da ya tuna irin kudin da suka kaso, Ayyarsa uwarsa Ayya manya.......

Zaune Ayya take saman kujera tana kallon yanda Agaishat ke dan turo baki tana kallon Ayyar da yannayin abin tausayi,
Daga ita dai gajeran wando da yar rigar da Ayya ta yi mata jan ido kafin ta yarda ta zauna da su dan ta shafa mata gomage a jikinta da fuskarta tamkar amarya, gefe hijab dinta ne baki dan kar kalar abin madarar ya bata hijab din Ayya ta dauko ko dan idan an yi baki, wani irin kulawa Ayya take baiwa Agaishat (Bak'a), kudi ta kashe na mamaki wajen siyen mayuka masu gyara fata ba canza kalar fata ba, sannan ta shiga kasuwa da kanta tare da Agaishat tana nununa mata abubuwa nasu na tubawa na gyaran jiki ta kwaso itacen magarya ta kwaso kayan gyaran jiki suka dawo gida, wata irin shakuwa ce ta shiga tsakannin Ayya da Agaishat, domin Ayya wayayiyar mace ce  ta yo anfani da irin yanda ta waye ta ja Agaishat a jiki tun tana tsoro tana baya baya har ya zamana sun shaku tana dora kanta saman cinyar Ayya ta yi baci ba tare da wani dar ba.

Yauma sun tashi da niyar yin gyaran jikin ne, Ayya ta dadaure mata gashinta da abin nan na saloon wanda idan an wanke kai ake sakawa a dadaure gashi da shi dan ya nanade ya bushe, ta kwaba abin gyaran jikin nan  ta samu ta shafa mata ta yi mata hayakin mai mugun zafi wanda

fuska kawai ake fitarwa, tana gamawa ta sakata ta yi wanka ta shafa mata na madarar nan suka zauna a fali sunna kallo aman ta hanata magana dan kar na fuskar ya saka fuskar ta yakune........

Mai gadi ne ya fara shigowa da jaka, Wardugu na biye da shi sai Mu.azam wa.inda shigowarsu ne ya ankarar da Ayya ta warci hijab din Agaishat ta ......

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

22

Da sauri Ayya ta samu ta rufa mata hijab din inda Bak'a ta yi mutuwar zaune a ranta tana ayana Ayya wayo daman sai da na fada maki Ayya ...........

Karasowa suka yi, Mu.azan na kallon inda aka rufe da hijab yana son sannin ko waye, Wardugu kuwa kallo daya ya yiwa wajen ya kawar da kai a ransa fadi yake" me Ayya ke son yiwa fatar nan da ta rine?

Da murna Ayya take kwalawa mai aikinta kira da ta zo ta dauke akwatin Mu.azam sannan ta kawo masa tarba,
```

Ayya ta tarbo shi tana murna ta kamo shi ta zaunar da shi sai murmushi take tana kallonsa ta ce" yarona, yaushe gamo?

Mu.azam dake jin wata nutsuwa na saukar masa ya dube duba irin na mahaifiya, a hankali ya duka kasa ya ce" Ayyana ina yini

Ayya ta kuma kamo shi ta tayar da shi tana kallonsa,  yannayinta ya fara canzawa ta kai hannunta wajen wuyansa ta ce" me ke damunka? Ya haka ka rame har haka? Ko dai ka je ka sakawa kanka ayuka ba hutu ne??

Dariya ya saki yana kallon  Ayya , kafin yake maida dubansa wajen Wardugu ya ce" freind Ayyana har yanzu akoy yannayin nan?

Wardugu ya yi dan murmushi yana kallon su,

Ayya ta yatsina fuska ta ce" ba wani nan, yanzu tashi ka je ka yi wanka ka fito zan fara yi maka dura ne tunda abin haka ne!

Yana dariya ya mike ya kalli Wardugu ya ce" mu je ko?

Wardugu ya gala masa harara ya ce" a matsayin matarka ko dan jagorarka?

Mu.azam ya yi murmusho yana ji a cikin ransa ya yi missing din abokinsa da mahaifiyar abokin nasa,
Juyawa ya yi ya nufi dakin da ake sauke shi wanda yake a matsayin nasa,

Ayya ce ta dubi wardugu, da idannuwanta ta yi masa nuni da ya tashi mana shima baya gannin mutun?

Wardugu ya daga kafadu ya ki tashin yama mayar da dubansa wajen tv inda ya dauki commande ya canza tasha ya kai Canal plus sport ya shiga kallon ball.

Ji take ta fara gumi , ga kuma ta kage a yannayin zaman nata, ba.a jima ba Mu.azam ya dawo daga wankan da ya tafi ya zu suka kara kasancewa mutun biyu maza kennan,

Ayya ta tashi da yannayin jin haushi ta dunguri kan Wardugu ta ce" ta yi maka kyau!

Wajen Agaishat ta karaso ta kamata ta mike kafarta ta yi mata tsami sosai, ta samu ta saka mata hijab din ta ce" je ki yi wanka  Agaishat ki sauko mu ci abinci .

Da toh ta amsa ta bi ta bayan kujerun ba tare da ta gaisar da su Wardugu ba,

Mu.azam da ayar tambaya ya kallo Ayya, bai yi nauyin baki ba ya ce" Ayya ina kika samo

wannan?

Ayya ta karasa kusa da su sosai ta zuba jus ta mika masa shima kamar yanda ta mikawa Wardugu ta ce" Me ke damunka tukunnan yarona??

Mu.azam ya shiga dan sosa bayan keyarsa, ya kallo wajen Wardugu, ya kuma kalli Ayya.

Haka kawai wardugu ya ji gabansa ya fadi, shima kure shi da kallon yake kafin ya ajiye yar wayar dake hannun nasa ya zuba masa ido,

Murmushin dai ya kara yi masu, ya ce" na yi rashin lafia ne Ayya, kuma yanzu alhamdulilah na samu sauki,

Ayya ta sauke ajiyar zuciya tana kallonsa ta ce" na tsorata da yannayinka, ka wani rame, ba komai haka ne idan jiki ya tabu sai a hankali aman yanzu ka zo kennan sai na ga yarona ya koma yanda yake da koma ya fi haka kafin ka bar gidannan,

Wardugu dake kallonsa ya shafa kansa shima kwata kwata bai yarda da maganar Mu.azam ba! Kai haba a irin yanda suka san juna Mu.azam ba zai layance masa ba

Mikewa ya yi ya nufi kofa da wayarsa a hannu inda suka bi shi da kallo,
Mu.azam ya ce" Ayya ya tafi fa kennan??

Ayya ta daga kafadunta ta dan yatsina fuska ta ce " ya gaishe su!

Mu.azam ya yi dariya yana kallonta, a ransa kuwa dadi yake ji yannayin, kai yana jin dadin zama da su, Wardugu rikitace, mahaifiyarsa ta iya zama da shi, ta kai ta kawo ne idan tama da bukatar ganninsa a wayarsa ya yi mata activen localization, du inda yake idan ta shiga nema za.a nuna mata kawai sai dai ya ganta kuma sam baya gigin kashewa doka ce!

Suna tsaka da tataunawa mai aikin Ayya ta shinfida ledar cin abinci ta kawo abincin ta ajiye, ta kawo kayan zubawa da na sha, ta kawo su jus na gida da Ayya ke yin abinta da kanta ta saka a frij du ta ajiye, Ayya ta umarci Mu.azam da ya sauko bara ta dubo yarta.....

Wardugu ya dawo, bayansa *ALHINAYET* kawarsa ce ke biye da shi,

Salama ta yi ta shigo dakin inda Ayya ta tsaya ta saki baki tana kallon Wardugu da Alhinayet din,

Alhinayett na zuwa ta shiga gaisar da Ayya cikin yannayin ladabi da mutunta mutun,

Ayya ta dan kebe baki, ta amsata ta juya dan dubo Bak'a

Mu.azam dake zaune ta juyo ta dafe habarta ta ce" su likitoci ne a garin namu???

Mu.azam ya sakar mata murmushi ya ce" lauya, lauya, lauya mai kunce mai laifi , zamani lauya iko, lauya mai saka kato ya duka,

Kai ta dafe ta ce" wace ni, rufani ka sayani, ai ba dan an san ni aminiyar *Aboki* bace da an fige ni a Niger!

Mu.azam ya ce" kai ai rigimama ta san waye *Oga*

Wardugu ya girgiza kai yana zama ya ce" *ALHIN* ki zauna mu hau wannan abubuwan kafin ku ci gaba da kirar da kuka koya!

Alhinayettt ta je kusa da Wardugu ta zauna tana fadin" General ka duba lamarin nan je ten conjure................(plz)

Wardugu ya kaleta zai yi magana sai ga Ayya ta dawo da Agaishat,
Doguwar riga simple irin ta zaman gida ce Ayya ta bata, bayan ta saka ayya ta bata Dan kwalin rigar nufin ta yane kanta sai dai suka hau rigima kan aa dan Allah ta bata hijab,

Gannin sai su bata lokaci ne ya saka Ayyar bata hijab ta zumbula suka sauko,

Sai a lokacin Agaishat ta duka ta ce" ina yinin ku,

Alhinayettt da Mu.azam ne suka amsa inda Wardugu ya kebe bakinsa bai wani amsa ba aman yana yi mata kallon tsaf, a ransa yake ayyana black, but ko a baki *BUZU MAI KYAU NE* 😂😂😂😂🤪😜😜😜😜😜😜😜😜😜🤪🤪🤪 na fada a zo a dake ni🧐🧐🧐🧐🧐🧐🧐🧐🧐🧐🧐🧐🧐

May be 23......zuwa dare in sha allah, idan comment ya birge ni😄😁😆😅😂🤣

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

2️⃣3️⃣

Waje Ayya ta samu ta zauna , nan Agaishat ta je kusa da ita sosai itama ta zauna ya kasance an saka baban plateau din a tsakiya,

Ayya ce ta bude inda abincin yake, tuwon tsaki ne da miyar kubewa wace aka yita da naman shanu ta sha dadawa da kayan miya 😋..ga kuma man shanu na kirki a gefe,
Sai su fruits da aka hi masu yanka mai kyau aka sasaka cikin plat plat, sai jus da ruwa,

A hankali Ayya ta dauko abincin, Agaishat ta dauko abin zubawa,
Cikin wannan banban plateau din Ayya ta zuba abincin ta daidaita miyar, ka.ida ne in dai ka zo gidan Ayya daidai cin abinci bata raba assiete, sai dai a hadu a ci a abu guda .......

Bayan ta zuba ta kare Agaishat ta kawo abin wanoe hannu da kuma cokula a wata yar roba,

Gaba dayansu cokulan suka dauka banda Agaishat da Ayya , hannayensu suka wanke ....

Ayya ce ta fara saka hannunta, sai Wardugu, sai Mu.azam, sai Alhinayettt, sannan Agaishat dake karamar cikinsu, hakane gidan Ayya baba ke fara saka hannu cikin kwanon cin abinci sannan yaro ke rike kwanon dan kar ya ringa yawo, ba.a magana idan ana cin abinci, ba.a dane danen waya, ba.a wani kale kale sai an gama, sannan bata yarda ana tsaka da cin abinci ana shan ruwa ko jus, sai an gama ake sha,   sannan ana cin abinci daidai ne ba.a matsawa ciki a yi mugun koshi, lamarin gidan Ayya sai yayanta (🤣),

Abincin nan ake ci cikin nutsuwa, Alhinayettt ta kure Agaishat da kallo, sam batai mata kama da tubawa ba, sannan ba bahausa bace ko daya  duda hijabin dake kanta gaban goshinta lufluf yake kwonce da gashi, girartama wani irin gazar gazar da ita, du bakinta lebenta haske ne da shi tas tas, ga girar ido ga manyan idannu, wannan cikin biyu daya ce ko bakar balaraba ko bakar buzuwa!
```

Alhinayettt dai ba wani yawan zuwa gidan Ayya ba take ba, sukan hadunsu ne da wardugu a wani wajen, yanzuma zuwa ta yi da rigimarsu ta kansu wace ta zo su yi kan irin yanda ake cece ku ce a gari na matarsama idan ta cika dare kwanan cel take bare wani banza!

Alhinayettt kwata kwata ta manta zancen ba.a magana idan ana cin abinci gidan Ayya  dan haka ta kali Agaishat da kyau, haka kawai ta yi niyar yi mata magana da buzanci dan ta gaskata zatonta,
*ABZIN?* , ta fada tana kallon agaishat,

Agaishat da ta hadiye abinci ta kaleta itama, itama ta so ta ayanna hakan cewa wannan buzuwa ce, gannin yannayinta sai  dai bata fadi ba dan ba wajen fadin bane,
Ai kuwa Agaishat ta washe baki itama da yaren buzancin ta maida mata cewa" eh , ke fa??

Alhinayettt zata maida mata maganar Wardugu ya tsimki hannunta na dama dake kusa da shi, sannan ya zabgawa Agaishat wata muguwar harara wace ta sakata sada kanta hannunta na rawa rawa,

Ayya yatsina fuska ta yi bata yi magana ba,
Sai da aka gama mai aiki ta shiga kwashewa, Agaishat na tayata kaiwa komai wajensa ta dawo ta zauna kasa kusa da kafar Ayya,

Wardugu ne ke kallon wayar Alhinayet tana nuna masa hotunnan birthday dinta da ta yi baya nan yana dan murmushi kasa kasa ya ce" Alhinayettt , ina tunanin kin girma ashe dai na daina tunanin nan?

Alhinayettt ta yi dariya ta dora hannunta saman nasa ta ce" na baka ka sha? (Irin su taba zata bashi wani labarin)

Ai kuwa Wardugu ya dan cafke hannunta yana sauraronta, inda ya bata hankalinsa suna ta hirar su,

Ayya ce ta dan ja tsaki, ta girgiza kai tana kallon Mu.azam ta ce" kana ji? Zamani ya zo mana da abubuwan mamaki, sai ka ga mace na tafawa da namiji, tana raba jikinta da nasa wai a zuwan mutunci kawarsa, !

Mu.azam ya zaro ido yana kallon Ayya, a fili kuwa ya furta" Lah, yana dafe bakinsa,

Wardugu da ya gama jin komai ya saki murmushi yana kallon Ayya, ya ce" Ayya, qna abota mace da namiji, abota sak ba wani soyaya ba kuwa,

Ayya ta juyo bangaren su a takaice , daman jira take wani abin ya hada su ta ce" wardugu ba abota ba dai yayan awaki! Nace yayan awaki, Ke yanzu Alhinayettt kike ko wa? Aman ke marainiya ce ko? Ina nufin mahaifiyarki ta rasu?

Alhinayettt dake kallon Ayya a dan tsorace ta ce" Aa Ayya,

Ayya ta dafe habarta ta ce" Toh abin mamaki, aman ita baku rainata kamar yanda kuka rainani ba ko? Ina nufin Wardugu baya zuwa gidan ku a matsayin aboki sai saurayi?

A tare suka kalli juna Alhinayettt da Wardugu, suka maida dubansu wajen Ayya,

Ayya ta ce" to in ba haka ba, ya za.a yi ni ina mahaifiyarki , kato ya ringa zuwa wajenki a matsayin aboki kuma na zuba ido yarinya kin kai kin kawo min a gida?

Wardugu ya shiga gyada kai yana kallon mahaifiyarsa, ta jima tana son aikata wannan aika aikar wa zumuncinsa da Alhinayettt, yau dai ta yi hankalinta sai ya kwonta kuma ko?

Ayya kamar zugata ake sai magangannunta take son ranta karshe ta ce" to ni ba tsohuwar banza bace, in sonta kake ka fito a mutun ka fada ku daina boyewa Allah kadai ya san tsakanin ku! Dan haka tun wuri a fasa daukana a wata marar ilimi ana ce min wai kawa! Aa abokiyar tagwaitakarka ce Wardugu!

Wardugu kallon Ayya kawai yake, inda Alhinayettt ta dan sada kanta kasa, a ranta ayannawa take ita bata ga laifin zumunci da suke da Wardugu ba, walahi da soyaya suke da ba haka ba, kwata kwata ba wani zance wai shi soyaya tsakaninsu, haka kawai Allah ya hada jininsu suke mutunci, Wardugu bashi da shamaki a gidan su, hakama saurayinta wanda zasu yi aure suna mutunci da Wardugu, aman haka ne itama kakarta ta sakawa zumuncinsu ido har sun mayar da ita tamkar mahaukaciya domin idan sun ga zata fice sai su shiga magana kasa kasa da yaren french ai kuwa ta kama zage zage tana fadin ita za.a munafinta? Toh gashi itama maman Wardugu kallon masu soyaya take masu bayan ita koda bindiga ba zata iya soyaya da wardugu ba domin ta san waye shi, Wardugu dan yana son ki ba zai hana ya yi maki dukan mutuwa ba, dan yana son ki baki fi hukunci a wajensa a gaban koma waye ba, hum soyayama da wardugu ai tashin hankali ce, ita mai ya kaita? Ta fi son namiji marar rigima mai bata damar ta yi rayuwarta cikin aminci........

Wardugu dake kallon Ayya tar, ya maida dubansa wajen Mu.azam ya ga sai gumtse dariya yake,
Kansa ya girgiza ya maido dubansa wajen Ayya, da hannunsa na dama ya daga ya sara mata, sannan ya yi mata nuni da ta ci wasanfa , ta more abinta,
Hannunsa na hagu ya mikawa Alhinayettt ta mike itama ya ja hannunta tana waiwaye tana so ta yi hira da agaishat aman ya jata kiiii sukai waje

Kusan motarta suka tsaya,
Alhinayettt bata bi ta kan fadan Ayya ba, bata nuna damuwarta ko a fuska ba, ta ce" Wardugu, rigingimunka sun isheni haka, ya isheka malan!

Wardugu ya shiga gyada kai yana kallonta bai bata amsa ba,
Ta ci gaba da maga domin ta san ba amsar zai bata ba, ta ce" ta ya zaka saka Walyn kwana a cel? Wardugu ina jin zafi idan na ji ana fadin baka da sasauci, baka wasa, baka sulhu, Wardugu matarka ce fa? Ya kake so mutane su fasaraka??

Wardugu ya tsura mata ido kawai,
Ta ci gaba murya a sanyaye" ka daina Wardugu, ina so idan na zo waje na tarda ana fadin alkhairi a kanka, ina so idan ana maganarka ta kasance ana yabonka Wardugu, ka ringa sasauci freind,

Wardugu ya yi mata dan murmushi ya miko hannunsa ya dungure mata kanta bai ce mata komai ba,

Alhinayettt ta ce" Wardugu ina kula samu buzuwa??

Wardugu ya yatsina fuska ya ce" hum, Ayya ce ta daukota wai ta yi y'a,

Alhinayettt ta ce" yarinyar ce ta birge ni, irin yanda tana buzuwa , bakar buzuwa aman bata bata bakinta ta hanyar shafe shafe ba, ina son mutun haka walahi.....
Wardugu ya daga kafada ya ce" daga kauye, can cikin kauyen kauye fa ta fito, inama ta ga man bale ta shafa? Allah dai ya sa idan ta dan waye ta zama dan kauye ya fi na birni shegantaka....

Alhinayettt ta ce " sai dai idan ba tare da Ayya take ba, Ayya ce zata wani bari haka ya faru? Yarinyar ce innocente,   dan Allah ka hada ni da ita mu zama kawaye,

Wardugu ya waro ido, a fili ya furta" kawaye? Ki kirani aboki kuma ki yi kawance da wannan? Aa!

Alhinayettt ta yi murmushi tana kai masa dan dukan wasa ta ce" ina son ta zama kanwata ne Wardugu, ina son na kara nuna mata shafe shafe karma ta saka kanta, sannan na kara wayar da ita......

Kafadunsa ya daga irin ita ta gano, kafin yake bude mata motar ya yi mata nuno da ta shiga

Dariya ta yi ta shiga , ta kunna wato dai ta ishe shi da magana ko?

Hannu ta daga masa, ya yi mata nuni da sai ya zo , ta tayar da dankareriyar motarta ta kama hanyar makarantar kannenta dan ta dauko su ta mayar da su gida

Komawa Wardugu ya yi, yana shiga ya tarar da su sai labari suke suna dariya abinsu, Mu.azam kuwa ya kasance du motsi sai ya kali Agaishat dake zaune tana kallon Tv kuri, ita har yanzu mamaki take mutane a cikin wannan allon suna ta magangannu suna komai abinsu, har bayan take lekawa wai ko zata gansu ta nan ta sha yiwa Ayya tambayar kuma yanzu idan suka fito fa?

Yanzunma Ayya ta kuna mata wakokin dandali, kalo take tana ta sakin murmushi kumatunta na lotsawa dimple har biyu a fuskarta, wani wajen sai ta rufe fuska idan namiji ya fara rawa, sosai take dan gane hausar da suke tana kara koya ta nan, shi kuwa abin na birge shi, sannan ya yiwa Ayya tambayar wacece ita? Da french, ayyarma ta shiga kora masa bayanin komai.....ya sha mamaki, ya ji wani lamari a tare da yarinyar, yana son inganta rayuwarta......

Wannan kennan.

Wardugu na zuwa ya ce" tashi mu je,

Mu.azam ya mike ya bi bayansa suka nufi dakin Mu.azam din , Ayya ta yatsina fuska a ranta ta ayanna mai yiwuwa ya yi fushi🤣.

Suna shiga Wardugu ya ce" c'est bon, maintenant tu me dit la verité sur ce qui t'arrive ( ya isa, yanzu sai ka fada min abinda ke damunka!)

Mu.azam ya tsare shi da kallo, a hankali ya zauna saman kujera yana kallon Wardugu,

Wardugu ya karaso ya zauna shima, ya ce" ka san dai kana iya yiwa kowa karya banda ni! So ka fada min tun kafin na hasala Mu.azam, wata irin cuta ce wannan wanda baka taba yi a gabana ba ta zugeka haka? Me ya samu kasan gashinka ? Kana tunanin ban lura ba? To gashinan kasan gashinka a aske! Sai ka janyo sauran ka rufe, du ka zama wani iri? Ka duba fa ka gani wandon vest ne a jikinka ka dauko riga rose (pink) ka saka sai kace mace? Hannunka ba agogo, yannayinka na nuna kama tare da damuwar da ta fi karfin furucinka, ina hawa aiki karfe goma na dare, ka fada mani na juya!

Mu.azan da wata irin murya ya ce" Cancer du cerveau  ke damuna..... (cancer ta kai)

Wani irin tsam Wardugu ya yi, ya kaste maganarsa a lokacin da bai shirya ba,

Zurbat ya mike yana duban Mu.azam, hannayensa duka biyu ya saka ya dafe kansa, baya baya yake ja ya......

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na          *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

2️⃣4️⃣

Wani irin tsam Wardugu ya yi ya katse maganarsa a lokacin da bai shirya ba,

Zurbat ya mike, duban Mu.azam yake da wani irin kallo, hannayensa duka biyu ya kai saman kansa ya shiga yamutsa gashin kansa , baya baya ya shiga yi da kafafuwansa, bai fi taku hudu ba ya tsaya ya juya ya juyo, hanunsa ya jimke ya daki dayan da shi,
A hargitse ya dawo wajen Mu.azam, so yake ya zauna aman ya kasa...... murya a cinkushe ya ce" yaushe, yaushe? Yaushe ka sani? Ya aka yi ka sani?????

Mu.azam ya mike yana dan sakar masa murmushi yana kokarin ganin ya saka shi ya dan nutsu aman ya kasa kama shi, dan haka ya tsaya yana kallonsa ya ce" Wardugu, har na kai wajen da gashina baya zama fa, ya jima a jikina ciwon ....nima ina gannin alamu a matsayina na likita sai dai ina turewa na ki maida hankali, ya kai ni sai na suma na yi awani a sume, na daina shiga tiyata ba yau ba, ina zuwa asibiti ne dan kar imanina ya yi rauni, ina zuwa ne dan haduwa da wa.inda suka fi ni damuwa, ina yi mana adu.a a tare, Wardugu idan na jima a gabannan na kara shekara hudu a duniya,...

"C'est faut!,(KARYA NE!)  Wardugu ya fada  tun karfi yana nuno Mu.azam da yatsarsa,
Taku ya yi wajensa ya ce" idan kai ka fada, idanma wani sakaran likitan ya fada na fada karya kuke, karya ne Mu.azam, ku baku isa ku fadi abinda Allah ya boye ba, ba wani mahalukin da ya san ranar mutuwarsa , mutuwa bata shawara, bata fadi sai an ganta, mutuwa na zuwarwa bawa a lokacin da bai sani ba, sannan a lokacin da bai shirya ba domin a kulun bawa baya cikin shirinta,

Wardugu ya yi shiru, gaba daya ji yake jikinsa ba karfi, a hankali ya kai kasa ya zauna nan kasa, waje guda ya tsurawa ido kafin ya ci gaba da fadin" sannan Allah kadai ya san gawar fari, ba wai dan wane bashi da lafia wane lafiarsa kalau za.a ce sai marar lafiar nan ya rigayi mai lafia
```

rasuwa,

Mu.azam da ya karaso , a hanakli ya duka ya dora hannayensa saman na Wardugu, murya a raunane ya ce" ban taba tunanin wani abin zai girgizaka haka ba Wardugu, menene a ciki? Ko dan abin ya shafeka ne baka so ka ji? Wardugu ka yi hakuri, ka daina tayar da hankalinka kan maganar nan, nima na fada maka ne dan na ji sanyi sannan na samu wanda ya san ciwona, Wardugu ka....

Bai tsamaci lamarin ba, sai jinsa ya yi jikin Wardugu, Wardugu da dan ya tsokane shi yake ce masa sai sun yi gaisiwar larabawa, yau gashi da kansa ya rungume shi,

Murya a cunkushe wardugu ya ce" bana so  bana so.....
Kasa karasawa ya yi kuma ya saki Mu.azam ya mike ya fice da wani irin sauri .......

A hankali Mu.azam ya hade kansa da gwuiwarsa, , tabas mutuwa Aya ce, duk mai rai mamaci ne, tabas ba karamar ni.ima bane da Allah ya boyewa bayi ranar mutuwarsu, shi gashi, hasashe ne aka yi, likitoci sukai a kansa, rayuwar turai da za.a fada maka komai kwaro kwaro ne, sun kiyasta lokacin da suke gani zai kai a raye a doron kasa sun fada masa, wai basu fada masa rana da lokaci bama aman gashi du ya firgice ya fice a hayacinsa,
Idannuwansa ya lumshe yana jin saukar zazafan hawayensa, zuciyarsa ce ta ci gaba da fada masa" ka zo kasar nan je dan ka kara ninninka ibadunka, ka kara yawaita sadaka da aikata abubuwan alkhairi, ka zo kasar nan ne dan ka samu ka raya sunnar ma.aiki idan Allah ya nufeka, mutuwa kowa yi zai yi Mu.azam, ka daina karaya ka yi hakuri har Allah ya yi ikonsa a kanka,

Wayarsa ce ta dauki kuka  ya kai dubansa wajen wayar ya mike daga tsugunnin nan ya daukota ya daga,

Docter me ka yi kennan? Na zo wajen aiki na tarar da takardar barin aikin ka? Saboda ni kake son yin nesa da aikinka ko saboda na fada maka ka yi hakuri a yi maka aikin nan? ......

Kansa ya shafa yana sauraronta, masoyiyarsa wace ke nuna masa kauna, tana son Mu.azam tamkar nama daya na cikin miya, tana son kasancewa da shi, labarin rashin lafiarsa ya gigitata har itama ta kwonta, nan ne ta yi ta fadi tashi har ta gano ana iya yi masa aiki a cire wajen, aman aikin ne keda hatsari sosai, yana iya samun tabuwar tunaninsa, ko ya kasance ya shiga coma wace shigekan daga ita ba zai tashi ba, ko idan Allah ya aminta ya yi jinya sumul ya samu sauki aman shi ya kara kai da kasa ba zai harda a wani buda kansa ba a dawo kuna ba wani succes,

MU.azam ya ce" Aisha,

Aisha ta ce" ka dawo na roke ka, ka dawo tun kafin lokacin a iya yi maka aiki ya shige,

Ki yi hakuri ki daina kirana Aisha, Mu.azam ya fada da sanyin murya, ya ci gaba da fadin" nawa kuka yiwa aikin? Nawa suka fita? Karshe dai du yawanci daga dakin aikin za.a fitar da su basu san inda kansu yake ba, zasu dawo kulun a jone da inji yana taimaka masu wajen numfashi, da na.urori masu basu abinci, da masu jan fitsari da masu karban kashin su, zasu dauki lokaci a wannan yannayin har ya kasance ko a cire masu na.urorin ko dare daya su tsaya sun daina aiki, su basu dauki kadara suka yi ta ibada suna shinfida a makwoncinsu na gaskiya ba, su basu san a inda suke tsakannin duniya da lahira ba, Aisha, Allah ya dora mani, ba zan kai labari ba! Ki yi hakuri......

Yana gama fadar haka ya katse kiran,

Docter Aisha dake kai kawo tsakannin dakinta da falonta ta dafe kai ta fashe da kuka, yar balaraba kyakyawa da ita, a fili ta furta" innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, Mu.azam, in sha Allah zaka warke, sai mun rayu da kai Mu.azam.......
(😔😔😔😔😔😔)

Bayan sati uku

Ayya ce zaune tana nunawa Agaishat yanda ake gyara lale ja domin tana son kunsa mata ne, Bayan ta tankade shi lukui ta kawo mahanabiya ta zuba masa sannan ta zuba dan madaidaicin ruwa ta kwabe shi sosai ya yi shar da shi ta zuba dan ruwa gefe ta ajiye tana kallon Agaishat ta ce" yi ki wanke kafar mana Agaishat, kin ga yayanki Mu.azam ya ce zaku fita ku zaga gari , ni kuwa na fi so idan mun gama kunshin nan sai ku tafi....

Agaishat ta yi sauri ta shiga darwaye kafar nata ta cire ta dauke ruwan ta kai ta zubar ta dawo ta dauki abin goge kafar ta gogoge ruwan kafin take zama ta tankwashe kafafiwanta Ayya ta shiga daura mata iskwace tana fadin"ki lura dan gobe ki daura abinki kin ji Yar Ayya,

Agaishat ta gyada kai tana murmushi, a kowani lokaci a kowani yannayi ta tsinci kanta tunda ta sauke kafarta a gidan Ayya sai iyayenta da yan uwanta da baba sofo sun fado a ranta, bale yanzu Wardugu kansa da yake yawan hararata a farkp ya daina, shi dai baya shiga lamarinta aman baya hana wani shiga, Alhinayettt ma tana lekowa wani sa.in idan Wardugu na gidan su sha hira da yaren buzanci domin tana jin dadin jin yaren raurau ana hira da ita ba wani kyama, sosai Alhinayettt ke dan gwada mata wasu abubuwan, da hikima take nuna mata wasu yan al.adun yan birni sannan Mu.azam na mugumugun sakata a jiki, yana sakar mata fuska fiye da tunanin mai karatu,  idan ta kali kayayakinta, suturun da suke malakinta a yanzu, sai ta ji hawaye na neman zubo mata, tunaninta me yan uwanta suke sakawa a yanzu? Wani hali suke ciki? Jiya i yau ne ki Baba ya canza halayensa?
Sai dai takan bi su da adu.a kawai, itace kadai abinda take iya yi masu a yanzu, kuma tanaiwa iyayen rikonta adu.ar gamawa da duniya lafia, ba.a wani sakata makarantar boko ba domin shekarunta sun tafi shekara goma sha takwas har ta kusa cike sha tara, aman a gida Ayya na koya mata abinda ya sawaka sai karatun islamiya da ta kara zurfafawa sosai tana kara neman

ilimin adininta.

Ayya na gama daura mata kunshin ta mike tana leka windows, mamaki take irin yanda yanzu wardugu ya ajiye kafarsa a gidan, duda ta san amininsa na nan dole za yana yawan zuwa aman abin na bata mamaki, bai jima da fita ba fa aman har ya dawo, sannan yanzu basa fada da mu.azam akasin da da sai ta shiga tsakani ko ta gindaya masa doka kan Mu.azam din kafin yake barinsa ya huta, yanzu kuwa bini bini ya shigo ya haye wajen Mu.azam su yi ta hirar da ita bata san ko ta meye ba, yanzun ma tsaye suke su uku, da yar jajar nan Alhinayettt sai hira suke suna dariya,
Rufe windows din ta yi ta juya ta fice ta bar Agaishat na zaune tana jira ya bushe ta wanke kamar yanda Ayya ta fada

Bayan kunshin Agaishat ya bushe, ta mike ta saka takalminta silifas ta yi bayi,
Wanke kunshin ta yi, jan kunshi yayi jajajir, ga mamakinta ya fito sosai a fatarta har ya haska mata  fatar kafar da hanayen,
Da sha.awa take kallon kunshin ya yi kyau a idannuwanta,
Ta dauki lokaci a bayi domin sai da rmta yi wanka ta fito ta je bakin madubi tana goge gaban goshinta inda ruwa ya taba kannanuwan kitson da Ayya ta dage akai mata wa.inda sai warwarewa suke dan kansu ,

Turarukanta ta zauna ta shafa na madara masu sanyin kanshi, ta shafa mai kadan a jikinta,
Kwali ta dauka tana adu.a domin har yanzu ta kasa sabawa da saka shi da dadi sai ta yi ta fama, bayan ta saka ta caje girarta, ta dauki wani jan baki mai ruwan lebe wanda Ayya ta fada mata kadan za tana shafawa a lebenta na kasa,
Hakan kuwa ta yi ta shafa kadan kafin take tsurawa madubin ido, tunda ta zo garin nan ka.ida ne a wuni sai Ayya ta tsareta yin wanka sau biyu wataran har sau uku, idan kuwa ta yi wanka dole ne ta zauna ta kula da du wata gaba ta jikinta, tun tana kallon haka a wani iri har ya kasance idan bata yin ba itama bata jin dadi, sannan ta yarda da mutun sai da gyara, wannan mugun bakin da take gani a jikinta a ruwan wanka ta ga yana sauka daga jikinta, tsabar rashin wanka na kirki ne da kuma karin bakin turkidi(tufafin buzaye), yanzu fatarta ta kasance bak'a mai haske, irin bakin nan mai kyau mai birgewa, ga gyara yana kara samu yau da kulun, har santsi santsi take ji fatar tata ta fara yi mata,

Mikewa ta yi dai ta shiga fitar da riga da siket din da Ayya ta rataya jikin abin turaren wuta tun da safe kan su zata saka,
Wani ni.imtacen kanshi suke na turaren tubawa,
A hankali ta saka slipe (pant) dinta, an ta kasa saka breziyar domin har yanzu bata iya aiki da ita ba, kai ita bata ma sonta ne ,
Kayan nan ta saka sket da riga, sun amsheta sun mata cicif a jikinta dinkin zamani ,
Tsaye take tana kallon lufayar da Ayya ta bata, ta nuna mata ta koya mata daurawa sai dai bata iya ba har yanzu (daura lufaya sai a slow),

Gashin kanta kawai ta sakawa ribom ta saka yar bakar hular da Ayya ta hada mata da kayan ta

Iuluba Lufayar ta fice da takalman a hannayenta dan Ayya ta nada mata da kanta,

Alhinayettt karfe nawa ne zaki je wajen auren? ,
Agaishat ta tsinci muryar Wardugu da bata da siri tana tambayar Alhinayettt dake zaune tsakiyarsu Ayya kuwa na wajen table din diner tana gyara shirin da mai aikinta ta yi mata domin bai mata ba!

A hankali ta sauko, ta karaso tana hangen yanda Mu.azan ke sakar mata murmushi,
Karasawa ta yi sosai kafin take gaisar da su a jimila ta hanyar fadin" Ina kwanan ku,

Alhinayett ta amsata tana yaba kunshinta da harshen buzanci wanda Wardugu ya ji me take fada ya yatsina fuskarsa yana girgiza kai.

Mu.azam ya kai dubansa wajen agogo ya maido wajenta ya ce" Agaishana, yanzu ne safiya, duba karanto min karfe nawa ne? Na ga ko kin gane yanda na koya maki,

Ai kuwa ta juya wajen agogo ta shiga nunawa da hannayenta tana irgawa tana faman fada masa lokacin Ayya ta karaso ta kama hannunta ta ce" a bar y'a na gama shiryata, ita da bata yi safiyar zuwa wajen namiji ba ai ba lale ne ta gane safiya ce ko rana ko yama ! Ayya ta karasa tana murguda baki irin na tsofafin nan masu rigima ta kai dubanta kan Alhinayettt, wato dai da Alhinayettt ake,

Wardugu ya mike ya karasa wajen Ayya, ya kasance sun saka Ayya a tsakiya shi da Agaishat wace hannunta ke cikin na Ayya tana so ta warware mata Lufayar nan ta nada mata,

Sosai ya so rage muryarsa, sosai ya yo yaki da muryarsa ya ce" kin ce baki tsufa ba? Da yaren tubanci,

Juyowa ta yi ta murguda masa baki ta ce" eh da saurana,

Wani tsadaden murmushi ya sakar mata yana dan juya kansa, ya kamo dayan hannun nata cikin nasa ya ce" kin san du duniya ba a yi ba ba kuma za.a yi ba macen da zan so kamar mahaifiyata ko?

Ta kawar da kanta bata bashi amsa ba, ya ce" in dai kina irin abin nan sai in fara tunanin na bani Ayyana ta fara tsufa,

Hannunta ta warce ta dungure kansa kamar yanda takan yi idan ya hasalata ta ce" ni ba wani tsufa ko rashin tsufa bane, ina jin haushin irin yanda kuka dauki al.adar yahudawa kuka mayar naku, tun da safe take gidan nan

Wardugu ya ce" Mu.azam ya gayace mu baki daya mu raka shi ya ga gari,

Ayya ta yi tsam tana kallon sa, Mu.azam ya gayace ku?

Wardugu ya gyada mata kai,
Hannunta ta kai wajen wuyansa ta taba wai ta ji da zafi,
Kalau ta ji wuyansa, ta saki ta dafe habarta da mamaki, ta ce" yaushe mage da bera suka fara shan innuwa daya har shawararsu ta fara zama daya? Me ke damunku? Shirin naku kuma ya fara bani tsoro,

Wardugu ya saki hannun nata yana murmushi ya karasa ya ce" ku fice mu je ta fito idan an gama shiryata, kai yama zaka hada mana fita da karamar yarinya? Yanzu fa dole ka saka mutun ya rike bakinsa gaban yara!

Mu.azam dake biye da shi yana dariya  Alhinayettt kuwa da naci ta zauna sai da Ayya ta nadawa Agaishat ta saka takalminta plat, suka kamo hanya Agaishat ta mugun yi mata kyau a idannuwanta, sai ta fito kamar wata chocolate color din balaraba, ta hade ta yi wani sihirtacen kyau

Haka suka karaso suka bude bayan suma suka shiga, ita dai Agaishat kanta a kasa, irin kalon da mu.azam ke jifanta da shi ke bata kunya, sai ta rasa me ya sa yake irin kallon nan,?

Alhinayettt ta mika hannu ta dauko wayar Wardugu ta dawo ta shiga nunawa Agaishat hotuna suna dariya,

Wardugu ya ce" ina muka nufa oga?

Mu.azam ya ce" ka kai mu Bienvenu a Wardugu place,

Wardugu ya taka wani wawan birki, ya kalo shi ya ce" wasa kake?

Mu.azam ya ce " aa can nake son zuwa, yana mai hade rai shima ya mayar da dubansa gefen titi (BIENVENU a Wardugu place, waje ne da mahifin Wardugu ya buda da sunnansa tun suna tare suna ganewa juna kafin abinda ya hada su ya hada su su bar shi da mumunar rantsuwa a tsakani, an ce yanzu matarsa da ya aura take kula da wajen wai ita Aisata ,......mugun tsama ne tsakanin wannan family masu matukar kaunar junansu a da, kuma har yanzu da daya kwal da ya malaka dai Warsugun ne..........).....

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na          *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

2️⃣5️⃣

Wardugu da ya mayar da dubansa gefen titi ya kai hannunsa yana shafa kansa a hankali, tabas Mu.azam yana tako shi kwanakin nan, in sha Allah shi kuwa zai yi iya yinsa dan gannin ya faranta masa...

Motar ya tayar ya dauki hanya, tafiya ce suka yi mai dan tsayi kafin suke karasowa wajen, Daga mu.azam har Alhinayettt sun yi mamakin yanda ya yarda ya zo wajen,
Mu.azam ya ji wani girman Wardugu ya karu a idannuwansa , kaunar aminin nasa ya linku a zuciyarsa, adu.a ya yi masa da fatan alkhairi ...

Sai dai me, suna shiga da motar suka fara hango wasu abubuwa,
Yan mata ne da muguwar shiga, shiga ta kananun kaya sosai, da samari suna kai kawo suna dan badalar su,

Gaba dayansu kalon wajen suke da mamaki, Wardugu ya jinjina kansa a ransa ya ayanna,
*Abinda ka zabarwa kanka kennan Uban Wardugu!*

Mu.azam ya yi tsam ya ce" Wardugu , ko mu juya dai? Domin wajen shi har ya fara bashi tsoro irin yanda ake shiga ana fita ana wasu abubuwan,

Wardugu ya juyo bangarensa, ya saki dan murmushi ya ce" ai mun zo  sai kun shiga,

Ya bude ya fice bayan ya dauki hularsa casquette dan baya so kowa ya gane ko waye shi,

Jiki a sanyaye suke bin bayansa har ya karbi tikect din su hudu wanda zai basu damar leka
```

ko.ina sannan su ci abinda ransu ke so, du tiket daya jika talatin ne, a wajen ba abinda babu, a da da aka bude shi an bude shi ne dan yara da iyayensu ranar weekend kawai ake bude shi, sannan ka.ida ne sai ka zo da mahaifiyarka ko da mahaifinka zaka shiga, ba.a barin budurwa da saurayinta shiga domin wajen an kawata shi da su piscine, su kayan lilo na zamani wajen game, wajen hutawa, da wajen cin abinci,
Aman a yanzu sai ta canza zani tunda ta karbi wajen da nufin zata kula masa da shi ta canza komai banda sunnan wajen, domin dalilin sunnan da ta bari doka ke tsalake su, Wardugunma bashi da labari , a yanzu wajen ba.a barin yaron da bai kai 18 shiga ba, sai gaga gagan yan duniya, sannan ba abinda ba.a yi a ciki, kan masu bushe bushen su, sai masu aikata zina a fili (wa.iyazubillah) shi kansa mahaifin wardugun bai san takamaimain abinda ake aikatawa a wajen ba, hasalima baya zama tunda abinnan ya faru da iyalansa ya ji niger din ta fice masa a rai, dan haka yake yawonsa yana kasuwancinsa a duniya, idan ya zo niger ba dan ya jima bane, koda an kawo masa korafi bai wani dubawa dan kuwa baya so ya baiwa yan tsunguri tsoma damar kawo masa korafin gidansa,

Jikin Agaishat haka yake rawa, gannin irin abinda baba sofo ke fada mata cewar ba kyau yawo jiki a bayane haka sannan ba kyau aikata zina, Ayya ma ta yi mata fadan ko a tv ta ga sun saka mace na namiji na rungumar juna ta canza tashar ba kyau aikata zina sannan ba kyau kallon tsiraicin wani banban zunubi ne ,

Wajen cin abinci Wardugu ya zame da su, domin daga nan du wani abin hange zai hango shi. Suna zuwa suka zauna a tsararun kujerun wajen, kamshi sai tashi yake, yayan sangartatu , yayan masu hannu da shuni, da kuma masu hannun da shuni, yayan talakawan da suka zabi rayuwar hutu da zama a inda Allah ya ajiye su, sai bushasha ake ana tafiyar da lamarin cikin tsarin yan gayu.....

Menu ne aka kawo masu aka aajiye masu, nan Wardugu da kansa ke a dan duke dan kar wani ya gane shi ya dauki menu dinya kare fuskarsa da ita,

Alhinayet da gabanta ke faduwa na yannayinsa, jikinsa ya nuna ya hau, yannayinsa ya nuna ransa a bace yake,
Ta kali Mu.azan da ya rapka tagumi bai taba Menu din ba ta kuma mayar da dubanta wajen Agaishat ta ga du a firgice take sai sada kanta take bata son kallon mutanen wajen , abin bako ne a gareta,

Hannunta ta kama ta ce" Agaishat, tashi mu je,

Ai kuwa tamkar jira take ta mike ta bi bayan Alhinayettt suka fito daga dakin cin abincin suka zauna a wata farar kujera inda suka baiwa wannan lamari baya.

A hankali yake karanta menu din, harda porc, da giya kala daban daban, sannan abinda ya fi daukan hankalinsa wani abu da aka zana fari shi kuwa aka rubuta masa kudi , shi idan dai ka dauke shi dole sai ka biya, kudi masu yawa haka,

Kiran serveuse din mai dan bingilin sket ya yi da hannunsa,
Tana zuwa tana wani irin juyi fa tafia ta karaso ,
Ta saman gilas dinsa ya kare mata kallo, kafin yake mika mata menu din  ya nuna mata abinda yake so,

Kallonsa take dan gane idan har dan hannun ne? Ko kuwa? Domin sunna taka tsantsan sosai bisa umarnin hajiarsu, dan ta fada masu au kula fa, kar su yarda wani mai bakin cikinta ya yi masu rami su afka, domin abin nan hoda ce, hoda ta shaye shaye,

Jikin wardugu wando ne wanda ya dan dara gwuiwarsa, sai bakar riga wace bata da zanen komai a jikinta, sai hular baka itama wace bata nuna ko ta meye ba  ya dorata saman gashin kansa wanda yake da dan tsayi kadan ba dayawa irin na samarin nan dai na zamani, yannayinsa ta karewa kallo, girkeken namiji, bai yi mata kama da police ba, in ba police ba kuwa wa zai zo masu leken asiri? A tunaninta, dan haka sai ta ce" oga, ka kawo carte din ka ko kach zaka biya?

Wardugu dake zaune a aljihunsa ba kudi, sai dai a mota, carte dinsa kuwa idan ya bada za.a iya gane ko waye shi tun kafin ta karasa wajen,
Yana tunanin mafita Mu.azam ya mita tasa carte din ta bank,
Karba ta yi ta karanta sunnan,
Kallonsa take shima, a take ta ayannawa ranta yan hannu ne, wani lokacin likitoci na zuwa siyen abinnan su dai basu san ko me suke da shi ga,

Juyawa ta yi ta tafi dan kawowa ,

Wardugu ya hade jimkaken hannunsa da wanda yake bude ya shiga murza su a tare,
Sannan yana kara bin wajen da mutanen wajen da kallo,
Table sun kai biyar da ya hango suna fan dukawa su ja wani abin da yake kyautata zaton hodar maye ne a saman plat dan karami mai ruwan zaiba mai shegen kyau kafin su dago su dora daga inda suka tsaya,
Abin mamaki harda yan mata, kananun yan mata wanda a cikinsu sai ya yi rantsuwar akoy wace bata kai 18old din ba!
Wajen a da kafin ya dawo haka yake etablissement privé, wanda etat gwomnati ta san da zamansa ta bada amanar a bude shi, bisa takardun fa aka gabatar a da an gabatar ne kan irin wancen tsarin na wajen hutun yara da iyayensu ranar da ba.a karatu, aman a yanzu ta sauya zani wanda shi dai da hannunsa bai saka hannun a bude haka da shi ba,
Kansa ya girgiza, yau ko uban wa ya daure masu zasu ci ubansu!

Dubansa ya kai waje, nan ya hangi su Alhinayet suna fan taba hira da Agaishat,
Idannuwansa ya tsaida kan Agaishat wanda bai ma san ya yi hakan ba, kallon me yake mata?
Sho kansa bai sani ba ko yannayinta ne ya fi yiwa idannuwansa dadin kallo?
Yana tsaka da kallon nan nata aka gabatar masa da harakar gabansa harda abin ja,

Ajiye carte din ta yi ta juya,

Wardugu ya dago hannunsa ya shiga dubawa da kyau, lale kwarai ita ce, ta ina? Ta ya aka yi take shigowa kasar?  A ina take samu? Ita ke oder ko mijinta ya canza yake samo mata? Wa yake basu? Ta wace hanya ake bi a kawo har nan? Ina polisawan dake bincike a bakin titi ba dare ba rana?, ina tsaron da yake takamar ya baza a sauran garuruwa ma bale a garin da yake ciki?, ya aka yi ya yi sake haka har wannan lamarin ya cin masa da ransa da lafiarsa?
Yana tsaka da tunanin ne sai gata ta shigo,
Mace har mace, farar buzuwa mai shegen kyau, ta sha wasu mahaukatan sket da riga kanta ko dan kwali babu, ra sha wani dogon takalmi mai tsini, tana tare da wani balarabe ya sha jalabiyarsa hannunsa rike da makulin mota ,
Wani na biye da su da jaka baka suka shige tana dan dadagawa mutanen da sukai sabo hannu,

A hankali Wardugu ya mikowa Mu.azam ky din motar da suka zo da ita,
Murya a bace ya ce" ka tashi ka dauki yarwn can ku koma gida, minti talatin na baku ku shige gida da abin hawan nan, ko ku je gidan su Alhinayet dan ya fi kusa da wajen nan, domin idan kame ya ritsa da ku sai kun kwana a cel!

Ido Mu.azan ya zaro, kame a karfe uku na yama? Gashi ranar asabar ne ranar da mutane da yawa kan fita dan shakatawa, aman me ya sa zai yi kame har cikin gari bayan a cikin nan ne ake badalar?

Yar karamar wayarsa ya dauka ya dana kira,

Daga dayab bangaren aka daga ana mai fadin' Chef👮🏻‍♂️ (Sir),

Wardugu ya ce" ina so yanzu ka yi kira wajen Gn na Gendaremeri, sannan ka hado min mahaukatana, ina son motoci masu yawa su cika gari, ina son mahaukatam su karaso nan Wardugu place, kana jina da kyau, polisai su kama du wani wanda ya yi masu shige da suspect, ba zancen takardunka ko wani abin  yau kamun yannayin mutun nake so a yi! Na fitar maka da iyaye mata wa.inda suka bayar da kwakwaran hujar daga inda suke, sai wa.inda suka kai yarensu wani wajen, bayan su a kama a cike mani cel!

Da a vos ordre ya amsa yana katse kiran ya mike ya shiga aikatawa ba jira,

Mu.azam mikewa ya yi da sauri ya fice ya tisa su a gaba da adu.ar Allah ya kai su inda zasu je lafia kar abin nan ya ritsa da su , duda motar Wardugu ne, da lambar shaida shi ne, ba zai hana a bincike su ba domin matarsa ta saka ya dora dokar ko motarsa a ringa bincikawa a gari! .........

Toh fa, An tabo Wardugu, an tabo tashin hankali🤔

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

2️⃣6️⃣

Bayan tafiyarsu da kamar minti ashirin, Wardugu dai na nan zaune yana bin kowa da kallo ta kafurin bakin glass dinsa,

Mintuna tsakani sai kukan jiniyar sojoji ta fara yin salama wajen,
Da farko tunaninsu ficewa zasu yi, sai dai abin kara yi masu salama yake,

Hajia Aisata dake zaune saman cinyar karuwinta suna shagali aka dokowa waya,
Dagawa ta yi da yannayin duniyanci ta ce" Ya?

Masu tsaron kofar Wardugu Place ne daya ya yi kiranta a tsorace ya ce" Hajia me motocin sojoji ke yi a kofar nan? Na ga sai jeruwa suke suna didirowa da alama wani suke jira,

Ai bata san lokacin da ta diro daga saman kafar mutumen ta ce" me me me ka ce? Sojoji? A nan?

Bata tsayin jin amsarsa ba ta fito da wani irin gudu ta ce" du wanda ya san da hoda gabansa ya yi gagawar rabuwa da ita ga arnawa a kofarmu!

Nan fa wajen ya rikice, mutane du suka tsorata,
```

Aka fara kokarin guduwa wasu na nufar motocin su da gudun tsiya wasu na auna tsayin katangar sai dai ba halin dirawa domin ga tsayi ga abin kama barawa an zagaye wajen da ita,
Du masu jan mayan nan suka aniya gudu suna boyewa wasu na watsawa cikin ruwa wanda kadan ta rage masa ya janye abinsa, manya manyan masu fada a jin wajrn suka fara nufarta suna tambayarta me hakan ke nufi? Dama ba da lamuncewar gwamnati ta bude wajen raba masu eh yane ba? Ba wanda ya daure mata a gwamnati?!
Ita dai ta cire dogon takalmi sai bi take table table tana kara goge dan sauran hodar da wani farin tishu ita da yarenta masu aikin wajen,
Du sun haukace sai ihu take yiwa mutane kan wa.inda tsiraicinsu ya bayanna sosai sai fadi take su yi maza su saka kayan da ya fi wannan,
Sannan da gudu wata bagwariyar yarinya ta fito da abaya ta kawo mata ta luluba mata daidai nan tuni sojojin sun cafke masu tsaron kofar sun fara tura su cikin motar wasu kuwa na tsare masu bi ta hanyar da wa.inda ke zuwa a lokacin,
Wani sergent ne ya kali abokinsa ya ce" yau fa akoy buro.uba a wajen nan, domin lamarin na gida ne, fadan gida ne,

Kai ya girgiza ya ce" ai ba na gida ba, ko na waye ta tarowa kanta dan oga ya yi mata tashi daya!

A guje ta karaso table din wardugu tana babala botiran rigar tana zuwa da mamaki mamaki haushi haushi ta ce" kai waye mai hular nan ne wai? Kai ana a yi maza a kawar da komai kai kana zaune kikam , to walahi bara ku ji kaf wajen nan dan na lura hoda ta coshe tunanin ku! Du dan iskan da aka kama da ita ba ruwana, tawa kaf ta wajen nan ta bi Wc! Ta hannayen ku kuwa ban sanku bama bale na san me kuka shigo da shi, kun kuwa san wajen da girma ba lale ne sojojin su yarda da ina iya control din kowa!

A hankali ya dago yana hangen yanda ake shan tsere da mutanen tsakar wajen fa sojoji suna yi masu cafkar fara suna yin waje da su,
Ransa ne ya kara baci , me ya kai su kokowa da su? Su saka lasifika su yi magana kan du dan akuyar da ya nemi gudu za.a watsa masa tire a gaz! Aman sai wani guje guje suke da juna harma su yi tunanin mu tsarensu ne!

Gilashin idonsa ya cire a hankali ya dago da jajayen idannuwansa ya sauke saman fuskarta , murya a dake a dage ya ce " aman kuwa da kin ci amanar clients din ki *AISATA*, na ji kuna fadin client sarki ne   ke kuwa kina ikirarin ba ruwanki dan an kama shi da hoda yana zuka,

Mutuwar tsaye ne Aisata ta yi, mutanen wajen kuwa gannin mai maganar sannan ya karasa mikewa tsaye du ya saka suka rude abinka da mai laifi suka fara neman hanyar fita,

A rikice ta nuno shi da yatsarta ta kusan baba ta ce" Wardugu? Wardugu! Wardugu,

Ya ce" ki ajiye yatsarki da nuna da ita, ko ki hade yatsutsanki ki nuno ni da hannun baki daya, rashin tarbiya ne nuna baban mutun da yatsa Aisata!

Wani irin juya ta fara ji, hankalinta tashe ta ce" aman kai da kanka zaka tonawa wajen nan asiri? Ka fa san mamalakin wajen,

Sergent Kabir da ya shigo da sauri ya zo dan jin me Wardugu zai fada kiran da ya tura nasa ya ja ya tsaya ya sara masa,

Wardugu ya juyo wajensa ya ce" ankwa!

Da sauri ya mika masa, sannan ya kara ja ya kame,

A bainar jama.a Wardugu ya ja hular kansa ya cire ya nufota ya ce" Madame *MARAHUT AISATA* iko ya kama ki bisa laifin buda gidan badala, yada mugayen ayuka a boye, da siyar da hoda a fili kuma a bayane, ki yi shiru ko dukan abinda kika fada zai yi aiki kan ki, kina da damar tsayar da lauya dan kare kan ki ko kwato incinki.........

Yana fada ne yana sarkafa mata ankwa irin na an kamo barawo, kafi yake turata gaba da kansa ransa bace ,

Suna fitowa ya daga murya ya ce" lasifikha sergent!

Ai kuwa da gudu aka fita aka kawo masa,

Ana kawowa tuni yan jarida sun halarta sun fara dauka abinsu,
Wardugu na amsa daidai kunenta yana rike da ita hannunsana dama ya daga, a dake kalamai a rarabe ya ce" Duk wanda ya yi gigin guduwa daga wannan waje zai jawa kansa rigima, zamu saki batkonon tsohuwa (🤣🤪), koda kana da rashin lafia kan ka! Ku hade gaba dayanku tsakiyar wajen nan minti biyar na baku, du wanda bai zo ba tawa ce ni da shi!

Ji kake wajen ya dan lafa da iface iface, nan fa dan koke koken yan matan ya fara tashi,, wasu na dora hannayensu a kai suna ihun sun mutu sun lalace yau asirinsu ya tonu, wasu na kaico da tunanin mai tsaya masu domin dama ba wani abin iyayensu gare su ba , irin sun samu dan masu kudi ne suka zubar da tarbiya aji daraja irin ta ya mace suke bin su ana shan kida, wasu samarin sun sato motar gida ne an zo a more da yan mata haka ta ritsa su, wasu manyan mutane ne masu iyalai a gida suka baro suka dauko wata yar shilar suka zo a cashe, waje dai ya fara daukan kimtsi, waje ya yi tsit sai iza keyarsu ake ana waje da su,

Murya kasa kasa Aisata ta ce" Wardugu, ka bar ni na kirayi abanka,

Bindigarsa karama ya daure a kugunsa kafin yake turata itama ya yi mota da ita,

A wannan rana Wardugu bai nufi gidan su Alhinayettt ba sai wajen karfe bakwai na dare,

Yana zuwa bai fita a motar su ta sojoji ba kira kawai ya yi suka fito ba tare da ya yiwa kowa magana ba suka duru a motar ya ja, inda Alhinayettt ta bi su da kallo ta koma tana shan dariyar mahaifiyarta na fadin" yau fa akoyta, Alhinayettt yau ana rigima a garinnan, kina ji shiru ? Ba galama basu fara kade kadensu ba

Alhinayettt ta yi dariya ta ce" Anna (Matar babansu ce), ai sai adu.a kawai, Wardugu Wardugu Kowa Wardugu, ni dai zan yi ta yi masa adu.ar Allah ya tsare shi........

Gidan Ayya ya kai su, wace ke zaune tsakar gida da waya a hannunta sai dokawa wardugu kira take aman ba.a dagawa,

Ai tana gannin sun sauko ta nufo wajen su sai dai bai tsaya ba ya yi gagawar juyawa ya fece abinsa, domin ya sani ne yanzu har an fara zuwa wajenta, bayan ta sani shima bai isa ba , shima yana bin dokar ne !

Gidansa ya yiwa tsinke,
Nan ya tarar da Mota uku a ciki bayan na kofa da aka hana shiga,
Mita daya dai ta mahaifiyar Walyn ce, biyun ne bai gane ba, dan haka ya shige bangarensa yana haharde kafafuwa yana so ya je ya zauna ya kashe du wata waya dake yi masa kuka a kunne ta hana shi sakat sai doko masa kira ake shi kuwa ba wanda zai daga kiransa domin ba wanda zai saurara, ba tonon asiri ne ya yi niyar yi masu ba, ba huce haushi ne ya yi niyar yi wa mahaifinsa ko matarsa ba, abin ne ya daje shi, ya diro masa a lokacin da bai yi tunani ba, tashin hankalinsa shi ne...ta ina ake shigo da hoda har ta gama gari haka? Ya sani ne sai sun sha masifa fa lauyoyi, inda ya san ya shige gabansu harda dan gidan banban lauya baki daya, in ya yarda ya ce a saki mutane, iyayen yara da manya masu daraja zasu sako shi a gaba ace dan da yaronsa ne !

Kansa ya shiga shafawa ya bude bangarensa ya shige ,

Kamar koda yaushe, sansanyen kamshi ne ya taro shi, wannan fa ba.a wasa da shi,
Agogon hannunsa ya fara kuncewa yana kokarin karasawa cikin dakinsa na baci dan ya samu ya yi wanka,

Wardugu" ta yi kiran sunnansa tana mikewa ta nufo shi,

Tsayawa ya yi yana kallonta, domin yanzu ya dan saka mata haushinta da yake ji na ta tafi ta bar su wai ba zata hada numfashi da yar gidan Anna ba,

Karasowa ta yi ta shige jikinsa du da yanda yake tarewa,
Murya a kasalance ya ce" Walyn bari na yi wanka , aiki na yi jikina ba tsafta,

Kai ta girgiza ta kara shigewa jikinsa tana rungume shi sosai a jikinta ta ce" baka wari kuwa Wardugu, kamshin turarenka na nan,

A hankali ya raba jikinsa da nata ya ce" aa tsaya na yi wanka, na yi zufa sosai kin ji?
Ya karasa yana mai zaunar da ita saman tsareren bed dinsa mai ruwan zeba,

Bayi ya zarce ya samu ya shige kasan shower,
Ruwa mai sanyi ya sakarwa kansa a jikinsa dan yana son jin sanyi
A hankali ya lumshe idannuwansa yana jin sanyi mai dadi na ratsa shi,

Sai da ya gama ya yi wanka na kirki ya dauro alwallah ya fito daga bayin , zuwa wannan lokacin har karfe tara ta kusa cikewa,

Yana fitowa , Walyn ta kara nufo shi

Tsayawa ya yi yana kallon yannayinta, magana ke tafe da ita domin batai masa yannayin tana bukatarsa ba,
Dan haka ya zarce ya dauko jalabiyarsa ya saka ya dauko salaya ya shinfida yana kokarin tayar da sallah,

Wardugu mana! Ta fada da yannayin damuwa,

Juyowa ya yi yana kallonta bai amsa ba,..
Ta karaso ta ce" su Mamanmu ne fa ke zaune a falona ka fito ku gaisa ,.

Wardugu yana kallonta, mamansu, har wannan lokacin?

Bai bata amsa ba ya tayar da sallarsa, dama dan ya yi shafa.i da wutiri ne,

Zama ta yi har ya karasa, ya zauna ya yi doguwar adu.o.insa na tsari da komai ya mike ya cire rigar daga shi sai gajeran wando ya yi bismillah ya haye bed,

Da mamaki take kallonsa, ranta ne ya baci ta ce" aman baka ji wace nace maka tana jira ba?,
Domin ta sani ne, yana mugun daraja mahaifiyarya, ko gaisar da ita zai yi sai ya dan duka,
aman yanzu ta fada masa ta ga ya wani kwonta abinsa,

Wardugu ta kara kiransa tun karfi,

A fusace ya dago zaune , murya a bace ya ce" ba zan je na gaisar da mamanki ba, na gaji baci nake son yi ki fice mani a daki!

Ido ta kwalalo tana kallonsa, kafin take juyawa ranta in yayi dubu a bace yake, tana son tsayawa ta ja maganar aman wani abin na hanata, dan kuwa dukan alamu sun nuna idan ta yarda ta kawo masa raini komai na iya faruwa ,

Juyawa ta yi tamkar zata tashi sama ta fita a dakin,

Karamar wayarsa ya bude,

Sheik ibrahim ya danawa kira,

An jima tana ringin kafin yake dagawa da salama,

Wardugu ya gaisar da shi da tambayarsa jama.a,

Sheik ya amsa yana mai tambayar Wardugu Aiki,

Wardugu ya amsa shi a nitse ya ce" Malan, a kara saka mu a adu.a,

Sheik ya yi murmushi ya ce" Wardugu , na ganka a tv, fatan Allah ya tayaka, Allah ya baka ikon yin aikin kirki, sai dai zan kara fada maka, a duniya karka ce sai ka birge kowa, ka yi lamarinka domin Allah, kar ka saka fushi ko gaba dan Allah ya baka dama mai girma ta jan wanda ka yi niya, ka ci gaba da kawar da kanka a kwadayi , sannan ka ci gaba da jan istighfari kana kaiwa allah kukanka ka ji?

Wardugu ya amsa a mutunce sukai salama,

A hankali ya lalubo cazbaharsa fara kar tana ta kanshin turaren  ruwa ya shiga ja daga kwoncen yana ta jan astghfari,

Me mijinki ke takama da shi a duniya Walyn? Ya rasa wa zai rufe sai aban iman? Ko dan yana auren yar yayata ai sai ya daga masa kafa, dan kawai ya kama da shi a wannan wajen, wajen ba na ubansa bane? Zance wajen sunnansa ma gare shi! Me yake tunani? Dan yana sanye da rigar iko shikennan ? Ai idan shine yau gobe ba shi bane zai ringa yiwa mutane rashin mutunci! Tunda haka ta faru muke gidannan aman ya zo ki wani zo ki ce wai ya gaji? Gajiyar kaniyarsa, mu da muke nan bamu gajin bane? To idan mijina ya kwana a cel nima na dauki alkawain sai na tozarta Wardugu sai na saka wardugu ya shiga uku, sai na

Aunty! Walyn ta fada tana daga murya sosai,

Da yatsarta daya ta ce" ke a wa? Wacece ke? Kike ikirarin tozarta Wardugu bayan Allah ya rike? Ke kin san da za.a shige shi da an shige shi ba yau ba Aunty! Wardugu baya zuwa maula, hukunci kuwa idan ya kama zai yiwa ko wani dan buro........ba, meye? Takamarki ki yi masa shari, ki hada shi da malame, ko ki same shi ta hanyar abin duniya?
Ban ce sihiri ba zai kama shi ba domin wanene shi, sai dai na miki alkwarin tunda kika fadi haka , sai dai mu mutu baki daya,!

Mahaifiyarta ce ta kasheta da mari, rai bace ta ce" kan namiji? Kan namiji zaki ciwa kanwata mutunci? Namijin ne ya kai dan goyo har haka? Ke Wardugun da kafin aurenku ma sai da ya karya maki hannu sau biyu shine kike daga jijiyoyin wuya dan ance za.a taba lafiarsa? Kin manta dan ya kauce ki malaki wannan daula na yarda yake tata maki rashin mutunci? Idan kin canza ra.ayi na sani da wuri dan Ubanki!

Wakyn dake yashe tun marin magaifiyarta, jikinta a mace, takan mance du wani kudirinsu idan tana tsaye gaban gwarzonta, namiji ne Wardugu, can dama tana sonsa sosai, damuwar kuna tana son kudi sosai!

Mu.azam, tashi ka kai ni ya sha maganin bakin nan ,
Ayya ta fada tana nuno masa wani dan kuli wai maganin baki ne dan kar baki ya fada masa

Mu.azam dake zaune kafa tankwashe Agaishat na koyar da shi bakara ya dago da mamaki yana kallo Ayya,
A hankali ya ce" Ayya, idan muka yarda muka fita a yau fa kama mu za.a yi a rufe, sai karfe takwas na safe za.a tsayar da kamen nan, ki rufa mana asiri Ayya kin j?

Ayya ta zaro ido ta ce" dan ubansa a rufe mun, bafa zai yi baci ba sai ya sha maganin bakin nan yau yanzu yanzu dan haka tashi mu je Mu.azam,

Mu.azam ya mike yana ayyana ta faru ta kare a ransa, dan ya san in dai suka fita titi za.a kama su ne, za.a rufe su, daga shi har Ayya har Agaishat din,

...........to fah🤣🤪🤪🤪🤪✌🏽

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

2️⃣7️⃣

Mu.azam ya ce" Ayya, ki bani na je na kai masa, kin ga ko an kama ni kadai ne za.a kama,

Ayya ta ce" yo kai na d'a bane, a hada har mu a rufe, ba yace doka ta hau kowa ba? Na tabata an hada da iyayen mutane a wajen,

Mu.azam kam ya rasa ya zai yi da Ayya , ta kuwa coge kofar daki inda Agaishat ma ta fito tace ba zai yiwu Ayya ta tafi ta barta ba,

Kallon agaishat yake kasa kasa, a hankali ya ce" idan aka rufe ki Agaishana, ba zan iya hakura ba, kar ki biyo mu na roke ki,

Irin na yara ta yi masa da kafadarta irin ta kiya, tama rigayi kowa karasawa wajen motar bayan ta amshi maganin bakin na hannun Ayya,

Haka Mu.azam ya fitar da motar dake da lambar Wardugu, ya dauko carte dinsa ta shaidar shi likita ne, da carte didentité dinsa,

Fitowa ya yi da motar Ayya ta shige baya ta hakimce, Agaishat ta shiga gaba aman a ranta a tsorace take, tana tsoron sojojin garinnan, daman ba.a saka soja a lamari a niger sai abin ya baci, su fa ba ruwansu hade kowa suke, idan ka yi masu gardama su tataka banza su barka nan zubde tamkar kayan wanki,

Tuki yake zuciyarsa kuwa sai adu.a yake, Agaishat ma adu.ar kawai take inda Ayya ke kara buga lambar wardugu aman a kashe, bata shigama bale a dauka,

Danja na tsayar da su aka haske su da cocila dall a idannuwansu,, gaba da baya sojoji suka
```

zagaye su har mutun uku,

Na kusa da direba ne ya  kwonkwasa kofa,
Mu.azam ya bude yana dubansa,

Mutumen ya ce" motar Gn ce Oga,

Ya ce" eh na gane ai,

Ya ce" malan daga ina , kuma ina zaka je? Wa ka dauko? Sannan ka bude mana bayan mota zamu yi bincike,

Mu.azam ya fara bude masu motar, sannan cikin nutsuwa ya ce" ina tare da mamanmu ne, mahaifiyar Wardugu da kanwarmu Agaishat sai ni kuma amininsa ne, daga gida muka fito zamu je gida wajensa bisa umarnin mamansa,

Menene shaidarka? Sojan ya tambaya ba alamun wasa,

Mu.azam ya mika masa cartocinsa, sannan ya sauke madubin bayan ya dayan ya leka wajen Ayya,
Kwarai kuwa itace, waye bai san Ayya ba? Mahaifiyar General,

Gaishe da ita ya yi cikin mutuntawa ya ce" yi hakuri mama muna bisa aikin mu ne, ki tabatar mana da abinda ya fada,

Ayya ta ce" eh haka ne, ina son gannin Wardugu me yanzu yanzu,

Sojan ya gyada kai yana kallonta,

Wanda ke bincika cikin motar ya shaida masu ba komai cikin motar, dan haka ya mika masa takardarsa ya basu damar su fice

Cikin ikon Allah haka sukai ta haduwa da sojojin nan suna kara titsiye su ,
Harda wanda bayan dukan bayannan nan yace ai shi bai wani san Ayyar ba a bashi shaidar da ta fi haka,
Nan fa aka sha rigima da kyar masu taya shi suka tsawatar masa ya batsu suka tafi,

Tun abin karfe tara sai kusan sha daya suka karasa gidan Wardugu nanma suka tarar da wani balakin an hana iyayen Walyn fita sai dai su kwana a nan in kuwa suka fita aka kama su toh su suka gano, sun izata sai balaki take kan wardugu ya fito ya raka su ko ya basu shaidar da zata sakasu su tafi har gida lafia,

Suma su Mu.azam sai da aka titsiye su kafin suke samun shiga gidan,

Mu.azam na tsayawa ya sauke ajiyar zuciya yana kallon hajia rigima, domin Ayya ta hade rai ta yi kicin kicin da fuska tana kallon yanda suke tsatsaye suna ta magana suna tafa hannu suna balaki,

Mu.azam ya ce" Ayya, kar ki kula koya na roke ki,

Ayya ta yi murmushi ta ce" oh yarona, yanzu kai ke yi min gargadin kar na kula kowa, ai ka san bana kula mutumen da bai iya tsawatarwa zuciyarsa ba!

Bude motar ta yi  ta sauka,

Ai kuwa tunkarar wajensu ta yi direct ba wani tsaye tsaye,

Tana zuwa ta ja ta tsaya itama tana yi masu kallon da suke mata,
Da yake akoy wuta ko.ina haske ya garwaye gidan kowa na gannin kowa ne,
Ayya bata fita sai ta shirya ko fitar da a rikice take ne, dan haka yanzuma sai baza kanshi take, ga lufayarta ta nada mai ruwan ja da baki, ta sha awarwarenta na zinariya,

Walyn ce ta ce" ina yini,

Ayya ta kai dubanta wajenta ta ce" lafia, sannan ta mayar da dubanta wajen iyayen Walyn din tanai masu kallon ido cikin ido,

Mahaifiyar walyn ta miko mata hannu ta ce" Hajaju ne, uwar gidan *MARAHUT*  ke ce da tsakiyar daren nan??

Ayya ta sakar mata murmushi ta mika mata hannun itama ta ce" wa.alaiki salam maman Walyn, ke ce a gidan Wardugu da wurin nan haka,

Kanwar maman Walyn ta kali Walyn ta kuma kallon sirikan biyu, ta juya bangaren Walyn tana ayyana taf, lale ana cakwakiya a gidan nan,

Ita kuwa walyn kitson kanta kawai take sosawa, susar da bata san ko ta meye ba,

Ayya ce ta fara cika hannunta ta kuma kallon Walyn ta ce" Aa, Walyn yaron nan yana nan ne dai ko? Bara na shiga na gani Wardugu sarkin aiki!

Juyawa ta yi ta nufi bangaren Wardugun cike da isa, sai a lokacin Mu.azam ya lalaba Agaishat ya cire mata tsoro suka fito daga motar,

Mu.azam ruwan sanyi sai ya nufi wajen su dan gaishe su,

Walyn ta daga ta watsar da idannuwanta sannan ta zabgawa Agaishat wata muguwar Harara da kallon kyama ta juya tana riko hannun mamanta suka koma bangarenta,

Agaishat dake dafe da kirjinta jin yanda zuciyarta ke dokawa Mu.azam ya kallo,

Murmushi ya sakar mata ya ce" mu je Matar Mu.azam,

Ido ta zaro kafin take daga kafa da sauri ta yi gaba tana jin wata kunya kunya da wani irin abu game da Mu.azam din, yakan mantar da ita wacece ita ta halin nuna mata itama mutun ce mai cike da cikeken inci, yana yaba kalar fatar jikinta ta hanya kawatata da kalamai masu tsari da sence, yakan ce Allah ya datar da shi samunta, ita Agaishat yar gidan Sofo? Tana so ta biye masa tana tsoron ko wasa yake mata? Tana son ta yarda tana tsoron yan birni,

Ayya na shiga ta zarce har dakinsa na baci tana fadin" ina kake janyau, ka hargitsa mana gari ka lafe a gado, tashi tashi kaima ka yi kwanan zaune dan nema kawai!

Da wani irin sauri ya mike ya diro ya warci doguwar rigarsa yana faman sakawa ta shiga dakin,

Wardugu ya ce" Ayya, wai yaushe zaki dauna shigo min haka zaraf kawai? Me ya fito da ke a tsohon faren nan? Ya aka yi kika ratso sojawan hanyar nan? Wa ya kawo ki?

Maimakun Ayya ta bashi amsa sai cewa ta yi" baka da sutura a jikinka ne kake kwonciya Wardugu?

Wardugu ya dafe kansa ya furrta" Ya Allah,

Bakinta ta yatsina ta ce" fito ina jiranka

Sai da ya saka kayansa ya biyo bayanta,

Yana fitowa ya ga Mu.azam, da bakuwar nan ta ayya da shi ba zai iya fadin sunnanta ba dan bai wani rike ba,

Sai dai mamaki yake, yanzuma wasu kayan ne jikinta, shi abinda ke bashi mamaki yaushe ta iya saka kayan tubawa har yake bin jikinta haka? Yaushe ta iya saka kayan kansa nema ?

Kawar da kansa ya yi da sauri yana yatsina bakinsa yana ayyana ina ruwanka yo, ba dai Ayya ta daure mata ba?

Ayya ta karbi kulin maganinta ta umarci agaishat da ta bude frij dake nan falon ta fauko ruwan roba

Agaishat ta nufi frij tana tambayar kanta ina wajen budewar yake? Domin ba irin na gidan Ayya bane, wannan wani glass nema a jikinsa ko.ina tar tar yake ana hangen abubuwan dake ciki tar sai dai ba lale ka san wajen kunawarsa ba,

Ja ta yi ta tsaya tana kallo,

Ayya dake jira ta kallo wajenta ta ce" Agaishta kawo mana,

Agaishat ta juyo tana raraba idannu ta ce" Ayya, ina zan bude??

Wardugu ya girgiza kansa, Mu.azam ya mike ya je ya nuna mata ya bude mata, ta nuna masa wanda take tunanin ruwan ne?
Mu.azam ya ce mata" wannan ai jus ne, gidansa da kamarsa yake yannayin ruwa, aman kin ga jerin ruwan nan,

Nan ta dauko suka dawo wajen Ayya dake ta yiwa Wardugu fadan ya kwonta bai ci abinci ba dan ba sai ta tambaya ba ta sani ne kwonciyarsa zai yi, aman kwata kwata bata sako maganar matarsa ba ko iyayenta, bata da wannan lokacin,

Wardugu dai kallonta yake, ta bude ruwa ta tsiyaye fiye da rabi ta zuba maganin ta girgiza ta mika masa ta ce" shanye,

Wardugu ya cee" Ayya meye kuma wannan
?

Ayya ta ce" Wardugu, magannin baki ne, bakin mutane, ka san baki fa ya fi maye mugunta, baki ai ba dan uwa bane, bare yau ka janyowa kanka maganar mutane

Robar ya rike a hannunsa ya ce" Ayya, bayan walahaulan da nake yi kuma dai kin bani wannan jike jiken naki?

Ayya ta ce" walahaula hanyarta daban, wannan ma nasa daban, kai harda garin hantiti nake tafe, maza shanye ka dauko min buta a bayinka na zuba maka ka yo wanka ka turaru sai mu juya,

Ido ya zaro yana kallonta, kafin ya maido dubansa wajen Mu.azam da irin kallon kai ka kawota ko?

Mu.azam ya juyar da kai wajen Agaishat dake zaune kasa yana kallonta, domin kallonta na saka shi nishadi

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

28

Bani da bakin da zan yi godiya a irin tarin kulawar da kuka nuna, da tashin hankalin da kuka nuna na wannan abin da ya faru, kunya ta kama ni, na ji kunyarku sosai na irin hada ni da Allah da kuka yi, wacece ni? Ni ba kowa bace da zan ki yin hakuri dan haka nake shaida maku ga *BAK'A* . Daga taku yar mutan niger

Kun yi sake , kuna gani tana zuwa ta shige dan ta samu ganninsa aman mu tun da yama muke zaune, a matsayin mu na iyayen matarsa yace ya gaji ba zai fito ba, kina ganni da takama bayan ta fada mana magana ta shige abinta,
Auntyn Walyn ke fada ranta na kara baci,

Mahaifiyar Walyn ta ja tsaki , ta ce" koma me take takama da shi ai mijin ya nuna mata iyakarta, yanzu ba da kishiyarta bace yaronta ke fada? Banza ita har ta isa ta nuna ita wata ce? Bayan an ci mata mutunci kowa ya sani?

Walyn dake zaune, gaba daya zuciyarta ke wani irin tashi, ta rasa me ke damunta kwanakin nan takan tsinci kanta a irin yannayin rashin jin dadin jiki, bata iya kara furta masu komai ba ta mike ta je dan ta saka a kara tsaftace masu wajen da zasu kwana, domin ba zata lamunci a rufe iyayenta ba, za.a samu matsala sosai,

Sai da aka sha rigima da Wardugu ya shiga wankan hantitin da Ayya ta jika a butarsa ta karfe,
```

Yana yin wankan ya fito yana jin yanda yake warin magannin, sai dai yana fitowa ta kuma tare shi da hayakin Hantitin nan yana ta bade shi ,

Jajayen idannuwansa kawai yake binta da su, in ba Ayya ba, wannan uwar gajiyar da ya kwaso ta zo ta tirke shi da wannan abubuwan? ,

Tana gamawa ta fita fallo da hayakin bayan ta debo turaren wutar dake jere saman coiffeuse din dakin tana tafe tana dan sakawa yana tashi a hankali,

Kansa kawai ya girgiza, ya cire jalabiyarsa ya saka rigarsa mai karamin hannun wace ta baiwa jikinsa damar bayanna ya saka wandonsa dogo fari na jalabiya saman gajeran ya fito,

Ayya dake kallon Tv, Mu.azam kuwa sai wani kara shigewa Agaishat yake yanai mata labari kasa kasa, wanin ta zaro dara daran idannuwanta, wanin ta dan yi murmushi, wanin kuwa sai dai ta rufe fuskarta da hannayenta wai kunya take ji,

Galala ya yi yana kallon kusancinsu da kuma yannayin su,

Ayya ce ta juyo wajensa , sai dai ranta ne ya baci gannin irin rigar da ya fito da ita, ita kam ya zatai da wannan sakarar dabi.a ta wardugu ta saka kannanun kaya? Sam ba al.adar batuben mutun bace, Batuben mutun yanda mace zata ji kunyar bayannar da jikinta haka shima namijin, sun fi saka manyan kaya sukan yi rawani ko su aza hula saman kansu, suna saka kananun kaya irin na zama aman dogon wando har kasa, riga mai mutunci su yi zanzaro abinsu, aman fa siri batube sai mata nai, shi ya saka take mamakin Wardugu, gatsai gatsai sai ya bi gari da wando daidai gwuiwa, riga mai yankeken hannu har yana wata takama,

Rai bace da yaren tubanci ta  ce" Wardugu ! Nigey medi nubazzu ? Ay kubu nukoy ? Anna gnuduro indi hadin ?  ( Wardu! damme bakajin magana , wannan wane irin rigane ? Idan mutane suka ganka me zakace?),

Wardugu ya kalli rigar jikin nasa, kansa ya shafa wanda haka kamar ya zame masa jiki, ya juya ya sako wata riga a saman wannan duda haka bai bala boturanta ba,

Yana dawowa ya zauna yana kallon Ayya,
Ayya ta girgirza kai ta ce" a gaskiya wannan abin sam bai yi ba, kai ba wani karamar kira ba , ka wani saka kananun kaya, yanzu haka a haka sirikanka suka ganka wardugu? Salon a fita da kai a baki ko?

Wardugu ya lumshe idannuwansa ya bude ya ce" basu ganni ba,

Me kake nufi da basu ganka ba?,

Wardugu ya daga kafada ya ce" ai na gaji ne, sai idan na huta Ayya,

Da kallo take binsa, a sanninta yana matukar jin kunyar iyayen matarsa yana darajasu, ko dan irin yanda sirikan namiji keda matukar daraja wajen mijin yarsu a al.adun tubawa, domin kuwa suna da dama sosai a kan mijin yarsu, aman yau yace wai ya gaji bai je ya gaisar da su ba? Ta so ta tsawatar sai kawai ta kyale, domin dai Walyn da Wardugu auren so suka yi, shi bai taba kawo mata karar matarsa ba, itama bata taba kawo masa karar rashin girmamata da Walyn bata yi ba, ai ido ba ma.auni bane abin duba ne, yana gani kuma yana sane, dan haka ta watsar ta mike tana duban Agaishat ta ce" ku tashi mu tafi kar mu kwana a gidan nan kun ji?

Wardugu ya kaleta yana talabe habarsa, ya ce" Ayya, ai yau sai dai ki yi hakuri da gorin wai kin zo gidana, yau kwana ma zaki yi Ayyar wardugu,

Ayya ta zaro ido tana kallonsa, ta ce" kai, ka rufamini asiri, ni na kwana a gidanka wardugu? Aa aa, ka tashi ka mayar da mu da kanka man,

Wardugu ya dubi Mu.azam ya ce" kai, zaka bado hankalinka nan ne? Bakin karfe dayan dare dokar ba wani karbar uzuri, motocin yan tafiya kawai za.a bari su je masaukinsu, suma sai dai su waye a can, ba zai yiwu ni na karta dokarnan ba Mu.azam zaka saka baki ko sai na ...

Mu.azam ya taso yana dariya ya ce" Ayya, karfe daya saura kadan, ki yi hakuri, mutuncinki, girmanki ya fi karfin ki je cel Ayyarmu, kuma ke ke fadin ya yi aikinsa tsakani da Allah a rayuwa, ki yi hakuri Ayya,

Ayya ta yi shiru tana kallonsu,

Dubanta ta kai wajen Agaishat, ta maido wajen Wardugu,
Kanta ta girgiza ta mike ta karaso wajen Agaishat ta kama hannunta ta ce" tashi mu je bangaren mata,

Agaishat ta mike tana biye da Ayya,

Mu.azam ya dan yi taku dan raka su Wardugu ya riko hannunsa,

Mu.azam ya dawo da baya ya ce" namiji, bangaren Walyn fa zasu je?

Wardugu ya ce" eh na gani,

Mu.azam ya ce" anya kuwa za.a kwashe lafia?

Wardugu ya yi murmushi, ya maida dubansa wajen Mu.azam da kyau, kallonsa yake yana karantarsa,
A nitse ya ce" me ke damunka da ita? Batai maka kankanta ba? Me ke jan ra.ayinka wajenta? Ko bakin nata?

Mu.azan ya dago da sauri yana kallonsa, Wardugu, yanzu mutun yanzu ba mutun ba,
Mu.azam ya ce" ban gane maganarka ba,

.......

........................

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

2️⃣9️⃣

Wardugu ya shiga dan shafa sajensa, ya gyada kai ya mike yana dan nuna alamun zan kamaka ne ya yi ciki abinsa

Mu.azam ya bishi da kallo, ya maida kansa yana duban wajen kananun fitilu fararen dake kara kawata dakin,
Murmushi ya yi shima ya lunshe ido a ransa yake ayanna zan so na rayu da ita koda na yini daya ne

Ayya na zuwa bangaren Walyn ta yi salama , ba wani hayaniya ko nuna isa ta ita mahaifiyar mai gidan ta samu waje ta zauna tana duban Walyn ta ce" Walyn muna son daki ni da y'ata , muma kwanan gidanki yau ya kama mu,

Walyn ta mike ta nufi wani dakin ba tare da ta ce komai ba, inda mahaifiyarta kuwa sai ta fara hura hanci ance gidan yarta,
```

Bata jima ba ta dawo ta ce" ga dakin an gyara Ayya,

Ayya ta mike Agaishatma ta mike suka nufi dakin da aka nuna masu

Suna zuwa Agaishat bayi ta nufa ta dauro alwallah,
Da nadin nan nata ta shinfida darduma ta tayar da sallar nafila domin dare ya yi sosai ya raba, ita kuwa yanzun ta zame mata jiki sai ta yita take iya rintsawa komai dare,

Kuri dai suke zaune suna kallon juna kowa da kudirinsa a kan dan uwansa, ita auntyn walyn mamaki take ashe wardugu har mahaifiyarsa, yo har mahaifiyarsa mana gashi itama dole ta kwana a gidan?

Dare ya raba , karfe biyu da rabi yayi aman wardugu ya kasa rintsawa,

A hankali yake sando ya sauka daga bed din domin nan Mu.azam ya zo ya kwonta bayan sun sha rigimar ba zai kwanar masa a gado ba yace shi kuwa nan zai kwonta,

Yana kokarin fita ya ji muryar mu.azam ya ce" ina zaka je?

Wardugu ya juyo da sauri, ganninsa zaune dare dare saman bed din ya saka shi zabga masa harara ya ja tsaki ya ce" matarka ce ni da zaka wani motsa dan na motsa? Wajen Walyn zan tafi

Mu.azam ya zaro ido ya ce" aman Wardugu baka da mutunci, wajen Walyn fa kace, bayan ka garza rashin mutuncin nan idan walyn ta kaleka komai jarabarka lale lale bata da zuciya!

Wardugu ya kama haba irin mamakin nan, ya ce" kai aman baka da mutunci, ohk dare ya raba kowa ya samu nutsuwa yana shara baci ni ina nan juye juye sai ta ki kulani dan na bata mata? Da a yau da asuba zan kara aure walahi talahi a masalaci!

Mu.azam ya zaro ido yana kallo Wardugu ya fice a dakin yana wata irin tafiya na ya kumsa masa haushi,

Kai ya girgiza ya koma kwonciyarsa

Wardugu na shiga bangaren ya tarar da su still nan saman kujeru, Walyn sai gyangyadi take, mahaifiyarta ta fara bacin itama , auntyn kuwa sai dan kada kafa take ,

Dakewa ya yi abinsa ya dan yi gyaran murya irin bai ahigo din nan ba, kafin yake yin salama ciki ciki ya shigo gaba dayansa

Su duka farkawa suka yi, yanzunma ya cire rigar ta sama sai mai karamin hannun hakan ya sa

iyayen Walyn din saurin kawar da kansu,

Da idonsa ya yi mata magana, da idonsa ya isar mata da sakonsa kafin yake juyawa ya koma bangarensa,

Yana fita kasa kasa maman Walyn tace" Walyn, mijinki abubuwan da ya tara suna da yawa fa, shi ne rashin mutunci, shine fada, shine rashin kunya!

Walyn ta lumshe idannuwanta ta mike ta nufi kofa bata ce da ita komai ba

Auntyn walyn da ta kume da haushi itama bata furta su ci kansu ba ta kawar da kanta tana dan kada kafa , niya ne ta yi yau ba zata yi baci a gidan Walyn ba!

Walyn na zuwa ta yi niyar nufa dakinsa sai dai ji ta yi ya riko hannunta ba tare da ya yi mata magana ba sun nufi dakinsa,

Suna shiga ya shiga kokarin janye zip din doguwar rigarta ta atampa,
Tana tsaye tana kallonsa ya janye ya cire mata tana kallo yake kokarin janta bayi domin mafi yawancin lokuta haka ne ida  zai sadu da ita sai sun je sun salo wanka kafin yake baje kolinsa,

Ja ta yi ta tsaya tana dubansa, kwarai ta so ta kiye masa sai dai ba zata manta wani lokaci da ta ki karbarsa ba irin yanda suka kwashi tsayin lokaci yana daure mata   ba shi ba ita a harkar har sai da ta yi ta fama kafin ya sauko,

Rai a dan dagule ta nuna ai ita ba sai ta yi wanka ba,

Wardugu ya yi kalar tausayi ya ce" walyn wardugu, me yasa ba sai kin yi wanka ba? Kinga jiki da danshi danshi ya fi dadi tabawa😌,

Kanta ta juyar ta shiga kokarin hana kanta garza masa rashin mutunci, a sama take kwarai take tausar kanta kar ta saki hanya ta hanyar karta masa rashin mutunci,

Binsa ta yi suka yo wankan,
Suna fitowa ya jata saman bed domin shima yana so ya yi ya jishi ya saku,

Da sauri sauri ya shiga romancing dinta, sai dai ya lura bata bashi hadin kai domin sai dan zile masa take, hakan ya saka shima ya zo mata kawai kai tsaye wanda hakan na wahalar da ita ainun, idan a dadi suke yakan bita a slow da dabaru ne aman yanzun shima sai ya je ya darza son ransa,

Yana samun nutsuwa ta shiga tura shi,
A hankali ya dagata yana duban yannayinta

Rai bace ta ce" sai yanzu ka san da anfanina ko? Bayan ka gama wulakantar da ni da iyayena? Wardugu yaushe zan yi daraja a idannuwanka? Yaushe zaka daina wulakantani kai tsaye ? Dan ana fadin kai rigimame ne ai na yi tunanin kana iya zubawa kowa rigimarka banda ni!

Walyn,
Ya fada a hankali, kafin yake cin gaba" ki yi hakuri kin ji? Dare ne ki daina daga muryarki, sannan ko ba dare ba na fada maki ki daina magana tun karfi har tana fice tawa amo, mace kike, yar kwalisa ba wai wata kara zube ba, sai da na yarda da class dinki kafin na dauko ki, ki yi aiki da iliminki mana? Nifa ba ni na yi kamen nan ba! Aiki ne , doka ce ta hau du wani mai laifi,
To kawai dan nine sarkin son kai sai na ware mijin auntyn matata?,

Wardugu, kana da ikon warewar, in ka ware ba wanda zai daga maganar , kana da ikon zuwa ka fitar da shi a yanzuma ba wanda ya isa ya ja da maganar,

Wardugu ya tashi zaune, tuni hankalinsa ya fara tashi ya ce" kina nufin in na je na fido shi shikenan nine general Wardugu ba wanda ya isa ya ja da ni?

Walyn ta kale shi ta ce" karya na yi ne?

Wardugu ya girgiza kai ya ce" a niger, a duniya ba wanda ya isa ya zo ya titsiye ni walyn  aman in fa a hanyata ta dawowa daga fido shi na mutu na tarda general din baki daya? Ya zata kare min? Shikennan dan ina tsoron bacin ranki da na iyayenki sai in bata tsakanina da mahalicina? Walyn wasa kike da lamarina, kina aurena aman baki san waye ni ba! Kema kin kwana a cel bare wani tsohon dan kacare! Kin san yana me na kama shi? Tare da wa? Ku kiyaye fitina sai ku zauna lafia walyn tashi ki bar min dakina!

Rai bace ta diro daga saman bed din ta saka rigarta ta bar pant din  a nan, sai da ta kai kofa ta ce" inma me yake yi shi a bayanne yake yi  wa ya san me wani ke aikatawa da Alhinayettt!

Tana gama fada ta yi waje da sauri abinta,

Da mamaki ya rakata da kallo,
Ya so abin ya bata masa rai sai kawai ya yi watsi da shi ya mike yana murmushi ya shiga ya tsaftato jikinta ya dawo falo ya kwonta

Tun karfe bakwai aka farka a gidan Wardugu,

Ayya ta fito da yarta su sai gida,
Mahaifiyar walyn ta fito da kanwarta su mijinsu,

Mu.azam ya fito cikin dakakiyar shadar wardugu sai kanshi yake bazawa,
Walyn na daki tana ramuwar bacin da suka kwana zaune suna masifa da iyayenta,

Agaishat dake zaune jikin Ayya, domin yanda ka san mage haka take, ta lafe jikin Ayya kanta a konce kan cinyar Ayya take hangen yanda Mu.azam ke aika mata da murmushi, ya aske gashin kansa ya yi irin askin nan na samari ya yi kyau abinsa sai daukan ido yake, a baza abubuwan kari a falon na wardugu hakama na walyn,

Takunsa ya shaida fitowarsa,
Tafiya ce yake cikin isa da takama,

Yana fitowa du suka kai dubansu wajensa,

Wani irin faduwar gaba ne ya samu Agaishat, a ranta ta ayana ya salam,

Wardugu ya karasa direct wajen Ayya,

Yana tafe ne yana kallon yarinyar dake kwonce saman cinyar Ayyarsa, wace irin gaisuwa zai yiwa mamansa ne?

Yana karasowa ya ja ya tsaya, kaki ne jikinsa tun daga hular kansa har takalmansu na sojoji, sababi ne bugagu ne na manya da galolinsa a jiki na shaidar shi din waye,

Gilashin idonsa ya cire ya saka idannuwansa cikin nata,
Wani irin tsam ta ji a gaba daya jikinta hakan ya saka ta kankame hannun Ayya,

Da ido yake nuna mata ta matsa ya yi hugin din mamarsa , aman Agaishat bata gane ba domin ba.a taba haka da ita ba,

Idannuwansa ya lumshe, a hankali ya duka ya kai hannunsa ba wani dar ko tsaye tsaye ya kama hannunta ya aniya dagata daga cinyar Ayya,

Agaishat da ta yi mutuwar kwonce🤣 ta zazaro ido tana kallonsa tartar

A hankali ya bude bakinsa ya busa mata iska wajen idannuwanta ya karasa mikar da ita kafin yake yatsina fuska,

Ayya dake kallon ikon allah ta ce" kai daina taba min hannun yarinya ita ba irin wannan kawar taka bace! Meye haka zaka hanata hutawa?

Wardugu ya turo baki sai kace wani shagwababe ya duko ya dan yi huging din Ayya, a hankali ya ce" ni ni ne na wajenki kar ki manta Ayyana, ina kwana,

Ayya ta rungume shi itama tana murmushi ta ce" sannu da tashi Wardugu , aman ka ga yarinyata yanzu na fi ji da ita kan ku, ai ku maza ne ,

Ya yi murmushi yana kallon yanda Ayya ke kokarin maido da Agaishat jikinta,

Cika Ayya ya yi ya ce" amini abin kauna,

Mu.azam dake danna waya yana faman blok din yarinyar nan docter, domin ta whatsup sai kuka take masa ta fame shi fa walahi gatannan zuwa nigeriar ta dawo da shi a yi masa aiki, ya dan dagawa Wardugu hannu,

Wardugu ya girgiza kai ya ce" tashi ka ja ku bi bayana na raka ku, aiki ne da ni fa ka sani,

Mikewa ya yi inda su Ayya ma suka fice suka nufi mota ba tare da Wardugu ya koma bangaren walyn ba domin ya san ko ya je wata rigimar ce zasu yi  dan haka ya shige dankareriyar sabuwar rangrover dinsa ya ja gaba su Mu.azam na biyr da shi a baya,

Du inda suka zo gilas kawai yake saukewa ya yi nuni fa yana tare da motar su mu.azam har suka karaso gidan Ayya

Wata mahaukaciyar mota fara ce fake a kofar gidan, suna karasawa mai motar da ya juya keyarsa ya juyo yana kallonsu waya a kage a kunnesa

Datijo ne dogo fari kal, cikin manyan kaya yake ya yi rawani aman ya  bude habarsa, Gabansa ne ya yanke ya fadi gannin yaronsa cilo da ya malaka yanda ya fito daga mota ya zama cikenken namiji mai jini a hanci,

A hankali ya hango matarsa, aminiyarsa, mai kaunarsa , ta fito daga bayan motar daya ta karaso wajen wardugu,

A hankali wardugu ya rike hannayenta yana dubanta cikin ido ya ce " mahaifiyata, ban kama matar Marahut dan na hada ki rigima da shi ko dan daukan fansa ba, ta cancanci kamawar ne, ina rokon ki da kar ki biyewa kowa ciki kuwa harda Marahut!

Ayya ta rike kuncinsa , ta sakar masa murmushi ta ce" na sani, kaida ba mace ba mai zai saka ka yi aikin mata? Na yarda da kai Wardugu, mahaifinka kai ya zo nema ba ni ba domin ya san wacece ni, ba abinda zai hada shi da ni , ka je aikinka, sai dai ina kara jadada maka ka kiyaye bakin mutane , ka yi aikinka domin Allah ,

Wardu ya gyada kansa ya mayar da ita mota inda tuni mai gadi ya bude mu.azam da ya sada kansa kar Aba Marahut ya gane shi ya ja motar ya shige gidan Ayya

Agaishat dake zaune gaban motar a hankali take hangen Wardugu har ya shige tasa motar ba tare da ya nuna ya ga halitar wani a wajen ba ya tayar ya ja motarsa ya nufi wajen aiki

Murmushi marahut ya yi bayan mai gadi yana kokarin rufe gidan ya dakatar da shi ya tura ya shige daidai Ayya ta fito daga motar,

Kokarin tafiya take domin ta ga shigowarsa sai dai me,
Muryarsa ta tsinta , muryarsa mai gigitata, a hankali cikin sanyi ya ce" *asalamu alaiki anmi Wardugu!*

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

3️⃣0️⃣

Dan jim Ayya ta yi, kafin take dora kafafuwanta ta fara hawa yan matatakala kwaya uku dake sadata da balbalin bangarenta,

A nitse a dake ya kuma furta" du musulmin kirki ya dace ya amsa salama koda iya abinda zai fada kennan,

Ja Ayya ta yi ta tsaya tinawa da ta yi tare take da su Mu.azam, ko ba komai bata so yarinyar da ta dauko riko, ta dauka tamkar yarta ta cikinta ta yi wani tunani a kanta, dan haka ta ja ta tsaya ta juyo a nitse tana kallonsa ido cikin ido ta ce" amen wa alaika salam,

A hankali ya kai hannunsa jikin karfen ginnin yana kallonta, matarsa uwar dansa, auren soyaya suka yi ba na hadi ba, auren fahimtar juna mai cike da nishadi, sai dai ya yi sake, ya yarda
```

laifinsa ne hakan ta faru, a hankali ya ce" wa ya baki izinin yin tafia har kasar agadez kauyen agadez timiya ? Kika je kika yi har kusan wata biyu? Anmi wardugu banda fitar ta cikin garin Niamey yanzu kuma har kin fara yin ta nesa haka? Ba dai a so zuciyata ta huta .....
Ya karashe yana dan sada kansa,

Mamaki take, al.ajabinsa take, uhum lalema, me yake nufi da ita? Kennan yana bibiyar rayuwarta ko me?
Fuska ta yatsina kafin take fadin" gidan nan ban yarda Wardugu ya saka ko sisinsa ba dan kar watarana ka zo da takamar danka ya gina,

Marahut ya ce" bayan Allah ya halita min ziyarta inda gonata take a duk lokacin da na yi niya?

Haushi ne ya cika Ayya, yana nufin ita, dan kuwa ai matayenku kamar gonakinku ne,
Dan juyawa ta yi ta ce" ka tarda shi inda yake ba gidana ba,

Dan daga murya Marahut ya yi , domin ta tafi ya ce" ki kiyaye fita kai sake ko dan yarmu da kika dauko kar ta koyi yawo ba izinin miji idan mun yi mata aure!

Wani irin bude kofar ta yi ta rufota da karfin gaske wanda da ba dan glas din mai nauyi kuma mai karfi bane da kasa zai zubo baki dayansa.

Murmushi ya yi, a hankali ya sauko wajen su Mu.azam dake tsaye cirko cirko,

Mu.azam ya gama yarda wajen wa Wardugu ya yi gadon abubuwa,
Gashi mahaifinsa ya kai shekaru sitin da yan kai aman yana abubuwa tamkar wani bajimin matashin sarki?

Yana karasowa ya saki fuskarsa sosai ya mikawa Mu.azam hannu,

A mutunce Mu.azam ya gaisar da shi,

Marahut ya amsa yana dubansa kafin yake kai dubansa wajen Agaishat, da yaren buzanci ya ce" ina murna da kasancewa Abanki yarinyata,

Agaishat ta ji abin sabo, abin ya zo mata a bawai, ikon Allah, mutun ya wannan, ya kirata da yarinyarsa, gashi fari karkarkar ita kuwa baka kirin aman bai nuna kyamata ba, harma ya fada mata ya yi murnar kasancewarta yarinyarsa,
Baki kawai ta saki tana kallon kama, kai har yannayin girman jikin domin Ayya bata da girman jiki irin wannan ,

Hannunsa da ya dora a kafadarta na dama ya ce" sannan ki yi ta kulawa da kanki ki yiwa Ayyarki biyaya, zan yi tafia sai na dawo ...........

Agaishat da wata kwallah ta tarun mata a ido tana kallo ya fice a gidan a kafarsa domin a waje ya bar motarsa,

Yana fita ta juyo wajen Mu.azam, da tsananin murna ta ce" ka ji me ya kira ni? *Yarinyarsa*,

Mu.azam na kallonta shima da murmuahin a fuskarsa yana kallo hawayen murna ya zubo daga idannuwanta,
Cike da zumudi ta ce" kuma kuma yace ya yi murna da kasancewata tare da su, yaya Mu.azam ni *BAK'A*,

ai bai kai ga bata amsa ba ta cikashi ta shiga taka matatakalar da gudun tsiya dan zuwa fadawa Ayya cike da murna,

Sai dai tana shiga ta tarar da Ayya zaune ta hade rai tamkar an yi mata mutuwa, yannayinta ya nuna tana cikin yannayin bacin rai mai tsanani

A hankali ta shiga dan takawa dan karasawa kusa da Ayya,
Tana zuwa ta dan duka tana kallonta murya a sanyaye ta ce" Ayya, lafia?

Ayya ta dago ta yi mata wani kallo na ta barta,

Agaishat bata fahimta ba ta ce" Ayya, *WANENE WANNAN?*

Ayya ta zuba mata wani kallon, rai a hade ta ce" ki je dakinki Agaishat!

Agaishat ta mike da sauri tana kallon Ayya kafin take juyawa da sauri ta nufi dakin nata a matukar tsorace,
Tana shiga ta karasa bakin bed ta tsaya jikinta na rawa, Ayya bata taba yi mata haka ba, dan haka hankalinta ya tashi ainun,............

Wardugu dake tsaye kan kafafuwansa tun zuwansa wajen aiki yana fama da jama.a, tun daga manyan mutane masu fada a ji da suka biyo sahun nasu, da tsagerun mutane da suka zo belin yan uwansu ko abokai, sai bayin Allah talakawa da yayansu suka kai su inda basu taba tunani ba, suma sun zo da kokon bararsu kuma cikin ikon Allah wardugu na sauraron mutane du wanda ya ga abin ba wani bane a nan take yake salamarsa da kwakwaran kashedin idan suka kuma hadewa a irin wannan waje ba zatai masa da kyau ba,

Daga karshe dai Wardugu na bincike ne cikin nutsuwa yana salamar mutanen da basa bushe bushen nan bisa kashedinsa wanda da kansa yake yiwa mutun ido da ido ba aike ba!

A hankali ya fara kawowa wajen masu zuwa dan kawai su kwale, wani saurayi aka shigo masa

da shi, yana zuwa ya zube kasa ya shiga gaisar da Wardugu,

Warsugu dake kallonsa, kana ganninsa ka san ba wani dan mai shi bane, aman ya tashi ya saka kansa a rayuwar halaka idan an yi magana ace kadara, ace Allah ya dora,

A dake ya ce" tashi ka zauna saman kujera,

Da sauri saurayin ya tashi ya zauna sai sasada kai yake tamkar ya yi karya gaban sarki, tsoro yake a ransa domin a gaban idonsa akaiwa wata dukan tsiya wanda ya sa har ta sume dan kirikiri ta yi ikirarin ita ko wacece ta tofar da yawu ta dura ashar ta ci alwashin gyatiminta zai zo ya fitar da ita har sai uban gidansu Wardugu ya bata hakuri hakan ya sa su kuwa suka nuna mata da gidan maza ta shigo ba gidan yara ba, suka murza kwonji a jikinta har ta some, labarin da ya kaiwa Wardugu da ya fito a gaban mutanen nan na cel ya zuba mata ruwa da kansa wanda hakan ya farfado da ita, sai dai tana tashi ya wanka mata wani marin da ya mayar da ita duniyar suma sannan ya nunata da yatsa ya ce" ban so tonawa kowa asiri ba shi yasa na saka aka shigarmin da iyayenku daga wancen dakin wanda ba wanda zai gane in an shigo da kai wanene mahaifinka kuma me ka aikata ba, sai gashi kin tonawa mahaifinki asiri a matsayinsa na dan siyasa kin kama sunansa har kin nuna mana halin kodin! Dole mu kai kararki wajen alkali kin zagi soji!
Haka aka kwasheta aka jefata cikin cel din ya koma ya ci gaba da aikinsa dan haka ne ya sa wannan saurayin kamar ya kwonta dan kadabi,

Wardugu ya ce" yaya sunanka?

Saurayin ya kalo shi kadan ya sada kai ya ce" sunana Murtala Tasiu,

Wardugu ya gyada kai ya ce" tun yaushe kake zuwa wardugu place? Kai da wa kuke zuwa? A nawa kuke biyan kudin shiga? Du sati sati kuke zuwa? Da yan mata kuke zuwa?

Murtala ya ce" ba.a fi shekara biyu ba,,
Ni da dan gidan Elhaji Dahiru muke zuwa,
Aa ba kowani sati ba dan kudin shigan da muke biya shima ba kulun yake da shi ba jika goma goma, sannan in mun shiga ga kudin kashewa , aa iya mu muke zuwa a can muke haduwa da yan mata kowani sati akoy a ciki,

Wardugu ya tsare shi da ido ya ce " tun daga bakin lokacin ka fara busa kodin?

Murtala ya shiga raraba ido, ya daga hannu zai fara rantse rantse Wardugu ya ce" murtala, ka fada mini gaskiya mai yiwuwa ka samu sasauci!

Murtala ya ce" oga, ka rufa mani asiri dan girman Allah, mahaifina gajiyaye ne, sai na bi abokin nan nawa yake bani wani dan abin na je na ciyar da mahifina da kanwata, kanwata bata gani,

mahaifina kuwa ya tsufa, ba a son raina nake saka kafata wajen nan ba,

Wardugu ya ce" ban tambayeka labarinka ba Murtala, ban yi niyar wulakanta ba ina rokonka kar ka wulakantani, kar ka kawo mani shirme a nan , da farko dai du idan ka ga soji rikeken dan tasha ne domin tashanci koya mana ake mu shanye sai dai muna aiki da shi ne kan tsari, na jima a aikina hakan ya saka ana yi min karya nake ganewa, ka bani amsata ko mu baje basirar rainin hankalin ni da kai!.............

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

3️⃣1️⃣

Da sauri Murtala ya ce" Eh eh , tun daga lokacin da muka je abokina ya siya ya saka na taba tun daga lokacin nima nake sha ,

Wardugu ya shiga gyada kai ya ce" kana iya fita,

Dan mikewa ya yi, sai ya mike sai ya dan duduka sai da wani soja ya shigo ya finciko shi ya mayar da shi cel,

Da mijin Auntyn walyn aka shigo,
Mutun har mutun, sai sasada kai yake na kunya,
```

Warsugu ya tsare da da ido, wai tun a nan duniya ka kasa hada ido da mutanen da basu baka ko cin wuni daya ba, ya zaka kare da wanda ya haliceka ya baka dukiya dan gannin ya zaka tafiyar da ita, ya ara mata lafia, gani  da ji, ya baka ikon motsi, ya baka damar magana, ya kaika kasar da ba yake yaken yu da kulun wa.inda zasu iya tayar maka da hankali , ya baka isashen lokaci dan kawai ka bauta masa ka yi masa biyaya, sai gaka tsofai tsofai a gidan badaka tare da yar shilar yarinya ta tube kusan zindir tana maka rawa tana ciyar da kai gasashen kifi, shine zakana wani sada kai a gabana kai ga cikenken dan iska! Du wardugu ke jifansa da wani matsiyacin kallo sannan yana ayyana du haka a ransa,

Wardugu ya ce" ya sunanka malan?

Mijin aunty da mamaki ya dago yana kallon wardugu ya ce" haba haba wardugu, ai ko me ake a san na gida, a fitar da na gida, ka yi hakuri kure na aikata ba zan kuma ba , ka salame ni na koma ba tare da wani bama ya ji abin kunya ne ace ka rufe mijin kanwar babar matarka!

Baki wardugu ya dan daga na mamaki, ka ji wani dogon bayani wai mijin kanwar babar matata, Kai ya girgiza a ransa ya yi murmushi, a fili ya kuma furta" ya sunanka malan!
Yana mai dagowa da yanayin dakewa,

Mijin auntyn walyn nan ya fara zufa, yana gagawar magana ya ce" tototo, sunana Lawali , Elhaji lawali,

Wardugu ya ce" me ya kai ka Wardugu place? Kai da wa ka je? Me ka je yi? Tun yaushe ka fara zuwa? Me ka lura ana yi a wannan waje?

Lawali ya ce" ni kam wannan waje na je ne bisa tsautsayi da rabon a yi, domin dai yarinyar nan na so na aura sai take shaida min na kaita mu sha iska, to da muka je shikenan sai muka mayar da wajen wajen zuwanmu lokaci zuwa lokaci yanzun dai an kai shekara uku,
Sannan a wannan wajen gaskiya na lura ana abubuwan da bai dace irin ahaye shaye, wannan da ka ganni tana yi wai karamin ne, eh wanda muke yi shine karamin ba Allah ja da kwana....
Ya karashe yana jinjina

Wardugu ya jinjina kai, ya ce" lawali kada daga Kokin ne?

Da sauri ya dago yana duban wardugu, ya ce" bilahilazi ban taba ba, ai ni ko warinta na ji juwa ke kayar da ni, ka rufa mani asiri rashin jina bai kai can ba,

Wardugu ya dago yana dubansa, wai rashin jinsa, kai ya girgiza da hannu ya yi masa nuni da ya fita,

Yana kokarin kara magiya Marahut ya shigo inda sojan nan ya biyo bayansa yana dan kame kame ya rasa me zai yi, su dai ba wanda bai san oga Marahut mahaifin uban gidansu ba, shi ya isa ya masa iyaka ne? Tun daga babar kofa ya samu shigowa ya ratso du zone na control ba.a

hana shi ba sai shi tal dake tsaye dan kula da bude kofa da kuma rufewa da kyau ne zai hana shi shigowa?

Kallon Lawali Marahut ya yi kafin yake girgiza kai yana murmushi daga cikin rawaninsa,,
Kai sade Lawali ya fice domin ya ji kunyarsa ainun

Marahut ya bi tsararen tankamemen office dan nasa, bMarahut ya ce" ya aka yi ka canza kanshin turarenmu ne Wardugu? Kuma ya aka yi ba hotona a office dinka bayan kai din dan halal ne koda shege ai ado yake da ubansa bale dan halal ,

Wardugu dake ta cika takardu yana dan dana laptop bai ce da shi ci kanka ba,

Marahut ya ce" Warsugu Abanka ne fa ni ? In ba ruwanka da mutane su ga kana min haka ba ruwanka da Allah ne??

Wardugu ya ajiye biron dake hannunsa ya dan shafa kansa ya dago da kallonsa wajen mahaifinsa wanda a kamaninsu haske ne kadan ya dan fi shi domin farin wardugu ba irin cancan din nan bane,
Warsugu ya ce" Aban Wardugu ra.ayi ne ya sa na daina anfani da turaren da ka sanni da shi, sannan ni ba mace bane da zan kawo hotonka office na buga, kuma shegema mutun ne!

Murmushi marahut ya yi ya karasa wajen kujera ya zauna ya ce" to ka fido mani matata mu tafi gida Wardugu,

Wardugu ya yi murmushi a bayane shima ya ce" ba zan so shakar iskar da kuke shaka ba ko na second daya, sai dai ya zama dole ne, matarka mai laifi ce

Meye laifinta wardugu? Me ta yi da tsanani haka? Ka san yara da kin ji suke,aman ai koma me ta yi ina gannin sai mu kashe mu birne abinmu a tsakaninmu ko wardugu? Marahut ya fada yana dubansa

Wardugu ya ce" zan so haka, sai dai ka ga rashin jin nata ne ya yi kamari, tana shigo da kwaya ne tana siyarwa wannan ba boyayiyar shaida bace, abinda nake bincike kawai na samu hanyar da take shigo da ita ko wanda ke bata sai na mika su kotu koda kuwa *kai ne*, sai dai ban san ba yin hakan ko Allah zai kama ni da shi?

Da sauri marahut ya ce" Quoi? (What?), wani irin kwaya? A Wardugu place din? Innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, wardugu ka kara mani haske a lamarin nan

Wardugu da ya ji ya dan samu sasauci, domin a sama yake, jininsa a saman akaifa, tsoro yake kar a je rinjayar nata ya kai ta saka Marahut a wannan harka? Aman yanzu ko ba komai ya ji dan sanyi a ransa dan kuwa har gobe da sunnan mahaifinsa yake anfani,

Wardugu ka fada mani mana, Marahut ya fada yana dubansa da yannayin serius

Wardugu ya yi umarnin a kawo AISATA,

Shigo da ita aka yi, dare daya tak du ta fara fita hayacinta abinka da wada ya saba da hutu,

Tana gannin Marahut ta sauke ajiyar zuciya mai nauyi kafin da sauri ta nufi wajensa ta saki kukan kirsa,

Tana kukan ta ce" ka ga abinda Wardugu ya yi mini? Wannan wani irin tsana da cin mutunci ne? A gaban jama.a ya saka mini anker tamkar wada na yi sata, ai a tunanina ya dace komai ya fice tsakaninmu ko me na yi sai ya hukunta ni a gida ba wai a gaban duban mutanen da zasu yi min dariya ba,

Hannunsa ya saka ya dagota daga jikinsa yana dubanta, kadara, Aisata kadara ce mai wutsiya, a dalilin Aisata ya rabu da farin cikinsa da girmansa a idannuwan iyalinsa, maciya ce Aisata, Aisata zinari ce,
A nitse ya ce" me da me kuke aikatawa a Wardugu place?

Aisata ta yi tsam kafin ta shiga cicira ido ta kali dan ta kali uban, cikin yannayin barikinta ta ce" me muke yi kuwa banda neman kudi? A wardugu place ba abinda muke yi,

Wardugu dake rubutu a takarda ya dan yi tsam ya dago ya dube su ya maida kansa ya ci gaba da aiki,

Bai jima ba ya daga wayar office din ya danna kira,

Cikin girmamawa ya gaisar da jujun kafin yake fadin" mai girma na gama nawa binciken, yanzu ana kawo maka takardu ka duba, daga nan na mika maka su kawai ,

Amsa shi ya yi kafin yake kashewa,

Marahut da ya gama fahimtar wayar da Wardugu ya yi shima yana dubansa, cikin yannayin nutsuwarsa dai ya ce" har yanzu baka daina jin haushina kan Aisata ba?

Wardugu ya juyo da sauri, ido ya zazaro baki daya kafin yake mikewa ya tofar da yawu a nan cikin office din ya ce" kan wannan? Ya fada yana nuna aisata,
Ya girgiza kai ya ce" ai koda me daraja ce bata kai na yi anfani da damata dan wulakanta ku ba, ka gane laifi ta yi, idanma baka yarda ba ai kai din oga ne kawai ka je wajen wa.inda zan mikawa takarda idan sun baka matarka ruwansu ni dai ai na tono barnar ko? Ka fi kowa sannin waye wardugu domin kaine mutun na farko da ka rikeni a duniya bayan likitar da ta fitar da ni daga cikin mahaifiyata!

Yana gama fada ya ja kys din motarsa ya dauki gilashinsa ya fice a office din yana mai jin haushin yanda mutane ke magiya kan a bari a ci gaba da yada barna!

Jikin Ayya ne ya yi sanyi bayan korar Agaishat da ta yi, a hankali ta mike ta nufi dakinta tana mai jin wani iri me ya yi zafi harda laifin wani zai shafi wani?

Tana zuwa ta shiga da salama,

Agaishat dake zaune kasa ta dora kanta a gefen gado tana jan carbi da hannunta ta dago da sauri tana kokarin mikewa tana duban Ayya,

Karasawa Ayya ta yi ta riketa ta zaunar da ita gefen gado,
A nitse ta ce" ki yi hakuri yar gidan Ayya, ba zan kuma yi maki irin haka ba ,

Agaishat ta sauke ajiyar zuciya tana dubanta,

Ayya ta ce" bara na baki labarin mu..... na fada maki wacece *AYYA?*, na fada maki waye *MARAHUT a rayiwar Ayya?*, na fada maki wanene *WARDUGU* sannan wani irin girman daraja yake da shi a rayuwar Marahut da Ayya? Yarinta bara na baki labarin da ba kowa ya sani ba................

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---
```

32

labarin Wardugu da tushensa a gajarce
.
........ ..................

Sunana *Zanaba SHAU*, sunnan Mahaifin Wardugu *MARAHUT ELUM*, ni marainiya ce gaba da baya, na taso a hannun kakata ta wajen uwa da ta yi min saura,
Marahut dan gata ne gaba da baya, ya kasance a lokacin anguwarmu daya domin gida uku kawai ke tsakaninmu,
Tun wayona bai gama fahimtar Marahut na sona ba har na gane domin kiri kiri idan na yarda wani lokacin na yi dan shirin atampa na yafa mayafi na fito zai rufe ido ya kora ni yana masifa,
A anguwa ana girmama kakata domin mace ce da ta san girmanta, ba abinda ya shafeta da abin hannunka, ga mutunci ga zumunci,...du juma.a zaki ga an kawowa kakata abinci daga gidajen anguwar nan ciki kuwa harda gidan su Marahut inda mahaifiyarsa shuwa arab ke turowa kakata da gurasa ta kasa, irin wace ake yi a kasa ta ainahin da miya mai dadi harma ki ga an zuba tawa miyar mai magi domin a lokacin an hana kaka shan magi.

Sosai muke soyaya da Marahut, duk da wani lokacin nakan zauna na yi shiru ina tunanin Marahut na so na kamar yanda nake son sa kuwa?
Hakan sai ya tayar min da hankali sosai domin Marahut dai jarumin namiji ne mai cike da abubuwan da mata ke marari har suna kai wawa, harma wani lokaci na kwatanta masa....
Tsareni ya yi da ido kawai, zuwa wani dan lokacin ya mike ya fice abinsa hakan ya haifar min da faduear gaban ko ya yi fushi ya bar ni ne?

Kwana biyu tsakani na dawo daga makarantar dare islamiya da nake zuwa a kusa da mu na tarar da kakata zaune tana jan carbinta da rufarta bata kwonta ba, ba kamar sauran lokutan ba,

Da sasarfa na karasa wajenta dan gannin abinda ke damunta sai dai ina zuwa ta rike hannayena tana kallona ido cikin ido ta ce" Zannaba, kina ta adu.ar neman Allah ya baki miji na garin nan kuwa?
Na amsata ina dubanta da wani irin yannayi ta ci gaba" an zo neman auren ki daga gidan Elum, Zannaba kin ji zuciyarki ta aminta da Marahut?

Wara irin kunya ce ta diro mani, domin fa Agaishat yata tubawa na da muguwar kunya, batuben mutun na da kunya harda ta mamaki, hakan ya saka na sada kaina kasa harma jikina ya fara rawa,

Kakata ta ce" kul, na hane ki da ki yi haka da ni, ke kawai gare ni kema ni kawai na rage maki, Allah shi ne gatanmu, zan so ace na bar ki hannu mai kyau, dan haka maza bani hankalin ki mu gama magana,

In takaice maki a wannan rana bamu kwonta ba du sai da muka dauki niyar istihara wace cikin kwana uku hankalin mu ya gama kwonciya har ma muka aminta da auren nan,

Marahut ya yi min gata , agaishat ya kai kudin aurena ya yi min kayan da aka jima ana labarinsa, aka daura aurena irin na kowace yar gata inda kakata ta bada mamaki ashe tana ajiye da sarkokin aurensu ita da mahaifiyata, ta kai aka buge akai min tafkekiyar sarka da abubuwan hannu na zinari irin na kowace batuba yar gata, sannan ta fitar da kadarorin mahaifanna harma da nata gaba daya ta raba aka yi min kayan daki sauran ta damkawa mai anguwar anguwarmu amana,

Wsshe garin auren mu Marahut ya dankara min wata makekiyar sarka ta zinari tatare da kwacakwablarta bisa al.adun tubawa wanda hausa ce cikin hausa, ba.a jima ba muka daga dan komawa bakin aikinsa inda aka maida shi domin baban likita ne kuma yana harkar kasuwanci da kiwo.....

Mun kasance cikin farin ciki, mutunta juna, da kaunar juna, muna tafiar da rayuwar aurenmu bisa tsarin islama muna kiyaye du wani abinda zai firgita mu sai dadaykun da baza.a rasa ba na yau da kulun!

A haka na samu cikin wardugu,
Mu kai rainon abinmu har na tashi haihuwa inda Allah ya taimake ni na haihu a hannun mijina a asibitin da yake aiki da taimakawar nurse..
.
Mun koma gida dan zanen sunna, nan Marahut ya gabatar da sunnan *WARDUGU*  a matsayin sunnan da ya zaba,
Kowa ya jinjina lamarin sai dai ikonsa ne, dansa ne, aman sunnan Wardugu linzami ne ga mutun mai zuciya, mai fada, mai balaki, kai ba.a zama lafia da mai sunna wardugu, Wardugu! HUM, ko canfawa ne mun yi kuma yana bin mu, kwarai zahiri ne Wardugu duniya ne guda, ba sai an koya masa ba da abinsa aka haife shi.......

Ina wanka a gida wajen kakata, tana kula da lamarina sosai da sosai, wata rana muka wayi gari da kyautar Allah, inda mutuwa ta sake zagayowa ta tsame min wace ta min saura a tarihin iyayena,

Ayya ta yi shiru ta share kwalar da ta zubo mata,
Agaishat da ta yi lamo ta dora kanta a hannun Ayya, Ayya ta ci gaba" Agaishat na ji mutuwar baiwar Allahn nan, domin ni ita ce duniyata, ko me na kwaso ita nake fadawa a nitse ta warware min, ta rasu ta bar ni da jaririn da a lokacin bana iya daukansa da garaje dan girmansa masha Allah, ta bar ni da dan labubun yaron da yakan calara kuka wai shima nice mahaifiyarsa, na ga rana na godewa Allah,

Agaishat ta kara jimke hannun Ayya itama tana jin yanda hawayen ya zubo mata, Ayya baiwar

Allah, bata da kowa gaba da baya, ashe du yanda mutun ya kai ga malakar arziki bashi da cikeken farin ciki na yanayin rayuwar yau da kulun?

Ayya ta ce" na dawo ga marahut, bani da kowa bani da komai sai Shi a nan cikin duniya,
Bayan an yi bakwai muka juya garinmu inda na dauki girma na ajiyewa kaina na karfi da yaji na ci gaba da karatun likitana da nake yi a Ensp,

Can tsakiyar dare nakan dadaba Marahut, idan ya farka sai nace" Marahut, kar ka wulakanta ni a duniya, kai ne duniyata, kai ne farin cikina,

Yakan riko ni jikinsa ya ce" ban aure ki ba sai da na gane ke ce lumfashina, a duniya baki daya me ya kai lumfashin mutun tsada? Ba zan yi garajen gannin hawayenki ba sai na kadara!

Magangannunsa da alkawarurukansa suka saka na samu nutsuwar zuciyata harma na warware na ci gaba da shagulgulana na yau da kulun tare da yarona,

Tun Wardugu na da wata bakwai ya mike, yana tafiya da kafafuwansa digir digir tamkar dan gwari,
Du inda na yarda na je da shi idan ya damki yaro ko matashi sai an kwace da kyar,
Ya kasance ba.a gardama da shi da ya warware, yana fama da ciwon athsm wace in dai na yarda ransa ya baci toh fa a kadan mu yi kwana uku a asibiti domin athsmar nan zata tashi ne ya kasance daga ta kwonta sai ta kuma tashi domin ba zai kwontar da hankalin nasa ba,

Wardugu zuciyar mahaifinsa ne, domin daga shi ko batan wata ban kuma yi ba, muna bibjyar komai nasa tamkar ranmu, kai har bama kawaici a nuna soyayarsa,

A haka Allah ya hada mu da baba tsofo, wanda kawai salama ya yi yace yana bayar da magungunnan hausa ne,

Nan muka zanta a bayan idon mahaifin Wardugu domin baya son lamarin hausan nan wai tsoro yake ya taba masa reins,

Cikin ikon Allah ya ki karbar kudina, muka ajiye magana idan Wardugu ya samu lafia zan yi masa kyauta,
Yakan zo lokaci zuwa lokaci ya kawo mana magannin da cikin ikon Allah muke bashi da nonon rakumi sabon tatsa da sasafe, tun ina boyewa har na bayannawa Marahut shima ya kama mani domin sauki kamar da wasa Wardugu na samu a hankali a hankali har ya daina lumfashi da bakinsa ya dawo yi da hancinsa,

Agaishat na kasance mutun mai shegen son mutane, ko dan na sakawa kaina bani da kowan nan a duniya sai Allah sai mijina? Ya kasance son yaya da yawan kula zumunci da jama.a,
A haka na hadu da babar aminiyata matar sarkin agadez, na hadu da kawata ta damagaran hajia Falmata, da sauran su,

Wardugu rashin lafiarsa kawai ya warke aman halaya na nan, a haka aka tsahe mu aka maido mu garin nan inda kwata kwata baba tsoho ya bace min na neme shi na rasa har muka taso aman abin na tsaye a raina sannan ina yawan tambaya,

Kwonci tashi wardugu ya tashi da niyar shi fa soja, soja, hakan ya sa mahaifinsa ya sama mana waje a Babar makarantar sojojin niger wace ke a kwalo, wace tun yaro na karami ake kai shi shikennan shi da iyayensa sai jifa jifa,

Karatu yake, sannan kwazo yake da shi ko a filin training,
Hakan ya sa babansu yake kaunarsa harma yake zumunci da mahaifinsa

Wardugu na da shekara ashirin da biyu ya fito gagarumin comandan, jikaken saurayi, kaukauran namiji, zakin zamani, yaro da kudi kamar yanda ake kirarinsa.......

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

3️⃣3️⃣

To tunda Wardugu ya dawo sai kuwa yan mata suka ce bismillah, ba kalar wace bata zuwa , kin dai ga yanda yake uwa kurman nan? Toh haka zasu zo su karaci haukansu sai dai su yi su gama su tafi,
Ban san ya aka yi, ta ina aka yi suke kawance da wannan mai sunna Alhinayettt wace ni hakanan nake gannin karya ne ba wani kawance may yiwuwa soyaya suke ba halin aurenta
```

domin aurensa bai wani jima ba,

Ana haka ya amincewa yarinya daya soyayarsa, yarinyar da ta yi kundubala da sauran yan matan,
Soyaya suke ta hauka irin soyayar yayan zamani, ni ba zan shaidi yarona ba ba kuma zan ce yana aikata masha.a ba, aman a lokacin da yake kwana a gidan nan har kwana ta sha yi a wajensa dan kuwa sai da na rufe idannuwana na ci masa mutunci sannan na daina kamata a dakinsa,
Waye shi da zai rantse min ba abinda ya shiga tsakaninsu? Namiji ne, ita kuwa mace, sun kadaice a wajen da ba kowa sai su sai Allah, ai hankalina ba zai dauka ba!

Ire iren abubuwan da sukai ta faruwa kennan da yarinyar da ta gama kwana gidan mu, mamaki nake da tsoro, Wardugu ina ya zubar da kunya irin ta batube? Gaba daya wannan karatu da ya yi ya saka du ya zama wani kiritace wani tsayaye! Sam ya zubar da al.adu da dabi.un tubawa idan na yi magana sai yace ai ba wani adini bane, shi gaskiya ya girma a birni ba zai ci gaba da rayuwa irin na daji ba, ! ALLAH ya shirya,

Ana haka ya tafi karo karatu inda suka hadu da mu.azam suka kula zumunci mai ma.ana, a can ya hadu da matar da yake aure yanzu wace a lokacin ba irin azabar da bata sha ba domin shi soyayarsa tana kan *AISATA* ,

Aisata? Agaishat ta tambayi Ayya,

Ayya ta ce" kwarai Aisata dai wace ubansa ya aura,

Agaishat ta ce" aa, Ayya na shiga rudani,

Ayya ta ce" bara na warware maki,....

Haka kawai mun ci gaba da fahimtar juna alhamdulilah har wardugu ya dawo daga tafia,
Nan ya zo da maganar a tura wajen yarinya a tambayo aurenta,

Tashin farko ya dira cewar ba da yawuna ba, kuma in har ni na haife shi ba za.a yi haka da ni ba, domin yarinya bata da da.a , zan so matar da zai aura ta fari ta kasance mutuniyar kirki ko dan fadar adini ku zabawa yayanku iyaye na gari,

Nan fa aka shiga tashin hankali, yarinya ta zo har gida ta tsire ni, nan ta yi ikirarin cewa" AYYA kike ko wa? Kin dai ganni, kin ga yanda nake, nice farar mace , kwakwa! Dole na shigo gidanki ko a sarakuwarki ko a kishiyar ki!

Abin ya bani mamaki, zuciya ta kama ni na tunkareta kafin take ankara na damketa, ina faman ihun sai na nuna mata ruwa ba sa.an kwondo bane malalaciyar banza da wofi sai ga Marahut

ya shigo da sauri

Kwaceta ya yi daga hannuna kafin yake fadin" ke Zannaba, baki da hankali ne? Kike ikirarin yarinya bata da tarbiya ke kina iya rantsewa waye malamin waye dalibin tsakaninta da dan naki? Ki shiga tatayinki ki daina abu tamkar wata yarinya karama!

Agaishat , a wannan rana, a gaban wannan yarinya Marahut ya wulakanta ni, ya yi min tas abinda bai taba shiga tsakaninmu ba,

Ke dai kwana biyu tamkar kura ta lafa, domin Wardugu da ya ga na nace sai kawai ya basar ya yi biris ya shiga wata sabgar gaban nasa inda ya fara kula Walyn,

Ba.a wani jima sosai ba, domin ba .a yi wata hudu tsakani ba Marahut ya zo da maganar zai yi aure,

Agaishat ban wani nuna halinmu na matan tubawa ba, na ja ajina na yi masa fatan alkhairi, na shiga rokon Allah da ya rufa min asiri kar a je dan haihuwana ya tsaya ne wani abin zai tunkaro ni,

Sannu sannu sai abubuwa ya fara bilo mani, halayen Marahut suka shiga canzawa,
Ya fara cika dare sosai a waje kafin ya shigo, ya dawo ya fara kin cin abincina sai yace baya jin yinwa tamkar wani inji,
A hankali ya kaurace min,
Na sha zuwa na duka nace da shi" menene damuwar? Wani abin na yi ne? Dan Allah ka yi hakuri , har ka manta alkawarin fa ka yi min? Marahut kace nice lumfashin ka, ka yi hakuri ka dawo min kamar da, ni ban wani hanaka aure ba, aman kar ka tayar min da hankali,

Marahut sai kawai ya yi min murmushi ya mike ya fice,

Du abin nan Wardugu bai san ubansa zai kara aure ba sai wani lokaci ya ji a gari, a lokacin ya garzayo gida da sanyin safiya ya tambayi uban, ashe auren ma a ranar sauran kwana biyu ni banma sani ba,

A wannan ranar na ga tashin hankali, na ga rikici, domin Wardugu idannuwansa sun rufe hakama na ubansa, ke sai  da na fita a guje na kira direbobi da masu gadi da yaren gida du suka shigo suka yi kokarin shiga tsakannin uban da dan dan kuwa Wardugu ya rike wuka hannunsa yana ta balaki!

Agaishat, wannan bai isa ba sai da aka shigo da amarya Aisata, aisata yar buzaye, aisata yarinya kyakyawa,
A ranar wardugu ya yi dan karamin hauka, ya ja iska ya zo kusan babansa ya ce" aban Wardugu ka sake ta, ka rufa mani asiri ka saketa , kar ka yarda wani abin ya shiga tsakaninka da ita, Aba, wannan bata da tarbiya, bata da haramun! Abanna  ya zaka kawo macen da ta

gama talatarmin da kanta a irin yannayin da ta fado duniya ni danka a matsayin matarka? Haba Abana, me mukai maka da zafi haka?

Marahut ya dube shi ya ce" ita ba mutun bace? Kun haihu da ita ne? Na yi niya ina sonta na aureta da kudinka ne? Ka bini a sannu Wardugu, ni na haifeka kar uwarka ta zigaka ka kauce hanya!

A lokacin ni tuni na fara gannin jiri, ni Marahut? Na sha dukan kirji nace ni mijina dan goyo ne, ba zai wulakanta ni ba, sai gashi haka ta faru, ni ba aurensa ya dame ni ba, tau da gobe ai sai Allah Allah wacece ni da zan ce ba za.ai min kishiya ba? Damuwana irin auren da ya yi, ya yi shi dan ya nuna min iyakata? Dan ya wulakanta ni? Ko wani abin ke tsakaninsa da yaronsa mai zafi haka?

A lokacin Wardugu ya fara wani irin numfashi, idannuwansa suka shiga canza launi zuwa ja, suka cicika da kwallah, ina gannin hakan na tisa shi gaba da kyar na samu muka shiga motarsa na ja muka nufi gidansa,
Muna zuwa muka tarar da Wakyn ta zo nemansa, a nan ya sauke haushin kanta domin sai da ya bala mata hannu du ya kusan canza mata halita baiwar Allah da kyar aka kwaceta,

Kin ji marabina da gidan Marahut domin akai ruwa aka yi iska Wardugu ya hau, ya gindaya rantse rantse, ya juye, nima fushi, mamaki, tsoron lamarin maza ya saka na yi watsi da shi na rungumi yarona wanda na san a duniyarnan ni ce duniyarsa ,.....

Ayya ta karasa tana dan shafa kan Agaishat,

Agaishat ta dago fuska shabe shabe da hawaye,, tana duban Ayya , ta sani bata da damar da zata iya tofa wani abin a wannan lamari domij ta yi imanin ba komai Ayya ta fada mata ba, tabas ta boye wani abin ko dan karancin shekarunta,
Sai dai wannan lamari ya tuna mata mahaifiyarta, Anna baiwar Allah, yoh ita haka rayuwarta ta kare fa, kuma bata da wani mai dauketa ya matsata daga wajen da ake cuzguna mata, ita bata san bama marainiya ce ko yar dangi, bata san daga ina ta fito ba, ba abinda ta sani,

A hankali ta mayar da kanta saman cinyar Ayya , daidai lokacin da Wardugu ya shigo dakin da salama,
Daga inda take kwoncen nan take kare masa kallo, tabas wardugu ko bashi da ko sisi sai mace ta yi haukansa, ko bashi da hali zai mitsa zuciyar mata, dan farin batube mai zamani,

Idannuwanta ta lumshe a hankali wani hawayen ya kuma zubowa daga gurbin su ta mike a hankali bayan ta share hawayen ta kai dubanta wajensa , kanshin turarensa ya cika mata hanci, A hankali ta ce" ina yini,

Gaisuwar da tunda suka daukota daga timiya shi dai bai taba jin ra yi masa ita ba, tsumamun idannuwansa ya zuba mata ba tare da ya amsata ba, yana kallonta har ta fice a dakin dan basu

waje su tatauna ta nufi wajen Mu.azam dan gannin ko ya ci abinci?

Ayya ce ta lakato shi tana yi masa murmushi tana saisaita kanta ta ce" dan gidan Ayya, sannu da dawowa,

Wardugu ya juyo da sauri yana dubanta, ya yi murmushi ya ce" Ayyana, ina yini?

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

3️⃣4️⃣

Amsawa ta yi tana dubansa da madaukakiyar kulawa kafin take mikewa ta kama hannunsa, Shima biye yake da ita suka fito daga dakin Agaishat suka nufi dakinta,

Walyn ce zaune a saloon mai suna Tawaye saloon, fitacen saloon ne na manya wanda sai ka isa kake saka kafarka,

Akifunta ake gyara mata bayan an yanyanke su an wanke su sosai aka dauko na kanti zako zako din nan aka shiga dora mata,

Kawarta dake gefenta tana karanta magazine, itama ana gyara atach din da za.a yanyara mata
```

kitso ........

Wata mata da ta tsare Walyn da kallo tunda ta shigo ce ta yatsina fuska, a ranta ta yi murmushi tana ayyana ba laifi , matar tasa bata da laifi,

Kadan ta dan muzguta ta dubi cousint dinta dan daudu wanda suka zo gyaran gashin tare da shi ta ce" ina son aikin General a rayuwana, ina son yanda yake cin uwar kananun yan iska!

Kallota ya , ya wani yi far da idannuwansa, ya yatsina fuska tamkar mace ya ce" ke kawa, ya iya tata rashin mutunci ne fa, mutumen nan kin san da matar tsohonsa ce ya rufe? Uhum ke ni ko a lahira bama fatan mu hade da General Wardugu domin bashi da mutunci, ya iya aiki da doka, ke matarsa fa ta yarda ta kai dare a waje sai ta kwana a cel!

Daman inda take so a tabo mata kennan dan haka ta maida hankalinta sosai ta kali dan daudun nan ta ce" kawaliya matar naci ta taba daraja ne?

Walyn dake kalonsu tana kada kafarta, ta kai dubanta wajen mai saloon din, ta maida wajen kawarta da ta yi kasake itama tana jiran gannin me zata yi? sai sauran matan dake wajen da yan tsirakun ya  daudun dake wajen suna suba nasu sha.anin.....

Walyn ta saki murmushi mai ciwo, ta daga idannuwanta cike da isa da takama ta ce" Wardugu kennan, mijin mace daya, jarimina mai ban tsoro, Warduguna zazafa ne, kawata kin san Wardugu baya bin kadangarun bariki? Ke na yi imanin da Wardugu na bin mata zai je ya zabo zuga zuga ne, wa.inda idan ya zaga zai dire chek ba wai ya dane karamar yar bariki ya kasa iyanta harda kason shekara sanadiyar rabuwa da mace ba!

Dan daudun nan ne ya sheke da dariya yana duban matar da suka zo tare, wace ta ji abin tamkar saukar guduma domin mijinta ne ya jewa wata yar bariki ya ki biya sannan ya yi mata duka hakan ya sa harda su kaso, wani tukukin bakin ciki ne ya taso mata, bata tsamaci jin haka ba , abin ya dake ta,
Kallonta ta yi da yannayin bacin rai ta ce" ke Walyn kike ko wa? Kin san ko wacece ni?

Walyn ta fizge hannunta daga hannun mai saka mata farcen ta ce" ke ce katuwar yar barki marar aji! Sai me kuma?

Mikewa ta yi itama ta ce" ke din ba yar barikin bace? Ke naki a boye kike yi ko ji kike ba.a sani ba? Meye bambancinki da yar bariki? Ke kawai bakya yi dan kudi ne aman menene bakya yin? Ko dan kina rufe takunki ne baki san wa.inda kuke labewar da falasawa ba? Ki jika ki ajiye Wardugu General ya fi karfin zama da mace daya wace na sani ne bakima goge a kai shi wata duniyar ba! Zaki ga aikin gogagiyar yar bariki domin Wardugu katuwar kadara ne wanda malakarsa sai tsayaye ba isa ce zata kai ki ba mu je zuwa!......

Walyn ta yi murmushin rainin hankali kafin take bufe jakarta,

Yan jika goma goma ta fitar dami guda ta bale yar takardar dake zagaye da su wace itama sai kyali take, ta dauki bakin gilas dinta ta jefa katuwar wayarta a jaka ta juyo sosai wajen matar da sauran mutanen saloon din ta daga kudin nan ta sake su a iska wanda hakan ya saka du suka shiga wawusoso harda mai saloon din da yarenta kiwa na nema har wasu suka shiga dambacewa , aman banda wace ake kira da kankana!

Walyn ta bi kawayen da kankana ta zo da su da ido ta ga suma sai wawa suke harda yan daudun,

Yatsina fuskarta ta yi ta ce" abokin mai kanwa ba ya rasa burbudi, Wardugu ya daure min a niger tunda ya sakar min yayan banki, na kwana lafia koda Wardugu ya shiga tsakiyar yan bariki ba zata motsa ba domin kyankyaminku yake!
Ta kara taku har gabanta ta zaro idannuwanta ta ce" ki sauke girman kai ki duka ki kwashi kudi.....su kike kwadayi!

Iska ta ja ta kaiwa Walyn duka warda itama ta damketa suka shiga dukan junnansu,
Sai da suka lilisa junnan su sannan mutanen wajen suka shiga tsakanin su kowace na haki,

Walyn ce ta warce jakarta ta yi gaba inda kawar tata ta biyota da gudu tana kiran ta tsayata, aman ina cikinta take ji yana wani irin hautsina mata, bata san me ke damunta haka ba yanzu, ya kasance tana yawan jin abubuwa a tatare da ita,

Wardugu ya jima wajen Ayya, inda suka tatauna sosai sannan ta saka shi a gaba kan sai ya ci abinci,

Agaishat na fitowa ta nemi Mu.azam, sai dai bata ganshi ba hakan ya saka ta fice ta nufi wajen runfar Ayya mai wani ni.imtacen sanyi tana neman Mu.azam,

Nan kuwa ta same shi, ya kurawa waje daya ido, ya zurfafa sosai a tunani wanda yannayin fuskarsa ta nuna ba tunanin dadi yake yi ba,

A hankali ta karasa ta kuma maimaita salamar da ta yi ta yi masa tun daga dan nesa da shi,

A dan tsorace ya kalota kafin yake daidaita yannayin fuskar sa ya amsata yana mai kokarin gyara mata kujerar dake kusa da shi,

A hankali ta ja ta zauna tana dubansa, yannayinta ya nuna itama ta shiga damuwar da yake ciki,
A hankali ta ce" me ke damunka ya Mu.azam?

Daman ita yake kallo, dan haka ya bi bakinta da kallo yanda ta fadi maganar a hankali sannan a cicire domin dai tana faman koyon yarensa ne,

A nitse ta janye idannuwanta daga cikin nasa, domin kallo nr yake mata tamkar zai fada idannuwan nata take ji,

A hankali ya ce" Agaishat,

Ta dago tana dubansa, inda a take ta ji gabanta ya fadi da yannayinsa,

Mu.azam ya ce" kin san soyaya?

Agaishat ta zaro idannuwanta tana dubansa, tama rasa me zata ce da shi,

Mu.azam ya ce" kin taba yin saurayi wanda kika ji kina so?

Agaishat ta saki murmushi mai kama da na sakalci, domin ita abin har ga Allah dariya ma ya bata, A hankali ta maimaita kalmomin" *So, Soyaya, Saurayi?*

Mu.azam ya dan kankance idannuwansa ya ce" yeah,

Agaishat ta dube shi, duba na ido da ido kafin take fadin" *Ban san shi ba*!

Da mamaki yake kallon ta, bata san shi ba tace fa? Aman daga ina Agaishat ta fito haka? Ko dai masu son nata ne basu yi mata ba?
Yin wannan tunanin ya saka gabansa ya fadi, a ransa ya ayanna ya salam, kar dai a je nima ban yi mata ba,?

Muryarsa sanyaye ya ce" du a maneman soyayar ki ba wanda kika taba jin kina so?

Agaishat dake dubansa itama, bata dago ina ya nufa ba, domin dai ita ba.a taba kamanta za.a ce ana sonta ba, dan haka ta bashi hankalin ta sosai ta ce" ba wanda ya taba fada min ya ake so din ne,

Dariya ya shiga yi kasa kasa yanai mata wani duba kafin yake fadin" ba fa zolayana nace ki yi ba Madame,

Bata san kalmar madame ba, aman ta gane yana nufin wasa take yi masa, dan haka ta ce" ban taba yin saurayi ba, ko an zo zaben yan mata a gidan mu ba.a taba zabena ba, Ba yace dan na cika baki da muni, ni ba alkhairi bace dan baki ba alkhairi bane, hakan ya sa ba mai zabena bare a biya sadakina, har kanwata an zaba sai dai kafin auren ta rasu ita,

Dubanta yake har ta gama yi masa bayani da kwatance da komai dan ya gane da kyau, ajiyar zuciya ya sauke a ransa ya ayanna na godewa Allah ai da basu zabe kin ba da sun saka ni a

ukunna,
A fili kuwa ya ce" wa ya fada maki baki ba alkhairi bane?

Agaishat ta ce" da alkhairin ne, da mahaifina bai kyamace ni ba  da alkhairin ne da nima ana yi min dinkuna irin na yan uwana, da alkhairin ne da jama.ar gari sun mutunta ni a matsayina da dan adam mai daraja a cikin halitun Allah, da alkhairin ne da na yi saurayi koda mahaukaci ne a *Gida*,

Katseta ya yi da fadin" aman sai na ga kina da ilimin adini sosai, ya aka yi kika kasa imani da haka?

*Agaishat , malamata, wa ya halici fari da baki,?*

Agaishat dake dubansa ta sada kanta a hankali, kafin ta ce" Allah ne,

Shin da ya halici baki ya kawo wata ayya a alkur.ani mai girma, a hadissai ko wani litafin na adinin fake nunin bakar fatar nan da ya halita ya haliceta ne dan wani laifi? Ko mai wani laifi?

A hankali ta kuma fadin" aa, ban karanci haka ba,

Mu.azam dake dubanta ya ce" Bilal, bawan Allah, wacece kalar fatarsa? Ya darajarsa take?

Dago da idannuwanta ta yi ta ce" baba tsofo ya ce shi ne ya fara kiran sallah , ya ce mutun ne mai daraja, makusancin fiyayen halita,

Mu.azam ya gyada mata kai kafin yake ciro wayarsa ya samo hoton ka.aba ya ce" zo ki ga ka.aba a hoto Agaishat, zo ki gani...
A hankali ta matsa tana kallo, kalar bakin ya tafi da imaninta, abin ya yi mata kyau a ido, a hankali ta kai yatsarta ta dan shafa hoton,

A hankali ya ce" ba wani bawan da ya fi daraja, ya fi kusanci fa ubangijinsa sai mai yi masa biyaya, mai tsoron shi, mai kiyaye dokokinsa, a cikin nan kin ji an ce *Farar fata ta fi bak'a?*

Agaishat da take jin wani yamyamyam a jikinta na dadi ta girgiza kanta,

Mu.azam ya ce" makafi ne ko kwakwaluwar su bata ja? Ya aka yi basu yiwa abin kaunata wawa ba?

Da sauri ta kallo shi,

Kansa ya dan sada ya ce" kina da tsararen kyau, fitinanan kyau, baki da tsayi Agaishat...baki da kiba har can, yannayin jikin ki ya tafi da yannayin tsayin ki,
Bakin ki ba mai tabo bane bare shaida, gaba daya ya tafi iri daya ne baki mai haske mai

nutsuwa, agaishat, fuskar ki yar doguwa ce mai dauke da dara daran idannuwan da a kowani yannayi kike su kadai sun ishi mutun, Agaishat Allah ya tsara ki da hanci mai tsayi mai yan kofofi wanda ya yi das da dan madaidaicin bakin ki,
Rashin hayanniyar ki ya hadu ya kara kawata halitar ki, ke da ba dan kar na kauce hanya ba da na fada maki sauran tsaruwar ki,

Dan dakatawa ya yi gannin yanda ta zuba masa ido, sai a lokacin ya tuna ya saki baki sai zuba yake mata,
Dan kimtsa kansa ya yi a hankali ya ce" Agaishat arrrakam (Agaishat ina son ki),

Wata irin faduwa gabanta ya yi, da wani irin firgici ta akle shi, tsoro, mamaki, surprise, murna suka hade suka saka jikinta ya dan fara rawa, So na? Ji ta yi wani nauyinsa ya diri mata,da sauri ta sada kanta kasa, kafin take mikewa da wani irin sauri ta jua inda Mu.azam ya mike yana kiran sunnanta daidai Wardugu ya yi kokarin kawar da kansa dan kar su ganshi bayan ya jima wajen,

Ganninsa ta yi yana ta faman taba labulen ayya wanda ke gyare tsaf a wajen aman kamar wanda yake gyara shi,
Kanta ta shiga sosawa kafin take dan rabar gefensa ta shige ta taka matatakalar da gudu gudu ta nufi dakin ta,

Da ido ya bita, da wani irin kallo, a hankali ya lumshe idannuwansa ya juya ya fice a dakin ya nufi wajen mu.azam da ya koma ya zauna ya dan dafe kansa da hannunsa cike da tsoron kar a je ta ki karbar sa,

Gaban wardugu ya ji na wani irin gudu wanda har ya ji wata yar zufa ta karyo masa,

A dan hanzarce ya karasa wajen amininsa yana mai cike da zulumin yannayinsa, a nitse ya kai hannunsa ya ce" Mu.azam?

Agaishat na shiga dakinta ta karasa da sauri wajen madubi, lufayar jikinta ta warware ta tsurawa kanta ido, du abinda ya fada take son gani sai dai ita bata wani gannin kyanta, , .....
A hankali ta kai zaune ta cuje abinda ta daure gashinta da shi wanda hakan ya baiwa gashin damar zubowa baki dayansa ya yi lumbuk a jikinta, hannayenta ta cusa ta fashe da wani kuka mai zafi, a hankali, muryarta na rawa ta ce" Anna, ina kike? Anna wai yana so na? Ashe nima mutun ce Anna? Anna wai ina da kyau, wai nima mai daraja ce, Anna nima na yi saurayi...........tana  kukan kuma ta shiga dariya a hankali ta furta" Mu.azam, nawa😌😌😌😌😊😊😊😊😊😊😊

I.m sowi fans , jiki da jinni ne 🤦‍♀️

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

3️⃣5️⃣

A hankali Wardugu ya kai hannunsa ya taba Mu.azam, murya a sanyaye ya ce" Mu.azam?

Da sauri ya dago da kansa daga yannayin da ya afka, ya kali Wardugu da kyau kafin yake sakar masa murmushi,

Wardugu ya ce" me me ke damun ka?

Mu.azam dake dubansa ya dan sada kai, ya kuma dagowa yana dubansa ya ce" jinta nake a raina har jikina Wardugu, sai dai ban san ba ko zata aminta ta aure ni a dan kankanin lokaci kafin mai yiwuwa ta yiwu da ni?

Wardugu ya ji gabansa ya fadi, Allah yana ganni idan da abinda ke tayar masa da hankali a yanzu bai fi rashin lafiar Mu.Azam ba, lamarin na girgiza shi in ya tuna, yakan tsinci kansa ba karfi bare laka a jikinsa idan ya tuna, .......
Duk da ya fahimci wa yake nufi aman sai ya kashe ido guda yana kallon Mu.azam ya ce" kai, soyaya ka afka daga zuwa garin mu? Fada mini wacece mai sa.ar samun abokina ?
```

Mu.azam ya lumshe idannuwansa ya ce" Wardugu, na kan ji wani iri idan muna hira da kai a yanzu, domin du ka canza min kan da, a da idan muna hira tamkar yaki muke, ka warto ni na tsokaneka mu yi ta shirirta har sai an shiga tsakanin mu, aman a yanzu du abinda zan maka sai na ga ka wani yi shiru ka kyale ni ko kuwa ka wani lalaba ni, malan matarka ne ni? Ko dan bani da lafia? Ni irin yanda muke da ya fi birge ni, sai ka wani dawo ladabi?

Wardugu dake kallonsa ya ji zuciyarsa ta mugun karye, hakan ya saka wata zufa ta karyo masa, a yanzu da suke zaune a haka ba mamakin shi wardugun shi ne gawar fari, aman kuma rashin lafiar Mu.azam da ta bayana kanta ne ake kiran kisan mumuke, domin dai ta hana kowa walwala tsakanin mutane ukun nan, Mu.azan din, docternsa, sai Wardugu da ya sani shima,

Wardugu ya saka hannunsa ya share gumin da yake , ya miko hannunsa kusan na Mu.azam ya ce" wa kake so? Ko yar gidan waye, ko wa take takama da shi nan duniya sai ta aure ka, kuma dole ta so ka!

Mu.azam ya kwace hannunsa yana dubansa da yannayin tausayi, ya san waye Wardugu farin sani, wannan yannayin da yake ciki yayi imanin da ace zai samu kuka da ya koka tun karfinsa ko zai samu sauki,

Goshinsa ya dafe yana dubansa, ya ce" ka daina damuwa da lafiata Wardugu,

Wardugu ya katse shi da fadin" idan muka gwada aikin nan fa?

Mu.azam ya ce" bayan ka tirsasa ni shan lemun tsami cikin ruwa masu zafi, kana tirsasani cin tafarnuwa, kuma zaka bijiro da maganar aikin da na guduwa ? Wardugu aikin nan fa mai yiwuwa shigar da za.a yi da ni a fitar maku da gawata,

Wardugu ya ce" kuma tana iya yiwuwa a fitar mana da kai ras ka sami lafia,

Mu.azam ya ce" mafi akasari idan Allah ya yi an sami lafiar ma kwakwaluwa na tabuwa, ko a samu shafewar tunani, cikin kaso dari bai fi 2/100 suke mikewa garas ba Wardugu, na fi son idan ta Allahn ce zata kasance da ni nan kusa ya kasance ina kusa da mutanen da nake so suke so na,

Wardugu ya kura masa ido, kallon cikin ido, ya ce" ba zan iya ba, zuciyata mai mugun rauni ce a kanka, ina jin rashin karfi a abinda ya shafe ka, baka yi min adalci ba idan har ka yi min haka, !

Ya mike ya dauki kys dinsa, ya dora hanayensa saman table din yana dubansa ya ce" baka isa ka min haka ba, ba zan taba barinka ka yi min haka ba! Zan nemi karin bayani ......

Juyawa ya yi ya fice inda yake jin kansa na mugun sara masa,

Mu.azam ya girgiza kansa bayan ya bi shi da kallo, a hankali ya furta" ban so ka ji ba, sai dai rigumarka ta saka ka tankalo abinda zai hana maka nutsuwa!, ya hana maka jin dadi!

Tukin garari ya yi wanda ikon Allah kawai ya kai shi gidansa lafia,

Yana zuwa ya sauka daga motar ya rufe ya nufi bangarensa kansa duke yana mai jin yanda yake sara masa,

Har zai bude ya shiga, sai ya fasa ya dubi bangaren Walyn,
A hankali ya juya akalar tafiar tasa ya nufi bangarenta yana wata irin tafia wace da ka gani zaka fahimci da karfi ne ake yinta ba dan ana jin dadinta ba,

Wardugu na shiga ya zarce falonta baba inda kamshin turaren da aka turara ya yi masa salama.

A hankali ya shige yana hangenta kwonce saman doguwar kujerar falon nata tana danna waya ranta da yannayin bace, sannan da maganin zazabi mai tafasa a gefe da alama dai ita ta sha bata jin jikinta,

Da sauri sauri ya karasa gareta yana mai cire rigar tasa ta sama ko zai ji dan sanyi sanyi ya karasa wajen Walyn da ta zabura ta mike tana dubansa da wani irin yannayi mai fasara abu uku, na farko ganninsa a bangarenta, na biyu yannayinsa ya firgitata, na uku mugun haushinsa da take ji domin yanzun ma a cikin grup dinsu na manyan mata ne ake tatauna maganar har wata na ikirarin ita walahi a duniya ba wanda ya yi mata irin wardugu halayensa na kasheta da dadi, idan ta kali hotonsa takan jita a wata duniya, tunani take wannan mutumen ya kasance hazarsa a gabanta kadai ya isheta, duda an kwabeta cewar da matarsa a gidan fa , kamar an zungureta ne an tirata domin a lokacin ne ma ta ce" Wardugu ai mijin mace hudu ne wanda Allah ya halita masa ba wani shege ba, duniya kuwa idan takamarka sauko wani a can ya kwana,

Tana wannan tunanin wardugu ya karaso jikinta, batai tunani ba ta ji ya rungumeta da karfi wanda sai da ta ji kamar numfashinta zai tsaya dan ya kanainayeta ya hana ta motsi,

A hankali ta rungume shin itama, ta shiga sauke ajiyar zuciya tana shakar turaran jikinsa wanda koda ya yi zufa bata hadewa da turaran ta bayar da wari wari, turaran ke cin karfinta bama zaka gane ba sai dai idan mafi kusanci da shi ta ji gishiri gishiri a jikinsa a irin wannan yannayi 🤣,

Gajiya ta yi da tsayuwar domin daman ba wani karfin jikinta take ji ba,

A hankali ya bita saman kujerar domin shi a wannan lokacin bashi da bukatar komai sai na ya jima a jikinta , ta rungume shi, yana so ne kawai ya ji shi a jikinta ba komai ba,

Haushi Walyn ta ji, aa me wardugu ya dauketa ne? Jiya ya gama wulakantata, ya fanshi jikinta,

ya tashi ya yi tafiyarsa, ta je saloon ta kwashi rashin mutunci dan shi, ta zo gida mata na wawarsa shi oga! Yanzu ya kuma dawo mata da bukatar sa? (Domin a tunanin ta , bukatuwa ce ta dawo da shi a irin wannan lokacin ),

A hankali ta zame jikinta tana dubansa yanda ya yake ringeshe jikin kujerar idannuwansa du a lumshe,

Baki ta dan yatsina, a fili ta ce" ka san yau a saloon wata karuwa ke ikirarin sai ka aureta?

Daga yanda yake kwonce yake dubanta, a hankali ya ce" ki zo gare ni Walyn.....
Ya mika mata hannunsa,

Kafadarta ta make irin na yangar nan na mata ta ci gaba da fadin" ka saurare ni mana, ina maka hira ka wani basar,

A hankali ya kai hannunsa wajen goshinsa kafin yake mata alama da ta ci gaba, domin ya lura kwata kwata matar tasa bata lura da yannayinsa ba, bata da niyar fara sauraronsa, zata tiso abinda ke damun nata wato *kishi da isa*,

Zamanta ta gyara tana mai dubanda da kyau ta ce" ni kuwa na bata amsar cewa , Wardugu mijin mace daya ne, ba zai kula wace ta san mutuncin kanta bama bare ita karamar yar bariki, Wardugu nawa ne ni kadai!

A hankali, ba tare da wani damuwa ba ya ce" *wa ya yi miki wannan albishir?*,

Da sauri ta dubo shi, da yannayin mamaki ta ce" me kake nufi?

Dagowa ya yi yana dubanta ya ce" *Auten zobe muka yi da ke?*,

Walyn ta kara zabura da mamaki ta ce" kana nufin sai ka kula wata macen?

Wardugu ya buda idannuwansa da kyau, ya ce" *To waye ni?* , an fada maki ni ba mutun bane?
,

Yanzu sai ka ci amanata Wardugu? Sai ka dubi wata macen da sunan so?

Kallon kar ki raina min wayo ya yo mata sannan ya ce" tunda hirar kike so mu yi bari ki ji, da farko dai ni mutun ne dan Adam wanda nake tara ba goma ba wanda nake cike da laifuka , nake dauke da zuciya mugun nama, wanda na kwonta da sannin Allah ya halasta min auren hudu na jera, nake da sannin ina da wajen saka su, ina da abinda zan ciyar da su, na tufatar da su, sannan ....ya yi murmushi ya ci gaba da fadin" na sauke hakinsu saman lit (bed) ba tare da gajiyawa ba! Ke kin san wa kike aure shi ya sa kike kishi! To a haka da nake, akoy wa.inda ban yi masu ba, sam bana gabansu, bana cikin tsarin da zan samu koda gaisuwarsu ne! Walyn, ana

aure dan soyaya, da tausayi, dan sha.awa, dan arziki, ba zan maki karya ba, ba zan yi maki rantsuwar ni na isa na kauce kaina daga kan *mace yar dagwas dagwas mai dorinar dukan maza ba* , ciki kuwa koda yar barikin ce da kike fadi mai yiwuwa na zama silar shiryuwarta!

Gaba daya har Walyn ta fara fita a hayacinta , ta hayayako ta ce" me na gaza da shi Wardugu da kake kiran min sunnan wata a gabana?, *Kyau, fari, tsafta, girki, iya tarairayarka,* wane na gaza a cikin nan?

Haushi ya kara kama shi, itace ke ikirarin iya tarairayarsa bayan yanzu ya shigo mata a wani yannayi maimakun ta dubi halin da yake ciki ta zauna a kusa da shi aa, sai ma ta tsankalo kabarun banza da wofi, kai da Walyn a wajen aikinsa take kai koda ficewa take ta hanyar da an kwashi yan kalo da ita da matan dake kai masa ziyara, wai kuma ta yi ikirarin ita ta san kanta ita mai kyau me memememe, *Isarta* ta hanata ta duka masa yanda ya dace, takamarta da halitarta sun hanata gane ainahin biyayar aure, sai idan baki ya bude ta shiga zubo masa abubuwa mararsa tsari, dan haka da yannayin haushin nan ya mike yana daukan rigarsa ya ce" *Kin san dadin miya ke sakawa a yi kari!*

Wai wai wai wai , shin fans zaku kuwa iya zama da mai hali irin na wardugu🤦‍♀️🤦‍♀️🤦‍♀️,

Su waye wardugu ke ikirarin ko arzikin gaisuwa baya samu daga wajen su? Me ke damun wardugu?

Me ke damun kwakwaluwar Wakyn? Ta hada kyau, fari, tsafta, kanshi, girki, bata isa ta daki kirjin mijinta na ita kadai bane?🤔

Mu.azam, zai kai labari kuwa?

Agaishat Ayya, Anna, Ba, Marahut, ya labarin su ne?🤔🤔🤔

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

36

Rigarsa ya rataya a kafadarsa, ya juya da niyar barin mata bangarenta domin bai ga dalilin fa zai saka a caza masa kwakwaluwa a waje, ya zo wajenta dan samun nutsuwar zucuya itama ta caza masa, yana bauwa Walyn damarta ta mace, na ta yi korafi a kan abinda bai mata ba, ya sha duba korafinta ya nuna mata ya tuba a aikantance ta hanyar daina abinda ta kawo masa korafin a kai, sai dai abubuwa na damunsa na irin yanda ita ba abinda ya sha kanta da damuwa da damuwarsa, bata wani damu da yannayin da zata ganshi ba indai da abin fada zata rufe ido ta fada da gatsali,
Murmushi ya yi yana girgiza kai bayan ya kare mata kallo du ta fice a hayacinta daga wannan yar maganar? To idan Allah ya kadarto min kara aure yaya zamu kwashe da Walyn?

Rai bace tana kokarin fashewa ta kuka ta ce" Wardugu, idan ka yarda, idan ka saki, ka yi saken kula wata mace sai dai a kwashi gawarwakin mu baki daya! Wardugu kamar yanda Batuben namiji zai iya suka da wuka dan an kali matarsa toh zan iya suka da wuka dan an rabe ka!

Tsayawa ya yi yana dubanta, iya gaskiyarta ta fada domin a tsaye take tana dubansa ido cikin ido, jikinsa ya ji ya dan yi sanyi, karasawa ya yi kusa da ita , ya dan sasauta murya aman a cunkushe ya ce" Walyn, bakya aiki da adini ne ke? Kin san da sunnar ma.aiki ce? Me ya sa zaki daukarwa kanki zafi haka? A haka Walyn ban ma nuna zan yin ba idan zan yi fa?

Idannuwanta ta dago dan sakawa cikin nasa domin ya darata tsayi, ta ce" na tsinci kaina a zazafar kaunarka, haka na wayi gari na ganni zundum , na shanye wulakanci kala kala dominka, kai da kanka ka sha wulakanta ni mai girma, karaya uku ka min a gabai na, du na shanye! Kai a tunaninka ba zan shanye azabar kawar da du wata tsagerar da ta tunkaroka ba? Wardugu, mahaukaciya ce ni a kanka! Sakara ce da a yaren ka! , kamar yanda ka sumar da saurayin da ya yaba maka ni, ni kuwa ka yi min marin da na yi ta ihu sai da kyar jina ya dawo dan na yi kwaliyar da aka yaba ni, haka zan iya rike makigwaron du wata yar iskar da ta yabe ka!
```

Kansa kawai yake dan girgizawa yana dubanta, Walyn, walyn Wardugu...ya saki murmushi ya juya,

Haushi ya kara rike mata zuciya ta daga murya ta ce" ciki kuwa harda wannan tsohuwar kilakin da ta ki aure take binka gida ma.aikata, anguwa! *Alhinayett*, ciki harda ita,

Dawowa ya yi ya tsura mata ido, kafin yake fadin" ki daina zagin Alhinayett domin mai son ki ce, tana yaki kan ki, tana yi min fada kan ki,

Karuwancin kennan! Karuwancin kennan Wardugu! Ta shiga jikinka har ka ji in ba ka kasance da ita ba , ba zaka ji nutsuwa ba!

Wardugu ya zauna saman kujerar dakin ya ce" Walyn, Alhinayett ba yar bariki bace, mutun ce mai daraja, mutunci ne tsakanina da ita, ke kin san da soyaya ne da tuni na auri abina na kilace, jimawarta ba aure kuwa Allah ne bai kawo lokaci ba, aman an kusa saka aurenta, ki daina magangannu irin haka Walyn , ke macece, ko a kan ki ba haihuwa zaki yi watarana, ba.a so mutun ya cika izgili,

Kai ta kawar ta ce" wardugu, gaskiya ne baka so? Alhinayett ai kowa ya san kilakin ka ce!

Wardugu ya mike a karo na uku kennan, ya karasa kusan Walyn yana mai binta da kallo, hannunta ya damko ya bude yana dubawa, ya riko fuskarta ya daga idannuwanta yana dubawa, ya gwale bakinta ya saka yatsunsa ya ciro harsanta yana dubawa, ya saki ya kama rigar dake jikinta ya dage sosai har biyu suka bayanna, nan ya tsura masu ido yanai masu kallon kurullah, Cikata ya yi , ya dan taka ya tako kafin yake nunota da yatsarsa manuniya, muryarsa ya saki baki daya ya ce" Ba karuwa bace! Aminiyata ce, du wanda ya zagar min ita zan bata ransa! Kika kuma kiranta da karuwa na rantse da girman mahalicina sai na aureta koda kuwa ta tsane ni , koda mutuwa zata yi dan kina na kawota na kwana da ita saman gadon ki! Ke da ba dan ina hangen kamar mai shigar ciki ba yau da na nuna maki tsagwaron rashin mutunci! Ya ina taro ki kina raina min hankali? Walyn ni in ban kara aure ba ni ba dan babana bane!, ni ba jinin tubawa bane! Walyn dole ki zauna da kishiya in baki kona mu ba ke ba yar babanki ba ce!

Fuuuuuu ya juya ya fice yana jin kamar ya koma ya yi kwalo da ita, sai dai yana tsoron kar a je ciki ne da ita, ta ja ya yi mata lahani bayan adu.arsa kennan shima allah ya azurta shi da haihuwa, yar bakin ciki kawai take jan sa masifa salon ya biye mata idan cikin ne su barar su shiga uku!

Haka ya koma bangarensa ya zube a falon sa ya yi ruf da ciki ya dora hannayen sa saman kansa yana yamutsawa yana tunanukan rayuwa,, walyn ba wayo , haka ya ayyana a ransa kafin ya kuma fadin....ta saka sai na kara zama da wata macen? Walyn shirme shirme🤦‍♀️,

*Timiya*

Amai take kwararawa har kamar ta shide, inda *Ba* ke tsaye ya dan duka dan tsayinsa, da rawaninsa yana dubanta,
Gefe guda kuwa su Anna ne da yayanta yauma Gaishat ta kawo mata ziyara da dan cikinta da ya tasa kafan wanda sarki ke mugun zumudi kansa tkar shi ne dansa ma fari,
Suna kasan bishiyar gidan suna zaman su suna yar hirar su , domin yanzu da safiya ta yi Mariama ke fitowa ta gyara wajen ta shinfida tabarmar kabar da Anna ta siyo daga garin agadez ta dauki du abinda zasu bukata su koma can su yini abinsu , nan suke sallah su ci abinci, ta dauki na baba tsofo ta kai masa domin Gaishat na tsaye kan abinda zasu ci, sarki baya wasa da ta nuna tana da bukata ake kwasa a kai mata itama ta kwasa ta kaiwa mahaifiyarta, inda ta saka sarki ya yiwa *Ba* gargadin kar ya kuma kwashe masu abincin su,

Bakinsa yake motsawa ya juya ya karewa Anna kallo da yarenta su uku sun zagayeta, ya juyo wajen amarya dake maida lumfashin kadangare bayan ta gama sheka amanta,
Tabar sansaninsa ce yake gumtsa a bakinsa,
Bakin ya bude ya totofar da yawu, domin du mai shan tabar sansani ya kasance yana tofe tofen yawu, ya juyo wajen amarya ya ce" sannu *Uwar mai uba biyu*,

Kallon kasan ido ta yi masa kafin ta kada kai,

Juya kansa ya yi wajen Anna ya ce" duniya, anai min kallon ina yiwa yarana aure suna tafia birni, ke gashi kin dauki yar santal ki badata yawon kilaki!

Da sauri Anna ta kallo shi, gabanta ya fadi,

Kura mata ido ya yi ya ce" karya na yi? Ke yanzu zaki daki kirjin yarinya na hannun kirki? To ni dai in tana aiko wani abin ake boyewa ana ci Allah ya isa! Dan ko dan ciyar da ita da na yi ya isa a yaga mini wani abin ba a rufe ni da baibai hannu ba!

Gaba dayansu dubansa suke,

Ya tako da fararan kafafuwansa da sukai fari fat na kasar garin ya dubi Gaishat ya ce" ke kuwa fa? Haka zaki saka mini ko? Kin samu na aura maki sarki , ya nada ki sarauniya aman ni kika saka kafa ki ka shure ni sai wannan tsohuwar matar kike baiwa abinki ko? Ai dukan ku Allah na kallon ku! Ko hakin ciyar da ku da na yi zai bi ku,

Ya kara tofar da yawu yana duban Mariama dake bin sa da wani mugun kalli itama da

sansanninta a bakinta kamar na sauran yan uwanta da Anna, ya ce" ke kuwa ke ce gagarara ko? Mai tarda ni wajen majalisa ki tirke ni gaban abokaina, ke mai karfi wace ta fi kowa iya rashin kunya, a gaban yan uba kika yi ikirarin zaki ga ubanda zai maki aure ko? Ba laifi, ba laifi Mariama, in sun zo sai mu basu gidan su saya su tafi mu kuwa mu koma zaman titi ,

Mariama ta yatsina bakinta ta kawar da kanta,

Babar rigarsa ya kabe ya ce" kudinku yanzu na fara ci, ni da ku ba shari.a domin ni na haife ku! Dole na yi maku aure na mori kudin ku! ,

Ke kuwa, ya nuna Anna da take jan dan karamin carbinta tana shamaninta ya ce" kin ji kunya, anai maki kallon saliha sai gashi kun hada baki da tsohon can kun tura yarinya nema; ana zaton wuta a makera su Annar yara sun kunata a masaka.

Yana gama fada ya fice a gidan yana ta tofe tofensa,

Mariama ta dantsa yatsarta a bakinta tana yiwa yayarsu kallo mai kama da harara, domin ita ta yi masu kashedin kar ta kuma gannin wani ya biye masa, dan ta lura hakan na masa dadi

Gaishat ta yi murmushi tana dubansu ta ce" baku lura ya fara yin sanyi ba?

Mariama dake hararar Amaryar Ba ta ce" sanyi? A wannan tsohin najad.....

Bige bakinta da Anna ta yi ya saka ta kasa karasawa tana turo baki,

Da yannayin bacin rai ta ce" in kina irin magangannun nan hankalina tashi yake, mahaifin ki ne fa, ko me ta zama adu.a ce tsakanin ki da shi, ya zaki ringa halaya irin na wace bata da tarbiya? Bana so Mariama ,

Aman Anna, kina ganni abinda yake yi fa, ke tsoronsa kike , to ni bana tsoron sa,

Kuma bakya tsoron Allah? Gaishat ta fada tana dubanta, hakin dake tsakanin ki da shi na matsayinsa na uba Allah ba zai bar maki ba, ki bi shi, ki yi masa biyaya, ki bar shi idan shi gobensa bata dame shi ba kai nasa,

Shiru ta yi tana duban fatimata dake dan zane a kasa ta ce" wacen matar ciki ne da ita fa? Kuma kum san ba cikin Ba bane,

Anna ta kwalalo ido tana dubansu, a dan harzuke ta ce" na ga mai isata yau da yaren nan, kun yi da shi ne? Bama wannan ba sa.anku ne? Du wace ta kuma gigin muguwar magana a kan mahaifin ku a gabana zamu bata da ita! Ba ruwana ban koya maku ba, baku ga ina yi ba, kuma idan na ji tsoronsa ai ba laifi ba, shugana ne, wanda aljannata ke karkashin kafafuwansa, a haka ma ya muka kare da shi bare na yi masa gatsali? Ku daina bana so!

Ta karasa tana dan dafe kanta domin har ya sara mata maganar nan da ta yi,

Da dadaya suke bata hakuri suna masu lura da yannayinta.............

Daga inda yake ringeshe yake biya bagara a fili hannunsa a kan zuciyarsa,
Sai da ya kai karshe ya samu ya dan daga ya jingina yana duban hanya dan ya san yanzu Mariama ta zo,

Yana jin dadin lamarin mariama sai dai ita ba.a hira da ita, kimkim take masa har yanzu haushinsa take ji, bata san irin yanda shima hankalinsa ke kan Agaishat ba, adu.arsa a gareta ne, da fatan saduwar fuskokinsu kafin ya koma ga mahalicinsa,

Jama.a Wardugu na neman karin aure🤣, du mai son karya kafa ta shigo layi🤦‍♀️🤦‍♀️🤦‍♀️.................. dan Allah aunty Alhinayett kar ki tura masa wannan page din wollah lalla batai kwari ba kar ya karya min kafar nima😟😟😟

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---
```

37

Yana nan zaunen kuwa sai gata ta shigo da salamarta ciki ciki,

Ajiye masa robar abincin ta yi bayan ta dan jefa masa wani kallo ,

Wajen ruwa ta je ta dibo masa ta zo ta tsuguna ya wanke hannunsa ta kuma cikowa ta ajiye ,

Dakin ta tatare kamar kulun shi kuwa yana cin abincin yana duban yannayinta, Mariama akoy shiru shiru sai dai yannayinta na yau kamar ranta a bace ne,

A hankali ya ce" me ke damun Mariama?

Tana gurza goron hannunta ta dan dago ta dube shi, ta ci gaba da gurzar abinta,

Can ta ce" idan ta zo hankalinta a tashe, ranta a bace, idan ta fada maka ka taba yi mata maganin damuwarta ne sofo?

Baba tsofo da ya gane Agaishat take nufi sai ya girgiza kansa a hankali , kafin ya ce" ban taba magance mata damuwarta ba Mariama, sai dai nakan saurare ta, na ji damuwarta, na yi mata nasiha a musulunce da girma, nakan ji ciwon damuwarta a raina na nuna mata ba dadi, aman kuma sai na nuna mata girman hakuri,

Shiru ta yi tana jinsa, can ta ce" wai dan na kire shi da mumunan sunna Anna ta dake min baki bayan bata taba koda shakunana ba, kana da labarin irin manya manyan munana halayansa, aman sai ta wani tare mashi?

Baba tsoho dai kallonta yake , har ta dasa aya tana hucin bacin rai, a nitse ya ce" su iyaye, sune masu madaukakiyar daraja in kika cire Allah da mazon sa a wajen dan adam, su iyaye Allah ya ce a bi su a yi masu biyaya banda hanyar sabonsa,

Shi abinda yake ba sobon Allahn bane yake?, ta fada tana duban Baba tsofo,

Baba ya gyada kansa yana dubanta ya ce" ya taba daukan y'a ya bayar ba.a daura aure ba?

Mariama ta girgiza kai,

Ya ci gaba da fadin" yana yin aurwn yayansa dan dukiya, adini bai jaramta hakan ba sai dai ta yannayin da yake yi ne,
Yana yi ne tamkar yana siyar da yayan,
Wa ke tafe da duniya da abinda ke cikinta Mariama?
Ya kuma watso mata tambaya,

Mariama ta ce" Allah,

Shin baki da labarin ya fi gannin abinda kike aikatawa? Ya fi ki jin abinda ke wakana a tare da ke?

Na sani , ta fada tana kawar da kanta,

Baba tsofo ya ce" shi zai kare ku!

Yana fadin hakan ya yi shiru tamkar ba shi ba,
Da mamaki take dubansa,  bata san lokacin da ta dawo facing dinsa ba ta riko hannunsa tana dubansa ta ce" shikenan? Hukuncinsa kennan?

Baba ya yi mata murmushi ya ce " ke kika halice shi da zaki hukunta shi?

A hankali ta sada kanta, muryarta ne ya yi rauni ta ce" ya cika cin zalinmu, bai san darajar matarsa ba wace take mahaifiya a wajen mu, mu yayansa yakan dauke mu ne ya yi kudin mu, yanzu ya tare da matar da wani ke ziyara a kan idannuwansa, shin yaya ake so dole dole sai na daraja wannan mutun?

Baba tsofo yana dubanta ya sada kansa shima, ya dago ya ce" muna tursasa ki yi masa biyaya ne dan goben ki, kar ki ga duban laifukan da kike hange nasa, idan kika taka hakinsa a kanki na matsayinsa uba a gare ki, Allah ba zai bar ki ba, ki yi masa biyaya, sai ki ga Allah ya jibanci lamuran ki Mariama,

A hankali ta cika hannun Baba tsofo ta juya ta hado goronsa ta kule sauran ta kula a harshen zannin ta,

Miko masa ta yi wanda ta gurzan ta duka gabansa tana dubansa ta ce"ya aka yi mutun mai mutunci irinka ya rayu shi kadai? Ni tunda aka haife ni kai kadai nake gani sai almajiranka wa.inda da sun fara tasawa suke tafiarsu birni neman kudi, ya aka yi baka da mata da yara?

Dubanta yake da mamakin ashe dai ta iya magana, sai dai tambaya ne da Mariama tamkar me, komai so take ta gane ya aka yi ? Ta ina aka bi aka yi? Wa ya yi? Su waye shaida? 😅,

Iyayena yaki ya tafi da su,

Na tashi ni daya sai Allahna,
Na yi aure sau biyu a rayuwana, sai dai rashin haihuwa ya saka matan na guduna,

Me ke birge ka a rayuwar wannan daji kai daya kwal da ranka?

Tsareta ya yi da ido kafin ya ce" nan ne muhalin da Allah ya ara min,

Kalonsa take da wani yannayi na tsoro, a hankali ta mike tana dan duban yannayin dakin baba tsofo,

Fitowa ta yi ta hangi anguwar ba wani mutun mai gitawa bukar baba tsofo a tsakiyar rana take sannan nesa da jama.a,

A hankali ta waiwaya bayanta ta tsurawa kofar bukar ido, a ranta ta ayanna " *Wannan mutun ne ko aljan?*
(🥺🚶‍♀️😳😳😳😳🚶‍♀️🚶‍♀️🚶‍♀️🚶‍♀️🚶‍♀️)

Rakiyar Aghali aeroport tamkar za.a raka shi tafiar da ba zai dawo ba,
Idan ma ya yi salama da iyayensa kuma yin salama suke ,

Har aka fara harama kiraye kirayen suna wanda hakan ya saka shi komawa wajen mahaifiyarsa ya dan duka kansa ya ce" Allah ya ja zamanin sarauniyar garin Agadez, sai Allah ya dawo da ni.

Dago da habarsa ta yi tana dubansa ta ce" Allah ya kai ka lafia yarimana, ka gaisar min da aminiyata domin ban lamunci ka sauka hotel ba bayan gata a gari,

Murmushi ya yi mata yana daga mata kansa , kafin ya juya wajen matarsa ya sakarwa yarinyarsa kiss a goshi da kunci, itama matar ya yi mata kiss a goshinta a hankali ya ce" *Tarhanine* (masoyiya)

Dago da kanta ta yi ta dube shi, da dara daran idannuwanta ta yi masa salama kafin take juyawa ta nufi dankareroyar rangrover din su

Sauka lafia Yarima Aghali .

Yai tunda ta farka a barci ta ahige bayi ta yo wankanta ta fito ta kimtsa jikinta domin ta farka da al.adarta wace ta zo mata tsakiyar dare,

Bayan ta gama ta kuma rufa ta turara turaren wutar da ya zame mata jiki karfi da yaji Ayya ta koyar da ita saka turaran wuta a jikinta da kowani lokaci, barema idan ta fito a wanka sai ta turaru kafin ta bushe,

Sai da ta gama turaruwa ta dawo ta ciro doguwar rigar atampa , jar atampa ce mai adon baki baki a jikinta, An yi mata dinkin mai turmi , saman ya dan rike daidai kirjinta ya yi mata das sai ya bude kasan , ,
A hankali ta zauna saman yar kujerar gaban madubin ta caje gashinta wanda Ayya tace yau za.a kitsa shi, domin ana kitsawa yana warwarewa ne Ayya kuwa tace sai an yi kitso mace ce dole ta yi kitso,

A ranta ta ayanna , ina yake? Ya ya kwana? Har yanzu yana kan bakansa? (Domin rabonta da Mu.azam tun guduwar da ta yi jiya,) yanzu har karfe goma ya gita na safe, tana jin lokacin da Ayya ta shigo take fadin zasu je su dauko Aghali dan aminiyarta , sannan ta ji lokacin da mai aiki ta shigo tana fadin Wardugu ya zo Ayya bata nan, aman ina ita barci ya ci kargfinta domin idan tana al.ada takan yi wani barci mai nauyi ne,

A hankali ta saki murmushi ta kuma furta "Mu.azam nawa ,

Ji ta yi an turo kofarta dan haka ta mike tana duban kofar,
Shigowa ya yi da salama a bakinsa, da sauri ta kai dubanta saman bed dinta, Allah ya so ta abin shinfidar ya rufe pant dinta da ta ciro ta zabi wanda zai riketa da kyau ta saka, bata rigaya ta mayar da sauran ba,

A hankali ta mayar da dubanta wajensa, kafin murya a sanyaye ta ce" i....i.ina kwana ,

Yauma bai amsata ba, sai kallo da yake binta da shi na mamakin yaushe ta iya saka kaya haka? Yana gannin yan aikin gidansa har kulun su shigarsu tamkar an tsamo su daga rafi, domin Walyn nata daukan yan aiki yan birni sai yan kauye, baya taba gannin sun waye su kulun tamkar mahaukata, shi ya sa koda wasa ya hana su taba wani abin a bangarensa, hakan ya sa ta samo masa namiji mai aikace aikacen bangarensa wanda ta yi ta rantsuwar ba dan daudu bane, shi kuwa dan daudu ne idan ya shigo gidan ne yake namiji!

A hankali ta karasa ta dauki dan kwalin atampar ta daure gashin kanta da kyar , wanda yake lumbuk gaban goshinta, ta koma gaban madubin ta zauna abinta ta shiga daure gashin kanta,

Wani irin mamaki ne zai kashe wardugu dake tsaye yana biye da ita da kallo, kai! Ya fada a ransa, ya shigo ne dan ya tambayeta kys din dakin Ayya dan ya san ita zata barwa, sai dai mamakinsa, ya hadu da macen da bata nuna tsoronsa, kakahin ta birge shi, shishigi a gare shi ba, ita bata nuna tana tsoronsa ba , ita bata nuna bata tsoronsa ba, ita dai ta gaishe shi, gaisuwar da ya tsana wai wani *Ina kwana*, sai kace wani sa.anta!

Yana nan tsaye har ta gama daurin dan kwalin da ya boye baki daya gashin kanta, ta dauki turaren ruwa ta kuma fesawa a jikinta mai sanyin kanshi wanda Ayya ta sayi kwali guda irinsa sunnansa princesse ,

Kwali ta dadage ta saka sannan ta shafa dan man lebe kadan,  ,

Mikewa ta yi ta juyo facing dinsa tana dubansa yana dubanta, a hankali ta shiga takawa tana nufo shi, wanda du takunta daya sai ya ji gabansa ya dadage ya fadi , da sauri ya kawar da dubansa a kanta daidai nan ya jiyo muryar Ayya,

Tamkar an hankada shi haka ya fito daga dakinta wanda har ya waiwaya da sauri yana duban kofar, hankali ya furta" innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, abinda Wardugu ya furta kennan kafin yake tura dakin Mu.azam dake kasa kadan da dakunnan su Ayya ya shige ya rufo ya nufi gaban madubi da sauri,

Duban kansa ya tsaya yi, kaki ne a jikinsa, sosai yannayinsa na ban tsoro ya bayana a jikinsa, sai dai kaki din wandon ne kawai sai bakar rigar da ya saka, a fili ya furta" ko dai makauniya ce?

😳😳😳😳😳😳

Ba laifi yau kun yi comment, dan haka ga kari😍😍😍😍😍😍

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

3️⃣8️⃣
```

Murmushi ya yi bayan ya tabatarwa kansa da yarinyar ba makauniya bace tana gani sosai,
To aman ayar tambayar shi ne me ya sa bata tsoronsa? Ko ta tsaya ta shagalta a kallon sa kamar yanda du yawancin mata da mata ke yi? Bale ita da ga irin wajen da ta fito wato kauye zai kasance shi ya zama abin kallo a wajenta, sai dai abin mamaki tamkar ba.a yi halitarsa a gabanta ba,

Kansa ya girgiza a fili ya furta" Ayya kwashe kwashe, idan kuma aljana kika kwaso mana ba sai ki huta ba🥴.

Sai da ya gama abubuwansa sannan ya juya ya fice ya tafi falo domin yana jin hayaniyar samarin biyu da muryar Annarsa.

Agaishat tsam ta yi bayan fitarsa ta sauke ajiyar zuciya, murmushi ya kubuce mata a fili ta furta" idan Mu.azam nawa zai aure ni, cikin abokan ango da zasu zo daukana a rakumi (🙁😕😟 ke malama a birni kike🙄), harda wannan mai kama da mutanen cikin alon nuno mutane (tv), Dariya ta yi tana dafe goshinta ta ce" kai aman katoto ne, kuma wai dan Ayya ne🤦‍♀️, ko ta yaya ta goya shi?

Kys din Ayya ta dauko ta juyo zata fita, ta ja ta tsaya ta dubi wajen da Wardugu ya tsaya ya zuba mata ido, nuna wajen ta yi da hannunta ta ce" kai katoto, ka daina irin kallon nan, baba sofo yace ba kyau irin kallon nan da kake!
Yatsina fuskarta ta yi , ambaton sunnan baba sofo da ta yi ya sace mata lakar jiki, a hankali ta shiga takawa da zancen zucin ko ya yake? Ya Annarta? Ya yan uwanta? Ko da wasa bata tuna yannayin mahaifinta, sai ta tuna da baba tsofo sau dari bata kawo sunnan Ba a layin zuciyarta ba, tsananin tsoronsa da ya dasa mata ya saka har a zuciyarta idan ta yi kamar ta tuna shi sai ta gargadi kanta cewar ki kula Agaishat kiyayarsa gare ki madaukakiya ce.

Agaishat na saukowa, kanshin turaranta ya fara karasowa, kafin a hankali ta idasa fitowa fallon,

Da murmushi Ayya ke kallon ta, domin ta ji dadin irin yanda yar tata ta koyi saka kaya da wuri haka,
Mu.azam da ya dago daga hirar da yake yiwa Wardugu ya zuba mata mayatatun idannuwansa , zuciyarsa na luguden kida yana dubanta da wani yannayi mai nuni da " kin azabtar da ni,

Wardugu dake gefensa yana saurаron sa, jin ya yi shiru ya saka shi duba wajen nasa, nan ya bi abinda ya tsurawa ido, ya kai dubansa wajen Aghali da yana tsakar waya da mamansa yana shaida mata ya sauka lafia, aman ya tsaya mamakin wai yarinyar da Ayya ta dauko ce haka?
Da sauri Wardugu ya mayar da dubansa wajen Mu.azam, shima zuba masa idon ya yi yanai masa kallo mai cike da ma.anoni,

Salama ta yi , kafin ta zarce wajen Ayya , inda a takaice ta ce" ina kwana.......... (wannan na

cikin abubuwan da Ayya ta koya mata, cewar ta ringa kiyaye sakin baki, kai ko gaisar da bako zatai ta takaita , in dai ta yi salama cikakiya halas!)

Tana zuwa ta zauna inda Ayya ta nuna mata,
Hannunta Ayya ta kama tana duba faratunnanta , domin ta umarce ta da sakawa yatsutsanta jan lale,
Ta kuwa saka , ya kama yai mata das a hannun ,
Ayya ta saki hannun ta lakaci kuncinta, kafin ta yi kiran Hanne, kan ta kawowa yarinyarta abin kari,

Kai Wardugu ya girgiza, ya mike yana daukan wayarsa ya kai dubansa wajen samarin dan ya ankarar da su , da haushi haushi ya ce" ni zan tafi,

Da sauri Aghali ya mike yana fadin" zamu tafi dai oga,

Wardugu ya ce" a mashin fa nake Aghali,

Aghali ya dafe kansa, ya kai duban sa wajen Mu.azam ya ce" docter tashi mu je ka kai ni ,

Mu.azam ya dubo su, irin yanda Wardugu ya yi kicin kicin da fuska ya san ko sun bi shi walahi zai bace masu ne, dan haka ya ce" ni sai na karya,

Idan kana so ka karye! Wardugu ya fada ya juya yana fadin" premiere dame (First lady, wato Ayyarsa), sai na dawo ,

Ayya ta amsa shi da" ka dawo lafia *War*,

Haka ya fice a gidan cike da takaicin girman kan yarinyar, domin shi kawai ya ajiye haka a matsayin girman kai, wai su *Ashak* ko? Ba buzuwa ba dai, su waye ma su buzayen nan da suka raina mutane har suke yiwa mutane Ashak?
Sosai ya kunsa a lamarin Agaishat ya bashi mamaki, wanda hakan ya saka ya dauki aniyar nazartarta a tsanake, shi zai koya mata ladabi da biyaya a haukace! (Toh fa),

Kuka take na tashin hankali tun da ta shiga bayin da kamar minti biyar, da gudu ta fito ta mikowa mamanta abinda ta yi gwajin fitsarin nata dan gannin ko ciki ne da ita? Domin tunda Wardugu ya yi maganar komai nata ya tsaya ya daina aiki,

Da yannayin farin ciki uwar ke dubanta, ta ce" kukan murna kike ko na me Walyn??

Da madaukakin tashin hankali ta ce" ba zan haihu yanzu ba, bana son cikin nan walahi sai an zubar da shi, bana so!

Da mamaki uwar ta mike tana dubanta, kafin take nunota da yatsa ta ce" ke ke ke, da hankalin ki kuwa?

Walyn ta dan tsagaita kukanta ta dubi uwar, kafin take kara barkewa da wani kukan ta ce" ba zan yarda na dauki ciki da Wardugu a wannan lokacin ba, a bai tabatar ina da ciki bama ya yi min rantsuwar sai ya yi mini kishiya ina da ya gane ina dauke da ciki?

La haula wala kuwata ila bilah, maman Walyn ta fada, ke bashi da hankali? Yaushe ma aka yi auren da har ya fara yi maki maganar zai maki kishiya? Me kikai masa da zafi? Ki bakya barinsa zuwa wajen ki yanda ya dace?, fada mani me ki kai masa da zafi haka?

Nan walyn ta warwarewa mahaifiyarta yanda suka yi da Wardugu,

Haushi kamar uwar zata dake ta ta ce" yaushe zaki gane mahaukaci ki ke aure ki iya takun ki da iya zama da shi?

Da sauri Walyn ta ce" Ma, Wardugu ba mahaukaci bane !

Uwar ta yatsina fuska tana dubanta ta ce" toh dan uban ki ba mahaukacin bane, aman wannan cikin ko aman jini kike sai kin haife shi kin sama mana magaji, ke ko me zaki yi sai kin kawo shi duniya, bara ma ki ga na fada masa, ai shi kina tsoron sa tamkar ran ki! banza sakarya marar tunani!.....

Rigima ta kirki suka kwasa kafin da kyar ta samu ta zaunar da ita ta ce" Walyn , kina bani kunya a rayuwa, wani lokacin har kokonto nake ko dai an canza min ke a asibiti ne? Ina yi bakin kokarina dan gannin kin yi fice a gidan ki aman a kulun sai da hadu da abin takaici abin mamakin da zai saka ni jin kunya,

Matar Batube, ta kasance tamkar abinda ya malaka kwalin kwal a duniya, wanda tamkar numfashinsa ne, yana ririta ta, yana kulawa da lamarin ta kafin na kowa, na sani ci sha sutura kilacewa, kayan burga ba wanda baki da, matsalar daya ne baki isa ki saka mijin ki ko ki hana shi ba! Menene dalilin haka? Na kasa ganewa, na kasa ganewa walyn,

Walyn dake zaune du ta hade jikinta, a ranta kuwa ayannawa take ko da jaraba sai ta zubar da wani tsinanan ciki, a haka ma tana cas cas dinta yanai mata maganar kishiya, ina da ta haife? Bama zai yiwu ba, idan ta haifi guda ai ta kama hanya, kofa ta budu, sauran zasu zo ko fa balaki ne, kennan shikenan kishiya ta tabata a gare ta ? Duda tana tsoron lamarin wardugu, ya yi aure haka ba tare da ya cika al.ada ba ba damunsa zai yi ba, tsohuwar uwarsa kuwa ba tirsasa shi zatai ba!

Mrning alll

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

39

*baki ba zai iya misalta maku irin yanda zuciya ke cike da farin cikin karanta ku Bak'a fans, Allah ya bar kauna baki daya*

Ya Allah, kar ka kai labarin mutuwarmu zuwa kunnen da baki ba zai fadi alkhairi kan gawarmu ba 👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻😭

Haka Walyn ta wuni wajen mahaifiyarta , inda uwar ke kwatanta mata yanda zata yi ta ci ribar zama da wardugu, ita kuwa tana tsara yanda zata rabu da ciki!

Tana komawa gidanta ta zauna falo, ko kayan bata iya cirewa ba tsabar tana cikin tashin hankali, fatar jikinta kuwa du ta yi ja abinka da jan mutun,

Tv ta kunna ta kamo tashar labaru,
```

An yi sa.a kuwa ana watso labarun su Aisata kan an yi bincike har an fara cafko masu shigo da kwayar, inda alkali zai yanke masu hukunci, , nan aka hasko sunnanta baro baro hade da sunnan mahaifin wardugu, aka fadi cewar ta bada hadin kai wajen kamo wasu masu harkar dan haka zata samu sasauci kan hukuncin da aka yanke mata,

Tsaki ta ja ta kashe tv din ta mike nan ta shiga baci domin ji take tamkar idannuwanta na dauke da yaji ne dan tsabar nauyin da su kai mata.

Wardugu na tsaka da aikinsa aka shigo aka shaida masa Marahut na son ganninsa, a shigo da shi ko kuwa?

Wardugu ya dafe goshinsa, a ransa ya ayanna me ke damun Elhaj Marahut ne da zai mayar min da office wajen zuwa haka?

Umarnin a shigo da shi ya bayar , ya ci gaba da aiyukansa yana hada takardun wasu yan gudun hijira ne da aka kamo , ya duduba da kyau ya ga du yawanci yan libia italia da dai sauran su, yana son mika su hannun likitoci a duba lafiarsu kafin su yi masu takardun tafia su juya garuruwan su!

Shigowa Marahut ya yi ya zo ya zauna saman kujerar zaman mutun daya yana duban Wardugu,
Kai shima yana alfahari da namijin yaron nasa, suna mugun kama aman ko a zamanin da yana saurayo bai kai Wardugu tsayi da yannayin karfi da cikowa irin nasa haka ba,

Murmushi ya yi masa ya miko masa hannu ya ce" Asalamu alaika Wardugu

Dago da kansa ya yi , a nitse ya miko masa hannun shima ya amsa da"  amine wa.alaika salam *Elhaj Marahut*.

Murmushi ya kuma yi ya rike hannun na wardugu, sam baya son sakin hannun, rabonsa da rike hannun yaron har ya manta,

Da ido Wardugu ya yi masa nuni da ya cika shi mana?

Sakin hannun ya yi , a nitse ya ce" Wardugu sunana kake kamawa haka ko?

Wardugu ya dube shi, ya yi masa murmushi ya mayar da dubansa kan takardarsa,

Ka saka baki wajen alkalin nan ya sasauta mata hukuncin da ya dauka a kanta, kaso har na shekara biyar ya yi tsauri Wardugu,

Wardugu ya dago yana dubansa , ya ce" ka san ba hurumina bane, sannan bana saka hanuna

a irin haka, kaima ai kana da hanyar hanata yin kason ma domin ka fi ni fada a ji a wajen su,

Wardugu sunana zai bace Wardugu, sannan hakinta a kaina yake! Marahut ya fada yana dubansa da yannayin iya gaskiyarsa kennan

Wardugu ya ce" ni nawa sunnan sai na kai na dulmiya ko? Ah koda yake daman sunana a bace yake a bakin al.umar da suka aikata laifi, sai ya yi ta baci jar a bakin wa.inda basu taka dokar bama?

Marahut ya dafe goshinsa, ransa ya fara baci ya ce" har sai yaushe zaka daina mugun fushin nan a kaina? Ni fa na haife ka! Baka tsoron goben ka? Kai idan naka suka ki yi maka biyaya fa? Wardugu ba laifina bane abinda ya faru a baya ,

Wardugu ya dube shi ido cikin ido ya ce" wannan tsohuwar magana ce Marahut, kana iya tafia ba zan saka bakina a maganar iyalinka ba!

Wardugu! Ya fada da dan karfi yana mikewa,

Wardugu ma ya mike ya ce" Marahut!

Marahut ya tsura masa ido, a hankali ya ce" dan na kula wata, na aureta , ba laifina bane, laifin uwarka ne! Sannan dalilin halayan da na gane nata na rabu fa ita yanzu,

Wardugu ya hadiye abinda ya tsaya masa a wuya, ya karya kansa ya ce" sai dai yanzu Wardugu bashi da budurwa bare ka kwace,

Marahut ya daga hannunsa ya zabga masa mari wanda ya yi mugun kara kara, ji kake tas, ya maya masa a gefen kuncinsa wanda hakan ya sa hularsa dagawa,

Kan Wardugu a kasa a hankali ya dago jajayen idannuwansa ya sauke a fuskar mahaifinsa, Mahaifinsa, ubansa, wanda ya haife shi, a yau ya so a ce wani ne ya kai hannunsa jikinsa, kai kai kai, balaki,
Ido cikin ido suke duban juna, Marahut ya ce" ko me ka zama, ko me kake takama da shi dai haihuwarka aka yi, na yi tunanin rashin mutuncin naka zai saka ka daga hannu ka rama! Ka rama marin mana Wardugu!

Wardugu ya sakar masa murmushi mai ciwo , a hankali ya ce" ko shege mai mutunci ba zai rama ba bare kai da ka haifi dan halal ka bashi tarbiya?, kar ka daga murya yarana su ji, domin ban san in zan iya rike kowa, wai ina gudun ba nan gaban idona ba, ka san soja shegen yawo ne da shi, gashi da ramuwar gaya,
Ka je kawai Marahut.

Jikin Marahut ne ya yi sanyi, ji yake dama da hali da ya rungume shi ya shafa wajen da ya mare

shi ya bashi hakuri,
A hankali zuciyarsa ke sauka har ya ji dumbin kaunar dan ta kuma mamaye khalbinsa  bashi da wani , baya tunanin zai samu daga shi, fatansa su sauko daga dokin zuciyar da suka hau bisa gangancinsa, sai dai ya rasa yaya zai yi, shi ba zai duka gabansu ya basu hakuri dan  ya kara aure ba, su ya dace su yi hankali su zubar da makaman yakin su, yanzuma ba wai ya zo ne dan Wardugu ya yi magana harkar Aisata ba, shima yana iya sakawa a saketa aman ya barta ta je ta yi kasonta kawai domin ta taka doka, ciki harda ta musulunci , da aurensa a kanta take bin wasu mazan.
Ya zo me dan ya kara ganninsa su sami hira ta kusanci na da da uba, sai dai ga yanda ta kare,

A hankali ya juya dan barin Office din,
Ja ya yi ya tsaya, a hankali ya dawo ya dube shi, hularsa da ta dage ya janyo ya gyara masa a kansa, ya gyara masa gaban rigarsa da kyau ya ce" Allah ya yi maka albarka, na yafe maka dukan abinda ka yi min wanda na sani da wanda ban sani ba, Allah ya kare gabanka da bayanka!

Yana gama fadar haka ya juya ya fice a office din,

Ran Wardugu a cakule ya hade takardun ya fito gaba dayansa a haukace ya mikawa Lieutenan Jalo takardun bai masa magana ba yana kallon mashin dinsa ya fice ya bar shi a wajen aikin ya kama tafia a kafarsa cikin sauri, ya yi niya a kafa zai je gidansa ba zai hau mota ko mashin ba, ya ki din , kai bama zai kuma hawa ba! Zai je a kafarsa , du wanda ya fasa kawo masa wargi ya ki Allah! (🥴 wani da laifi , wani da shan duka? Tap🤔),


Bayan kwana biyu, fitina ta dan lafa gefen Wardugu,

Juma.a ce yau, ranar da ake bada damar shiga gannin yan gidan kaso harma a dan jima a wajen su,
A wannan ranar ne mutane ke cika prison dan gannin nasu,

Wannan damar Walyn ta rike ta yi shiga irin ta larabawa ta yane kanta da dan kwalin bakar abayar da ta saka ta yane har habarta sannan ta saka bakin gilas,

A kafa ta samu ta fito bakin titi nan ta ja ta tsayar da mai taxi ta yi shatar ita daya.

Basu zame ko.ina ba sai justice ta ciri takardar gannin dan prison ya dauketa ya sadata da gidan kason,

A hankali ta cire gilas din idonta, sannan ta dan ja mayafin dan bude habarta dan kar ta jawa kanta matsala da masu tsaron gidan kason

Takarda ta nuna, ta je saman kuje ta zauna inda aka shiga aka kirawo mata wanda ta zo nema,

A hankali take takowa har ta karaso wajen warda aka nuna mata a matsayin uta ke nemanta,

Kallonta take, irin kallon san sannin wacece? Hakan ya sa Walyn ta bude rufarta dan ta shaida ta,

Murmushi Aisata ta yi tana dubanta, aman a kasan zuciyarta mugun kishin Walyn take, kai da tana da dama da ita ce ajalin yarinyar da ta auri gwarzonta!

Walyn ta kare mata kallo sama da kasa, cike da yanka da jan aji ta ce" *wanene shi*?

Bata amsa ba , sai da girarta irin na rikakun yan duniya da suka san kansu ta yi mata tambayar *Wane?*

Walyn ta fara shaka ta dubeta da kyau ta ce" *waye malamin da ya miki aiki kan Wardugu da mahaifinsa?* waye shi?, idan kika fada mani komai, zan saka a fitar da ke daga wajen nan.

Murmushin rainin hankali ta yi tana dubanta, cikin kissa ta ce" kina da damar sakawa a fitar da ni din ne kika shigo cikin gidan kaso dan samu adress din malamina?
Kina son samun kanki ne a wajen Gwarzona?

.........

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---
```

40

*Walahi ni ba kowa bace, ni ba komai bace, Allah ne gatana👏🏻😕👏🏻*

Walyn ta zaro ido, rai bace ta ce" zan datse harshen ki idan kika kuma kiran mijina da gwarzon ki!

Aisata ta ce" da kuwa na ji dadin yin makota da ke, da zan gani idan kema da ya kilace zai saka ki a kaso dan kin zalinci wani!

Walyn ta tsareta da ido, a hankali ta ce" zan biya ki, ki fada min kar lokacin da aka bamu ya kare ,

Aisata ta ce" na sani kina da damar iya biyana aiki, dan ni mai nema ce, ina nema kamar me, kudi baya isata, da yana isata da na tsaya da sirikin ki kawai!

Walyn ta ja tsaki ta ce" lokaci!

Aisata ta ce" kar ki damu, yau ai akoy lokaci isashe ,

Walyn ta kuma tsareta da ido, ta ce" me zai rage ki dan kin fada mani? Kin san dai kin haramta wa wardugu tunda kika kwonta da ubansa!

Aisata ta lumshe idannuwanta, a hankali ta lashe lebenta na kasa, rage murya ta yi kamar zataiwa Walyn rada ta ce" *Ke ba fa kowa ke da haram ba*,

Walyn ta daki table din ta ce" zaki fada mani ko ba zaki fada mani ba?
Har sai da hankali ya kawo kansu inda wani soja ya karaso yana tambayar lafia?
Nan Aisata ta kalamance shi da"Oga ba komai,

Juyawa ya yi ya koma, Aisata ta dubeta da kyau ta ce" kina tunanin na taka farar kafata na je wajen Boka dan tsibu dan ya malaka min saurayi? Kina tunanin aikin boka ya malaka min mazaje biyu ?

Walyn ta ce" kin gane, ni fa ba yarinya karama bace, kuma na san bariki ki ka yi ! Dan haka kar ki bi min ta wannan hanyar ba gyara mu zata yi ba.

Aisata ta ja rigarta kadan, hakan ya baiwa saman mamarta damar fitowa sosai, ta ce" *kin ga malamaina*

Walyn dake kallonta ta yi dariya tana girgiza kai ta ce" ba dai Warsuguna ba, Wannan abin bai isa ya ja ra.ayin namiji mai sunna namiji ba!

Aisata ta ce" haka ya fada maki? Ko irin zaman da kike yi da shi?

Walyn ta ce" ba sai ya fada mani ba, haka ne, Wardugu kamili ne, girman kansa ba zai bar shi bama ya lura da wani abin jikin yar bariki!

Aisata ta bushe da dariya har tana rike ciki, nunata ta yi da yatsa ta kuma kecewa da dariya, sai da ta yi mai isarta ta ce" lale kin rako mata, ina mai baki albishir din in dai kallon da kike masa kennan ki farka tun kafin ki kuma jaza mana wata yar balakin da ta fi mu ta karbe mana Gwarzon mu!

Walyn bata ce mata komai ba, sai duban kin raina min wayo da take mata,

Aisata ta tsagaita tana duban Walyn ta ce" Walyn Wardugu, ba kowace mace ce ta san kofar boka ba, koda kina jidana da na yi bariki dan na fita da d'a na kuma dawo kan uba , ina mai tabatar maki ba boka ne ya tsaya min ba.

Ya zan zo cikin wannan wajen mai fitar da wari ki saka ni gaba kina yi min rainin wayo? Walyn ta fada,

Aisata ta juya idannuwanta ta ce" kar ki yi garaje, zuwa gidan yari rubutu ne wanda Allah ke kadara shi, diyawa a wajen nan basu taka basu karya ba....
Walyn bara ki ji wani abu....: du namiji na duniya yana da abinda idan ya ganshi a gabansa yakan ji ya rasa dabararsa,
Wani namijin mace mai kissa, mai kisisina, mace mai kyan dan maciji ke tafia da imaninsa, wani namijin mace mai adini mai rufe jikinta, mai mutunta kanta ke tafia da imaninsa, wani namijin yana son mace mai halaya irin na yan bariki ce zabinsa, wanin mace mai kyau ko muguwa ce zasu taka rawar, wanin yana son mace mai shiru shiru, wanin yana son mace mai kamar maza irin mai kafkaf da ita, wani baya jure gannin mace a cikin yannayi na abin tausayi...zaki ga ya fada tarkon kaunarta, wani farar mace ce zabinsa, wani kuwa *bak'a*, ke wani duka biyun yana so....tambayar a nan shi ne *Sai ka karanci mutun kake gane waye shi harma ka tabo wajen da ba zai jure ba, da kansa zai nuna shi sai kai*,

Walyn kallonta kawai take,

Aisata ta ci gaba" mijin ki dan ra.ayi ne, gwarzona ya bani wahalar da wani namijin bai bani ba , kyauna, zubina, yannayin rayuwana na saka shi fadin"Aisata ke matar kilacewa ce, ki yi zamanki a gida zan zo na dauke ki na mayar da ke matata. kafin na samu kansa na jigata.da kuka da komai ya furtan kalmar so, domin na kai karar tsohon saurayina wajensa inda na biya mutumin ya yi min dukan tsiya, ke dai na takaita maki sai da na zama tamkar kaska, du inda wardugu yake ina nan, da naci da taimakon aminiyarsa ya furtan kalmar so...
Sai dai abin haushi du irin yanda muke soyaya da shi idan na nuna koda shan minti ne a dan zaga sai ya fatatake ni,
A ranar da na tube zindir a gabansa sosai na kusa cin masa wani tsinanan abokinsa ya shigo dakin domin ke shaidan ba abinda baya hasawa , kwana dakin wardugu na kusan cinma burina nan na fahinci irin zaman da ake tsakanin matar Marahut da shi,

Ayya ta kasance mace mai tsafta, ta iya girki, tana yiwa mijinta biyaya ....sai dai na sha na fito tsakiyar dare falon su na kunnuwana su tsinkayo min rigimar ba zata bashi ba, ta gaji da ayyuka ya bari sai da safe!

Wani wal wal wal ta yi da idannuwanta ta ce" *Walyn ba.a matsa lamarin nan, idan aka tashi a yi kawai!*,

A lokacin da na gama gane Ayya ba zata aminta na auri farin cikina ba, na dauki damarar itama sai na cusa mata bakin ciki , kuma ko da kwaya sai na kwonta da d'anta!

Walyn ta ce" shi Marahut din asiri ki kai masa ko?

Aisata ta ce" na fada maki ban san wannan ba!

Walyn ta rafka tagumi ta ce" fada mani yanda kika tarwatsa su , mai yiwuwa na yarda da labarin wai Wardugu ba asiri ki kai masa ba.

Aisata ta buda bakinta zata fada mata kennan aka zo aka ce ya isa haka sun jima suna hira domin dai Aisata harkar kwaya ya kaita kaso, ido a kanta yake dan kar a kawo mata har gidan kaso...

Haka Walyn na ji na gani ta fito ta kama hanyar gidanta ba tare da ta samu komai ba!

Alhinayet ce zaune tare da saurayinta, malamin university ne, saurayi ne domin bai taba aure ba, bazabarme ne baki dogo , hira suke cikin nishadi nan yake shaida mata yana son turowa,

Alhinayet ta fada masa zata fadawa abanta tukunnan , abinda ya ce in sha Allah.

Haka suka gama hirar su ya mike ya yi mata salama ya shige motarsa ya tafi,

Mikewa ta yi ta je cikin gidansu ,
Shiryawa ta yi ta saka dogon hijab dinta blue, ta dauki bakar leda ta je wajen mamansu , wato matar mahaifin su ta shaida mata zata je ta kaiwa Agaishat hijaban

Adu.a ta yi mata kafin take fita ta shiga motarta ta tayar ta nufi gidan Ayya.............

Aghali ya zo garin Niamey ne dan duba gininsu da ake yi a unguwar cité laraba,
Ya gama abinda ya kawo shi aman ya ki tafia bisa bukatarsa na Wardugu ya siyar masa da mota , sun tsayar zai shigo ranar lahadi wato gobe baya aiki sai su fita su je ya gani......

Soyaya suke a nitse, a hankali yake koya mata mecece soyayar ma wace a kulun sai sun gama bitar zai jefo mata tambayar" Agaishana, shin kina jin du abubuwan da na zana maki a kaina?

Dariya take yi a fili sai tace" ni yaya Mu.azam gudun fankan dakin Hane mai aiki kawai ke saka zuciyata gudu, ka ci gaba da koya mani na san zata yi gudun wata rana idan na ganka

Yakan tsareta da ido ne kawai , bai san me zai da ita ba, soyaya ai shigar farat daya take yi, shi da yake so ya kai kudirinsa wajen Ayya kan a aura masa ita da wuri? Kai ba zai wani jira har ta kamu da sonsa ba, zata so shi a zaman da zasu yi, shi kam yana kwadayin zama da ita a rayuwa....

Docter Mariam ce tsaye tare da shugabansu ta asibiti, kanta duke kuka ne take har jikinta na bari ta ce" nima marainiya ce docter, a lokacin da na zo wajen nan shi ya tarbe ni, ya ciyar da ni da aljihunsa, kafin na tsaya da kafafuwana shi ne komaina, tun a lokacin nake mugun son sa, ba zan yafewa kaina idan ban je na dawo da shi ba, ki taimaka mani ki sama mani takardar nan na roke ki,

Cike da tausayi take dubanta, su musulmai haka suke ko kuwa wasu da wasu ne? Tana jinjina girman son da Mariama ke yiwa docter mu.azam, in sha Allah zata sama mata takardar su biyu wace zata bata damar zuwa ta zo da shi su shiga aiki, koda bai tashi ba , ba zata tsangwami kanta ba,

A hankali ta dafa kanta ta ce" kar ki damu Docter, ki je zan neme ki, zan nema maki takardar

Da murnarta ta yi godiya ta fito ta shiga office dinta, hotonsu ta kaiwa duba kafin a fili ta ce" wai baka son farar mace ko? Dole ka so ni docter, ni ina son ka😭😭😭

Wayo hanuna😕😕😕😕😕😕

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

4️⃣1️⃣

Ayya ki duba lamarina na roke ki,
Mu.azan ya fada kansa a kasa, kunya ta hana shi dago da kansa ya dubi Ayya domin ya fadi abu mafi nauyi a bakinsa

Da mamaki take kallonsa, so? Aure? Yana son Auren Agaishat? Aman yaushe suka yi wata soyaya da fahimta har za.a kai ga aure?

A nitse ta ce" Mu.azam, aman me ya sa kake sauri haka?

Mu.azam dake kallin kasa ya ce" Ayya , ina so ne a yi mu juya tare da ita.

Aman ai ka san sha.anin aure na bukatar nutsuwa ko? Sannan yarinyar nan amana na daukota daga garin su, eh lale mahaifiyarta ta bani damar ko aure ya tashi na yi mata aman da ransu da lafiarsu ba zan yanke hukunci irin na aure ba tare da yawun iyayen yarinyar ba ko? .... Ayya ta fada jikinta sanyaye tana dubansa

Mu.azam ya gyada kansa, hankalinsa ya dan fara tashi ya ce" Ayya, ki tura ni wajen dagin nata, na je na nemi a bani aurenta, bana son jan abin ne
```

Ayya ta kuma kale shi da mamaki, bai taba naci kan abu irin wannan ba, jikinta ta ji ya kara yin sanyi, aman Agaishat dinta dukanta ma nawa take da har za.a yi gagawa a lamarinta haka? Sai dai kuma bata tunanin Mu.azam zai wulakanta mata yarinya, duda haka tana son bin hanyar da kakarta ta bi da ita, zasu kai kulansu wajen Allah, a hankali ta ce" yarona, na ji, kuma zan fi kowa farin cikin sannin tana hannu mai kyau, kar ka damu zan san abin yi nan kusa in sha Allah, in dai Agaishat matarka ce zaka aureta kisa ba da jimawa ba.

Cike da murna ya yi mata godiya ya mike ya nufi dakinsa dan yin wanka,

Tsaye take a tsakiyar gidan tana kallon manyan tantabarun gidan dake kiwo nan balbalin gidan , tana yi tana duba kofa domin ranar juma.a da alhinayet ta zo tace zata dawo ranar lahadi su je gidan kitso Ayya sai fadan kitso take,

Kallonta yake daga inda yake tsaye, inda ya shiga takowa a hankali har ya karaso inda take tsaye, ma.ana suka jera,

A hankali ta dago da kanta daga kallon tantabarar ta kai dubanta wajensa , nan da nan ta matsa gaba sannan ta sada kanta kasa cikin yanayi na bawa wanda ke kusa girma.

Aghali ya ce" a garinku ke yar gidan waye?

Agaishat ta dube shi, ta kuma sada kanta, sarkinta ne, ita talakarsa ce, sarkinta ma talakansa ne, dan haka cikin yannayi na girmamawa ta ce" sunnan mahaifina *Ba*,

Ba , ai sunnan du uba ne a garin buzaye! Aghali ya fada yana kara tsareta da ido,

Agaishat ta ce" ka yi hakuri,

Aghali ya ce" baki min laifi ba,
Soyaya kike da shi? Kina tunanin zai mutunta ki zai so ki da zuciya daya?

Kallonta ta dago wannan karon ta sauke kan nasa,,

Bata kai ga bashi amsa ba Wardugu ya shigo da wata galeliyar mota fara kar, kusa da shi Alhinayet ce da ya dauko zai ajiye su wajen kitso wai🤦‍♀️,

Birki ya ja irin na ka taka baka shiryan nan ba, da bakin gilas dinsa ya dan kale su kafin yake taka motar ya karasa wajen da ya dace a ajiye motar.

Yana tsayawa ya kai dubansa wajensu, gani ya yi aghali na magana, yar gidan Ayya kuwa na kallon kasa, kansa ya girgiza kafin ya maida dubansa wajen Alhinayett ya ce" Alhi, Aba ya saka na yi bincike a kansa, yace bai yarda da adinninsa ba , hakan ne kuwa ba musulmi bane yace shi musulmi ne dan ya saje da jama.ar garin nan,

Alhinayett ta ce" General ya kuke so na yi ne? Ina zan shiga na samo wanda ya yi 100/100? Wannan na uku kennan yana zuwa da niyar aure abin na watsewa tun kafin a je ko.ina, Wardugu bana son auren Lieutenan na fada maka bana son auren soja.

Wardugu ya yi musrmushi yana dubanta ya ce" kuma ki ce ke aminiyata ce, a gabana kina fadin bakya son auren mai sana.ata, me zamu yi maki ne? Me muke yi?

Alhinayet ta girgiza kanta ta ce" Wardugu, bana iya zama da namiji mai mugun karfi, ba zan iya rigimar sojoji ba, ba zan iya firirita irin ta matan sojoji ba, ka san ko ni wacece ban iya fada ba, ban iya ihu ba Wardugu ina son namiji mai sanyin hali ne,

Wardugu ya ce" ba daga nan take ba, sai ki ga kin auri wanda ba sojan ba kuma ya kasance irin wanda bakya so din, kin gane Alhi ke dai ki yi adu.a , aman na san kina son lieutenant sosai, ke ra.ayinki na ba zaki auri soja ba dan bakya son mai fada, wannan ai shirme ne, ni na fi son ki auri wanda yake na san shi , du ranar da ya taka min ke na nuna masa bashi da wayo!

Murmushi ta yi ta kai hannunta suka cafke ta ce" Wardugu, aa fa, ba zaka dakar min miji ba wollah....

Ido ya zaro ya ce" kai, har kin fi son shi da ni?

Bakinta ta yatsina tana hararsa da wasa ta ce" oyah bude na gaishe da Ayya mu tafi kar yama ta yi sosai ,

Idannuwansa ya kai wajen su, nan ya ga Aghali baya wajen aman ita tana tsaye,
Cikin hijaban da Alhinayet ta kawo mata ne ta saka milk mai haske, hijabin har kasa yake mai hannaye sannan tamkar zubin riga aka yi masa ya dinku ya yi kyau sosai, ta saka takalminta mai dan tsini kadan da igiyoyinsa ta daure abinta das da ita,
Ajiyar zuciya ya sauke ya kai dubansa wajen Alhinayett da ya ga ta tsare shi da ido, sarai ta ga me yake kallo duda ya saka bakin gilas ya tamke kar a gane me yake ciki,

Kuma kallon wajen ta yi ta ga Agaishat ta juya wajen kofar falon ayya tana murmushi,

Wajen ta mayar da dubanta sai ta ga Mu.azam ne ya fito cikin shigarsa ta shada ya yi shar da shi , daga inda yake tsayen sai turo mata irin abin nan na soyaya yake sai yace Muah,

Ita kuwa sai ta rufe ido tana dariya,

Tsaki wardugu ya ja ya ce" ji wani shirme kuma?

Alhinayett da lumshe idannuwanta, ta ce" na me? Ba wani shirme walahi sai soyaya,

Dubanta ya yi kafin ya yi murmushi ya girgiza kansa, motar ya bude ya fita inda itama ta fito,

Tafiya ya fara da sauri sauri kamar yanda yake yi kulun, dakatawa ya yi ya dubota ya ce" kuma na saka ya tura magabatansa wajen Aba ,

Ido ta zaro ta ce" Wardugu, Wardugu,

Ina tuni ya yi tafiarsa,

Murmushi ta yi itama a fili ta ce" Wardugu zai min auren dole da soja.........

Yana zuwa suka gaisa da Mu.azam ya tsare shi da ido ya ce" haka ka koma kan mace? Ka saka yarinya gaba kana abu irin na yara?

Mu.azam ya daga girarsa ya ce" kai raba ni amini, soyaya ce,

Kai ya dafe yana mai jin matsanancin faduwar gaba, juyawa ya yi ya shige ya barshi nan kar ya hadasa masa hawan jini,

Ayya bata falo dan haka ya haye sama dakinta dan ya san Aghali wanka ya shiga .....

Yana zuwa ya gaisheta kamar yanda ya saba sannan ya zauna daf da ita yana dan mamatsa mata kafarta,

Ayya ta ce" Mu.azam ya zo min da maganar yana son auren Agaishat,

Wardugu dake rike da kafar Ayya yana matsawa sai tsayawa ya yi tsam da matsawar yana duban kasa,

Baka ji bane? Ayya ta fada,

A hankali ya dago dubansa ya sauke kanta, idannuwansa ya lumshe dan ji yake har kansa ya fara sara masa sanadiyar faduwar gaban da yake ji, me ke damuna? Ya tambayi kansa, me ya sa da an kirayi sunnan yarinyar nan ko na ganta sai na ji faduwar gaba?

Kansa kawai ya gyadawa Ayya,

Bakinta ta yatsina ta janye kafarta da haushi haushi ta ce" Wardugu bafa na son rainin hankali, ya zan fada maka magana ka wani gyada min kai sai kace inai maka wasiya?

Wardugu ya hadiye yawun bakinsa da kyar ya ce" Ayya, wai ya aka yi bakya yiwa sunana kara irin na d'An farin nan? Sai kawai in ji kin kama sunana kai tsaye wai Wardugu,

Ido ta zaro tana dubansa yanda ya yi maganar walahi sai ta ji wata kunyarsa ta kamata, ai kuwa ta juya ta dauki filo ta juyo dan buga masa sai gani ta yi ya fice da gudu a dakin,

Murmushi ta yi ta ce" ja.iri, ja.iri, ja.iri, !

Zan yi magana da yarinyata , in dai tana son sa, zan baiwa Aghali sako ya je da kansa wajen Mahaifanta idan sun amince ya kai kudin aurenta a daura kawai, Allah ya sa Alhairi ne......

To fa🥴🥴🥴🥴
😎😎😎😎😎😎😎😎😎😎

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

4️⃣2️⃣

Alhamdulilah Alla kulli halin...

A wannan rana bayan Wardugu ya ajiye su agaishat saloon dan yin kitso suka zarce park dinsa tare da samarin, inda Aghali ya zabi daleliyar mota irin ta ratsa rairai mai shegen tsada,
```

Bayan sun gama magana da yaron Wardugu, Mu.azam ya tsaya gurin wata mota mai ruwan ash , karama mai kyan gaske, kallonta yake yana murmushi,

Wardugu ya gama da Aghali yace" ku mu je ....

Mu.azam ya ce" wardugu, wannan motar nake so,

Aghali ya ce" me zaka yi da motar nan kai kuwa? Ta mata ne fa,

Mu.azan zai bashi amsa ya ji lumlumlum lema a hancinsa,
Da sauri ya juya yana mai ciri hankicin a aljihunsa ya goge jinnin da ya zubo masa ta hanci, a hankali ya karasa motar Wardugu ya bude baya ya shiga ya jinginar da kansa jikin kujera,
Ajiyar zuciya yake saukewa yana kara goge jinnin inda wata number ta fara shigowa saman screen dinsa, number saudiya ce,
A kasan zuciyarsa ya ji nutsuwa da number dan haka ya daga ya yi shiru ba tare da ya yi magana ba,

Ajiyar zuciya ta sauke kafin take share dan guntun hawayenta, so take ta yi magana tana tsoron kar ya ji muryarta ya kashe , ta godewa Allah da da ransa, ta godewa Allah da ya daga wayarta duda bai san ko wacece ba,
A hankali ta ce" ina son ka Mu.azam

Sai da ya ji wata kasala, a hankali ya dubi screen din, ya mayar kunnensa, ji ya yi wata nutsuwa na kara ratsa shi, a nitse ya ce" docterna, me kika je yi saudiya a tsakiyar shekara?

Idannuwanta ta lumshe ta ce" na zo rokar Allah ya baka lafia, ya nuna min jininka a duniya,

Murmushi ya yi ya girgiza kai, ya ce" kin ga jini ke zuba a hancina, bayan ina son na yi aure, har na saka a tambaya min auren yar, ina son yarinyar a raina ina son na aureta koda shi kadai zan yi a duniya,

Wani irin faduwar gaba ta ji, jikinta ya dauki rawa, a hankali hawaye ya shiga zarya a idannuwanta, a hankali ta ce" zaka aureta, kar ka damu, zaka rayu Mu.azam,

Shima idannuwansa nasa ya lumshe yana mai jinta gaba daya jikinsa, yana son yarinyar nan fa tamkar ransa, sai dai ba zai yarda haka ta faru da ita ba, ba zai yarda yana ji yana gani ya tsareta haka ba, ya sani ne idan ya nuna mata eh yana so zata sakawa ranta da zata jima da shi bayan yana ji a jikinsa an kusa zare sauran numfashin da ya ragewa gangar jikinsa,
A hankali ya datse kiran inda ya shiga shafa kansa yana mai jin jikinsa ya dauki zafi,, a hankali ya furta Agaishat ki aminta da ni na dan lokaci, ina son ki kema (🙄)

Wardugu da kansa ya fitarwa da Aghali motar nan dan baya so a komawa su yi mota daya, yana gama fitar masa da komai ya bashi hannu ya ce" aboki, ka gama da Muhsin ni sauri nake,

Amanda aghali ya yi inda ya raka Wardugu da kallo yana ayyana a ransa ko lafia?

Wardugu na tafiya yana sake sake a zuciyarsa, yakan tsinci kansa wani sakarai idan ya ganshi gaban wanda yake so a ransa yana cikin wani halin da ba zai iya fitar da shi ba,
Motar ya bude ya shiga, a hankali ya juya fuskarsa gefensa ya ga ya lumshe ido tamkar mai barci,
Motar ya tayar ya juya a hankali ya nufi saloon din da ya ajiye su Alhinayett

Yana zuwa ya yi mata message cewar ta turo masa Agaishat, yana kofa,

Ba tare da ta tambayi komai ba ta dubi Agaishat da aka gama yi mata tsararan kitso a kanta mai dan girma girma aka saka wani dan roba a karshen kitson dan kar ya warware , ta mugun yin kyau tace da ita ta je mota wardugu na kiranta,

Duda gabanta ya fadi, aman sai ta dake ta mike tana tunannin lafia? Domin yace idan sun gama su yi tafiarsu, wani abu ya faru ne?
Bata da amsar da ta fi ta fice a nitse tana mai jin faduwar gaba,

Wardugu dake kallonta tunda ta fito, du takunta daya na kayar masa da gaban da bai san na meye ba, ya dai ajiye hakan a matsayin zai shige gaban abinda bai taba shiga ba, zai shiga rayuwarsu ba tare da izininsu ba, zai yi iya yinsa dan faranta ran aminínsa,
Kare mata kallo yake, a kasan zuciyarsa ya ayanna""""""meye na naci a kan bakar mace? Menene sirin Mu.azam?,
Tana kara kusanto motar yana kara dubanta dan so yake sai ya karanto sirin a tare da ita, ,
Da yake ta gaban motar take nufo motar, kuma Wardugu ne ke tuka motar hakan ya saka idannuwanta sauka cikin nasa, manyan idannuwanta masu ruwan madara da bakin dake tsakiya mai girma wanda ke watso da hasken ruwa ruwa yana sheki , kallon nan mai shige da mai jin bacu shine kallon Agaishat wanda hakan ya samo asali da tun tana karama mahaifinta bata isa ta daga ido ta kale shi ba, sai ta saba da yin kalli a lumshe tamkar zata rufe idon aman kuma ta fi wanda ke kallo tar tar ganni domin wata kibiya ce ke jefo gannin nata har wajen inda ta yi niyar kallo,
A hankali ta lumshe idannuwanta wa.inda ta yi niyar cire nata idannuwan a idannuwan Wardugu, domin kuwa tsai kallo na cikin ido sukaiwa juna wanda basu san da haka ba sai fa ta cire nata ya farka ya yi gagawar mayar da dubansa wajen Mu.azam dake jingine da kofar motar, Murya a dake ya ce" malan dan bani waje zan tatauna da yarinyar can,

Sai a lokacin Mu.azam ya ga Agaishat ce ke karasowa wajen motarsu , a wannan lokacin har ta karaso sosai jikin motar tana jira a bude mata kanta a kasa,

Mu.azam ya kali Wardugu , murya a raunane ya ce" war, kar ka yi min haka , me ta yi? Dan

allah kar ka yi mata fada ko ka rikitata, na tuba ,

Wardugu ya tsare shi da ido yana mai jin wani tsoro a ransa da faduwar gaba, mutun ne shi tamkar kowa, dole abinda zai kayarwa kowa gaba ya kayar masa, sai dai ba zai taba nunawa ba, ba zai taba bari wani ya san halin jin tsoronsa ko faduwar gabansa ba,

Da ido ya nunawa Mu.azam ya fice fa,

Mu.azam ya turo baki ya bude motar ya fitar da kafa daya ya juyo fa haushi haushi ya ce" idan ka batawa abin kaunana rai , sai na tarar da wannan matar taka na nuna mata waye bos Mu.azam!

Wardugu dai bai ce da shi komai ba har ya fita a motar ya tsaya yana kallonta kafin ya bude mata gidan bayan ta shiga motar jikinta a sanyaye ta gyara hijabinta ta kai dubanta Wajen Wardugu,

Yana son magana da ita wanda zai fuskanceta, ya sani shi ya dace ya koma baya ko dan saboda gaban ana iya kallon su ta gaba du wanda zai fice, aman wani abu ya tsaya masa ya hana shi fita ya koma bayan motar,

Dakewa ya yi , ya ce" dawo gaba.

Agaishat dake duban gaban motar ta kai dubanta wajensa, a ranta fadi take" shi koda yaushe fuskarsa ba wani fara.a zai wani tantankewa yake yiwa mutane, to ni me na yi masa ?

A hankali ya dago da kansa ya juyo fuskarsa dan bai ji ta motsa dan bin umarninsa ba,
Kamar na dazu yanzun ma idannuwansu ne suka sarke da juna, a tare gabansu ya shiga luguden duka ,
Wannan karin Wardugu kasa cire idannuwansa ya yi a nata , tsai ya tsaya cikin kogin idannuwanta yana mai jinsa baki daya a cikin idon,
Da sauri Agaishat ta janye kwayoyin idannuwan nata a nasa ta shiga kokarin bude motar hannayenta na rawa baki daya tana neman nutsuwarta na neman gagararta,

Bude motar ta yi ta fita, shakar sansanyar iskar duniyar ta yi kafin ta juya da dukan kuzarinta ta bude gidan gaban ta shiga,

Shi kam binta kawai yake da kallon da bai ya kureta da shi har haka ba, sam bai san yanai mata kallon da ya fice ka.ida a adinnance ba,

A hankali ta ja ta rufe kofar, aman wannan karon ta gagara dubansa cikin ido kamar yanda shi ya tsareta da idannuwansa wa.inda ta rasa gane me yake kallo,

Zuciyarta ke ingizata da ta dube shi, domin bayan ta dawo gaban ma ya yi shiru ne bai ce da ita komai ba, hakan ya saka a hankali ta kuma buda dara daran idannuwanta cikin nasa,

Lumshe ido ya yi ya kuma budewa kan fuskarta, haka kawai ya ji baya iya yi mata magana tun karfi ko eani gatsai gatsai, ji yayi yana kokarin sanyaya muryarsa fiye da yanda yake yiwa kowa magana a duniya, girmanta, tausayinta ne ya ji a lokaci guda, yana jin kunyarta wace bai san ko ta meye ba, ya ajiye hakan kan dan tana abar kaunar amininsa, tabas zai ci gaba da jin haka a tare da ita balema idan ta aminta da zuciya daya zata kular masa da amininsa,

Sangartar da muryarsa ya ci, marainiya ta zama a makogwaron sa, da kyar ya iya sarafata wajen fadin" *Kina son sa? Zaki rayu da shi?*

Ajiyar zuciya ta sauke mai cike da ma.anoni, kanta ta sada a hankali ta ce" *shi ne zabina*

Furucinta da faduwar gabansa ba zai tantance wane ya fi wani karfi wajen saka jinnin jikinsa gudu a karfin da ya zarce yanda yake, kirjinsa ke duka da sauri sauri inda ya ji hankalinsa ya tashi, ya rasa menene haka? Me ke faruwa da shi,
Dakewa ya yi ya cire hular kansa yana dan alamun fifita da ita, bai daina kallon Agaishat ba, ya ce" zaki iya rayuwa da shi da zuciya daya? Ki so shi domin Allah? Zaki sadaukar da komai na rayuwarki wa shi?

Dagowa ta yi ta tsurawa fuskar Wardugu ido, a hankali ta ce" *ka damu da amininka ko ka damu da amanarka?*

Bai bata amsa ba, domin bai fahimceta ba, dan haka ta gyara zamanta ta ce" a gida, muna da Anna daya, du yaran gidan yan uwa ne, daga bakin ranar da Anna ta baiwa Ayya ni na zama yar Ayya, hakan na nufin ni kanwarka ce, baba tsofo yace idan iyaye ko yayu kai dangi baki daya zasu yiwa yarinya aure hankalinsu a tashe yake, su ne bincike kan waye mijin? Halaya da sauransu, su ne tabatarwa idan yarinyar na son sa ne domin Allah, kai dai a firgice suke,
Dan Allah, *zaka zama yayana?* mai saurare na? Mai share kukana kamar yanda yayuna ke yi?

Tunda ta fara labarin lebenta yake kallo tamkar mai koyon yaren da take magana da shi, a hankali ya ringa jinta a jikinsa har ta zagaye ilahirin jikinsa, wani irin nanauyan abu ya ringa ji wanda zaka ji shi ne idan kana son abu, ko dan uwanka ko wani na jikinka sosai , farat daya Wardugu ya ji ya yi kanwa daya kwalin kwal, jal, kwara , wace yake mararin samu, ya jima yana son samun kanwa daga mahaifiyarsa dan ya shagwabata , ya ririta ta, ya sangarta ta, ta fi yar shugaban kasa gata, a yau a yanzu ya aminta da bakuwarsu, ya ji ta zama jikinsu, zai iya cewa ya samu kanwa, zai kare mata duka cuta, zai iya yin fito na fito da koma waye kanta! Agaishat Agaishat kanwa ce a ransa wace yaje jinta tamkar jini daya suka fito,
Ji ya yi zai iya sakewa ya yi hira da ita irin ta dan uwantaka, lokaci daya ta shiga kokonta idan ya aura mata mu.azam ya kyauta mata kuwa? Nan da nan zuciyarsa ta kwabe shi ta hanyar tunasar da shi ai komai na Allah ne , .

A hankali ya dan jirga jikinsa bangarenta yana dubanta , ya dan saki fuskarsa ba laifi, dan karamin yatsarsa ya miko mata ya ce" zaki zama kanwata?

Murmushi mai hade da dariya da farin ciki ta dan yi masa ta ki bashi hannun sai alamu da ta nuna zata hade hannayen nasu ita da shi ,

Shima murmushi ya sakar mata yana mai nuna alamun dimple dinta har biyu sun shige sosai,

A hankali ta ce" yayana,

Duda suna ne wanda kowa ke fada, karamin suna, sai da ya ji dadin abin, ya amsa mata da ido,

Agaishatt ta ce" *ina son sa!*...................................

I.m back😕😕😕

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

4️⃣3️⃣
```

😕😊😊😊😊😊😊😊

A hankali murmushin fuskar nasa ya bace, shima ya yi kalar serius ya ce" kina son sa? Zaki aure shi?

Agaishat ta dan kawar da kanta daga dubansa, ta ce" *eh zan aure shi,*

Ajiyar zuciya ya sauke ya wauga bangaren Mu.azam, ya ga yana zaune kasan wata bishiya yana dadana wayar hannunsa, dubansa ya dawo wajen Agaishat, ya dan jima kafin ya ce" *Zan aura maki shi*,

Agaishat bata ji wani yannayi na daban game da abinda wardugu ya fada kan aure da za.a yi mata, duda abu ne da take cike da murnar itama zata yi, aure da mutun kamar Mu.azam, itama zata yi rayuwar aure, aman zumudin da farin cikin ba wani can can ba , bata san dalili ba ko fargaba ne ya hanata jin madaukakin farin ciki kan lamarin?
Murmushi ta sakar masa ta kai dubanta wajen Acn motar da ya gama kashe mata gabobin jiki dan mugun sanyin sa,

Wardugu a hankali ya kai hannun sa wajen ky din motar zai kashe sai kuma ya bari, duban Agaishat ya yi ya ce" mu ga kitson yan matan Ayya?

Ai kuwa ya washe baki tana zabga murmushi cike da farin cikin irin yanda ya sauko daga harara nta ya mayar da ita mutun gashi har ya damu da kitsonta take dubansa tana kokarin jan hijabin baya ta bude masa kitson tana fadin"  Alhinayett ne tace kar a yi min kananuwa dan kar na wahala sosai, ka san me, kuncewa yake yi fa, Ayya ne taki yarda na daina kitson nan, kuncewa yake yi shi kadai.....ta karashe tana dan turo bakinta irin na shagwababun yaren nan,

Murmushin da a yau ya kai sau hudu da ya yi du a gabanta ya kuma sakar mata yana duban kitson har ta rufe , bai san ta ina ba bai san lokacin ba sai ji ya yi ya ce" aa, ki yi ta yin kitson ki, yana yi maki kyau,

Tsai ta yi tana dubansa, a ranta fadi take...da gaske ne ko kuwa? Me ke damunsa yake magangannu irin haka yau ne?
Bata bashi amsa ba sai lumshe idannuwanta da ta yi ta bude motar tana fadin" Allah ya tsare

ka,

Da ido ya bita bayan ta bude motar inda yana kallo Mu.azam ya karaso wajenta da sauri yana alamun tambayoyi inda ya hangi ta sakarwa Mu.azam din murmushi bata ce komai ba, daga nan ta juya ta tafi cikin saloon din.

Karasowa motar ya yi ya bude gidan gaba ya shiga ya tsare Wardugu da kallo,
Wardugu ya tayar da motar ya juya akalarta zuwa gidan Ayya

Tafiyar kurame ne suka yi har suka karasa gidan Ayya, suna tsayawa Wardugu ya daga karamar wayarsa ya danna number ya kara a kunne

Ana dauka ya ce" ka cira min tiket biyu zuwa agadez yau.

Yana gama fada ya katse kiran ya fita a motar shima ya bi bayan Mu.azam

Yana shiga dakin Ayya ya zarce direct, yana zuwa ya tarar da ita tana ninke abin shinfidar da ta cire
Kama mata ya yi suka ninke sannan ya gyara mata wanda ta shinfidar da kyau ya nemi waje ya zauna ya tsura mata ido,

Bakinta ta tabe ta karasa inda yake zaune ta ce" menene?

Murmushi ya yi mata yana dubanta ya ce" sai da wani abu d'a zai kali mahaifiyarsa kyakyawa Ayya?

Kanta ta girgiza , ta ce" da ace uwar bata san halayen dan nata ba, me ke tafe da kai malan?

Wardugu ya yi murmushi kafin yake yannayin magana mai mahinmanci, ya ce" na tambayeta idan tana son sa, amsarta ita ce" *Ina son sa, zan iya zaman aure da shi* , zan je na nema masa aurenta domin shima yana son ta,

A hankali ta zauna tana mai yi masa wani irin duba, ta ce" baku da hankali ne? A me kuka dauki kalmar aure? Sai kace wani abin wasa? To ko yar zan baku ai sai da alwalin da zan gindayawa dokoki kan yata bale ni bamu wani yi magana da ita ba, aikin banza gagawar me kuke haka ne? To naki din!

Kallonta kawai yake har ta dasa aya tana kawar da kai da yannayin haushi a fuskarta,

Murmushi ya yi , a hankali ya ce" Ayya, aure ai tayashi ake ko? Sunnar mazon Allahn salalahu alaihi wa salam din kike cewa baki bada ba? Haba Ayyana,

Yatsarta ta nuno masa ta ce" Wardugu ka kiyayeni, ni ban ce ba zan bada kwata kwata ba,

aman yannayin yanda kuke maganar ne ya fara bani tsoro, meye na gagawa bayan kun san aikin shedan ce? Sannan yarinyar nan dai amana na dauko daga gidansu, idan wani abin ya sameta ba zan yafewa kaina ba!

A hankali ya dawo kusa da Ayya ya zauna, hannunta ya kamo ya rike yana dubanta ya ce" abinda ke sakawa ana jan aure bincike, da halin rayuwa na yau da kulun, Mu.azam namu ne, mun san waye shi, sannan Allah ya hore mana abinda zamu kawo mu nemi auren ko nawa ne, Ayya, bana son mu zurfafa bincike ne, ina so ki yi min lamuni ki duba , ba zan saka kaina a maganar idan na san shirme ne, ba zan tarki tarbenta a haka da garage ba idan na san cutarwa ne wa amanarki, ina iya yiwa aminina alwali, kuma tare da shi zamu tafi namiji alwalin kansa ne, ki taya mu raya sunna da yar ki, kina da damar bibiyar rayuwarta da shi ...idan an yi maki abinda ba shi ba ki raba

Ayya kam du jikinta ya yi sanyi, tana dunansa gabanta na faduwa tana ayana lale da kwakearan dalilin da ya saka Wardugu shiga wannan maganar auren,
A hankali ta ce" menene? Me ke faruwa ne?

Wardugu ya kara sada kansa yana jin yanda zuciyarsa ke bugawa ya ce" alkhairi ne, ki taya mu.

Can daman Ayya ba mai musa maganar wardugu bace, hakan ya sa ya yi gagawar shawo kanta kan zasu je garin su Agaishat neman aurenta wa iyayenta......,
Bai bar dakin Ayya ba sai da ya tabatar da ya samu kanta ta bada amanarta da dukan yawunta, ta yi fatan alkhairi

Haka ya fito ya tisa keyar Mu.azan dake cike da mamakin lamarin sukaiwa Ayya salama suka nufi aeroport dan tafia garin agadasawa su nufi timiya gari mai gawo 🙁

........sowi kadan ne.....

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻

44

Basu dauki tsahon lokaci a jirgi ba Allah ya sauke su lafia,
Direct hotel suka nufa infa Wardugu ya yi kira kan q shirya masa mota da yan tsiraku sojoji zasu je kauyen Timiya,

Sai bayan ya yi wanka ya mike saman bed ya danna wayarsa ya danawa hajia Walyn kira yana mai lumshe ido,

Daga bangarenta ta daga tana duban agogon dake dakinta, hakimce take ta hada uban maltina tana son kwankwada tana tsoro, ance mata yana zubar da jaririn ciki wai, dan haka ta gyara zama da niyar sha sai ga kiran Wardugu,

Dagawa ta yi gabanta na faduwa kar a je ya zo yana nemanta ne,

Walyn........ya fada yana mai jan sunnan,

Idannuwanta ta lumshe ta kwontar da kanta saman hannun kujerar tana sauraron yanda ya wani ja sunnan har tsakiyar kanta,

Bakya neman mijinki wuni guda? Ki ji na ci abinci? Me ke damuna? Da wa na hadu? Karshema inda nake? Ko kin yarda da kanki har haka ne?

Walyn ta yi murmushi ta ce" na yarda da kaina ne,

Murmushin ya yi shima ya ce" baki da matsala,

Kana ina? Ta jefo tambayar

Wardugu ya daga kai yana karewa dakin kallo ya ce" ina hotel , a Garin Agadez.

Me? Hotel? Agadez? Yaushe ka je? Me ka je yi? Kuma a hotel? Kai da wata yar iskar?,

Idannuwanda ya lumshe, a hankali ya dora hannunsa na hagu saman kansa, shafawa yake yana lalabar kansa, shiru ya yi mata wanda hakan ya saka take ta kiran sunnansa da karfi tana fadin ka fada min da wata tsinaniyar kake hotel? Har ka bar gari da gari ka je garin agadez? Me ka je nema? Farin, kyan, ko gashin? Wanene bani da? Ka ban amsa Wardugu,

A hankali ya katse kiran da wayar baki daya ya furzar da wata zazafar iska ta kai dubansa wajen Mu.azam da ya yi tsai cike da takaicin matar abokin nasa yana dubansa, mamakin irin rashin hankalin Walyn yake, du yanda wardugu ya kai ga zafin rai yana raga mata, yana matukar kawar da kai a shirmenta, tunda ya zo niger bai ga inda Walyn ta taka kafarta gidan mahaifiyar mijinta dan ta gaisheta, bayan kulun sai ta fice yawo kwararo kwararo,, ga abubuwa na rashin da.a da take shukawa suna zuwa kunnuwansa , sai ta tafkawa talaka rashin mutunci ta yi ikirarin me ka isa ka yi bayan ikon a hanuna yake a matsayina na matar General Wardugu, Karfi da yaji ta saka wasu talakawan na shayin tunkarar iko koda da gaskiyarsu , suna tsoron gawo ya juye da mujiya!  Sam halayar Walyn suna bukatar gyara,

Bai iya cewa Wardugu komai ba,  domin du tsakaninsu basa irin maganar nan, sam Wardugu baya bada fuskar a yi maganar iyalinsa da kowa, idan abu ya ishe shi yakan ja dogon numfashi ya ce" Mata kennan, kwakwaluwarsu irin ta yara ce,

Wardugun ma dubansa yake har ya karasa wajen bed yana dana waya ya ce" Wardugu, yanzu kayan buzaye ne zamu nada , kawai kai tamkar diarhee kake idan ka tashi abu yi kake? Bamu wani shirya ba, bamu zo da datijo ba zamu je a bamu aure? Ni dai kar ka ja iyayen yarinyar su hana min Agaishat ba zan jure hakan ba , zan haukace maka ne!

Tsuru ya yi masa daga kwoncen yana jin wani iri da maganarsa, wani irin tashi ya yi zaune yana dubansa ya ce" kai zo zauna mu yi magana!

Mu.azam na dubansa ya karaso ya zauna yana kara kare masa kallo,

Wardugu ya ce" dan tausayi zaka aureta ko dan so domin Allah?

Mu.azam ya yatsina fuska ya ce" ina sonta mana, meye a tare da ita na tausayi? Nine ma ai abin a tausayawa,

Wardugu ya ce" kana ji, bana son ka yi auren nan da wata manufa, Mu.azam, ba zan jure gannin hawayenta ba koda kai ka jawo shi ranka zai bace, ka kara tunani !

Yana gama fada ya muke ya nufi bayi dan ji yake kamar ya yi ta ihu, sam baya jin dadin duniyar,

Yana kasan shower idannuwansa rintse, zuba take da karfin gaske ga ruwan sanyi karara da su,

Idannuwansa da sukai ja ya bude ya barsu haka ruwan na shigar masa ido , hanunsa na dama ya jimke ya daki bangon yana wani irin nishi mai nuna tsananin tashin hankalin da yake ciki,
A kadan Wardugu ya kai minti arba.in a bayin nan sai da ya saisaita kansa ya kashe gudun showern ya dubi hannunsa da ya daki bango a kala sau uku wajen ya dan tashi abinka da farar fata,

Towels ya dauka ya daure jikinsa ya fito ya nufi bed ya kwonta rigingine yana adu.a a cikin ransa

Da ido Mu.azan dake saman salaya ya bishi, kansa ya dukar ya ci gaba da jan carbinsa yana tunani barkatai a kasan zuciyarsa..........

Bayan ta gama ibadarta , zuwa ta yi ta hada complet dinta biyu ta saka a jakar computerta, ta duba kudin dake jakarta , ta kuma duba wayarta da passport dinta ta koma bakin dan madaidaicin bed din da take kwana tun zuwanta ta dauki carbinta fari kar ya fito tana mai kuma kiran docter Elisabeth

Dagawa ta yi suka gaisa, nan docter Khadija ta yi shiru,

Docter Elizabeth ta ce" kina ji, sati biyun nan shi dai kawai na iya sama maki  domin kin ga aikinki ya kasance aiki mai daraja, bangaren zuciya bama so koda wasa masu kula da lamarin mu rasa daya koda na minti daya ne, na yi iya yina a haka aka tsaya, dan haka ki hanzarta zuwa niger din ki gama komai kafin likaci ya cika, ni dai fatana ki yi ki dawo da shi mu shiga aikinsa ,

Kanta kawai take gyadawa , bata san ya zasu kwashe da masoyin nata ba, ta so ta samu lokaci isashe sai dai hakan bai samu ba , zata je da wannan din ma Allah ya sa ya amince.

*Timiya*

Tunda suka iso suka sauka wsjen baba tsoho suka fada masa abinda ke tafe da su,

Baba kam tsufa ya kara rufe shi, bawan Allah daga ringeshe yake binsu da kallonsa domin idannuwansa ramram suke ganni, murya irin na datijai ya ce" na ji dadi na yi farin ciki, aman me zai shaida min da gaskiyar maganarku? Ina mahaifiyar taku? Ina agaishat? Ina alwalin mai neman auren? menene shaidar da zata saka na aminta da ku?

Wardugu dake dubansa ya karaso a hankali kusa da shi, kai shi yanzu yana jin nauyin tsohon

wanda a da nauyin bai kai haka ba,
Yana karasawa ya kama hannun Baba tsoho cikin yaren buzanci  ya ce" bamu zo da su ba, sai waya da na dauke su suna magana, mai neman auren Agaishat abokina ne , aminina, shine wannan , ya nuna Mu.azam, ya ci gaba da fadin" Allah ne shaidar mu, shi ne alwalin kansa, idan kuwa ni zaka baiwa amanar yarka zan dauka baba domin ina jinta tamkar kanwata ta jini,

Baba tsoho yana dubansa da wani yannayi, a lamarin Agaishat du idan ya yi istihara yakan hango wani duhu kafin ya ga haske, , dubansa yake ta kaiwa kan samarin biyu, Mu.azam da bai sani ba , da kuma Wardugu da ya zubawa ido, ya rasa me ya sa bai ji wani zumudi ba,

Bashida ikon hanawa ko sakawa a lamarin agaishat duda shine silar zuwanta da mutanen nan, bai isa ya yanke hukunci ba, sannan idan ba zaka fadi alkhairi ba ka yi shiru,
Shiru ya yi ya yi masu jagora inda suka talabe shi sosai suka shiga motar aka nufi gidan Ba

Zaune suka same shi kofar gida , ya tisa sansaninsa a gaba yana zaune kan tabarmar kaba yana ta gyara sansanin yana kukulewa da zaren daure abu yana kashi kashi , shi nan sana.a ce ya fara,
Da ido ya bisu har suka firfito infa ya hade rai yana hararar baba tsoho

Daidai wannan lokacin suka karaso inda sukai masa salama,

Wani kallon ya bisu da shi, yana tatare sansaninsa,
Wani uabn tsaki ya ja ya ce" ai ko ba.a birne gawarta ba sai na siyar da tabata , ka ga bakin ciki, du ranakun nan baku zo fada min ta mutu ba sai ranar da zan fara sana.a? Ni na san *Bak'a* bata son ci gabana, wato  dan ubanta mutuwarma ba zata yi ba sai ranar da zan fara sana.a

Baki dayansu dubansa suke, wardugu da tunda gari ya waye jikinsa a mace yake bai iya ce masa komai ba sai sakin baba tsoho da ya yi wajen Mu.azam ya karasa saman tabarmar ya zauna ,

Hannunsa ya mika wajen sergent,

Da sauri ya karaso ya dire wata bakar jaka ya koma wajen da suke tsaitsaye,

Bude jakar Wardugu ya yi ya shiga fitar da daurin daurin kudi cefa yan jika goma goma yana direwa gaban Ba,

Du daurin nan million guda na cefa ne, sai da ya dire ashirin wanda zuwa lokacin Ba sai zufa yake jikinsa na rawa yana fitar da harshe tamkar kare shi ya ga kudi,

Wardugu ya ce" bata mutu ba, da ranta da lafiarta, aurenta zaka bamu, ga gudin auren nan idan kuwa sun yi kadan a karo! Domin *Darajarta* ta fi karfin a yi cinikinta! Ta fi karfin a aureta dan kudi, *Agaishat* na da daraja a idannuna!

Gaba daya dubansa suke, magana ne yake daga zuciyarsa, fuskarsa ta nuna wani yannayi mai wuyar fasara, ba zai iya jure wulakancin Ba a wannan halin ba, sannan ba zai iya biye masa su yi ba dadi ba ko dan albarkacin haihuwar Agaishat da ya yi,

Wani irin rawa jikinsa yake, auren bak'a da sadakin da ba.a taba bashi ba na sauran yayansa? Wani irin zama ya gyara yana fadin" ai kawai a matso a daura domin kuwa ya shirya, ba ruwansa da tambayar da wa za.a daura, ina take? Tana so? Ina zata zauna? Waima da ranta?

Jiki na rawa Ba ya umarci baba tsofo ya yi alwalin Agaishat inda nan da nan sarki ya karaso da jama.ar anguwa ana ta yaba sadaki (kar abin ya baku mamaki ko ya girgiza ku, na gani da idanuwa sadakin buzuwa million arba.in na kudin nigeria bama niger ba, ana amsan karamin sadaki kamar jika hamsin  aman yawanci auren garinmu kama daga agadez da kauyukan bugaje ana kashe kudi na mamaki wanda ba.a dauki hakan a matsayin laifi ko wani almubazaranci ba,),

A wannan rana , gaban duban shaidu, Mu.azam ya zama alwalin kansa inda Baba tsoho ya zama na agaishat, aka daura auren Mu.azam da Agaishat bisa sadaki mai tsoka lakadan,

Sai bayan an gama daura aure Ba ya tatare kudin nan jiki na rawa ya zube a cikin rawaninsa ya daure, bai wani tsaya ya bi ta kansu ba ya yiwa gidan tsinke sai washe baki yake yana ihun kiran sunnan Anna inda ya yi fatali da sansanin,

Da amarya ya fara cin karo sai murkashi take ymtana rauda kai domin cikin nata mai matukar bata wahala ne, tana ta fama da kanta du ta lalace,
Tsayuwa ya yi ya tofa mata yawu a fuska ya ce" ke kadarara, jeki na sake ki!
Daidai lokacin da Anna ta fito tana dubansa sai kiranta yake yana kashe murya irin za.a tuna da din nan,

Yana karasowa ya ce" ashe *Agaishat alkhairi ce?*

Da mamaki take dubansa tana jiran karin bayani, Agaishat kuma? Ita tana tunanin rabonsa da ya kama sunnanna da daraja haka tun rada mata shi da ya yi, me ke faruwa? Ina yarta ? Innalilahi wa ina ilaihi raj.une, sam bata daukan fara.ar Ba a alkhairi, hakan ya sa ta fito da sauri ta yi waje ko zata ga Agaishat din

Baba tsoho ta tarar yana yiwa Wardugu magana kansa a sade yana sauraronsa inda jikinsa ke fitar da hucin zafi gaba daya bashinda laka tamkar wanda ruwa ya daka zazabi ya rufe shi, zuciyarda kuwa ba dadi, dandannon bakinsa daci firit, sam baya jin dadin yannayin ranar nan.

Tana zuwa ta tsuguna infa suke,

Muryarta na rawa cikin yaren buzanci ta ce" me ya same ta?

Idannuwansa ya dago ya sauke kan fuskar Anna, duda turkudi ya rine mata fata ba wani kula take samu ba, aman idan kana neman ainahin kyau, tsararan kyau ka ja ka tsaya wajen Anna, Agaishat kama take da ita sai dai hasken fata da ya bambanta, yaren tubanci ya juye da shi inda ya shaida mata komai cikin nutsuwa da sada kai da girmamawa,

Kunyarsa ce ta kamata, har ta hanata yi masa wata tambaya,
Kanta ta sada bayan ta hangi Mu.azam dake tsaye ya rungume hannayensa yana kallonsu ta kawar da dubanta ta mayar wajen Wardugu,
Muryarta a nitse ta ce" *kar ka damu da bani hakuri d'ana, na saba da gannin auren yayana a wulakancema bale ita nata kun mutunta, ai dama halal malak na baiwa Ayya Agaishat, koda a can kuka daura mata aure bani da ja, fatana zaku ci gaba da riketa da amana, sannan ba sai ka kawota ba, ka barta a can kawai bara na kawo maka sako ka bata, ka fada mata Ayya uwa ce a wajenta, ta yi mata biyaya!*

Asalamu alaikum,

Rayuwa ce da aka yi nake bi maku, duda na rufe abu dayawa, na kuma gyara wani dan labarina ya yi ma.ana, aman kar ku manta rayuwar nan an yita, kuma a gidan bak'a akoy Alhinayett dake yayata uba daya, team Mu.azam da Wardugu,,.....ku biyoni sanu zamu ji meye sirin, sanu zamu yi murmushi😍😍😍😍😅😅😅😅😅

Hhhh yau kam na cika da yawa😕😕😕😕

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation
```

Yana kallonta ta shige bata jima sosai ba ta fito da yayun Agaishat, inda Mariama ta hade rai tamkar ta zunduma ihu dan bacin rai,

Sai dai suna zuwa wajen Wardugu ta ji ba zata iya yi masa wulakanci ko kashedi ba, dan haka ta sada kanta ta ce " Amana kanwata,

Kalonsu kawai yake har suka koma inda Anna ta bashi wani zani a kule wanda bai san ko menene ba,

Kamar bashi da laka haka ya mike jiki a sake inda su Mu.azam suka kama baba tsoho suka saka shi a motar suka dauki hanya,

Mu.azam na lure da yannayin Wardugu, inda gabansa ya yi ta faduwa kan lamarin, tambayoyi me cike da zuciyarsa *Me ke damun Wardugu? Me ke adabarsa haka? Bashi da lafia ne? Me ya fauke murmushinsa?*
Sai dai bashida mai bashi amsoshin tambayoyinsa domin rabinsa da jin muryar wardugu tunda suka baro kofar Baba tsofo inda baba ya baiwa Wardugu wani kuli a baiwa Agaishat shima harda carbi fari ya shaida masa cewa ya fada mata bata da gata sai na Allah.

Rike yake kamkam da sakon Baba da Anna, carbin kuwa sai ja yake yana duban hanya har suka karaso garin Agadez,

Fir Wardugu yace qi sai dai su tashi a jirgin sojoji , inda nan da nan aka taso daga garin niamey aka zo Agadez aka dauke su su biyu tal aka juya da su duka a cikin awowi hudu har jirgin ya sauke su inda dare ya fara tsalawa,

Tunda ya fito a jirgin ya daga kansa sama, garin niamey da yannayin zafi hakan ya sa ya fara jin har kamar ya cire rigar nan ya yar,

Dubansa ya kai wajen Mu.azam ya kirkiro murmushi ya ce" zan karasa gida, zamu hadu gobe in sha Allah,

Mu.azam ya amsa shi da kai yana kallonsa har ya bace masa da gani,
Wardugunsa ne ya juye haka lokaci daya? Hannayensa ya dora saman kansa ya furta"
innalilahi wa ina ilaihi raj.une, me na aikata haka? Na kutsa wajen da ba nawa bane ko me?

Da sauri ya kawar da zacen nan ya nufi wajen da ya tabata ba za.a rasa motar wardugu ba dan yawan tafiye tafiyensa yakan zo da mota ya bari a aeroport,
Yelemun kuwa ya samu ya shiga ya tayar ya nufi gidan Ayya ransa cike da tunani,

Wardugu bai zame ko.ina ba sai kofar gudan su Alhinayett

A lokacin karfe goma na dare ya kusa, anguwar ana dan kai kawo domin ba laifi suma anguwar yan gayu ce, manyan yan mata da samari sai kai kawo suke suna bada kala.

Wayarsa ya danna mata kira, tana dagawa ya ce" ina kofa,

Da sauri ta mike ta daga labulen tagarta, hango mutun ta yi duke a kofar gidansu,
Da sauri ta fito da zumbulelen hijabinta infa kanwarta dake kusa da ita ta nace ita sai ta bita,

Dubanta ta yi da kyau ta ce"  *Tghmass*, wajen yaya Wardugu ne fa?

Thgmass ta turo baki ta koma saman bed tana kunkunnin je ki, ba zan biki ba ya yi min muhunta wannan katoton da bai san yara ba!

Murmushi ta yi ta fice da sauri ta fito ta karasa da sauri tana fadin" Wardugu lafia? Me ke damunka? Me ya faru? Baka taba zuwa gidan nan a wannan lokacin ba, menene? Wani ne ba lafia?

Wardugu ya dago kansa daga duken ya kamo hannunta na dama murya a dake ya ce" Alhinayett, zuciyata ke min ciwo, ina jina tamkar zan mutu, ina jin dari sosai, na kasa tabuka komai, ina jin tamkar na rasa wani baban abu a rayuwana, ina jin iskar duniya ta yiwa kofofin hancina kadan, ji nake tamkar jikina na gasuwa da wani irin azabeben zafi da sanyi, ina jin jikina ya yi min nauyi, Alhinayett me ke damuna? Menene wannan?
Ban taba jin wannan abin ba, mutuwa zan yi!

Da sauri ta dafe kirjinta gabanta na bugawa,
A hankali ta duka inda yake ta ce" innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, Wardugu baka da lafia ne?
Jikinka zafi, ka je asibiti ne? Daga ina kake yanzu? Ayya ke ce min ka je Garin su Agaishat nemawa Mu.azam aurenta, ko ka yi gamo ne? Bara na kira Abanmu,

Kokarin tashi take ya riko hannunta ta dawo gwarab kusa da shi tana share hawayen aminінta yayanta a wani hali, a firgice ta kuma fadin" ka bari na tado abanmu ya baka magani ya yi maka

turare ko ka yi gamo da wani mugun ne Wardugu

Wardugu ya ce" bana tunanin hayaki, tashin hankali, likita, kudina, ko mulkina zasu warkar da ni, tabas zuciyata sakara ce banza ce da take da gagawar yanke hukunci, ke kin fi kowani makusancina saurarata , na zo ne dan nima yau ki saurareni kamar yanda nake sauraronki, Alhinayett, a yau da inada mace nutsatsiya da na kwontar da kaina saman cinyarta ta taya ni saisaita bugun numfashina, Alhinayett halayen Walyn na tayar min da hankali, ina sane, ina hankalce, kawar da kai ne nake dan ta kula da kanta ta gyara, Alhinayett nima mutun ne, kuma inada rauni fa, ina da zuciya, ita a kulun hirarta da ni tuhume tuhume da zargi ne, a jiya jifana ta yi da maganar wai ina tare da watatsinaniyar? Ni ba mashayi ba, ni ba mazinaci ba, aman ta ki godewa Allah sai fata take yiwa kanta? Yau da zinar nake ta isa ta hana ko ta yi wani abin? *Wani lokacin nakan dauki niyar zuwa na yin na ga sai me?* (hatara mata, walahi yawancin lokuta mu ke jawowa kanmu masifa da bakinmu da banzan tunanin mu), sai dai har yanzu ban aikatan ba,

Alhinayett sauraronsa take cike da yannayin tashin hankali, ko me ya firgita mata Wardugu ba karami bane, meye shi da yace ba zai iya masa ba? Ya fi karfinsa? Meye wannan? Gashi ya hanata kiran Aba,

Sai da ya gama ya ce" ki daina kuka, yau nima na yi jajen abinda ke raina ne.
Alhinayett ta ce" me ka fada bayan komai a dunkuke ka fada Wardugu? Me ke damunka a ranka?

Tsai ya yi yana tambayar kansa takamaiman damuwarsa har haka? Kan matar wani ko me? Da sauri ya mike ya mikar da ita ya jata har kofar gidansu ya tura ya turata ya ce" asuba alkhairi Alhi........,

A wannan rana Wardugu ya ga dare tamkar rana, ya kwana bautawa allah inda ya roke shi yafiya da nutsuwar zuciya, kuma alhamdulilah ya samu nutsuwar harma ya kwonta da safe bayan ya gama salar asuba ya samu baci

Gidan Ayya,

Kallon Mu.azam take  kafin ta ce" aa, toh shi wardugun ya aka yi baku zo tare ba? Mu.azam yaushe abokinka zai yi hankali? Ina wayar da na ce ku dauko min komai?

Sai a lokacin ya tina ya mike da sauri ya je dakinsa ya dauko wayar wajen Ayya da ta basu lale lale su dawo mata da dauka,

Yana zuwa ya kunna mata ya mika mata inda ta tsurawa komai ido tana kallo har karshe domin daya daga cikin yaran wardugu ya dauko komai,
Baya ta maido kadan tana duban yannayin wardugu,
Kanta ta dago da niyar yin magana ta hango Agaishat ta farka tana saukowa a hankali, kanta

na duban kasa, hankalinta a yannayin tashe, kayan bacinta ne jikinta dogon wando sakake da riga budadiya, kitson kanta cikin hula baka, a hankali ta sauko ta dago idannuwanta ta sauke kan Ayya,

Kuka ta fashe da shi ta karasa da gudu jikin Ayya tana ta shesheka

Hankali tashe Ayya ke bubuga bayanta ta ce" me ke damun ki? Lafia? Y'ata menene?

Agaishat ta kankame jikin Ayya ta ce" Ayya, mugun mafarki na yi, wai wuta na cin gidanmu, Aya gobara a gidanmu, an yi an yi  da Anna ta fito ta kiya tana jira sai Ba ya bata umarni domin bata fita sai da umarninsa , shi kuwa ya tsaya yana ta dariya ya ki bata umarnin!

Ayya tana shafa kanta ta ce" mafarki ne fa Agaishana, mafarki ne, ki kwontar da hankalinki, kin ga jiya su Wardugu sun je din , an gama komai kuma harma Mu.azam yace da sakonki da Annarki ta bayar a kawo maki,

Gabanta ne ya yanke ya fadi, an gama komai? Kennan yanzu ita ta zama matar aure? Ta zama matar wani? Ta zama sa yi hani bari?
A hankali ta dago da dubanta ta kai wajen Mu.azam,
Ido ta tsura masa kamar yanda ya tsura mata,
Murmushi ya sakar mata yana dubanta kafin yake karasowa dan kusa da su kadan ya ce" Anna lafiarta kalau, hakama su Mariama, du sun fito mun gaisa, baba tsofo yace a gaishe ki, du suna nan kalau,

Maimakun ta bashi amsa sai ta mayar da kanta jikin Ayya ta lafe tamkar mage, sannan ta lumshe idannuwanta gamgam

Da ido Ayya ta yi masa magana tana murmushi tana shafa kan Agaishat inda ya mike jiki ba karfi ya nufi tsakar gida.

Karfe shida na yama jirgi ya ajiye su, inda fito bakin titi ta tsaya tana kallon yanda motoci ke ficewa,
Tsarin garin ya yi mata ba dati ga kyau.

Taxi ta tsayar, don ta san ba wanda ya kai dan taxi sannin gari, ta san garin akoy tsaro, sannan ta san da wuya a samu wanda bai sani ba,

Tana tsayar da shi ta ce" *Gidan Elhaj Wardugu Marahut nake so ka kai ni*

Juyowa ya yi yana dubanta ya ce" gidan su ko gidansa?

Tsai ta yi ta tuna yace mata idan ya zo wajen Ayya yake sauka, fan haka ta ce " *gidan sa* domin tana son fara magana da shi kafin ta je ga Mu.azam!

To fa fans, shin bata san walyn ba? Ya kuke hangen wannan cakwakiyar?

Ga kari😕

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

4️⃣6️⃣

Tafia mai nisa suka yi kafin ya dangana da tankamemen kofar gidan wardugu,
Kamar kowani gidan baban iko , kofar gidansa sojoji ne ke gadi wa.inda suka canji wasu,
Can gefe katuwar motarsu ce ta iko, sunna dan hira tsakanninsu lokaci zuwa lokaci kuma suna kule da aikinsu yanda ya kamata,

Tana sauka ta biya mai taxi ya juya inda ta nufi wajen sojojin .
```

Kamar yanda suke kallonta haka itama ke kallon su, har ta karasa dan kusa da su
Daya daga cikinsu ne ya yi mata tambayar wa take nema a nan?

Amsa ta bashi gamshashiya ta kuma nuna masa carte dinta shaidar ko ita wacece din,

Waya ya dauka ya yi kiran layin ogan,
Ya jima yana ringin kafin ya daga,
Yana dagawa ya kora masa bayani,

Wardugu dake bacin gajiya ya bada umarnin a sayota a gwada mata part din Walyn su hadu a can.

Mikewa ya yi ya shiga wanka, bai wani jima ba ya fito da alwalarsa ya tayar da sallah ya yi ramuea domin wani nanauyan baci ne mai wahala sosai ya yi,

Yana gamawa ya bi ta dayar kofar ya fice dan nufan bangaren Walyn wace ya gama tunanin kar a je tana can tana zuba hauka!

Maradin Walyn baya kunya,
Yana tura kofarta ya tarar da bakuwar tsaye rike da jaka tana kallon kasa, jikinta da bakar abaya doguwa ta yane kanta da mayafin Abayar,
Walyn kuwa na zaune saman kujera ta dora kafa daya kan daya tana kadawa ta turo daurin dan kwalinta gaba tana kaskaskas da cingan

Salama ya yi mata yana duban Walyn, kafin yake fadin bismillah zauna mana ga kujera,
A hankali ta karasa wajen da ya nuna mata ta zauna tana mai duban Walyn,

Gaisawa suka yi cikin mutunta junna, kafin ya yi shiru yana sauraronta

Gyaran murya ta yi ta ce" Wardugu sunana Nana khadija Canel Noor, muna tare da Mu.azam ne a can wajen aikinsa inda yake aiki can muka hadu, akoy shakuwa tsakanina da shi mai girman gaske , na biyo.....
Bata kai ga karasa maganar ba walyn ta bushe da dariya tana dubanta,
Hannunta ta nuno mata ta ce" halan saurayinki ne?

Da mamaki take duban Walyn, ashe tana jin french? Da ta zo ba yanda bata yi ba Walyn ta fahimci maganarta aman ta juye yaren tubanci ta yi ta dura mata zagi da hannayenta kuwa ta nuna bata san yarenta ba, sannan ta daure fuska ta tsare gida ta jefa cingan a bakinta tana taunawa tana kada kafa tana chating.

Walyn bata yi kasa da gwuiwa ba ta ce" wace irin shakuwa ce tsakanin mace da namiji? Ke jiya fa aka daura masa aure, jiya suka je suka dauro aurensa,

Walyn! Wardugu ya fada da kakausar murya wace ta saka ta yi shiru tana binsa da kallo sai kikifta ido take uwa ta yi karya,

Kansa ya juya ya ce" ki je dakinki,

Baki ta turo gaba ta mike ta yi wata girgiza ta juya ta nufi dakinta tana rauda jiki ita matar general,

Tunda ta fadi maganar nan, jikin Khadija ya mutu, ta sada kanta kasa, hankalinta ya gama tashi, innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, shine abinda take ta fada a ranta, kuka take so ta yi aman ya ki zuwa,

Wardugu da ya dago ya yi mata kallo daya ya kawar da kansa ya ce" desoler (Sorry),

Wani abin ta hadiye da kyar kafin ta ce" ko ka san da bashi da lafia?

Wardugu ya rintse idannuwansa, ya gyada mata kai,

Ta tatara dukan kuzarinta ta ce" Wardugu, ana iya yi masa aiki, tabas aikin na da mugun hatsari aman idan Allah ya nufa sai ka ga an dace, ana tashi sosai, wa.inda nasu ya yi mugun tsanani ma sun tashi , ka taimakeni ka saka baki ya biyoni mu je a yi masa aikin nan, bana tunanin idan ya mace a haka zan iya wata rayuwa, Wardugu ka taimake ni,

Menene tsakaninki da shi mai girma haka? Excuse moi (excuse me), kina magana ne tamkar rayuwarsa na tafe da taki, na san ki, ya min maganarki a matsayin kawa, kawance ne ko da wata maganar? Wardugu ya fada , bai yi niyar yi mata wani kwakwaf ba, aman yannayinta ya tsorata shi, kar dai Mu.azan nada wata ya zo ya auri Agaishat?

Khadija ta sada kanta kasa ta ce" ni ke binsa yana guje min, ya fada mij zai yi aure, kennan dai auren ya yi? Meye laifina dan Allah ya dora min soyayarsa? Bani da ja da aurensa, bani da damuwa da matarsa, ni dai burina a yi masa aikin nan, idan da rabo ya samu tsayin rai,

Mikewa Wardugu ya yi, ya dubu wajen Tv din Walyn, kys din motarta ya dauka ya yiwa Khadija alama da su je,

Mikewa ta yi itama gabanta na faduwa, bayansa ta bi tana tunanin ya zasu kwashe da Mu.azam? Ya zata tsinci kanta idan ta gane shi da wata? Adu.a kawai take a kasan zuciyarta, sannan miskilancin Wardugu ya sakata shiga tatayinta sosai,

Gudu yake na balaki, jalabiyar nan ta jikinsa baka wace ta mahaukacin haska fatar jikinsa itace a jikin nasa bai canza ba, sai gajeran wandondake kasa, daga su ko yannayin gashinsa bai caje ba, fuskarsa fayau da ita ta bada wani ni.imtacen kyau du kuwa da irin yanda ya hade ta.

Da garajen dai ya danna cikin gidan Ayya inda ya fito da tarin balaki ya nufi wajen mai gadi domin ya bar kofar a bude, (za.a dai sauke masa fushi ne)

Nemansa yake bai ganshi ba, hakan ya sa ya dawo wajen motar inda take tsaye tana duban ikon Allah,

Tun shigowarsu Mu.azam yake kallonsu, domin yana kasan inuwar tsakar gidan Ayya yana ta tunanin rashin gannin Wardugu da yanda Agaishat ta kaurace masa kwata kwata bai ga fara.arta ba, danma tun dazu Alhinayett ta zo wajenta. Baii ga fuskar Khadija ba domin ta dayan bangaren ta fito kuma ta ba inda yake baya sai lokacin da Wardugu ya karaso ya yi mata nuni da bayanta ba tare da yace da ita ci kanki ba

Juyawa ta yi, inda likaci daya Mu.azam ya mike tsaye yana zaro ido,
Da sauri ta nufi wajensa inda shima ya tako suka hade tsakiya suna yiwa juna wani kallo mai wuyar fasara,

Hannunsa ya kai fuskarta ya shiga share mata hawayen da suka fara zaryo mata a fuskarta suna masu yiwa juna murmushi.....

Alhinayett ce ta fara fitowa, inda hankalinta ke kan Agaishat dake biye da ita suna hira harda dariya domin Agaishat ce ke fadin" ashe itama zata ga ranar da za.a ce ta yi saurayi wai harda aure? Ashe yan birni ba haka suke ba? A kauye bata taba tunanin ko mahaukacin kauye zai kulata ba,

Dif ta yi da maganar inda idannuwanta suka sauka kan Mu.azam da wata kyakyawar mata fara kar , jikinsu tamkar zai hade, sannan sai shafa fuskarta yake kamar mai rarashinta,,
Sanye Agaishat take da atampa an yi mata dinkin riga da sket, dinkin zamani ne ya mugun karbar jikinta ga dauri da Ayya da kanta ta caka mata mai shegen kyau,
Fuskarta ba wata kwaliya sai dan jan baki mai ruwan atampar sai annurin amarci domin amarya ko ta daji ce tana fita daban,
Sosai take fitar da kamshi mai nutsar da zuciya, annuri na fita a fuskarta, idan ta yi murmushi kuwa kaima zaka tsinci kanka da yi ne dan irin murmushinsu ke saka murmushi,
Idannuwanta dara dara da su sun sha kwali, dogon hancinta ya sauka kusa da dan madaidaicin bakinta mai lebe masu santsi da kyali domin kida yaushe tana amfani da rob san gyaran bushewar lebe da saka su laushi da kyali,

A hankali ya dora hannayensa duka biyu saman motar ya dora kansa ya tsura mata ido,
Wani abin ya fargar da shi inda ya yi saurin watsakewa ya juya da sauri ya nufi wajen garden,

Sai a lokacin Mu.azam ya ankara da su Agaishat, shi din ma gabansa ne ya fadi, inda har ya ji kafarsa na dan rawa, aman ya dake ya kama hannun Khadija suka suka nufi wajen su Agaishat........

👏🏻

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*🐫🐫🐫

Na *SAJIDA*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

4️⃣7️⃣

Yana karasawa ya dan fara kame kame yana dan susar kai, da kyar ya iya sakin murmushi yana duban Agaishat ya ce" wife, ga Khadija, khadija ga matata.

Kanta ta juyo daga duban su Agaishat ta sauke kwayar idannuwanta cikin nasa, wanda ya ki bari su hada idon ya kawar da nasa wajen Agasihat wace itama su kawai take kallo inda ta ji wani irin faduwar gaba,

Khadija ta yi iya yinta ta karasa kusa da Agaishat da Alhinayett ta mika masu hannu tana sakin murmushin yake ta ce" asalamu alaikum,

Hannu Alhinayett ta fara bata tana mai amsa salamarta suka gaisa, hakama Agaishat wace
```

Khadija ta ji hannunta wani irin laushi (toh ba dole ba, tunda ta zo Ayya ke tsaye kan du wata gaba ta jikinta , jiki kuwa na samun gyara nan da nan yake hadewa ya yi cas), ta yi mamakin irin kaushin hannunta duda ta tarar da ita a gidan su Wardugu,
Daga nan dugunzuma suka yi cikin falon Ayya inda Agaishat ta haye dan kanta ke sara mata, ita ta kasa gane wacece kuma tare da mijin da aka aura mata jiya? Sai a lokacin ta mike zaune daga saman bed dinta ta nufi wajen window ta daga labule dan gannin ina ya je? Ina ya tafi ne? Ta ganshi harma sun yi ido hudu inda ta yi masa murmushi shi kuwa ya hade fuska, daga nan bata san ina ya nufa ba, aman motarsa na nan wajen hakan na nufin yana gidan.

Tunda ya je ya ja ya tsaya waje guda yana duban yanda lambun yake da irin sanyayan sanyin dake tashi a ciki ya afka tunani, tambaya daya ya yiwa kansa wace ta saka kansa sarawa, idannuwansa ya lumshe ya dubi hannunsa a ransa ya shiga yiwa kansa fada kamar haka" ba kanka farau ba, da yawa sun rasa sun ci gaba da rayuwa, dole ya girgizaka domin kaima mutun ne mai rai da lafia mai zuciya mai motsi, aman kuna yarda da wannan jarabawa zai kara daukaka darajarka a wajen ubangijinka, kai ba kowa bane face dan adam da Allah subahanahu wata ala kan jarabta a rayuwar yau da kulun, dan ka shiga hali na jarabawar rayuwa ka aminta shine cika namiji,

Murmushi mai ciwo ya yi a fili ya ce" Wardugu, ? Kana bata time dinka bayan wannan baya cikin tsarin rayuwarka! ........
Zai ci gaba da yiwa kansa magana yar wayar da baima yi tunanin ya dauko ba ta dauki tsuwa a hankali tana kidan nan na sojoji tamkar ana harba bindiga,

Shiru ya yi da maganar ya tamke fuska bai dauki wayar ba , bai kuma ci gaba da magangannun da yake ba,
Ya kai sau biyar ana kiran wayar dan haka ya saka hannunsa ya cirota ya duba sunnan, WALYN,

Dagawa ya yi ya kara a kunnensa yana sauraro,

Asalamu alaikum General, docter Sagir Sulaiman ne, an kawo matarka emergency minti sha biyar da suka shige ne, yanzu da muka dan daidaita lamarin ne ta bamu wayar dan mu yi kiranka,

A dake ya ce" wani asibiti?

Likitan ya ce" dan clinique dan gawo ne domin a inda ta samu hatsarin nan ne mafi kusanci da ita.

Katse kiran ya yi bai bashi amsa ba ya saka hannunsa cikin gashin kansa ya yamutsa ,
Juyawa ya yi da tafiyarsa mai kama da yana sauri aman a gadarance ya nufi cikin gidansu wajen Ayya,

Tunda ya nufo wajen ta tsura masa ido, kallonsa take tana murmushin da bata san na meye ba, Dan yatsanta ta nuna inda yake zuwa ta ce" ban taba gannin mutun mai rihima irin dan Ayya ba, ya san kan rigima, ko dan Allah ya bashi dama ne? Wannan mutumen idan kokowa ta hadaka da shi ba zan so ganninka a karshe ba,

Dan bakinta ta murguda ta ce" ke Agaishat kin manta karfi daga zuciya ne?
Juyawa ta yi wajen madubi tana kallon kanta, a fili ta ce" nima mai karfi ce!

Yana shiga falon ya tarar da su Mu.azam da Ayya da Khadija dake zaune zuru Ayya fuskarta a dan hade ba kamar kowani lokaci ba,

Tana ganninsa ta bala masa harara ta kauda kanta,
Murmushi ya yi a fili ya zauna yana duban Alhinayett dake son karantar yanayinsa, ya maida dubansa wajen Mu.azam,
Murmushi ya sakar masa sannan da ido ya yi masa maganar da shi kawai ya gane,

Mikewa ya yi ya bi bayan Ayya da ta mike ta yi sama dan ya san tana son ganinsa ne aman ba zata fada ba a gaban mutane

Yana shiga ta mike da zafi zafi tamkar zata wanke shi da mari ta ja tunga gabansa ta ce" kai! , kai! Ka fita a idona na rufe! Kai Wardugu na fika danyen kai, yanzu dan raini ka zo na baka damar zuwa daurowa yarinya aure ka dawo dan bahagumen tunani ba zaka zo ka fada min ya aka yi ba? Sannan yau ya shigo min da zankadediyar budurwa ya fada min aminiyarsa ce? Ohk tare kuke amintar kai da shi da yan matan ko? Ba zai yiwu ba, ba zan bashi y'ata a wannan halin ya je min da ita wata uwa duniyar ba, ba zan lamunci ya dauki y'ar amana ya tafi nesa da ita ba, wannan yarinyar tamkar marainiya take nesa da iyayenta, nice uwarta nice ubanta, kuma ina son abina, Wardugu ba zan lamunci shashancin nan ba!

A hankali ya ja hannunta har bakin gado ya zaunar da ita, idannuwansa sun kade sun masa ja, ya kamo hannun nata ya ce" *Ayya, a cikin gidan duniya, lungu lungu, ba inda kafata ba zata shigaba dan gannin halin da take ciki, ba zan lamunci ko kuda ya yi mata ilah ba!*

Da mamaki take dubansa, yannayin yanda ya yi maganar har wata jijiya a gaban goshinsa take motsawa irin magana ne yake da zuciyarsa da gangar jikinsa,

Mikewa ya yi ya yi taku biyu zuwa uku ya dawo yana mai yamutsa gashin kansa ya zauna ya ce" Mu.azam bashi da lafia, wannan aminiyarsa ce mafi kusanci da shi, ta zo min da maganar tana so a yi masa aiki wanda idan Allah ya taimake mu aka dace zai tashi, Ayya na roke ki, ki saki ranki, ki yiwa dukan lamarinnan kyakyawan gani, ki bashi matarsa su tafi,

Galala take dubansa har ya karasa maganar ya mike ya nufi fita,
Kuma juyowa ya yi ya ce" Walyn ce ta ba lafia, zan je clinik

Damuwarta ta nuna da yi masa adu.a, taso ma binsa aman ya nuna ta yi zamanta dan yayi imanin in dai Walyn na cikin hayacinta sai ta batawa mahaifiyarsa duda tana boyewa shi ai ba makaho bane,

Yana fitowa ya tsurawa kofar Agaishat ido, wani abin na tunzura shi ya je wani na hana shi,
A hankali ya taka ya je kofar dakin ya tsaya,
Hannunsa ya dora saman abin budewar ya lumshe ido,
Da sauri ya saki ya juya sai dai me  Alhinayett ce tsaye, bai san lokacin da ta hayo ba, bai san ko tun fitowarsa take wajen ba, idannuwansa sun rufe,
Hade fuska ya yi tam irin karma ta ga fuska ta kawo masa raini,
Rabata ya yi ya fice ya sauka kasa inda ta bi shi da wani irin kallo,

Hannayenta biyu ta dora saman kanta, ta shiga girgiza kai da yaren buzanci ta ce" na shiga uku Nauyin baki ya saka aminina tafka barna, Wardugu me ka aikata haka?

Tura kofar Agaishat ta yi ta shiga da salama,

Agaishat dake kwonce saman bed ta mirgino tana amsawa da murmushi shinfide a fuskarta tana duban Alhinayett,

A nitse Alhinayett ta karasa kusa da Agaishat inda ta mike zaune tana duban yannayinta,

Hannayenta Alhinayett ta kamo tana dubanta cikin yaren buzanci ta ce" Tarhanine (masoyiya), ina son mu yi magana da ke.

Agaishat ta bata hankalinta sosai ,
Alhinayett ta ce" ban taba aure ba, aman a islamiya an fada mana irin girma da darajar aure da kuma girman ikon miji a kan mata,
Sunna ce ta ma.aiki, daga lokacin da aka daura aurenki maganar mijinku ta fi iko kanki fiye da ta iyayenki, kin ga kuwa banban nauyi ne da bawa zai kasa rintsawa idan ya tuna,
A yanzu ba maganar kina sonsa ko bakya sonsa, ba maganar ke wata ce ko wani ya tsaya maki, in dai mace na tsoron haduwarta da ubangiji to ya zama dole ta gane itace karama mijinta ne baba, ta yi masa biyaya.
Agaishat, ki yiwa Mu.azam biyaya, kin samu tarbiya domin zaman da nayi da ke na dan lokaci jifa jifa ban ga rawar kai , tsayaya a tare da ke ba, zan so mijin aurenki ya yabe ki, ki ci gaba da girmama Ayya domin uwace a gare ki, ki nuna mata hankalinki ya kwonta da auren ko natama zai kwonta, kar ki tsananta bincike Agaishat, ke dai ki yi ta rokon Allah ya sa hakan shi ne mafi alkhairi,

Tunda ta fara Agaishat kallonta take, ita sai yanzuma tsoro ya shigeta, aure, aure, bautar Allah, sunnar ma.aiki, da tana tunanin ta yi nisa da iyayenta a hankali hankalinta ya kwonta da su Ayay harma ta samu gurbi mai girma ta basu a zuciyarta, aman yanzu gashi an mata aure?
Kuma bama a kasar zasu zauna da mijin ba domin Mu.azam na shirye shiryen su daga da

Agaishat ne?
Hannayen Alhinayett ta damke tana dubanta ta ce" *ina jin tsoro, bana son barin su*,

A hankali ta dora kanta saman cinyar Alhinayett inda ita kuwa take dan bubuga bayanta alamar rarashi

Yana zuwa kai tsaye office din likitan ya je, wanda ya tataba za.a mika takardun matarsa can ne dan hatsari ne

Gaisawa suka yi inda likitan ya nuna masa wajen zama,

Labarin lokaci da yannayin da aka kawota ya bashi, inda ya ce" tanada shigar yaron ciki ne kuma ta karya da cokacola mai karfi bata ci komai bayan hakan ba,
Shi ya hadasa mata ciwon ciki mai tsanani ko nace mara hakan ya saka gudan jinin ya shiga barazanar zubewa, tana cikin wannan halin ta samu hatsarin domin ciwon ya girmami nutsuwarta,

A hankali ya dago da idannuwansa ya sauke kan doctern, idannuwansa ya lumshe yana jin wani irin dadi na ratsa shi, ciki, a daidai lokacin da ya rasa wani abin ya samu wani,

Murya a kausashe ya ce" *Cikina, ba abinda ya samu cikina?*

To fa😔😔😔, na zama raguwa, tun safe nake tsakurar rubutun nan😔😔😔😔😔😢😢😢😢😢😢😢

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

Da sauri docter ya bai Wardugu amsa gamsashiya tare da nuna masa echo din cikin, cewar bai yi kwari ba ya so zubewa aman Allah ya tsayar da shi, dan haka a kiyaye du wani abinda zai zo mata da garaje har ya zauna ya yi kwari,

Kansa kawai yake gyadawa kafin ya mike ya nufi number dakin da aka fada masa take

Yana zuwa ya kwonkwasa , bai tsaya an bashi izinin shiga ba ya tura ya shiga,

Walyn ce zaune tana rusawa mahaifiyarta kuka inda uwar ke fadan da bai fahinci na meye ba, Gannin mai shigowar ya saka gaba dayansu sukai kit suka daina maganar inda Wardugu ya nuna tamkar bai ga abinda suke ba,

A hankali ya karasa wajen kujerar dake dan nesa da su inda mahaifiyar Walyn ta saki hannunta ta mike daga kujerar dake kusa da  walyn din tana mai son ta bar dakin

A nitse ya gaisar da ita inda ta amsa kafin take barin dakin tana jin wani irin haushin Walyn, ta sha jus din nan ne dan cikin ya zube, da ba.a yi gagawar kawota asibiti ba da tabas sai mai afkuwa ta afku, bata san wa zata fadawa dan ya tsoratar da Walyn ba domin ba wanda take tsoro!

 Bayan fitar mahaifiyarta a hankali ta kwonta saman bed din tana kallon sama,

Wardugu dake yi mata kallon kasa kasa ha jima a haka kafin yake tasowa ya dawo kujerar dake kusa da ita ya ja ya zauna,
Rigar jikinta ta atampa wace akai mata dinkin zamani ya dora hannunsa wajen mararta ya samu ya dage rigar a hankali,
Lalausan hannunsa ya dora saman mararta, a hankali ya shafa ya jara shafawa, ba zai gane komai ba shi dai yanda cikinta yake ne bai wani canza ba, tana da dan teba kadan, ko dan an ce cikin bai girma bane?

Kalonsa ya maida wajen fuskarta a hankali tamkar bai so magana ba ya ce" ina son cikina Walyn, kema kina so?

Wani katutun abu ya tsaya mata a makogwaro, ina ita fa ba zata iya wannan lamarin ba, ka haifi dan uban ya dawo sonsa fiye da kai, ba zata iya barin wannan cikin ba duda kuwa azabar da ta sha,

Gannin tana ta yamutsa fuska ne ya saka shi kara kusanta kansa da ita ya ce"wani waje na maki ciwo ne?

Da haushi haushi ta dube shi ta ce" tun cikin bai zama gudan jini ba, ba.a kai ga halitarsa ba, har ka fara manta abinda ya dace ka fara damuwa da shi? Har ka fara manta nice damuwarka

ta farko domin nice zahiri?

A hankali ya janye hannunsa daga wuyanta yana dubanta da wani irin yannayi, tafia ya yi ya dawo basu wani hadu ba, tun maganar da ta yaba masa a agadez basu wani hadu ba, shima ya shareta ya shiga harkokin gabansa, yanzu sun hadun zata wani saka shi gaba da hayaniya kamar yaronta,  du irin murnar karuwar da ya samu da dokin da ya afka sai ya ji lokaci guda ya dishe, dubanta ya yi irin na tsai din nan,

Hannunsa ya saka a aljihun doguwar jalabiyarsa ya ciro cart dinsa ta bank,
Ajiye mata ya yi nan ya juya ba tare da yace da ita ufan ba,

Tana kallonsa har ya fita a dakin,
Ba.a jima ba mahaifiyarta ta shigo dakin tana dubanta ,

Wani uban tsaki ta ja ta ce" kin masa haukan ne?

Walyn ta dafe kanta ta dauki cart din ta mikawa uwar ta ce" Ma, ga abinda kike nema! Plz kama ki barni na ja numfashi mai dadi!
Yannayin maganar walyn, da irin furucinta bai taba zuciyar mahaifiyarta ba, hasalima dokin karbar tikitin bankin Wardugu ya sakata sakin murmushi ta karba ta fita da hanzari bayan ta shaidawa yar zata turo a tayata komawa gida ta karbi code number dinsa.

Bayan ya karaso gida dakinsa ya shige,
Yana shiga ya cire rigar da ya kusan wuni da ita ya kaita wajen injin wankinsa ya ajiye ba tare da ya wanke ba dan hankalinsa ba nan yake ba
Dawowa ya yi ya shige bayi ya yi wanka ya dauro alwallah,

Sallah ya yi a nitse, bayan ya salamce ya mika hannu ya dauko wayarsa android ya kuna,
Yana kunnawa data na hawa domin baya kasheta kwata kwata,
Ba.a jima ba messages suka shiga shigowa na mutane daban daban, tun daga abokan aiki, manyan mutanen da yake hulda da su, da yawa kan harkar mota ne da yake siyarwa, wasun kan kamen da ya yi ne watani da suka shude, wasun baima bude ba dan bakin number ne,
Yana bin messages din yana karantawa sai dai baya bada amsa,
Nan ya fita ya shiga Facebook, roger banasaran da suke harkar motoci da shi ya masa sababin zubi, zubi na sababin motaci na manyan mutane,
Yana dubawa ya ga number yarinyarnan dai sai kara turo masa gayata take , a whatsupp ma sai message take turo masa tana karawa,

Fita ya yo ya koma whatsupp ya shiga message dinta,
Duka kalamaine na rarashi, da magiyar ya kulata, da yannayin kaskantar da kai, wai ita BASMA yar gidan minister,

Hotunanta da take ta turo masa ya bude,

A hankali ya tsurawa hotunan ido yana kallo,
Kansa ya girgiza ya fita ba tare da ya bata amsa ba,
Mesage ta turo kamar haka" du bakin da zai furta kalmar so ba makiyi bane, sannan adini bai haramta mace ta nuna tana son namiji ba, kuma ni ban roki wayar gari da kaunarka ba, kar ka ja zuciyata a kasa dan Allah ya baka dama,

Mesage din yake bi yana karawa,  bai iya bata wata doguwar amsa ba sai mikewa ya yi da wayar a hannunsa ya haye saman bed dinsa ya kwonta ya jawo pilow ya dora kansa, a ransa ya ayyana" haka fa suke idan suna so, da dama ta same su sai su fara gwada halaya na rashin tarbiya da hadama,

Yana kokarin neman baci wayarsa ta shiga ruri,
Kansa ya shafa yana jan tsaki,
Kin kula wayar ya yi sai da ya ga mai kiran ya fishi naci ya dauko wayar ya daga yana fadin" ai aikin nan sai kai daman!

Mu.azam ya yi murmushi, ya ce" me tace da kai Wardugu,

Wardugu ya yatsina fuska ya ce" wace fa?

Mu.azam dake zaune yana hangen shige da ficen Agaishat kicin tana girki ya ce" wardugu mana, bakuwata man

Wardugu ya bude idannuwansa ya ce" meye tsakaninka da ita bayan amintaka?

Mu.azam ya yi tsam gabansa na dan faduwa, a hankali yake goge zufar da yake ya ce" amintaka ce mafi kusanci,

Budurwarka ce? Wardugu ya kaste shi,

Mu.azam ya sauke ajiyar zuciya, ya kasa magana hakan ya tabatarwa da Wardugu zarginsa Ransa ne ya ji ya mugun baci, hannunsa ya jimke ya kaiwa garu duka ya kausasa murya ya ce" dan me ka shigi yarinyar mutane bayan ka san amana ce?

Mu.azam ya mike zumbur dan yannayin muryar Wardugu ya shaida masa ransa ya baci,
A nitse ya ce" ka kwontar da hankalinka Wardugu, bamu yi soyaya da ita ba, itace ke so na, bamu tana soyaya da ita ba, ban zowa Agaishat dan na cuceta ba, kuma ba zan taba gigin cutar nata ba,

Wardugu dake tsaye shima ya dafe gaban goshinsa, baya jin zai baiwa Mu.azam amsa a wannan maganar,

Mu.azam ya ce" Wardugu, dan *ina sonta* na aureta,

Wardugu ya matse karfen jikin bed dinsa yana rintse ido, kansa yake ji na mugun sara masa, hakama juwa na dibansa,

Mu.azam ya kara sasauta murya ya ce" ina son mu tafi , na san ka san komai game da abinda yarinyar nan ta zo da shi, Wardugu koda ban auri Khadija ba tana da darajar da ba zan misalta maka ba a raina, tamkar yar uwata na fauketa kamar yanda na dauke ka, zan bita a min aikin nan, idan Allah ya yi na rayu zan tashi na rayu da *Matata*, idan ban rayu ba na san zaka kula da *Iyalina*, gobe ake bani passport din Agaishat, Khadija bata zo ba sai da ta shirya domin komawata da shigana block duka ta irga min kwana tara ya yi saura, Wardugu ka......
Wardugu ya katse shi da wani irin yannayi ya ce" *Zaka rayu in sha Allah*! Ku ci gaba da shirin tafia, in sha Allah ina nan za.a shiga aikinka, zaka rayu Mu.azam......

😔

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

49

Bai jira amsar Mu.azam ba, Wardugu  ya silale yana dafe kansa, a fili ya furta" *ban shirya ba,

ba zan iya dauka ba, bani da karfin kokowa da hakan, sannan haramun ne a gareni, ya Allah baka dorawa rai abinda ba zata iya dauka ba, Allah ka cire min wannan gingirmin mikin , domin ni dai ban saba ba*!!!!!

Timiya

Duniya sabuwa ce ta budewa Ba, wannan karon da sabon salo domin kuwa tafe yake da isa da takama da nuna kansa a matsayin uban *BAk'a*,

Anna dubansa kawai take idan yana abubuwansa, bata taba buda bakinta tace da shi uffan ba, a cikin kudin ya basu million guda wada Mariama ta karbe , ya canza masu katifa ya kawo masu buhun dawa guda ya yar masu sannan ya shiga fakar takun Anna yana so ta koma turaka

Kamar yau, zaune suke su hudu domin Gaishata ta zo masu , labari suke duka yawan zancen a je a dawo ne a tile kan maganar Agaishat,

Anna ta sauke ajiyar zuciya tana dubansu ta ce" mahakurci mawadaci, du wanda ya ce zai yi hakuri Allah ba zai bashi kunya ba, sannu sannu kuma bata hana zuwa, sai dai a jima ba.a je ba,

Gaishata ta yi murmushin itama da tsohon cikinta haihuwa ko yau ko gobe ta ce" ni abinda ke bani mamaki Ba, wai shine har yake yi mana kallon mutunci?

Mariama ta tabe bakinta ta ce" na dan lokaci ne, idan kudin hannunsa ya kare zai dawo kamar da,

Anna ta ce" ki daina mumunan zato Mariama

Mariama ta yi mata wani malalacin murmushi dan kar ta yi fada,

Suna tsaka da zancen sai gashi ya shigo yana jan arzizimin wando bakinnan kuwa jajajir sansani su ta bata shi,

Bai yiwa yaren magana ba sai Anna ya kalla ya yi kiranta ya shige dakin

Da kallo suke binta dan gannin zuwa zata yi kuwa?
Gani sukai ta mike ta nufi dakin ba tare da ta yiwa kowa cikinsu magana ba

Tana shiga ya damko hannunta yana washe baki ya ce" Ke bakya marmarina? Kin jima baki neme ni ba, kin ga baki fice haihuwa ba, ki zo mu kara samun wata Bak'ar, ina son samun yarinya a gidannan,

Sakai kawai ta yi tana dubansa, kanta ta girgiza ta janye hannunta ta juya da niyar barin masa dakin

Ba da yannayin fushi ya ce" in kika yarda kika fita a dakin nan , sai na nuna maki na fi yan yamai *Niamey* iya rashin kunya!

Wani irin birki ta ja ta juyo da madaukakin tashin hankali da kuma tsoron da ya bayana karara a fuskarta,

Bakinta ta buda zatai magana sai dai ina jini ne ta shiga bin hancinta, juwa ta kwasheta ta zube nan tana fida wani irin numfashi

Karar faduwarta ya saka Mariama mikewa domin da marfin kwano a hannunta marfin ne ya kai kasa ya bada kara wanda sam Mariama bata yarda da shi ba dan haka da hanzari ta fada dakin tana mai kiran sunnan Anna,

Tana shiga daidai Ba ya kai kasa zai kamata jikinsa sai rawa yake,
Da mugun gudu da taratsi ta ce" kar ka tabata, kar ka taba mini uwata!

Bai sanma tana yi ba, shima fama yake ya ga ta mike, yau dai haukansa ya kaishi taka dokar da aka dodora masa na ya kiyaye kama mata sunnan garin haihuwarta, ya kiyaye du abinda zai alakantata da garin makarin duhun kan Anna shine Ba ya kusantata da asalinta, ya kama sunnan garin haihuwar Anna garin neman jarabarsa,

Ihun da Mariama ke yi masa ne ya saka yan uwanta shigowa suma a guje sunna nufar inda Ba da mariama ke turayar juna kan sai sun taba Anna

Gaishata ce ta dora hannayenta saman kanta da karfi ta ce" innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, Ba Mariama ku dagata ku dagata na ce!

Tsai Ba ya yi , jikinsa na rawa ya nufo Gaishata tamkar zai maketa ya raba ta gefenta ya fice a gidan yana dumumuwa shi kadai ,

Da kyar suka iya cicibata domin Gaishata ba wani kokari zata iya yi ba sai su biyun ne suka iya kamata suka dora saman tabarmar kaban dakin

Hurhutu suke mata suna shafa mata ruwa aman ko motsi, sai numfashinta dake fita a hankali iamar a cicire ta samkame ita ba gawa ba ita ba rayaya ba,

Gaishata ce ta ciciba ta mike tana jin yanda mararta ke wani irin juya mata ta nufi kofa tana takawa da kyar tana saurin da zata iya ta nufi fada

Tunda ta karaso dogaran sarki ke mata sannu inda aka sakar mata hanya ta shige fadar suna

mamakin ganninta domin sarki ya hanata zuwa fada kar a kake masa ita,

Kanta tsaye ta nufe shi inda ya mike da sauri daga kujerar mulkinsa dogarai suka shiga baza manyan rigunansu suna kare su, yan zama fada suka fara darewa da sauri sauri

Tana isa jikinsa ta zube wanda sukai taga taga dalilin kibar da ta kara ga kuma tsohon ciki,

A hankali ya samu ya daidaitata a jikinsa ya dora hannunsa inda ta dora nata wato saman cikinta da take ji baki daya yana wani irin yamutsa mata bayanta na sarawa,

Me ke damunki Gaishana,
Ya fada yana mai nuna tsantsar damuwarsa da tashin hankali, yanaiwa Gaisha soyaya mai karfin gaske,

Da kyar ta iya sauke ajiyar zuciya muryarta na rawa ta ce" Anna ce, Anna ce ta fadi, kuma tana numfashi aman ta ki farkawa,
Rigarsa ta jimke jin ciwon na tsananta ta ce" idan wani abin ya sami mahaifiyata zan shida duhu sarkina👏🏻

Zaunar da ita ya yi saman kujerar ya cire babar rigarsa ta turkudi ya rufa mata ya yi gyaran murya,

Dogari ne ya amsa masa,
Sarki ya ce" ka je wajen jakadiya ingozoma ka fada mata Gimbiya na Daka.

Da gudu ya juya inda sarki ya daga karewar da akai masa ya fita da niyar zuwa gidan su Ba, yau kam za.a yita ta kare, ba zai yarda haka ana tayarwa matarsa hankali ba, ! Gashinnan tashin hankali ya sakata nakudar dole,

*Niamey*

Tunda Ayya ta fara magana tana duban Agaishat da dukan kulawa kan Agaishat ke kasa tana zubar da hawaye,
Abaya ce baka mai shegen kyau , bata da wata kwaliya sai zif din da ya hadeta a jikinta, gyaran fatar kwana biyun da Ayya ta yi ta dilketa ya saka fatarta ta kara wani haske da santsi wanda ko a ido ka dubeta zaka ga ta gyaru iya gyaruwa,
Dan kwalin Abayar ne ke dan zamewa tana rikeshi har ya kai karfinta ya kare ta sake shi ta duke sosai tana kuka inda gaba daya jikinta ke jijiga

Idannuwansa ya rintse da karfin gaske, sannan ya jimki kujerar da yake kai,
Kansa ya juyar gefe yana jin saukar kukan nata tamkar ana narkar masa da dalma a kahon

zuciya,
Mu.azam dake gefensa shima cike da tausayin matar tasa ya mintsini hannun Wardugu yanai masa nuni da ya yi wani abin mana?

Wardugu ya juyo inda take suke Ayya na rarashinta itama na sharar hawayen ya hade fuska sosai ya ce" ke!

Yannayon yanda ya ambaci ke din sole ka tsorata, yannayi ne ya garwaye da halin da yake ciki,
Da sauri ta juyo tana kara shigewa jikin Ayya,

Mikewa ya yi ya ce" mu je!

Da sauri ta waigo wajen Ayya, wace rake cikin damuwar rabuwa da yar tata, wace kamar da wasa shakuwa mai girma ta kara shiga tsakaninsu,
Tun jiya ya dace su tafi aman cikin ikon Allah Agaishat ta rikice ta yi ta kuka har zazabi ya rufeta wai ita ba zata bisu ba,
Ayya ta yi gargadin ta yi fadan, ta dawo lalaba tana mai shaida mata tamkar suna tare ne, ga waya, ta bi mijinta zai dawo da ita da wuri

Kamar da gaske ta yarda a jiya da dare, a yanzu da suka shirya har Wardugu ya zo rakiyarsu ta kuma birkicewa,

Ayya ta ce" Wardugu kar ka yi mata da zafi mana, rabuwa da iyaye ba dadi ka lalabata na roke ka,

Wardugu ya juyo yana duban Ayya, idannuwansa sun kade sun yi jajir, a ransa kam birgeshima suke , su sun samu kukan, sun huta,
Lebensa ya dantse kawai ya girgiza kai ya dawo da wani irin taku ya dauki dan kwalinta dake kasa ya rufa mata , da idannuwansa ya yi mata nunin ta fice ko jikinta ya gaya mata,

Da sauri ta yi gaba tana waiwayen Ayya, wace ta koma saman kujerar tama fasa rakasu dan ba zata juri yanda Agaishat ke kukan ba zata je wata kasa ba, ba zata je ba ta fasa auren!

Ko a cikin mota Mu.azam na gaba ne, Agaishat da Mariama na baya, direba na jansu, ta madubi yake duban yanda ta yi lakwas da ita, yana matukar son ya rarasheta aman yana jin nauyin Mariama, baya so ran Mariamarma ya bace dan haka ya adanna rarashin idan sun sauka zai mata, duda har yanzu Mariama bata ce komai game da auren nasa ba, bata nuna damuwarta ki farin cikinta ba, haka shima kwata kwata baya nuna zumudinsa ko wata shakuwa tsakaninsa da amaryar tasa,

Mita wajen biyarce ke tafe har aeroport, suna karasawa inda ake ajiye motoci du suka firfito banda taron sojojin dake tare da su,

Wardugu ya bude gefen da yake ya fara fitar da kafarsa ta dama kafin ya fitar da ta hagu,
Yau a kakin sojoji yake, ya nanade hannayen rigar har saman damtsen hannunsa hakan ya baiwa rigar damar tamke shi, jijiyoyin hannunsa sun yi rado rado ,
Da karfinsa ya taka ya shiga inda iya su suka bi bayansa

Bakin gilas ne rufe da idannuwansa , duda haka zaka gane fuskarsa a tamke take ba alamar fara.a

Polisan dake aiki a wajen du idan ya zo ficewa sai sun sara masa, shi kuwa sai dai ya shige yau arzikin daga hannunma basa samu

A haka har suka karaso, yauma Allah ya so su da sun rasa jurgin domin lokaci ya tafi har an fara shiga

Tsaye ya yi a inda iyakar yan rakiya kennan, ya juyo wajen Mu.azam dake biye da shi,

Hannunsa ya kamo suka damke juna,
Murmushi Mu.azam ya sakar masa yana mai nuna masa ba komai ya kwontar da hankalinsa,

Bai bashi amsa ba sai kafadarsa da ya daka da hannunsa ya nuna masa sai ya zo,

Gaba Mu.azam ya yi shima yana mai jin zuciyarsa na tsintsinkewa ya nufi wajen da zai shiga jirgi dan an kirayi sunnan Khadija har ta yi gaba .

Du takunsa dan nufar wajen da take tsaye wanda wajen ya kasance hanyarsa ta fita, daidai da bugun zuciyarsa ne, bai so tsayawa ba, sai dai ya ji ya tsaya facing dinta

A hankali ya dora hannunsa dake dan bari kan habarta ya dago da ita inda ya tsare idannuwansa da kallo,

A hankali ya saka hannunsa na hagu ya share mata hawayen dake mata zarya,

Wayar hannunsa ya saka cikin hannunta ya dan ja gefe ya kama hannunta ya jata a hankali har inda Mu.azam yake ya saka hannun nata cikin na Mu.azam ya dan yi tsai sannan ya juya da wani mugun saurin da sai da ya gansa a waje shi kansa

Da sauri Mu.azam ya kama hannunta suka shiga taka matatakalar jirgi, wanda ya kasance hawanta ya farki, shigarta ta fari suka shiga
Kusa da Khadija ya zaunar da ita shi kuwa ya je kujerar bayansu , du yana haka ne kar Khadija ta kulace ahi, wanda shirunta ke damun nutsuwarsa

😅😅siga baya kiran kansa siga, sai dai wani ya fada,😅😅

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤️*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝🏻😘

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

5️⃣0️⃣

Allah ya sauke su lafia, du kuwa da irin yanda Agaishat ta jigata domin har amai ta yi a lokacin fa jirgi zai tashi da irin yar jijigar nan da yake kafin ya mike da tafia, sannan a lokacin saukarsa wannan kasan da abubuwan ciki ke yi suka saka shima ta yi tamakar ta sume,
Mu.azam na kule da ita , tausayinta yake ji, khadija ce ke kiran yan matan nan na jirgi da ta ga zata shiga wani yannayi , su ke zuwa su bata kulawa har jirgin ya sauka,

Agaishat dai na mamakin irin halin shariyar da Mu.azam ke nuna mata idan suna tare da Khadija, tun bata gane komai ba har ta gane sai dai bata nuna ko a fuska ba,

Ko wajen sauka shi ne gabansu su kuwa suna biye da shi a baya inda Agaishat ta zama ta karshe

Kanta ne ta ji yana juya mata lokacin da ta ganta cikin tankamemen aeroport din *Paris*

A hankali ta sada kanta dan ta lura du idan ta daga kan ta ga irin tsaruwar garin ne hankalinta ke tashi,

Fitowa suka yi inda manyan motocin taxi ke laye, da yawa an yi kiransu je, daidaiku ne suka zo wajen dan radin kansu

Wajen motar suka nufa , nan Mu.azam ya juyo gannin Khadija bata biyo su ba,

Budewa Agaishat ya yi ta shiga ta zauna inda Direban ya saka akwatinta bayan motar,

Wajen Khadija ya nufa yana son sai ya karanci fuskarya aman ta ki bashi dama,
Yana zuwa hannayenta ya kama yana dubanta ya ce" ba zaki biyo mu ba?

Murmushi ta sakar masa ta girgiza kai ta ce" ku je da matarka, nima zan dauki wata taxi din, zan leko ka, ka kular min da kanka nan da kwana hudu zaka dawo asibiti ka kwana biyu bisa kulawar docters kafin a shiga aiki da kai,

Murmushi ya sakar mata ya lakace hancinta ya saki hannayenta ya juya ya nufi motar inda sai a lokacin Agaishat ta kawar da fuskarta gefen madubin motar

Satar kallonta ya yi, sai a lokacin ya ji wani nauyinta, rabonsa da ya yi wani maganar nutsuwa da ita tun da Khadija ta sauka a gidan Ayya,
Kwarai Ayya ta yi masa mutunci ta nuna komai ba komai ba ta hanyar kawar da kanta ta kuma karbi bakuwarsa duda tsanar akidar kawance tsakanin mace da namiji da ta yi kuwa, sannan koda suka tashi tafia ta yi masa gargadi nasiha kamar yanda iyayensa zasu yi masa, sai dai kuma ta nanata ya rike amanar baiwar Allah,
Gabansa ne ya ji ya fadi, amanar Agaishat ya karbo fa, amana ya karba, anya kuwa haka amana ta ce?

A hankali ya mika hannunsa na hagu ya dora saman cinyarta , wanda ke nuni da yana son kara kusancinsa da ita,

Agaishat ta juyo ta dora tsararun irannuwanta saman hannunsa, daga nan bata kai dubanta sama ba ko dan kar idannuwansu su shaku da juna, sai ta kawar da kanta ta mayar bakin titi tana kallon hanya da mamakin irin tsarin garin da irin shigar mutanen garin

Bai dauke hannunsa ba, bai kuma yi mata magana ba har suka karaso kofar wani gida
Daga kofa raga ne na karfe baki, haka ya ja jakar tana biye da shi tamkar kazar da kwai ya fashewa a ciki har ya saka cod din kofar gidan nasa suka shiga,

Fulawowi ne a gidan, ba wani tankamemen gida bane , dan madaidaici ne tsarare,
Matatakalar suka hau suka shiga ainahin falon gidan,
Plat ne, ba bene, dakuna kwaya biyu ne sai katon bayi da kicin mai girma da tsari da wajen buga game, kujeru farare kar ne a falon sai dan table fari, tv tankamemiya jikin bango sai wajen da ake kuna wuta dan dakin ya dau zafi , sai ac biyu a iya falon

Kofar ya mayar ya rufe ya saki akwatin nata nan,
A hankali ya juyo yana takowa inda take tsaye kanta na kallon kasa,

Yana isowa ya kama hannayenta yana yi kata kallon kurullah,
Jin ya jima bai yi magana ba ta dago a hankali ta sauke tsumamun idannuwanta cikin nasa,
Fuskarsa ya shagwabe ya jata zuwa saman kujera mai zaman mutun biyu ya zaunar da ita,
Kusa da ita sosai ya zauna yana so sai ta kara yi masa kallon da ta yi masa aman du yanda ya so ta kiya,

Muryarsa ya kimtsa ya ce" kin daina so na😭, me ya sa kika daina so na?

A hankali ta juyo da dubanta wajensa, kurawa fuskarsa ido ta yi, a ranta ta ayyana, ai bamu kai ga gane menene so din ba aka daura auren mu, a fili kuwa sai ta kifta idannuwanta da suka fara cika da kwallah,

Murmushi ya yi ya ce" ki yi hakuri Agaishana, kar ki yi fushi da ni, na san kina da tarin tambayoyi aman ki yi hakuri ki bar su a wajenki har sai lokacin yin su ya yi , ki sani ina son ki ba zan daina son ki ba, ina gannin girmanki ina daraja ki a rayuwana, ban aure ki dan cutarwa ba,

Wani sanyi ta fara ji a ranta , nan da nan ta ji ta fara manta shaku da rudannin da ta shiga dalilin nesanta kansa da ya yi da ita kwanakin nan, (kar ku ga laifinta, baki daya a duhu take),

Dan murmushi ta sakar masa aman batai magana ba,
Mikar da ita ya yi ya ja hannunta suka nufi daki............🙄

*Timiya*

Wasa wasa sai da Anna ta wuni ta kai tsakiyar dare wajen karfe biyun dare ta wani irin kwala karan da ya firgita yayanta dake zagaye da ita ta aniya amsa kira tamkar ana kiranta , fadi take" *Na.am, Na.am, Na.am?*,
Kuftaya ta shiga yi da dukan mai kokarin riketa, idannuwanta rufe suke ruf tana ihun amsa kiran da basu san mai kiranta ba,

Digarin da Sarki ya bari ya kula da lafiar Gaishata dake ta faman nakuda tare da Jakadiya har zuwa lokacin bata haihu ba gashi da ta dora masa kuka sai da aka sakata cikin kurakura aka kawota gidan Annar, haka suka wuni har gashi rabin kwana zar suna fama ne ya shigo da sauri jin hayaniya,

Fitikar kwan da ya kunna ce ya kara masu haske a dakin da ta wajensu , subahanallah shine abinda yake ambata gannin irin yanda suka kasa tareta ga kuma Gaishata sai murkashi take tana kuka gashi kusa da ita suke jakadiya sai tarewa take kar a fado mata,
Gannin ana iya fado mata a samu matsala ya saka shi saurin shiga dakin ya je suka hadu su

uku suka kai Anna kasa inda Jakadiya ta shiga fadin ya taho ya taho,
Da sauri Dogari ya mike ya kama Anna da ta fara dan yi lakwas ya cicibeta su kai waje domin ya gane Gimbiyar sarkinsa zata haihu ne,

Nishin Gaishata da nishin Anna du tare ne, cikin ikon Allah Gashata ta haihu lafia ta sako yaronta har Jakadiya ta yanke cibi ta dauke uwar da ta fado ta nade a zanin Gaishata bayan ta dora mata yaron saman cikinta ta aniya kimtsata tana ta murna,

A galabaice Gaishata dake lumshe ido tana budewa na ni.imar nakuda 🤣 ta kallo jakadiya, murya a disashe ta ce" Annata?

Jakadiya ta ce" Allah ya ja da zamaninki kar ki damu in sha Allah da sauki, ai dogarin nan dan gidan cheik Ne, baban almajiri ne gayacan sunai mata adu.a,

Sosai suka dukufa suna yiwa Anna du adu.o.in da suka iya inda shi kuwa dogari ya dauro Alwallah ya zo shima da ruwa a kwanon kwano ya zauna ya shiga karanto mata manyan adu.o.in karya sihiri, na rukuya kai harma da na tsari duka yana tofeta da shi kuma yana tofawa a cikin ruwan,

Mikawa Mariama ya yi ta shafa mata gaba daya jikinta suka ci gaba da adu.o.in ,

Wasa wasa sai da garin Allah ya waye domin kuwa sai da aka kirayi salar asuba Anna ta ja wata irin ajiyar zuciya ta yi wata irin mika kafin take zabura ta ce" *Ayya, Ayyana, wani abu zai rufe min ido, wani abu Ayya* (kar ku manta tubawa ke kiran Mama da Ayya, wace Ayya xce haka? Shin Anna ta dawo hayacinta?))))

Kadan ne

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

50

Allah ya sauke su lafia, du kuwa da irin yanda Agaishat ta jigata domin har amai ta yi a lokacin fa jirgi zai tashi da irin yar jijigar nan da yake kafin ya mike da tafia, sannan a lokacin saukarsa wannan kasan da abubuwan ciki ke yi suka saka shima ta yi tamakar ta sume,
Mu.azam na kule da ita , tausayinta yake ji, khadija ce ke kiran yan matan nan na jirgi da ta ga zata shiga wani yannayi , su ke zuwa su bata kulawa har jirgin ya sauka,

Agaishat dai na mamakin irin halin shariyar da Mu.azam ke nuna mata idan suna tare da Khadija, tun bata gane komai ba har ta gane sai dai bata nuna ko a fuska ba,

Ko wajen sauka shi ne gabansu su kuwa suna biye da shi a baya inda Agaishat ta zama ta karshe

Kanta ne ta ji yana juya mata lokacin da ta ganta cikin tankamemen aeroport din *Paris*

A hankali ta sada kanta dan ta lura du idan ta daga kan ta ga irin tsaruwar garin ne hankalinta ke tashi,

Fitowa suka yi inda manyan motocin taxi ke laye, da yawa an yi kiransu je, daidaiku ne suka zo wajen dan radin kansu

Wajen motar suka nufa , nan Mu.azam ya juyo gannin Khadija bata biyo su ba,

Budewa Agaishat ya yi ta shiga ta zauna inda Direban ya saka akwatinta bayan motar,

Wajen Khadija ya nufa yana son sai ya karanci fuskarya aman ta ki bashi dama,
Yana zuwa hannayenta ya kama yana dubanta ya ce" ba zaki biyo mu ba?

Murmushi ta sakar masa ta girgiza kai ta ce" ku je da matarka, nima zan dauki wata taxi din, zan leko ka, ka kular min da kanka nan da kwana hudu zaka dawo asibiti ka kwana biyu bisa kulawar docters kafin a shiga aiki da kai,

Murmushi ya sakar mata ya lakace hancinta ya saki hannayenta ya juya ya nufi motar inda sai a lokacin Agaishat ta kawar da fuskarta gefen madubin motar

Satar kallonta ya yi, sai a lokacin ya ji wani nauyinta, rabonsa da ya yi wani maganar nutsuwa da ita tun da Khadija ta sauka a gidan Ayya,
Kwarai Ayya ta yi masa mutunci ta nuna komai ba komai ba ta hanyar kawar da kanta ta kuma karbi bakuwarsa duda tsanar akidar kawance tsakanin mace da namiji da ta yi kuwa, sannan koda suka tashi tafia ta yi masa gargadi nasiha kamar yanda iyayensa zasu yi masa, sai dai kuma ta nanata ya rike amanar baiwar Allah,
Gabansa ne ya ji ya fadi, amanar Agaishat ya karbo fa, amana ya karba, anya kuwa haka amana ta ce?

A hankali ya mika hannunsa na hagu ya dora saman cinyarta , wanda ke nuni da yana son kara kusancinsa da ita,

Agaishat ta juyo ta dora tsararun irannuwanta saman hannunsa, daga nan bata kai dubanta sama ba ko dan kar idannuwansu su shaku da juna, sai ta kawar da kanta ta mayar bakin titi tana kallon hanya da mamakin irin tsarin garin da irin shigar mutanen garin

Bai dauke hannunsa ba, bai kuma yi mata magana ba har suka karaso kofar wani gida
Daga kofa raga ne na karfe baki, haka ya ja jakar tana biye da shi tamkar kazar da kwai ya fashewa a ciki har ya saka cod din kofar gidan nasa suka shiga,

Fulawowi ne a gidan, ba wani tankamemen gida bane , dan madaidaici ne tsarare,
Matatakalar suka hau suka shiga ainahin falon gidan,
Plat ne, ba bene, dakuna kwaya biyu ne sai katon bayi da kicin mai girma da tsari da wajen buga game, kujeru farare kar ne a falon sai dan table fari, tv tankamemiya jikin bango sai wajen da ake kuna wuta dan dakin ya dau zafi , sai ac biyu a iya falon

Kofar ya mayar ya rufe ya saki akwatin nata nan,
A hankali ya juyo yana takowa inda take tsaye kanta na kallon kasa,

Yana isowa ya kama hannayenta yana yi kata kallon kurullah,
Jin ya jima bai yi magana ba ta dago a hankali ta sauke tsumamun idannuwanta cikin nasa,
Fuskarsa ya shagwabe ya jata zuwa saman kujera mai zaman mutun biyu ya zaunar da ita,
Kusa da ita sosai ya zauna yana so sai ta kara yi masa kallon da ta yi masa aman du yanda ya so ta kiya,

Muryarsa ya kimtsa ya ce" kin daina so na😭, me ya sa kika daina so na?

A hankali ta juyo da dubanta wajensa, kurawa fuskarsa ido ta yi, a ranta ta ayyana, ai bamu kai ga gane menene so din ba aka daura auren mu, a fili kuwa sai ta kifta idannuwanta da suka fara

cika da kwallah,

Murmushi ya yi ya ce" ki yi hakuri Agaishana, kar ki yi fushi da ni, na san kina da tarin tambayoyi aman ki yi hakuri ki bar su a wajenki har sai lokacin yin su ya yi , ki sani ina son ki ba zan daina son ki ba, ina gannin girmanki ina daraja ki a rayuwana, ban aure ki dan cutarwa ba,

Wani sanyi ta fara ji a ranta , nan da nan ta ji ta fara manta shaku da rudannin da ta shiga dalilin nesanta kansa da ya yi da ita kwanakin nan, (kar ku ga laifinta, baki daya a duhu take),

Dan murmushi ta sakar masa aman batai magana ba,
Mikar da ita ya yi ya ja hannunta suka nufi daki............🙄

*Timiya*

Wasa wasa sai da Anna ta wuni ta kai tsakiyar dare wajen karfe biyun dare ta wani irin kwala karan da ya firgita yayanta dake zagaye da ita ta aniya amsa kira tamkar ana kiranta , fadi take" *Na.am, Na.am, Na.am?*,
Kuftaya ta shiga yi da dukan mai kokarin riketa, idannuwanta rufe suke ruf tana ihun amsa kiran da basu san mai kiranta ba,

Digarin da Sarki ya bari ya kula da lafiar Gaishata dake ta faman nakuda tare da Jakadiya har zuwa lokacin bata haihu ba gashi da ta dora masa kuka sai da aka sakata cikin kurakura aka kawota gidan Annar, haka suka wuni har gashi rabin kwana zar suna fama ne ya shigo da sauri jin hayaniya,

Fitikar kwan da ya kunna ce ya kara masu haske a dakin da ta wajensu , subahanallah shine abinda yake ambata gannin irin yanda suka kasa tareta ga kuma Gaishata sai murkashi take tana kuka gashi kusa da ita suke jakadiya sai tarewa take kar a fado mata,
Gannin ana iya fado mata a samu matsala ya saka shi saurin shiga dakin ya je suka hadu su uku suka kai Anna kasa inda Jakadiya ta shiga fadin ya taho ya taho,
Da sauri Dogari ya mike ya kama Anna da ta fara dan yi lakwas ya cicibeta su kai waje domin ya gane Gimbiyar sarkinsa zata haihu ne,

Nishin Gaishata da nishin Anna du tare ne, cikin ikon Allah Gashata ta haihu lafia ta sako yaronta har Jakadiya ta yanke cibi ta dauke uwar da ta fado ta nade a zanin Gaishata bayan ta dora mata yaron saman cikinta ta aniya kimtsata tana ta murna,

A galabaice Gaishata dake lumshe ido tana budewa na ni.imar nakuda 🤣 ta kallo jakadiya, murya a disashe ta ce" Annata?

Jakadiya ta ce" Allah ya ja da zamaninki kar ki damu in sha Allah da sauki, ai dogarin nan dan gidan cheik Ne, baban almajiri ne gayacan sunai mata adu.a,

Sosai suka dukufa suna yiwa Anna du adu.o.in da suka iya inda shi kuwa dogari ya dauro Alwallah ya zo shima da ruwa a kwanon kwano ya zauna ya shiga karanto mata manyan adu.o.in karya sihiri, na rukuya kai harma da na tsari duka yana tofeta da shi kuma yana tofawa a cikin ruwan,

Mikawa Mariama ya yi ta shafa mata gaba daya jikinta suka ci gaba da adu.o.in ,

Wasa wasa sai da garin Allah ya waye domin kuwa sai da aka kirayi salar asuba Anna ta ja wata irin ajiyar zuciya ta yi wata irin mika kafin take zabura ta ce" *Ayya, Ayyana, wani abu zai rufe min ido, wani abu Ayya* (kar ku manta tubawa ke kiran Mama da Ayya, wace Ayya xce haka? Shin Anna ta dawo hayacinta?))))

Kadan ne

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤️*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

5️⃣1️⃣

Da kyar suka samu kunnayenta suka jiyo magangannunsu, domin du magangannun nan da take sun firgice basu san me take fada ba  da yaren Tubanci take magana,

Shiru ta yi ta shiga bude idannuwanta a hankali numfashinta na sama da kasa da sauri sauri ta kankame hannayenta a jikin kirjinta tana mai bin mutanen wajen da kallo,
A hankali numfashinta ke daidaita  rayuwar da ta yi a wannan kauye ke dawo mata daki daki,
Da sauri ta tsurawa y'ayan da suke malakinta ido, kafin ta kai dubanta wajen Gaishata dake rabe jikin garu tana duban mahaifiyar tata , domin da Jakadiya zata tafi kaiwa Sarki albishir bayan an yi kiran sallah ta umarceta da ta kamata su fito wajen yan uwanta, nan ta luluba mata katon bargon nan baki mai ciyayi ta fitar da ita dan kuwa har zuwa lokacin batai wanka ba, yo yaronma ba wani kulashi ta yi ba hankalinta na kan mahaifiyarta,

A hankali Anna ke girgiza kanta kafin ta furta" innalilahi wa.ina ilaihi raj.une,
Hannayenta ta dago tana bi da kallo wa.inda turkudi ya rike su da duhu aman ana ganni za.a gane fatarta ta fara nuna alamar gajiya irin ta zama datijuwa,

Tana tsakar haka sai ga ison Sarki na son shigowa,

Da sauri dogari ya tatare abin tatarewa ya karbi tabarma a hannun Mariama ya shinfida dan nesa da su kafin yake zuwa ya dage buhun dake a matsayin makarin shiga cikin gidan,

Shigowa Sarki ya yi bayan ya tsayar da yan rakiyarsa ya karasa cikin gidan yana mai salama ,

A hankali suke amsa masa,
Dubansa ya kai wajen Gaishata dake rabe itama ta dago kanta ta dube shi ta sada kanta,
A hankali ya kai duban nasa wajen Minata dake rike da jariri ta lulube shi a cikin jikinta,
Ajiyar zuciya ya sauke ya duka yana gaisar da Anna,
Kanta kawai ta iya daga masa bata bashi amsa ba,

Zama ya yi ya ce" Anna ya jiki? Da yaren buzanci

Anna ta dago manyan idannuwanta ta sauke kansa, idannuwan kawai ta lumshe a zuwan amsawa,

Shiru ne ya biyo baya tana duban yaren, bakinta cike da magana,
Can ta ce" ina Yake?

Mariama dake son ta mike daga irin zaman da ta yi ta matsa kusa da ita sosai ta ce" ANNA tun jiya ta fita bai dawo ba, Anna ki tashi ki wanke jikinki , ko sallah baki yi ba fa,

Anna jin maganat sallah ta samu ta ciciba inda Mariama ta kamata suka nufi dan zagayen dake bayi ,
Mariama ce ta kai mata ruwa a butar karfensu kafin take zuwa ta shiga kiciniyar dora ruwan zafi , inda Sarki ya karbi yaron ya dan matsa kusa da Gaishata yana rarashinta dan ta sake ,

Ta jima tana fama da ruwa , da omo blue din da ta bata wanda shi ne sabulun wankan, ta jima kafin ta sakawa fatarta shi, ta samu da kyar ta dan rage datin jikinta ta fito ta daura alwallah ta raba su ta shige daki ta tayar da sallah,

Ta jima tana salolinta dan kuwa baki daya sai da ta rama su, tana gama tahiyar karshe ta zauna zaman adu.a , nan ta fashe da kuka mai shiga zuciya tana jijiga gaba dayanta,

Hankali tashe suka shigo dakin gaba dayansu inda Mariama ta bude takar dakin dan haske ya kara shigowa,

Zuwa ta yi itama ba wani jira ta shige jikin Anna tana kuka ta ce" Haba Anna, haba Anna, menene ne? Me ya yi maki haka? A rayuwa mun ga tashin hankali kala daban daban , baki taba tankawa ba, aman jiya karar faduwarki kawai muka ji, shin me ya miki kika suma haka? Anna ki yi hakuri, ki dawo hayacinki domin ke ce nutsuwarmu👏🏻,

Anna ta sasauta kukanta, tausayin y'ayan nata ya shiga zuciyarta,

Kanta a rufen nan ta vikin yaren tubanci ta ce" Amma ay yini zundu yigustiya, ayyinira unga ci? Dudonur? Tani ayyinira baranniri, abbanur dudonur ( fasara: wannan mutumen ya cuce ni, ina iyayena? Ina yar uwata? Ku taimaka ku kaini wajen mamata, da babana, da yayata.)

Mariama ta juyo wajen sarki hankali tashe ta ce" ka ji yaren da take, tun da ta farka wannan yaren ne take yi, mu bamu san me take cewa ba, Anna ki taimake mu, shin kin manta yarenmu ne?

A hankali Sarkin ya karasa shigowa ya duka dan nesa da ita ua tausasa murya sannan ya sada kai irin girmama siriki  da yaren tubancin ya ce" Halasss de wonnuy? Ammanuma ngalla cuku? Tussu ko ka yogodi taha tani tudaqanur cussu qunu. (FASARA: ki kwontar da hankalin ki, ni ban fahimci komai a magangannun nan ba, waye ya cuce ki? Sannan ki taimaka ki fada min da buzanci ko zan gane da kyau.)

Ajiyar zuciya ta sauke kafin take gyara zamanta tana dubansu ta ce" Sunana *ALLATCHI* yar gidan *GUKUNNI* kannin sarki Mahamat na *Ngimi*,
Sunnan mahaifiyata *Hatimi*, sunnan yayata *Herde*
Shiru ta yi tana duban yanda yayanta da sirikinta ke binta da wani kallon mamaki, ta yi murmushi ta ce" mahaifiyata fara ce kar kar tamkar ka taba jikinta jini ya fito, inda mahaifina ya kasance baki sidik , bakinsa har shuni yake domin bakin batube ne na usil, yayata ta yi bakin mahaifina duda ta kasance mace bakin nata bai kai can can ba inda ni kuwa na yi hasken mahaifiyata,
Da zaku tuna yannayin *Agaishana* fatar jikinta, kamanun fuskarta na mahaifiyata ne ba zan taba manta kamanun mamana ba, sai fatar ta yo ta abanna duda nata nada haske sosai kan na mahaifina, aman wannan yannayin shiru, tsayuwa kan kafafuwanta du kuwa da irin halin da take ciki du tana satar yannayin Abanna,

Sarki ya tafka tagumi cike da mamakin dake neman zauta shi  yana duban Anna, da saurin maganar da ba maganarsa ba tsabar firgita ya ce" kina nufin ke din Jinnin Honorable *GUKUNNI CE?*

Anna ta lumshe idannuwanta ta ce" ni yarsa ce ta biyu, wanda a sanina daga haihuwata aka juyar da mahaifar mamana dan rashin lafiar da take fama da ita daga bakin da ta samu ciki har haihuwa, ban san bayanna ko Abana ya kara aure ba . Mu biyu kawai iyayenmu suka malaka a sanina,

Sarki ya ce" na san honorable *GUKUNNI*, alkalin garin Niamey banban alkalin dake yanke hukunci masu laifi? Shi dai kike nufi?

Anna ta dago dubanta ta gyada ba tare da ta amsa ba, wani irin nauyin baki ta bude ido da shi may be haka take da.

Da mamaki sarki ya ce" aman aman ya aka yi kika tsinci kanki a nan?

Anna ta rintse idannuwanta ta ce" watarana mun fito daga saloon ni da yayata, muna cikin tuki muka bige wani saurayi mai rawani
A rikice muka tsaya nan yayata da ta fara aiki ta nunawa police din da ya zaburo wajen dan duba abinda ke faruwa da kuma kama mai laifi takardarta ta shaidar ita din likita ce mai zaman kanta ga kuma sunnan mahaifin mu dan haka aka hanzarta aka kama shi muka nufi likita a rikice sai kuka nake dan a rayuwa na kasance mai shegen tausayi da shigewa mutanen da ban sani ba du kuwa da irin gargadin mahaifiyata kan na ringa kiyayewa dan ba kowa ya zama na kirki mai zuciya sanyaya ba,

Mun kula da wannan mutun har ya samu lafia, iyayen mu sun ziyarce shi har asibiti bisa uzura masu da kuka da na yi ,
Bayan an salame shi ne ya duka yana kukan dan Allah mu taimake shi mu bashi aiki ya shigo garinnan bashi da kowa, daman zuwa ya yi neman kudi dan ya ciyar da iyayensa

Haka na nace du kuwa da irin ma.aikatan gidanmu, na kara kai da kas cewar mu dauke shi, buzu ne sai ya koya min buzanci ,
Gannin hankalina ya ki kwonciya Abana ya dauke shi aiki a matsayin mai baiwa fulawowin gidan ruwa,

Mun shaku da wannan bawan Allah domin ya kasance mai barkwonci da bayar da dariya , ni kuwa du inda za.a bani dariya ina wajen, sannan ni ba kawaye ba, gashi a lokacin yayata tana zuwa aiki, ni kuwa makaranta dan wajen shekara goma ne tsakanina da ita,

Sunnan wannan Bawan Allah *Algabittt*, Algabiitt buzu , Saurayi kyakyawa, Algabiitt mai kyan dan maciji,

Ni dai abinda zan iya shaidawa wata rana na fito daga zance da wani dan ajinmu wanda ya nuna yana so na dan nima ina karantar fannin likita ne a lokacin, na dawo zan shige na ga Algabittt tsaye da wani abu a hannunsa jikinsa na rawa sannan da ya saka wani irin turare mai karfi da wani irin abu mai juyar da kwakwaluwa, daga nan na manta wacece ni, na kasance Jelar Algabiitttttt, !
Mahaifina, mahaifiata sunna raye? Ina suke? A ina ka san su?
Anna ta jefo masa tambayoyi tana mikewa tsaye, dan ta lashi takobin yau ko wace wace, sai fa ta danganta da danginta ko a kafa ne!

*Paris*,

Sunna shiga dakin ya ajiye mata akwatin nata kusan dirowa, tsayuwa ya yi yana dubanta ya ce" Agaishana, bara na samo mana abinda zamu ci , ki yi wanka ga bayi can, idan kin gama ki yi sallah.

Da kanta ta amsa masa inda ya fice ya barta nan tsaye,

A hankali ta taka gaban katon madubin dakin ta yi tsaye tana duban kanta,
A nitse ta yi adu.a ta cire kayanta ta bude akwatinta ta dauki hijab dogo mai ruwan milk color ta saka bayan ta daura tawul mai tsayi a kasa,

Bayin ta bude ta shiga , a gidan Ayya du ta san yanda ake anfani da su domin du irin na gidan Ayyar ne, dan haka cikin nutsuwa ta sala wankanta da ruwa masu dumi kafin take karawa da masu sanyi a kasan shower ta gama ta dauro alwallah ta mayar da kayanta ta fito,
Salaya ta dauka wace ta ganni ajiye nan ta shinfida,
Wata doguwar rigar ta canza ta kabarta sallah,
Bayan ta gama sallarta ta zauna ta yi adu.a mai tsayi ga iyayenta, iyayen rikonta, da mijinta da al.umar musulmi da kanta,

Agogon dakin ta daga kanta tana kallo, a kadan ya yi awa biyu da fita,
Ajiyar zuciya ta sauke, da ba dan can daman ta saba da zaman kadaici da kuma rayuwar daji ba da ta tsorata da zama a daki irin wannan ita daya,

Mikewa ta yi ta ninke salayar nata ta gyara hijab din jikinta bayan ta fesa turare mai sanyin kanshi wanda fitarsu da Wardugu da Alhinayeeet wardugu ya kwaso mata su,

Ji ta yi ta kasa nutsuwa da jin shirunsa, dan haka ta mike a hankali ta bude kofar dakin nata da ba kara gare shi ba ta fito,

Abinda idonta ya ganni ne ya tayar mata da hankali,
Mu.azam ne zaune saman kujera, Khadija na gefensa da kaya irin sakakun nan na baci ta yane

kanta da farin dan kwali tana bashi abinci cikin cokali tana fadin" sai fa ka kara haka kake son baci? Ka san ba zan yarda ba fa!

Tsaye ta yi ta harde hannayenta ta tsayar da dubanta kan su,

Khadija ce ta fara ganninta wanda ya saka ta mike da sauri cikin yannayi na jin kunya, ya salam shi ne ta furta a kasan zuciyarta, ita fa har ga Allah ta sha.afa da mai mata yake yanzu, irin yanda a da take tsare shi sai ya ci abinci yanzu hakan ma iya taba zuciyar matarsa,
Kanta ta dan sosa ta sakarwa Agaishat murmushi ta ajiye spoon din ta juya kanta na kallon kasa ta bar dakin dan wani irin shakar Agaishat din ta ji na lokaci guda da tsoron hada ido da ita...........

Shima kansa ya sada  kasa ya kasa dago da kan,

A nitse ta karaso wajen da yake zaune ta duka ta dauki plat guda ta saka spoon din da ba.a yi anfani da shi ba ta debi abincin da ta san zai isheta ta ce" yunwa ya fito da ni, bara ka ga na yi na ci😊,

Shatata ya yi yana kallonta har ta shige dakinta,

Agaishat na shiga ta ajiye abincin dan nesa da wajen da ta yi sallah ta cire hijabinta ta zauna ta tankwashe kafafuwanta ta dauko wayar da Wardugu ya saka mata a hannunta da kuma wayar da Ayya ta saya mata ta ajiye gefenta ta yi bismillah zata fara cin abincin

Tsai ta yi ta tsurawa abincin ido, a fili ta ce" *Me ya sa ban ji wani abu wai shi kishi kamar yanda alhinayett ta fada min wai idan kana son mutun kana masa makahin kishi?* , shi din kishin kansa waye shi? Ya ake jinsa? Ta ce min idan na ga mijina da wata zan ji hankalina ya tashi, wasu na kuka wasu kuwa na nuna bacin ransu karara,
Ko dai bani da zuciya ne a jiki na?

Arrrakham

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤️*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

5️⃣2️⃣

Kafadunta ta daga tana mai baiwa kanta amsa" ai kawance ne, ba ga Alhinayett da Wardugu ba? Shi ya sa ban damu ba, kuma a hankali ai zan so shi, idan na so shin mai yiwuwa na kamun da kishin nasa?

Murmushi ta yi kafin take kuma wata bismillar ta shiga cin abincinta a nitse domin a gaskiya yunwa take ji , ita kuwa ko a daji ta saba du tashin hankalin da take ciki in dai ta samu sanwa bata raga mata , tana ci ta yi nak sai ta dora daga inda ta tsaya.

Tunda ta dauki abincin nan ya bi bayanta da kallo har ta kurewa ganninsa,
Hannayensa duka biyu ya dora a habarsa yana shafawa yana kai kawo, mamaki shi ne ya baibaye shi, ya mace zata tarar da mijinta zaune da wata a irin wannan lokacin a irin shigar Khadija duda ba wani shiga ne na kadaici ba, a irin kusancin zamansu, sannan tana ciyar da shi abinci ta juya ba tare da tace da shi ci kanka ba? Me hakan ke nufi? Ina , ina, wannan ba maganar dan ta fito a kauyen nan bata san so bane, su yan kauyen basa so ne? Su basu da zuciya ne? Su basa kishi ne? Bata nuna komai ba, shi bai ga wani yannayi na bacin rai a irin halin da ta tarar da shi da watanta ba, wani irin sanyi jikinsa ya yi harma ya katse masa hanzarinsa a kanta inda ya yi ta kai kawo ya kasa shiga dakinta dan kunyarta yake ji ya kuma kasa shiga ainahin dakinsa, har dare ya raba masa.

Su Walyn basu zo gida ba sai da ta yi kwana shida a gidansu, domin da likita ya salameta ta daure fuskar a fice gidansu da ita,
Mahaifiyarta ta bi umarninta suka je gidan su inda take samun kyakyawar kulawa daga iyayen nata tamkar su hadiye ta, dan du motsi za.a je ne a dauko kudi a banki sai dai Wardugu ya ji alert a wayarsa wace layin bankin ke ciki, yakan yi murmushi ya ci gaba da shagulgulan gabansa,

Wanka ta yi yau ta dandasa kwaliya da lifayar da ta sa mamanta ta sayo mata,
Sosai ta sha kwaliya ga kitso kananu ta yarfa a kanta ta hade karshe tana fitar da dadadan

kanshi,
Yar jakar hannu ta dauka ta karbi kys din mamanta inda ta rakota bakin motar sunna bankwaba yau ta yi niyar komawa gidanta,

Zama ta yi wajen direba ta mikowa mamanta hannunta ba tare da ta yi magana ba,
Maman nata ta yatsina fuska ta mika mata carte din Wardugu ta banki ba dan ranta ya so ba ta juya ta tafi bayan ta kara jadada mata ta kiyaye hayewa Wardugu sannan in ta je ta san irin zaman da zata yi da shi!

Haka ta kamo hanyar gidan da ta bari tsawon kwana shida. (WALYN shagali)

Aiki mai tsanani ne ya rike shi yauma kamar jiya, an yankewa mutane hukucin zaman gidan yari wa.inda aka kama hannayensu dumu dumu cikin harkar shigo da miyagun kwaya da abubuwan maye wanda alkali mai girma mai shari.a *GUKUNNI* ya tsaya tsayin daka ba mai kudin ba talakan sai da ya binciko abinda ke kasan kasa kafin ya tafka gudumarsa mai nauyi ya zayano irin adadin lokacin da du mai laifi zai yi a gidan yari, ba damar daukaka kara domin babar kotu ta niger ce ta yanke hukunci,
Wannan lamari ya saka Wardugu kansa ya dau zafi domin sunna ta kai kawon canzawa masu laifin waje, ga tsare tsaren kara tsaro da aka baza a cikin gari, ga mutanen dake damunsa da magiyar ya fitar da y'ayansu su kuwa da sun san bashi da damar hakan, ga niyar zuwansa Paris a yau da dare dan a gobe karfe bakwai na safe za.a shiga aiki da amininsa dan uwansa, aikin dake tatare da hatsari, du wani masoyinsa yana cikin zulumin lamarin domin a daidai wannan lokacin Ayya ta san komai, .........

Bai gama saita abinda zai saita ba sai bayan magariba wanda a lokacin bai fi masa sauran awa hudu jirgi ya tashi da shi zuwa Paris ba.

Da gagawa ya fito ya shiga bayan motar da bodyguard ya bude masa, nan direba ya shiga ya ja shi( sabon tsarin da ya fitar , yakan yarda direba ya ja shi yanzu, wanda a da kuwa sam baya yarda), ya nufi gidan Ayya da shi,
Baiwar Allah tana zaune a tsakar gida , hasken fitulu sun garwaye gidan tana dan kada kafafuwanta da jarida a hannunta ta saka gilas na ganni a idannuwanta, shi kawai take jira

Wardugu na zuwa ta bayan kujerar ya rungume Ayya yana mai dora kansa saman kafadarta yana rintse idannuwansa,

A hankali ta dan tapng din hannunsa ta ce" Me ke damun ka?

Wardugu ya sauke ajiyar zuciya yana kokarin sakin Ayya ya dawo facing dinta ya ce" zan je na tafi Ayya,

Ayya ta girgiza kai gannin ya basar da tambayar da ta yi masa,
Hannunsa ta kamo ta rike ta ce" idan ka je ka zama jarumi , kar ka saki ambaton Allah ko me

zai faru, ka kasance mai hakuri gaban abinda ya fi karfin ka, ka taimake ni ka kular min da yar amanata, ban so ka hana ni tafia ba, dan ban san ya zata tsinci kanta a ciki ba, yarinya ce, yarinya ce karama,

Wardugu ya lumshe idannuwansa kafin yake budewa a hankali yana duban Ayya, hannayenta duka ya hade ya dora a kirjinsa kafin yake sada kansa, a kadan ya kai minti biyar a wannan yannayin, wanda Ayya ta dora habarta saman yalwatacen sumar kansa utama ta lumshe idannuwan nata,

Shi ya fara motsawa a hankali yana duban mahaifiyar tasa, murmushi ya sakar mata mai tsari kafin yake cewa" adu.arki muke bara ya Anmi👏🏻,

Allah ya kare ka, ya bashi lafia, ya kare min yarinta....Ayya ta fada tana shafa gefen fuskarsa

Murmushi ya saki yana amsawa saman lebensa kafin yake mikewa su jero da Ayya har wajen motar ya bude ya shiga,

Tukashi ake aman yana kara gannin girman soyayar dake tsakannin Ayya da yarinyar nan, Murmushi ya yi ya muzkuta ya dauki wayarsa ya dannawa Khadija kira,

A lokacin Khadija na zaune saman salaya tana jan carbi, Agaishat na saman doguwar kujera mai zaman mutun guda ta lumshe idannuwanta da irin carbin nan wanda ake makalawa jikin yatsa tana danawa a hankali a hankali,
Mu.azam kuwa na baci wanda na allurar bacin da ake yawan yi masa ne dan ya samu cikaken hutu tunda aka kawo shi asibitin,
Ba wani magana tsakanin su aman suna mutunta juna....
A nitse ta daga wayar Wardugu, wanda a kwana biyun nan yakan kirata sau hudu du kuwa da irin yanda aiki ya sha kansa,
Tana dagawa kamar yanda ya saba , salama ya yi mata sai kuma ya ja bakinsa ya yi gum,
Murmushi ta yi , kai halayan abokin Mu.azam na bata mamaki, wannan da mace aka yi gaskiya za.a sha yanga,
Khadija ta mike a hankali ta fita dan kar ta yi wani dan motsinma da zai iya tayar da shi ta ce" Alhamdulilah general, jikinsa na karbar magungunnan yanda ya kamata kuma yana supporter, yanzu haka ya samu baci

Ajiyar zuciya Wardugu ya sauke kafin ya ce" Agaishat?

Khadija ta shafa gaban goshinta ta ce" gatannan zaune,

Ta ci abinci? Ya fada

Wayar ta ciro a kunnenta ta kuma duban sunnan, idannuwanta ta bude da kyau, tana mai jefawa kanta tambayar" wannan damuwa haka? Dan tana yar uwarsa ko dan tana matar

abokinsa? Kamar wata baby kulun ya yi kira zai tambaya ta ci abinci? Idan bata ci ba zai kashe ne da an jima ya kuma kira har sai ta shaida masa da ta ci, kuma ita ba cewa yake ta bata wayar ba, koma ba wannan ba ai Ayya na kiran Agaishat din a waya, tana da waya, baya kiranta ya tambayeta sai dai wani?
Amsa ta bashi kan ta ci, kafin yake cewa" Merci (thanx) ya katse kiran

Wayar ta bi da kallo, daga inda take tsaye ta hango Agaishat na dan motsa kafa kennan dai idannuwanta biyu,
Ajiyar zuciya ta sauke ta samu waje nan ta zauna

*Kwana uku da suka shige kafin a kai Mu.azam asibiti*

A wannan kwanakin tsakannin Agaishat da Mu.azam an samu shakuwa, shakuwa irin ta zama waje guda, shakuwa irin ta sosai din nan domin Khadija ta daina shigowa gidan sai dai shi yakan fita a kai a kai ya leka wajenta dan makotan juna ne  sai dai Agaishat ta hango shi ta windows

Ya nunawa Agaishat kulawa, sukan zauna su yi hira, harma su buga gem din da ya koya nata,
Ya koya mata cacakar waya ta iya shiga ta yi abinda take so,
Ya shaku da ita sosai , sai dai da magariba ta yi zai yi mata salama ne ya rakata dakinta ya fito, shima ya je dakinsa,
Bai taba hada shinfida da ita ba, kai ko kissing din hannunta bai taba ba bale ya zarce gona da iri, yana dai bata kulawar da ya saka Agaishat ta shaku da shi, har in bata ga wulginsa ba takan shiga yannayin damuwa har sai ta ganshi sun yi hira hankalinta ke kwonciya,

Ba zaka ga yanda halitar Agaishat ta kara kawatuwa ba sai ta saka wando dogo ko gajere , damame ko sakake irin shigar bacin nan da take, nan zaka ga mace a tsaye komai ya ji sai hamdala, Agaishat irin matan nan ne da sun san su waye su sai a slow, dan kuwa zasu iya anfani da halitar da Allah ya kawata su da shi dan firgita dubu su take dubu,
Zama waje daya, cin dadi, kwonciya baci tsala wanda sai sallah kawai da suka kasance ayyukanta na yanzu ya saka ta dauki yannayi na babar yarinya, daidai da murmushinta takan dan murmusa ne ta basar, koyon danna waya ya saka ta iya zama a karkace saman kujera, takan dan karkace kadan ta shiga danna wayarta tana gem na princess tana sakin dan murmushinta mai kawata fuskarta,
Mayukanta da Ayya ta siya mata dan kara gyara fatarta bata sanya da su, tana murzawa ne a duk lokacin da ta yi wanka ko alwallah, jikin Agaishat ya zama fresh ta kara haskawa sai santsi da fatarta ta kara,
Wannan fannin kam alhamdulilah ko ita tana gannin sauyi bale mai kallonta, hakan ya sa Khadija ke kara sarewa, bata iya zama na lokaci mai tsayi a tare da Agaishat, kamshin da take bazawama na turaran tubawa ya isa ya rikita maka tunani,

Tunda ta zo abu daya ya saka ta kuka, a ranar da ana gobe za.a shiga asibiti da mijinta,
Mu.azam ya kasa zuwa ya fada mata ainahin abinda ke faruwa da shi, sai da macen da yake

kira da aminiya ta yi masa jagora har cikin dakin barcinta, ta samu waje ta zauna ainahin wajen da Agaishat ke zama dan lumde jikinta da humura,
Ta wani kada kai kafin ta shiga zayanno mata rashin lafiar mijinta, ta fada mata cutar cancer ce aman za.a shiga aiki da shi, ta karashe tana mai sakin gungurmen kukan da ya karasa dode kunnuwan Agaishat da ta rasa ina ta dosa, me hakan ke nufi, ta kai dubanta wajen Mu.azam da ya mike jiki a mace ya karasa wajen Khadija ya shiga rarashinta da nuna mata ba ta yi masa allawarin ba zata yi kuka ba? A wannan rana Agaishat ta yi masu kallon tsaf, a wannan rana ta ji idannuwanta na rufewa, hankalinta na tashi, a hankali ta kwonta saman bed din dakinta ta rintse ido, bata san fitar Khadija ba sai jin hannunsa ta yi saman fuskarta yana share mata hawayen da suka shiga zubo mata wa.inda batama san suna yi ba, a wannan lokacin ta buda idannuwanta da sukai mata nauyi ta sauke su saman fuskarsa, ta shiga rudani tsakannin abu hudu
Na farko, rashin lafiar mutumen da yake mijinta, wanda akai mata kira da cancer, ba.a fada mata aimahin menene cancern ba, ba.a yi mata bayani sala sala ba sai fada mata da aka yi cewar yana dauke da kansa wace za.a yi masa aiki nan da kwana uku, za.a shiga da shi asibiti a gobe gobe, wato mijinta na fama da babar cuta ne ko me?
Na biyu: irin yanda mijinta ne ke dauke da cutar, ita bata sani ba, sai da aminiyarsa ta sani, sannan aminiyarsa ce ta zo ta fada mata, du kuwa da irin kusancin dake tsakanin mata da miji?

Na uku" irin yanda aminiyar mijinta ke kauce mata, irin yanda ta hango halin shiga uku kan rashin lafiar aminihta, irin yanda ya zabura ya nufeta ya dora kanta saman kirjinsa a gaban ita da take ainahin matarsa ta sunna wada ba zata nuna ranar da ya yi mata haka ba, ya rarashi aminiyarsa harma ya yi mata rakiya

Na hudu: sai a lokacin komai ya shiga dawi mata daki daki, ta kasance a dukan lamarin mu.azam tana zuwa ta biyu ne, wato Khadija ce fa fari!

Da wannan kallon cikin idon da ta yi masa na tsayin lokaci inda ya dora hannunsa na dama yana gyara mata dogon gashinta da ya bazu kan bed dinta kafin a hankali ya ce" ki yafe mini,

A haka ya ja mata bargo ya  lulubeta ya kashe mata fitilar dakin ya fita da nufin ya barta ta yi baci ko me?
A haka ta hangi ficewarsa wajen ainahin aminiyarsa , Aminiyarsa, aminiyarsa!

Abinda ya faru da Agaishat da Mu.azam da khadija kennan kafin a kawo Mu.azam asibiti bisa kulawar likitoci sa Agaishat da Khadija aka shiga saka masa magungunna ta hanyar karin ruwa da nanauyan magugunnan baci dan ya samu isashen hutu.....
Wannan kennan

Wardugu na karasawa gidansa ya fita ya nufi sashensa,

Yana budewa ya shiga da sabon cerrure din da ya canza ,
Yana shiga ya ga sabuwar mai aikin da ya dauka, wace a da babu namiji a yan aikin

bangarensa bisa umarnin walyn, aman a yanzu ya dauka ta gyara falon ta saka turaren ruwa mai kanshi ta ajiye abinci,

Ya san tana can bangaren da ya saka aka kaita wanda ke nesa da wajensa sosai dan haka ya zarce dakinsa

Sauri sauri ya yi wanka ya dauki jakarsa irin ta sojoji ya saka kananun kayansa na bukata da maclean da bros, da complet daya ,
Kananun kaya ya saka a jikinsa bakin dogon wando da bakar riga kafin yake dora costume (veste) saman rigar ya caje gashinsa ya gyara sosai ya fesa turare mai kanshi,

Jakar ya dauka da passport dinsa sai cart dinsa ta can wace a bankin can ya yita,

Fitowa ya yi yana duba dakin bai bar komai a jone ba?
Nan ya ga hajia Walyn tsaye, ta sha kwaliya mai kyau da birgewa tana masa murmushi ,

Kallo daya ya yi mata kafin ya kawar da fuskarsa ya juya ,
Yannayin hade fuskar da ya yi ya saka bata iya tankasa ba, tsoro ya hanata tambayarsa inda zai je duda ta sani ne fita ne zai yi ya dawo dan haka sai ta nemi waje ta mike tana jiran dawowarsa ta lalabe shi ya manta fushin da yake su shirya (to ka ji)!

Bai dauki mota ba, bai kuma bi ta kan kowa ba ya fice a kafarsa yana mai duba agogo

Taxi ya tsayar ya shiga ya fada masa aeroport,

Timiya

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

53

Timiya

A wannan ranar da kyar aka samu Anna ta koma ta zauna , shima sai da y'ayata suka rikice da koke koken dan girman Allah ta zauna a zana sunnan jaririn nan da aka samu sai su tafi, dan Gaishata ta kara kai da kasa yan uwanta da mahaifiyarta ba zasu tafi su duka su barta ba, kar a je su ki dawowa,
Gannin haka shima sarkin hankalinsa ya tashi dan haka harda shi a yan magiyar ta zauna a yi suna sai ya yi masu rakiya wajen wanda yake da alaka da gidan , wato sarkin agadez, shima rakia ya yi masa wani lokaci da suka je banban birnin, suna ganewa junna,

Haka dai Anna ta yarda ba dan hankalinta ya kwonta ba, sai dan tinawa da ta yi y'ayanta, idan ta tafi wajen wa zasu rabu su ji sanyi? Dama gashi ya fara tado maganar mutanen da suka kawo kudin aurensu sun waiwayo zasu zo a daura aure,
Wani murmushi ta yi mai ma.anoni da dama kafin take fita ta juye zuwan zafin dake tafasa Mariama ta kama suka kai bayi ta fito fuska a dan hade ta zanawa sirikin nata du abin bukata na wankan jego kan a yi gagawa a kawo kafin ruwan ya huce, (abinda da bata iya ko tsayuwa gata ga shi, Annar yanzu ba ruwanta ba wani shaka ko tsoro),
Da sauri ya amsa ya fita a gidan, inda Anna ta tube jaririn sai hada rai take na yannayin tsaftar gidan , du hankalinta da nutsuwarta ba a waje daya suke ba, sai ma da aka tashi neman turare abinka da batuba, kaf gidan Mariama ce kawai mai turare , itama irin na duran nan ne mai karfin tsiya, dan haka dole su Mariaman suka karbi makulin dakin Gaishata suka nufi gidan sarki dan ita tana da dan turaran wuta da na ruwa dan idan sarki ya je cikin birni yana bada kudi wajen mai dakin sarkin agadez q harhada masu tsumamun turaruka da sauran su,....

Wannan kennan

*Paris*

Jirgi na sauke shi ya kunna abin localisat@ din wayarsa ya shiga carte cikin iphone dinsa ya danna localisation din wayar Mu.azam, domin a kunne take kuma ya tabata nasama ba a kashe ba,

Taxi na ajiye shi kofar asibitin ya je wajen shiga ya nuna takardar shaidar waye shi, ya bada cikenken kwatancen wajen wanda ya zo da ranar da aka kawo shi da komai kafin ake barinsa shiga dan an rigaya an hana shiga, suma da suke tare da shi dan Khadija na ma.aikaciyar wajen ita da Mu.azam din,

Yana shiga ya fitar da wayar ya shiga bin kwatancen da ta dora masa saman screen dinsa har ya iso dakin da yake kwonce,

Da yake akoy katon madubin da ana tsayawa a ga marar lafia ta nan, sai Wardugu ya tsaya ya harde hannayensa ya zuba masu ido,
Khadija na nanade saman salaya carbinta ya fadi da alama tana ja baci ya kwasheta,
Agaishat na zaunen dai saman kujera kuma lokaci zuwa lokaci takan dan motsa kafarta idannuwanta a rufe har yanzu kamar mai baci, da dogon hijabinta mai ruwan jini,
Sai Mu.azam dake sheme saman gadon mararsa lafia, an aske kansa kwalkwal har kyali yake , wanda shi ya saka aka aske masa da kansa tun kafin a shiga aikinma, yana ajiye numfashi a hankali,
Idannuwansa ya rintse ya karasa wajen doguwar kujerar silbar da ya ganni a wajen ya zauna ya daga kansa sama yana jan carbin hannunsa ya tsurawa fitilar dakin ido

Yanda Wardugu ya ga rana haka ya ga dare, wajen karfe biyu ya ji motsi a dakin nasu wanda ya kyautata zaton alwalla aka dauro dan an jima ana dan motsi kafin ya ji shiru, a hankali ya leka nan ya ga Agaishat ce ta kai sujada kanta kasa tana adu.a, kawar da kansa ya yi da sauri ya koma ya zauna ya ci gaba da jan carbinsa, har karfe biyar ta yi
Ba kiran sallah zasu ji ba dan haka da agogo suke aiki , da lokaci ya yi zasu mike su yi sallah ne,
Zuwa ya yi ya samu ya dauro alwallah ya dawo,
Tapis ya dauka cikin jakarsa ya kebance kansa dan likitoci sun fara dan kai kawo ya tayar da sallarsa,
Ya jima yana rokom Allah ya sa a yi aikin nan lafia, yana gamawa ya mike dan shida ta gota ya dauki jakarsa ya dan kwonkwasa dakin

Agaishat dake kusa da kofar ta mike ta bude ,
Gabanta ne ta ji ya wani tsintsinke ya fadi a lokaci guda,
Kanta ta daga kafin take iya kallon fuskarsa, wanda shima ya dan duko da kansa ya sauke idannuwansa kan fuskarta,
Ba zaka iya karantar yannayin fa yake ciki ba, fuskarsa ba yabo ba falasa,
Shigowa ya yi ya mayar da kofar ya rufe,
Fuskarta da idannuwanta sun kumbura, hakan na nuni da ta yi kuka,
Kawar da dubansa ya yi daga kanta ya mayar kan Khadiha da ta mike itama tana dubansa,
Fuskarta itama ta bumbura ta yi jajajir,
Bai amsa gaisuwar da suke masa ba sai zarxewa da ya yi wajen Mu.azam,

Kujerar dake kusa da gadonsa ya ja a hankali ya zauna yana kallonsa, karfe bakwai saura yan

mintuna  Mu.azam ya farka,
Farkawarma ba can bace, ya fan buda idannuwansa da sukai masa wani irin nauyi ne,
A hankali ya ga Wardugu dake zaune ya rike hannunsa na dama,
Allah ya bashi ikon yin murmushi yana duban Wardugu,
Magana yake a hankai wanda Wardugu ya kunnayensa aman bai ji komai ba dan haka ya nuna masa da ya yi shiru,

Da idannuwansa ya nuna ya yi shirun inda ya lumshe idannuwan sai ga hawaye sun fito daga cikin idannuwan nasa,
Docter Ce ta shigo da farar riga irin ta likitoci tare da nurse da uku da gadon tura marar lafia

Wani irin mikewa Khadija ta yi ta zuba masu ido inda docter ta girgiza mata kai, haka ne daman idan kana son gannin  rikicewa sai idan ciwo ya taba likita, yakan fice a hayacinsa ya zama wani kala, yakan rude komai kankantar ciwo bale mai tsanani,
Hakan ce ta faru da khadija, domin a lokaci daya ta rikice ana nuna mata kar ta yi gabansa aman ina bata san lokacin da ta dora hannayenta duka biyu saman kanta ta fashe da kuka , da sauri Wardugu ya juyo ya cire gilas din idannuwansa domin har ya mana dan baya so a san halin da yake ciki,,

Da sauri Docter ta kama hannunta suka fice inda wasu likitocin maza biyu suka shiga kokarin daukansa suka dora saman dayan bed din

A hankali Wardugu ya saka hannunsa cikin sumar kansa ya shiga yamutsawa inda gaba daya jijiyoyin jikinsa suka mike tsabar yana cikin tashin hankali

Agaishat dake tsaye sai zarar ido take gannin yanda Khadija ta fashe da kuka aka fita da ita, da yanda aka dauki Mu.azam ranga ranga aka dora saman wani gado, du fuskokin likitocin a hade irin sun ci kalar serius din nan sai ta rikice,
Tana ta zaro ido tana kallon yanda suka saka masa oxygen suka gyarashi da kyau saman gadon ,
Sai bayan sun gama gyara shi wani likita ya zo da takarda a hannunsa cikin file , da yaren faransanci ya ce" Chef, (sire), docter Khadija tace Nan zan samu Wardugu?

Wardugu dake tsaye shima yana kallon yanda aka yiwa amininsa, nan zuciyarsa ta kara tsorata da girman ikon ubangiji, kaga mutun yanzu yanzu ka zama tamkar gawa ko gawar,

Da kai ya amsa masa cewa shi ne, dan haka likitan ya mika masa wata takarda kafin yake kara masa bayani kamar haka" Docter Mu.azam ya bar maganar cewa idan za.a shiga aikinsa a baka wannan takarda ka saka hannu, takardar na nufin idan Har Allah bai yi ya fito kalau ba kai za.a ba gawarsa ba likita zata birne shi ba,

Wani irin sarawa kan Wardugu ya yi, Wardugu dai soja ne, sojan ma baba, wanda ya shiga gwagwarmaya da manyan yan ta.ada, wanda ya kwana cikin rami, wanda ya shiga hatsari kala

daban daban na rayuwar yau da kulun, yau gashi gaban ikon mai duka, yana ji yana gani ya karbi biro ya saka hannun idan amininsa ya mutu a dakin tiyata a bashi gawarsa,

Yana saka hannun suka karba suka juya da Mu.azam dake sheme tamkar gawa,

A hankali wardugu ya kai wajen garu ya silale dan baki daya kafafuwansa rawa suke masa,

Agaishat da ta bi su da kallo sun fice mata da miji ta juyo da sauri wajen Wardugu ta karasa ta duka daidai inda yake yana kallon waje guda , murya a rikice ta ce" Ina zasu kai shi? Ina zasu kai min shi? Ina zasu kai min mijina? Ya mutu ne? Me ya sa suka tafi da shi? Wayyo Allahna, Wayo Allahna ,
Ta fada tana karasa zubewa kasan ta fashe da wani irin kukan da ya jima yana cin zuciyarta,

Wardugu dake kallonta ya lumshe idannuwansa kafin yake budewa,
Hannunsa dake rawa ya mika ya janyo hannunta kusa da shi sosai,
Murya can kasan makoshi ya ce" ba mutuwa ya yi ba Agaishat, aikin ne aka shiga da shi, ki daina kukan nan na tuba ki rufa min asiri ki yi shiru👏🏻,

Maimakun ta yi shirun sai kara kukanta da ta yi tana ta rike hannunsa tana kiran ya kaita wajensa, ya kaita ta ganshi, kar ya mutu ya barta, tana son sa!

Ido kawai ya lumshe ya yi shiru ya damke hannun nata, bai kuma yi mata magana ba sai sauraron sambatunta da yake tamkar ta zauce ,

Wasa wasa awa daya, awa biyu  awa uku, awa hudu, awa biyar, awa shida ba.a fitar da Mu.azam ba, daga dakin sun canza waje ya fi a kirga inda karshe suka dangana dan nesa da dakin tiyatar kusa da Khadija dake zaune tana wani irin numfashi tamkar mai athsma, da kyar aka barsu suka tsaya nan din sai da aka kusan kwasar rashin mutunci da Wardugu kafin masu tsaron asibitin su bar shi,

Agaishat zaune take jikinta hade da garu itama tana rawar sanyi, zazabi ne jikinta inda Wardugu ya kasa zaune ya kasa tsaye sai kai kawo yake hankalinsa ba a kololuwar tashe.

Suna haka baban likitan asibitin ya fara fitowa, nasara ne mai sunna,Roger , shi ya jagoranci aikin inda likitoci kamarsa biyar suka taya shi,

Khadija ce ta fara mikewa ta nufe shi jikinta na rawa baki daya,

Daidai nan wasu uku suka fito suma suka tsaya kusan docter Roger,

Tambaya ya yi cewar" ina Wardugu?

Wardugu da ya tsaya yana hangensu ya ji gabansa ya fadi, a hankali ya shiga takowa inda wata

zazafar zufa ke karyo masa, du takunsa guda daidai da mutuwar tunaninsa yake har ya karaso kusa da likitocin,

Likitan ya dago kansa cikin wani yannayi ya ce""".......

😳

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

5️⃣4️⃣

Likitan ya dago kansa cikin wani yannayi ya dubi Wardugu kafin ya dubi Khadija, ya ce" mun fito aiki, za.a fitar da shi a saka shi dakin observation na sati biyu, komai nasa zai dawo hannunmu na tsayin wannan lokacin, cinsa , tsaftarsa, komansa, tsakaninku da shi sai dai ku ringa hango shi ta jikin madubin dake makale da dakin, ni kadai zan iya shiga in daidaita komai in fito, za.a baku takardar magani da kuma irin abincin da za.a ringa saka masa ta mesa ta hancinsa, fatan ka fahimta idan baka gane wani abin ba sai ka tambaye ni ko ka tambayi matar tasa *Docter Khadija* ai ta san komai itama zata kara maku haske,

A hankali ya karkata dubansa wajen Khadija inda Docter Rogger ya raba ya fice, sauran docters din suka shiga bata hannu sunai mata murnar an samu nasarar aikin ciki sai fatan ya farka daga dogon barcin da aka luluka shi wanda farkawar shi ne zai shaida aiki ya yi ko bai yi ba wanda a kala zai iya kai sati biyun idan komai ya je daidai ko sama da haka abinda ba.a fata , sannan

aka bata abinda aka cire a cikin kan , du suna yi suna nuna itace matarsa suna tayata murna wardugu na tsaye a wajen kuma da yarwn French ne ba abinda baya ji

Dubanta dai kawai yake uwa ya samu tv, ita kuwa ta ki yarda su hada ido da shi ko su samu zama daga ita sai shi,
Tana gannin likitocin samu tafi ta dan dubo shi a yannayin daburce ta ce" zan zan je na karbo takardun,

Bai bata amsa ba har ta bacewa ganninsa tana sauri tamkar zata fadi,

Juyawa ya yi yana kallon Agaishat da itama tunda suka nufi wajen likitocin take kallon su, bata san abinda ake ciki ba, bata iya yaren su ba, sai ta zama bakon Tv, dan dukan idannuwanta ta bude tana bin kowa da kallo ko zata fahimci wani abin,

Yana nan tsaye yana hangenta yana tunanin me zai ce mata Khadija ta dawo ,
Kanta take dan sosawa irin na mai laifi wand Wardugu ya gama karantarta watsi ne ya yi da lamarin da baya son shiga abinda bai shafe shi ba,

Rakardun ta mika masa ta shiga masa bayani kamar haka" kasancewarsa ma.aikacin asibitin nan wanda suka dauka da kansu yake karkashinsu zai biya rabin kudin aikin wanda ya kama millions 3 da dari takwas, sai riko gado kulawa shima tabin kudin ne ya kama jika dari bakwai namu na cefa,
Sai takardun magungunna da za.a ringa karbo masa a nan cikin pharmacy na asibitin shima yanzu zan je na karbo takardar da zata bamu damar biyan rabin kudadan magungunnan du zamuna karbowa ,

Sai da ta gama yi masa bayannin du yana karbar takardun kafin take miko masa carte din Mu.azam da kuma tata ta banki ta ce" ga carte din mu na banki, ga takarda mai dauke da code din mu wato reference din mu, idan aka hada na mu biyun na tabata kudin zasu isa har a salame mu,

Da yake du bayannan nan da take idannuwanta basa kallonsa dan mugun kwarjini yake mata sai da ta ji bai karbi takardar da carte din ba ta dago da dubanta a hankali ta dube shi,
Fuskarsa ya yatsina ya juya ya barta nan tsaye da takardar da kuma carte din, aman ya karbi baki daya na asibiti da za.a biya, na magungunnan,

Tana nan tsaye tana kallon sa ya fice ya tafi infa Agaishat ta bishi da kallo,

Kanta ta daga sama ta lumshe idannuwanta, a yau ta ji wani irin takaicin da bata ji ba na rashin karatun zamani da basu samu ba, ta zama tamkar kurma marar wayo a cikin mutane, bata gane yaren su , sun zame mata sababin mutane sun zame mata sabin halitu, gashi wanda ya kawota kasar take zaune dominsa kansa ake bayani aman bata san komai ba, yau kam ta yarda da maganar Ayya inda take ce mata" Agaishat, ban ki maganar baba tsofo fannin karatun zamani

ba, aman ina son ki sani a rayuwa komai yana da anfani, karatun adini, karatun bokon ne , neman sani kan abubuwa ne, shi dan adam ana so ya zama mai yawan bincike kan lamarin zaman yau da gobe, neman ilimi ba laifi bane, jahilci baban ciwo ne wanda bashi da magani, idan aka ce jahilci kuwa ba ana nufin mutun jahili ba, ana nufin abinda baka sani ba yake a cikin duhu gareka .

Idannuwanta ta dan bude gannin Khadija ta koma wajenta na da ta zauna, bata ko nemi zuwa wajen da Agaishat take ba bare ta kwatanta mata wani abin,
Tabas hasashen Agaishat ya gama tabata a kan Khadijar da mijinta,
Dan ka fito daga birni, baka yi karatun boko ba, ba ana nufin kai din wawa sakarai bane, kana hankalce da komai, hasalima ka fi wasu yan birnin lura da gane lamura a kallo kawai bama sai an fada maka ba,
Ji ta yi an shiga hakkinta da yawa, ji ta yi ba.a mata adalci ba, zuciyarta ke ingizata da ta mike ta tarar da khadijan ta fada mata ta gane soyaya suke da mijinta, aman tana so ta fada mata halin da yake ciki, ko ba komai a tunaninta kusancinta da shi zai fi da kowa duba da itace matarsa, wada ya dace ta zama sirinsa, aman sai ya kasance itace wace bata san komai game da shi ba, wata zuciyar ta ce" ki ce da ita me? Wato ke mai hayagaga ko? To dan ya mayar da ke baya cikin komai nasa sai me? Me kika sani , ina kika sani, me zaki iya yi masa a cikin lamarin? Ke ko a kauye kin zama koma baya cikin y'ayan Ba bale a birni, birni mai abin mamaki, birni mai mota mai jirgi mai kalolin fata? Birni mai madafi a daki? Birni mai tv mai abin allo? Ke kama kanki a hakama ya isa, ki saka ido ki yi adu.a, ki godewa Allah hakama ai ci gaba ne!

Idannuwanta ta yiwa wal wal wal irin ta harari kantan nan, ta dafe gaban goshinta da hannunta na hagu sannan ta dafe daidai zuciyarta da hannunta na dama, ji take zuciyarta na doka mata da sauri, takan shiga irin yannayin nan idan tana cikin yannayi na tsoro,

Ya kai minti talatin da fita kafin yake dawowa shi da wasu mutane biyu , dayan ya girmanta dayan kuwa shima saurayi ne mai jini a jika,
Su duka hannayensu da wasu manyan takardu masu dauke da tambarin asibitin wa.inda a cikinsu ne aka zuba magungunnan da take a way,

Karba ya ringa yi yana ajiyewa kusa da khadija ba tare da ya yi mata magana ba,
Sai da ya gama ajiye komai ya dawo wajensu suka yi magana ,
Khadija dai na kallon su inda Agaishat ta kawar da dubanta daga bangaren kowa kawai ta sada kanta tana mai dana carbinta,

Sara masa suka yi kafin su yi musabaha , kys din motar saurayin ya mikawa Wardugu yana mai nuni da takardun motar da komai a ciki kafin su juya, ashe yaransa ne dake zaune a kasar da sunnan Niger.

Kys din ya saka a aljihun wandonsa, ya dawo wajen Khadija dake kallonsa tana sarawa girmansa harma ya fi yanda Mu.azam ke fada mata, lale Wardugu ya nema kuma ya samu, rikeken hamshaki ne da baya nunawa ko yinkaho sai dai ka dube shi kawai ka gane nitsatsen

hamshaki ne,

Takardun shaidar ya biya komai ya mika mata, a gajarce a kuma dunkule ya ce" an gama da wannan , sai na gaba.

Take a way din ya duka ya dauki takarda biyu ya bar mata guda ya juya ya nufi wajen Agaishat,

Yana zuwa Ya tsaya ya ce" mu je,

Maganarsa kawai ta ji saman kanta, dan haka ta dago da sauri, sai ganninsa ta yi saman kanta fuskarnan a hade,
Mu je? Mu je ina? An salame mu ne? To ina Mu.azam din?
Tambayoyin da ta yi ta jerawan kanta kennan ,
Gannin bafa mai amsa mata gareta ba sai ta mike tana leken Khadija dake kallon su , tana so ta yi mata magana aman Wardugu ya tsare wajen dama gidan baki daya, dan haka ta juya sumui sumui ta fara fita a wajen kafin yake daga kafa ya shiga gabanta

Sai da suka fito harabar asibitin wajen motocin dake parke ya ciro ky din ya danna dan command din dan gannin wacece motar?

Motar da ta yi kara dan amsa kiran da akai mata ya tsurawa ido yana dan shafa gefen fuskarsa, aman lale comandan Munkaila ya raina masa wayo, wannan motar ta samari wanda suma idan zasu shan iska suke hawa ne ya  bashi? Gaske da ya tambayeshi marque dinta ya ki fadi ,

Kansa ya girgiza, shi ba shiba yake ji, yarinyar nan zata iya zama cikinta? Bata da sama , gaba daya saman a bude yake gashi garin ana yannayi na sanyi ,
Zuwa ya yi ya bude ya shiga inda ya waiwayo gannin Agaishat bata biyo  bayansa ba,
Da ido ya yi mata nuni me take jira? Dan haka ta karaso tana kallon inda zata bude ta shiga, ita bata taba gannin kalar mitar bama dan ba wani yawo aka kaita ba, yar fitar da suka yi daga gida zuwa asibiti kuwa hankalinta a tashe batama kalli garin ba bale ta san me ke zuwa da zowa,
Bude mata ya yi daga ciki ta shiga ta zauna tana gyara hijabinta da kyau,

Tayar da motar ya yi ya dauki hanyar gidan Mu.azam dan ya san gidan kuma bai ji yace da shi ya kaura daga nan ba,

Ita dai kanta a kasa dan ji take iska ta yi mata yawa, aman da ta sada kan sai ta ji sauki sauki,
Tuki wardugu yake yana tunanin abubuwa da yawa da ya ganni kan zuwansa zuwa yanzu,

Ko yanzu sai da ya koma wajen docter Rogger ya nuna masa komai tsarin a tsanake ya kwatanta masa inda za.a mayar da shi da kuma bashi takardar da ko a wani lokaci ya zo zai iya shiga kansa tsaye

Yana tunanin nan har ya karaso kofar gidan nasu,

Fita ya yi itama ta fito tana biye da shi ya dana ya bude suka shiga,
Ita dai kallonsa take har ya je ya daga wani katon peau na flower ya dauko ky ya zo ya bude mata,

Tsaye ya yi har ta zo ta shiga, sai kuma ya mika mata take a way din guda wato rabonta ya juya da niyar tafia,

Agaishat ta yi kundunbala da tsoronta da komai ta ce" shi fa?

Birki ya ja, a hankali ya dan juyo yana mai cire gilas din da ya mayar  ya yi mata kallo daya jal,
Mayar da gilas din ya yi ya saka ya juya bai bata amsa ba ya fice a gidan,

Abincin ta saki nan ta juya da sauri ta karasa wajen kujera ta zauna kasa ta hada kanta da gwuiwarta ta fashe da kuka, da yaren buzance take fadin" wayo Annata, wayo baba sofona, wayo Ayyata ku zo ku dauke ni, bana so, bana son auren, shi auren haka yake? Wayo zuciyana ciwo yake,

Bata ji motsi ba, sai karan ajiye kys da ta ji dan haka ta dago a tsorace
Shi ta ganni da abincin nata ,
Bai ce da ita komai ba ya je ya dauko plat da spoon ya darwaye ya zo ya bude ya fitar da abincin ya bude ya juye cikin plat din,
Zuwa ya yi inda take zaune shima ya zauna ya ajiye mata abincin kusa da ita, sai da ya yi da gaske kafin ya iya fadin" ki yi hakuri, an masa aikin kuma in sha Allah zai warke ya dawo gida,

To ka kai ni wajen shi Wardugu , Agaishat ta fada tana hade hannayenta,

Wannan karron kam ba kallo daya ya yi mata ba, tsai ya yi da idannuwansa kan fuskarta,
Hannunsa ya sa ya shafa goshinsa da kyau kafin ya ce" ki yi hakuri zai dawo kin ji?

Da kai ta amsa shi , ya nuna mata abincin,

Dauka ta yi ta shiga ci a hankali tamkar tana cin magani,
Wardugu ya yi ajiyar zuciya har ta gama ya mike ya ce da ita" zo ki rufe ba.a barin gida a bude kin ji? Idan kin rufe ki samu ki yi wanka ki huta zan dawo na kai ki ki ga Mu.azam,

Da to ta amsa shi da alamar murna, dan kam so take ta ganshi, ta yi missing dinsa fiye da tunanin mai karatu a dan lokacin da bata ganshi ba, sabo tirken wawa, Agaishat kam ta kamu da son mijinta, tana son abinta,

Haka Wardugu ya fice a gidan Agaishat ta rufe ta cire hijabinta ta nufi dakinta,

Tana shiga ta je wajen gadonta ta dauke matasan kan dake ajiye ta yaye abin shinfidar ,

Nan takarda ta fado wace in ba zata manta ba tun lokacin da Mu.azam ya raka Khadija ya dawo a lokacin da ya janyo abin rufa zai rufawa Agaishat ya saka mata kasan matashinta wanda ya san ta ganni , bayan ya saka din ne ya dubeta ya furta kalmar "Ki yafe min",

Gannin takardar ta fado ne ta je ta dauke duda ba wata baba bace ta kai wajen shafe shafenta ta ajiye tana fadin" bawan Allah ya mance *Takardarsa* ko ajiya ne ya bani? Bara na kara kilaceta,
Dan haka ta dauke daga nan ta kai cikin akwatinta ta saka ta dawo ta canza zannin gadon ta canza na jikin pilow din ta kwashe wa.infa ta cirw ta yi bayi dan wankewa, dan kuwa sam bata wani kai kaya wajen tara kayan dati, ita ke wanke abinta da kanta.

*Takarda kuma?*

Yawan comment samun wani page ehe🙄🙄🙄🙄

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

Wardugu na fita hotel din da aka kama masa ya nufa,
Yana zuwa ya fiya ya baiwa mai gyara mota ky ya yi gaba ba tare da ya dau komai ba,
Mai gyara motar nan ya gama gyarawa ya ciro komai a motar ya mikawa masu shigar da kaya hotel din,
Sai fa aka yi scaning din jakar kafin a dora saman abin turawa a nufi guichet, nan suka fada masa dakin da Wardugu ya sauka ya tafi kai masa

Daidai wannan lokacin Wardugu na zaune ya lumshe idannuwansa saman kujerar dakin hotel din fara kar ,

Mikewa ya yi ya bude ya karbi jakar , nan wanda ya haudo masa kayan ya mika masa wani album mai dauke da hotunnan yan mata kala daban daban , na kasashe daban daban ciki harda hausa girls, cikin shiga na tsiraici suna tala , idan mutun na so zai zabi wace ta yi masa da farashinta da numberta ya danna kira ta amsa kiransa (🙁)

Jefar da album din ya yi ya nufi bayi bayan ya danna kira katon butik din hotel din ya yi order kaya da siz dinsa da coler

Wanka ya yi kamar zai canza fata dan rabonsa da yi tun jiya da dare,
Ya dauro alwallah dan gabatar da sallar magarib

A nitse ya kamala komai ya saka kayan da aka kawo masa kannanun kaya ne masu tsari na manyan mutane, kalar baki ne dai sai chemise din ta ciki fara kar da cravate .
Agogo ya daura a tsintsiyar hannunsa ya fesa turare ya dauki katuwar wayarsa dan sai a lokacinma ya kula da waya,
Ayya ya fara kira , wada kamar jira take ta daga, tun kafin su gaisa ta jejefo masa tambayoyi,

Murmushi ya yi ya kora mata bayani cikin girmamawa da shagwaba irin na dan shagwaba a wajen mamansa,

Murmushi ta saki jin Alhamdulilah, ta yi adu.ar Allah ya tashe shi lafia, ta ce" ya yarinyata? Ta warware? Ta kara jiki? Ta yi kyau? Tana da wani abu ne? Hankalinta kwonce? Tana samun kulawa ne?

Tsai ya yi ya ciro wayar daga kunnensa ya tsurawa sunnan ido, Ayya, Ayya, kai ya girgiza ya mayar a kunnensa ya ce" idan na hadu da ita sai na baki ita Ayya ku yi maganar ko?

Ayya ta ce" kai wardugu bana son wulakanci , an gaya maka bama waya ne? Muna waya da ita aman kulun sai tace wai lafiarta kalau komai kalau, aman yanzu kai da ka je ba sai ka fada mani ba? Tana da wani abu ne?

Wardugu ya ce" wai menene wani Abu kuma?

Ayya ta ce" kai, baka san wani abu ba? Ina nufin an samu karuwa ne?

Kansa ya dafe , shi fa bai san me take nufi ba, dan haka ya ce" Ayya zan yi kiran ki , zan je wajen Mu.azam din,

Bai jira amsarta ba ya kashe kiran yana sauke ajiyar zuciya, toh shi yaushe zai tsaya kallon ta yi kyau ko wani abin? Shi inama ruwansa da kurewa matar mutane kallo🙄.

Kira a whatsupp masu yawa inda yarinyar nan wato *BASMA* kiranta ya fi a kirga, ga na Walyn da messages dayawa, ga na abokan aiki da mutanen arziki,
Wa.inda ya dace ya maidawa ya shiga ya maidawa, wa.inda ba lale sai a lokacin zai maida masu ba kuwa ya bari sai ya zauna ya jefa wayar a aljihu ya fice

Garin dare ne aman kamar rana, haske ne ko.ina, wasu a lokacinma suke dawowa daga gudun motsa jiki, wasu na yawon kafa da iyalansu, kowa dai na sha.aninsa ba wanda ke kula da sabgar wani,

Yana tuki har ya karaso gidan Mu.azam

Agaishat ta sala wankanta ta saka wata doguwar rigar sai dai bata kai har kasa ba da dogon wando a kasan rigar ya rike kafarta tam dan rif ne da shi daga can kasa wajen idon kafa,
Tana zaune a falo suna vidio Call da Ayyanta, sosai Ayya ke yi mata hira dan sakata nishadi inda ta maida hankalinta har tana murmusawa sosai tana tambayar ayya abin tambaya tana bata amsa daidai labarinsu

A haka karaurawar dakin ta shaida da mutun wato ana son shigowa,

Mikewa ta yi tana warware dan kwalin dake daure a kanta ta yana shi a fuskarta ta je ta danna wajen budewa dakin ya bude,

Kallo daya ya yi mata ya ce " mu je,

Da wani dan gudu gudu  ta juya da wayar tana fadin" Ayya, ya Wardugu ne zamu tafi wajen Mu.azan din,

Da sauri ya juyar da kansa daga kanta, irin fizgar jikinta da ta yi bai kai idannuwansa da gangan ba sai akasi da aka samu yana tsaye a wajen,
Astagafari ya shiga ja yana zabgawa idannuwansa fada, fitama ya yi a gidan ya je wajen motar ya zauna yana jiranta har ta fito da lulubeben hijab dinta mai ruwan blue da takalmi plat blue sai carbinta, ko wayar bata dauko ba ta barta a gida,

Suna zuwa suka tarar da Khadija tsaye wajen da ake hangen Mu.azam din, ta jinginar da kanta jikin madubin , tana kallon wajen wanda basu san adadin lokacin da ta dauka a haka ba, basuma san ko ta je gida ta dawo ba, su dai sun tarar da ita,

Jin motsinsu ya fargar da ita zuwansu, juyowa ta yi gare su ta sakar masu murmushi kafin murya a sanyaye ta ce" sannun ku da zuwa,

Agaishat ta karasa inda take tsaye ta ce" ina yini, ya mai jiki?

Khadija ta waiwaya eajen madubin ta waiwayo ta sauke ajiyar zuciya ta ce" Alhamdulilah,

Wardugu kam bai amsa ba ya zarce wajen madubin ta tsaya yana kallon yanda aka dadaura masa na.urori da mai taimakawa lumfashinsa, da mai aiki jikin bugun zuciyarsa, da wada in ya motsa zata yi kara, da karin ruwan dake jone , da ledar fitsari a ajiye gefe wace idan ta cika ake tsiyayewa, da fo kasan bed din,
A hankali Agaishat ta karaso inda yake tsaye itama itama ta tsaya ta kai dubanta inda yake kallo,

Idannuwanta ta zaro tana duban Mu.azan da tsoro karara a fuskarta, ai kuwa me zata yi in ba kuka ba? Ta aniya fashe masu da kuka tana nuna yanda Mu.azam yake kwonce,

Hankali tashe Wardugu ya dubeta, nan da nan ya turbune fuska tamkar bai san wata halita daria ba, rai bace ya ce" la ferme tu veut? (Chut up nah?!) ,
Ki rufe min bakin ki !

Ba wani da ihu ya yi maganar ba, sai dai a kausashe ya yita wanda dole ka yi shiru ko baka shirya ba,

Tsorata ta kara yi ta shiga ja da baya baya ,
Khadija bata taba jin Matar Mu.azam ta bata tausayi sai yau ba, dan haka ta rike hannunta ta baya ta jata suka fice a wajen,

Kuka Agaishat take tana shasheka inda du ta tsorata da komai,
A hankali Khadija ta zaunar da ita a balbalin wajen kusa da fulawowi,

Da tsinkakiyar hausarta take son rarashin Agaishat dan haka ta ce" ki yi hakuri, zai samu lafia, ki bar kuka kin ji?

Agaishat dake dubanta zuru bata iya amsara ba, dan haka Khadija ta jimke hannayenta , da kanta ta yi mata alamar ta kwontar da hankalinta sannan da dayan hannun ta yi mata nuni da sama cewar Allah na nan,

Ajiyar zuciya ta sauke ta sada kanta,

Wardugu ne ya karaso wajen ,
Ganninsa ya saka khadija ta mike ta yi masu salama ta koma ciki,

Wardugu ya zauna yana lura da yanda Agaishat ke dan ja baya, tsorata take son yi da shi baki daya dan haka ya zauna yana facing dinta,

A hankali ya ce" menene na kukan? Bakya so ki rasa mijin ki? Bakya so ya mutu?

Agaishat ta dube shi da sauri, bata san lokacin da ta ce" Wardugu,,
Sai kuma ta sada kanta kasa, a hankali ta ce" bana so ya mutu, *ina son sa*,

Shiru ne ya biyo baya,
Jin shirun ya yi yawa ya saka ta dago a hankali, dan ta ji kunyar fadin gatsai gatsai tana son mijinta, sai dai itafa iya gaskiyarta kennan, duda da alama shi hankalinsa rabe yake gida biyu, zata zauna da shi, to meye ma fan ya so watanta? Ai ba ita kadai ce mace ba, dan haka ita ba wani zata ja ba, yo irin rayuwar da ta gani a gidansu da Ba ke sheka abinda ya ga dama Anna ta bi shi ita mema akai mata? Ba zata zama mai raki da rashin godiyar Allah ba,

Wardugu dake zaune tamkar mutun mutuni gannij zata dube shi ya saka shi mikewa da sauri ya yi gaba,

Da sauri saurin itama ta bi shi dan ta fara karantar halayensa , yakan yi magana da ido, ko da jikinsa.

*Timiya*

Gari mai gawo, Timiya garin sarki ne,

Yau aka zana sunnan Gimbiyar garin Timiya, sarauniyar birnin zuciyar sarki wato Gaishata, Taron sunnan da ya tara mutanensa na arziki, garin ya dauki jama.a ya cika makil inda aka soke amale biyar aka yanka aka shiga gashi da wasu wasu aka kai wajen madafa inda mata ke tone alkabut da gurasa na kasan kasa suka aza miya,

Cuwa cuwa ake wanda sai ka leka bangaren Amaryar jego zata ci karo da mamaki,
Wato amarya ce hakimce cikin shiga ta alfarma sabon turkudi mai fari da maroon, ta sha sarkar zinari da amarwaraye, hakama yan uwanta sai kai kawo suke sunna tarbar baki inda dakinta ya sha sababin kayan daki da gado sabo dal irin na yan birni ga inji ya bada wuta panka na sheko masu sanyi, jariri a lulube a wajen tsohuwa mai kulawa da mai jego,
Kadan kadan zaka ga Mariama ko Fatimata sun duko wajen bakinta ta fada masu abin tambaya ko na shawara, cike da aji su fice su nufi gidan da sarki ya maido su kafin a gama zanen sunna su daga wajen Anna dake zaune cikin runfar kara mai sanyi saman tabarmar leda ta sha jan kunshi a kafafuwanta da hannayenta, ta nada lifaya ja, idannuwanta dauke da kwali shar, sai

zobuna da awarwaraye na zinari da ta saka itama uwar mai jego ta kuwa hakimce abinta , su zo su fadi maganar yarta ta fari ta kuwa mike idan na mikewa ne ta yi iya yinta dan gannin ta daidaita komai, idan sako ne ta tura daga inda rake cike da aji da sannin abinda take yi a je a yo a zo har yama ta yi aka shigo da kyautar kayan jariri da na uwarsa daga mai girma sarkin garin timiya....

Mai karatu zai yi tambayar ina ta samu kudade haka na sayen zinari?
*Ba* na ajiyar kudadansa idan ya samu a cikin gidansa, kuma Anna itace kadai ta san ma.adannin kudin aman koda yinwa zata kashe su ba zata iya tabawa ba dan tsabar tsoron ransa ya bace,
Bayan warwaren kulin da ya kula mata, ya kasance su har yanzu basu da labarin inda yake dan haka ta je da kanta ta kwaso baki daya kudaden da suka rage wanda bai masu mugun kashewa ba ta zo ta samu sarki a lokacin da suna ya matso ta bashi ta zana masa bukatarta baki daya yayanta harda Agaishat wace kudin aurenta ne danma sun tafi da sadakinta, ta saka a yo masu sarkar zinari da awarwaraye, ta saka a kawo masu turaren wuta na arziki da na feshe na ruwa masu kanshi, ta saka a kawowa yan matan kayan kwaliya da lale na hausa da sauransu, ta saka a yo masu siyayar kayan jiki ba wasu masu yawa ba aman masu kyau da tsada da ma.ana, nan ta kawo maganar kayan dakin Gaishata inda sarki ya nuna a bari yana da niyar canza masu su duka matan nasa, duda haka ta nemi alfarma ta kara wasu abubuwan irin zannin shinfida na gado, kayan jere na zamani, karshe dai kudin da suka rage a hannunta basu fi million daya ba inda Mariama ta kawo mata ta wajen Ba da ya basu ta hada ta rike a wajenta da niyar zasu rike saboda hanya.

Bayan zanen suna da kwana biyu,

Zaune suke suna kallon yanda Anna ke gyara miya , suna yi suna hirarsu a nitse ba wani hayaniya ko rawar kai,
Gashi gidan ya bade da sanyayan kanshin turaran wuta

Dogari ne ya yi salama daga kofa,
Mariama ta leka nan yake shaida mata sakon sarki na yana son magana da Sirikarsa

Kimtsawa Anna ta yi, ta saka hijab sai baza kanshi take ta nufi gidan sarki

Tana zuwa ta karasa bangaren y'arta ba wani dari dari ko labe labe irin na da,

Sun jima suna hira tsakanin Anna da gaishata kafin sarki yake karasowa,

Kan maganar tafiarsu ne, Sarki ya shaida masu in sha Allah zasu je agadez a jibi, su gana da sarkin agadez sai ya sada su da *Gukunnin*

Amsawa Anna ta yi , sannan suka kara daidaita maganar inda dole dai da Gaishata za.a tafi dan ta kafe , yanzu kuwa Anna ta zama mai son y'ayanta, tausayinsu na mamaye zuciyarta,

takan yi tir da wannan rayuwa, sai kuma ta godewa Allah da ya  dawo da ita hanyacinta tun yanzu.

*After 2 weeks*
Paris

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

5️⃣6️⃣

Barka da juma.a

A kwanakin nan 14 da aka yi ,duka kaf Wardugu na nan , ba.inda ya je, yana tsaye kan lamarin aminínsa, du wani abinda za.a fitar da kudi komai nauyinsu yakan karba ya je ya dawo da abinda aka bukata,
Ya kasance du idan lokacin cin abinci ya yi zai fita ya shigo masu kowa da nasa ci uku a yini,
Yakan yi jim idan ya ga sun yi jigum jigum ya ce da su" zai tashi, ku mu yi masa adu.a

Wannan abubuwan ya saka Khadija ta mugun zube kasa, wato ta ga ita ba komai bace a wajen son kyautatawa Mu.azam, wani irin girman wardugu da kwarjini, da kunyarsa suka karu a wajenta,

Ya kasance a yanzu ta yarda ba ita ta fi kowa son Mu.azam ba, sannan ta dan ja baya in dai Agaishat na wajen takan rage yawan leka wajen da Mu.azam din yake ma, sai dai idan bata nan kuma zata je ta tsurawa wajen ido,

Agaishat kanta da ya kasance kulun da sasafe zai zo ya dauketa su je asibiti, idan abinci zai je siya sai ta fadi wanda take iya ci, idan rana ta yi ya mayar da ita gida kuma sai bayan magariba ya daukota, duda ba wani hira ke hada su ba, sai kusancinsu ya karu, shakuwa ta shiga tsakaninsu, wanda hakan ba karamin illah ne ga dayansu ba,
Idan ya kawo abinci bata ci ba kuwa zai kama dago kansa jefi jefi yana duban abincin ya dubeta ya kawar da kansa, idan har ya ga lokacin cin abincin zai shige bata ci ba zai mike daga inda yake ya zo ya bude ya ajiye mata ba tare da yace da ita kala ba ya koma mazauninsa,
Kudi sun ji jiki, wai danma wasu abubuwan rabi yake biya albarkacin yana ma.aikacin asibitin, sannan likitocin nan tsaye suke kansa, baban likitan kansa ke kula da komai na Mu.azam har zuwa wannan rana inda suke tsaye a kofar su duka suna hangen likitoci uku dake tsaye kansa,
Tunda safe ya dace ya motsa, aman shiru ba alamu,
Wannan zuwansu na hudu ne wanda ya kama karfe shida daidai aman shiru Mu.azam bai motsa ba,
Zuciyoyi sun karaya, hankali ya tashi, a tsaye suke cir da kafafuwansa inda cikinsu ba wanda ya saka komai a bakinsa bale ya kai cikinsa, kai da azumi ma Wardugu ya tashi, su kuwa ba wace ta kula da wani cikinta ,
Agaishat hankalinta a karshen tashi yake, dan sala sala khadija ta kwatanta mata komai a jiya da yama, dan Gaskiyarta ta fadawa khadijar cewa ita ba karatun boko ta yi ba, bata san komai game da abinda ke faruwa ba,

Khadija ta yi mamaki ainun, daman wanda bai yi karatun boko yana iya zama wayis haka? Ita bata ga wani kauyanci a tare da Agaishat ba, ko aman da ta yi ta kelayawa a jirgi ta yi tunnanin ko irin mutanen nan ne da basa son tafiar jirgi ko mota yanzu sa kama amai,  du kai kawon nan da ake a tunaninta ta gane komai idan likita ya fito ya yi bayani da french a tunaninta ta iya ta san me aka ce,
Kwarai ta ji ba dadi, ta yi tunanin da itace fa? Hakan ya sa ta zauna ta yi iya yinta da kwatance da cicirarar hausarta ta fada mata komai a nitse wanda sai da ta yi data sannin fada mata dan sai a lokacin Agaishat ta birkice fiye da da ta ringa irgen lokaci tana fadin ya taimaka ya buda ido, ita a barya ta je ta tashe shi,
Wannan karon wardugu bai iya wani tsawata mata ba, shima zuciyarsa a hautsine take

Jikinta duka rawa yake, a hankali ta kai hannunta wajen Khadija dake tsaye tamkar ba jini a jikinta ta damie hannunta ko zata ji sasaucin tsoron da take ciki,
Khadijarma ta rike hannun nata gamgam suna gannin yanda likitocin ke ta aune aune suna magana suna rubutu a takarda,

A yannayin da suka fito, dole ne hankali ya tashi,
Wannan karon kam ba wani boye boye suka tsaya gaban Wardugu, Khadija, da Agaishat suka yi masu bayannin bai farka ba kuma basu san dalili ba,

Sun auna basu ga abinda ya tare mashi farkawar ba,
Suna fadi ne fuskarsu cike da alhini,
Khadija ta kwala kara ta ce" non, non impossible non (no, no imposible no!),

Wardugu dai na duban likitan dake bayani, ya ci gaba fa fadin" cikin wasiyarsa ya bar maganar, in dai bai farka ba, kar a ci gaba da rayashi da inji, a cire masa injin dake taimakawa lumfashinsa a bar shi ya tafi, lokacinshi je ya yi ba yanda za.a yi, dan haka ku saka ranar da za.a cire masa na.urar dake bashi lumfashi,

Wayo ba za.a cire ba, wayo na shiga uku, Mu.azam kar ka yi kin haka, Wardugu ba za.a cire masa ba, in dai kuka cire mashi kun kashe ni nima  walahi ko kwana daya ba zan kara ba sai dai ku kaimu mu biyu, khadija ke fada tana girgiza Wardugu kan kar ya saka hannu a wannan decision din,

Agaishat ta matso da sauri ta kama dayan hannun Khadija itama tana kuka a rikice da yaren buzanci ta ce" ya mutu ne? Ya mutu? Khadija Mijina ya mutu? Innalilahi wa.ina ilaihi raj.une ,
Ta cika hannun khadija ta damki na Wardugu fake tsaye yana dubansu zuru tamkar bai san yaren kowace cikinsu ba, tamkar wanda ya rayu cikin jeji shi kadai, sun zame masa sababin halita a gabansa,

Agaishat ta rike shi da kyau ya dago hannunsa ta dora gefen fuskarta ta girgiza hannun da kyar ta ce" Wardugu, ya mutu? Mutuwa ya yi? Wardugu ya mutu ne?

Wardugu ya janye hannayensa a jikin nasu ya juya da wani irin sauri ya fice a wajen baki daya,

Khadija ta zube kasa tana kuka inda likitocin abokannan aikinta ke rarashinta, Agaishat ta karasa jikin madubin ta jinginna kanta ta hadiye kukan a ranta ta shiga zabga masa adu.a tana tofawa tana duban ba.a rufe shi ba,

Wata likitar ta zo wajenta itama ta shiga rarashinta tana dafa kafadarta da yaren frency inda Agaishat dubanta kawai take aman bata san me take fada ba, ita dai zuciyarta ta cunkushe kukan ya tsaya cak, adu.a take ta yi kan Allah ya sa ba mutuwa ya yi ba!

Wardugu na fita ya je ya tsaya bakin titi ya tsurawa hanya ido,
Ba komai idannuwansa ke ganni ba sai zaman da suka yi da Mu.azam, abubuwa da dama wanda yawancinsu irin girman hakurinsa da zama da Wardugun ne, da wanda in ya juye wani sa.in sai an nemo Mu.azam din,

Ina son na rayu War, ina son na rayu na haihu nima na ga yarana sun girma, sai dai ban san ba ko zan samu haka?
Magangannun suka fadowa Wardugu a rai,
Idannuwansa ya rintse suka kara rikidewa sukai wani ja mai duhu!

Wani lokaci sun je kauye mai sunna Matamai nan yankin damagaran kusa da nigeria ya ga yanda garin keda ni.ima,  tsarin rayuwar garin ta mugun birge shi inda ya nace sai da suka kara kwanaki kan wa.inda sukai niyar yi,
Suna lambu ne cikin garin sansayar iska na kada su yace" ka san Wani abu Wardugu?, duda an ce mutun idan ya mutu halayensa ke binsa, khairin ko sharin gwargwadon aikinsa gwargwadon kabarinsa, aman zan so na mutu a garinnan   ni.imar garin ta yi min ,
Wardugu ya daki kafadarsa ya ce" sai kace wani saudiya? Kai fa haka kake motsi kadan mutuwa motsi kadan mutuwa, du inda ta zo fatan shine a cika da imani,

Ji yake jikinsa na yi masa nauyi, zuciyarsa ta cinkushe,
Wayarsa ke kuka kamar ta fasa aljihun wandonsa ta fito aman kunnayensa basa ji,
A fili ya ce" ya zaka bar wasiyoyinnan a kaina Mu.azam? Wa ya fada maka ni inada karfin zuciyar da zan iya saka hannu a takardar da zata bada damar a cire maka damar shakar numfashi ka tafi na dindindin? Wa ya fada maka cewar ni inada karfin da zan iya daukan gawarka na kaita inda zan kaita? Kai wama ya fada maka cewar ni din zan jure gannin an rufa maka dara? Innalilahi wa.ina ilaihi raj.une,!

Wayarsa ya lalubo jikinsa na wani irin kadawa , zafi kuwa ya dume masa jiki baki daya ya danna numbobin da bai yi tunanin idan an daga zai samu mutumen ba,

Da asalamu alaikum aka amsa wayar,

Wardugu ya ce" Mu.azam ne yace wai na saka hannu a takardar cire masa oxygene,

Shiru ya yi , inda hankalinsa ya tashi, murya a dan rikice ya ce" kana ina? Kuna ina?

Wardugu ya amsa da " muna paris, muna ma.aikatar Mu.azam, Mu.azam ya ki tashi!

Mikewa ya yi daga zaunen da yake , da hannunsa ya yiwa abokinsa alama da ya tafi ya fice ya nufi aeroport dan gannin ko zai samu jirgin da zai sada shi da Paris a yau yau, inda hali a yanzu????

😭

Wa Wardugu ya yi kira,?

MU.azam ya tafi kennan?

Agaishat, Khafija, Wardugu👏🏻🙁😢😔😔😔😔😔

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

5️⃣7️⃣

Tafia ta manya ce ya yi, in ba dan manyan ba daga shi sai suturar jikinsa sai cart dinsa ta banki, da ita ya ciri tiket, ya zauna yan mintuna inda jirgi ya daga da su, da ita ya ciri kudi ya yi shatar taxi ta kai shi asibiti

A kofar asibitin aka hana shi shiga, domin dare ya ratsa har wajen karfe biyun dare,
Ba yanda bai yi ba, da kwatance da komai aman masu tsaron kofar suka kiya dan su basu sanshi ba, gashi mushulmi, su kam aa yama bar masu kofar asibiti
Gashi bai san numbersa na garin ba,

Waje ya samu dan nesa da asibitin ya shiga kai kawo, dare ne ba damar ya sayi wata wayar du an rufe, gashi ba wata takarda ya zo da ita ba ko tiket ciran kudi muraran ya yi masa sun san shi a yanda yake da yawo kasashe ya shige abinsa idan ya so ya san yanda zai yi,

Kansa ya shafa a lokacin da ya tuno da whatsupp, duda ya san abune mai wuya wai ya duba whatsupp , aman sai ya shiga ya aniya kiran number Wardugu baya dagawa,
Ya yi masa kira ya fi a kirga, dan haka ya nemi guri ya zauna hankali kwonce dan waje ne mai tsaro, kuma da garaje ba za.a kama mutun ba duda suna da tsarguwa da musulmi suna tsoron yan jihad,

Daga nesa yake hangen tafiyarsa, da kyar yake daga kafarsa,
Ido ya tsura masa, daga ina yake?

Wani tausayinsa ne ya lulube shi, dan kuwa Wardugu in dai hankalinsa a tashe toh baya zama, zai yi ta yawo ne a kafa, idan wani abin fada ne ya hada shi da wani toh a hanyar yawon nan nasa kan mai tsautsayi zai kare ne,
Aman yanzu yana hangensa a wani yannayi na rashin karfi, har ya karaso inda yake zaune,

Dama Wardugu na hangensa, tun zuwansa har artabun da suka sha da masu tsaron asibitin da kiran da ya yi ta faman yi,

Yana zuwa tsaye ya yi gabansa yana dubansa,

A nitse ya mike shima yana dubansa,
Hannu ya mika masa da nufin su yi musabaha,
Wardugu ya miko masa nasa hannun shima, nan ya ji wani irin zafi hannun nasa,
Hankali tashe ya ce" aman Wardugu me kake yi haka?  Yau ka fara yin rashi ne ko yau ka fara shiga tashin hankali mai tsanani? Ka tina wannan lamari gaban wanda baka da ikon motsi, jan numfashi sai ya umarta ne, kaima lokacinka na nan tafe, dan kulu nafsin za.ikatul maut,
Ba wanda ya isa, ba wanda zai iya, ba wanda zai yi in ba shi ba, kar ka manta ya rasa iyayensa a lokacin da yake saurayi, ya karba da hannu bibiyu ya rayu a cikin duniyarnan mai cike da rudani,
Idan Allah ya karbe mana shi a yau sai mu yi masa  biyaya , mutuwa ta zama rigar kowa, mutuwa mai yankan kauna ne, mutuwa ba ruwanta da baba ko yaro, itace mai dauke uwa a lokacin da ta sako dan jariri, itace mai dauke jariri daga hannun mahaifiyarsa ta mika shi a kaishi wajen wanda ya fita son sa, mutuwa mai raba miji da mata, ta raba abokai, ita ba inda bata ratsawa da lokaci ya yi ya dauka ta yi gaba abinta, a halin arziki ko talauci, birni ko kauye,
Ka yiwa amininka gata mafi girma wato adu.a da kyakyawan sutura,

Wardugu ya zube kasa nan wajen kasa zaune,
Bakinsa na rawa dan ciro magana , da kyar ya iya samu bakin ya bude masa ya ce" ya ya ya bar wasiyun da sukai min tsauri da yawa, *MARAHUT* na tsinci kaina a halin da bana iya aiwatar da komai, karfin ikon Allah dole na karba, na kasa kuka, na kasa saka hannun, ana min ikirarin ni jarumi ne? Na gwada jarumta ta hanyar sadaukar masa da abinda nake so a nan gidan duniya aman yau an wayi gari na kasa daukan jarumtar saka hannu a bakar takardar da za.a cire masa abin numfashi,

Marahut ya zauna shima kusa da shi ya daga kansa sama ya ce" kalu *INNALILAHI WA INA ILAIHI RAJ.UNE*, innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, innalilahi wa.ina ilaihi raj.une.......
Haka Murahut ya yi ta maimaita masa har shima ya karba sukai ta yi , sukai ta yi , sukai ta yi,

Can Wardugu ya shiga ajiye zuciya, a hankali ya dora kansa saman kafadar Murahuttt,

Murahutt ya yi shiru na dan Lokaci kafin ya ce" ka san cirewar ko shi ne samun rahama a gare shi? Idan ka yi duba da musulunci ya zo mana da idan mutun ya rasu a yi gagawar yi masa sutura?

Shin wace hikima ce a boye a nan? Allah baya abu kawai,
Idanfa an jima da zare ransa kune ke gannin yana numfashi? Idanda gawar ce kwonce kuke kallo?

Wardugu ya rintse idannuwansa da karfi ya ce" mai yiwuwa kuma likacin ya buda idannuwan nasa ne basu yi ba?

Kennan dai ba zaka hakura ba ? Marahut ya tambaye shi,

Wardugu ya ce" bani da karfi, ban isa na ja ba,

Marahut ya gyada kai, sukai shiru su duka

Can Marahut ya ce" ina Agaishat?

Wardugu ya dago da sauri ya dubi Marahut, shi sai yanzu suka fado masa a ransa, mikewa ya yi zurbat ya yi gaba da sauri inda Marahut ya bishi da kallo, bai yi wani gigin binsa ba dan tuni ya yi nisa a tafiar sai ido da ya zuba masa har aka barshi ya shiga asibitin,

Yana shiga ya zarce wajen da ya tabata suna nan wato wajen dakin Mu.azam,
Bayin Allah sun dunkule waje guda sun rufa da hijabin Agaishat sai sauke ajiyar zuciya suke su duka,

Tausayinsu ya kara karyar masa da zuciya, tun ranar da Khadija ta je gidansa ya gama gane ba wai kawance ne kawai ya hada su da Mu.azam ba, duda ya ga irin yanda Agaishatma ke son Mu.azam din, aman yayi imanin da wuya in ta kai khadijar dan kuwa Khadija ta jima a soyayarsa, wa.innan bayin Allahn biyu su ne marayu kan rasuwar Mu.azam, shi kuwa ya rasa amini, aboki, dan uwan shawara, dan uwa na jini

A hankali ya raba su ya nufi wajen hangen Mu.azam din,

Ja ya yi ya tsaya ya tsura masa ido, irin kallon nan na kurullah,

Idannuwansa ya lumshe yana kada kai, dan kuwa idonsa nuna masa yake ya motsa yatsarsa manuniya,

Da yake kafafuwansa rufe suke da bargo ba.a gannin motsinsu, sai da ya kara motsa yatsar nan, a hankali fatar idonsa ta dan fara rawa, bugawar zuciyarsa ya fara karuwa kan na da da ya yi kasa sosai ya yi nisa,
A hankali bugawar zuciyar ke dan karuwa wanda ya saka injin dake sasarkafe jikinsa suka kwashi kuka,

Zabura Wardugu ya yi ya kara kurawa Mu.azam ido,

Tun karfinsa ya ce" MU.AZAM, MU.AZAM, MU.AZAM!

Ba.a jin komai daga ciki, sai su Agaishat ne suka mike a firgice, daidai nan likita ya shigo da gudu ana biye da shi ana taya shi daura rigar aikinsa da safar hannu da na rufe hanci,
Wata na tura abinda ke dauke da kayan aiki,
Ai kuwa sai gasu suna ta bilowa da gudu gudu , nanfa aka shiga kokowar fitar da su Wardugu daga nan din ma ,
Da kyar aka fitar da su waje inda du suka haukace sai tambaya suke jefo masa wai ya farka ne ? Farkawa ya yi ne?

Wardugu kam bai iya amsawa ba sai kai kawo yake yana kama sunnayen Allah a zuciyarsa , baya so ya amsa masu dan bazai so ya basu espoir kuma abin ya kasance ba haka ba,

A kadan sun dauki minti arba.in, lokaci lokaci zaka ga wani ya fito da gudu ya nufi can wajen dakin kayan aiki ya dawo da wani abin da gudu ya shige, koda sun tarye shi baya bada amsa har suka hakura suka dawo bin mutane da kallo. ( ya Allah ka jikan mama da gafara, wannan ciwo da ya kaita Allah ka sa bakin wahalarta kennan alfarmar annabi muhamadu sallalahu alaihi wa salam)

Ba su su gama kimtsa komai ba sai da aka dauki wajen awa da minti talatin kafin kake gannin sun fara fitowa suna tafia makwoncinsu,

Su kam sun zama tamkar mararsa wayo,
Can sai ga docter Rogger da Elizabeth sun fito,
Murmushi kwonce saman fuskarsu,

Hannu suka shiga mikawa su Wardugu, harda Agaishat dake binsu da kallo aman ta kasa karbar hannun ko daya dan ta kagauta ta ji halin da yake ciki

Wani murmushi ne Wardugu ya saki, wanda gaba daya hakoransa suka bayana,
Da sauri ya juya ya nufi bayi dan dauro alwallah, domin lokacin nafilfilu bai shige ba, tabas zai raya wannan dare wajen godewa Allah,

Khadija ta rungume Agaishat tana murna ga hawaye na malala a idannuwanta ta ce " Agaishat, ya farka, kuma ya yi kyakyawan farkawa, dan ya gane su su duka, yanzu an ce a barshi ya huta zuwa safe mu shiga mu ganshi, Agaishat *Mu.azam dinmu ya farka*

Agaishat ta saki murmushi itama ta ce" Alhamdulilah, Allah mun gode maka, Allah ka bashi lafia mai anfani

Da amen take amsawa,
A haka Wardugu ya  fito da tapis a hannunsa ya saci kallonsu kadan ya sauke ajiyar zuciya ya

fice a asibitin,

Inda ya barshi nan ya same shi,
Goron ruwa ya mika masa bai masa magana ba ya samu waje ya shinfida dardumar ya tayar da sallah,

A sujadarsa ta karshe, Wardugu ya jima yanaiwa Allah kirari, ya gode masa bila adadin,
Bai tashi daga saman salayarsa ba sai da rana ta fara fitowa, dadaykun mutanen da suke fitowa motsa jiki na safe har sun fara tsayawa daga nesa suna kallon su Wardugu suna mamakin musulmai ne suna masu sallah a wuri,

Bai wani damu ba sai da ya gama jan carbinsa ya shafa fatiyarsa , ya kai dubansa wajen Mahaifinsa,
Fuska ya hade ya yi kicin kicin da fuska ya ce" ya farka a jiya,

Marahutt ya ce" na gane tun jiyan a yannayinka,

Wardugu ya dan tabe baki ya mike ya dauke abin salayar ya kai dubansa wajen asibitin ya ga an bude an fara shiga, dubansa ya kai wajen Marahutt ,
Kafin ya yi magana Marahut ya ce" na san hanya

Kansa ya juyar ya ajiye salayar nan kusa da mahaifin nasa ya juya yana neman taxi dan ba zai koma ciki daukan mota ba gaskiya.

Hotel ya je ya saka kaya masu sauki ya shiga fakin gymnastic ya motsa jikinsa sosai ,
Dawowa ya yi ya yi wanka da ruwa masu sanyi karara ya fito ya saka kaya ya fesa turare ya dauki kys ya bude dakin ya sauka , nan ya karbi kayan da ya yi order ya shige taxi din dan ya mayar da shi asibiti

Yana zuwa ya shige ,

Nan ya gansu zaune Marahutt na kusa da su  suna hira jifa jifa inda Agaishat ta bada hankalinta suna hira dan sosai yake sake mata gashi yana kiranta da yarsa, hakan ya saka take son datijon da gannin girmansa

Wardugu na shigowa idannuwansu suka sarke ita da shi,
Wata harara ya sakar mata kafin ya dauke kansa,

Kamar yanda ya saba ya mikawa kowa nasa harda Marahutt,

Karban dai yan matan suka yi aman ba wada ta kai niyar ci,
Bai takurawa kowa ba, ya dai bude ya dan tataba nasa dan a jiya da azumi ya wuni banda bakin ruwa ba abinda ya sha,

Wajen karfe tara likita ta zo da kayan pensement, shiga ta yi ta yi masa ta fito,
Wajen karfe goma docter Rogger ya zo ya shiga ya bashi abincin da ya dace ya ci,
Bayan ya fito ne ya ce" da bibiyu zaku shiga, kuma kar ku yi masa hayaniya da yawa, kar ku saka shi magana, kar ku nuna yannayin damuwa a fuskarku a gabansa,
Zamu kara rike shi na dan lokaci har mu kare yi masa pensement sai mu sake shi, Docter khadija ki zo ki karbi takardunsa baki daya ki kawowa Wardugu,

Musabaha sukai da Wardugu kafin Khadija ta bi bayansa tana faman ta yi ta dawo ta shiga,

Wardugu ne yad dawo daga rakiyar doctern ya nufi dakin da niyar shiga

Marahut ya ce" Wardugu, ka shiga da matarsa mana?

Ja ya yi ya tsaya , a hankali ya waiwayo, da hannunsa ya yi mata nuni da ta shiga,

Da sauri ta mike ta tafi ta kama kofar a hankali ta tura ta shiga inda wardugu ke biye da ita a bayanta,

Tunda suka shigo ya tsura masu ido gabansa ya fadi, kunyarsu ya jo ta lulube shi, wato dai  a duniya bashi da gatan da ya fi Wardugu da ahalinsa, ya san yanzu zai ji haushinsa a yanzu, aman ya tabata daga baya idan ya ji dalilinsa, zai fi kowa murnar hakan

Murmushi ne shinfide a fuskarsu har suka karasa kusa da bed din da yake kwonce,

A hankali Wardugu ya karasa kusa da shi ya dan rage tsayinsa,
Hannunsa ya kama ya damke musabaha da nuna farin ciki,

Agaishat dake tsaye ta zagaya dayan gefen ta taho kamar zata kwonto gefensa,
Ido ya zaro yana dubanta, hannunsa ya dago yana son tsayar da ita,
Ja ta yi ta tsaya tana sakar masa murmushi,

Tsoro ne ya kama shi, me hakan ke nufi? Jikinsa ne zata hau?

A hankali ya kai dubansa wajen Wardugu, duda yana halin rashin lafia, duda ya tabata A wannan lokacin wardugun na cikin farin ciki, aman abin ya daure masa kai,

Murya ciki ciki ya samu a hankali ya ce " War, babababa ga message dina ba?

Wardugu ya ce" sakon wasiyoyin har a wayar ka turo min ko? Allah ya shirye ka.

Mu.azam kam kasa cewa komai ya yi, ya sakar masu murmushi shima, a haka har suka gama ganninsa sukai masa salama da fadin sai kuma shigar gobe dan sau daya tak zasuna leka shi,

Nan suka wuni a ranarma, sai a wannan ranar da zasu tafi Khadija ta bi su, rabonta da gidanta tun fitar da Mu.azam da aka yi,

Suna zuwa ya sauke su ya yi tafiarsa masaukinsa

Bayan gama al.adunsa na yau da kulun ya mike saman bed hankali kwonce ya shiga wayarsa, Whatsupp ya fara shiga, nan ya nutsu ya yi ta yiwa mutane response kan message dinsu, harda su voice,
Yau kam Basma ta ja ra.ayinsa, dan ya ga dan kokari harda su voice,
Shiga ya yi ya kunna voice din nata yana saurara,
Kansa ya girgiza yana murmushi kafin a fili ya ce" Mata kennan,

Fita ya yi ya shiga wajen message dan daukan number da sergent ya turo masa na mutumen da zai canzawa su Mu.azam gida, dan angiwar batai masa ba,

Nan ya ga message din Mu.azam har guda tara,

Shiga yayi yana fadin" shi kennan tun ina Niger ya tura min wasiyoyi dan ya kashe ni lokacina bai kai ba ko?
Murmushi ya yi yana mai jin nishadin da ya kwana biyu bai ji ba tunda aka yiwa Mu.azam aiki,
Message din ya fara karantawa kamar haka

*Na yi shigar wuri, sauri sauri nake na dandanna zakin aure kafin na tafi*

*Ni mai laifi ne, ban san ya zaka dauki lamarin ba*

*Kar kai hukunci cikin fushi, kamar yanda na jima ina neman shawara da bin lamarin a hankali , ban aikata ba sai da na yi zurfin binkice da neman zabin Allah*

*An ce abinda ka ji hankalinka ya fi karkata ya fi kwonciya idan ka kasance ka barwa Allah zabi ta hanyar yin stihra, Wardugu a kulun na kwonta da barwa allah zabi na farka wannan dai shi ne zabin*

*ban rainata ba, hasalima na sota fiye da tunaninka, sai dai a lokacin ban gani ba, sai da muka dawo na fahimta*

*Wardugu, gagawa na yi, na yi gagawa, na yi mugun gagawa, ka yafe min*

*ni wani sadaukarwa na tabai maka? Ka mini da yawa wardugu ciki harda kudin karasa karatuna, ka mini dayawa*

*Wardugu, na bata a rubuce, shaida, zan kuma turo maka.....Ni Muhammad Mu.azam na

sawakewa matata Agaishat aurena dake kanta, wato na tsinke igiya daya cikin uku, ba dan ta min laifi ko wani abin ba, zamanna da ita ne ya kare*

Daga nan Wardugu ya tsaya a bin messages din Mu.azam wanda sauranma na ban baki ne,

Wayar ya saki ya mike tsaye cir daga kwoncen da yake,
Gabansa ne ke wani irin dokawa , hankalinsa ya tashi,
Wani irin ihun bakin ciki ne ya saki wanda da a lokacin Mu.azam na a gabansa ba abinda zai hana ya shake shi har sai ya shaka masa kanshin mutuwa,

Daga shi sai singiletin nan ya fito rai a mugun bace hankali a tashe ya karbi kys dinsa ya fitar da motar a garaje ya.......

Comment comment

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝🏻😘

Na
*SAJIDA*

5️⃣8️⃣

Tuki yake na garari, ba bin doka , ba tsare iyakar gudu da mota a cikin garin paris, wanda hakan

ya saka motar police bin bayansa tana mai nunin ya tsaya aman fir ya ki ya tsaya,
Bai zame ko.ina ba sau gidan Mu.azam,
Yana fitowa daga motar police din ta fito da sauri tana mai nuno shi da bindiga da fadin ya tsaya ko ta harbe shi,
Hakan ya janyo hankalin daidaikun mutanen dake anguwar, wasu na dan lekowa ta takarsu, wasu na fitowa dan ganninnko barawo ne aka biyo har anguwarsu? Ciki kuwa Harda Khadija da ta ji haya hayar ta yi yawa,

Rai bace ya ja ya tsaya ya juyo yana mai saka hannunsa cikin aljihunsa na wandon dake jikinsa hakan ya saka ta kwala karan ya tsaya kar ya kara wani motsi a yanda yake!

Tsayawa wardugu ya yi, dan ya san in ya kara motsin a hakan hukuncin harbi ya hau kansa,

Da gudu ta karasa tana fadin ya daga hannayensa sama,
Kansa ya girgiza da yaren french ya bude baki rai bace ya ce" sunana General Wardugu Marahutt, ki barni na ciro maki shaidar hakan, kar ki saka min hannu a aljihu!
Ya karasa yana mai kuwa a kanta,

Da sauri ta ja ta tsaya daga niyar caje aljihun nasa ta dan ja baya still dai bata sauke bindigar ba, ta shishiryawa ko ta ware ko ta walare,

Ciro mata baje dinsa ya yi ya mika mata a dake,
Da sauri ta karba ta karanta, ta ga hoton sama da komai,
Da sauri ta sara masa, domin karatun da wardugu yayi na bashi power a kasashen wajema ba a iya niger kadai ba, dan haka ta bashi hakuri tana mai fada masa ta biyo shi ne daman dan ya taka dokar fice ka.idar gudu a cikin gari

Karba ya yi ya juyo inda itama ta shiga magana da wayar hannunta tana fadin shikennan kar a turo mata kowa General Wardugu Marahut ne na Niger .

Ko kallon Khadija dake masa magana bai yi ba ya shiga gidan ya karasa ya shiga danna karaurawar dakin ba tare da ya bari ta numfasa ba ya ci gaba da dannawa,

Dirowa ta yi daga bed, kayan baci masu santsi sakaku ne a jikinta dogon wando da riga har gwuiwa, kanta ta kunce shi ya bazu a gadon bayanta sai turaran ruwa da ta shafa a jikinta ta kwonta ta huta bacin da bata yi ba wannan karan haka ya firgitata,

A firgice ba tare da ta tuna da wani rufe kanta ba ta fito da gudu gudu ta zo ta bude dakin

Bata shirya ba, bata san zata ji ba, kai batama san wai hakan zai faru ba sai jin saukar wani fitinanen, gigitacen  hautsinanan mari da ta yi imanin da bata yi fitsari kafin ta yi shirin kwonciya ba da ta sake shi ba wani ja.
Jinta da ganninta ne suka dauke na wani dan lokaci kafin take samu su dawo, a tsorace ta

shiga ja da baya jikinta ya kwashi bari tana dubansa ba tare da ta yi masa magana ba,
Khadijama a tsorace take biye da bayansa tana mai dora hannu a kai da fadin" Wardugu?

Wardugu da har jikinsa ke rawa shima na bacin rai ya ce" ashe ya sake ki kike zaune a gidansa? Wannan wani irin natacen so kike masa da har zai sake ki , ki ci gaba da zama a gidansa kina shan ruwan gidansa? Tir tir tir da wannan zuciyar Agaishat sai yaushe zaki fadi cewar ya sake ki? Ko jira kike ya dawo ki lalabe shi ki bashi hakuri ya mayar da ke? Tambayarki nake kike kallona tamkar kin samu sabuwar halita?

Bakinta na rawa tana kankame jikinta dan har lokacin marin na ratsata, sannan wani mahaukacin tsoronsa ne ya diro mata wanda bata taba ji ba, a yanda ya zo bata taba ganninsa daga shi sai yar rigarnan ba, ga abin bacin rai gaba daya wani yannayi nasa dake boye sai ya bayanna, kirar jikinsa, jijiyoyin jikinsa, gashin kansa ba a nitse ba aman a waje guda sama saman ne ya tatashi,
Bakinta na bari ta ce" ban ban gane me kake nufi ba Ya Wardugu, ban gane me kake cewa ba, wa aka saka? Me me

La ferme Agaishat, (churup Agaishat) ki min shiru kar ki fada min karya a nan, bai baki takardar saki ba? Ko don son da kike masa zaki ki gwadawa ne? Na tashi na je gidanku mahaifiyarki ta damkan amana gashi ba.a je ko.ina ba har na ci? Ina takardar da ya baki tun kafin na karya ki gida biyu!?

Zubewa ta yi kan gwuiwoyinta ta hade hannayenta inda tuni kuka ya kece mata, tana kukan ta ce" sai nake jin kana nufin kamar mijina ya sake ni? Ya sake ni? Me na masa? Yaushema aka yi auren da har ya mayar da ni karamar bazawara? Wani umarninsa na taka? Sannan ni dake zaune a gidansa ban san da ya sake ni ba? Har aka tafi da shi asibiti *yana shigowa har dakina*,

Ido Wardugu ya rintse tare da shiga wani tashin hankalin, yana shiga dakinta? (Kalma mai fasara biyu),

Katseta ya yi ta hanyar fadin" bai baki takarda fara ba?

Kai take girgiza cikin yannayin firgici kafin ta tsaya tsak,
Mikewa ta yi da gudu ta fada dakinta ta bude akwatinta ta ciro takardar da ta adanawa Mu.azam wace a iya sanninta da shi ita kadai ce takardar da ta taba wani hada su,

Jiki na bari, tana jin kamar ta kifa ta karaso ta mikawa Wardugu takardar inda ya bude ya karanta,
Tsaf takardar saki ce Mu.azan ya dankarawa yarinyar da suka dauka suka wanke suka bashi, a cikin kasar da bata san kowa ba sai shi, a lokacin da ta shaku da shi, sai wata yar takardar a hade da dayar inda ya rubuta" Agaishat, ki yafe min, ina son ki ba dan bana sonki ba, sai dai hakan da na yi shi ban yi kai tsaye ba. *Ina son ki*,

Dubansa ya kawo kan Agaishat dake tsaye tana jiran karin bayani daga nesa kadan da shi , sai khadija dake kukan gannin rashin dacewar abinda Mu.azam yayi duda kuwa da hakan na iya mata dadi da a lokacin da bata san su waye Wardugu a rayuwar Mu.azam ba, aman a yanzu da ta ga waye Wardugu, ta kuma ga irin halacinsa sai ta ji ta shiga wani yannayi na rashin jin dadin abinda abin kaunarta ya aikata, duba da irin yanda ran Wardugun ya baci sai hankalinta ya kara tashi,

Murya dake ya ce" fice mu tafi,

Ido ta zaro tana dubansa kafin ta shiga yarfe hannu, murya na rawa ta ce" ina son sa, ina son mijina, ka hashi hakuri ya maidani dakina, ba zan kuma yin abinda na yi ya sakenin ba, ba zan yi ba, Wardugu daga aure sai a sake ni? Me Anna zata ce? Me baba sofo zai ce? Ya zasu yarda da wannan abin? Wardugu ina son sa,

Wardugu ya dan saki hanya ya nuna mata hanya fuskarnan a hade tamkar ya shaketa haka yake ji, dan rashin sannin ciwon kai wai a bashi hakuri,

Da sauri ta ratsashi ta fice tana waiwayen Khadija dake son ta baiwa Wardugu hakuri aman tana tsoro,

Itama murya na rawa ta ce" Wardugu toh bari na dauko mata hijabinta fan Allah, kafin na je na same shi asibitin,

Ja ya yi ya tsaya, juyowa ya yi yana dubanta kafin ya ce" *Tana da gata fa, itama yar dangi ce, ko bata da kowa a duniya tana da ni, idan kin je asibiti wajen masoyinki! Ki fada masa na gode! Na juya nigeria zan dawo gannin jikinsa in sha Allah, zancen hijab ki bar shi, wannan suturar ta jikintama zan dawo da ita, na haramta mata du wani abinda zai fito daga hannunsa komai kankantarsa! Mu.azam da Ni Wardugu yake magana!*

Haka ya tafi ya bar Khadija tsaye cikin tashin hankali ya shiga motar ya jata a tsoyace yana tukin irin na dazu inda Agaishat ta hade kanta da gwuiwarta ta afka duniyar tashin hankalin da ya fi na kulun, wai ita Agaishat har namiji ya nuna mata hali tun ba.a je ko.ina ba? Ita Agaishat, itace aka dankarawa sakin da ba laifi? Ita agaishat itace zaune a gidan kato da sakinsa a kanta tana wadaga tamkar gidan ubanta? A yau ta karasa yin tir da rashin ilimi, a yau ta ji duniyar ta fice mata a rai, a yanzu da aka ce ya saketa ta ji wani kaunarsa ita kuwa, ta shiga tsaka mai wuya ga Wardugu yaki koda kallonta bale ya nuna mata wani yannayi na tausayawa, ya tafi a bacin ran irin wulakancin da Mu.azam ya yi masa da tunanin yanda zasu kwashe da Ayya,

.........bai koma hotel ba sai da ya je ya samu takardar komawa Niger ta mutun biyu kafin ya juya Hotel da ita!

Timiya

Tafiar su Anna tafia ce mai nawa, domin dai ana fitowa daga cikin Timiya saman rakumi ne, gashi Anna sai da ta dauko baba tsofo du kuwa da irin yanda ya kiya aman fir itama ta kiya sai da shi ya saka aka yi dabara aka dora shi amale tun yana tsugune , maza hudu suka tatare har amalen ya mike kafin suma sauran su hau nasu su kama hanya,

Tafia ce mai tsayi idan ba.a gagawa, tafiar sahara ga tarin yan rakia da guzurinsu, dan jariri kuwa a nade a cikin tufafi mai laushi a jikin Anna rata yi masa goyon gaba,

Ana tafiar ne ana tsayawa a baiwa baba Tsofo abinci da ruwa hakan ya sa suka wuni cir kafin su shigo gari

Dogarai ne suka juya dabrakuman inda su kuwa suka dauki motar sarki daya kwal mai baya bude suka nufi garin Agadez

Ba su su shiga garin ba sai da isha ta yi, suna zuwa direct gidan sarkin suka je

Bayan an sauko daga salar isha.in ya kara ganawa da sarki, wanda ya bukaci gannin Anna,

Anna na shiga Sarki ya mike yana dubanta, kamar gatanan a fili ta mahaifiyarta, mace mai mutunci da mutunta mutane,

Ba bata lokaci ya hada vidio call da aminin nasa,

Dagawa ya yi yana mai saka gilashinsa na karin gani yana fadin" Sarkin agadez da kansa

Sarki ya amsa yana murmushi mai kayatarwa kafin ya hasko masa Anna dake tsaye

A zabure ya mike tsaye yana mai......

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

58

Tuki yake na garari, ba bin doka , ba tsare iyakar gudu da mota a cikin garin paris, wanda hakan ya saka motar police bin bayansa tana mai nunin ya tsaya aman fir ya ki ya tsaya,
Bai zame ko.ina ba sau gidan Mu.azam,
Yana fitowa daga motar police din ta fito da sauri tana mai nuno shi da bindiga da fadin ya tsaya ko ta harbe shi,
Hakan ya janyo hankalin daidaikun mutanen dake anguwar, wasu na dan lekowa ta takarsu, wasu na fitowa dan ganninnko barawo ne aka biyo har anguwarsu? Ciki kuwa Harda Khadija da ta ji haya hayar ta yi yawa,

Rai bace ya ja ya tsaya ya juyo yana mai saka hannunsa cikin aljihunsa na wandon dake jikinsa hakan ya saka ta kwala karan ya tsaya kar ya kara wani motsi a yanda yake!

Tsayawa wardugu ya yi, dan ya san in ya kara motsin a hakan hukuncin harbi ya hau kansa,

Da gudu ta karasa tana fadin ya daga hannayensa sama,
Kansa ya girgiza da yaren french ya bude baki rai bace ya ce" sunana General Wardugu Marahutt, ki barni na ciro maki shaidar hakan, kar ki saka min hannu a aljihu!
Ya karasa yana mai kuwa a kanta,

Da sauri ta ja ta tsaya daga niyar caje aljihun nasa ta dan ja baya still dai bata sauke bindigar ba, ta shishiryawa ko ta ware ko ta walare,

Ciro mata baje dinsa ya yi ya mika mata a dake,
Da sauri ta karba ta karanta, ta ga hoton sama da komai,
Da sauri ta sara masa, domin karatun da wardugu yayi na bashi power a kasashen wajema ba a iya niger kadai ba, dan haka ta bashi hakuri tana mai fada masa ta biyo shi ne daman dan ya taka dokar fice ka.idar gudu a cikin gari

Karba ya yi ya juyo inda itama ta shiga magana da wayar hannunta tana fadin shikennan kar a turo mata kowa General Wardugu Marahut ne na Niger .

Ko kallon Khadija dake masa magana bai yi ba ya shiga gidan ya karasa ya shiga danna karaurawar dakin ba tare da ya bari ta numfasa ba ya ci gaba da dannawa,

Dirowa ta yi daga bed, kayan baci masu santsi sakaku ne a jikinta dogon wando da riga har gwuiwa, kanta ta kunce shi ya bazu a gadon bayanta sai turaran ruwa da ta shafa a jikinta ta kwonta ta huta bacin da bata yi ba wannan karan haka ya firgitata,

A firgice ba tare da ta tuna da wani rufe kanta ba ta fito da gudu gudu ta zo ta bude dakin

Bata shirya ba, bata san zata ji ba, kai batama san wai hakan zai faru ba sai jin saukar wani fitinanen, gigitacen  hautsinanan mari da ta yi imanin da bata yi fitsari kafin ta yi shirin kwonciya ba da ta sake shi ba wani ja.
Jinta da ganninta ne suka dauke na wani dan lokaci kafin take samu su dawo, a tsorace ta shiga ja da baya jikinta ya kwashi bari tana dubansa ba tare da ta yi masa magana ba, Khadijama a tsorace take biye da bayansa tana mai dora hannu a kai da fadin" Wardugu?

Wardugu da har jikinsa ke rawa shima na bacin rai ya ce" ashe ya sake ki kike zaune a gidansa? Wannan wani irin natacen so kike masa da har zai sake ki , ki ci gaba da zama a gidansa kina shan ruwan gidansa? Tir tir tir da wannan zuciyar  Agaishat sai yaushe zaki fadi cewar ya sake ki? Ko jira kike ya dawo ki lalabe shi ki bashi hakuri ya mayar da ke? Tambayarki nake kike kallona tamkar kin samu sabuwar halita?

Bakinta na rawa tana kankame jikinta dan har lokacin marin na ratsata, sannan wani mahaukacin tsoronsa ne ya diro mata wanda bata taba ji ba, a yanda ya zo bata taba ganninsa daga shi sai yar rigarnan ba, ga abin bacin rai gaba daya wani yannayi nasa dake boye sai ya bayanna, kirar jikinsa, jijiyoyin jikinsa, gashin kansa ba a nitse ba aman a waje guda sama saman ne ya tatashi,
Bakinta na bari ta ce" ban ban gane me kake nufi ba Ya Wardugu, ban gane me kake cewa ba, wa aka saka? Me me

La ferme Agaishat, (churup Agaishat) ki min shiru kar ki fada min karya a nan, bai baki takardar saki ba? Ko don son da kike masa zaki ki gwadawa ne? Na tashi na je gidanku mahaifiyarki ta damkan amana gashi ba.a je ko.ina ba har na ci? Ina takardar da ya baki tun kafin na karya ki gida biyu!?

Zubewa ta yi kan gwuiwoyinta ta hade hannayenta inda tuni kuka ya kece mata, tana kukan ta ce" sai nake jin kana nufin kamar mijina ya sake ni? Ya sake ni? Me na masa? Yaushema aka yi auren da har ya mayar da ni karamar bazawara? Wani umarninsa na taka? Sannan ni dake zaune a gidansa ban san da ya sake ni ba? Har aka tafi da shi asibiti *yana shigowa har dakina*,

Ido Wardugu ya rintse tare da shiga wani tashin hankalin, yana shiga dakinta? (Kalma mai

fasara biyu),

Katseta ya yi ta hanyar fadin" bai baki takarda fara ba?

Kai take girgiza cikin yannayin firgici kafin ta tsaya tsak,
Mikewa ta yi da gudu ta fada dakinta ta bude akwatinta ta ciro takardar da ta adanawa Mu.azam wace a iya sanninta da shi ita kadai ce takardar da ta taba wani hada su,

Jiki na bari, tana jin kamar ta kifa ta karaso ta mikawa Wardugu takardar inda ya bude ya karanta,
Tsaf takardar saki ce Mu.azan ya dankarawa yarinyar da suka dauka suka wanke suka bashi, a cikin kasar da bata san kowa ba sai shi, a lokacin da ta shaku da shi, sai wata yar takardar a hade da dayar inda ya rubuta" Agaishat, ki yafe min, ina son ki ba dan bana sonki ba, sai dai hakan da na yi shi ban yi kai tsaye ba. *Ina son ki*,

Dubansa ya kawo kan Agaishat dake tsaye tana jiran karin bayani daga nesa kadan da shi , sai khadija dake kukan gannin rashin dacewar abinda Mu.azam yayi duda kuwa da hakan na iya mata dadi da a lokacin da bata san su waye Wardugu a rayuwar Mu.azam ba, aman a yanzu da ta ga waye Wardugu, ta kuma ga irin halacinsa sai ta ji ta shiga wani yannayi na rashin jin dadin abinda abin kaunarta ya aikata, duba da irin yanda ran Wardugun ya baci sai hankalinta ya kara tashi,

Murya dake ya ce" fice mu tafi,

Ido ta zaro tana dubansa kafin ta shiga yarfe hannu, murya na rawa ta ce" ina son sa, ina son mijina, ka hashi hakuri ya maidani dakina, ba zan kuma yin abinda na yi ya sakenin ba, ba zan yi ba, Wardugu daga aure sai a sake ni? Me Anna zata ce? Me baba sofo zai ce? Ya zasu yarda da wannan abin? Wardugu ina son sa,

Wardugu ya dan saki hanya ya nuna mata hanya fuskarnan a hade tamkar ya shaketa haka yake ji, dan rashin sannin ciwon kai wai a bashi hakuri,

Da sauri ta ratsashi ta fice tana waiwayen Khadija dake son ta baiwa Wardugu hakuri aman tana tsoro,

Itama murya na rawa ta ce" Wardugu toh bari na dauko mata hijabinta fan Allah, kafin na je na same shi asibitin,

Ja ya yi ya tsaya, juyowa ya yi yana dubanta kafin ya ce" *Tana da gata fa, itama yar dangi ce, ko bata da kowa a duniya tana da ni, idan kin je asibiti wajen masoyinki! Ki fada masa na gode! Na juya nigeria zan dawo gannin jikinsa in sha Allah, zancen hijab ki bar shi, wannan suturar ta jikintama zan dawo da ita, na haramta mata du wani abinda zai fito daga hannunsa komai kankantarsa! Mu.azam da Ni Wardugu yake magana!*

Haka ya tafi ya bar Khadija tsaye cikin tashin hankali ya shiga motar ya jata a tsoyace yana tukin irin na dazu inda Agaishat ta hade kanta da gwuiwarta ta afka duniyar tashin hankalin da ya fi na kulun, wai ita Agaishat har namiji ya nuna mata hali tun ba.a je ko.ina ba? Ita Agaishat, itace aka dankarawa sakin da ba laifi? Ita agaishat itace zaune a gidan kato da sakinsa a kanta tana wadaga tamkar gidan ubanta? A yau ta karasa yin tir da rashin ilimi, a yau ta ji duniyar ta fice mata a rai, a yanzu da aka ce ya saketa ta ji wani kaunarsa ita kuwa, ta shiga tsaka mai wuya ga Wardugu yaki koda kallonta bale ya nuna mata wani yannayi na tausayawa, ya tafi a bacin ran irin wulakancin da Mu.azam ya yi masa da tunanin yanda zasu kwashe da Ayya,

.........bai koma hotel ba sai da ya je ya samu takardar komawa Niger ta mutun biyu kafin ya juya Hotel da ita!

Timiya

Tafiar su Anna tafia ce mai nawa, domin dai ana fitowa daga cikin Timiya saman rakumi ne, gashi Anna sai da ta dauko baba tsofo du kuwa da irin yanda ya kiya aman fir itama ta kiya sai da shi ya saka aka yi dabara aka dora shi amale tun yana tsugune , maza hudu suka tatare har amalen ya mike kafin suma sauran su hau nasu su kama hanya,

Tafia ce mai tsayi idan ba.a gagawa, tafiar sahara ga tarin yan rakia da guzurinsu, dan jariri kuwa a nade a cikin tufafi mai laushi a jikin Anna rata yi masa goyon gaba,

Ana tafiar ne ana tsayawa a baiwa baba Tsofo abinci da ruwa hakan ya sa suka wuni cir kafin su shigo gari

Dogarai ne suka juya dabrakuman inda su kuwa suka dauki motar sarki daya kwal mai baya bude suka nufi garin Agadez

Ba su su shiga garin ba sai da isha ta yi, suna zuwa direct gidan sarkin suka je

Bayan an sauko daga salar isha.in ya kara ganawa da sarki, wanda ya bukaci gannin Anna,

Anna na shiga Sarki ya mike yana dubanta, kamar gatanan a fili ta mahaifiyarta, mace mai mutunci da mutunta mutane,

Ba bata lokaci ya hada vidio call da aminin nasa,

Dagawa ya yi yana mai saka gilashinsa na karin gani yana fadin" Sarkin agadez da kansa

Sarki ya amsa yana murmushi mai kayatarwa kafin ya hasko masa Anna dake tsaye

A zabure ya mike tsaye yana mai......

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤️*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

5️⃣9️⃣

Bai iya magana ba sai nunata da yayi a tsayen da yake inda zufa ta shiga wanke masa fuska,

Matarsa da ta shigo da tuwon tsakin da ta yi masa mai dan banzan dadi, wato mahaifiyar Anna ta ja ta tsaya da mamakin yannayinsa,

A hankali ta karaso dan gannin me ya firgita shi haka? Me yake kallo a waya?
Kurawa Anna ido ta yi, duda dan duhun wajen dan da haske aman ba irin tau din nan ba, sannan da yannayin girmanta da ya fara kama Anna, ba zai yiwu ta bace mata ba, tun usul mai kama da ita haka mutun daya ne, wanda suka nema suka rasa, kwararo kwararo har tsayin shekaru, wanda daga karshe ta yi hakuri kamar yanda mijinta ya roka, suka ajiye a jiyu, in da ranta Allah ya bayana masu ita , sannan sukai sadaka idan ta mutu ne Allah ya nuna masu gawarta ya sa ta huta,
A hankali ta karbi wayar inda jikinta ya kwashi rawa tana kallo ta kara kurawa wayar ido, a hankali ta ce" *ALLATCHI?* ALLATCHI ke ce?

Anna ta fashe da kuka, bata san lokacin da ta karaso kusa da wayar ta karbe a hannun sarkin ba ta matso wayar sosai kusa da ita tana kallon iyayen nata,

*Hatimi* wato mahaifiyar Anna ta yi taga taga zata kife inda mijinta *Gukunni* ya tareta jikinsa da wayar a hannunsa sunna duban Anna,
Shima muryarsa na rawan ya ce" Allatchi, dama kina raye? Ina kike yanzu mu zo Allatchi? Ki dawo gare mu, muna son ki Allatchi,

Anna ta lumshe idannuwanta ta bude ta ce" ina so na ganni wajenku yanzu , sai dai ba hali ,

Mahaifiyarta ta ce" mu gamunan zuwa!

Kit suka datse kiran inda Anna ta kifa kanta cikin cinyoyinta tana kuka, iyayenta du tsufa ya fara zuwan masu danma ana cikin rayuwar dadi, duda auren wuri sukai tsakaninsu dan tun suna yan university suka yi aure,
Girman soyayar da suke mata ta tuna, ta tuna irin yanda suka rayu babu ita tsayin shekarunnan danma an san musulmi da tawakali, Ba Ba hm!

Hajia aminiyar Ayya ce ta shigo dalilin kiran da Sarki ya saka a yi mata domin itace uwar gidan sarki

Tana zuwa Suka gaisa da Sarkin Timiya,
Sarki ya nuna mata Anna a matsayin y'ar gidan aminінsa da ta bata  wato Gukunni

Ta sha mamakin wannan lamari, daga baya ta shiga murna,
Nan ta matso kusa da Anna ta duka inda Anna ta zauna kasa wajen cafet ta ce" ki yi hakuri da kukannan haka, muma mun san da batanki, dan a lokacin sarki bai hau sarauta ba, baima aureni ba (Sarkin Agadez dogon karatu yayi , dalilin da ya saka bai yi auren wuri ba, aka ajiye masa yar kanwarsa karama sosai domin dai sarauniyar Agadez itama ba zata wani fi su Annan ba)

Sarki dake dan nesa ya yi gyaran murya ya ce" ai mai yiwuwa sunma taso, duda na fada masa kar yayi tafiar gagawa aman fir ya kiya,

Anna ta kale shi da sauri ta ce" aa, kar su taso a mota bayan har dare yayi, dan Allah su bari mu mu tarar da su,

Sarki ya yi murmushi ya ce" mota fa, aa, ai yanada jirginsa da ya malaka wato ket privé, sannan yanada damar tashi a lokacin da ta kama dan sune hukumar.

Wani sanyi ta kara ji a ranta a yau yau kennan idan Allah ya yarje mata zata ga mahaifanta? Kai Allah da girma yake, Allah da jinkan bayi yake.

Paris

Wardugu na kowama Hotel ya fice a motar ba tare da ya cewa Agaishat ta fito ba, hasalima kule motar ya yi tana ciki ya shige hotel din

Yana zuwa dakin da ya dauka ya dauki jakarsa ya zuba abinda yake iya dauka ya goya ya dauki echarp na maza na wuya ya rike a hannunsa ya fito ya basu kys dinsu ya fice abinsa

Yana zuwa motar ya ga ta kara volume din kukanta aman yana zuwa ta yi dif tana kikifta ido,

Motar ya bude ya shiga ya ja,
Bai zame ko.ina ba sai butik,
Yana zuwa ya fada masu kaya yake so a zaba mata  cikin gagawa da dan kwali,

Abinka da kasar ......, sai ya kasance suturun da ake nuno masa du daga dogon damamen wando, sai yan bintiyalan riguna, sai dogayen riguna aman masu mugun bin jiki,
Kansa ya dafe gannin lokaci na neman yi ba damar ya je wani butik din sai jirgi ya barsu, ransa ne ya kara baci wai su basu da Abaya ne?

Basu da Abaya, sai da babarsu ta mike da kyar ta zakulo cikin kayansu masu tsadar gaske wa.inda sai wane da wane suke nunawa su ko a kasar, ta cirota wata riga blue mai hasken sama ta kawo masa tana tunanin bama zai iya ba dandai idan batai masa ba ya dauki wata ne dan tsadarta

Dagata ta yi inda suka bita da kallo, doguwar riga ce itama mai rike jiki bale daga sama, aman tanada dogon hannu daya kwal, sai dan siriri tamkar na shimi da akai masa wani irin kwana aka malaka shi jikin rigar daga sama,
Sai dan kwali irin kananuwan nan sosai shima mai sharashara mai ruwan fari fari da blue blue din

Kansa ya dafe yana duban kayan, ba kudin da aka fada masa bane damuwarsa dan kudin sun kai jika dari hudu, aa, yannayin rigar ne, aman gannin ya yi rantsuwa, sai kawai ya bata umarnin ta shiga wajen saka kayan ta saka su fice,

Da sauri mai  butik din ta nuna mata ta bita ta tsaya daga kofa ta saka kayan sannan ta shiga ta gyara mata sosai, ta saka dan kum ta dan cacaje mata lalausan gashin kanta ta dora mata dan kwalin ya nadu ya yi kyau a fuskarta,
Wani irin kyau kayan sukai mata sannan suka fitar da kirar jikinta inda cikarta ta bayanna ,

Waouh macen ta fada kafin su fito tana nunawa Wardugu,

Mikewa ya yi bai kaleta ba dan shi ba dan hakan ya zo siyen kayan ba ya karbi jakar takalmin

ya mikawa macen sannan ya juya bayan ya cewa Agaishat idan ta saka takalmin ta dauko wa.inda ta cire din maza su tafi

Da sauri ta saka takalmin, Allah ya taimaketa bai daukar mata mai tsini ba, plat ne mai igiya dan haka ta daura igiyar ta dauki wa.inda ta cire ta fito da sauri sauri ta nufi motar

Ja yayi suka tafi, tana ji tana ganni ya tsaya kofar gidan da bada jimawa ba yake gidan mijinta ya jefa kayan da ta cire ya dawo ya shiga motar yana tafe yana waya da yaronsa har suka karasa aeroport din

Nan suka iske shi har ya karaso dan haka wardugu ya  bashi ky din motar sukai salama suma suka daga sai Niger Garin taraya Niamey garin zabarmawa, garin ka zo na zo

*Niamey*

Mota na tsayawa na fice da gudu daga motar inda sai a lokacin ya bita da kallo, yanda ta kwasa a gujen har dan kwalin kanta ya sulube daga saman kan nata ga yanda jikinta ya jijiga ya jijigo ne ya saka shi kawar da kai yana astagafari dan kuwa matar da batai idar sakin mijinta ba kalonta haka ai ba kyau🤨

Dan zama ya yi yana tunanin ya shiga ne ko kawai ya yi tafiarsa?
Wata zuciyar ta fada masa Wardugu Ayya fa mahaifiyarka ce, kuma indai kere na yawo, zabo na yawo watarana an hade, dan haka ka je!

Ayya dake zaune tana kallon tv, a lokacin wajen karfe takwas da rabi na dare ne,
Sai jin kukan y'arta ta yi da ganinta ta fado da gudu ta fada jikinta ta kankameta tana rizgar kuka,

A rikice Ayya ta shiga kokarin tashi da ita tana fadin" Agaishat? Agaishat? Innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, Agaishat ke ce? Lafia ? Ke da wa kuka zo? Me aka yi? Ina mijin naki? Ina wardugun? Ke?

A daidai lokacin Wardugu ya shigo yana tafia a hankali ya karasa saman kujerar zaman mutun guda ya zauna yana dubansu yanda ta makalkale Ayya da irin yanda Ayya ta rikice sai tambayoyi take tana duban wardugun,

Kamar daga sama ta tsinci maganarsa, koma tace kamar saukar mari, ya dan ja iska yana duban Ayya ya ce" *Ya saketa ne*,

Dif Ayya ta yi da tambayoyinta tana duban Wardugu, saki? Abinda kunnayenta suka jiyo mata kennan?

A hankali ta kankace idannuwanta tana duban Wardugu zatai magana kennan ta ji Agaishat ta

ce" Ayya wai ya sake ni, Ayya ban san laifin da na yi masa ba,

Ayya ta kallo wardugu ta ce" Saki,? Aka yiwa y'ata? Shin ciwon nasa haukata shi yayi kafin a gane har na dauki y'a na bashi ? Mahaukaci ne da riga?

Wardugu ya dago yana duban Ayya da auna yannayinta, daga muryarta ya fara dauko cewa Ayya ta fara hawa, wato tana harhada dukan abinda gareta na tashin hankali wanda yayi imanin zata saki a yanzu yanzu,

Ajiyar zuciya ya saki ya ce" da hankalinsa

Ayya ta zabura ta mike tsaye,  idannuwanta ta karasa kankancewa ta nuno wardugu da dan karamin yatsarta ta ce" ni? Ni zaku yiwa wulakanci? Ni zaku tozarta? Ni zaku watsawa kasa a ido? Ni zaku tonawa asiri? Ni zan dauki yarinya na baku ko wata batai ba ku sako mini bayan ba kangarariya na baku ba kuma ba hujajen buhu na baku ba? Ba nakasashiya na baku ba kuma ba neman kai nake da ita ba na dauka na baku ba? Gaskiyar Aghali, a lokacin da ya zo min bankwana nake fada masa maganar kun tafi neman aurwn yarinyata yace da ni haba Ayya, ai da ni zan ce ina so, na yi mata dukan abinda za.a yiwa yar gata na aureta a kaita gidana na kula maki da yarinya, aman yanzu kika baiwa abokin Wardugu kin tabata zai rike maki y'a?

Wardugu ya dago kansa da sauri, dan tunda ta fara maganar kansa ke sade, bai yi niya ba, bai so tanka Ayya ko daya ba, dan an bata mata tanada damar yin fada ta yi abinda take so, shine mai laifi dan shi ya uzurata , ya lalabata har ta aminta da a je a dauro auren, ya so yin shiru ta kare kansa, shi kuwa tasu shi da Mu.azam ne, Takunsu na gogagu ne, zasu goga ! Sai dai ji yayi bakinsa ya ce" Haka yace kennan?

Ayya ta ce" Ubanka yace Wardugu, nace Uban nan naka yace! Ba gashi ba ya nuna halin ba.a je ko.ina ba? Sai na yi shara.a da shi! Ba zan barku ba ku duka! Wato an baku y'ar a saukin kudi ko? Baku yi tade tadensu na buzaye ba kun samu abin a bagas ko?

Agaishat dake kallon Ayya, ta ce" Ayya, dan Allah a bashi hakuri ya mayar da ni , walahi ba zan kara yi masa koma mene yace na yi masa ba,

Ayya ta juyo da mamaki ta rike habarta ta yi tsai tana kallon Agaishat inda dakin ya dauki wani dan shiru, can ta ce" kina ji? Ki tashi, ki je dakinki ki cire mini wannan rigar ki yi mini wanka ki wanke ruwan gidan wannan banzan, ki yi sallah ki kwonta ki yi baci tun kafin na yi baja baja da ke a gidannan! Ka ji rashin sannin ciwon kai? Namijin zaki turani lalabo shi? To ko ku haka kuka a tadanku na buzaye na soke maki hakan a rayuwarki na haramta maki hakan! Walahi walahi walahi ni Ayya in dai na rike ki ko na kwana daya ne karya ne ki kuma waiwayar wani Mu.zzam koda shi daya kwal ya rage a duniya! Agaishat bace min da ganni kafin na maki marin da zai kufumta maki kunne!

Da sauri ta mike tana karkarwa ta shiga taka matatakalar benen ta haye da gudu ta nufi dakinta

tana waiwayen Ayya dake tsaye sai da ta bacewa ganninta ta juyo wajen wardugu,
Takowa ta yi har gabansa ta tsaya ta ce" in sha Allah na dauki alwashin sai ta zama abin hangensa daga nesa, sai ya yi dan daman bai sakar min y'a ba, ubankuma bai isa ba bale ku (wato Marahut), wasan kuke so bugawa da ni ko? Ni zaku kawowa wargi a wannan lamarin ko? Na gode , aman ka fada masa gidana da gaishe da ni sun haramta a gare shi! Yarinyata nada gatanta, in da hakinta kuma ban yafe ba!

Shi dai Wardugu kansa na kallon kasa, shi ganima yake da sauki tunda bata kai ga kifa masa mariba, sannan a haramtawar tata banda shi, dan haka ya sada kai sai da ta kare fadanta ta juya ta haye sama ya samu wuf ya fice a gidan,

A wannan dare kwana Ayya ta yi tana fada tana kai kawo tsakannin dakinta da na Agaishat tana duba lafiarta da banka mata harara danma karta yarda ta kuma kawo mata shirmen wai a lalaba shi, yo Allah ta tuba ko ita dake tsohuwa ta wani bi namiji a yanzu bare y'arta yarinya mai jini a hanci son kowa kin wanda ya rasa? In sha Allah zata kulata ta gama idarta tsaf sai su san abin yi, fatanta Allah ya sa bata dauko ciki ba dan a yanda take cikennan kar a je sai da ya kumsa mata ciki ya saketa (wato dai du a tunaninsu wani abu ya shiga tsakannin Agaishat da Mu.azam.....)

Wardugu kuwa na shiga gidansa ya tarar da gidan shiru kamar koda yaushe,
Bai wani damu da neman gannin matarsa ba ya nufi bangarensa,

Yana shiga ya tarar da farar takarda an ajiye ya dauka ya karanta, mai aikinsa ce ta yi masa salama da fadin ba zata iya ba madame ta koreta ta mata alkawarin in dai ta zauna mata a gida zata soketa da wuka!

Murmushi yayi ya yarda takardar nan ya shiga dakin da kyau, falon ya danyi kura abinka da fararan kaya nan ya yarda jakarsa ya nufi wajen wayar dake dakin ya daga ya shiga latsa numbobi.....

Tafiar awa gudu suka yi kafin su karasa garin Agadez capital de l.aïr

Hilux din sarki ce ke jiransu da direba, suna sauka direba ya dauko su inda kamshin turaransu ya cika motar

.....................comment comment.comment

🐪🐪🐪🐪 *BAK'A CE* 🐪🐪🐪🐪

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤️*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

6️⃣0️⃣

Motar na saka hancinta cikin gidan *Hatimi* ta rike hannun mijinta gam,
Shima din a zaunen kawai yake aman du gani yake ba.a sauri an kasa karasawa,

Anna dake tsaye a falon sarki dan baki daya can ya dugunzuma su sai kallon kofa take tana kai kawo ,

Turo kofar da aka yi ne ya saka ta tasayawa cak tana kallo ,
Direban ya fara shigowa kafin *Gukunni* sai *Hatimi*,

Dan tsai suka yi kafin Hatimi ta daga kafa da sauri sauri jikinta na bari ta karasa wajen Anna da kafafuwanta suka kasa dagawa daga tsayuwar ,
Tana zuwa rungumeta a jikinta inda Gukunnima ya karaso kafafuwansa na hardewa ya hadasu su duka ya rungume,

Ido kawai ta lumshe wanda jin nauyinta ya yi yawa ya saka Hatimi sasauta rikon da tai mata tana talafeta tana faman kufce mata dan ta yi nauyi da yawa,
Da kyar suka samu suka talafota, Anna ta suma
Nan fa hankali ya tashi sai ihun a fitar da mota a tafi asibiti suke suna talafe da ita a jikinsu,

Sarki je ya karaso da ruwa da sauri aka shafa mata
Wani irin numfashi ta ja kafin take buda idannuwanta a rikice irin farkawar sumarnan da mutun ke yi.

Ganninta jikin mahaifinta , wanda yake da dan gemu kadan fari wato furfura sai girarsa da ta fara farin itama, sai hannun mahaifiyarta fa dake jimke da nata ta dan daga a hankali ta ga hannun ya dan fara yakushewa irin na tsufan nan,
Kuka ta fashe da shi tana kara shigewa jikinsu, ji take tamkar idan ta sake su zasu bace a gabanta ne, dan haka ta ririke su tana kallonsu tana kara shigewa jikinsu

Sun jima a wannan yannayi, inda yayanta ke zaune can gefe , kukan yarima jariri ne ya fargar da su inda Anna sai a lokacin ta tuna da y'ayanta,
Dan sasauta rikon ta yi masu gannin ana dan waiwayawa inda yaran nata suke zazaune suna fama mimika Yarima boy sunna jijiga shi a tsakaninsu,
Tsare su Hatimi ta yi da ido kafin a hankali ta dawo da dubanta wajen Anna,
Murya na rawa ta ce" *Allatchi?*, ina kika shiga kika barmu cikin tashin hankali da rashin nutsuwar zuciya?

Anna ta tsareta da idon itama,
Gukunni ya riko hannunta ya ce" Allatchi, kin san irin tashin hankalin da na shiga dalilin dawowa daga wajen aiki da na yi na tarar da anmanki da *Herde* tsakar gida suna kuka wai baki motarki aka ganni a kofar gida aman ke baki dawo ba kuma wayarki bata shiga? Ina kika je?

Anna ta sada idannuwanta kafin a hankali ta ce" ban san da me ya juyar da hankalina ba, wanda tunda na baiwa gida baya ban san takamaiman abinda ya faru da ni ba sai nan da kwana goma na dawo hayacina, hasalima ban san *zaman da na yi da shi na shekara da shekaru ko da aure muka yi shi ko kuwa zaman haka muka yi?* , gashi harda y'aya suma sun fara haihuwa,

Zabura Gukunni ya yi ya mike tsaye, nan da nan jikinsa ya dauki rawar bacin rai da tashin hankali, murya bace ya ce" waye? Dan gidan waye? Wanene ubansa da kuma shi din kansa? Ko wanene ina mai tabatar maki da sai dai a yi daya cikin ni da shi, sai na rufe shi rufewar da ba zai fito ba sai dai a fitar da shi!, koda ya ki fitowa yaransa zan rufe sai ya bayanar da kansa! Sai na nuna masa danyen kai koda ubanshi sarki ne!

Anna dake zaune ta dago da kanta da sauri gabanta na faduwa, muryarta na rawa ta ce" yaranshi? Ko yarana? Abanna, bai damu da yaren ba dan ya yi rayuwarsa ne ta hanyar siyar da su, wato yana karbar sadakin yarana a tafi da su shikennan , ba sai ua damu da yaranba zai damu dan an rufe su? Aa ba za.a taba mini yaranna ba dan ina son su!
Ta karashe tana mai fashewa da kuka ta ce" mun yi rayuwa cikin dajin Timiya,
*Algabitt* ya kasance dodo , kura, fitina a rayuwarmu ni da yaranna,

*Algabit?* Hatimi ta tambaya tana mai son karin bayani kan waye hakan? Dan ta manta, bata taba kawowa a ranta ba,

Anna ta dubeta da kyau ta ce" Algabitt wanda Muka kade da Mota ni da Herde daga karshe Abanna ya dauke shi aiki a gida,

Hatimima mikewar ta yi a tsorace tana fitar da idannuwanta baki daya tana kallon Anna,

Anna ta dago kanta ta shiga kora masu dukan abubuwan da kwakwaluwarta ke iya tinnawa,

Mahaifiyarta kawai mutuwar tsaye ta yi, dan abin ya mugun daketa, wai Algabitt? Yaron da ta dauka tamkar dan gida? Eh lale aikinsa baiwa fulawowi ruwa, aman tunda ta ga y'ayanta na son lamarinsa ta yarge masa shiga falonsu, a zauna da shi a sha dariya,  bale da ya fada masu shi maraya ne shikennan suka kara yarda da shi duda wani lokacin mahaifin su Anna na fadin yaron nan yanada wani kallo irin na munafukai, sai ta yi daria ta jinjina hannunta tana fadin sai alkalina, kai fa ka saka na aminta da mu dauko yaronnan, sai yanzu da muka shaku da shi kai kuwa ka fara hango wani abin?

Bayan Anna ta yi shiru da labarinta Hatimi ta duka inda take zaune ta jata jikinta irin rarashi,

Gukunni kuwa sai wani irin numfashi yake fitarwa na bacin rai, bai ko kalli inda su Gaishata suke ba, dan shi kama suke masa da yaron, sai yanzu ya tina yaron, kam, lale haduwarsa da wannan bakin macijin za.a sha mamaki,

Hatimi ta dago tana share hawayenta ta ce" Gukunni, ka yi hakuri, yanzun ya dace mu yi murnar ganninta, na tabata asiri yayi mata, mu yi fatan da aure ya rayu da ita , mu rungumi jikokinmu, na san Herde sai ta fi kowa murnar yarannan , ta kwashi yayan wasuma bare na yar uwarta wace suka shaku ? Ai ni da zaka amince minma da ba zamu wani yi shara.a da wannan yaro ba, idan har ya sanar mana gaskiyar da aure ya rayu da ita? Ya sawake mata salim alim ya je, duniya ce, sannan mai duka na madakata, ya je ya yi abinda yake so idan tunaninka kai din wani shege ne a duniya toh tabasa akoy wanda ya dameka ya shanye, ba zan yi shara.a da shi ba, bai isa ba, cuta ya gama cutata , sai dai na gode Allah da tun kasa bata rufe mani idannu ba Allah ya bayanar min da ita,

Gukunni ya juya yana kallon su Agaishat , ya juya wajen su sarki dake zaune sun yi zuru suma, Da kai Sarki ya jinjina masa irin nuni da ya yi hakuri, ya tausasa zuciyarsa,

Dan yatsansa karami ya dantsa a bakinsa kafin ya kada kai ya nufi wajen su Agaishat da suka tsurewa nufo sun da ya yi,

Yana zuwa ya duka ya dauki Yarima Boy dake kuka ya juya ya fice a falon da shi,

Murmushi Hatimi ta yi tana duban su ta ce" zai huce, ko dan dan jaririn wannan fushinsa ba zai

yi tsayi ba, dan yana son yara kamar me, burinsa ya samu dan jika ,

Sarki ya sauke ajiyar zuciya, ya kuma kiran uwar gidansa domin ba a gabanta akai komai ba,

Tana zuwa ya umarceta da ta baiwa baki wajen hutawa,

Dukansu suka mike suka je bangaren sauke bakin alfarma aka basu dakunna wanda matar sarki ta nuna masu kowa dadaya, aman Anna ta kiya kan su hade suka,

Hakan kuwa aka yi dan haka sai aka shigo da sauran gadajen dan dakunnan akoy girma aka yi masu shinfidun alfarma inda suka shiga gaba dayansu,
Sai a lokacin Hatimi ta zo wajen su Agaishat dake tare waje guda ta zauna tana kallonsu,
A hankali ta ringa rungumarsu tana tausaya masu, zuka zukan yan mata ya wannan aman a cikin duhun kai, suturun jikinsuma abin tausayi wai a nan sun wanku ne? , ko.ina yar uwar tasu take ita? Shiga halin kaka naka yi har ka cire da ka mika kyauta, karshe a zo a aure shi bada izini ko saninka ba sai komai ya wakana a sanar da kai,
Kai bata tunanin akoy kotun da zata iya yi mata shari.a da Algabitt a nan gidan duniya.

*NIAMEY*

Jakar hannunsa ya yar a nan ya shige dakansa yana yatsina fuska dan kyankyamin wajen yake,

Samu ya yi ya buda wajen tufafinsa ya ciro kaya masu tsafta
Yana kokarin rufewa ta shigo dakin, yauma dai cikin kwaliyar take duda bata san da zuwansa ba,
Walyn kam akoy kama jiki, akoy kanshi, akoy iya kwaliya,

Karasa shigowa ta yi tana duban hannunsa da mamaki, wasu kayan ne ya dauka, ina zai je kuma? Shida yanzu shigowarsa har zai juya?
Da sauri ta idasa kusa da shi tana mika hannu wajen kayan ta ce" Wardugu, ina zaka je? Dan Allah yanzu fa ka dawo, daga ina kake haka wajen sati uku? Kuma ka dawo yanzu ka kuma fita?

Bai tsaya sauraronta ba ya goce kar ta karbi kayan ya rabata zai fice
Hankalinta ne ya kara tashi, ta san waye mijinta wajen harkar mu.amalarsa da matarsa(aurataya), aman yanzu har tsayin wannan lokacin bai wani nemeta ba?

Da sauri ta je ta bayansa ta rungume shi, hannunsa ta kamo ta dora saman rigarta wajen mararta ta ce" baka tambayi ajiyarka ba zaka tafi? Baka damu da cikinka dake jikina ba?

Wardugu ya janye hannunsa ya juyo yana kallonta tun daga kanta har kasa, idannuwansa ya

dan bude kafin ya ce" kudin account din ki sun yi kasa ne?

Wani abu ta ji marar dadi a ranta, tabas tana yawan yi masa biyaya idan tana son kudi, aman ita yanzu bama kudin ya kawota ba, gannin baya gida ne ya fara daga mata hankali,
A hankali ta kai hannunta bayan zip dinta ta zuge shi har kasa, ta ja rigar ta cire ta shiga nufo shi tana mai kokarin jan ra.ayinsa,

Bai wani kawar da kai ba, sai da ya kureta da kallon tsaf kafin ya saki wani murmushi irin na ka raina abu ya juya ya fice a dakin ya barta nan tsaye tamkar mutun mutuni,

Ido ta kwalalo da matsanancin mamaki ta kwala wani ihu kafin tace" walahi ban yarda ba, kai ka ga haka ka tsalake? Kawai ka tare da wata yar iskar, walahi sai na bika na gani,

Wardugu na jan dankareriyar motarsa ya fice Walynma ta fito da tata ko dan kwali babu saman kanta tsabar neman fitina da jayowa kai fitina ta shiga bin bayansa a hankali inda ya ganta ta miroir tunda danja ta tsayar da shi,
Murmushi ya saki mai tsada kafin ya ciro wayarsa ya nemo lambar Basma a cikin whatsupp dinsa ya danna mata kira

Ka na rana, in sha Allah za.a samu na dare

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀️IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤️*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

Motar na saka hancinta cikin gidan *Hatimi* ta rike hannun mijinta gam,
Shima din a zaunen kawai yake aman du gani yake ba.a sauri an kasa karasawa,

Anna dake tsaye a falon sarki dan baki daya can ya dugunzuma su sai kallon kofa take tana kai kawo ,

Turo kofar da aka yi ne ya saka ta tasayawa cak tana kallo ,
Direban ya fara shigowa kafin *Gukunni* sai *Hatimi*,

Dan tsai suka yi kafin Hatimi ta daga kafa da sauri sauri jikinta na bari ta karasa wajen Anna da kafafuwanta suka kasa dagawa daga tsayuwar ,
Tana zuwa rungumeta a jikinta inda Gukunnima ya karaso kafafuwansa na hardewa ya hadasu su duka ya rungume,

Ido kawai ta lumshe wanda jin nauyinta ya yi yawa ya saka Hatimi sasauta rikon da tai mata tana talafeta tana faman kufce mata dan ta yi nauyi da yawa,
Da kyar suka samu suka talafota, Anna ta suma
Nan fa hankali ya tashi sai ihun a fitar da mota a tafi asibiti suke suna talafe da ita a jikinsu,

Sarki je ya karaso da ruwa da sauri aka shafa mata
Wani irin numfashi ta ja kafin take buda idannuwanta a rikice irin farkawar sumarnan da mutun ke yi.

Ganninta jikin mahaifinta , wanda yake da dan gemu kadan fari wato furfura sai girarsa da ta fara farin itama, sai hannun mahaifiyarta fa dake jimke da nata ta dan daga a hankali ta ga hannun ya dan fara yakushewa irin na tsufan nan,
Kuka ta fashe da shi tana kara shigewa jikinsu, ji take tamkar idan ta sake su zasu bace a gabanta ne, dan haka ta ririke su tana kallonsu tana kara shigewa jikinsu

Sun jima a wannan yannayi, inda yayanta ke zaune can gefe , kukan yarima jariri ne ya fargar da su inda Anna sai a lokacin ta tuna da y'ayanta,
Dan sasauta rikon ta yi masu gannin ana dan waiwayawa inda yaran nata suke zazaune suna fama mimika Yarima boy sunna jijiga shi a tsakaninsu,
Tsare su Hatimi ta yi da ido kafin a hankali ta dawo da dubanta wajen Anna,
Murya na rawa ta ce" *Allatchi?*, ina kika shiga kika barmu cikin tashin hankali da rashin nutsuwar zuciya?

Anna ta tsareta da idon itama,

Gukunni ya riko hannunta ya ce" Allatchi, kin san irin tashin hankalin da na shiga dalilin dawowa daga wajen aiki da na yi na tarar da anmanki da *Herde* tsakar gida suna kuka wai baki motarki aka ganni a kofar gida aman ke baki dawo ba kuma wayarki bata shiga? Ina kika je?

Anna ta sada idannuwanta kafin a hankali ta ce" ban san da me ya juyar da hankalina ba, wanda tunda na baiwa gida baya ban san takamaiman abinda ya faru da ni ba sai nan da kwana goma na dawo hayacina, hasalima ban san *zaman da na yi da shi na shekara da shekaru ko da aure muka yi shi ko kuwa zaman haka muka yi?* , gashi harda y'aya suma sun fara haihuwa,

Zabura Gukunni ya yi ya mike tsaye, nan da nan jikinsa ya dauki rawar bacin rai da tashin hankali, murya bace ya ce" waye? Dan gidan waye? Wanene ubansa da kuma shi din kansa? Ko wanene ina mai tabatar maki da sai dai a yi daya cikin ni da shi, sai na rufe shi rufewar da ba zai fito ba sai dai a fitar da shi!, koda ya ki fitowa yaransa zan rufe sai ya bayanar da kansa! Sai na nuna masa danyen kai koda ubanshi sarki ne!

Anna dake zaune ta dago da kanta da sauri gabanta na faduwa, muryarta na rawa ta ce" yaranshi? Ko yarana? Abanna, bai damu da yaren ba dan ya yi rayuwarsa ne ta hanyar siyar da su, wato yana karbar sadakin yarana a tafi da su shikennan , ba sai ua damu da yaranba zai damu dan an rufe su? Aa ba za.a taba mini yaranna ba dan ina son su!
Ta karashe tana mai fashewa da kuka ta ce" mun yi rayuwa cikin dajin Timiya,
*Algabitt* ya kasance dodo , kura, fitina a rayuwarmu ni da yaranna,

*Algabit?* Hatimi ta tambaya tana mai son karin bayani kan waye hakan? Dan ta manta, bata taba kawowa a ranta ba,

Anna ta dubeta da kyau ta ce" Algabitt wanda Muka kade da Mota ni da Herde daga karshe Abanna ya dauke shi aiki a gida,

Hatimima mikewar ta yi a tsorace tana fitar da idannuwanta baki daya tana kallon Anna,

Anna ta dago kanta ta shiga kora masu dukan abubuwan da kwakwaluwarta ke iya tinnawa,

Mahaifiyarta kawai mutuwar tsaye ta yi, dan abin ya mugun daketa, wai Algabitt? Yaron da ta dauka tamkar dan gida? Eh lale aikinsa baiwa fulawowi ruwa, aman tunda ta ga y'ayanta na son lamarinsa ta yarge masa shiga falonsu, a zauna da shi a sha dariya,  bale da ya fada masu shi maraya ne shikennan suka kara yarda da shi duda wani lokacin mahaifin su Anna na fadin yaron nan yanada wani kallo irin na munafukai, sai ta yi daria ta jinjina hannunta tana fadin sai alkalina, kai fa ka saka na aminta da mu dauko yaronnan, sai yanzu da muka shaku da shi kai kuwa ka fara hango wani abin?

Bayan Anna ta yi shiru da labarinta Hatimi ta duka inda take zaune ta jata jikinta irin rarashi,

Gukunni kuwa sai wani irin numfashi yake fitarwa na bacin rai, bai ko kalli inda su Gaishata suke ba, dan shi kama suke masa da yaron, sai yanzu ya tina yaron, kam, lale haduwarsa da wannan bakin macijin za.a sha mamaki,

Hatimi ta dago tana share hawayenta ta ce" Gukunni, ka yi hakuri, yanzun ya dace mu yi murnar ganninta, na tabata asiri yayi mata, mu yi fatan da aure ya rayu da ita , mu rungumi jikokinmu, na san Herde sai ta fi kowa murnar yarannan , ta kwashi yayan wasuma bare na yar uwarta wace suka shaku ? Ai ni da zaka amince minma da ba zamu wani yi shara.a da wannan yaro ba, idan har ya sanar mana gaskiyar da aure ya rayu da ita? Ya sawake mata salim alim ya je, duniya ce, sannan mai duka na madakata, ya je ya yi abinda yake so idan tunaninka kai din wani shege ne a duniya toh tabasa akoy wanda ya dameka ya shanye, ba zan yi shara.a da shi ba, bai isa ba, cuta ya gama cutata , sai dai na gode Allah da tun kasa bata rufe mani idannu ba Allah ya bayanar min da ita,

Gukunni ya juya yana kallon su Agaishat , ya juya wajen su sarki dake zaune sun yi zuru suma, Da kai Sarki ya jinjina masa irin nuni da ya yi hakuri, ya tausasa zuciyarsa,

Dan yatsansa karami ya dantsa a bakinsa kafin ya kada kai ya nufi wajen su Agaishat da suka tsurewa nufo sun da ya yi,

Yana zuwa ya duka ya dauki Yarima Boy dake kuka ya juya ya fice a falon da shi,

Murmushi Hatimi ta yi tana duban su ta ce" zai huce, ko dan dan jaririn wannan fushinsa ba zai yi tsayi ba, dan yana son yara kamar me, burinsa ya samu dan jika ,

Sarki ya sauke ajiyar zuciya, ya kuma kiran uwar gidansa domin ba a gabanta akai komai ba,

Tana zuwa ya umarceta da ta baiwa baki wajen hutawa,

Dukansu suka mike suka je bangaren sauke bakin alfarma aka basu dakunna wanda matar sarki ta nuna masu kowa dadaya, aman Anna ta kiya kan su hade suka,

Hakan kuwa aka yi dan haka sai aka shigo da sauran gadajen dan dakunnan akoy girma aka yi masu shinfidun alfarma inda suka shiga gaba dayansu,
Sai a lokacin Hatimi ta zo wajen su Agaishat dake tare waje guda ta zauna tana kallonsu,
A hankali ta ringa rungumarsu tana tausaya masu, zuka zukan yan mata ya wannan aman a cikin duhun kai, suturun jikinsuma abin tausayi wai a nan sun wanku ne? , ko.ina yar uwar tasu take ita? Shiga halin kaka naka yi har ka cire da ka mika kyauta, karshe a zo a aure shi bada izini ko saninka ba sai komai ya wakana a sanar da kai,
Kai bata tunanin akoy kotun da zata iya yi mata shari.a da Algabitt a nan gidan duniya.

*NIAMEY*

Jakar hannunsa ya yar a nan ya shige dakansa yana yatsina fuska dan kyankyamin wajen yake,

Samu ya yi ya buda wajen tufafinsa ya ciro kaya masu tsafta
Yana kokarin rufewa ta shigo dakin, yauma dai cikin kwaliyar take duda bata san da zuwansa ba,
Walyn kam akoy kama jiki, akoy kanshi, akoy iya kwaliya,

Karasa shigowa ta yi tana duban hannunsa da mamaki, wasu kayan ne ya dauka, ina zai je kuma? Shida yanzu shigowarsa har zai juya?
Da sauri ta idasa kusa da shi tana mika hannu wajen kayan ta ce" Wardugu, ina zaka je? Dan Allah yanzu fa ka dawo, daga ina kake haka wajen sati uku? Kuma ka dawo yanzu ka kuma fita?

Bai tsaya sauraronta ba ya goce kar ta karbi kayan ya rabata zai fice
Hankalinta ne ya kara tashi, ta san waye mijinta wajen harkar mu.amalarsa da matarsa(aurataya), aman yanzu har tsayin wannan lokacin bai wani nemeta ba?

Da sauri ta je ta bayansa ta rungume shi, hannunsa ta kamo ta dora saman rigarta wajen mararta ta ce" baka tambayi ajiyarka ba zaka tafi? Baka damu da cikinka dake jikina ba?

Wardugu ya janye hannunsa ya juyo yana kallonta tun daga kanta har kasa, idannuwansa ya dan bude kafin ya ce" kudin account din ki sun yi kasa ne?

Wani abu ta ji marar dadi a ranta, tabas tana yawan yi masa biyaya idan tana son kudi, aman ita yanzu bama kudin ya kawota ba, gannin baya gida ne ya fara daga mata hankali,
A hankali ta kai hannunta bayan zip dinta ta zuge shi har kasa, ta ja rigar ta cire ta shiga nufo shi tana mai kokarin jan ra.ayinsa,

Bai wani kawar da kai ba, sai da ya kureta da kallon tsaf kafin ya saki wani murmushi irin na ka raina abu ya juya ya fice a dakin ya barta nan tsaye tamkar mutun mutuni,

Ido ta kwalalo da matsanancin mamaki ta kwala wani ihu kafin tace" walahi ban yarda ba, kai ka ga haka ka tsalake? Kawai ka tare da wata yar iskar, walahi sai na bika na gani,

Wardugu na jan dankareriyar motarsa ya fice Walynma ta fito da tata ko dan kwali babu saman kanta tsabar neman fitina da jayowa kai fitina ta shiga bin bayansa a hankali inda ya ganta ta miroir tunda danja ta tsayar da shi,
Murmushi ya saki mai tsada kafin ya ciro wayarsa ya nemo lambar Basma a cikin whatsupp dinsa ya danna mata kira

Ka na rana, in sha Allah za.a samu na dare

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

6️⃣1️⃣

Hanya ya canza ya dauki ta gidan minister,
Kiran da ya yi mata daya kwal ta daga ya fada mata yana anguwarsu kishi ya kama shi yana muradin ruwa,

Abinka da yan gayu, dama a wanke take a lume cikin katuwar kujerar falonsu, tana jin haka ta mike da gudu ta haye sama ta feshe jikinta da turare ta ajiye wayarta ta sauko kicin ta dauki faranti fari ta dora goran ruwan Awa, ta kuma kiran saurayinta da zai zo zance cewar kar ya zo ta fita!

Dan nesa da gidan ya tsaya, domin a kofar gidan gwomnatin yaransa ne ke gadi suna baiwa gidan tsaro,
Yana nan zaune yana hangen Motar Walyn sannan ya dan dago ya hangota ta fito daga gidan nasu,

Cancandi inji ni, yarinyar fa ta gama haduwa, farin ne? Tana da shi, kyan ne? Ta gaje shi, tsarin halitar ne? Ta ninka Walyn sau biyu, yarinya Shuwa Arab, gashinta ta yi kwaliya da shi ta sake shi, taku take da dogon takalminta dan kara jan ra.ayinsa, inda ya kawar da kansa daga dubanta , wani uban tsaki ya jawa kansa, wani haushin kansa ya ji a lokacin da zuciyarsa ta raya masa wani lamari a kan wada ba zai so zuciyarsa ta falasa shi ba, zuciyarsa ce ta hasko masa gudunta na dazu da rigar dake jikinta Blue mai ruwan samaniya, zuciyarsa ta fada cewa" ta zarce misali,
Idannuwansa ya rintse daidai nan ya ji tana buga masa glas din mota,

Cire lock din ya yi dan haka ta bude ta taka ta shiga
Tana shiga ta juyo da ruwan da iya kwarkwasar da ta san tana tafia da duban samari ta yi masa salama,

Dubanta ya yi irin na tsaf din nan kafin yake karbar ruwan ya yi mata nuni da tana iya tafia,

Ido ta zaro kafi ta shagwabe fuska ta ce" haba abincin ruhina, daga zuwa sai ka kore ni?

Wardugu ya hade fuska ya ce" fitarmin a mota na ce!

Da sauri ta kama marfin motar ta dira daga motar tana kallonsa ya watsa mata wani kallon kyama ya yi ribos ya nufi hotel dan ba zai iya kwana a gidan ba ya yi masa dati,

Walyn kam kamar mahaukaciya ta tada motar tana zabga gudun sai ta kamo shi , ta yiwa yarinyar kuma kallon tsaf tana kwafa kan zata dawo gareta

Yana tsayawa da mota ya fito, ta fito da sauri ko rufe motar batai ba ta tunkaro shi

Sai dai kafin ta karaso yannayin fuskarsa ya saka ta rage saurin da take,
A haka ya shiga cikin Hotel din inda take binsa da sasarfa

Du daki daya kwana daya jika dari uku ne , ky ya karba ya juya ya je wajen accenseur ya shiga,

Tana tsaye har ta ga wajen da ya tsaya ya nuna ya dawo ta danna itama ta shiga ya daga da ita,
Yana budewa ta sako kafarta guda wajen ta ji an yi sama da ita sannan an rufe bakinta,

Wutsil wutsil take har ya shiga dakin ya direta saman kujera,
Kafarsa guda ya dora gefen kujerar yana dubanta kafin ya ce" ke, kin raina ni ko?

Fashewa ta yi da kuka , tana kuka ta ce" yanzu wardugu amanata kake ci? Budurwa ka yi? Wannan yarinyar dake yawo itace ta dauke min hankalinka har sati uku? Wardugu cikinka nake dauke da shi fa? Wardugu kai fa batube ne, ka san ko a al.adunmu ba.a yiwa mace kishiya sai ta haihu kamar uku ko hudu, yanzu Wardugu ko cikin na fari bai fito a jikina ba ka fara zuwa

wajen budurwa ka yi zamanka ka manta da ni du irin kiran da na yi ta yi maka?

Sai da ta kare magangannunta ya ce" auren zobe na yi da ke?

Ni ka daina fadin maganar auren zobe, ba wani auren zobe, ai mu ba auren zobe ya kawo mana wannan ba, al.adunmu suka hana.

Adini ne? Ya fada yana kara tsareta da ido,

Walahi ba adini bane aman muna rike da su da karfin gaske, kuma ko Ayya ba zata bari ka taka su ba, ta fada tana son kauce dubansa dan ba zata iya ba,

Wardugu ya yi murmushi ya nunota da yatsarsa manuniya ya ce" Baki da kunya Walyn, Ayyata kike nufi? Wace kika raina,

Walyn ta ce " ni ban raina Ayya ba, ba zan taba iya rainata ba.

Kansa ya girgiza ya sauke kafarsa ya tsaya gabanta ya ce" kin san me? Nifa da a tsarina babu maganar na auri macen da ta furtan kalmar so , gaskiya wayewata bata barina gannin matar nan a mace, kema kin shigeni da yawa ne

Kin gane, ina son mace mai aji , wace ta san kanta,

Walyn ta mike ta ce" ai koda ni na fara cewa ina sonka kaima daga baya kace kana so na,, Wardugu walahi in dai ina raye ba kai ba wata mace a duniya sai ni,

Wardugu ya yi murmushi yana kallon yanda take girgiza ita ga marar kunya, kansa ya kada ya shiga cire rigarsa ya ce" je ki,

Walyn ta dube shi, ta je fa?

Wardugu da ya gama balewa ya juyo yana dubanta tana dubansa ya ce" ki tafi.

Walyn ta ce" aman ka san idan na fita yanzu za.a rufeni ne ko? Dan umarninka ne,

Wardugu ya daga kafada ya ce" eh ki je,

Ido ta shiga kikiftawa tana dubansa, matsowa ta yi tana dubansa ta ce" Wardugu, shin baka san ciwona bane? Ai ko albarkacin cikinka dake jikina sai ka sasauta mini,

Wardugu ya buga wayarsa dake hannunsa da kasa ya yi taku biyu ya shaketa ya kaita jikin bangon dakin ya hadeta ya firfito mata idannuwansa baki daya ya daga murya ya ce" bayan wanda kika zubar? Ke daba baki da hankali? Kina tunanin zan aureki na sakeki sakaka kina

yawo tamkar tinkiya? Du motsinki, du abubuwan da kike ina sane da ke, wada ta nuna maki hanyar zubar da cikin tana rufe, ke da kika zubar ba sai na kara kwonciya da ke ba bale ki kara daukan cikin? Walyn kauce maki nake kina biyo ni a filin rashin mutunci? Kin manta waye ni? Halaya basa sakewa sai dai a sada kai dan kunya! Ke taraki nake, bana son ki ga ranar da zan dago ki, kike ikirarin aure? Toh bari ki ji ba.a yi ba ba za.a yi ba macen da zata dora min dokar ba zan kara aure ba tunda ba dokar Allah bace,
Zan dauki yan aiki mata a gidana daga gobe tunda ke baki san ana daga maki kafa ba, yan mata zan kula na ga me zaki yi?  Walyn ikirarinki ki soke ki kashe ko? Ni da ke za.a ga ainahin asalin batube, zamu gwada sokewar!

Cikata ya yi ta zube wajen tamkar mataciya tana jan numfashi ya dauki ky din motarsa da carte dinsa ya fice a dakin ya yi tafiarsa

Wakyn kam suma ta yi na dan lokaci kafin take dawowa hayacinta,
Ta jima kwonce kafin take janyo numfashi ta zabura tana zaro ido tana neman inda yake, hannayenta biyu ta dora saman kanta , ya sani? Ya san na zubda cikin? Ya sani? Wayo na shiga uku,

Da kyar ta iya rarumar ky dinta tana dingisawa ta fito ta shiga motarta ta tayar tana tafe tana labe labe har ta karasa gidansu

Wardugu kam a nan cikin mota ya kwana idonsa biyu yana duban titi, da safe bayan ya dawo daga masalaci ya shiga motarsa ya tayar, kokarin harbata titi yake ya dan yi tsai ya afka tunani:
Tun yana can aka turo masa bayanin an maidota asibiti tana zubar da jini,
Doctern da ya dubata aka turawa wardugu numbersa, nan yake shaida masa maganin zubar da ciki ta sha,
A hankali Wardugu ya binkita ya gane da wa da wa ta yi mu.amala har aka gano masa wanda ta kaita da wanda ya siyar mata,
Su duka aka rufe ita kuwa ya yi murmushi cewar zata gaje kurenta, daga lokacin ne ma ya kara daukar niyar sai ya kara aure koda zata mutu, kuma ba zai saketa ba su je zuwa tunda har shi zata zubar da cikinsa dan wani shirme nata na kar ta haihu da wuri ya kara aure? Zai kula matan ya ga wanda zai hana shi!,

Kansa ya girgiza a zaune a motarnan, yaushema aka yi aurensa da Walyn? Yarinyar da ta nuna masa zata rayu da shi komai bakin halinsa? Ta shanye wulakancinsa? Yanzu ta zame masa fitinaniya?  Shi kam baya ra.ayin sakinta, da zata gyara halayenta ma zai rayu da ita a haka, aman ba zai daina kudirinsa na aure ba.

To wa zaka aura? Ya yiwa kansa tambayar nan,
Basma? , ko cikin sauran yan matan? Ko zuwa kake ka samu wata yar liman ka aura?

Murmushi ya yi gannin du sai ture shawarwarin zuciyarsa ke yi, a fili ya furta" ke ki nutsu, *wada kike hange ba zai yiwu ba, domin ko ba ransa ta taba zama tasa*

(Toh Fa)

Sai wajen karfe goma na safe Ayya ta shiga dakin Agaishat,

Zaune ta sameta tana kallon waje guda,
Ayya ta karasa ta zauna kusa da ita,
Hannunta ta kamo tana dubanta , da dukan kulawa ta ce" Agaishat, ki yi hakuri, ki yi hakuri, ki barwa Allah kin ji? Bana tunnanin saka lamarinnan a rai zai saka ki ji sanyi, ki dauka lokacin mutuwar aurenki ne ya yi ba dan wani mugun halaya ko wani abin ba, ki roki Allah ya maye maki gurbinsa da wanda ya fi zama alkhairi , ki yafe min kin ji?

Agaishat ta matsa ta dora kanta a cinyar Ayya, murya na rawa ta ce" Ayya ba abinda kikai min, na tsorata sosai da jin wai ya sake ni, Ayya na yi tir da rashin ilimina, da zan samu na je makaranta da na ji dadi, dan bana son a sake maimaita min abinda akai min Ayya, ashe zaune nake gidan mutumen da ya sake ni? Kuma ya kasa dubana ya fada min ya sake ni? Me na yi da zafi haka? Wannan lamari ya girgizani Ayya,

Ayya ta lumshe ido tana shafa kan Agaishat ta ce" in sha Allah, da aljihuna, da lokacina zasu kare a kanki har sai kin samu ilimi, fatana ki yi hakuri , ki daina damuwa,

Agaishat ta kara kwontar da kanta tana jin wasu hawaye masu dumi na gangaro mata daga gurbin idannuwanta, ba zata so ta rayu kamar mahaifiyarta ba, ka zama tamkar abin wasan namiji? Ai matayenku ba takalmanku ba aka ce, abokan rayuwarku ne, idan dadi bai hadata da miji ba, ba zata so ta yi rayuwar wulakanci da shi ba.

Paris

Yau kwana na uku kennan Mu.azam baya gannin Wardugu ba kuma ya gannin Agaishat sun zo ganninsa sai Marahutt dake nan wanda shima yace zai juya a gobe tunda jikin da sauki,

Ya tambayi khadija sai dai gargadin likita ya saka bata ce masa komai ba, daga nan ya gane kawai Wardugu ya ga sakonsa.

Marahutt dake tsaye kan lamarin Mu.azam khadija ta fada masa komai, ya ji ba dadi sosai abinda Mu.azam din yayi, aman ya yi masa uzuri da jiran jin bayaninsa ta waya dan juyawa zai yi gida

Mu.azam ya birkicewa Khadija sai da ta bashi wayarsa , nan ya yi ta gwada kiran number Wardugu aman amsar daya ce ba zai same shi ba.
Abinda ba.a so din ne dan kuwa ya fara tada hankalinsa , dan ya kasa samun nutsuwa dalilin rasa Wardugu har kansa ya fara ciwo

Hakan ya daga hankalin su Marahutt dan haka ya shirya ya juya gida, wato niger

Direct office din Wardugu ya je, nan ya same shi yana cikin aiki,

Kamar yanda ya saba hawo shi kai tsaye , yanzun ma kai tsayan ya hau shi inda ya dana vidio call ya ajiye masa ya fice a office din,

Kaĺlon junna suke ,
A hankali Mu.azam ya ce" ka yafe mini War, ka yafe mini na roke ka,

Wardugu bai bashi amsa ba sai kallonshi da yake

Mu.azam ya ce" ya kake so na rayu da macen da ka fini son ta?

Wardugu ya mike tsaye yana dubansa kafin cikin karaji ya ce" *Ni na fada maka ina son ta?* *a ina muka taba yi da kai cewar ina son ta?*

🙄🙄

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

Ka kasance mai zama da mutun da zuciya daya, na yi imanin koda wani ya zo rayuwarka dan ya cutar da kai Allah zai kare ka👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻

Mu.azam ya rintse ido dan harga Allah baya son yannayin wardugu na fushi, shi walahi tsoronsa yake,
Tausasa murya ya yi ya ce" Wardugu nine fa? Ni ne Mu.azam,

Idan kaine Mu.azam sai aka yi yaya? Ko an fada maka dan kai ne Mu.azam shikennan ka san ko ni wanene? Harma ka san abinda yake raina ko me?

Mu.azam ya sauke ajiyar zuciya yana dubansa, a hankali ya ce" ka yafe mini,

Wardugu ya daki table din gabansa da hannunsa ya nuna wayar ya ce" dan ka san kana cikin halin rashin lafia ka yi min wannan gangancin?
Mu.azam baka da huja, hujarka bata da wani ma.ana, ya zaka saki yarinyar da na je na karbo amanar aurenta wajen iyayenta a gabanka wai kan wata banzar hujarka ni Wardugu ina son ta?,

Mu.azam ya yi shiru yana duban wayar,

Wardugu ya dan rage ihun bacin ran aman muryarsa a kausashe ya ce" dan kana da wace kake so ka wulakanta mini ita?

Mu.azam ya kwararo ido da mamaki,
Wardugu bai barshi ya ce wani abu ba ya ci gaba" Mu.azam ka san irin halin da na tsinci kaina na irin kukan da ta ringa gumzawa a kanka?
 Bakai min adalci ba, baka rike min amana ba, kai ka isa ka yi hukunci ne? Kan zaton da kake?a abinda ka yi hasashe? Ko akoy wanda zai fito yace na taba fada masa ina son ta ?
Mu.azam ya talafe habarsa da hannunsa na dama yana yiwa Khadija alama da kar ta leko wayar, (😳),
Wardugu ya juya ya juyo ya tsare shi da jajayen idannuwansa ya ce"
Yau koda hakan ne, koda ace wai na taba soyaya da ita bama maganar ana tunanin ina sonta ba, Mu.azam aure? Aure abin wasa ne? Da ace ita ta fito maka da hanyoyin da suka girgizaka , da ace ita ta nuna maka kiyaya da idan ka saketa da hujar bata sonka ba zaka iya zama da ita ba hankalina zai dauka, aman Mu.azam ka saka mini ita ta yi ta kuka? Wanda yau kwana hudu tunda na ajiyeta ban koma ba dan ban san shin ta daina kukan rashinka ba ko bata daina ba?

Ni kadai nake da alhakin sakata kuka, daga lokacin da na karbo amanarta wajen mahaifiyarta ta zama abin karewana ta gaske,
Ba zan lamunta ba, ba zan iya kawar da kaina daga du wani wanda zai sakata zubar da hawaye ba!

Yana kai karshe ya datse kiran ya zauna yana saka hannunsa cikin sumar kansa,

Marahut dake daf da kofar office din, kasancewar murya dage Wardugu ya yi magana da Mu.azam ba abinda bai ji ba,

Ido ya kurawa kofar, kafin yakr kada kai ya juya ba tare da ya shiga daukar wayarsa ba, dan ya tabata idan ya shiga a haka zasu kara hawa sama ne, dan ransa a bace, kansa ya girgiza yana adu.ar Allah ya shiryi wardugu da zuciya, kuma abu gashi zahiri sai ya take sai ya ji jiki ya lalubi mutun.

Yau kwananta daya a gidan Ayya,
Tunda ta je wajen mahaifiyarta ta kora mata bayani , uwar ta buga ta buga suka ga basu da hanyar bi da ta wuce su je wajen mahaifiyarsa dan sun tabata itace kawai ke zabga masa mari ya sada kai, ta tankwasa shi ya yi koda baya so,

Ayya ta sha mamakin ganninsu, sai dai da ta ji abinda ke tafe da su, domin mahaifiyar Walyn nunawa ta yi ta zo da gaskiya dan a gaban Ayya har marin Walyn ta yi tana fadin irin gangancin da ta yi na zubar da ciki, da kukanta daa komai take rokar Ayya ta ji kanta ta kama mata, harda fadin yayan zamani ne ka haife su baka haifi halinsu ba,
Sosai ta nuna bacin ranta na irin halayan Walyn duka Ayya na kallonta,

Ayya bata da yanda zata yi, na farko dai ita ta yi imanin idan da zuciya biyu ne Allah zai iya masu, na biyu ko ba komai ta ji dadin ashe matar dan nata ta san bata kyautawa ? Duda bata nemeta ba sai a yanzu da take gannin ta masa madaukakin laifi? Na uku gaskiya ne, yayan yanzu sunna abubuwa ne gabam kansu, ba zata so a saki yar wani ba dan an saki tata bata ji dadi ba, a gaskiya sakin da akaiwa Agaishat ta ji shi har cikin ranta, dan haka ta amince ta zauna nan gidanta na dan lokaci har ta iya da lamarin Wardugu sai ta koma dakinta,

Duda ba haka suka so ba, sun so ne ta yi kiransa a lokacin ta bashi umarni, aman sai suka hakura dan matakin da suka taka na neman galaba kar ya kubuce masu,
Dalilin da ya saka Walyn ke zaune a gidan Ayya yau kwana biyu, inda take cikin dakin da yake na Mu.azam, domin dakin Wardugu daman Agaishat ta zaune shi ,
Tana zaune a gidan ne ba tare da shiga sabgar kowa ba, idan lokacin cin abinci ya yi mai aiki zata je ta fada mata, wani lokacin ta fito a ci da ita inda tana ci tana dana waya, wani lokacin kuwa tace bata ci sai sun gama ci ta zo ta diba ta ci,

Sai abinda ke bata mamaki irin yanda yarinyar nan yar kauye da suka dauko ta zama, duka dukama wani lokaci ta dauka a gidan? Aman cikin ikon Allah yarinyar ta wanku ta zama wata

big girls irin yayan yan gayun nan, komanta irin na yan gayu ne, ita tambayace cike da cikinta, ba ita bace Mu.azam ya aura? To ina Mu.azam din? Duda tana yawan zama da doguwar riga da dan kwalinta a kanta, bata wani harkar samari dan Ayya na kilaceta wai ida take, sai karatu da aka daukar mata malamar makaranta dake zuwa tana koyar da ita sau biyu a wuni dan Agaishat dai ba komai take yi ba, ita kuwa malamar apbashin koyar da agaishat din yama fi na wanda ake biyanta a makaranta , dan haka ta rike damarta take aikinta da zuciya daya inda suke bi a hankali suna karatun su,

Ba abinda ke hada su , dan walyn bata taba zuwa ta tarar da Agaishat zaune ta nuna ta san da mutun a wajen ko ta yi kata salama ba, itama Agaishat ta gwada gaisheta sau uku aman Walyn bata amsawa dan haka sai ta kama kanta, domin wani yatsina fuska Walyn take idan ta ganta, wai yar kauye ta samu waje,

Zaune suke a fali, Ayya na saman kujera baba inda Agaishat ke zaune kasa da litafi a hannunta tana bitar hada sunna tana karantawa a hankali Ayya na gyara mata wajen gyarawa,

Bayan sati biyu

Fitowa ta yi ta sha shada tana baza kamshi ta dan tsaya nesa da su Ayya kadan ta ce" Ayya, zan je wajen auren kawar tawa,

Ayya ta dago tana dubanta, ta so ta share ta tafin, sai dai fa tunanin yanzu fa a wuyanta take ya saka ta ce" bari na fadawa mijinki,

Wayarta ta saka Agaishat ta dauko mata domin wayar a kashe take wajen sati biyu kennan dan kara nunawa Wardugu tsananin fushin da take ciki,

Agaishat ta mike yau kuma da yake ta san ba wani namijin dake shigo masu iya su ne, dogon wando ne jikinta mai dan santsi sannan daga kasa da irin igiyar nan ta daure kasan da shi, bai kamata ba aman ya bi shap din jikinta, sai fara kar din riga body wace bata da kwaliyar komai jikinta, sai dan kwali karami da ta yane gaban goshinta da shi , idan ka ganta kamar irin beautiful din balck americain din nan, ga kamshin turaran wankanta mai karawa fata santsi da take bazawa du idan ta gita,

Da ido Walyn ta bita kafin take yatsina fuska, kamar tace a barshi kar a yi kiransa dan bata so, ko da wasa bata shirya tarbansa a yanzu yanzu ba, ita gaba ta kaita rashin zuwansa gidan, da farko a dari dari take daga baya ta sake abinta take lamuranta hankali kwonce , ba abinda ta nema ta rasa, dan haka ta kwontar da hankalinta ta san dai ko ba jima zai nemeta tunda bai saketa ba,

Kafinma Agaishat ta dawo da wayar karan dankareren babur din nan nasa ya isar da zuwansa gidan,

Wani irin juyawa Walyn ta yi wajen kofar gabanta na faduwa da wani irin sauti da cikinta ya bada, Wardugu ne a gidan warhaka?

Ai bata san lokacin da ta cire dogon takalmin nata ta jefar nan bayan kujerar Ayya ta yi sauri ta karasa saman cafet ta zauna ba saman kujera ba,

Ayya dake binta da kallo ta dago sukai ido hudu, wata kunya ta ji ta kamata, tunda suke bata taba zama a kasa Ayya ta zauna a sama a matsayinta na wace ta girmeta bale a je ga maganar sirikarta, zama take duwaiwanta da nata ba abinda ya shafeta aman yanzu da ta ji motsin Wardugu ta zo da gudu ta zauna a kasa,

Murmushi Ayya ta yi tana waiwayawa dan jin tafiar Agaishat wato ta dauko wayar,

Tana saukowa shi kuwa yana shigowa,
Matatakalar ba a saitin kofar shigowar take ba aman dan fitina idannuwansa suka hasko masa ita ta cikin bakin gilashin da ya saka,

Kara kicin kicin ya yi da fuska ya maido dubansa wajen Ayya wace itama ta hade fuska inda Agaishat ta juya da gudu ta koma dan saka hijab

Harga Allah bai ga Walyn ba, domin tunaninsa ba zai taba kawo masa wai Walyn na zaune a gidansu ba, sannan Walyn a kasa a zaune? Bai kawowa ransa haka ba, dan haka ya karasa kujerar dake facing din Ayya ya zauna yana kallon Fuskar Ayya, a ransa ya ayyana bata huce ba dai,

Murmushi ya yi kafin ya ce" Maman Wardugu barka da yama,

Ayya ta zabga masa harara kafin ta ce" ni zaka gaisar da gilash?

Cire gilash din ya yi wanda ya saka ta ga idannuwansa sun yi ja, ko na meye oho?

Wardugu na cirewa ya ce"  ina son Ayyana 👏🏻

Ayya ta yatsina baki tana duban Walyn, hakan da ta yi ya saka shi duban inda take kallo,

Zoben hannunta na zinari ya toni ko wacece domin shi ya sayi zoben,,
Juyar da kansa ya yi tamkar bai gane wacece ba, kamarma bai ga wanda ke zaune ba,

Ayya ta girgiza kanta dan sarai ta san ya gane ko waye aman ya wani basar,
Ayya ta ce" kai, mace na karkashinka aman bata gidanka tsayin wannan lokacin baka bibiyi inda take ba? Kana da lafia kuwa Wardugu?

Wardugu ya kaleta irin kallon nan na tsai, murmushi ya yi ,

Ayya ta ce" wani ahu ta yi maka ne?

Wardugu ya girgiza kai bai yi magana ba,

Ayya ta ce" Wardugu ka min magana mana ko kurma ka zama?

Wardugu ya yi murmushi dan kuwa ko ba komai yanda ta masa magana haka ya ji dadi, dan haka ya ce" wace matata?

Ayya ta kale shi inda Walyn ta dago da sauri itama tana dubansa,

Ayya ta hade fuska ta ce" ka dauki matarka ku koma gidanku , koma me ta yi ka yi hakuri ,

Wardugu ya dago da sauri ya ce" Ayya?

Ayya ta hade fuska ta kawar da kanta ta ce" na ce ka yi hakuri.

Wardugu ya dan matso bakin kujerar,
Hannunsa mai dauke da zoben azurfa ya dago a hankali ya shafo kansa zuwa sajensa,, ya yi haka sau wajen biyu kafin yake dan dagowa ya kalli Ayya, itama shi take kallo sannan da idannuwanta ta nuna masa da ya bi umarninta,
Wani murmushi mai ciwo ya sakar mata kafin yake dan muzgutawa ya koma cikin kujerar ya zauna ,

Ayya ta dubi wajen Walyn dake zaune ta ce" ki tashi ki koma dakinki, ki kiyaye dukan abinda mahaifiyarki ta fada

Mikewa ta yi zurbat ta dan sosa kanta tana duban Ayya, aman batai masa gargadin kar ya mata wani abin ko ya daina fushin da yake da ita ba,
Sai dai ba halin ta kawo maganar domin ko a fuskar Ayyan bata ga fuska ba,
Dan haka ta samu ta raba Ayya ta fice da sauri ta shiga motarta ta nufi gidanta.

Tana fita Ayya ta maido hankalinta wajensa tana dubansa, ta sani sarai shirunnan da ya yi gwara ya yi magana, aman sai ta share, idan tana son tankwasa shi bata nuna wani tausayi ko tsoron zuciya,
Rai ta hade ta ce" an yi maka laifi mai girma, ka yi hakuri , kar ka ci gaba da nuna mata wani abin, ka kwontar da hankalinka, dukan tsanani yana tare da sauki.

Idannuwansa ya lumshe ya kai dubansa wajen matatakalar Ayya, kansa ya juyo yana duban Ayya ya ce" alfarma faya nake nema a wajenki Ayyana,

Ayya dake dubansa ta ce" wace alfarma ce?

Idan na tashi neman aure , ina so tsakanina da ke ki sanya mani albarka, ba ruwanki da maganar wani al.adu da me za.a dube ki, Ayya bafa adini bane, dan na taka ba Allah zai kama ni ba, ba kuma wani zqi hana mini ci ko sha ba, ba wanda zai hana ni shiga inda nake so, hasalima koda za.a yi da ni sai dai a yi a boye, ki toshe kunnayenki na roke ki!

Ayya ido kawai ta zuba masa, zata fi kowa murnar gannin wardugunta ya samu wani canji bangaren mata,
Ya kasance mai farin jinnin mata, suna likun masa a duk inda ya saka kafarsa, sai dai abin takaicin cikin matan nan wa.inda ya samu wani kusanci da su du sun saka ya ji dan damanma, har yanaiwa mata kallon zuma daga nesa, idan suka karaso gareka sun zama madaci,
Me ya rasa? Ya kasance namiji har namiji sai dai ya rasa macen mutunci,

Ya mace zata zubar da cikinka wai a zuwan ba zata haihu da wuri da kai ba dan tana maka tsananin son da ba zata so ka auri wata ba?
Ta iya zubar da gudan jininta, dan sunna dan tsaninin kishi ya zata dauki lamarin zaka auri wata?
Danma a haka wai tana shayinsa, du haukanta tama tsoron su hade daga ita sai shi idan ta yi masa laifi, aman lamarinta na saka Ayya a shakun jin wai wardugu zai dubi wata bare ya aureta,
Sai dai ina, ba zata shiga hakinsa ba , ba zata shiga ba, ya isa haka, harda laifinta irin yanda take tsawata masa idan ya dace ya hukuntata, ta samu damar da take sakawa ranta ita daya kwal ta ishe shi ko kowa ya rasa,

Ajiyar zuciya ta sauke tana kawar da kanta, zatai ta adu.a, aman ko wacece zai aura zata hadu da fitinar matarsa sai dai idan ita dinma wata kwaron kanta ce!

Gidan su Anna

Tunda suka sauka a gidan su Anna ba rajar banza da ba za.a yi baki ba, sun zo yi masu barkar gannin y'arsu,

Abin har mamaki yake baiwa su Gaishata, sai dai duba da irin mukami da datijantakar tsohon gidan ya tarawa kansa daraja,
Wani abu dake baiwa gaishata mamaki, shi ne irin kirarin da ake yiwa mahaifiyar Anna,
Sai dai zaman da ta yi da ita na dan lokacin nan ya saka ta gane ba wai likawa aka yi ba, ta cancanci hakan ne,
Ita bata taba gannin mace irinta ba, a duniya duda tsufan da ya kamata ko me take, ko da wa take, mijin nan nata yana gaba da komai,
Wato wani irin kulawa, wani irin cancanna, wani irin salo da take bazawa a cikin gidan ba ruwanta da jikokinta ki yayanta ko wasu sirikai, ta iya tafia da mijinta a gaban kowa, kuma cikin ikon Allah du irin zafinsa idan ya kwashi zafi ya fice zatai murmushi ne idan ya je ya dawo ta bi bayansa zai fito kamar ba shi ba,

Har wani kirari take masa namijin mazaje ja gaban Hatimi aban Herde da Allatchi,
Zaka ga yana wani kayatancen murmushi,

Ko yanzu gaba ta saka Gaishata bayan ta gama lumdarta da turare, domin ita ke kula da harkar wankan jegonta koda yaushe tana daka tana lumdeta da shan zafin daki ta dubeta ta ce" ni kishiyoyinki nawa?

Gaishata ta ce" biyu,

Yara ne suma kamarki ko sun manyanta?

Gaishata ta ce" dayar na fita, dayar kuma ta manyanta,

Hatimi ta gyada kanta ta mike ta dauko wani kindirmo da ta dada ta zuba wani ruwan itace da ta dafa da kanta ta bata ta ce" ya mu.amalarki da su? Irin zumunta?

Gaishata ta ce" a gaskiya bama fada kuma bama shiga harkar juna,

Hatimi ta ce" me yasa bakwa shiga harkar juna? Kina nufin a cikin gida daya kuke aman ba ruwan kowa da kowa? Irin rayuwar idan wani na cikin wani hali ma ba ruwan dan uwansa da shi?

Gaishata ta ce" da na je na tarar da ita bata taba nunan hanyar zumunci ko akasin hakan ba, yayanta basa zuwa inda nake, hakan ya sa nima nake rayuwana, da ya kara aurema itama da ta zo bata shiga sabgarmu,

Hatimi ta tsaya tana dubanta da mamaki, kafin take cewa" kuma ya shi yake daukan haka?

Gaishata ta ce " yakan yi jajen wani lokacin, aman wani lokacin baya nunawa,

Hatimi ta girgiza kanta ta ce" bakwa tsoron Allah? Kishin ne haka ko hauka? Ku baku yi zubde zubden hauka ba , aman kuna zama tamkar masu gaba da juna? Me hakan ke nufi?????????

Gaishata ta ce" ni ban san ya zan yi ba,
Akoy lokacin da ta haihu na je barka, ina shiga aka rufe jaririn, ni kuwa da na dawo ban koma ko zaman wuni ba,
Kuma yanzu da na haihu cikinsu ba wanda ta leko ni, har ranar sunna, sai ana gobe zamu taho na ji hayaniyarsu suna fadan dan me zai biyo mu, shi kuwa ya fada masu ba zai iya zama ba

Ajiyar zuciya ta sauke ta umarceta da ta shiga wanka, ita kuma ta fita ta je ta dauki waya suka gama waya da wanda ta saka a kawo sabin kayan daki dan canzawa gaishata idan ta tashi komawa, sannan ta je tsakar gida ta fice yan matan biyu wato su mariama suna ta dariya da

aku suna magana yana maimaitawa,

Su Herde ta gani zaune suna hira, kanta ta girgiza ta ga halamar idan ba da gaske aka yi ba zasu daina tuno da suna kukannan ba,

Da kyar ta ga mijin nata da jikansa a cinyarsa dan jariri ya rungume, ga kuma sirikin suna zaune saman tabarmar leda kasan inuwar mangwaro suna hira a nitse,

Salama ta yi masu ta samu waje ta zauna,
Nan sarki ya mike dan basu waje

Hatimi ta dube shi ta ce" aa mai gida, ai ni da san samu na yi wajenka na zo,

Dawowa ya yi ya zauna yana dubanta,

Ajiyar zuciya ta sauke kafin ta ce" ban san ta inda zan fara ba, aman zan so ka sani ba kawo min hirar gidanka ta yi ba  hasalima mamaki ne ya ishe ni gannin garinku akoy network, kuma yarinyar nada kishiyoyi, sai dai ban ga suna wani kiran juna ba, duda da wuya idan basu da waya?
Ka yi hakuri, ina jin yaran nan har tsokar jikina, a yanzu da ta yi nesa da yan uwanta bata da kowa sai su sai kai a garin, rayuwa zai mata wahala idan ya kasance ba wani zumunci ko fahimtar junna tsakanin su,
Menene matsalar? Zan so a gane a yi masalaha tsakaninsu, dan kai namiji ne, ba koda yaushe zaka zauna ka yi hira da ita ba, duba da ba ita kadai keda kai ba, ga fita nema da sauransu.

Ajiyar zuciya sarki ya sauke, a nitse ya ce" an samu matsalar ne tun daga aurenta, ita ta nuna ba zata zauna da kishiya ba , ni kuwa na jima daman ina son na samu aurenta, shine na yi rantsuwar sai na rabu da ita idan ta kawo min wani abin a cikin maganar aurena,
Shi ne tace ba komai na je na auro yar gwal, ita kuwa zata zuba mana ido ta ga ta zaman lafia,

Hatimi ta jinjina kanta tana dubansa ta ce" eyah,
Ga tushen fadan,
Ka yi hakuri d'ana, aman na tabata kana nuna wani fifiko tsakanin su?

Gukunni dake dubansu ya kai dubansa wajen sarkin ya ce" aboki, shin ka kasance mai nuna wani wariya tsakanin matanka wanda har matan naka suka fahimta suka san ka fi son wani da wani tsakanin su??

Kansa ya sada ya shiga tunani kafin yake dagowa ya ce

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤️*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

6️⃣3️⃣

Ya jima kafin yake cewa" ni babu wani madaukakin bambanci da nake nunawa a tsakaninsu, abu daya dai na sani idan sako ne zuwa wajena fada du wace ya kasance dole sai na ji a lokacin da nake zaune da talakawa sai an bi ta kanta, wannan kuma dalilina shi ne, zata shigo min da nutsuwa koda kuwa sakon mai firgitarwa ne,

Abu na biyu, sababin suturuna na ajiye a wajenta, dan ita ke kilace min ta yi masu wajen da ba mai zuwa sai ni,

Sai idan zan yi bakin kunya, ita ke girkinsu dan ta iya girkin sannan takan sako mini a kwanon da ba zan ji kunya ba

Ni kam iya abubuwan da zan iya tinawa kennan, sai wa.inda a rashin sani ne,

Hatimi ta gyada kanta ta ce" wa ke saya masu kwanoni? Shin kai ne? Idan kai ne kana saya kowace iri guda?

Ka taba baiwa wata cikinsu ajiyar kayan aka bata? Ka nuna mata dalilin da zai sa zaka kwashe bata kula ba?

Sai maganar tarar da kai wajen taronka da talakawan garinka, shin watansu ta taba zuwar maka a hargitse ne? Ta tayar maka da hankali? Ka zaunar da su ka nuna masu ga yanda kake so su kasance idan zasu je wajenka  basu kiyaye ba?

Ajiyar zuciya ya sauke ya ce" kwanoni ni ke sayan masu du idan na shiga birni,
Nasu na bacewa ne da wuri sai su ce wai yara ke lalatawa, kuma ba ruwansu ba zasu nemi gyarawa ba idan na yi bakon sai dai na ga wani abin tashin hankali cikin har hada min marfi ake daban da kwano,

Sannan gaskiya ban taba zaunar da su na fasa masu su kilace min suturuna ba, a ganina irin girman miji a gurin matarsa har sai na fada masu haka? Da girmansu da komai? Ita ai ba fada mata na yi ba,

Sannan a gaskiya sau biyu aka yi irin ina cikin mutane, idan abin kuka ne za.a shigo mini da gudu jiki fata fata a ja a tsaya an ci damara a gwaza kuka ana jijiga , har sai na yi rarashi da roko kafin a gwaza min abinda ke faruwa, hakan ya saka na soke tarar da ni fada ,

Murmushi ta yi ta ce " ka yi hakuri mai martaba, mace du girmanta idan ta takarkare ta tafka maka wani abin wani lokacin sai ka yi mamaki,
Kar yannayin da Gaishata ke nunawa na kimtsi ya saka ka tunanin ita kadai xe kimtsatsiya a cikin matanta ko mai tarbiya, idan fa tana haka ne dan bata fara haihuwa ba?

Yau da gobe ai sai Allah, dole rayuwar yau da kulun sai ana tarowa ana gargadi, ana uzuri, ana nuna hanya, ana nuna bacin rai a abu kafin ka ga dan daidai,
Kar ka yi mamaki idan nace da kai dan daidai, domin daidai fa sai Allah, ita mace a karkace take, wata barazana ke tsoratar da ita , wata sai an nuna mata jan wuya, wata yar a bi a laluma ce, aman du miji a gidansa kafin ya zama laushi sai ya zama tauri,
Nufina a nan shi ne, kai mai mata uku reras a jere, dole sai ka cire maganar so a ranka ka kamanta adalci
Kar ka ga kamar sun nuna basu damu ba, sun damu fiye da tunaninka, kuma shirunsu halaka ne a wajenka a lahira, don kuwa idan a nan ka fi karfinsu na zasu iya yi maka komai ba a lahira fa? Kuma ba zasu taba jituwa da wada ka fifita a kansu ba,
Dole ka kwatanta zaunar da su lokaci zuwa lokaci, kanai masu nasiha, wace ta taka dokarka ko wacece ka hukuntata daidai tsarin adinni, idan ka ga lamarin zuwa wajenka sun kasa daidaitawa ka soke zuwan , koda wani irin abin ne a yi hakurin zuwanka,

Numfasawa ta yi ta dubi mijinta da ya mike da jariri a hannunsa dan ya fara dan kuka ta maido dubanta wajensa ta ce " ka yi hakuri, ina barar ka duba shawarwarina,

Murmushi ya yi yana gyada kai, shi fa wly du abubuwan sun shige masa ba wai dan bai sani ba , aa , sai irin yanda cikuluftun shara.ar mutanen garinma kadai ta ishe shi, gashi ita din irin yanda ta kasance mai masa biyaya daga bayan nan, hakan ya saka du ya watsar da wani ya zasu ji ko me suke tunani da hukuncinsa yake yanke abinsa , tabas yanzu ya yarda da laifinsa a irin zaman doya da man jan da ake a gidansa, .

Bayan wata uku

Taro ne na jama.a, datijai ne , bakake da fararan buzaye an cika kofar gidan yau asabar wajen karfe shida na yama,

Sojoji makil suna zazaune kan fafaran kujerun da aka jejera du yawanci da kayansu na aiki domin wasu daga aikin suke wasu kiwa zasu hau suka biyo wajen karbar sadakin abokin nasu,

Can kusan kofar gidan kuwa sun dukufa wakilan ango da amarya ana zantawa kafin ake miko jimgin kudin sadakin da ya baiwa jama.a da yawa mamaki, ba.a taba ji ba, yau aka fara, sadakin farar buzuwa haka?
Domin ana miko kudin mahaifin amaryar ya juyo wajen Wardugu da jimkin kudin a hannunsa , dan dukawa ya yi kusan kunnensa ya yi masa magana, inda Wardugu ya shiga gyada kai yana jinjinna girman datijon a ransa,
Kudi na mamaki har million goma ne suka zo da su a matsayin sadakin wannan zukekiyar yarinya sai dai mahaifinta ya katse masu hanzari ta hanyar irgar jika hamsin ya cire ya mika masu sauran kafin yake fadin" Allah ya saka masu Albarka, wannan ya isa sadakin *Alhinayett*, kaya ka yi mata abinda ka ga dama aman iya sadakin y'ayana kennan,

Du wajen sun yi mamaki inda suke bin datijon da kallo kafin a shiga shaidar an karbi sadaki,

Uzurinsu na bukatar a yi  auren da wuri suka kawo inda mahaifin Alhinayett ya nuna in sha Allah ba damuwa dan haka a nan ya yanke ranar aure wata guda danma ya aan ba zasu rasa dan shirshiryensu na mata ba da me zai yi jira? Shi daman baya so a saka auren yaro ya jima yana yawo da sadakin wani a kansa, kayan daki kuwa in sha Allah ba zasu gagara ba domin mahaifin Alhinayett ba wani hamshakin mai kudi bane, yana nema alhamdulilah yana samu sosai.

A wannan lokacin aka karbi sadakin mai neman auren Alhinayett wato colonel Aba gana bisa sadaki jika Hamsin , inda aka saka aure nan da Wata guda.

Wardugu ne tsaye kan lamarin nan, ba wani washe baki yake yana babaga dariya ba, aman du wanda ya sanshi idan ya ga fuskarsa zai gane yana cikin farin ciki,

Bai samu ya dan zauna ba sai da mutane suka watse , inda mahaifin Alhinayett da yan uwansa sukai ta saka masa albarka kafin yake shiga motarsa ya nufi gidan da suke yana mitar wai dan za.a kawowa mutun sadaki sai ya bar gida?

Kamar yanda ya yi tunani hakan ne,
Alhinayett bata da wasu kawaye, sai abokanannan aiki wa.inda bata fada masu ba tace sai aure

zasu ji,

Tsakar gida suka shinfida tabarma gidan kanwar matar Abansu ce mai suna Fatima zahra suka je,
Gefe sun jika zobo sun saka masa kankara suna yi suna kurba,
Gefe guda kuwa nama ne suka yanyanka suka tsitsira a tsinke Agaishat ta yi garwashi suka dora gashi saman abin gashin auntyn nasu ,
Redio ne kanwarta mai suna Sajida wato jida ta kuna sai shayin da ta dora masu wanda yake dahuwa a yar tukunyar shayi,
Su takwas ne, su uku nr zaune saman tabarmar inda Alhinayet ta sha lafaya fara kar , Sajida ta saka doguwar riga blue wace kadan ta fi gwuiwarta , Agaishat ma lafaya ta dora kan doguwar rigarta wace itama bata kai har kasa ba sannan ta dan kama jikinta ta yi mata kyau mai ruwan ja, suna zuwa suka cire lafayar suka shiga shagalinsu suna dan taba rawar buzaye domin sun saka guitar ne a redion yana tashi,
Gefe kuwa yan matan ne wa.inda kanun Alhinayett ne suma suna ta raharsu suna casunsu dan kowa murna yake domin Alhinayett ba ruwanta da wani bambaci tsakaninsu, tana taimakawa kowa da abinda Allah ya hore mata, ba ruwanta da kai kararsu, idan abin ta fada maka gaskiya ya kama zata dubeka ta fada maka sai dai idan ka gama fushin ku dawo ku shirya,

Jida wato sajida ce ta dubeta a lokacin da take ziga shayi ta ce" Aunty, wai ke ina kawayenki ne?

Agaishat dake juya naman dake saman abin gashi ta juyo itama da yaren buzanci ta ce" ba gamu ba?

Alhinayett ta girgiza kanta tana duban message din Aba tana murmushi,

Jida ta ajiye zugar shayin ta nufin Wajen Agaishat ta dan duka irin yanda Agaishat din ta yi , ta saka hannunta tana gyarawa Agaishat gashinta dake zubo mata yana faman hanata aikin da take kafin take cewa" mu? Mu fa kika ce? Ko ban san shekarunki ba na san aunty ta fi ki sosai, kawa fa kamar ana nufin kamar ni da Leila, da Nana, da Mariam, aman kin san da aunty Alhinayett bata da kawa sai aboki?

Agaishat dake jin dadin hira da yar budurwar buzuwar ta bada hankalinta kanta tana ji tamkar kanwarta da ta rasu , a hankali ta daga kai tana hangen yan matan, take yan uwanta da mahaifiyarta suka fado mata a rai, ko ina suka shiga? Wardugu ya je kauye a lokacin sarkima bai dawo ba wai sun shiga birni wajen dangin Anna, gashi ya ce zai koma aman har yau bai samu ya koma ba dan aiki ya sha kansa,
Hankalinta ta maido wajen jida da ta hi zaman yan bori gabanta ta ce" sai ki fada waye abokin nata?

Jida ta yatsina fuska tana girgiza kai irin abu ya bata takaicin nan ta ce" ko kin ji ana fadin wani Wardugu?

Agaishat ta zaro ido bata bata amsa ba,
Jida ta ci gaba da fadin" bana zaki kasa sannin General Wardugu ba, wannan gabjejen katon mai ruwan samudawa, yana nan dogon nan fari aman fuska uwa kashin safe takwaf ba annuri, ni du zaman da nake rayuwana zan ce saurayinta ne, domin dai kin ga Abanmu tsauri ne da shi baya barinmu kula maza in ba wa.inda zamu aura ba, aman abin mamaki wai shi abokinta ne, Ai ni kalonsu kawai nake, har a school ina fadawa kawayena ai yayata soyaya take da General Wardugu du wace ta taba ni zamu rufeta,
Wai kawai yanzu wai ace wani Aba? Hm na yi mamaki

Agaishat ta yi murmushin da ya bayanar da wutsiryarta ta mike dan dauko abin fifita wutar dan garwashin ya yi sanyi sai dai me? Ganinsa ta yi tsaye daga bakin kofar shigowa gidan, ya harde hannunsa saman kirjinsa, idannuwansa sanye da gilashi, aman yannayin fuskarsa kamar ita yake kallo,

Gabanta ne ta ji ya fadi, tunda suka dawo daga Paris bai fi sau a kirga ba suka hadu, ya yi tafia kan aikinsa, da ya dawoma baya wani yawan zuwa gidan sai jifa jifa  sai matarsa dake dan lekowa a tsatsaye ta fice abinta,
Kallo daya ta yi masa kafin take juyar da kanta ta nufi wajen Alhinayett ta fada mata cewar Wardugu ne, ita kuwa ta dauki lafayarta ta nada a iya kugunta ta juya neman abin hura wutar,

Alhinayett ce ta sanyo shi gidan, inda yan matan du suka shiga watsewa a hankali dan kowace ta san shi farin sanni basa son abinda zai hada su da shi, ya rage daga Alhinayett dake zaune facing dinsa, sai Agaishat da Jida dake dan nesa da su suna aikinsu na dafa shayi da Barbecue.

Gilashinsa ya cire yana duban Alhinayett kafin ya sakar mata murmushi ya ce" inyeh amarya,

Alhinayett ta turo baki ta ce" kafa ce ba zakana tsokana na ba.

Murmushi ya sakar mata ya ce" ai ba tsokana bane ,

Alhinayett ta ce" War, wai dan Allah da gaske an karbi kudin?

Wardugu ya kanance idonsa guda ya ce" ke baki da kunya ko? Da ba.a karba ba ya zaki yi?

Kafadunta ta daga ta ce" ba sai in ci gaba da zama a gidan ba, kai kuma in ci gaba da damunka ba, 🤷🏻‍♀️

Ya miko hannunsa zai lalace hancinta yana murmushi dan wani nishadi yake ji Aminiyarsa kanwarsa zata yi aure kwana kusa kennan jiddah ta kwala ihu ta shiga bura tana kokarin dage lafayar Agaishat

Agaishat din kuwa ta rintse ido ta kasa motsi inda take tsugune

Da sauri Alhinayett ta nufe su tana tambayar lafia?

Jida ta nuna mata cinyar Agaishat ta ce" ina ziga shayi ne ashe ta kawo hannunta ni kuwa na juyo shine ya zubun mata a nan,

Alhinayett ta aniya janye lafayar bayan ta dungure kan Jidda tana fadan ke komai zaki yi ba zaki yi shi hankali kwonce ba sai da katsamniya tamkar wata saniya?

Agaishat kam zufa ce ta ji a goshinta inda idonta ke rintse, dan Walahi bata ji zuwan abin ba sai zubarsa ta ji saman cinyarta , gashi ya gama tafasa kennan ga zafin shayi, ji take gaba dayama kamar kafar ce ta tsoma cikin ruwan zafi

Wardugu dake zaune bai san lokacin da ya rintse ido ba jin abinda ya faru, kokowa ya shiga yi da zuciyarsa da tunaninsa kan kar ya mike, kar ya je, kar ya je, ga kururuwar kanwar Alhinayett din nan dake kara caza masa kwakwaluwa, a hankali ya lalubi hanki yana kokari goge fuskarsa da bai san me zai goge ba wayarsa ta shiga kuka,

Lalubar wayar ya yi da sauri ya daga kiran baima tsaya gannin waye ba,

Walyn dake tuka mota ta ce " Wardugu, gamu mun fito daga gidan su Alhinayett din an ce wai ba can take ba, ina ne gidan da take mu je?

Wardugu ya shiga yi mata kwatancen gidan kafin yake datse kiran ya tsurawa yatsotsin Agaishat ido domin Alhinayett ta kawota wajen tabarmar ta zaunar da ita da kyar ta samu ta bude wajen ta saka a kawo mata ruwan gishiri ta shiga tofa mata adu.a,

A hankali idannuwansa lumshe yake kallon yatsutsan kafar nata, dogayen yatsutsan kafa gareta, wa.inda suka kawatu da faratuna masu dan tsayi farare kar kar aman can samansu da dan jan lale, kafarta ta dama na dauke da dan karamin yatsa irin shidanin nan, sai yan kananun gashi dake saman kowace yatsa luflufluf da su,
Tsikar jikinsa ne ya ji ta tashi a hankali yake kokarin kawar da kansa sai dai ruwan gushirin da Alhinayett ta zuba mata ya saka ta jimke hannun Alhinayett da hannunta guda sannan ta kawo dayan hannun wajen kafar nata mai shidanin ta damki kafar ta cije lebenta kafin take kifa kan nata saman kirjin Alhinayett ta shiga sauke ajiyar zuciya,

Zabura ya yi ya karbe kofin ruwan giahirin kafin ya zabgawa Jida wata uwar hararar da ta sakata juyawa sumui sumui ta bar wajen ta koma wajen gashinsu a ranta tana ayanna kumurci!

Tsayuwa ya yi a kansu wanda ya saka Alhinayett dagowa tana dubansa,

Murmushi ta saki kafin ta girgiza kai a ranta tana ayanna zan ga gudun ruwanka gide, in sha Allah yar buzuwa ba zata bika ba kamar yanda sauran yan matanka ke binka, da yardar Allah zaka kawo kanka ne,

A hankali ya duka ya ci fuaka ya kai hannunsa ya daga wajen da ta kone din,
Wajen ba wani tashi ya yi ba aman ya yi duhu alamun jini ya kwonta,
A rayuwarsa ya ga ciwon da ya fi wannan girma, shi kansa a jikinsa ya ji mugun ciwon  da ya fi wannan dan har harbinsa an taba yi,
Maganar zubuwar ruwan zafi kuwa idannuwansa sun ga abinda da za.a maimaita a yanzu ba zai iya fayacewa ba,
Sai dai abin mamaki wannan dan ciwo da ta ji ya ji hankalinsa ya yi mugun tashi, bai san lokacin da bakinsa ya buda ya dubi Alhinayett kan wada ya ji haushin tunda ya shigo gaisuwa daya kwal ta yi masa bata wani zo inda yake ba ta kara gaishe shi ba, ya ji bakinsa na fadin" mu kaita asibiti alhi

Alhinayett ta dube shi da mamaki, zata bashi amsa wayarsa ta kara daukan kuka,

Mikewa ya yi ya daga yana cusa hannunsa cikin sumar kansa ya amsa kiran,
Eh kawai yace kafin yake datse kiran ya juyo da dubansa wajensu inda ya sauko da gilas dinsa ya rufe jajayen idannuwansa wa.ina a yanzu ne suka dauki jan, labarin zuciyarsa ne ke isarwa gare su

Fitowa suka yi daga motar, ita da aminiyarta yar gidan gwomna matar minister,
Kowace ka duba sai ka kara duba domin tun daga suturun jikinsu zuwa kalar fatarsu da irin adon fuskarsu da takalman kafafuwansu da jakunkunnan hanayensu da irin kanshin da suke bazawa zaka gane manya ne ,

Fuska Walyn ta yatsina tana duban kawarta kafin suke bushewa da daria,
Kawar ta ce" wai ke da yarinyar yar gidan talakawa dangin talakawa ce har haka? Ke da Alhinayett din basu da komai a gari har kike tada hankalinki kar a je budurwar Oga ce?

Walyn ta yatsina fuska kafin take bushewa da daria ta ce" ba zaki gane ba, na rasa wani irin abu ne tsakaninsu, aman yau mu shiga mu keta mata rashin mutunci yar gidan taki zama!

Tafawa suka yi suka nufi yar kofar gidan da niyar shiga su shikawa Alhinayett rashin mutunci da ikirarin ta rasa wardugu sai dai yaransa (han)😬

Wayo azumi na matsowa, ni kam kamar nace da ku da sai mun hade in da ranmu bayan azumi🙁

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*
___________________________________________

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

6️⃣3️⃣

Ya jima kafin yake cewa" ni babu wani madaukakin bambanci da nake nunawa a tsakaninsu, abu daya dai na sani idan sako ne zuwa wajena fada du wace ya kasance dole sai na ji a lokacin da nake zaune da talakawa sai an bi ta kanta, wannan kuma dalilina shi ne, zata shigo min da nutsuwa koda kuwa sakon mai firgitarwa ne,

Abu na biyu, sababin suturuna na ajiye a wajenta, dan ita ke kilace min ta yi masu wajen da ba mai zuwa sai ni,

Sai idan zan yi bakin kunya, ita ke girkinsu dan ta iya girkin sannan takan sako mini a kwanon da ba zan ji kunya ba

Ni kam iya abubuwan da zan iya tinawa kennan, sai wa.inda a rashin sani ne,

Hatimi ta gyada kanta ta ce" wa ke saya masu kwanoni? Shin kai ne? Idan kai ne kana saya kowace iri guda?

Ka taba baiwa wata cikinsu ajiyar kayan aka bata? Ka nuna mata dalilin da zai sa zaka kwashe bata kula ba?

Sai maganar tarar da kai wajen taronka da talakawan garinka, shin watansu ta taba zuwar maka a hargitse ne? Ta tayar maka da hankali? Ka zaunar da su ka nuna masu ga yanda kake so su kasance idan zasu je wajenka  basu kiyaye ba?

Ajiyar zuciya ya sauke ya ce" kwanoni ni ke sayan masu du idan na shiga birni,
Nasu na bacewa ne da wuri sai su ce wai yara ke lalatawa, kuma ba ruwansu ba zasu nemi gyarawa ba idan na yi bakon sai dai na ga wani abin tashin hankali cikin har hada min marfi ake daban da kwano,

Sannan gaskiya ban taba zaunar da su na fasa masu su kilace min suturuna ba, a ganina irin girman miji a gurin matarsa har sai na fada masu haka? Da girmansu da komai? Ita ai ba fada mata na yi ba,

Sannan a gaskiya sau biyu aka yi irin ina cikin mutane, idan abin kuka ne za.a shigo mini da gudu jiki fata fata a ja a tsaya an ci damara a gwaza kuka ana jijiga , har sai na yi rarashi da roko kafin a gwaza min abinda ke faruwa, hakan ya saka na soke tarar da ni fada ,

Murmushi ta yi ta ce " ka yi hakuri mai martaba, mace du girmanta idan ta takarkare ta tafka maka wani abin wani lokacin sai ka yi mamaki,
Kar yannayin da Gaishata ke nunawa na kimtsi ya saka ka tunanin ita kadai xe kimtsatsiya a cikin matanta ko mai tarbiya, idan fa tana haka ne dan bata fara haihuwa ba?

Yau da gobe ai sai Allah, dole rayuwar yau da kulun sai ana tarowa ana gargadi, ana uzuri, ana nuna hanya, ana nuna bacin rai a abu kafin ka ga dan daidai,
Kar ka yi mamaki idan nace da kai dan daidai, domin daidai fa sai Allah, ita mace a karkace take, wata barazana ke tsoratar da ita , wata sai an nuna mata jan wuya, wata yar a bi a laluma ce, aman du miji a gidansa kafin ya zama laushi sai ya zama tauri,
Nufina a nan shi ne, kai mai mata uku reras a jere, dole sai ka cire maganar so a ranka ka kamanta adalci
Kar ka ga kamar sun nuna basu damu ba, sun damu fiye da tunaninka, kuma shirunsu halaka ne a wajenka a lahira, don kuwa idan a nan ka fi karfinsu na zasu iya yi maka komai ba a lahira fa? Kuma ba zasu taba jituwa da wada ka fifita a kansu ba,
Dole ka kwatanta zaunar da su lokaci zuwa lokaci, kanai masu nasiha, wace ta taka dokarka ko wacece ka hukuntata daidai tsarin adinni, idan ka ga lamarin zuwa wajenka sun kasa daidaitawa ka soke zuwan , koda wani irin abin ne a yi hakurin zuwanka,

Numfasawa ta yi ta dubi mijinta da ya mike da jariri a hannunsa dan ya fara dan kuka ta maido dubanta wajensa ta ce " ka yi hakuri, ina barar ka duba shawarwarina,

Murmushi ya yi yana gyada kai, shi fa wly du abubuwan sun shige masa ba wai dan bai sani ba , aa , sai irin yanda cikuluftun shara.ar mutanen garinma kadai ta ishe shi, gashi ita din irin yanda ta kasance mai masa biyaya daga bayan nan, hakan ya saka du ya watsar da wani ya

zasu ji ko me suke tunani da hukuncinsa yake yanke abinsa , tabas yanzu ya yarda da laifinsa a irin zaman doya da man jan da ake a gidansa, .

Bayan wata uku

Taro ne na jama.a, datijai ne , bakake da fararan buzaye an cika kofar gidan yau asabar wajen karfe shida na yama,

Sojoji makil suna zazaune kan fafaran kujerun da aka jejera du yawanci da kayansu na aiki domin wasu daga aikin suke wasu kiwa zasu hau suka biyo wajen karbar sadakin abokin nasu,

Can kusan kofar gidan kuwa sun dukufa wakilan ango da amarya ana zantawa kafin ake miko jimgin kudin sadakin da ya baiwa jama.a da yawa mamaki, ba.a taba ji ba, yau aka fara, sadakin farar buzuwa haka?
Domin ana miko kudin mahaifin amaryar ya juyo wajen Wardugu da jimkin kudin a hannunsa , dan dukawa ya yi kusan kunnensa ya yi masa magana, inda Wardugu ya shiga gyada kai yana jinjinna girman datijon a ransa,
Kudi na mamaki har million goma ne suka zo da su a matsayin sadakin wannan zukekiyar yarinya sai dai mahaifinta ya katse masu hanzari ta hanyar irgar jika hamsin ya cire ya mika masu sauran kafin yake fadin" Allah ya saka masu Albarka, wannan ya isa sadakin *Alhinayett*, kaya ka yi mata abinda ka ga dama aman iya sadakin y'ayana kennan,

Du wajen sun yi mamaki inda suke bin datijon da kallo kafin a shiga shaidar an karbi sadaki,

Uzurinsu na bukatar a yi  auren da wuri suka kawo inda mahaifin Alhinayett ya nuna in sha Allah ba damuwa dan haka a nan ya yanke ranar aure wata guda danma ya aan ba zasu rasa dan shirshiryensu na mata ba da me zai yi jira? Shi daman baya so a saka auren yaro ya jima yana yawo da sadakin wani a kansa, kayan daki kuwa in sha Allah ba zasu gagara ba domin mahaifin Alhinayett ba wani hamshakin mai kudi bane, yana nema alhamdulilah yana samu sosai.

A wannan lokacin aka karbi sadakin mai neman auren Alhinayett wato colonel Aba gana bisa sadaki jika Hamsin , inda aka saka aure nan da Wata guda.

Wardugu ne tsaye kan lamarin nan, ba wani washe baki yake yana babaga dariya ba, aman du wanda ya sanshi idan ya ga fuskarsa zai gane yana cikin farin ciki,

Bai samu ya dan zauna ba sai da mutane suka watse , inda mahaifin Alhinayett da yan uwansa

sukai ta saka masa albarka kafin yake shiga motarsa ya nufi gidan da suke yana mitar wai dan za.a kawowa mutun sadaki sai ya bar gida?

Kamar yanda ya yi tunani hakan ne,
Alhinayett bata da wasu kawaye, sai abokanannan aiki wa.inda bata fada masu ba tace sai aure zasu ji,

Tsakar gida suka shinfida tabarma gidan kanwar matar Abansu ce mai suna Fatima zahra suka je,
Gefe sun jika zobo sun saka masa kankara suna yi suna kurba,
Gefe guda kuwa nama ne suka yanyanka suka tsitsira a tsinke Agaishat ta yi garwashi suka dora gashi saman abin gashin auntyn nasu ,
Redio ne kanwarta mai suna Sajida wato jida ta kuna sai shayin da ta dora masu wanda yake dahuwa a yar tukunyar shayi,
Su takwas ne, su uku nr zaune saman tabarmar inda Alhinayet ta sha lafaya fara kar , Sajida ta saka doguwar riga blue wace kadan ta fi gwuiwarta , Agaishat ma lafaya ta dora kan doguwar rigarta wace itama bata kai har kasa ba sannan ta dan kama jikinta ta yi mata kyau mai ruwan ja, suna zuwa suka cire lafayar suka shiga shagalinsu suna dan taba rawar buzaye domin sun saka guitar ne a redion yana tashi,
Gefe kuwa yan matan ne wa.inda kanun Alhinayett ne suma suna ta raharsu suna casunsu dan kowa murna yake domin Alhinayett ba ruwanta da wani bambaci tsakaninsu, tana taimakawa kowa da abinda Allah ya hore mata, ba ruwanta da kai kararsu, idan abin ta fada maka gaskiya ya kama zata dubeka ta fada maka sai dai idan ka gama fushin ku dawo ku shirya,

Jida wato sajida ce ta dubeta a lokacin da take ziga shayi ta ce" Aunty, wai ke ina kawayenki ne?

Agaishat dake juya naman dake saman abin gashi ta juyo itama da yaren buzanci ta ce" ba gamu ba?

Alhinayett ta girgiza kanta tana duban message din Aba tana murmushi,

Jida ta ajiye zugar shayin ta nufin Wajen Agaishat ta dan duka irin yanda Agaishat din ta yi , ta saka hannunta tana gyarawa Agaishat gashinta dake zubo mata yana faman hanata aikin da take kafin take cewa" mu? Mu fa kika ce? Ko ban san shekarunki ba na san aunty ta fi ki sosai, kawa fa kamar ana nufin kamar ni da Leila, da Nana, da Mariam, aman kin san da aunty Alhinayett bata da kawa sai aboki?

Agaishat dake jin dadin hira da yar budurwar buzuwar ta bada hankalinta kanta tana ji tamkar kanwarta da ta rasu , a hankali ta daga kai tana hangen yan matan, take yan uwanta da mahaifiyarta suka fado mata a rai, ko ina suka shiga? Wardugu ya je kauye a lokacin sarkima bai dawo ba wai sun shiga birni wajen dangin Anna, gashi ya ce zai koma aman har yau bai samu ya koma ba dan aiki ya sha kansa,

Hankalinta ta maido wajen jida da ta hi zaman yan bori gabanta ta ce" sai ki fada waye abokin nata?

Jida ta yatsina fuska tana girgiza kai irin abu ya bata takaicin nan ta ce" ko kin ji ana fadin wani Wardugu?

Agaishat ta zaro ido bata bata amsa ba,
Jida ta ci gaba da fadin" bana zaki kasa sannin General Wardugu ba, wannan gabjejen katon mai ruwan samudawa, yana nan dogon nan fari aman fuska uwa kashin safe takwaf ba annuri, ni du zaman da nake rayuwana zan ce saurayinta ne, domin dai kin ga Abanmu tsauri ne da shi baya barinmu kula maza in ba wa.inda zamu aura ba, aman abin mamaki wai shi abokinta ne, Ai ni kalonsu kawai nake, har a school ina fadawa kawayena ai yayata soyaya take da General Wardugu du wace ta taba ni zamu rufeta,
Wai kawai yanzu wai ace wani Aba? Hm na yi mamaki

Agaishat ta yi murmushin da ya bayanar da wutsiryarta ta mike dan dauko abin fifita wutar dan garwashin ya yi sanyi sai dai me? Ganinsa ta yi tsaye daga bakin kofar shigowa gidan, ya harde hannunsa saman kirjinsa, idannuwansa sanye da gilashi, aman yannayin fuskarsa kamar ita yake kallo,

Gabanta ne ta ji ya fadi, tunda suka dawo daga Paris bai fi sau a kirga ba suka hadu, ya yi tafia kan aikinsa, da ya dawoma baya wani yawan zuwa gidan sai jifa jifa  sai matarsa dake dan lekowa a tsatsaye ta fice abinta,
Kallo daya ta yi masa kafin take juyar da kanta ta nufi wajen Alhinayett ta fada mata cewar Wardugu ne, ita kuwa ta dauki lafayarta ta nada a iya kugunta ta juya neman abin hura wutar,

Alhinayett ce ta sanyo shi gidan, inda yan matan du suka shiga watsewa a hankali dan kowace ta san shi farin sanni basa son abinda zai hada su da shi, ya rage daga Alhinayett dake zaune facing dinsa, sai Agaishat da Jida dake dan nesa da su suna aikinsu na dafa shayi da Barbecue.

Gilashinsa ya cire yana duban Alhinayett kafin ya sakar mata murmushi ya ce" inyeh amarya,

Alhinayett ta turo baki ta ce" kafa ce ba zakana tsokana na ba.

Murmushi ya sakar mata ya ce" ai ba tsokana bane ,

Alhinayett ta ce" War, wai dan Allah da gaske an karbi kudin?

Wardugu ya kanance idonsa guda ya ce" ke baki da kunya ko? Da ba.a karba ba ya zaki yi?

Kafadunta ta daga ta ce" ba sai in ci gaba da zama a gidan ba, kai kuma in ci gaba da damunka ba, 🤷🏻‍♀️

Ya miko hannunsa zai lalace hancinta yana murmushi dan wani nishadi yake ji Aminiyarsa kanwarsa zata yi aure kwana kusa kennan jiddah ta kwala ihu ta shiga bura tana kokarin dage lafayar Agaishat

Agaishat din kuwa ta rintse ido ta kasa motsi inda take tsugune

Da sauri Alhinayett ta nufe su tana tambayar lafia?

Jida ta nuna mata cinyar Agaishat ta ce" ina ziga shayi ne ashe ta kawo hannunta ni kuwa na juyo shine ya zubun mata a nan,

Alhinayett ta aniya janye lafayar bayan ta dungure kan Jidda tana fadan ke komai zaki yi ba zaki yi shi hankali kwonce ba sai da katsamniya tamkar wata saniya?

Agaishat kam zufa ce ta ji a goshinta inda idonta ke rintse, dan Walahi bata ji zuwan abin ba sai zubarsa ta ji saman cinyarta , gashi ya gama tafasa kennan ga zafin shayi, ji take gaba dayama kamar kafar ce ta tsoma cikin ruwan zafi

Wardugu dake zaune bai san lokacin da ya rintse ido ba jin abinda ya faru, kokowa ya shiga yi da zuciyarsa da tunaninsa kan kar ya mike, kar ya je, kar ya je, ga kururuwar kanwar Alhinayett din nan dake kara caza masa kwakwaluwa, a hankali ya lalubi hanki yana kokari goge fuskarsa da bai san me zai goge ba wayarsa ta shiga kuka,

Lalubar wayar ya yi da sauri ya daga kiran baima tsaya gannin waye ba,

Walyn dake tuka mota ta ce " Wardugu, gamu mun fito daga gidan su Alhinayett din an ce wai ba can take ba, ina ne gidan da take mu je?

Wardugu ya shiga yi mata kwatancen gidan kafin yake datse kiran ya tsurawa yatsotsin Agaishat ido domin Alhinayett ta kawota wajen tabarmar ta zaunar da ita da kyar ta samu ta bude wajen ta saka a kawo mata ruwan gishiri ta shiga tofa mata adu.a,

A hankali idannuwansa lumshe yake kallon yatsutsan kafar nata, dogayen yatsutsan kafa gareta, wa.inda suka kawatu da faratuna masu dan tsayi farare kar kar aman can samansu da dan jan lale, kafarta ta dama na dauke da dan karamin yatsa irin shidanin nan, sai yan kananun gashi dake saman kowace yatsa luflufluf da su,
Tsikar jikinsa ne ya ji ta tashi a hankali yake kokarin kawar da kansa sai dai ruwan gushirin da Alhinayett ta zuba mata ya saka ta jimke hannun Alhinayett da hannunta guda sannan ta kawo dayan hannun wajen kafar nata mai shidanin ta damki kafar ta cije lebenta kafin take kifa kan nata saman kirjin Alhinayett ta shiga sauke ajiyar zuciya,

Zabura ya yi ya karbe kofin ruwan giahirin kafin ya zabgawa Jida wata uwar hararar da ta sakata juyawa sumui sumui ta bar wajen ta koma wajen gashinsu a ranta tana ayanna kumurci!

Tsayuwa ya yi a kansu wanda ya saka Alhinayett dagowa tana dubansa,

Murmushi ta saki kafin ta girgiza kai a ranta tana ayanna zan ga gudun ruwanka gide, in sha Allah yar buzuwa ba zata bika ba kamar yanda sauran yan matanka ke binka, da yardar Allah zaka kawo kanka ne,

A hankali ya duka ya ci fuaka ya kai hannunsa ya daga wajen da ta kone din,
Wajen ba wani tashi ya yi ba aman ya yi duhu alamun jini ya kwonta,
A rayuwarsa ya ga ciwon da ya fi wannan girma, shi kansa a jikinsa ya ji mugun ciwon  da ya fi wannan dan har harbinsa an taba yi,
Maganar zubuwar ruwan zafi kuwa idannuwansa sun ga abinda da za.a maimaita a yanzu ba zai iya fayacewa ba,
Sai dai abin mamaki wannan dan ciwo da ta ji ya ji hankalinsa ya yi mugun tashi, bai san lokacin da bakinsa ya buda ya dubi Alhinayett kan wada ya ji haushin tunda ya shigo gaisuwa daya kwal ta yi masa bata wani zo inda yake ba ta kara gaishe shi ba, ya ji bakinsa na fadin" mu kaita asibiti alhi

Alhinayett ta dube shi da mamaki, zata bashi amsa wayarsa ta kara daukan kuka,

Mikewa ya yi ya daga yana cusa hannunsa cikin sumar kansa ya amsa kiran,
Eh kawai yace kafin yake datse kiran ya juyo da dubansa wajensu inda ya sauko da gilas dinsa ya rufe jajayen idannuwansa wa.ina a yanzu ne suka dauki jan, labarin zuciyarsa ne ke isarwa gare su

Fitowa suka yi daga motar, ita da aminiyarta yar gidan gwomna matar minister,
Kowace ka duba sai ka kara duba domin tun daga suturun jikinsu zuwa kalar fatarsu da irin adon fuskarsu da takalman kafafuwansu da jakunkunnan hanayensu da irin kanshin da suke bazawa zaka gane manya ne ,

Fuska Walyn ta yatsina tana duban kawarta kafin suke bushewa da daria,
Kawar ta ce" wai ke da yarinyar yar gidan talakawa dangin talakawa ce har haka? Ke da Alhinayett din basu da komai a gari har kike tada hankalinki kar a je budurwar Oga ce?

Walyn ta yatsina fuska kafin take bushewa da daria ta ce" ba zaki gane ba, na rasa wani irin abu ne tsakaninsu, aman yau mu shiga mu keta mata rashin mutunci yar gidan taki zama!

Tafawa suka yi suka nufi yar kofar gidan da niyar shiga su shikawa Alhinayett rashin mutunci da ikirarin ta rasa wardugu sai dai yaransa (han)😬

Wayo azumi na matsowa, ni kam kamar nace da ku da sai mun hade in da ranmu bayan azumi🙁

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤️*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

64

Zaune yake cikin talakawansa ana shari.a kan wani datijo da ya karbi kudin auren yarinyar wajensa sai da aure ya zo yace ai sai an linka kudin idan ba haka ba ba zai bayar ba, Wannan rigimar suke ciki tunda safe inda ya umarci a je a kawo masa shedun da aka karbi kudin auren a gabansu ,

Daga inda yake zaune yana iya jiyo kukan Sultan, yaron wajen Gaishata , yaron akoy rigima, baya baci kuka ne da shi sosai wanda duda da yarinya mai tayata raino aman baiwar Allah sai ramewa take dan bata son tsotsa da kuma rigimar,

Gaban goshinsa ya dan dafe yana mai jin tausayinta a ransa, shi kam Allah ya jarabe shi da son yarinyar nan a ransa, hakan ya sa komai nata ke shigarsa ba tare da ya shirya ba.

Hangen Asadeek da rakumansa suke tun daga nesa abinka da waje a bude hayam ba a kasan rumfa suke ba, har ya matso kusa da su inda suka ga ai mutun ne saman rakumin,

Mikewa dogaran suka yi suna tsayar da shi tare da tambayarsa abinda ke tafe da shi
Asadeek baban dan kasuwa ne a garin Timiyar, ya kasance makiwaci, yana kiwon rakumansa yana shiga sahara da su, a kadan idan ya yi tafia sai ya kwashe wata shida sai dai abin mamaki wannan tafiar duka duka kwanansa uku da tafia abinka da karamin gari an san kowa an san me wane ke ciki, dan haka suka shiga mamakin ganninsa a irin wannan lokacin gashi kuma dauke da mutun

Asadeek ya janyo akalar Rakuminsa ya matso kusa da su,
Kamawa suka yi aka sauke mutumen dake saman rakumin, ba rawani a kansa wanda da sauri aka shiga neman rawani dan a nada masa domin buzu ba rawani tamkar tsirara yake jin kansa , tozarci ne a gare shi, ko alwallah zai yi yana yawan yi bayan idon mutane dan kar a ganshi ba rawani,

Da sauri suka luluba masa rawani , kafin suke maida hankalinsu kan Asadeek dake gurfane gaban sarkinsa ,
Duda da yawan cikinsu sun gane ko waye a wajen, aman basu nuna ganewar tasu ba gannin sarkin bai wani gane shi ba domin ya kyankyadare ya fita a hayacinsa tun ba.a je ko.ina ba,

Asadeek ya ce" Allah ja zamani, na je wajen rijiya dibarwa rakuma ruwa na ganshi kwonce gefen rijiyar a sume, da alama ruwan ya je dina sai dai karfinsa ya kare hakan ya sa ya fadi wajen ga zafin rana ga kishirwa ga iska ga idan yama ta yi sanyin sahara ya jigata ban san adadin kwanakin da ya dauka a haka ba ni dai na yi iya yina ya farfado inda ya hada wuta ya tatsi sabon nono na dan tafasa na bashi , hakan ne ya saka ya dan dawo hayacinsa aman gashinnan baya magana sai dai bina da ido da yake sai zazabin dake ta hawa yana sauka a jikinsa,

Da tausayi Sarki ke amsawa inda ya dubi mutumen da ya yakune tsofo sak ya ce" bawan Allah daga ina? Tafia ta riskeka yankin sahara? Kai din dan ina ne?

Da mamaki dogarai ke dan kara sada kansu dan sun gane sarki bai fa gane ko waye ba, sai dogari mai maimaici da ya daga murya ya maimaita maganar sarki,

A hankali ya dago kansa inda gaba daya jikinsa ke bari ya dubi sarki, wanda hakan da ya yi ya saka sarki zabura ya mike tsaye yana dubansa,

Hannunsa ya nuna ya ce" Algabiit? Daman kai ne? Daman kana yankin timiya ko dawowa ka yi?

Algabiit dake zaro idannuwa murya irin ta wanda ya sha wahala ya dago hannunsa zai nuna sarki da yatsarsa wani yaron dogarin ya saka mafici ya buge hannun yana fadin" hatara dai

tsofo kar a nunawa mai garin timiya yatsa, kimtsa zamanka da lafazinka ga sarkin timiya

Sarki ya juyo ya yi masa wani kallo mai nuni da bai ji dadin duke hannun da aka yi ba, hakan ya sa suka kwashi masa kirari da ban hakuri,

Algabiit ya dan ja baya yana dubansu , baki na rawa ya ce" ina ka kai mini ita? Da yarana? Masu neman aurensu sun zo bakwa nan sun baza nemana kan idan ban biya ba sai dai su tafi da ni? Ina zasu kai ni? Me zasu yi mini? Ka fada mani inda suke ta bani yarana in basu ko zasu shafa mani lafia!

Sarki ya girgiza kansa yana dubansa, wato dai bai nutsu ba, alamun gajiyawar ba har cikin zuci ba,? Baya tunanin zai iya dogon bayanin fahimtar junna da wannan bawan Allah, arziki daya ya ci na haihuwar matarsa da ya yi, dan haka ya ce"
Baka da labarin ta dawo hayacinta? Tana garin Niamey gidan Kugunni ka je can ka dauko su,

Wata zabura ya yi yana dafe kirjinsa, yana duban sarki ya ce" Gukunni? Shikennan ka tona mani asiri, ka wulakanta ni, sai ka sakar mani y'ata, idan baka sakar mani y'ata ba sai na zame maka fitina a rayuwa da mulkin da kake takama da kwonciyar hankalin gidanka!

Dogarai du suka mike inda sarkin bulala ya zabura ya mike bulalar hannunsa ta shiga wulgawa tana karawa,

Sarki ya lumshe idannuwansa kafin yake budewa,
Fuska hade ya bada umarnin a shiga da Algabitt dakin sirri!

Jansa aka yi yana ihun a sake shi , aman ina ba zai iya kwatar kansa ba aka nufi dakin sirrin sarki da shi, wanda bai san wani dakin sirri a gidan ba sai yau, su kuwa suna zuwa tamkar wani kayan wanki suka jefar da shi suka fito abinsu suna baza rigunnansu, inda sarki ya ci gaba da shara.arsa kafin yake gamawa su tashi salar isha.i,
Bayan salar ne da ya shiga gida bai fito ba domin ya hada tarin gagawa na matarsa da sirikinsa da shi din kansa wanda zasu wakanar a dakin sirrinsa dake daf da shiga cikin gidan matansa.
Wannan kennan

Niamey

Kanta na rawa , dan malolon mayafinta a hannunta ta afka gidan inda kawarta ke biye da ita,
Sai dai me? Kafin take idasa shiga ba da salama ba ta hango keyarsa don ya baiwa kofar shigowar baya ne,
Bata taba sannin ta iya gagawa irin wannan ba, domin a lokaci kankani har ta ja mayafinta ta rufa a kanta sai jansa take dan ya dan sauka hakannanma, ta shiga gyara daurin dankwalinta,

sannan ta dan waiwayo dan fadawa kawarta Wardugu ne , sai dai da mamakinta ta fice tuni a gidan, wato ta yi baya, kennan ta gane ko waye,

Nutsuwa ta gayato karfi da yaji kafin take watsawa yayan buzayen harara ta kakaro murmushi ta yi salama tana karasawa gurin su, don zuwa lokacin Wardugun dai ne ke tsaye kikam cikin zafin ranar garin ya tsurawa wajen da randa take kamar hankalinsa na wajen shinkuwa idannuwansa kawai suke wajen,
Su Alhinayett kuwa suna zaune a tabarma inda Agaishat ta ja ta rufe wajen da ya bude ya ganni ta dauki wayarta dake ta ruri ta daga,

Ayya ce ke kiranta dan haka ta amsa murya sanyaye inda Ayya ta shiga tambayarta lafia? Dan muryarta ta yi mata kama da wace ta yi kuka,
Ajiyar zucia ta sauke ta ce" lafia kalau Ayanna,

Ayya ta ce" Madame Rukaya ce ta zo karbar excercice din da ta baki , ni kam ko kin yi? Kina dokin zuwa sadakin nan tun jiya?

Agaishat ta kwabe fuska ta ce" Ayya, na yi , yana cikin dakina kusan gado, Ayya ni fa ke zaki zo daukana ni dai
Ta karashe tana kyakyabe fuska irin na batatun yaran nan,

Ayya ta ce" kar na ji an min kuka, meye a su zuwa dauko ki? Da kin gama ki yi kirana zan zo na dauko ki yar autana,

Murmushi ta saki kafin su kashe wayar,

Alhinayett da ta gama amsa barkan Walyn ta dan zunguri Agaishat ta cuni mata baki ta ce" mai baci kawai,

Agaishat ta yi mata gwalo kafin take kokarin mikewa dan tunda ta juyo ta lura da uban hararar da ta samu daga wajen matar banban yaya,

Wardugu dake zaune shima saman kujerar kwal dake wajen a ransa ya ayyana ina kuma zata je?

Ta cikin gilashin yake kallon yanda da ta mike sai da ta daga hannayenta biyu ta harhada gashin kanta ta saka dan ribom dinta fari ta daure shi, sannan ta juya masu baya ta kwonce laylfayarta da kyar ta dan kakabeta a jikinta sannan ta samu ta nada kayanta har kanta,
Juyawa ta yi ta shiga dingisa kafarta ta koma wajen gashin naman dai inda Jidan dai take,
Kuma tana zuwa suka shiga kokowar sai ta karbe cokalin juyawar tana fadin ita ba dafa shayi bane aikinta,

Ina ba zai yiwu ba,

Shi ne abinda ya fada a fili, kafin yake mikeqa ya hade fuska ya ce" Ke, dawo ki zauna,

Tunda ya ce ke din, du ke din dake wajen ta dawo da hankalinta wajensa dan kar a je ita ke din yake nufi, domin ke dai lakanin suna ne da ake cewa mace halita wato Ke,

Inda hankalinsa ya fi kaiwa du suka kuma mayar da dubansa, wace qkiwa kallon itama ta ji uwa ta tsunduma a guje dan tsoron ihun da ya yi da kuma du kallon da suka yo mata,
Ajiye cokalin ta yi, zuwa lokacin du sun kawar da dubansu banda Walyn, Wardugu da Alhinayett,
Walyn mutuwar zaune ne ta yi, bata gane komai ba, aman irin ihun da ya yi kan ta zo ta zauna ya sakata itama tsura mata ido, a hankali ta maida dubanta kansa, ita din dai ya tsare da kallo har sai da ta karaso ta zauna kafin yake daukan babar wayarsa ya shiga dadanawa,

Zama ta yi tamkar mai kallon tv, don ta yi juyi ya fi a kirga tsakanin yannayin mijinta da shirun da wajen da ya yi, da yar hirar da su Alhinayett din ke yi fa yaren buzanci inda Alhinayett ta rage murya wajen fadin" ke da kika ji ciwo me ya kai ki tashi?

Agaishat ta ce" wannan har wani ciwo ne  Alhinayett? Wajen da ko tashi bai yi Allah ya yi masa tsawa? Ina dan dingisawan nan ne dan zaman da na yi kafafuwana a tankwashe sun min tsami,

Alhinayett ta ce" Eyah, ai shi Wardugu bai gane ba,

Warsugu da suke zancen da yaren buzanci shima da yaren nasu ya ce" kar ki saki ki tashi, ki zauna ya huce, kin ji na fada maki,

Agaishat ta dube shi, yanda ya yi magana da yarenta abin sai ya mugun birgeta, murmushi ta saki kafin ta kawar da kanta ta tuna ashe fa yana jin Buzanci, Allah ya taimaketa ba wani abu ta fada ba da ya ji,

Alhinayett ta kai dubanta wajen yan matan gannin sun fitar da kayan zuba abincin sannan sun fara zuba shayin sai dai du suna tsoron zuwa wajen dan Wardugu da ya hade rai,

Walyn ta hadiye wani abu a zuciyarya kafin take kokarin cicibawa ta mike tana duban Wardugu ta ce" mu tafi Wardugu dare na yi kar dare ya yi,

Dubanta ya yi da kulawa, ko dan mutanen dake wajen baya saurin gwasaleta gaban mutane, dan haka ya dubeta da kyau kafin ya ce" ke da motarki daban tawa daban, kuma ba ke kadai bace? Ki je kawai gani nan zuwa,

Tsam ta yi tana bin yan matan da kallo, yanzu a cikin wannan zuga zugan yan matan zata tafi ta bar mijinta?

Sai dai ta makaro tunda ta mike idan tace zata zauna ko wani abin za.a  samu matsala, dan

haka ta yi masa murmushi ta juya ta fice ba tare da tace da su sai an jima ko su ci kansu ba, sai Alhinayett ce tace da ita ta gode,

Bata bata amsa ba ta fice tana ta tunani ta tarar da kawarta na shating da waya inda ta gyara zamanta ta tura masa sako kamar haka" namijin duniya , jarumin jarumai, na hangoka, ka kara sacen zuciya Warduguna, ina son ka koda kuwa kai baka so na,

Hango Walyn da ta yi ya saka ta yi gagawar gogewa ta fita a whatsupp din baki daya ta daidaita kanta daga tafia yabon mijin aminiyar nata da ta afka, ita fa ta fice da class din Walyn aman saboda ta samu shiga wajen Wardugu ya saka take yawo da ita a gari,

Motar ta bude ta shiga ta rufe da karfi kafin take juya dubanta wajen kofar shigan,
Dankwalin kan nata ta tuje ta yi tsai tana tunani kafin ta dubi kawar tata ta ce" kina tunanin Warduguna zai iya kula *Bakar Mace?*

Ido ta zaro ta ce" Bak'a kuma?

Walyn ta gyada kai tana dubanta,

Shewa ta yi kafin ta juya idannuwanta ta ce" ke, kina zaune da mijin naki baki san waye shi ba? Wardugu? Mutumen da a jarida ake bayannin kasashen da ya taka? Kin san kasashen da ya je mata tamkar su suka halici kansu? Ke dan ki zama mai sa.a a cikin mata shi ne zaki yi tunanin wai Wardugu zai dubi wata bak'ar mace? Me aka yi aka yi *Bak'a*? , me zai tayar da hankalinsa ya ja ra.ayinsa a bak'a ko yar gidan uban waye? Ke a bakar mace ina jin dadi? Bare harka? Me zai duba? Bakaken yan biyun ko bakin ogan?

Daria suka kwashe da ita suka tafa kafin walyn take sauke ajiyar zuciya, aman a zuciyarta ta yi waje ta ajiye irin shiga zuciyar da *Bak'ar* yarinyar ta yi a wajen uwar mijinta da mijin nata kansa, zata so sannin asalin yarinyar duda ta ga a inda aka daukota aman bata san meye dalilin daukotan ba!

Ba wardugu ya bar gidan ba sai wajen magariba, ba komai ba kuwa ya hana shi tafia sai dan kar ta tashi ta shiga wani aikin, yana zaune ya hade rai tamkar hadarin gabas komai sai dai a kawo mata rabonta har sai da ya tashi tafia ya saka ta yi kiran Ayyanta a gabansa kafin ya fice ya bar gidan,

Alhinayett kam tunda ya fada mata aure nan da wata guda jikinta ya yi sanyi, bai ce da ita komai ba sai dai ya dubeta ya yi mata murmushi , ita kuwa du tsoro ne ya gama kasheta a zaunen da take, abin ya zo mata da gagawa, ita tsoronta Allah tsoronta auren soja!

Dare ne ya tsala, a lokacin da bayi ke hutawa shi kam juyi yake saman makeken bed dinsa,
A bukace yake da ainahin matarsa, sai dai ya jima rabonsa da ya wani kai mata kansa, idan ta

zo halas idan bata zo ba sai dai ya yi ta juyi abinsa har safiya ta yi,

Kamar daga sama ya fara jiyo kamshinta,
Lamo ya yi bai nuna zalama ba har ta karaso gareshi,
Jikinsa ta shige ta shiga kokarin sarafa shi,
Ya jima kafin yake bata amsa inda sai da suka hau sama ya mike dan saka abinda ya tsiro mata da shi tun bayan dawowarta gida, ya daina yarda ya zuba mata wani abinda ya fito daga jikinsa, danma tsaro yakan aiki da abinda zai tare masa tana jintana gani,

Mikewa ta yi tana dubansa jiki sanyaye ta ce" Wardugu, me yasa kake haka ne? Danme kake anfani da irin wannan abin bayan da matarka ta sunna kake tarawa?

Dubanta ya yi tsaf kafi yake turata baya ta fada saman bed din,
Kafin ya bi bayanta ya ce" kamar yanda kika kawo kanki a yau, haka zan yi yanda na ga yana gyara ni, ko ba komai hankalina kwonce ba sau ya rikide ya fara zama gudan jinina a markade shi ba kafin mai rikewa ta zo !

🤦‍♀️ ba zan iya fadin sunnaye gatsai ba😭

🐪🐪🐪🐪 *BAK'A CE* 🐪🐪🐪🐪

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤️*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝🏻😘

Na
*SAJIDA*

Haka walyn ta yi gum da bakinta, domin ita dai bata iya rarashin miji wai dan ta yi masa laifi komai girmansa kuwa,
Wannan laifinma da ta tafka masa, ta bi ta hanyar da baya iya ja an maidota, da baya kulata ta kuma bi ta hanyar da koke koke an yi masa tsawa, hakan ya sa ya dawo kulatan aman da nashi takun, domin idan zai yi aurataya da ita sau dubu sai ya saka roba , yana gamawa yake tashi ya bar mata dakin koda nasa ne, baya irin na da ya rungumeta a jikinsa,
Karara nisa ya shiga tsakanin su, wanda du macen arziki ta lira da irin nisan nan tsakaninta da mijinta toh fa hankalinta zai tashi ta shiga neman hanyar sulhu da gyaran abinda ya hadasa haka, aman ina, ta ci gaba ne da bibiyar dukan motsinsa, tana kaiwa du wata mu.amalarsa da mace izgili, ta ci gaba da yawon bukukuwanta, ta ci gaba da kawance da kawayen banzan da basu zauna suka baiwa cikinsu bama bale su yi tunanin gyaran aure wai har a je ga biyayar miji,
Ita dai ta fito a ganta, mawaki ya waketa, ta koma gida gida ta tarar da miji ya leleta, (Anya kuwa? Abin da kamar wuya gurguwa da auren nesa),

Haka ya gama ya sauka ya fito daga dakin da tawul a kugunsa ya nufi bayin falonsa,

Juyawa ta yi saman bed din abinta tana mai jin wani iri a jikinta dan zafi, ta jima sosai kafin take mikewa ta fito dan tafia dakinta, nan ta gansa zaune saman cafet ya lumshe idannuwansa,

Tsai ta yi ta tsura masa ido,
Tunda suka yi aure ya kasance cikin tsaf tsaf, ko dan sun raba bangare suna haduwa lokaci zuwa lokaci ne? Ba zata ce ga ranar da ta ganshi da kazanta ko ta tarar sumar kai ce ko saje bale jiki,
Yana da kula da adininsa, baya wasa da sallah da ibadun da yake a bayanne da wa.inda yake yi a boye,
Yana da fitina, rigima, tashin hankali aman fa idan an shiga hanyarsa, tabas bashi da saurin hadiye wulakanci ko.na waye, aman yana da kawar da kai, abinsa ba zai hada ka da shi ba, uwa uba mijinta tsarare ne, Allah ya yi halita mai nitsa zuciya , ko a cikin kawaye idan aka tashi maganar dogon yaro ga fari ga farin jini ga yayan banki sai an fara ajiye masa gaisuwarsa kafin a hangi wani dan tafe yake da zamaninsa, sai dai kash zuciyar nan tasa na tayar mata da hankalinta, zata so ya zama yanda take son ya zama, da ta yi ihun ta more miji,

Kafa ta saka ta fice a falon , bata wani damu da irin zamansa, da dalilin zaman ba, ita dai abinda ta saka a ranta zatana zuwa ta kawo masa kanta, ya samu nitsuwar da ba zai dubi wata y'a da wannan muradin ba, sauran zata ji da su , dan ita dai ba aikin fari take ba na baki ba, tana kwashe salarry kafin a yiwa ma.aikatan gwanati biya, tana shiga babar mota tana zuba zinaria ta saka shada, damuwarta Wardugunta, zako ta ci uwar uban du wata mai rawar kan da zata rabar mata miji!

Basa zama a kwanakin nan,
Shirye shirye suke tun karfinsu,
Ba wai wani yawon kaiwa yan mata cati ko wani gayace gayace ba, aa siyaya ne suke a hankali na abubuwan da zata bukata a gidan miji inda matar mahaifin Alhinayett ke saka su a hanya da zuciya daya tana mai basu kyawawan shawarwari,

Ayya kam ta hakura da jajen ita gaskiya a bar fitar mata da y'a gannin fitar da y'ar nata na kawo ci gaba ta hanyar kara iya mu.amala da mutane kala daban daban da take gani a wajen siyaya ne, a saloon, da wajen gyaran jikin da Alhinayett ta biya suke zuwa tare a yi masu dan kuwa itama tsale ta yi ta dire kan tana so ,

Sukan tsalake kwana biyu basu fita ba, idan aka ce zasu fita kuwa Ayya kanta har mamakin itin tsararen shirin da y'ar tata ta koya,
Ta iya saka kaya masu saka jiki a nutsuwa, ta fi nacewa atampopi dinkunnan dogayen rigunnan zamani masu tsari irin na yayan yan gayu ba masu fitar da tsiraici ba,
Wani sa.in takan zurmuka hijab dinta a saman shigarta mai kyau da birgewa, wani sa.in kuwa sai ta yafa dan gyalenta ,

Idan ka ganta ba zaka taba kawowa ta taba aure ba, hakan ya saka du fitarsu sai ta samu mai tayawa dan ba karya dorinar kyau ne da ita ga dorinar ado, kaya saka su kawai take su yi mata das  ba ciko ba acuci ko daya.

Alhinayett na lure da irin kokarin da mahaifinta ke yi, dan haka ta kwatanta zuwar masa da shawarar tana da yan kudadenta a banki, idan ya amince ra kawo ya kara ya yi mata gadon, sai dai ya yi murmushi ya ce" Alhinayett, ke dai Allah ya yi maki albarka irin dawainiyar da kike da mu baki daya, aman ba zan amshi kwandalarki ba, zan yi kamar yanda na yiwa kannun ki, ki je kudaden ki ki kara abubuwan nan naku na zamani na gayu ,

Haka ta mike ta yi godiya ta fito, itafa tausaya masa take domin nauyi ne ba kadan ba a kansa, gashi da y'aya mata masu cikuluftun yau a sayi kaza gobe a sayi kaza, gashi dangi na kauye du a kansa suke, ta so ya karba ko ba komai zai rage wasu abubuwan aman ya kiya gashi aure har sauran sati biyu,

Zuwa ta yi dakinta ta tsala wanka ta saka abayarta baka sannan ta daura nikaf a fuskarta ta fito ta yiwa yan gidan salama kan zata je wajen gyaran jiki da karbo dinki da kai wasu dinkunnan, wai a nan du irin tarin suturun da take saya ne , lefe an ce sai gobe za.a kawo,

Tuki take hankalinta kwonce a yar karamar motarta ta nufi gidan su Wardugu dan dauko kawalin nata wace take kanwa a wajenta kuma kawar shawara dan a duniya nitsuwa da hakuri Agaishat ya saka ta aminta da ita,

Tana tsayawa ta bude ta fito sai jin karan shigowar messages ta yi a wayarta rututu,

Dakatawa ta yi ta bude pos dinta ta ciro wayar inda ta maida hankalinta wajen tagar Agaishat tana hangen ko zata ganta ta nuna mata ta zo fa,

Tana buda wayar ta shiga, wata sabuwar number ce ta Niger, dan haka ta shiga cikin messages din,
Hotunnan ne , hotunnan gadaje, kujeru, table din tv, na tsakar daki, na cin abinci, show glass, kowane da katon tambarin katon butik din da ake siyar da su, irin kayan wajen nan ne,

Murmushi ta yi tana fita a wajen ta ayanna a ranta yo wannan ko gidanmu za.a siyar ba zai kai kudaden wadinnan kayan ba, ni me ya kai ni?

Murnushi ta yi ta shiga gidan,
Ai kuwa ta shirya cikin wata doguwar rigar atampa A yi mata dinkin mai dogon hannu aman a bude sosai dan kuwa du hannun ya cinye sauran atampar,
Ta yi daurin dan kwalinta da irin carto din nan baki, ta dan fitar da yalwatacen gashin kanta daga kasan dan kwalin,
Kunnenta dauke da yan kunayen azurfa mararsa nauyi da fadi sai dai tsayi,
Hannunta dauke da dan zobe karami na azurfar shima,
Fuskarta ba wata kwaliya sai dan kwalin da ta saka sai lebenta na kasa da ta shafawa dan jan baki kalar ja aman ta murje shi ya kasance kadan ne ya fito a jikinta,
Kamshi take bazawa ta dora kafarta ta dama saman ta hagu tana dan kadawa ta cuno baki wai Ayya ce ke fadan bata son saka takalma masu dan tsayi ita kulun sai plat kamar wata tsohuwa wanda ko ita Ayyan na saka mai tsayinta idan ta yi ra.ayi, dan haka ta karbe katon hijab din da ta dauko da takalmin ta koma ta dauko mata wani mayafi fari kal mai shara shara da takalma masu dan tudu farare da pos fara kar mai igiya yar doguwa ta dawo tana fadan sai kace wata datijuwa ta wani kinsima hijab kulun kulun? Ke da nake so kema na wanke ki abina na maki aure mai sunnan aure?

Alhinayett ta yi dariya tana kallon yanda ta daura takalman a kafarta tana cuno baki ta dauki pos din ta saka wayarta a ciki kafin take juyawa wajen Ayya ta sakar mata murmushi ta ce" Ayyana, ni ba zan yi auren ba, na hakura da auren, kin ga ba kin mini auren ba aman na dawo maki? Kawai mu yi zamanmu ,

Ayya ta gala mata harara ta kawar da kai irin ta shakan nan bama zata bata amsa ba, dan haka sukai mata salama ta bi su da adu.a suka fice a motar Alhinayett din.

Tafe suke suna dan hira inda wakar guitar ke tashi kadan kadan a motar suna bin mawakin Buzun mai sunna Bombino bisa wakarsa ta *Arakkham nah*,

Wayarta ce ta dauki kara dan haka ta samu waje ta dan tsaya,

Tana dagawa ta ji yana cikin kayaniya dan haka bai tsaya sun yi wata doguwar gaisuwa ba ya

isar mata da sakon inda zata tardo shi yanzu yanzu ,

Da to ta amsa ta datse kiran tana duban Agaishat ta ce" Wardugu ne, yace mu tarda shi shagon nan na siyar da kaya yanzu ko lafia?

Agaishat ta tsura mata ido bata ce da ita komai ba har ta tada motar ta dauki hanya, Agaishat kam na so tace da ita dan Allah ta ajiyeta ta je ta dawo sai dai ta san bama zata saurare ta ba , dab gaja ta tsurawa hanya ido,
Ita ba komai ke rikitata ba sai irin yanda gabanta ke faduwa idan ta hadu da shi, ko dan ya cika fada ne? Wani lokacin yana da saukin kai, aman yawancin lokutan ya cika fada da daure fuska, ita kuma tsoron hakan take.,

Sun jima suna tafia kafin ta tsaya kofar tankamemen shagon kayan dakin,

Baki da hanci Agaishat ta saki tana duban wajen da suka tsaya,

Alhinayett ce ta fara fita a motar ,
Gannin Agaishat bata fito ba ta leka dan gannin abinda ya hanata fitowa,

Agaishat kamar an mintsineta ta juyo wajen Alhinayett ta ce" ke gala, ko dai mun bace da wajen ne? Na ji kin ce yana gudan siyar da gadaje , ke kuwa na ga kin kawo mu wannan waje dake shige da manyan ma.aikata?

Alhinayett ta bushe da dariya ta ce" Agaishat yanzu wannan ne ma.aikatar? Ba na ce da ke ba idan har kin ga waje ki ringa karantawa kar ki yarda ki nuna wani kauyanci ba?

Agaishat ta shafe gaban goshinta ta ce" hm, ke dai bari, yo ni ta karantawana nake? Wajen gadaje kayan katako an saka su a wannan waje an kilace? Lale du abu idan ya kasance yana da daraja zaka ga an kilace shi,

Alhinayett ta zagaya ta bude mata motar tana fadin malama fito kar ya kagauta ya yi mana abinda ba shi ba, mu je mu fito mu yi tafiarmu

Tana fitowa ta gimtse dariar da take yi ta kama kanta ta bi bayan Alhinayett,

Sai da suka je wajen wani madubi da mutun da tsaye ya saka dan injin caje mutun din nan ya caje su kafin suke shiga cikin boutik din,

Gaskiya ne, idan har ba kai din dan gayun bane, toh fa ka san wajen, in ba haka ba kana shiga kana iya faduwa fan kallo,
Wannan shi ake kira murmushin amarya, kukan iyaye kennan,
Tafdi, haduwa, karshen haduwa, tsari, kaya ne na manya,

Saman luntsumemiyar kujera suka hango shi zaune da mai wajen baki daya,
Yau kam shada ce jikinsa mai ruwan maroon , an yi masa tazarce kawai, ba.ai mata adon komai jikinta ba sai kace karamar shada, abinka da an wanku an jiku sai ta yi bada wani samfari a jikin nasa, ga wata hula da ya kafa yar daidai da kan nasa da ra kuma hau da kayan jikinsa,
Kai wardugu mai kyau ne,
Hira suke da mutumen, da alama ba yau ya fara zuwa wajen ba, koma sun san juna ,
Yau baki dayansa annuri yake fitarwa, inda suka tsinci muryar Elhajin na fadin" Oga, ai sai ka fada min gaskiya kawai zaka gwangwaje ne, kai zaka dauki amarya haka? Gaskiya Oga kana ja,

Wardugu ya yi murmushi yana girgiza kai, daidai sun karaso ya ce" aminiyata ke aure ba ni ba, Alhinayett fada masa ko ya bani lafia,

Yana ganninsu ya juya wajen yaronsa ya ce" kai Idrissa, zo kakabe kujerun nan maza, ai ko yanzu aka ciro su a leda sai an goge domin hajiyoyin ne da kansu,

Alhinayett kawai ta yi murmushi tana duban wajen da za.a goge masu wai, wajen sai daukan ido yake a hakama, aman dan da mai ajin suke tare sai suka caje inda suke har aka zo aka goge masu wajen zaman suka zauna,

Gaishe shi suka yi,
Wardugu ya amsa da Ify, kamar yanda ya saba amsa gaisuwa a datse,

Duban Alhinayett ya yi, a kasan ransa kuwa ya ji kamar ya shige su da fada, wai ita ba zata daina yawo da yarinyar nan ba? Ba zata barta a gida ta yi zamanta ba? Han,

Katon albom aka kawo masu aka ajiye,

Dubanta ta kai itama wajen Wardugun da yannayin tambaya,

Wardugu ya ce" ki bude ki zabi wa.inda sukai maki

Kallon kur take masa bata kawar da fuskarta ba dan neman karin bayani ,

Mai shagon ne ya ce" hajia, ai idanma a nan basu yi maki ba sai na yi kira su turo mana sababi ki zaba cikin sati zaki ga kayanki,

Sai da ya gama magana tana dubansa kafin ta maido dubanta wajen Wardugu,

Fuska ya hade ya kawar da kansa,

Ajiye litafin ta yi ta katsa kusa da shi,
Murya ta rage ta ce" Wardugu, me kake nufi?

Wardugu ya ce" ban gane me nake nufi ba? Kayan daki zaki zaba Alhinayett mana, kin san minti nawa na yi a wajen nan ? Ina da taro fa ,

Alhinayett ta juyo da kallonta wajen Agaishat, gani ta yi ita kawai ta tsurawa wata agogo ido mai ruwan dawisu sai kyali take ta hadu karshe,

Dubanta ta maido wajensa, hannayenta ta hade waje guda ta ce" Warsugu, kennan zagin nawa da ake cewar na makale maka wai kawance dan dai na tsotsi abin hannunka ne zai tabata? Wardugu, kayan dakin ka rasa a inda zaka siya min sai a wannan tsadaden shagon da idan ba isa ka yi ba zaka saka kafarka bama koda dan kalo ne? Wardugu Abanna me zai ce? Wardugu wahalar ta isa haka, dan Allah ka rufa mani asiri ka bar maganar kayan nan ,

Wardugu ya zaro ido da mamaki, murya a kausashe ya ce" ni zaki rainawa wayo Alhinayett? Ni zaki fadawa irin magangannun nan? Ni?

Da sauri Agaishat ta juyo da dubanta wajensu, mikewa ta yi tsaye domin ta ga ya nuna Alhinayett da yatsa alamun ransa ya mugun baci,

Muryarsa ta kuma ji ya ce" walahi yau da wata ce ta mani irin haka sai na dauke mata hakora kafin ta karasa maganar, an gaya maki ni sakarai ne mai daukan jita jitan mutane? Ko qn gaya maki idan ban yi magana da Aban ba zan yi gaban kaina? Malama da na kiraye ki ki zaba dan na san halayenku mata da shegen tsare tsare ana iya zabar maki ki ce basu yi maki ba! Ki zaba ku bace min da gani kuma idan na kara gannin wacen ba hijab sai na kade ku!

Hawaye ne ke zubar mata a idannuwanta, wasu na korar wasu, rayuwa kennan, ita ta taba tunanin zata hau irin wannan gadon? Wajen Agaishat dake tsaye tana kikifta ido ta dawo da sauri ta dauki litafin ta mika mata ta ce" zabar min,

Agaishat ta dubeta ta canza harshe zuwa yaran buzanci ta ce" me kuma mukai masa da zai kade mu?  Yaushe ne zai kade mun? Kuma muna cikin motar za.a iya kade mu daman? Kin ga Ayya amanata ta baki idan kika bari ya kade ni ke da ita ne.

Alhinayett ta ce" Agaishat kin manta yana jin yarenki ne?

Da sauri ta zaro ido, ran harga Allah ita ta manta da yana jin yarenta, dubanta ta waiga wajensa ta ga yana danna waya, da alama bai jita ba, dan haka ta sauke ajiyar zuciya ta ja Alhinayett suka kara matsawa tana duban har yanzu ta ki yin shiru,
Hannu ta dago tana dubanta ta ce" to wai kukan fa?

Alhinayett dake shasheka ta ce " Agaishat, wai na zabi kaya fa yace?

Agaishat ta ce" to menene?

Alhinayett ta ce" Agaishat, ba zaki gane ba,
A wajen nan kayan masu tsada ne na yayan gata, sun fi karfina, ni wa? Yar wa?

Agaishat ta yatsina bakinta wanda du idan ta yi sai dimple dinta ya loma, ta karbi litafin ta shiga dudubawa,

Hankalinta kwonce ta kallo tana ta santi a ranta, a fili ta ce" kin ga ni na rikice, karbi ki zaba,

Alhinayett ta karba ta ja hannun Agaishat har gaban Wardugu dake dan zantawa da Elhaj, duda ransa a bace aman yana amsa shi,

Suna zuwa Alhinayett ta ce" War?

Wardugu ya dubeta bai bata amsa ba,

Ta ce" ka yi hakuri, na tuba👏🏻,

Idannuwansa ya dan lumshe ya bude a kansu,

Alhinayett ta turo Agaishat gabansa, irin sosai ta matso kusa da shi domin turota ta yi da biyu, ta ce" Agaishat, ki taya ni godiya wajensa, bani da bakin gode masa ki kama mani,

Agaishat ta zaro ido ta juyo da dubanta wajen Alhinayett , kafin take juyawa kusa da shi,
Kamshin turaransa ne ya saka ta fara jin wani irin dadi a ranta,
Wardugu dake kallon kasa kasa ya shiga wani yannayi na jinta gashi gata,

Agaishat ta shiga kame kame tana dan shafa gaban goshinta,
Dago idannuwansa ya yi ya zuba mata saman fuskarta, yanda take shafa fuskar tana dan waige , tana kuma kallon wajen da yake abin sai ya saka shi nishadi, irin ta daburce ne? Ai kuwa sai ya saki murmushin da ya nuna fararan hakoransa,
Yan wushiryarta ne suka bayana na sama wajen hakoranta biyu da suka dan yi kasa kamar na zoma sai dai basu fito sosai ba sun bada wani kala mai birgewa da tsari ne, suka bayanna, ta lumshe manyan idannuwanta ta bude ta ce" Mun Gode, Allah ya kara arziki, Allah ya kare ka a duk inda kake, ya baka kaima masu yi maka domin Shi👏🏻,

Bai iya amsata domin yakan zama wawa a duk lokacin da suka samu kusanci irin haka, shi ya sa ya daina yawan zuwa gidan Ayya, domin a gidan Ayya wani lokacin yana tarar da ita tana zuba tabara shi kuwa uwa wawa sai ya saki baki da ido yana rakata da kallo yana sakin murmushi 🤦‍♀️🤦‍♀️🤦‍♀️🤦‍♀️🤦‍♀️

Paris

Alhamdulilah, jiki ya yi kyau, a hankali har ya fara dan fita daga gidansa yana gannin gari ya koma,

Khadija dake fama da shi ta fara kosawa kan maganar aurensu aman abin mamaki ya nace aa, ba yanzu ba, shi ba zai iya auren da ba Wardugu ba, shi sai wardugu ya aminta zai iya auren ko wace mace!

Takan ji takaici da gannin bai san darajarta ba, sai ta nuna ta yi fushi , sai ta kasa ta dawo ko dan ya ci abinci dan idan bata nan baya ci!

Kamar yau yana zaune yana kallon fulawowin tsakar gidansa,
Iska mai dadi na busa shi ya.....

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

66

Kai jama.a ni dai wollah Azumi🙄🙄🙄🙄

Iska mai dadi na busa shi yana mika hannunsa a kai a kao yana dan tsigo fulawar ya sinsina hat sai ta yi laushi sai ya zubar ya kuma tsinko wata,

Tsaye take bayansa tana dubansa, ta dan dauki lokaci kafin ta juya ta shige gidansa ta dauki wayarsa ta dana masa kira,

Ya jima, kai harma ta cire rai da zao daga domin ta kira ta kara bai daga ba , da kyar dai ya daga bai yi magana ba sai dan hayaniyar muryar Alhinayett bakinta ya kasa rufuwa dan murnar abin alkhairin da ta samu na aurenta,

Salama ta yi a hankali na wajen uku kafin yake amsawa shima,

Ajiyar zuciya ta sauke ta ce" Wardugu Khadija ce,

Wardugu ya ce" na gane,

Khadija ta  yi tsam ta ce" Wardugu kun san gaba ta fi kwana uku salar mutunma ba.a karba?

Wardugu ya ce" eh na sani,

Khadija ta cire wayar da mamaki a kunenta, kafin take maidawa ta ce" kun sani aman kuke yi?

Wardugu ya ce" ke din wa ya baki damar kirana ki min tambaya irin haka? Ni mace ne da zan tsaya gaba da wani?

Khadija ta sauke ajiyar zuciya ta ce" Dan Allah ka yi hakuri, baya jin maganar kowa idan ba taka ba,

Me saurayin naki ya yi maki? Ya tambayeta kai tsaye,

Wata kunya ce ta kamata, kennan ya san halin da take ciki ko me? Ai tunda ya sani bara kawai ta fito a mutun, ta ce" Wardugu, ya ki maganar aurenmu, yana irgawa Agaishat ta fita a ida, wai shi sai ka yafe masa, dan Allah ka yi wani abu, idanma hada mu za.a yi a yi auren ni da ita in dai zaka yafe masa dan Allah ka yi,

Idannuwansa ya rintse, ya jima kafin ya bude ya furzar da wata iska ya ce" haka yake tunani ko tunanin ki ne?

Khadija ta ce" neman mafita nake,

Warsugu ya girgiza kai yana murmushi ya ce" ki iya da shi kin ji?

Kit ya datse kiran,
Juyawa ya yi wajen da suke, ta daura mayafin a kugunta ta yi tsaye gaban katon madubin dake jikin bed din da Alhinayett ta zama tana juyi suna daria wai ga yanda Alhinayett zatana yi a dakinta ita daya gaban madubi,

Dubansa ya kai wajen Elhaj ya ga yana tsaye shima yana dariar domin tana abin ne gwanin sha.awa,

Ji ya yi ransa ya baci da hakan, dan haka ya karasa wajensu ya ja ya tsaya ya gala mata hararar da ta sakata tsayawa bata shirya ba,

Hankalinsa ya mayar wajen elhajin ya ce" Elhaj sun gama ne?

Elhaj ya ce" sauran su kayan kyale kyalen falon Elhajinmu

Wardugu ya ce" ai su je kawai, sauran a duba tsarin kayanta a hada mata wa.inda zasu yi kyau,

Elhaj ya amsa da an gama ya juya wajen yaransa ya shiga basu umarnin yanda za.a shirya kayan a loda maza a kai adres din Alhinayett wasu cikinsu kuwa ya saka su karasa hada abubuwan da ba.a hada ba,

Alhinayett ta karasa kusan wardugu ta tsaya daf da shi, irin idan tana sin yi masa maganar siri ta ce" War, Mu kam mun yi kasuwa a nan fa,

Wardugu dake dubanta daman ya san magana take da shi, dan haka ya yi mata duban bai fahimta ba,

Alhinayett ta ce" Elhajin nan yana ciki fa,

Wardugu ya gimtse fuska yana dubanta dan ta fara gajiyar da shi sai wana masa magana take, ya ce" cikin ina wai?

Alhinayett ta ce" yaja son Agaishat mana,

Wani irin dago da idannuwansa ya yi ya sauke a kan fuskar Alhinayett dake murmushi tana dubansa irin ta yi da biyu dan ta ga reaction dinsa, aman da yake ya fita iya duniyanci sai ya yatsina fuska ya watsa hannayensa yana mai tausar zuciyarsa ya ce" shi zai iya jimawa da ita ko? Dan kam na gaji da yi mata aure ana sakota ,

Ido Alhinayett ta zari tana rufe bakinta da mamakin Wardugu, ta ce" Wardugu har sau nawa ta yi auren? Ai ko abokin ka da ya sake ta bai ganta a haske ba, sannan bai san ciwonta ba, na tabata du wanda ya dauki Agaishan ayya a yanzu zai yi mata rikon gold ne

Ido ya kankance yana dubanta ya ce" meye zai saka a yi mata rikon hakan? Yarintar? Ko kanantar? Kin san me ke rikita maza kuwa? Mace ginaniya, wace idan ta motsa zata motsa da shi ba yar jaririya ba, shima Elhajin Mubarack din nan nake yi masa duban baban yaro ashe dai yaro ne,

Ido ta kara zarowa tana dubansa yanda ya gama magangannun ya gimtse fuska yana kuma kallonta kafin yake juyawa ya ce" ta yafa mayafin nan a saman kanta,

Tafiya ya yi Alhinayet na kallonsa baki sake, murmushi ta saki kafin take girgiza kanta , ta yiwa Agaishat dake kara kallon kaya magana suka kara gaba,

Ko a wajen gyaran jiki yau da aka fara jika jikin Alhinayett da turare haka ta kara kudin wajen Agaishat itama aka shiga yi mata sak irin gyaran amare,
Tsume tsumen nan da ake basu kansa tana shanye abinta kai tsaye inda Alhinayett ke yi mata kallon ta san ko na meye tunda ta taba aure, hakan ya sa itama ta kama abin da karfi karfi gannin wace ta taba aure batai masa da wasa ita kuwa Agaishat na sha ne dan dadi yake yi mata, ,

Sosai suka wuni cikin farin cikin da Wardugu ya saka su, suna dawowa suka tarar d Ayya a wajen hutunta tana zaune da jarida a hannunta,

Gannin su ya saka ta ajiye jaridar hannunta tana dubansu da yalwatacen murmushi a fuskarta dan yau an yi masu dilka sai sheki suke,

Suna zuwa Alhinayett ta karasa kusa da Agaishat kadan ta duka har kasa kanta na kallon kasa ta ce" Ayya, ina rokon Allah subahanahu wata.ala ya kara rufa maki asiri ke da kika yi silar zuwan Wardugu duniya da mahaifinsa da dukan wani wanda ya shafe shi, ya Allah ya yi maku sakaya da gidan Aljana, Allah ya rabaku da kunyar duniya da ta kiyama, Allah ya.....sai ta yi shiru sanafiyar hawayen dake zubar mata ,

Ayya ta dafe kanta ta ce" ya salam, Ke Alhinayett tashi tashi maza goge hawayen ki, menene haka? Haka Mahaifin ki da da maman ki basu dade da fita a gidannan ba, ke idan bai yi maki haka ba , ni da kaina sai na ga bakinsa irin yanda kuke tare da zuciya daya? Maza daina wani kuka ba yayanki bane?

Alhinayett ta shiga share hawayenta tana duban Ayya,

Ayya ta sauke ajiyar zuciya tana duban Agaishat da ta yi narai narai ta ce" kin ci abinci kuwa?

Agaishat ta daga kanta,

Alhinayett ta dungureta ta ce" ta sha solani dai, bata ci abinci ba,

Ayya ta dafe kai, ta ce" kin ga, frij cike yake da kalolin solani tunda na fadawa Wardugu ta mayar da solani abincinta ya kasance kafin ta gama da ta frij an kawo wasu an cika a frij, du wajen yarar gidannan ki ka duba zaki ga ledojinsu na yawo a ciki, tsorona ya saka mata ciwon ciki gata ba shan maganin zafi ba sai ina tsaye,
Ayya ta karasa tana dafe kanta,

Agaishat ta zauna gefen kujerar da take zaune ta dora kanta saman jikin Ayya ta dora hannunta wajen jaridar da ta ke karantawa ta ce" Ayya, wai mai siyar da kayan gadajen nan ya ce yana so na,

Ayya ta zaro ido tana dagata daga kwonciyar da ta yi kamar mage ta ce"  ke kuwa ki ka ce da shi me?

Agaishat ta dubi Alhinayett ta ce" ni kalon sa na yi, kafin nake dan motsa bakina, na kada kaina sai kuma na yi gaba na bude motar Alhinayett na zauna na sada kaina, kin ga ban nuna zumudi ba, ban kuma yi masa rashin kunya ba, ko Alhin

Ayya ta yi murmushi tana duban Alhinayett ta ce" Alhinayett zauna mana,

Alhinayett ta zauna sosai, dan ta lura yau Ayya na yi da ita, ta sake mata fiye da kulun, dubanta ta kai wajen Agaishat ta ce" auta, dauko min faro,

Agaishat ta mike ta nufi ciki

Ayya ta dubi Alhinayett ta ce" Alhinayett, ki yafe ni kan wasu abubuwan da nake nuna maki kin ji? Kin san rayuwa, yau ko Wardugu na dan cikina dole na saka ido a mu.amalarsa da kowa bale mata, gashi a zamanin ku ake kawance mace da namiji, har ga Allah na sha saka shi gaba da fadan ya aure ki sai yace da ni kawarshi ce ba zancen soyaya tsakanin ku, hakan ke saka ni a halin tsoro , idan kika yi duba da tsakanin mace da namiji akoy shedan,

Alhinayett ta gyada kanta tana duban kasa ,

Ayya ta ce " tun yaushe mahaifiyar ki ta rasu?

Alhinayett ta dago da kanta tana duban Ayya, ya aka yi ta ji? Sai dai bata da amsa ta san tunda ta yi mata tambayar toh tana da labarin yanzu, dan haka ta ce" rasuwar mamana , wani soja ne ya kadeta, kuma sojan mahaifinsa ne baban mutun hakan ya saka suka rufe akama ki bin maganar,

Mafarin haduwana da Wardugu kennan, ba wancen labarin ba, domin na je na kai masa kukana, na fada masa komai hakan ya sa ya yi bincike, cikin ikon Allah ya tarbi abin da karfinsa inda ya samu baban Alkalin nan datijo mai sunna *Gukunni* ya zama lauyana a lokacin baban lauya ne da ake shayi , nan ya shige gaba suka hada karfi da karfe cikin ikon Allah suka kada

shari.ar , dalilin da ya saka mahaifina ya cirewa Wardugu shamaki da cikin gidan mu, dalilin da ya saka na samu sa.ar zama abokiyar Wardugu, har ake mamakin irin kusancin mu da irin yanda muke hira da Wardugu, kuma duda haka sau biyu yana yi min dukan da ba zan taba mantawa ba , dayan kan karatuna da na so na yi wasa da shi, ya yi magana ya yi magana na kiya har Abana ya bashi damar ya yi maganina, a ranar sai da na kwana asibiti, na biyun da na fara samari masu hatsari, irin yaran nan yayan masu kudi dake hurewa yara kunne, suka so su saka ni a uku a lokacin yana Spain, ya yi min nasiha, ya gwada min ilar abin du na kasa fahimta sai da ya dakar min fata na suma sau biyu , tun daga shi na yi byby da samarinma baki daya sai yanzu Allah ya yi,

Ayya ta girgiza kai tana dubanta kafin ta yi murmushi, ta ce" daga yau ku daina zuwa gyaran jikin, in sha Allah zan karasa maki a gida,

Godiya Alhinayett ta yi ta yiwa Ayya har ta dakatar da ita,

Ayya ta hangi Agaishat tafe da faro ta ce" kin san menene, ina son Agaishat tamkar yar da na haifa a cikina Alhinayett, na yi sake aurenta da na tashi na baiwa yara haka , har ina tuhumar kaina da ni na haifa zan ko yi haka? Ina jin haushin kaina,

Alhinayett ta ce" Ayya, ba maganar sake, abinda Allah ya tsara sai ya kasance a kan bawansa, aure kuma ai lokaci ne , idan ya yi ko a halin yaya sai an yi shi idan kuwa lokacin mutuwarsa ya yo komai so sai an rabu, Agaishat na girmama girmanki a zuci da fili, bata taba nuna laifinki kan komai ba, koda ta san ta yi laifi takan yi murmushi ne tace Ayyana zata min fada, kuma ta je ta kasa barci, kin ga kuwa karara shakuwa ta iyaye ta bayana a lamarin,

Ayya zata yi magana ta karaso dan haka ta yi shiru, ko ba komai bata so ta san irin girman son da take mata dan karta sangarce mata, Agaishat duka duka bata fi 21 ba, har yanzu yarinya ce

Wardugu ne zaune da waya a hannunsa yana amsa kiran Elhaj Mubarack,

Elhaj Mubarak ya ce" Elhaj, nafa ga iri a wajenka,

Wardugu da ya dago zancen , ya gane inda ya nufa sarai, ya san me yake son fada masa , dan haka sai ya dantse lebensa na kasa yana sauraronsa,

Elhaj Mubarack ya ce" zan so a bani na kai gidana, wannan Hajia ce , sai Elhaj Mubarack,

Wardugu ya lumshe idannuwansa, bai san lokacin da ya ce" wai menene a tare da ita dake saka mutane bibiyarta ne?????????

Elhaj Mubarack ya yi wata dariya ta manya yana lumewa cikin kujerar falonsa inda matarsa ke gefe zaune tana zuba abinci tana jin abinda yake fada ya ce"..........

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

6️⃣7️⃣

Sai da ya gama murmushi ya shafa gemunsa ya kara kafin ya ce " Elhaj, ai fure ce, zan so na yi mata yayafi,

Wardugu ya rintse idannuwansa, kansa ya kawar kafin yake ajiye wayar ba tare da ya kasheta ba,

Jikinsa ya matsa ya jinginar da jikin kujerar da yake kai, idannuwansa ya lumshe yana mai jin wani tukukin tashin hankali na taso masa daga zuciyarsa yana yin sama,

Idannuwansa ya rintse irin ruf din nan ya shiga kokowa da zuciyarsa, aman ina ya kasa ba zai iya ba!

Mikewa ya yi rai bace ya dauki kys din sa ya fito yana gannin garin ya yi duhu sosai ,

Motarsa ya shiga ya bale da gudun gaske ya yiwa gidan Ayya tsinke,

Yana karasawa ya fice a motar kys dinsa a hannunsa ya nufi falo dan ya tabata irin wannan lokacin suna zaman falo ne

Yelemin kuwa, suna zaune Ayya na yi mata dankwashi ita kuwa tana zuba shagwabarta , Jikinta doguwar riga ce har kasa sai dai irin yadin nan ne mai likewa a jikin mutun ko ya ka motsa zaku motsa tare ne kuma komai rashin kabrin jikin ka zayana nuna motsin halitar jikinka, tana da irin rigunnan da yawa dan yannayin zafi Ayya ta kwaso mata a lokacin da akai mata aure.

Da katon takalminsa ya shigo falon domin bai riga ya cire takalmin da kayan dake jikinsa ba ya samu kiran Elhaj Mubarack,

Haka ya takawa Ayya capet din falonta, abinda ta tsana a rayuwa , dan haka da mamaki take dubansa dan shi ne mutun na farko da zai fadi bata son a shigo mata daki da takalmi, hasalima shi din ma ya tsani hakan a rayuwarsa,

Takim takim yaa tunkaro su inda suka dago su duka suna binsa da kallo har ya karaso gaban table din kwalbar dake gabansu mai dauke da ruwa da jus
Yana zuwa ya zuba kys din hannunsa da garaje saman table din hakan ya saka suka bada wani kara tamkar zasu fasa table din,

Hannunsa na hagu ya doro saman table din, da na dama kuwa ya dago yatsansa na kusa da baba ya nunata ya ce" ke , daga yau, daga rana mai kamar ta yau, na soke du wani shige da ficen ki a shigar da ba nikaf, hijab dogo da safa, idan kuwa ba haka ba sai na babala ki Agaishat!

Ya karashe yana mai daga muryar da ya saka ta mike tsaye da sauri ,
Mikewar da ta yi ya ainahin girgiza jikinta da karfi domin irin mikewar tsoracen nan ce,

Ido ya zaro ya ce" ba ga irinta ba! Ba ga irinta ba! A ce yarinya baki da kimtsi sai tsale tsale da guje guje da juye juye a gaban ko wani karamin dan iska? Ke ko kunya bakya ji zaki fito da wani mayafi mai kama da rariya ki wani zo kina juyi gaban madubi? Ke ke......
Da haushi haushi ya nufeta da niyar gaura mata mari domin a tsaye da take baki ta turo tana kikifta masa ido, wanda hakan ya kara hautsina masa lisafi

Ayya da ta yi mutuwar zaune cike da mamaki, da kuma darsuwar vakon zargi a kan tilon dan nata game da yar amanarta ta yi sauri cewa" walahi ka dakar min y'a sai ran ubanka ya baci Wardugu!

Ja ya yi ya tsaya, a hankali ya juyo wajen Ayya ya ga ta mike tsaye, kansa ya sada ya karaso kusa da ita a hankali kafin ya ce" Ayya, ya zaki sakawa yarinya ido tana fita da mayafi dan Allah?

Ayya ta ce" Wardugu, auren wani ke kan yarinyata ko bakon abu ne fita da mayafi a matar aure ma bare wace bata da aure? Ba wani shigar tsiraici take yi ta fita ba, aman idan ka saka mata irin dokar nan ba zan dauka ba !

Wardugu ya dago jajayen idannuwansa ya ce" Ayya, sai ta fita da dan mayafi zata samu miji ne? Wani irin miji take nema a rayuwarta ne? Shin ba karatu kika ce tana yi ba? Dan Allah du yanda za.a dagawa mutun hankali an sani? Yaya kuke so na yi ne?

Ayya ta kwalalo idannuwanta kafin ta tafa hannayenta ta ce" Warsugu wani laifi muka yi maka ne?

Wardugu ya yi shiru ya tsurawa cafet din falon ido, can ya fago idannuwansa ya sauke saman fuskar Agaishat dake tsaye tana dubansa, idannuwan su ne suka sarke da juna, kallon second 5 , idannuwan Wardugu jajaye jir da su tamkar gauta, sai dai da wasu yan kwala da ba zata iya kiransu da kwallah ba sai dai tace da su na bacin rai, wani irin kallo mai nauyi, mai tafe da sakwonni, mai dauke da ma.anoni ne ya zuba mata a cikin maraitatun idannuwanta da ta yi tsai ta jefe shi da kallo mai tura sakon *Ka ji tausayi na*,
A hankali ta lumshe idannuwanta ta ji wani irin sulbi a cikin idannuwan nata sannan suka fara rawa sanadiyar irin dokawar da zuciyarta ke yi du idan ta yi arba da shi,

A hankali ya taka ya nufe ta, wanda du takunsa ke barazana da tunanin kwakwaluwarta har ya kasance tunanin ya tsaya cak, ba wani sauran abinda ke aiki a cikin kwakwaluwar nata sai tarin kwalar da ta cika gurbin idannuwanta a hankali ta shiga zubowa,

Kure mata waje ya yi, ya shaki kamshin turarenta,
Idannuwansa ya lumshe ya kai hannunsa ya riko nata , riko na ya riko hannun kanwarsa, riko na ya kamo hannun kanwar sa dan ya jadada kashedinsa a gareta,
Sai dai laushin su ya saka shi dago da hannun da kyau ya bude idannuwansa ya tsura masu ido,
Ajiyar zuciya ya sauke kafin yake daga dan yatsarsa ya ce" ki bi dokana ki tsira, idan ki ka kiya zaki saka mu a uku ne, dan zan farauce ki a duniya ne, zan yi maki farautar kwai ne, Agaishat ki rufa mana asiri ki bamu lokaci, ki rufawa Ayyanki asiri kar ta yi zaman jinya !

Yana gama fada ya juya ya dauki kys dinsa ya juya yana tafe yana hada hanya ya fice a fallon,

Kuka Agaishat ta fashe da shi wanda ya farfado Ayya daga uwar sumar mamakin abinda ya faru da raka Wardugu da ido da ta yi,

Da sauri ta nufi wajen Agaishat ta kamota ta ce" ke Agaishat, menene? Tsoro kike ji ko? Kar ki ji wani tsoronsa in sha Allah ina tare da ke ba abinda zai yi maki!

Agashat ta rike hannun Ayya da kyau , da kyar ta bude bakinta ta ce" Ayya zuciyata ke bugawa, Ayya jikina rawa yake min, Ayya wayo zuciyata gabana ke faduwa du idan na ga yaya Wardugu, Ayya ciwon zuciya ne nake ko????

Shiru Ayya ta yi itama gaban nata ya fadi, kai ina! Aa ba su ba, menene haka? Me ke shirin faruwa ne?

Wardugu na komawa gidansa bangaren Walyn ya nufa,
Kai tsaye ya ritsata zaune tana kallon film a nollywood hankali kwonce,

Hannunsa ya saka ya mikar da ita, a hankali ya jata jikinsa ,
Idannuwansa lumshe ya lalubo lebenta jajir ya kai masu lalausan harshensa ya shiga kissing dinta passionately,

Fama take a kai fage, domin itafa ta fi gane can duda takan jigata aman gani take wani sakwanin wasani bata lokaci ne dan haka ta yi kokarin juya wasan zuwa ga fage mai rikitarwa, hakan ya saka ta yi gagawar cire yar rigar dake jikinta wace ta bayanar da yan berayen halitun jikinta,

Hannunta ya ja yana so ta yi tafia a gabansa duda ya kashe hasken fitilar dakin, dan damemen gajeran wandon dake jikinta yake so ta motsa ta bashi ma.ana, so yake ta bashi spectacle, yana so idannuwansa su juye kamar yanda a dazu suka juye daga kallon abinda bai zama halalinsa ba,

Saman kujerar ya zauna yana dubanta gannin faman ta baje take, wato ita dai kulun ta baje shi ta iya,

Kansa ya shafa yana dubanta, farar mace jajir, yar suwaiwai mafarkin dubunai, me ke damunsa? Ga hargitsinsa a gabansa ba wani ba, ga cakula kwakwaluwarsa a gabansa ba wani ba,

Hannayensa ya daga duka biyu ya dora saman kansa kafin a fili ya ce" kai kai, ina ba zai yiwu ba, wace wanina ya shiga? Gidan da aminina ya malaka? Wace irin kunya nake son kwasarwa kaina haka?

Walyn dake jiransa ta  dube shi da kyau ta ce" Wardugu?

Wardugu ya bude idannuwansa yana dubanta, bai taba sakar mata nauyinsa mai suna nauyi ba, yakan shigar da gaban motarsa ne dan gannin gidan motar ba zai iya da shi ba, wai ko dai tausaya mata ne  da yake yake sakata daukan raini tana sauke masa? zata iya da shi ne? Kai yau bara ya sakar mata nauyinsa , ko dai dan yana rage sauran nauyin nasa nema take tunanin karfin su daya?
Abinka da  shawarar keta mai samun mazauni, nan da nan ya ji wani karfi na kara shigarsa, karfi irin na namijin saurayin zaki,

Mikewa ya yi ya nufeta da irin bukatarta ya..........

(Rashin kunyar ta isa haka woolah😢)

Dama kyawawa ne, suka kara da wanka, hakan ya saka yan matan suka wani fito fas da su, Mariama da Zainaba sun wani haska suna taku irin na manyan yara,
Abu daya ke kawo masu cikas a zamansu a birni shi ne rashin iya french, su kuwa yan mata da samarin garin Niamey sun dauki yaren French tamkar yaren haihuwarsu, karkadaf idan ka yi wasa zaka bace a hira da su, wato sun lakance shi ne ya saka har ruwa ruwa suke da harshe da gagawar magana tamkar jikokin macron (😕),
Kakarsu tana cikin koya masu wanka na yayan gayu da suka jiku a cikin gayu,
An koya masu mota, su ke zuwa alimentation siyayar kayan kicin da na frij, suna koyan su cake da sauransu,

Anna ta murje, ta murje ta faso, Anna bata magana daya biyu ba tare da ta jefa turanci wato inglish a ciki ba domin makarantar da ta yi ana koya masu yaran ne duka biyu a tare,
Rayuwarta na da ya dawo, ta dawo cikakiyar yar birni mai wayayen kai da iya tafiar da rayuwarta a nitse ba da hayaniya ba,

Takan shiga damuwar rashin labarin Agaishat, sai dai hankalinta na kwonciya idan ta tuna ai ta bada aurenta tana dakin mijinta kuma ko ba dade ko ba jima zata neme su fatanta dai Allah ya sa tana cikin rayuwa mai nagarta a gidanta,

Sai maganar Algabitt da suke jiran bilowarsa dan abinda ya tsaye masu a rai ya sakar masu y'a !

Timiya,

Sarki ya kada , ya raya, yana so ta janye maganarta aman fir ta rikice masa kan walahi ita magana daya ce tana so a fitar mata da hakinta a matsayinta na yar gari wace take da inci a kan wanda ya cuta mata,

Ya so su yi lamarin a sirri aman ta kiya ita kawai a yi masu shari.a da Algabitt dake rufe a matsayin mai dauke da laifi mai girma a gidan sarki,

Garin ba wanda bai san halin da ake ciki ba dan haka kananun magangannu ke yawo cewar za.a ga idan sarki zai hukunta sirikinsa bisa laifin da ya yi, idannuwa dai a kansa wanda hakan ya saka dole ya fitar da shari.ar fada,

Komai na son sirri, abinda ya yi ta nanatawa Gaishata dake kukan wannan lamari,

Gigirigin kennan ranar fadin gaskiya,

Tare wajen yake dankam, cike da jama.a, an taru an cika an yi makil abinka da kauye kowa ya zo ya ga kwaf,

Sarki zaune ya hakimce da rawaninsa na turkudi, gefe da gefensa du dogarai ne da yaran gidan sarki,
Sarkin bulala tsaye yana dan kadata lokaci zuwa lokaci,

Gefe guda matan sarki ne laye cikin shiga ta alfarma kowace na isa da kanta a matsayin na matar mai garin timiya,

Gaishatama zaune take ta sha turkudinta mai kala biyu blue da maroon an yi mata dinkin zamani ta rufa da katon mayafi hannayenta dauke da warwarayen zinari , ba yara a wajen domin ko yayansu a gida a aka bar su ,

Dayan gefen kuwa Algabiittt ne ke zaune shima yana ta kale kale alamomin rashin gaskiya sun bayana a tare da shi,

Gayaran murya sarki ya yi kafin ya ce" kamar yanda Timiya yake karamin gari mai dauke da sarki ni Ibrahim Asadeek, timiya ta kasance garin da talakanta ke da inci, muna zakulo du wanda ke tayar da zaune tsaye mu hukunta shi bisa tsarin adini,

Dogarai sai amsa shi suke kafin ya ci gaba da fadin" a yau , mun zauna a wannan waje dan tuhumar Malan agabitt kan manyan laifuka da muke tuhumarsa da su wa.inda matar da yake zaune da ita ta shigar da karar tun kafin ta bar gari , yanzu da bata nan bisa madadinta ga y'arta wato gimbiya gaishata , muna masu umartar Algabiit da ya bayana mana haduwarsa da mahaifiyar yayansa, dalilin da ya saka ya yi rayuwar wulakanci da ita....

Shiru ya yi yana kifta ido ya ki yin magana,

Ajiyar zuciya Sarki ya sauke kafin ya ce" idan har mai laifin ya yi gardama, kadarorinsa na gida da gonarsa da ake yi masa noma za.a karbe sannan ya fuskanci hukunci mai tsanani,

Ido ya zaro yana duban Sarki, shi bashi da damuwar wai mutanen wajen su ji abinda ya aikata, shi damuwarsa hangen daya daga cikin wa.inda suka bashi kudaden su Mariama da ya yi, ya tabata idan sarki ya kore ahi daga Timiya ya kade, dan haka ya gyara rawanin kansa ya shiga bada labari kamar yanda Anna ta bada har zuwa ranar da zai tafi da ita inda ya ce" a ranar safiya na yi na koma wajen bokana, wanda yake anguwar Talagué pays ba, ina zuwa na karbo

abubuwan da na bashi ajiya domin ni ke kai masa abubuwa shima yana neman kudi da ni, inda ya dora ni a hanyar da zan hadu da yar masu kudi,

Maganin cire ne, wanda hasalij kirana daga garin haihuwana wato tanut dan ina yawan ciren yayansu,

Dakatar da shi aka yi ta hanyar tambayar menene cire?

Dago da kansa ya yi ya ce" Cire, wani asiri ne da fulanin daji ke yi , wanda na gada wajen kakana na wajen mahaifiyata dan shi filo ne, cire asiri ne da idan aka yiwa mace take bin namiji , bata da wani ra.ayi nata sai nashi,
Na hada da cire da asirin da bokan ya samo wajen wani bokansa dan dogon dutsi cewar idan na aikata idona idonta an kare zata bi ni ne du inda zan je, kuma ko me zan mata ba zata iya barina ba dan zatana jin tsoron zuciyata da bacin raina , sai dai kar na yarda ni da bakina na ambata mata sunnan garin su , ko sunnanta na asali, ko na yan uwanta, in dai ba ni na fada ba koma wa zai fada sai dai ya shiga tunani kamar ta san abin aman ta watsar daga baya dan zai tayar mata da hankali sosai

Na ci sa.a na cireta, muka fice a gidan daidai salar azahar muka dauki hanya da kudaden jakarta inda na yi wurgi da wayarta muka dauki yawon duniya,
Masalatai sun fi a kirga na je dan a aura mana aure, aman sai su ce koda bamu da kowa a duniya sai sun yi magana daga su sai ita, daya na amince sun fara maganar na ga sai wani tambayoyi yake yana faman tona asirina na bige shi da sadanta na dauketa muka kara shiga yawon duniya kafin daga baya na yada zango a nan,

Zufa ce ta shiga karyowa Gaishata, sarki kansa ji ya yi lumfashi na neman gagararsa,

Gaishat bata san lokacin da ta ce" kana nufin ba.a daura aurenka da matarka tsawon zaman da ka yi da ita harda hayayafa ba?????

To fa

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀️IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤️*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝🏻😘

Na
*SAJIDA*

6️⃣7️⃣

Sai da ya gama murmushi ya shafa gemunsa ya kara kafin ya ce " Elhaj, ai fure ce, zan so na yi mata yayafi,

Wardugu ya rintse idannuwansa, kansa ya kawar kafin yake ajiye wayar ba tare da ya kasheta ba,

Jikinsa ya matsa ya jinginar da jikin kujerar da yake kai, idannuwansa ya lumshe yana mai jin wani tukukin tashin hankali na taso masa daga zuciyarsa yana yin sama,

Idannuwansa ya rintse irin ruf din nan ya shiga kokowa da zuciyarsa, aman ina ya kasa ba zai iya ba!

Mikewa ya yi rai bace ya dauki kys din sa ya fito yana gannin garin ya yi duhu sosai ,

Motarsa ya shiga ya bale da gudun gaske ya yiwa gidan Ayya tsinke,

Yana karasawa ya fice a motar kys dinsa a hannunsa ya nufi falo dan ya tabata irin wannan lokacin suna zaman falo ne

Yelemin kuwa, suna zaune Ayya na yi mata dankwashi ita kuwa tana zuba shagwabarta ,
Jikinta doguwar riga ce har kasa sai dai irin yadin nan ne mai likewa a jikin mutun ko ya ka motsa zaku motsa tare ne kuma komai rashin kabrin jikin ka zayana nuna motsin halitar jikinka, tana da irin rigunnan da yawa dan yannayin zafi Ayya ta kwaso mata a lokacin da akai mata aure.

Da katon takalminsa ya shigo falon domin bai riga ya cire takalmin da kayan dake jikinsa ba ya

samu kiran Elhaj Mubarack,

Haka ya takawa Ayya capet din falonta, abinda ta tsana a rayuwa , dan haka da mamaki take dubansa dan shi ne mutun na farko da zai fadi bata son a shigo mata daki da takalmi, hasalima shi din ma ya tsani hakan a rayuwarsa,

Takim takim yaa tunkaro su inda suka dago su duka suna binsa da kallo har ya karaso gaban table din kwalbar dake gabansu mai dauke da ruwa da jus
Yana zuwa ya zuba kys din hannunsa da garaje saman table din hakan ya saka suka bada wani kara tamkar zasu fasa table din,

Hannunsa na hagu ya doro saman table din, da na dama kuwa ya dago yatsansa na kusa da baba ya nunata ya ce" ke , daga yau, daga rana mai kamar ta yau, na soke du wani shige da ficen ki a shigar da ba nikaf, hijab dogo da safa, idan kuwa ba haka ba sai na babala ki Agaishat!

Ya karashe yana mai daga muryar da ya saka ta mike tsaye da sauri ,
Mikewar da ta yi ya ainahin girgiza jikinta da karfi domin irin mikewar tsoracen nan ce,

Ido ya zaro ya ce" ba ga irinta ba! Ba ga irinta ba! A ce yarinya baki da kimtsi sai tsale tsale da guje guje da juye juye a gaban ko wani karamin dan iska? Ke ko kunya bakya ji zaki fito da wani mayafi mai kama da rariya ki wani zo kina juyi gaban madubi? Ke ke......
Da haushi haushi ya nufeta da niyar gaura mata mari domin a tsaye da take baki ta turo tana kikifta masa ido, wanda hakan ya kara hautsina masa lisafi

Ayya da ta yi mutuwar zaune cike da mamaki, da kuma darsuwar vakon zargi a kan tilon dan nata game da yar amanarta ta yi sauri cewa" walahi ka dakar min y'a sai ran ubanka ya baci Wardugu!

Ja ya yi ya tsaya, a hankali ya juyo wajen Ayya ya ga ta mike tsaye, kansa ya sada ya karaso kusa da ita a hankali kafin ya ce" Ayya, ya zaki sakawa yarinya ido tana fita da mayafi dan Allah?

Ayya ta ce" Wardugu, auren wani ke kan yarinyata ko bakon abu ne fita da mayafi a matar aure ma bare wace bata da aure? Ba wani shigar tsiraici take yi ta fita ba, aman idan ka saka mata irin dokar nan ba zan dauka ba !

Wardugu ya dago jajayen idannuwansa ya ce" Ayya, sai ta fita da dan mayafi zata samu miji ne? Wani irin miji take nema a rayuwarta ne? Shin ba karatu kika ce tana yi ba? Dan Allah du yanda za.a dagawa mutun hankali an sani? Yaya kuke so na yi ne?

Ayya ta kwalalo idannuwanta kafin ta tafa hannayenta ta ce" Warsugu wani laifi muka yi maka ne?

Wardugu ya yi shiru ya tsurawa cafet din falon ido, can ya fago idannuwansa ya sauke saman fuskar Agaishat dake tsaye tana dubansa, idannuwan su ne suka sarke da juna, kallon second 5 , idannuwan Wardugu jajaye jir da su tamkar gauta, sai dai da wasu yan kwala da ba zata iya kiransu da kwallah ba sai dai tace da su na bacin rai, wani irin kallo mai nauyi, mai tafe da sakwonni, mai dauke da ma.anoni ne ya zuba mata a cikin maraitatun idannuwanta da ta yi tsai ta jefe shi da kallo mai tura sakon *Ka ji tausayi na*,
A hankali ta lumshe idannuwanta ta ji wani irin sulbi a cikin idannuwan nata sannan suka fara rawa sanadiyar irin dokawar da zuciyarta ke yi du idan ta yi arba da shi,

A hankali ya taka ya nufe ta, wanda du takunsa ke barazana da tunanin kwakwaluwarta har ya kasance tunanin ya tsaya cak, ba wani sauran abinda ke aiki a cikin kwakwaluwar nata sai tarin kwalar da ta cika gurbin idannuwanta a hankali ta shiga zubowa,

Kure mata waje ya yi, ya shaki kamshin turarenta,
Idannuwansa ya lumshe ya kai hannunsa ya riko nata , riko na ya riko hannun kanwarsa, riko na ya kamo hannun kanwar sa dan ya jadada kashedinsa a gareta,
Sai dai laushin su ya saka shi dago da hannun da kyau ya bude idannuwansa ya tsura masu ido,
Ajiyar zuciya ya sauke kafin yake daga dan yatsarsa ya ce" ki bi dokana ki tsira, idan ki ka kiya zaki saka mu a uku ne, dan zan farauce ki a duniya ne, zan yi maki farautar kwai ne, Agaishat ki rufa mana asiri ki bamu lokaci, ki rufawa Ayyanki asiri kar ta yi zaman jinya !

Yana gama fada ya juya ya dauki kys dinsa ya juya yana tafe yana hada hanya ya fice a fallon,

Kuka Agaishat ta fashe da shi wanda ya farfado Ayya daga uwar sumar mamakin abinda ya faru da raka Wardugu da ido da ta yi,

Da sauri ta nufi wajen Agaishat ta kamota ta ce" ke Agaishat, menene? Tsoro kike ji ko? Kar ki ji wani tsoronsa in sha Allah ina tare da ke ba abinda zai yi maki!

Agashat ta rike hannun Ayya da kyau , da kyar ta bude bakinta ta ce" Ayya zuciyata ke bugawa, Ayya jikina rawa yake min, Ayya wayo zuciyata gabana ke faduwa du idan na ga yaya Wardugu, Ayya ciwon zuciya ne nake ko????

Shiru Ayya ta yi itama gaban nata ya fadi, kai ina! Aa ba su ba, menene haka? Me ke shirin faruwa ne?

Wardugu na komawa gidansa bangaren Walyn ya nufa,
Kai tsaye ya ritsata zaune tana kallon film a nollywood hankali kwonce,

Hannunsa ya saka ya mikar da ita, a hankali ya jata jikinsa ,
Idannuwansa lumshe ya lalubo lebenta jajir ya kai masu lalausan harshensa ya shiga kissing dinta passionately,

Fama take a kai fage, domin itafa ta fi gane can duda takan jigata aman gani take wani sakwanin wasani bata lokaci ne dan haka ta yi kokarin juya wasan zuwa ga fage mai rikitarwa, hakan ya saka ta yi gagawar cire yar rigar dake jikinta wace ta bayanar da yan berayen halitun jikinta,

Hannunta ya ja yana so ta yi tafia a gabansa duda ya kashe hasken fitilar dakin, dan damemen gajeran wandon dake jikinta yake so ta motsa ta bashi ma.ana, so yake ta bashi spectacle, yana so idannuwansa su juye kamar yanda a dazu suka juye daga kallon abinda bai zama halalinsa ba,

Saman kujerar ya zauna yana dubanta gannin faman ta baje take, wato ita dai kulun ta baje shi ta iya,

Kansa ya shafa yana dubanta, farar mace jajir, yar suwaiwai mafarkin dubunai, me ke damunsa? Ga hargitsinsa a gabansa ba wani ba, ga cakula kwakwaluwarsa a gabansa ba wani ba,

Hannayensa ya daga duka biyu ya dora saman kansa kafin a fili ya ce" kai kai, ina ba zai yiwu ba, wace wanina ya shiga? Gidan da aminina ya malaka? Wace irin kunya nake son kwasarwa kaina haka?

Walyn dake jiransa ta  dube shi da kyau ta ce" Wardugu?

Wardugu ya bude idannuwansa yana dubanta, bai taba sakar mata nauyinsa mai suna nauyi ba, yakan shigar da gaban motarsa ne dan gannin gidan motar ba zai iya da shi ba, wai ko dai tausaya mata ne  da yake yake sakata daukan raini tana sauke masa? zata iya da shi ne? Kai yau bara ya sakar mata nauyinsa , ko dai dan yana rage sauran nauyin nasa nema take tunanin karfin su daya?
Abinka da  shawarar keta mai samun mazauni, nan da nan ya ji wani karfi na kara shigarsa, karfi irin na namijin saurayin zaki,

Mikewa ya yi ya nufeta da irin bukatarta ya..........

(Rashin kunyar ta isa haka woolah😢)

Dama kyawawa ne, suka kara da wanka, hakan ya saka yan matan suka wani fito fas da su, Mariama da Zainaba sun wani haska suna taku irin na manyan yara,

Abu daya ke kawo masu cikas a zamansu a birni shi ne rashin iya french, su kuwa yan mata da samarin garin Niamey sun dauki yaren French tamkar yaren haihuwarsu, karkadaf idan ka yi wasa zaka bace a hira da su, wato sun lakance shi ne ya saka har ruwa ruwa suke da harshe da gagawar magana tamkar jikokin macron (😕),
Kakarsu tana cikin koya masu wanka na yayan gayu da suka jiku a cikin gayu,
An koya masu mota, su ke zuwa alimentation siyayar kayan kicin da na frij, suna koyan su cake da sauransu,

Anna ta murje, ta murje ta faso, Anna bata magana daya biyu ba tare da ta jefa turanci wato inglish a ciki ba domin makarantar da ta yi ana koya masu yaran ne duka biyu a tare,
Rayuwarta na da ya dawo, ta dawo cikakiyar yar birni mai wayayen kai da iya tafiar da rayuwarta a nitse ba da hayaniya ba,

Takan shiga damuwar rashin labarin Agaishat, sai dai hankalinta na kwonciya idan ta tuna ai ta bada aurenta tana dakin mijinta kuma ko ba dade ko ba jima zata neme su fatanta dai Allah ya sa tana cikin rayuwa mai nagarta a gidanta,

Sai maganar Algabitt da suke jiran bilowarsa dan abinda ya tsaye masu a rai ya sakar masu y'a !

Timiya,

Sarki ya kada , ya raya, yana so ta janye maganarta aman fir ta rikice masa kan walahi ita magana daya ce tana so a fitar mata da hakinta a matsayinta na yar gari wace take da inci a kan wanda ya cuta mata,

Ya so su yi lamarin a sirri aman ta kiya ita kawai a yi masu shari.a da Algabitt dake rufe a matsayin mai dauke da laifi mai girma a gidan sarki,

Garin ba wanda bai san halin da ake ciki ba dan haka kananun magangannu ke yawo cewar za.a ga idan sarki zai hukunta sirikinsa bisa laifin da ya yi, idannuwa dai a kansa wanda hakan ya saka dole ya fitar da shari.ar fada,

Komai na son sirri, abinda ya yi ta nanatawa Gaishata dake kukan wannan lamari,

Gigirigin kennan ranar fadin gaskiya,

Tare wajen yake dankam, cike da jama.a, an taru an cika an yi makil abinka da kauye kowa ya zo ya ga kwaf,

Sarki zaune ya hakimce da rawaninsa na turkudi, gefe da gefensa du dogarai ne da yaran gidan sarki,
Sarkin bulala tsaye yana dan kadata lokaci zuwa lokaci,

Gefe guda matan sarki ne laye cikin shiga ta alfarma kowace na isa da kanta a matsayin na matar mai garin timiya,

Gaishatama zaune take ta sha turkudinta mai kala biyu blue da maroon an yi mata dinkin zamani ta rufa da katon mayafi hannayenta dauke da warwarayen zinari , ba yara a wajen domin ko yayansu a gida a aka bar su ,

Dayan gefen kuwa Algabiittt ne ke zaune shima yana ta kale kale alamomin rashin gaskiya sun bayana a tare da shi,

Gayaran murya sarki ya yi kafin ya ce" kamar yanda Timiya yake karamin gari mai dauke da sarki ni Ibrahim Asadeek, timiya ta kasance garin da talakanta ke da inci, muna zakulo du wanda ke tayar da zaune tsaye mu hukunta shi bisa tsarin adini,

Dogarai sai amsa shi suke kafin ya ci gaba da fadin" a yau , mun zauna a wannan waje dan tuhumar Malan agabitt kan manyan laifuka da muke tuhumarsa da su wa.inda matar da yake zaune da ita ta shigar da karar tun kafin ta bar gari , yanzu da bata nan bisa madadinta ga y'arta wato gimbiya gaishata , muna masu umartar Algabiit da ya bayana mana haduwarsa da mahaifiyar yayansa, dalilin da ya saka ya yi rayuwar wulakanci da ita....

Shiru ya yi yana kifta ido ya ki yin magana,

Ajiyar zuciya Sarki ya sauke kafin ya ce" idan har mai laifin ya yi gardama, kadarorinsa na gida da gonarsa da ake yi masa noma za.a karbe sannan ya fuskanci hukunci mai tsanani,

Ido ya zaro yana duban Sarki, shi bashi da damuwar wai mutanen wajen su ji abinda ya aikata, shi damuwarsa hangen daya daga cikin wa.inda suka bashi kudaden su Mariama da ya yi, ya tabata idan sarki ya kore ahi daga Timiya ya kade, dan haka ya gyara rawanin kansa ya shiga bada labari kamar yanda Anna ta bada har zuwa ranar da zai tafi da ita inda ya ce" a ranar safiya na yi na koma wajen bokana, wanda yake anguwar Talagué pays ba, ina zuwa na karbo abubuwan da na bashi ajiya domin ni ke kai masa abubuwa shima yana neman kudi da ni, inda ya dora ni a hanyar da zan hadu da yar masu kudi,

Maganin cire ne, wanda hasalij kirana daga garin haihuwana wato tanut dan ina yawan ciren yayansu,

Dakatar da shi aka yi ta hanyar tambayar menene cire?

Dago da kansa ya yi ya ce" Cire, wani asiri ne da fulanin daji ke yi , wanda na gada wajen kakana na wajen mahaifiyata dan shi filo ne, cire asiri ne da idan aka yiwa mace take bin namiji , bata da wani ra.ayi nata sai nashi,
Na hada da cire da asirin da bokan ya samo wajen wani bokansa dan dogon dutsi cewar idan na aikata idona idonta an kare zata bi ni ne du inda zan je, kuma ko me zan mata ba zata iya barina ba dan zatana jin tsoron zuciyata da bacin raina , sai dai kar na yarda ni da bakina na ambata mata sunnan garin su , ko sunnanta na asali, ko na yan uwanta, in dai ba ni na fada ba koma wa zai fada sai dai ya shiga tunani kamar ta san abin aman ta watsar daga baya dan zai tayar mata da hankali sosai

Na ci sa.a na cireta, muka fice a gidan daidai salar azahar muka dauki hanya da kudaden jakarta inda na yi wurgi da wayarta muka dauki yawon duniya,
Masalatai sun fi a kirga na je dan a aura mana aure, aman sai su ce koda bamu da kowa a duniya sai sun yi magana daga su sai ita, daya na amince sun fara maganar na ga sai wani tambayoyi yake yana faman tona asirina na bige shi da sadanta na dauketa muka kara shiga yawon duniya kafin daga baya na yada zango a nan,

Zufa ce ta shiga karyowa Gaishata, sarki kansa ji ya yi lumfashi na neman gagararsa,

Gaishat bata san lokacin da ta ce" kana nufin ba.a daura aurenka da matarka tsawon zaman da ka yi da ita harda hayayafa ba?????

To fa

🐪🐪🐪🐪 *BAK'A CE* 🐪🐪🐪🐪

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

67

Sai da ya gama murmushi ya shafa gemunsa ya kara kafin ya ce " Elhaj, ai fure ce, zan so na yi mata yayafi,

Wardugu ya rintse idannuwansa, kansa ya kawar kafin yake ajiye wayar ba tare da ya kasheta ba,

Jikinsa ya matsa ya jinginar da jikin kujerar da yake kai, idannuwansa ya lumshe yana mai jin wani tukukin tashin hankali na taso masa daga zuciyarsa yana yin sama,

Idannuwansa ya rintse irin ruf din nan ya shiga kokowa da zuciyarsa, aman ina ya kasa ba zai iya ba!

Mikewa ya yi rai bace ya dauki kys din sa ya fito yana gannin garin ya yi duhu sosai ,

Motarsa ya shiga ya bale da gudun gaske ya yiwa gidan Ayya tsinke,

Yana karasawa ya fice a motar kys dinsa a hannunsa ya nufi falo dan ya tabata irin wannan lokacin suna zaman falo ne

Yelemin kuwa, suna zaune Ayya na yi mata dankwashi ita kuwa tana zuba shagwabarta ,
Jikinta doguwar riga ce har kasa sai dai irin yadin nan ne mai likewa a jikin mutun ko ya ka motsa zaku motsa tare ne kuma komai rashin kabrin jikin ka zayana nuna motsin halitar jikinka, tana da irin rigunnan da yawa dan yannayin zafi Ayya ta kwaso mata a lokacin da akai mata aure.

Da katon takalminsa ya shigo falon domin bai riga ya cire takalmin da kayan dake jikinsa ba ya samu kiran Elhaj Mubarack,

Haka ya takawa Ayya capet din falonta, abinda ta tsana a rayuwa , dan haka da mamaki take dubansa dan shi ne mutun na farko da zai fadi bata son a shigo mata daki da takalmi, hasalima shi din ma ya tsani hakan a rayuwarsa,

Takim takim yaa tunkaro su inda suka dago su duka suna binsa da kallo har ya karaso gaban

table din kwalbar dake gabansu mai dauke da ruwa da jus
Yana zuwa ya zuba kys din hannunsa da garaje saman table din hakan ya saka suka bada wani kara tamkar zasu fasa table din,

Hannunsa na hagu ya doro saman table din, da na dama kuwa ya dago yatsansa na kusa da baba ya nunata ya ce" ke , daga yau, daga rana mai kamar ta yau, na soke du wani shige da ficen ki a shigar da ba nikaf, hijab dogo da safa, idan kuwa ba haka ba sai na babala ki Agaishat!

Ya karashe yana mai daga muryar da ya saka ta mike tsaye da sauri ,
Mikewar da ta yi ya ainahin girgiza jikinta da karfi domin irin mikewar tsoracen nan ce,

Ido ya zaro ya ce" ba ga irinta ba! Ba ga irinta ba! A ce yarinya baki da kimtsi sai tsale tsale da guje guje da juye juye a gaban ko wani karamin dan iska? Ke ko kunya bakya ji zaki fito da wani mayafi mai kama da rariya ki wani zo kina juyi gaban madubi? Ke ke......
Da haushi haushi ya nufeta da niyar gaura mata mari domin a tsaye da take baki ta turo tana kikifta masa ido, wanda hakan ya kara hautsina masa lisafi

Ayya da ta yi mutuwar zaune cike da mamaki, da kuma darsuwar vakon zargi a kan tilon dan nata game da yar amanarta ta yi sauri cewa" walahi ka dakar min y'a sai ran ubanka ya baci Wardugu!

Ja ya yi ya tsaya, a hankali ya juyo wajen Ayya ya ga ta mike tsaye, kansa ya sada ya karaso kusa da ita a hankali kafin ya ce" Ayya, ya zaki sakawa yarinya ido tana fita da mayafi dan Allah?

Ayya ta ce" Wardugu, auren wani ke kan yarinyata ko bakon abu ne fita da mayafi a matar aure ma bare wace bata da aure? Ba wani shigar tsiraici take yi ta fita ba, aman idan ka saka mata irin dokar nan ba zan dauka ba !

Wardugu ya dago jajayen idannuwansa ya ce" Ayya, sai ta fita da dan mayafi zata samu miji ne? Wani irin miji take nema a rayuwarta ne? Shin ba karatu kika ce tana yi ba? Dan Allah du yanda za.a dagawa mutun hankali an sani? Yaya kuke so na yi ne?

Ayya ta kwalalo idannuwanta kafin ta tafa hannayenta ta ce" Warsugu wani laifi muka yi maka ne?

Wardugu ya yi shiru ya tsurawa cafet din falon ido, can ya fago idannuwansa ya sauke saman fuskar Agaishat dake tsaye tana dubansa, idannuwan su ne suka sarke da juna, kallon second 5 , idannuwan Wardugu jajaye jir da su tamkar gauta, sai dai da wasu yan kwala da ba zata iya kiransu da kwallah ba sai dai tace da su na bacin rai, wani irin kallo mai nauyi, mai tafe da sakwonni, mai dauke da ma.anoni ne ya zuba mata a cikin maraitatun idannuwanta da ta yi tsai ta jefe shi da kallo mai tura sakon *Ka ji tausayi na*,

A hankali ta lumshe idannuwanta ta ji wani irin sulbi a cikin idannuwan nata sannan suka fara rawa sanadiyar irin dokawar da zuciyarta ke yi du idan ta yi arba da shi,

A hankali ya taka ya nufe ta, wanda du takunsa ke barazana da tunanin kwakwaluwarta har ya kasance tunanin ya tsaya cak, ba wani sauran abinda ke aiki a cikin kwakwaluwar nata sai tarin kwalar da ta cika gurbin idannuwanta a hankali ta shiga zubowa,

Kure mata waje ya yi, ya shaki kamshin turarenta,
Idannuwansa ya lumshe ya kai hannunsa ya riko nata , riko na ya riko hannun kanwarsa, riko na ya kamo hannun kanwar sa dan ya jadada kashedinsa a gareta,
Sai dai laushin su ya saka shi dago da hannun da kyau ya bude idannuwansa ya tsura masu ido,
Ajiyar zuciya ya sauke kafin yake daga dan yatsarsa ya ce" ki bi dokana ki tsira, idan ki ka kiya zaki saka mu a uku ne, dan zan farauce ki a duniya ne, zan yi maki farautar kwai ne, Agaishat ki rufa mana asiri ki bamu lokaci, ki rufawa Ayyanki asiri kar ta yi zaman jinya !

Yana gama fada ya juya ya dauki kys dinsa ya juya yana tafe yana hada hanya ya fice a fallon,

Kuka Agaishat ta fashe da shi wanda ya farfado Ayya daga uwar sumar mamakin abinda ya faru da raka Wardugu da ido da ta yi,

Da sauri ta nufi wajen Agaishat ta kamota ta ce" ke Agaishat, menene? Tsoro kike ji ko? Kar ki ji wani tsoronsa in sha Allah ina tare da ke ba abinda zai yi maki!

Agashat ta rike hannun Ayya da kyau , da kyar ta bude bakinta ta ce" Ayya zuciyata ke bugawa, Ayya jikina rawa yake min, Ayya wayo zuciyata gabana ke faduwa du idan na ga yaya Wardugu, Ayya ciwon zuciya ne nake ko????

Shiru Ayya ta yi itama gaban nata ya fadi, kai ina! Aa ba su ba, menene haka? Me ke shirin faruwa ne?

Wardugu na komawa gidansa bangaren Walyn ya nufa,
Kai tsaye ya ritsata zaune tana kallon film a nollywood hankali kwonce,

Hannunsa ya saka ya mikar da ita, a hankali ya jata jikinsa ,
Idannuwansa lumshe ya lalubo lebenta jajir ya kai masu lalausan harshensa ya shiga kissing dinta passionately,

Fama take a kai fage, domin itafa ta fi gane can duda takan jigata aman gani take wani sakwanin wasani bata lokaci ne dan haka ta yi kokarin juya wasan zuwa ga fage mai rikitarwa, hakan ya saka ta yi gagawar cire yar rigar dake jikinta wace ta bayanar da yan berayen halitun

jikinta,

Hannunta ya ja yana so ta yi tafia a gabansa duda ya kashe hasken fitilar dakin, dan damemen gajeran wandon dake jikinta yake so ta motsa ta bashi ma.ana, so yake ta bashi spectacle, yana so idannuwansa su juye kamar yanda a dazu suka juye daga kallon abinda bai zama halalinsa ba,

Saman kujerar ya zauna yana dubanta gannin faman ta baje take, wato ita dai kulun ta baje shi ta iya,

Kansa ya shafa yana dubanta, farar mace jajir, yar suwaiwai mafarkin dubunai, me ke damunsa? Ga hargitsinsa a gabansa ba wani ba, ga cakula kwakwaluwarsa a gabansa ba wani ba,

Hannayensa ya daga duka biyu ya dora saman kansa kafin a fili ya ce" kai kai, ina ba zai yiwu ba, wace wanina ya shiga? Gidan da aminina ya malaka? Wace irin kunya nake son kwasarwa kaina haka?

Walyn dake jiransa ta  dube shi da kyau ta ce" Wardugu?

Wardugu ya bude idannuwansa yana dubanta, bai taba sakar mata nauyinsa mai suna nauyi ba, yakan shigar da gaban motarsa ne dan gannin gidan motar ba zai iya da shi ba, wai ko dai tausaya mata ne  da yake yake sakata daukan raini tana sauke masa? zata iya da shi ne? Kai yau bara ya sakar mata nauyinsa , ko dai dan yana rage sauran nauyin nasa nema take tunanin karfin su daya?
Abinka da  shawarar keta mai samun mazauni, nan da nan ya ji wani karfi na kara shigarsa, karfi irin na namijin saurayin zaki,

Mikewa ya yi ya nufeta da irin bukatarta ya..........

(Rashin kunyar ta isa haka woolah😢)

Dama kyawawa ne, suka kara da wanka, hakan ya saka yan matan suka wani fito fas da su, Mariama da Zainaba sun wani haska suna taku irin na manyan yara,
Abu daya ke kawo masu cikas a zamansu a birni shi ne rashin iya french, su kuwa yan mata da samarin garin Niamey sun dauki yaren French tamkar yaren haihuwarsu, karkadaf idan ka yi wasa zaka bace a hira da su, wato sun lakance shi ne ya saka har ruwa ruwa suke da harshe da gagawar magana tamkar jikokin macron (😕),
Kakarsu tana cikin koya masu wanka na yayan gayu da suka jiku a cikin gayu,
An koya masu mota, su ke zuwa alimentation siyayar kayan kicin da na frij, suna koyan su cake da sauransu,

Anna ta murje, ta murje ta faso, Anna bata magana daya biyu ba tare da ta jefa turanci wato inglish a ciki ba domin makarantar da ta yi ana koya masu yaran ne duka biyu a tare, Rayuwarta na da ya dawo, ta dawo cikakiyar yar birni mai wayayen kai da iya tafiar da rayuwarta a nitse ba da hayaniya ba,

Takan shiga damuwar rashin labarin Agaishat, sai dai hankalinta na kwonciya idan ta tuna ai ta bada aurenta tana dakin mijinta kuma ko ba dade ko ba jima zata neme su fatanta dai Allah ya sa tana cikin rayuwa mai nagarta a gidanta,

Sai maganar Algabitt da suke jiran bilowarsa dan abinda ya tsaye masu a rai ya sakar masu y'a !

Timiya,

Sarki ya kada , ya raya, yana so ta janye maganarta aman fir ta rikice masa kan walahi ita magana daya ce tana so a fitar mata da hakinta a matsayinta na yar gari wace take da inci a kan wanda ya cuta mata,

Ya so su yi lamarin a sirri aman ta kiya ita kawai a yi masu shari.a da Algabitt dake rufe a matsayin mai dauke da laifi mai girma a gidan sarki,

Garin ba wanda bai san halin da ake ciki ba dan haka kananun magangannu ke yawo cewar za.a ga idan sarki zai hukunta sirikinsa bisa laifin da ya yi, idannuwa dai a kansa wanda hakan ya saka dole ya fitar da shari.ar fada,

Komai na son sirri, abinda ya yi ta nanatawa Gaishata dake kukan wannan lamari,

Gigirigin kennan ranar fadin gaskiya,

Tare wajen yake dankam, cike da jama.a, an taru an cika an yi makil abinka da kauye kowa ya zo ya ga kwaf,

Sarki zaune ya hakimce da rawaninsa na turkudi, gefe da gefensa du dogarai ne da yaran gidan sarki,
Sarkin bulala tsaye yana dan kadata lokaci zuwa lokaci,

Gefe guda matan sarki ne laye cikin shiga ta alfarma kowace na isa da kanta a matsayin na matar mai garin timiya,

Gaishatama zaune take ta sha turkudinta mai kala biyu blue da maroon an yi mata dinkin zamani ta rufa da katon mayafi hannayenta dauke da warwarayen zinari , ba yara a wajen domin ko yayansu a gida a aka bar su ,

Dayan gefen kuwa Algabiittt ne ke zaune shima yana ta kale kale alamomin rashin gaskiya sun bayana a tare da shi,

Gayaran murya sarki ya yi kafin ya ce" kamar yanda Timiya yake karamin gari mai dauke da sarki ni Ibrahim Asadeek, timiya ta kasance garin da talakanta ke da inci, muna zakulo du wanda ke tayar da zaune tsaye mu hukunta shi bisa tsarin adini,

Dogarai sai amsa shi suke kafin ya ci gaba da fadin" a yau , mun zauna a wannan waje dan tuhumar Malan agabitt kan manyan laifuka da muke tuhumarsa da su wa.inda matar da yake zaune da ita ta shigar da karar tun kafin ta bar gari , yanzu da bata nan bisa madadinta ga y'arta wato gimbiya gaishata , muna masu umartar Algabiit da ya bayana mana haduwarsa da mahaifiyar yayansa, dalilin da ya saka ya yi rayuwar wulakanci da ita....

Shiru ya yi yana kifta ido ya ki yin magana,

Ajiyar zuciya Sarki ya sauke kafin ya ce" idan har mai laifin ya yi gardama, kadarorinsa na gida da gonarsa da ake yi masa noma za.a karbe sannan ya fuskanci hukunci mai tsanani,

Ido ya zaro yana duban Sarki, shi bashi da damuwar wai mutanen wajen su ji abinda ya aikata, shi damuwarsa hangen daya daga cikin wa.inda suka bashi kudaden su Mariama da ya yi, ya tabata idan sarki ya kore ahi daga Timiya ya kade, dan haka ya gyara rawanin kansa ya shiga bada labari kamar yanda Anna ta bada har zuwa ranar da zai tafi da ita inda ya ce" a ranar safiya na yi na koma wajen bokana, wanda yake anguwar Talagué pays ba, ina zuwa na karbo abubuwan da na bashi ajiya domin ni ke kai masa abubuwa shima yana neman kudi da ni, inda ya dora ni a hanyar da zan hadu da yar masu kudi,

Maganin cire ne, wanda hasalij kirana daga garin haihuwana wato tanut dan ina yawan ciren yayansu,

Dakatar da shi aka yi ta hanyar tambayar menene cire?

Dago da kansa ya yi ya ce" Cire, wani asiri ne da fulanin daji ke yi , wanda na gada wajen kakana na wajen mahaifiyata dan shi filo ne, cire asiri ne da idan aka yiwa mace take bin namiji , bata da wani ra.ayi nata sai nashi,
Na hada da cire da asirin da bokan ya samo wajen wani bokansa dan dogon dutsi cewar idan na aikata idona idonta an kare zata bi ni ne du inda zan je, kuma ko me zan mata ba zata iya barina ba dan zatana jin tsoron zuciyata da bacin raina , sai dai kar na yarda ni da bakina na

ambata mata sunnan garin su , ko sunnanta na asali, ko na yan uwanta, in dai ba ni na fada ba koma wa zai fada sai dai ya shiga tunani kamar ta san abin aman ta watsar daga baya dan zai tayar mata da hankali sosai

Na ci sa.a na cireta, muka fice a gidan daidai salar azahar muka dauki hanya da kudaden jakarta inda na yi wurgi da wayarta muka dauki yawon duniya,
Masalatai sun fi a kirga na je dan a aura mana aure, aman sai su ce koda bamu da kowa a duniya sai sun yi magana daga su sai ita, daya na amince sun fara maganar na ga sai wani tambayoyi yake yana faman tona asirina na bige shi da sadanta na dauketa muka kara shiga yawon duniya kafin daga baya na yada zango a nan,

Zufa ce ta shiga karyowa Gaishata, sarki kansa ji ya yi lumfashi na neman gagararsa,

Gaishat bata san lokacin da ta ce" kana nufin ba.a daura aurenka da matarka tsawon zaman da ka yi da ita harda hayayafa ba?????

To fa

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

68

Asalamu alaikum
*Allah ya kawo mu wata mai albarka, banban wata mai tare da lada ,wata mai cinye zunubi, RAMADAN, ALLAH KA KARAWA ANNABI DARAJA TARE DA WASILA DA FARILLAH A ALJANAR FIRDAUS Allah ka jikan magabatan mu, ka sa sun huta, idan tamu ta zo ka sa mu cika da imani ka sa mu tarda alkhairi 👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻 Ya Allah, muna rokon ka, ka shirye mu, ka inta mu, ya ubangiji ka yafe mana zunubanmu, Allah ka hane mu saba maka,Ya Allah ka dora mu a hanyar bautarka, ka karbi ibadunmu, Ya Allah ka sa mu bayansa lafia ka maimaita mana, ni sajida ina mai yi mana fatan Alkhairi da fatan Allah ya kai.mu rai da lafia bayan sallah*

Algabitt ya dago da dubansa ya sauke kan Gaishata dake wani irin numfarfashi gabanta na faduwa tana duban mahaifin nata,

Algabitt ya kauda kansa yana bin mutanen dake zaune daya bayan daya da ido,
Kansa ya girgiza kafin ya kai dubansa wajen sarki ya ya buda bakinsa zai yi magana sarki ya mike tsaye ya ce" ya isa, kar ka fadi komai,

Muryar uwar gidansa ne ta ce " sarkina, talakawa na zaune suna jiran hukunci,

Amaryarsa ce ta gyara zama ta saki murmushi ta ce" sarkina, muna masu neman alfarmar a yi hukunci yanda aka saba yiwa sauran talakawa,

Gaishata dake bin su da kallo su duka biyu ta maido dubanta wajen Sarki da ya tsurawa matan nasa ido cike da takaici,

Gaishata ta share hawayenta ta sada kanta kasa,

Sarki ya koma ya zauna yana duban dogarai dake muzurai , sun so su tsawatarwa da matan sarki sai dai gannin matan sarkin ne tsoro ya hana su su yi masu magana domin ba wanda yake da hurumin yin magana idan sarki da kansa na shari.a duda kauye ne, idan baya nan akoy mai wakiltarsa ,

Hade rai ya yi ya ce" du wanda ya kara buda baki ya yi magana a wajen nan zai karbi hukunci komai kusancinsa da Sarki!

Idan Dogarai suka ga abin tsawatarwa basu tsawatarba zasu fuskanci fuahina!

Ji kake suna fadin" tuba muke sarkin talakawa,

Sarki ya maida hankalinsa wajen Algabittt ya ce" tabas ka kasance mutun mai son kansa, ka yi rayuwa bisa umarnin zuciyarka, tabas munada muradin jin bukatar wace aka fi cuta duda ta bada amanar yarta ta wakilce ta, dan haka zamu iya sauraron zuwanta ko maganarta a waya,

Magana yake hankalinsa ba a kwonce ba domin tunda Gaishata ta sada kanta bata dago ba,

Mikewa ya yi ya danna kira kan number Gukunni ,
Bayani ya kora masa na komai cikin nutsuwa , yana gamawa Gukunni ya tarda matarsa da y'arsa, cikin hikima ta manya ya zayane masu komai wanda ya saka Anna fashewa da wani irin kuka har tana dukewa tana dafe cikinta da dukan hannayenta,

Mahaifiyarta dake kuka itama tana duban jikokin nata da suka dora hannayensu saman kansu sun kasa magana tsabar shiga firgici da tashin hankalin jin wai su din ashema ga ta hanyar da aka same su duniya ta kawar da kanta wajen mijinta dake zaune sai zufa yake ta rintse idannuwanta zafafan hawaye suka zubo mata ta bude murya ta ce" na haifi Allacthi ta hanya mai kyau wace Allah ya nufe ni,
Ban bi kowa ba, haka mahaifinta ya kasance mai kiyaye wannan lamari,
Wannan kadara ce mai girma wace ta girmi tunanina,
Tabas na zama wawa a wannan lamari,
Shin wa zan kaiwa kuka a nan gidan duniya?
Yau du abinda za.a yiwa wannan bawa in dai ba dawo da shekaru baya za.a yi ba a dawowa da y'ata martabarta bana tunanin zan ji zuciyata wasai,
Yau ko yikuwa na cakawa wannan mutun ban goge komai ba,
Idan rufe shi aka yi ma ba.a dawo baya ba,
Wai wai wai ni Herde wai rayuwa Hamdulilah, Allah na gode maka,
Gukunni, dan Allah ka yi kiran wannan yaron ka fada masa ni nace dan Allah ya saki wannan mutumin da ba zan so maimaita sunansa ba,

Ya bar shi, *wata shari.ar sai a lahira*,

Tana fada tana ta share hawayenta ne tana kula da irin yanda Anna ta dafe zuciya tana gumurzun kuka,

Wajenta ta nufa dan ta lura Gukunni sauraronta kawai yake,

Kama Anna ta yi ta kwontar da ita ta dubi Mariama,
Hade fuska ta yi danma kar su daga mata hankali ta ce" ke maza je ki yi kiran docter Aliyu, maza ya zo ina jiransa,

Maida dubanta ta yi wajen Gukunni ta ce" ba zai ga bayan farin cikin gidanna ba, ba zan yarda wani katon gardin dan kauye saka baki a rayuwar da ta doso ni mai tsananin haske,
Zan so na ga jarumtar ka a wannan lamari Gukunni? Zan so na ga dauriyarka, ka kama mani kar na rasa y'ata, sannan ka fadawa Ibrahim Asadeek cewa idan ya ga zama da Gaishata wani damuwa ne, ya dawo min da ita da yaronta,

Gukunni dake zaune yana dubansu ya mike ya fice a gidan ,

Zuwa ya yi aeroport neman jirgin da zai kai shi agadez domin mai tuka nasa jirgin yana hutu ba zai so takura shi ba,
Sai dai ina ba jirgin agadez kwata kwata a ranar, dan haka da kansa ya tuka mota zuwa gidan yaron nasa soja kuma matukin jirgi ya je masa ya fada masa bukatarsa inda ya baiwa matarsa hakuri cewar idan har sun kwana hali ne ya kama babu niyar hakan!

Abinka da manya masu garin, haka suka zarce inda ya yi kira ya nemi alfarmar zai tashi da jirgi tafiar gagawa abinda ya shafi familynsa domin koda kana da jirginka ba kyau tashi lokacin da ka yi niya sai an baka izini

Basu wani sauka a Agadez ba, tafia suka yi mai dan tsayi sai garin timiya inda ya yi ta shawagi dan samu wajen sauka wajen da ba rere da kuma duwatsu, sannan wajen da idan zai tashi zai samu dan hanyar tafia kafin ya cira,

Da kyar dai , da kyar ya samu wajen da ya nuna masa zai iya sauka, inda yara tuni suka fito baki bude sunna kallon wannan abu mai kara mai ficewa can sama yau yana yin kasa kasa cikin gari, hakan ya saka wasu firgita da tsoron fadowa zai yi ya kashe su,
Inda wannan lamari ya ja hankalin mutanen fada da suka ki watsewa du suka dugunzuma zuwa gannin abinda ke faruwa kuma,
Dole sarki ne zai je gaba , dan haka ya mike ya kai dubansa wajen Gaishata dake yanda take ya juya da sauri ya tafi dan duba lamarin kauyensa inda yake tafe yana ayyana dole ya ajiye sarauta , shi kam ya kai wajen da ya ji takaicin kasancewarsa sarki,

Suna samun tsayawa Gukunni ya mike ya fito domin ya bude masa kofa inda shi kuwa ya zauna ciki yana gyare gyare da duba idan komai lafia dokin wajen ba wajen saukar jirgi bane

Ido Sarki ya kwalalo gannin Gukunni,
Mutane kuwa kallon mutun da baki haka a cikin jirgi suke, daman bakima na shiga?

Wajen sarkin ya nufa inda Algabitt ya kusan zubewa kusa da dogarin dake tsare da shi,

Ai kuwa juyawa ya yi da jiyar baiwa wandonsa iska sai dai an tare ko.ina,

Hayaniyar a sake shi ta ja hankalin Gukunni waje sa, dan haka ya saki hannun sarki da suka

gaisa ya nufi wajensa yana dubansa da kyau

Yana zuwa ya tsaya gabansa inda Algabity ya zama wani cirit a gabansa,

Gukunni ya girgiza kansa, a fili ya ce" wai a gaban halita irinka kana haka ina ga ka je gaban wanda ya halice ka? Tabas ba sauran abinda zan yi shari.a a nan,

Yana gama fada ya koma wajen sarki ya ja hannunsa gefe,
Cikin nutsuwa ya ce" ina gaishata ne?

Sarki ya sada kansa kafin ya ce" tana cikin wani hali, ba yanda ban yi da ita kan a yi shari.arnan a sirince aman ta kada kai ita sai an yita a fada, hakan ya hadasa mata tashin hankali,

Kansa ya girgiza idannuwansa da sukai ja ya ce" ka san me? Shi du abinda Allah ya hanna, ma.aiki ya kawo mana mu yi aiki da shi,
Shi tsananta bincike ba kyau,
Yanzu wa gari ya waya?

Sarki ya kada kai yana duban gefe da yannayin damuwa,

Gukunni ya ce" zan so ka bani ita mu je gida, idan har kana ra.ayin hakan, zan so ta je ta huta, zamu so mu hada su su duka mu yi magana da su, zan so su saurari gargadi da nasiha ta zaman da zasu yi na rayuwa,
Tanas duniya ta ci gaba aman banda wajen mata,
Wannan bakin fentin na iya hana su sukuni cikin mata yan uwansu,

Zan so ka yi min wannan alfarma,

Sarki ya gyada kansa ya ce" tabas mata suna girma aman suna cin kasa, a yanzu haka har na so soke maganar abokan zaman nata suka takalota,
Dan haka yin hakanma ba laifi bane, nima ina kan duba wani lamari na nan , zan yi shawara da tsofafi magabata in sha Allah, a taya mu da adu.a Allah ya sa abinda za.a shiga alkhairi ne

Gukunni ya amsa shi cike da farin cikin zai bashi Gaishatar da zuciya guda,

Juyawa suka yi dan shiga ciki Gukunni ya ce" ita dai dayar har yanzu ba labarinta ko?

Sarki ya ce" aa, da wasika da wanda take hannunsa ya kawo, bara na dauko wasikar ni ai na sha.afa abubuwa sun shige mini,

Juyawa ya yi cikin gidansa inda Gukunni ya karasa wajen Gaishata ya duka,

Hannunsa ya saka ya dago habarta, kir idannuwanta abude suke sannan a soye,

Sauke idannuwanta da ta yi saman fuskar kakanta ta ji bakinta ya bude, murya na rawa ta rike hannunsa ta ce" ashe mu shagu ne ba aure Algabitt ya rayu da mu? Ya zamu yi rayuwa a cikin wannan lamari? Ya zan rayu cikin kishiyoyi da kauye a haka?
Ya kanuna da basu samu miji ba zasu samu a irin wannan rayuwa ta yanzu? Idan Agaishana ta ji haka, ya zata dauka? Ya mijin dake aurenta zai dauka?

Gukunni ya lumshe idannuwansa ya mike ya samu ya dagata ya dubi mai aikinta ya yi mata umarnin maza a dauko sultan,

Bai bata amsa ba sai jan hannunta da ya yi suka nufi wajen jirgi inda ha baki bude aka raka su da kallo , da yawan mutanen da fadin ko dai Uban Agaisha ne? Wato Bak'A?

Nan ya tsaya jira har sarki ya fito suka kara gaisawa ya bashi takardar da Wardugu ya kawo dauke da wasikar da bai karanta ba,

Juyawa ya yi ya basu waje shi da matarsa su yi salama kafin suke dagawa,

Wajen yama tuni sun dawo garin niamey inda mai tuka shi ya ja su har gidan su,

Suna zuwa ya saka ta fice shi kuwa yana rike da Sultan dake dan wasansa na jarirai ,

Ajiyar zuciya ya sauke ya daga idannuwansa sama yana kallon sararin samaniya,

Takardar nan ya bude ya duba,

Number waya ne kawai tsararu masu bin juna sai sunnan da ya zirawa ido da mamakin gannin sunnan , shin sunna ne ya zo daya haka ko kuwa shi din ne?

Wato jan gwarzon nan, yaro mai hazaka, yaron da yake ji fa shi dan aiki na yawan hada su, yaron da idan yana kallon abubuwan da ya yi a duniya har wani tsam yake ji da jin wani yannayi na shauki da jinjina masa da gannin girmansa tamkar wani datijo, yaro karami mai watsa taron yan daba, wato *WARDUGU BATUBE DAN MARAHUT*

MA.ASALAM

🐫🐫🐫 *BAK'A CE*

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*
___________________________________

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

7️⃣0️⃣

Barkan mu da sallah jama.a,

*KUTKALE*

*Aure yakin mata ne*

*Kamarta bata da niyar cutarwa*

Kar ku bari a baku labari.....

Mikewa ta yi tsaye, nan doguwar rigar da ta saka wace ta bi jikinta ta sauka kasa ta kara ainahin fitar da surar jikinta da wani tsararen kyau mai fizga,

Lafayar ta dauko da niyar sakawa sai dai me, tana dubawa da kyau ta ga ai wannan ta ranar dinern da aka shirya ce,

Juyowa ta yi wajen Alhinayet dake zaune cikin shigar turkudi riga da zani sannan ta yaye kanta da shi ta fiti fit Buzuwarta ta ce" Alhi, dan Allah ki saka a kaini gida na dauko Lafayata, wannan ta gobe ce na dauko ashe,

Alhinayet ta ce " Ohk ki je wajen Salisu motar a hannunsa dan tun jiya colonel ya hana na kuma fita da ita ,

Agaishat ta amsa inda ta dauki Abayarta ja mai adon baki baki a jiki mai mabalai ta saka sannan ta yane kanta da mayafin abayar,
Kai Agaishat fa ta gama haduwa, dogon hancin nan nata ya zo har kusan bakinta mai dan girma kadan, gashin girarta kuwa ta caje shi ta daidaita shi ya yi tsaf da shi ya bada kala, tsarin fuskarta kyauta ce daga Allah, gashi kuma ya hadu da nutsuwar yannayi,

Cikin nutsuwa take takawa har ta samu fitowa inda ta hange shi domin an saka fitilu ko.ina,

Tana zuwa da muradinta ya mike ya tafi wajen motar suka shiga ya jata sai gidan Ayya, wato mahaifiyar ogansu,

Suna shiga gidan Agaishat ta ga motoci har shida,
Biyar din kalarsu daya, sannan ga sojoji tsatsaye du sun hade fuska tamkar an zage su,

Tsayar da ita aka yi sai da aka cajeta dan kuwa ogansu na ciki ko wa bai isa ya shiga kansa tsaye ba,

Ji ta yi kafafuwanta na rawa, dan ba alamar sasauci a fuskokin su, dan haka a hankali ta samu ta raba ta haye inda ta fura kofar falon ta shiga da salama murya a dan dage kadan dan mutanen dake ciki su ji ta,

Salamar ce ta katse, a daidai lokacin da idannuwanta sukai mata arba da su,
Da Farko dai Wardugu ne da kakin soja sai dai botiraan rigar a bale inda rigar shi ta ciki fara kar ta samu damar bayana kanta da pecto dinsa,
Kafarsa daya kan daya ya dora, yana danna waya aman salamarta ya saka shi dago kansa da sauri tare da bugawar zuciyar da ta saka shi lumshe dara daran idannuwansa,

Gefe kuwa mijinta ne, uhum ba mijinta ba, tsohon mijinta, wato Mu.azam, docter Mu.azam ne zaune sanye da costume bakake da cravate dinsa ya daure cif da shi, duda kansa a aske kwal aman bai hanna bayanar kyansa ba,

Sai Ayya dake zaune cikin lafayarta , daga kasa kuwa Khadija ce ta duka da alama neman gafara take,

Idannuwanta ta lumshe, ta kara,lumshewa, dukan wata jarumta da take tunanin tana da ne take gayatowa , sai dai ina, gaba daya jikinta ne ya kwashi rawa wanda hakan ya yi sanadiyar sakin dankareriyar samsung dinta kasa inda ta bada Pats screen ya mutu🤦‍♀️,
Dubanta ta kai wajen wayar , ta yi azamar dukawa dan dauka, sai dai gaba daya ta shiga raruma tana saki, ta kasa daukan!
Dan haka ta mike ta tsalaka wayar ta juya da gudu gudu ta shiga hawan bene dan neman

dakinta tana kokarin dane wani katoton kuka dake taso mata da karfin tsiya,

Ayya ce ta mike da sauri, inda ta ga gilmawarsa kawai, da karfinsa yake taka matatakalar yana nufar inda take inda idannuwansa suka rufe hankalinsa ya tashi,

Ayya ta ce" Wardugu,

Ina baya jinta, shima adu.a yake, fata yake na Allah ya sa ba kukan abinda yake tunani take yi ba,

Dakinta ya tura ya shiga,

Idannuwansa kyam saman kanta inda ya ga ta cire abayar jikinta sauran doguwar rigar nan ta cire dan kwali ta yar , ta kifa kanta saman abin bed, kuka take har tana jijiga,

Innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, shi ne abinda ya iya furtawa kafin yake karasawa inda take,

Hannayensa ya saka wajen kafadunta ya dagota tsaye gaba dayanta,

Kokarin bude jikakun idannuwanta take , sannan zufa ta jike gashinta daga gaba tamkar ta watsa ruwa, fuskar nata ta jike jagab tana hakin kuka,

Bai bari ta karasa bude idannuwan nata ba ya janyota gaba dayanta cikin ni.imtacen jikinsa, wani irin riko ya yi mata gaba dayanta tamkar sabon babyn da baya so a kwace masa,

Kamshinsa, da wani irin bugawar da zuciyarsa ke yi wada tana iya ji a irin rikon da ya yi mata, da kuma bakon lamarin wai ita Agaishat kwonce a kirjin Wardugu, namiji daya ya daya, Wardugu zaki, wardugu guguwa lahaula wala kuwata, wani juuu ta ji wata juwa na neman debarta ita dake kwonce luf a saman kirjinsa, kukan ta nema ta rasa, hasalima mantawa ta yi ta yanda ake rera wakar kukan,  sai wani ajiyar zuciya da take zaukewa mai dumin gaske saman kirjinsa dake bude,

Hannunsa dake rawa ya dago a hankali ya dora saman gashin kanta dake malale saman gadon bayanta ya dora ya dan ja hannunsa kasa sannan ya maido sama,

Tsayar da hannun ya yi yana kokarin bude idannuwansa da ya rufe ruf,
Muryarsa na rawan da bai taba yi ba, hannunsa na rawa ya ce" menene? Mu.azam ne?

Shiru ta yi bata iya bashi amsa ba, hasalima kokowa take da numfashinta domin yana buda baki maganarsa na watso mata kanshin turaran baki da yake anfani da shi mai kanshin banana

A hankali ya dora hancinsa saman goshinta, hakan ya baiwa bakinsa damar zuwa wajen jikakun idannuwanta,
Ji ta yi ya damki hannunta na dama da dan karfi kadan, sannan ya ce" *Son shi ki ke yi ko?*,
*KUKAN SON TSOHON MIJINKI KI KE?*

masha Allah, Alhamdulilah, barkan mu da sallah yan uwa. ALLAH ya karba mana .....Amen

*TALLAH TALLAH TALLAH*,

*KUTKALE*

*PRISON KUTKALE*

Kwonce take inda aka gama jibgarta dan ta yiwa Eliz gardama, wani bacin wahala me ya kwasheta inda kamar daga sama ta ji ana lalubarta,,
Hannu ne, kokarin kai hannun ake cikin dadaudan sqet dinta wanda ko karamin wando babu a ciki, wato dai malan shigo...........

Domin karin bayani ka tumtubi +22791466605

Labaru masu zuwa in sha Allah

*AURE....YAKIN MATA NE*

*KAMARTA BATA DA NIYAR CUTARWA*

DAGA ALKALAMIN *SAJIDA* YAR MUTAN NIGER MARUBUCIYAR

*DUK KARYAR KADA*,

*YAR MAHAUKACIYA*

*DAGA TAFIA DAUKAR SOJA*

*BANI DA ZABI*

*NEMAN NA KAINA*

*BAK'A......*

Fan's barka da sallahna🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔😢😢🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔😢🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔🤔😢🤔😢😢😢😢😢😢😢😢

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤️*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝🏻😘

Na
*SAJIDA*

68

Asalamu alaikum

*Allah ya kawo mu wata mai albarka, banban wata mai tare da lada ,wata mai cinye zunubi, RAMADAN, ALLAH KA KARAWA ANNABI DARAJA TARE DA WASILA DA FARILLAH A ALJANAR FIRDAUS Allah ka jikan magabatan mu, ka sa sun huta, idan tamu ta zo ka sa mu cika da imani ka sa mu tarda alkhairi 👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻 Ya Allah, muna rokon ka, ka shirye mu, ka inta mu, ya ubangiji ka yafe mana zunubanmu, Allah ka hane mu saba maka,Ya Allah ka dora mu a hanyar bautarka, ka karbi ibadunmu, Ya Allah ka sa mu bayansa lafia ka maimaita mana, ni sajida ina mai yi mana fatan Alkhairi da fatan Allah ya kai.mu rai da lafia bayan sallah*

Algabitt ya dago da dubansa ya sauke kan Gaishata dake wani irin numfarfashi gabanta na faduwa tana duban mahaifin nata,

Algabitt ya kauda kansa yana bin mutanen dake zaune daya bayan daya da ido,
Kansa ya girgiza kafin ya kai dubansa wajen sarki ya ya buda bakinsa zai yi magana sarki ya mike tsaye ya ce" ya isa, kar ka fadi komai,

Muryar uwar gidansa ne ta ce " sarkina, talakawa na zaune suna jiran hukunci,

Amaryarsa ce ta gyara zama ta saki murmushi ta ce" sarkina, muna masu neman alfarmar a yi hukunci yanda aka saba yiwa sauran talakawa,

Gaishata dake bin su da kallo su duka biyu ta maido dubanta wajen Sarki da ya tsurawa matan nasa ido cike da takaici,

Gaishata ta share hawayenta ta sada kanta kasa,

Sarki ya koma ya zauna yana duban dogarai dake muzurai , sun so su tsawatarwa da matan sarki sai dai gannin matan sarkin ne tsoro ya hana su su yi masu magana domin ba wanda yake da hurumin yin magana idan sarki da kansa na shari.a duda kauye ne, idan baya nan akoy mai wakiltarsa ,

Hade rai ya yi ya ce" du wanda ya kara buda baki ya yi magana a wajen nan zai karbi hukunci komai kusancinsa da Sarki!

Idan Dogarai suka ga abin tsawatarwa basu tsawatarba zasu fuskanci fuahina!

Ji kake suna fadin" tuba muke sarkin talakawa,

Sarki ya maida hankalinsa wajen Algabittt ya ce" tabas ka kasance mutun mai son kansa, ka yi

rayuwa bisa umarnin zuciyarka, tabas munada muradin jin bukatar wace aka fi cuta duda ta bada amanar yarta ta wakilce ta, dan haka zamu iya sauraron zuwanta ko maganarta a waya,

Magana yake hankalinsa ba a kwonce ba domin tunda Gaishata ta sada kanta bata dago ba,

Mikewa ya yi ya danna kira kan number Gukunni ,
Bayani ya kora masa na komai cikin nutsuwa , yana gamawa Gukunni ya tarda matarsa da y'arsa, cikin hikima ta manya ya zayane masu komai wanda ya saka Anna fashewa da wani irin kuka har tana dukewa tana dafe cikinta da dukan hannayenta,

Mahaifiyarta dake kuka itama tana duban jikokin nata da suka dora hannayensu saman kansu sun kasa magana tsabar shiga firgici da tashin hankalin jin wai su din ashema ga ta hanyar da aka same su duniya ta kawar da kanta wajen mijinta dake zaune sai zufa yake ta rintse idannuwanta zafafan hawaye suka zubo mata ta bude murya ta ce" na haifi Allacthi ta hanya mai kyau wace Allah ya nufe ni,
Ban bi kowa ba, haka mahaifinta ya kasance mai kiyaye wannan lamari,
Wannan kadara ce mai girma wace ta girmi tunanina,
Tabas na zama wawa a wannan lamari,
Shin wa zan kaiwa kuka a nan gidan duniya?
Yau du abinda za.a yiwa wannan bawa in dai ba dawo da shekaru baya za.a yi ba a dawowa da y'ata martabarta bana tunanin zan ji zuciyata wasai,
Yau ko yikuwa na cakawa wannan mutun ban goge komai ba,
Idan rufe shi aka yi ma ba.a dawo baya ba,
Wai wai wai ni Herde wai rayuwa Hamdulilah, Allah na gode maka,
Gukunni, dan Allah ka yi kiran wannan yaron ka fada masa ni nace dan Allah ya saki wannan mutumin da ba zan so maimaita sunansa ba,

Ya bar shi, *wata shari.ar sai a lahira*,

Tana fada tana ta share hawayenta ne tana kula da irin yanda Anna ta dafe zuciya tana gumurzun kuka,

Wajenta ta nufa dan ta lura Gukunni sauraronta kawai yake,

Kama Anna ta yi ta kwontar da ita ta dubi Mariama,
Hade fuska ta yi danma kar su daga mata hankali ta ce" ke maza je ki yi kiran docter Aliyu, maza ya zo ina jiransa,

Maida dubanta ta yi wajen Gukunni ta ce" ba zai ga bayan farin cikin gidanna ba, ba zan yarda wani katon gardin dan kauye saka baki a rayuwar da ta doso ni mai tsananin haske,
Zan so na ga jarumtar ka a wannan lamari Gukunni? Zan so na ga dauriyarka, ka kama mani kar na rasa y'ata, sannan ka fadawa Ibrahim Asadeek cewa idan ya ga zama da Gaishata wani damuwa ne, ya dawo min da ita da yaronta,

Gukunni dake zaune yana dubansu ya mike ya fice a gidan ,

Zuwa ya yi aeroport neman jirgin da zai kai shi agadez domin mai tuka nasa jirgin yana hutu ba zai so takura shi ba,
Sai dai ina ba jirgin agadez kwata kwata a ranar, dan haka da kansa ya tuka mota zuwa gidan yaron nasa soja kuma matukin jirgi ya je masa ya fada masa bukatarsa inda ya baiwa matarsa hakuri cewar idan har sun kwana hali ne ya kama babu niyar hakan!

Abinka da  manya masu garin, haka suka zarce inda ya yi kira ya nemi alfarmar zai tashi da jirgi tafiar gagawa abinda ya shafi familynsa domin koda kana da jirginka ba kyau tashi lokacin da ka yi niya sai an baka izini

Basu wani sauka a Agadez ba, tafia suka yi mai dan tsayi sai garin timiya inda ya yi ta shawagi dan samu wajen sauka wajen da ba rere da kuma duwatsu, sannan wajen da idan zai tashi zai samu dan hanyar tafia kafin ya cira,

Da kyar dai , da kyar ya samu wajen da ya nuna masa zai iya sauka, inda yara tuni suka fito baki bude sunna kallon wannan abu mai kara mai ficewa can sama yau yana yin kasa kasa cikin gari, hakan ya saka wasu firgita da tsoron fadowa zai yi ya kashe su,
Inda wannan lamari ya ja hankalin mutanen fada da suka ki watsewa du suka dugunzuma zuwa gannin abinda ke faruwa kuma,
Dole sarki ne zai je gaba , dan haka ya mike ya kai dubansa wajen Gaishata dake yanda take ya juya da sauri ya tafi dan duba lamarin kauyensa inda yake tafe yana ayyana dole ya ajiye sarauta , shi kam ya kai wajen  da ya ji takaicin kasancewarsa sarki,

Suna samun tsayawa Gukunni ya mike ya fito domin ya bude masa kofa inda shi kuwa ya zauna ciki yana gyare gyare da duba idan komai lafia dokin wajen ba wajen  saukar jirgi bane

Ido Sarki ya kwalalo gannin Gukunni,
Mutane kuwa kallon mutun da baki haka a cikin jirgi suke, daman bakima na shiga?

Wajen sarkin ya nufa inda Algabitt ya kusan zubewa kusa da dogarin dake tsare da shi,

Ai kuwa juyawa ya yi da jiyar baiwa wandonsa iska sai dai an tare ko.ina,

Hayaniyar a sake shi ta ja hankalin Gukunni waje sa, dan haka ya saki hannun sarki da suka gaisa ya nufi wajensa yana dubansa da kyau

Yana zuwa ya tsaya gabansa inda Algabity ya zama wani cirit a gabansa,

Gukunni ya girgiza kansa, a fili ya ce" wai a gaban halita irinka kana haka ina ga ka je gaban

wanda ya halice ka? Tabas ba sauran abinda zan yi shari.a a nan,

Yana gama fada ya koma wajen sarki ya ja hannunsa gefe,
Cikin nutsuwa ya ce" ina gaishata ne?

Sarki ya sada kansa kafin ya ce" tana cikin wani hali, ba yanda ban yi da ita kan a yi shari.arnan a sirince aman ta kada kai ita sai an yita a fada, hakan ya hadasa mata tashin hankali,

Kansa ya girgiza idannuwansa da sukai ja ya ce" ka san me? Shi du abinda Allah ya hanna, ma.aiki ya kawo mana mu yi aiki da shi,
Shi tsananta bincike ba kyau,
Yanzu wa gari ya waya?

Sarki ya kada kai yana duban gefe da yannayin damuwa,

Gukunni ya ce" zan so ka bani ita mu je gida, idan har kana ra.ayin hakan, zan so ta je ta huta, zamu so mu hada su su duka mu yi magana da su, zan so su saurari gargadi da nasiha ta zaman da zasu yi na rayuwa,
Tanas duniya ta ci gaba aman banda wajen mata,
Wannan bakin fentin na iya hana su sukuni cikin mata yan uwansu,

Zan so ka yi min wannan alfarma,

Sarki ya gyada kansa ya ce" tabas mata suna girma aman suna cin kasa, a yanzu haka har na so soke maganar abokan zaman nata suka takalota,
Dan haka yin hakanma ba laifi bane, nima ina kan duba wani lamari na nan , zan yi shawara da tsofafi magabata in sha Allah, a taya mu da adu.a Allah ya sa abinda za.a shiga alkhairi ne

Gukunni ya amsa shi cike da farin cikin zai bashi Gaishatar da zuciya guda,

Juyawa suka yi dan shiga ciki Gukunni ya ce" ita dai dayar har yanzu ba labarinta ko?

Sarki ya ce" aa, da wasika da wanda take hannunsa ya kawo, bara na dauko wasikar ni ai na sha.afa abubuwa sun shige mini,

Juyawa ya yi cikin gidansa inda Gukunni ya karasa wajen Gaishata ya duka,

Hannunsa ya saka ya dago habarta, kir idannuwanta abude suke sannan a soye,
Sauke idannuwanta da ta yi saman fuskar kakanta ta ji bakinta ya bude, murya na rawa ta rike hannunsa ta ce" ashe mu shagu ne ba aure Algabitt ya rayu da mu? Ya zamu yi rayuwa a cikin wannan lamari? Ya zan rayu cikin kishiyoyi da kauye a haka?
Ya kanuna da basu samu miji ba zasu samu a irin wannan rayuwa ta yanzu? Idan Agaishana ta ji haka, ya zata dauka? Ya mijin dake aurenta zai dauka?

Gukunni ya lumshe idannuwansa ya mike ya samu ya dagata ya dubi mai aikinta ya yi mata umarnin maza a dauko sultan,

Bai bata amsa ba sai jan hannunta da ya yi suka nufi wajen jirgi inda ha baki bude aka raka su da kallo , da yawan mutanen da fadin ko dai Uban Agaisha ne? Wato Bak'A?

Nan ya tsaya jira har sarki ya fito suka kara gaisawa ya bashi takardar da Wardugu ya kawo dauke da wasikar da bai karanta ba,

Juyawa ya yi ya basu waje shi da matarsa su yi salama kafin suke dagawa,

Wajen yama tuni sun dawo garin niamey inda mai tuka shi ya ja su har gidan su,

Suna zuwa ya saka ta fice shi kuwa yana rike da Sultan dake dan wasansa na jarirai ,

Ajiyar zuciya ya sauke ya daga idannuwansa sama yana kallon sararin samaniya,

Takardar nan ya bude ya duba,

Number waya ne kawai tsararu masu bin juna sai sunnan da ya zirawa ido da mamakin gannin sunnan , shin sunna ne ya zo daya haka ko kuwa shi din ne?

Wato jan gwarzon nan, yaro mai hazaka, yaron da yake ji fa shi dan aiki na yawan hada su, yaron da idan yana kallon abubuwan da ya yi a duniya har wani tsam yake ji da jin wani yannayi na shauki da jinjina masa da gannin girmansa tamkar wani datijo, yaro karami mai watsa taron yan daba, wato *WARDUGU BATUBE DAN MARAHUT*

MA.ASALAM

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

https://www.facebook.com/Idan-rana-ta-fito-writers-association-114558343535568/?referrer=whatsapp

*☀IDAN RANA TA FITO WRITER'S ASSO🌤*

---

*Fad'akar da al'umma tare da nishad'antar da masoya shine fatanmu*😘🤝😘

Na
*SAJIDA*

7️⃣1️⃣

*KUTKALE* (prison)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan Niger in sha Allah,
........kar ku bari a baku labari...............

Wannan karron ma bata iya bashi amsa ba, ina ba zata iya budar bakinta ba, wani irin nauyi bakinta ya yi mata, sannan wani haushi take ji, *SO?* yo ita ba Mu.azam ba, ko waninsa bata tunanin zata kuma aminta ta so dan gudun idan ya wulakanta ta ta afka damuwa, dan haka sai ta dan motsa hannunta da ta fara jin zafin irin rikon da ya yi masa sannan ta bude idannuwanta a hankali ta dan janye goshinta daga wajen hancinsa sannan ta dago da dubanta a nitse ta sauke saman fuskarsa,

Kallon kasan ido yake yiwa du wani motsinta, hakan ya sa ya dan sasauta kusancin da ya saka a tsakanin su kafin yake bude idannuwansa gaba daya ya zuba cikin nata da kallon da ta tsare shi da shi,

Da sauri ta sada nata idon, domin idon Wardugu ya kada yay jajir, tsoro ne ya shiga dirar mata duda irin magangannun da ta fadawa kanta na ba zata kuma bari tana irin tsoron nan ko a

gaban waye ba,

A hankali ta dan ja baya ta zauna saman bed din , ta sada kanta kasa,
Wani irin abu take ji, wata faduwar gaba da take ji da wani sanyi sanyi, sai uwa uba wani irin dadi da take ji na kulawa da damuwarta da Wardugu ya yi a daidai wannan lokacin,

Bayansa ta dago ta tsurawa ido , dogon namiji, namiji ingarma,
Hannunsa da ya dafe goshinsa ta kalla , wato damatsunan hannun , da sauri ta sada kanta domin sai da gabanta ya fadi, a zuciyarta take ayana shi wannan wani irin jiki ne da shi haka?

Wardugu kam kokarin saita kansa yake, gabba daya ransa ne yake ji a jagule, hankalinsa du a tashe dalilin kukan nan, shi kukan yake son sani na menene? Kuka? Ta zubar da hawayenta haka kawai? Bata san girman darajar hawaten ba? Sai ya waka ne? Ya ilahi,
Juyowa ya yi yana dubanta kafin yake daga kafarsa a hankali ya dangana shima da bakin bed din,

A dan tsorace ta dago dan gannin ya zauna kuma, kar ta ja ya daketa a banza kafin a amsheta wannan ai har ya sumar da ita, haba dole su suma idan yana dukansu yo wannan hannu haka?

Bana son yawan magana da tambayar mutun yana kyaleni. Wardugu ya fada hankali kwonce.

Dagowa ta yi inda bakinta ya shiga dan rawa rawa kafin ta ce" ina cike da tunani ne....

Wardugu ya tsura mata ido yana mai jin zuciyarsa na dokawa, a hankali ya ce"  *Tunaninsa?*

Agaishat ta sauke ajiyar zuciya ta yatsina fuskarta , tunananinsa? Kanta ta girgiza ta ce" aa, ina yawan tunanin a yan kwanakin da na yi da shi, menene girman laifin da nayi masa da har ya kai shi mayar da ni karamar bazawara? Wani kure ne wannan na tafka masa da ya saka shi ahiga jikina sannan ya sake ni?

Da sauri Wardugu ya dago da idannuwansa ya sauke kanta, *SHIGA JIKINA* kalma mai ma.ana biyu, innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, ji ya yi kansa ya fara juya masa, duda yana da wani tunanin da wuya ta yi irin furucin nan a gabansa, aman wani lamarin ya rinjaye shi,
Innalilahi kawai yake maimaitawa domin ya jima da daina jin me take fada da idannuwansa ruf a rufe suke,
Da kyar ya iya mikewa ya shiga dan takawa a hankali , bai ce da ita ufan ba ya bude kofar nata ya fice a dakin yana mai dan dafe kansa,

Maganarsa ya tsinta inda yake cewa" Ayya, a facebook ne na ga sanarwar auren Alhinayett, abinda ya sa muka zo kennan, dan girman Allah Ayya ki duba maganata , ki zauna ki nazarceta, zaki ga iya gaskiyata kennan, Ayya ba zan yi maki karya ba, ba zan iya wannan gangancin ba👏🏻

Bai iya tsayawa a falon ba ya zarce zai fita, nan ya taka wayarta dake yade hakan ya saka ya duka ya dauka idannuwansa na kara rikidewa da tsabar masifa a cikinsu,

Da kallon tsoro, da kuma mamaki Ayya ta raka shi, kafin take juyowa da sauri wajen Mu.azam tana mai tarababin abinda ya fada kan Wardugu, ya salam! Shi ne abinda ta iya furtawa, sai kuma abubuwa suka shiga dawo mata daki daki,
Tana kallo Mu.azam ya mike ya bi bayan Wardugu, tana son tsayar da shi aman tunanin lamarin ya saka harshenta yin nauyi,

Da sauri ya karasa inda yake tsaye ya mika hannu ya taba kafadarsa,

Da sauri Wardugu ya juyo jin an taba shi,
Wani irin kakausan kallo ya jefawa Mu.azam , kallo mai nunin zan iya kasaraka, kafin ya furzar da wata iska ya maida dubansa wajen yarensa da suke tare hakan ya saka suka matsa suka basu wuri domin sun biyo Mu.azam ne kar ya karasa wajen ogansu

Kansa ya dafe , muryarsa a dan dage sannan cike da tashin hankali ya ce" dan me sai ita? Me yasa zaka ringa kokarin sakata kuka? Ka san ya na jure wanda ta yi ta yi min a lokacin da ka wulakanta ta? Ya zaka biyo mini ita nan ka kara sakata kuka?

*Ka CUCE NI*, me yasa Mu.azam? Me ya sa? Me na yi maka ka huce a kanta? Ya aka yi ka min haka? *Ban cancanci haka ba*, wayo wayo wayo Allahna.......! WARDUGU ya karashe yana mai dukan hanayensa a kansa da karfinsa,

Mu.azam ya dan ja baya, ransa bace da yannayin nan ya ce" danme ba zaka fuskanci lamarin ba? *Agaishat* *KADARA* ce! Nauyin baki, tsoro! Zai saka ka yin aikin dana sani, domin idan ni na kawar da kai ga tarin ni.imarta wani ba zai iya ba!

Wardugu ya harzuka ya cakumi wuyan rigarsa cikin karaji ya ce" ni zaka fadawa maganar banza maganar ni.imarta? Ni kake nufi ina tsoron mace ko me? Na taba fada maka wata magana a kanta ne?

Mu.azam da ya rike hannunsa da kyar yana so ya sakar masa wuya aman ya kasa suka ji muryar Ayya tana tafa hannu,

Hankalinta tashe ta karaso wajen su ta saka hannunta bibiyu ta kama jan hannun wardugu da iya karfinta,
Da kyar ya cika hannun kafin rai bace ta nuna masa hanyar fita ta ce" jeka gidanka! Tafi ka bani waje!

Rigar kakinsa ya ja ya cire baki daya ya yi masa sauran ta cikin kawai , ya juya ya nufi wajen motocin dake parke du sun yi cirko cirko suna sauraron fadan cike da taoron su shiga abin ya juye kansu,

Zuwansa ya saka aka bude masa ya shige suka tayar suka dauki hanya,

Kansa kawai ya jinginar ya lumshe idannuwansa kafin ya shiga hasasota a idannuwansa, ya Rab shi ne abinda ya iya furtawa ya kule bakinsa yana saurare har suka karasa gidansa ,

Ficewa ya yi ba tare da yace da su su ci kansu ba ya shige part dinsa ,

Walyn ce kwonce saman doguwar kujerar dakin daya kwalin kwal wace aka canza kayan dakin da kallolin aka saka masu ruwan zeba da dan ratsin fali aka saka kujerar zoguwa ta yi kwana ita daya mai wani irin zubi irin kujerun gidan sarakai, gannin idoma zai nuna maka da an kashe kudi a kanta, domin da ka kaleta zaka ga tamkar tana gayatarka ne zama samanta

Ido ya tsura mata ta saamu baci abinta, hankalinta kwonce abinta, ta sha yar karamar rigarta ta baci baka mai shara shara ta daure gashin kanta waje guda ta yi shar da ita ,
Da ita ya yi tafia ta wajen sati biyu,

Zagaye kujerar ya yi ya nufi dakinsa na baci yana faman neman bayi ya watsa ruwa mai sanyi ko zai ji zuciyarsa ta rage nauyi,

Bayan ya fito a wanka wayarsa ya tarar tana ringin,
Wajenta ya nufa ya dauka ya amsa kiran Alhinayett ce, sauraronta ya yi ta gama maganar kafin yace" kin ga ki raba ni Alhinayett, idan ni ina uban gidansa a wajen aiki ke uban gidanki ne a rayuwar aure, kar ki yarda ki ringa fada min laifinsa domin idan ina yawan yi masa magana tsanarki zai yi, ke wai ke din ba mace bane ba? Dole sai kin masa katsalandan  a abubuwan da ya tsara maku na rayuwa? Haka kawai yara kananu kuna saka mutane yawan magana da tashin hankali? Ohk yanzu da kika kirani kika fada mani so kike in kiraye shi in tirsasa masa saka turkudi a ranar da za.a yi masa murnar aurensa na sojoji ni babansa ko? Kawai dan kina buzuwa shikenan zaki sako shi a gaba dan wulakanci ranar  sojoji ki saka shi ya nada rawani kamar sarkin wani gari ko wani tsohon baruma? Yaki ba zai saka ba, nace ba zai saka ba!

Ya karashe da dan karaji,

Alhinayett da ta rafka tagumi tana tarababi da fadin ikon Allah wa ya tabo shi a ranta, ta zaro ido ta ce" Toh, ikon Allah

Wardugu ya ce" ni ne toh din ko? Ni ne toh din?

Ai kuwa kitt ta kashe kiran tana zazaro ido ta kai dubanta wajen matar abansu ta saki wani murmushi mai kama da ba.a dace ba,

Haka ya bi wayar da kallo kafin ya yi kwafa ya ajiye wayar

Har zai karasa kusan bed ya kai dubansa kan wayarta samsung da ta farfashe,

Juyowa ya yi ransa a jagule ya jujuya wayar,
Abin cire sim ya dauka a gaban sif dinsa ya ciro sim din wayar kwaya daya na airtel ya bude wayarsa iPhone 11 ya saka layin a ciki ya kunna wayar ya ajiye nan kafin ya zarce wajen bed din ya kwonta ya lumshe idannuwansa,
Kansa yake ji na sara masa sosai, dan haka ya yi adu.ar baci da fatan Allah ya sa ya samu bacin ya lumshe idannuwansa bayan ya kashe fitilar dakin

Ayya kam sosai abin ya daketa, ta yi mamaki, sannan ta tausaya masa, anya kuwa? Anya ta taba gannin abinda ya yiwa irin wannan son da idannuwansa ke rufewa idan tana waje ? Jikinsa fuskarsa, da act dinsa baki daya ke nuna kariya ga abin? Ita kam ta shiga wani yannayi, ta yaya? Yaushema ya yi aure?
Gannin damuwa na neman hadasa mata ciwon kai ya saka bayan su Mu.azam sun tafi hotel domin wannan karon a hotel suka sauka ta haye sama wajen Agaishat, nan ta tarar da ita ta yi baci hannunta dafe da goshinta,

A hankali ta zauna gefenta ta sauke mata hannun dan kar ya sage sannan ta tofa mata adu.o.in tsari ta ja mata rigarta ta rufe mata inda ya bude a jikinta ta mike ta tafi ta ja mata kofa tana tausaya mata , ko me ya dawo da ita daga wajen sabgar auren?

Tanaa shiga dakinta ba kwonciya ta yi ba, alwallah ta daura ta raba dare saman salaya tna mai neman zabin Allah da kawar da du wata fitina............

Wannan kennan

Ranar daurin Aure

Tun karfe biyar Ayya ta tayar da Agaishat ta barta ta kimtsa inda itama ta koma dakinta ta karasa shiryawa,

Wanka ne ta darza sosai domin bakonta ya zo mata tsakiyar dare,

Tana fitowa ta saka auduga da pant, sannan ta zauna a yar kujerar turaren wutarta ta yi turare mai sanyayan kamshi sosai har gashin kanta,

Tana gamawa ta mike ta mayar da komai wajensa sannan ta daura tawul a jikinta ta zauna gaban coiffeuse dinta,

Cikin nutsuwa take kimtsa kanta, hodar ruwa mai duhu duhu irin fatar jikinta ta dan shafa yar madaidaiciya wace ta kara haska mata fuskarta da wani sirri,
Nan ta samu ta kara bin gashin girarta ta gyara shi tsaf,
Jan baki ta dauka ta dan shafa kadan kalar pink domin koda Agaishat nada duhun fata lebenta

kalar pink ne na kasan na saman ne mai duhu hakan ya saka na kasan kawl take sakawa jan bakin hakan sai ya bada kala.

Tana kokarin zirara kwali a idannuwanta ta ji dirar motoci,

A hankali ta mike ta leka ta windows,
Ya Allah, shi ne abinda ta iya furtawa ta saki labulen ta koma wajen gyaran kanta ,
Su Wardugu ne, motoci ne laye farare kar, du sun sha shada ruwan Baka, color din ya wani irin fito da shi, ya kafa hular da......

Tunaninta ne ya katse lokacin da Ayya ta turo dakin,

Hannunta dauke da wani Lafayar ta karaso ,
Ayya ta ce" tashi ki saka kayanki su Wardugu sun zo daukarmu

Mikewa ta yi ta karbi lafayar mai mahaukacin kyau da wani tsare tsare mai ruwan turkudin ta je ta ciro yar doguwar riga mai gajeran hannu fara kar a kayanta ta dawo ta saka rigar ba wani bars a ciki,

Ayya ta mike da Lafayar ta shiga nada mata cikin nutsuwa har ta gama tana dubanta,
Hancinta ta ja ta ce"ki karanta lahaula wala kuwata illa billah ki shafa a jikinki da li.ilafi, masha Allah kin yi kyau Yata,

Agaishat ta saki murmushin jin dadi ta ce" Ayana na gode😊,

Ayya kam binta take da kallo inda Agaishat ta juya ta dauki takalmi da yar jaka wace ta ado ce kawai domin ko wayar babu batama san inda ta yarda wayar ba,
Nan ta shafa humura da turaren feshe na hamata sosai ta shashafa sannan ta karasa kusan Ayya tana duban irin yanda Ayya ke kallonta

Fitar dakin ta kashe da Ac suka rankaya kasa ,
Tun daga sama gabanta ya buga, domin Walyn ce hakimce ta hade cikin shadar baka itama ta yi wani irin kyau tamkar sarauniyar mekka,
An zuba zinari an coge da dogon takalmi da jaka , tana danna watsetsiyar iPhone dinta tana sakin dan murmushi da alama chating take kuma yana birgeta,

Da sauri ta kawar da kanta daga dubanta domin ta dago ta watsa mata kallon da ta rasa na kyama ne ko na raini ne take mata a kulun idan sun hadu?,

A hankali ta dube shi kanta a kasa ta ce" ina kwana Ya Wardugu,

Amsawa ya yi da "Lafiya,
Kawai, aman kuma kyam kallonta yake, lafayar ta yi mata kyau da yawa, gashi dan jaraba

harda gayar yan daurin aure yake yawo maza masu farauta kuwa!

Fuskarsa ya gimtse ya mike ya fice gaba kafin du suke biyo bayansa,

Ja ya yi ya dan tsaya inda Walyn ta zarce wajen motar da suka shigo shi da ita, da dan mayafinta sai isa take bazawa ta shige motar ta hakimce abinta,
Ayya ce ta karaso kusa da shi, nan ya samu damar kara dubanta murya kasa kasa da yaren tubanci ya ce" yanzu Ayya fisabililahi a haka zata je wajen daurin auren? Gidan bikin da ya tara shegun masu jar fatan nan?

Ayya ta zaro ido tana dubansa kafin ta tafa hannayenta ta ce""""

Barka da safiya

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

7️⃣2️⃣

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga ALKALAMIN yar mutan niger *SAJIDA* in sha Allah,

.............kar ku bari a baku labari.........................

Ayya ta tafa hannayenta ta ce" ni ban ga aibun shigar yarinyata ba,!

Gaba ta yi taki tsayawa maganar ta yi tsayima inda Wardugu da mamaki ya dan rike habarsa yana girmama irin son da Ayya ke yiwa yarinyarnan , dan kuwa idan ba a kanta ba , bai ga abinda zai fada ba Ayya ta musa masa,
Kansa ya kada yana hangen inda aka bude masu, motar dake gaban tasa nan suka shige bayan su duka,

Ajiyar zuciya ya sauke sannan ya hanzarta ya tafi wajen tasa da Walyn ya shiga shima,

Tafia suke inda Walyn ta narke masa kan kudin jakarta sun mata kadan shi kuwa ba tsayawa zai yi bank ta ciri kudi ba,

Yana dubanta da kulawa ya ce" menene marar dadin da ya hada ki da Agaishat ne da bakya amsa salamarta?

Tsai ta yi da shagwabarta ta dan tsura masa ido kafin ta dan hade yannayin farin cikinta ta ce" Wacece haka?

Wardugu ya juyo da kansa saman fuskarta da kyau, wacece? Taf, shi ya ayanna a ransa kafin yake gimtse fuska dan kar ta yi kokarin kawo masa raini da safiyar nan,

Walyn ta hadiye tashin balagar fitsararta ta ce" to aman Heart ka ga ai kai kadai ta gaisar, bayan kuma ni na girmeta, kuma ni ta tarar a zaune ko? Haka take min yarinyar ban san me take jin kanta da shi ba idan ta ganni ba zata girmamani yanda ya dace ba sai dai a wani dake ta min magana, ni shi yasa bana shiga sabgarta ko daya !

Wardugu kam tunda ya kawar da kansa bai kara ce da ita komai ba, shiru ya yi inda ya kai dubansa kan Wayarsa da sim din Agaishat ke ciki,
Wannan number tun jiya take kira da tura messages, messages sakarkarun messages, messages masu ban haushi,
A hankali ya bude wanda ya shigo yanzu ya karanta kamar haka " haba targui, tau ashak din naki ne ya motsa tun jiya an ki a kula ni? Ni kam zan yi maza na kawo kudin gaisuwa gida a san da zamana ko za.a yi maganarmu, bafa na son wasa da zuciya Targui,

Murmushi ya saki wanda ba zaka gane manufarsa ba kafin yake ajiye wayar yana kallon sun

karaso sun parke ana jira daga gare shi,

Duban Walyn ya yi , da yatsarsa ya yi mata nuni da ta tsaya kar ta fita, sannan ya fita a kotar

Yana fita du suka nufo wajensa suka shiga kakare shi daga maroka da masu son su gaisa kai harma da masu harin rayuwarsa, su kam a shirye suke, tabas shadoji ne a jikinsu aman kasan rigarsu ba wanda bashida bindiga yar karama wace a koni lokaci suna iya cirota idan bukatar hakan ta tashi,

Tsayuwa ya yi ya kali gabas da yama, kudu da arewa, can ya yafito kanin Alhinayett dan saurayi sannan ya yi masu nuni da su barshi ya karaso,

Musabaha suka yi kafin ya ce" ina so a bude hanya a shiga da mahaifiyata,

Ai kuwa da sauri ya matsa dan zuwa ya bude hanyar sannan a bude kofar shiga da motar,

Wajen motar ya karasa wajen direba ya bude ya masa umarnin fita,
Yana fita shi kuwa ya msye gurbin direban sannan ya tayar da motar a hankali ya fitar da ita daga layin motocin ya shiga tukata cikin nutsuwa har cikin gidan su Alhinayett inda sojoji masu kaki dake wajen du suka kame masa wasu kuwa suka rufe motar dan bata tsaro har ya dangana da wajen da zasu fito sannan ya fita ya zagaya ya budewa Ayya gefen da take,
Jakar hannunta ya karba ya kamo hannunta na dama ya taimaka mata ta fito cikin nutsuwa sannan ya kai dubansa kan Agaishat dake ta son ta bude gefenta ya ki buduwa bata san sai da kys din hannunsa kowani bangare na motar ke iya buduwa ba,

Hannunsa ya mika mata fari kal fafada da shi inda ya dan leka dan ta gane nufinsa,

Hannun ta bi da kallo, kafin take dago nata dake rawa rawa a hankali ta dora saman nasa ta yunkura ta sako kafarta daya mai dauke da takalmi mai dan matsakaicin tsayi kafa ciki na fata aman an yi masa adon fari kar, zamo kafar da ta yi ya saka lafayar ta dan dage har kaurinta a waje,
Ita dai bata san ya aka yi ba, sai gani ta yi ya saki hannunta ya saka hannayensa biyu ya ja lafayar ta sauka ta rufe wajen da ya fito, sannan ya dago da fuskarsa suka hada ido cikin ido ,
Idannuwansa ya wani irin lumshewa a hankali, ya rage masu girma sosai , hakan ya sa samansu suka kumburo kamar mai jin baci kafin yake saka hannunsa ya ja rufar kan ta rufe gashin kanta da kyau domin kadan ya dan fito da siririn yan kunayenta masu tsayi da suka kara kawata kwaliyar,

Karasa fitar da ita daga motar ya yi ta hanyar kara kamo hannun nata,
Rawa rawa kafafuwanta ke yi, hakan ya sa ya bi cinyoyinta da kallo, dan kuwa lafayar dake jikinta bai hana cinyarta kadawa ba sakamakon rawar da kafafuwanta ke yi, dubansa ne ya kai kan yarensa, ya ga suraj kyam na kallonta, wani uban harara ya zabga masa wanda ya saka shi juyawa gaba dayansa lokaci guda,

Ayya ya ga bata wajen, wato ta shigewarta wajen matan , dan haka ya kara kusanta kusancin dake tsakaninsu ya rage murya ya ce" ki daina haka mana, ki daina rawa rawar nan, domin ba iya kafarki da cinyarki ke motsi ba😔,

Agaishat kam da ido take binsa tamkar ta ga sabuwar halita, inanta ke motsi? Ya Allah, da sauri ta kara jan mayafinta ta gyara rufar lafayarta kafin ta mika hannu ta dauki jakar Ayyarta da ya ajiye nan dan gyara mata lafaya ta hada da tata kanta na duban kasa ta shiga neman ta inda zata raba ta bar wajen domin gaba daya idannuwanta basa nuna mata hanyar bi , du ya cika wajen,

Tsayuwa ta yi gabansa hakan ya bata damar tsayuwa daidai kirjinsa domin ya fita tsayi, ajiyar zuciya ta sauke a lokacin da ta dago da fuskarta ta dube shi ido cikin ido, gabanta ne ya kara faduwa , wasu hawaye take ji suna kokarin zubo mata domin ji take sam jikinta tamkar ba laka, da kyar ta iya shagwabe fuskarta kamar koda yaushe idan zata yi magana ta ce" zan je wajen Alhinayett,

Wardugu ya yi murmushin da bai yi niya ba ya dan kauce ta raba gefensa ta shiga tafia mutanen na kadawa tamkar wace ke yi da gangan ,

Idannuwansa ya kara lunshewa sannan ya juya da kafarsa suka rankaya da jama.arsa suka koma waje,

A jikinsa yake jin Walyn na binsa da kallo, , niyarsa yana fitowa ya je itama ya sanyota, sai dai ya tarar wajen angwaye sun karaso an fara haramar daurin aure gashi kuma shi ke zama kusa da mahaifin Alhinayett din,

Hakan ya sa ya bada kys din motar ya bada umarnin a sanyota domin sosau waje ya dauki harama,

Captain Ashiru ne ya karasa wajen motar ya bude ya sanar mata abinda Wardugu ya ce,

Idannuwanta da sukai ja na bacin rai da tashin hankali kawai ta iya budewa ta watsa masa kafin ta mika hannunta ta ciro kys din motar ta fito ta shiga gidan gaba ta tayar da motar ta fita da ita ta yi tafiarta

Bata zame ko.ina ba sai gidan aminiyarta, tana shiga hankali tashe ta je ta zauna saman kujera,

Dubanta take tana tambayarta lafia?

Walyn ta ce" menene tsakaninsa da ita? Wacece ita?

..................gidan biki.............

Shagali kawai ake, biki irin na buzaye, guitar ake ta kadawa inda du suka hakimce suna dan shiga rawa da dadaya maza da mata ana cashewa cikin nutsuwa , sai ruwan kudin da ake zuba masa domin fitacen mawakin nan ne Bombino.,

Maza kuwa tunda aka gama daurin aure suka tatara suka daga sai compagni baba inda suka je suka wuni.suna gashin shanun da suka yanka sai dai udan lokacin sallah ya yi a tashi a gabatar ga masu yi , a ci gaba da gashi , wasu na buga coss, wasu na game din buil, wasu na zukar shishar su, abin dai ya kankama domin kowa da gayarsa ne, haka Mu.azam ya saje da su dan kuwa ba wani abinda Wardugu ke nuna masa na bacib rai a gaban mutane normal yake amsa shi idan hakan ta kama har yama ta yi suka watse kowa ya nufi gida dan a shirya daukan amarya,

An kai amarya gidanta, yan matan amarya sun sha adonsu ba.a kama hannun yaro, an sha shagali a tsare a tafiye irin ta sojoji, tsari irin na sojoji,

Daga nan aka kwashe yan matan amaryar kowace aka shiga maida su gida, Agaishat ta zo shiga motar gugun yan matan wani soja da kaki yace da ita General yace a mayar da ita gida,

Tsai ta yi da dan alamar tsoro tana dubansa dan bai nuna mata shaidar hakan ba, sai da mijin Alhinayett ya fito da waya a kunensa yana amsawa ya karaso inda suke tsaye ya ce" in sha Allah sire,

Yana kashewa ya dubeta ya fada mata General ya sa a mayar da ita gida,

Wajen motar ta karasa ta shiga ya jata suka dauki hanyar gidan Ayya ba um ba umum tsakaninsu dan tukinsa kawai yake duda tarin tambayar dake cin ransa,

Ranar diner............

*Chaina*

Garin da aka kawo Anna dan neman lafia tun daga lokacin da suka kaita asibiti docter ya tabatar masu da ta samu shanyewar barin jiki sanadiyar hawan jinninta da ya mugun tashi wanda take da shi da jimawa yanzu ya yi karfin da ya kaita haka, damuwa, faduwar gaba,

fargaba, tashin hankali, da rike damuwa a cikin rai suka taru sukai mata ruf daya suka kwontar da Anna,

Likitan da ya dubata, shi ne ainahin wanda suka yi karatu da shi, wanda suka hadu lokacin da ta kawo fatimata jinyar yoyon fitsari, amininta, cike da mamakin itace haka? Ina ta shiga ya yi masu maganar su fita da ita, domin akoy halin hakan alhamdulilah sannan tana da bukatar nesa da kasar ko zata kwontar da hankalinta ta karbi magani yanda ya dace.

Toh Alhamdulilah za.a ce domin dai yanzu wajen sati uku kennan tana daukan magani da massage, da kulawar famillynta dake zagaye da ita, tana yakar kanta dan gannin bata saka su a damuwa ba, tana raha duda kasan zuciyarta na cike da kawar Agaisharta,
Sai abinda ke bata haushi irin yanda *Aminullah* damun mutane da kira da nacin ya take!

Zan iya cewa du wani mai tsoro a kusa ba zai iya shiga wajen ba,
Domin kuwa a yau ranar sojoji sun fito sun nuna su din su ne,
Kaki suka saka mai ruwan tsanwa da fari, baki dayansu,
Kowa ya karbe shi da tsarin halitarsa,
Sai hulunansu , sai wukake farare kar masu lankwasa,

......laye suke su....

Wayo hannuna😕😕😕😕😕😕😕😕

Hey readers more comment plz🙄🙄🙄🙄

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

73

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA* in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

Laye suke tun daga bakin hall din har ciki suna jiran karasowar amarya da ango, inda mutane ke zauzaune gefe da gefe wato hagu da dama bisan kujerun karfe farare kar da aka dan daudaura masu wani dan kyale pink da fari a jikinsu sai yan table table a gabansu ,
Can gaba kuwa kujeru shida ne masu shige da kujerun falo na alfarma wa.inda aka tanada domin zaman ango da amarya da aminin ango da matarsa da kuma general da matarsa
Guitar kuwa sai tashi yake inda mutanen da suka riga suka zo suka nuna takardar gayatarsu aka barsu suka shiga suke dan rausaya daga zaune abinsu domin an hana kowa shiga rawa tukunnan

Kannen amarya da sukai anko da kawayensu cikin shadarsu bugagiya sai meko take kowace ka kala sai ka kara kala don sun hadu ba wani kwaramniya sun fito ba ta yarwa,

Haka akai motarsu hudu, sai motar amarya wace ke tare da Agaishat ,
Ta sha dinkinta da ta zaba, yau kam bata lulube gashin kanta ba daurin dan kwalin da akai mata daga gaba aka fitar da shi sosai sannan daga tsakiya daure shin da aka yi da dan karamin ribom sai aka fitar da shi gaba dayansa, hakan ya sa ya malalu a bayanta, ga rigar kanta yau mai wuyan Bateau ce wato irin wuyan nan na zamani mai tsayawa a kafada , sai yar siriryar sarka mai wani dan dutsi kwaya daya tal fari kar da yan kunayensa, sai farin takalmi da farar pos mai kyalkyali mai forme din heart, gashin idonta ta saka masa maskara hakan ya sa ya kara tsatsayawa ya kara yin duhu sosai, lebenta ta shafa masa jan baki ja mai dan haske kadan ba dayawa hakan ya kara fitar da kwaliyar tata dan daidai masha Allah wace ko a cikin duhu zaka

iya gannin hasken fuskarta komin karancin hasken waje kuwa,

Kusa take da amarya wace ta sha nadin Lafaya fara kar aka zuba mata sarkar gold dinta da awarwaraye sai takalmi mai dan tudu itama mai ruwa sarkar wato zeba zeba hannunta bata rike da komai dan zai zame mata kaya,
Su biyu ne kawai a cikin katuwar motar da irinta kwaya biyu ce , dayar basu san ko su waye a ciki ba, aman baki daya motocin bakake ne wuluk har madubansu baka gannin na ciki ko daga gaba inda direba daya rak ke jan su cikin ayarin motocin,

A lokacin da suka karaso nan yan matan suka shiga fitowa inda Kanwar Alhinayet ta kara jadada masu tsarin shigar, dan kuwa sai amarya da ango sun fara shiga gaba, sannan General da matarsa, sannan aminin ango da matarsa, sai su kawayen amarya kowace da dan bouquet dinta na flower dan karami sai ta layu da soja daya wa.inda suke cikin yan tafiar makusanta da ango ne sosai manyan mutane ne suma daga colonel sai captain su shida ne wato harda Agaishat nada daya su bi bayan Amaryar da angon a haka su ratsa ta tsakiyar sojojin dake tsaye suka hada kawunnan wukaken nan na hannayensu sukai masu runfa da su, gldaga can gefe kuwa da yan yara biyu yayan buzaye dake watsa wani kyalkyali kyalkyali ga du wanda ya zo shigewa,

Wayarta dake jakar Agaishat ce ta shiga kuka a hankali da kidan celine dion i love u,

Cirota Agaishat ta yi ta mika mata , nan ta daga ta kara a kunnenta tana hangen motar dake kama da tasu mutanen ciki basu fito ba aman ta hangi angon nata ya fito ya karasa wajen motar,

Kallon Agaishat ta yi dake son a bude mata ta je wajen su sajida ta riko hannunta kafin take amsa shi da ohk in sha Allah,

Tana kashewa ta dubi Agaishat ta ce" Agaishana, dan Allah kar ki layu da kowani namiji kin ji? Ki zo mu shiga tare da ke mu saka Colonel tsakiya (wato mijinta)

Agaishat ta zaro ido da mamaki ta ce" wani irin ku saka shi tsakiya ba wani tsari sai kace mai.mata biyu? Allah ya sawaka yo dan me ba zan layu fa wani ba sai kace matar wani?

Alhinayett ta zaro ido ta hada hannayenta ta ce" ki rufa mini asiri dan Allah kar ki yi haka, walahi idan kika yi ina tsoron wajen nan ya hargitse 👏🏻

Agaishat ta yi mata wani kallon mamaki, da tarin tambayar me take nufi? Sai fai kafin take aika mata da tambayar aka bude motar,
Colonel ne, cikin shigarsa ta kakin shima, ya hade ya gama haduwa, hannunsa ya mikowa Alhinayett nan ta saka nata ta sauko,

Idannuwan Agaishat ne suka sauka kansa, shine a cikin motar ashe, ta madubi take hangensu,

shi da matarsa, ta sha doguwar riga baka mai shegen kyau, ko dan ta san ita din fara ce take son saka bakin kaya? Sai dan gyale baki da ta dan yane kanta ta yi irin daurin larabawa da shi ya zagaye kyakyawar fuskarta, sai tanfatsetsiyar jaka baka mai adon fari fari wace ke cike da yayan banki domin yau ranar ta kara kankarowa kanta mutunci ne .

Kanta ta kauda cikin jin zuciyarta wani iri, a hankali ta kara kai dubanta wajensa, kaki ne jikinsa irin na kowa, sai hular kansa da ta dan banbanta, sai bakin takalmi dake walwalwal ko daga nesa ka hanga ka san zai yi kudi,
Fuskarsa a hade take yana duban yanda ake laya mutanen dan shiga wajen diner da yake fatan a yi a gama lafia,
Bai ga adonta ba, bai san a ya ta zo wajennan ba, yana fatan bata yi dinki irin na yan matannan ba , domin doguwar riga ce du suka yi sai dai an yi mata fant har saman kaubri, so yake ta fito a motar aman har yanzu shiru .... shi ne damuwar Wardugu!

Kallonta ta kawar daga dubansa ta mayar kan Alhinayett dake tsaye tana jiranta,

Murmushi ta yi ta saki kafarta ta fito a motar ta tsaya gabansu,

Innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, shi ne abinda Wardugu ya fada a file kafin ya kawar da kansa daga dubanta ya maida wajen gugun mazan wajen,
Ido hudu suka yi da Mu.azam dake tsaye tare da Khadija da kuma daya daga cikin Kanwar Alhinayet tanai masu magiyar su zo su bi layin masu shiga da amarya aman fir ya kiya kan shi da ba soja ba ya zai bi lafi ya bata masu tsari

Kawar da kansa wardugu ya yi ya maida inda suke tsaye, nan ya yi ido hudu da mijin Alhinayett dake masa magana da fuska aman bai gane me yake nufi ba,

A hankali ya maida dubansa wajenta, dinkin shadar doguwar rigar da akai mata da sket , an saba lesh da shada ne cikin juna, leshen kuwa mai manyan tiloli ne, sannan du inda aka saka shi mai yawa ake sakawa, ga tsagun da akai gefe da gefe har saman ciki duda sket din ya hau har saman cikin aman du yanda ta yi wani juyi sai rigar ta dage dan kuwa an rage mata nauyi sosai tana daguwa du yanda aka so ta dagun,

Rintse idannuwansa ya yi lokacin da ta juya tana dafe kanta da alama fafatawa suke kan maganar ba zata jera da wani gardi ba bisa umarninsa, juyawar da ta yi, kamar da gangan ta hargitsa bayin Allah dake biye da ita ba dare ba rana wa.inda Allah ya halitata da su dan ta ringa  zaman kawai (🤣), sai da sukai sama sukai kasa hakan ya saka shi jin kansa ya sara sakamakon tunanin ko ba shi kadai ya ga hakan ba?

Juyowa ta yi tana duban mijin Alhinsyett ta ce" dan me ni kadai za.a hana cikin mu duka? Wani abin na yi? Ni a maida ni wajen Ayyana dan kuwa ba zan zo dan taron ba ace ni ba zan shiga ba
Ta karashe tana yin takwaf takwaf da fuskarta tamkar zata fashe masu da kuka,

Alhinayett ta matso ta kama hannunta zata yi magana kennan sai ga Farid, cikin shigar shada gizner ta sha aiki simple ruwan sararin samaniya ya dan dora wani mayafi fari kar a kansa abin rawaninsa ne sai ya yi yafe da shi, dogon buzu fari, bashi da jiki ko kadan ,
Ya jima a wajen tun kafin motar amarya ta karaso yana ts nemanta,

Gaban Alhinayet ne ya fadi ta yi saurin kara damkar hannun Agaishat tana dan waiwayen Wardugu ta ga kyam a tsaye yake su kawai yake kallo,

Da dan karfi ta janyo Agaishat da ta ga Farid ta sakar masa dan murmushi tana kokarin gaisawa da shi Alhinayet ta janyota,

Alhinayett ta hade fuska sosai ta ce" ki rufa mana asiri, ki rufawa kanki asiri Agaishat,
Kar ki tabo abinda ya fi karfinmu,
Kina wasa da lamarin da ba zaki iya tara ba,
Kar ki kula kowani namiji a wajen nan, idan ba haka ba ina mai tabatar maki zaki janyo rigimar da zamu kwana muna tserere a wajen nan a yau!

Ido ta zaro da yannayin tsoron yanda Alhinayett ke magana, ga mijinta shima sai waige waige yake yannayinsa na nuna bashi da nutsuwa,

Bata kara tsurewa ba sai da ya matso ya ce" Alhi, idan ta ki amincewa mu juya gida mu duka a fasa dinern,

Agaishat ta ce" wai me ke faruwa? Meye aka yi?

Mijin Alhinayett ya dubeta da kyau ya dan karancin yannayin firgicin da ta shiga , dan haka ya ce" wajen ne da hatsari, shi yasa ake kare lafiarki domin ba.a san me dauke da hatsarin ba,

Ai kuwa nan da nan ta shiga kifta ido ta rike hannun Alhinayett ta shiga waiwaye, ganninsa ta yi kyam a tsaye, ba zata iya fadin yannayinsa ba domin dare ne koda kuwa wajen ya kawatu da hasken fitila dare dare ne,
A yanzu muradinta ta kasance kusa da Ya Wardugu, snce waje da hatsari? Dubanta ta maida wajen shigar, an layu su kawai ake jira,
Sai ta maida wajen Farid ta ga yana tsaye da wayarsa a hannunsa, ita yake kallo, hakan ya saka da hannunta ta masa nuni da ya biyo bayansu,

Juyawa suka yi suka je gaban layin inda Wardugu ya cira kafarsa da Walyn da hannunta ke cikin nasa ta gama wayar da take amsawa suka bi bayansu,
Da farko tsakiya suka saka mijin Alhinayett, daga baya ta bar wajen ta koma bayan su Alhinayett ya kasance su Wardugu da Alhinayett sun sakata tsakiya,

Yau Wardugunma bata iya gaisarwa ba, dan a dan rikice take , fama take su yi su shige, aman

ganninta kusa da shi sai ta ji ta samu nutsuwa, ko ba komai ta san idan wani abin ya nufota da yardar Allah zai tare mata, kai ba ita ba, du wanda ke wajen bashi da dar!

A hankali suke takawa, salon kidan ya canza, daga can gefe aka harba bindigar toka ta yi kara sannan aka saki kidan harbin bindiga wanda ya saka du jiki ya kwashi wani tsam,

Idannuwansa a kanta, du wani motsi nata , sannan hankalinsa du a tashe yake, sai dai a fuskarsa ba zaka taba fahimtar hakan ba domin ya hade fuskar tamau ba wani fara.a, hakama yaran nasa ba wani mai isashen sakewa dan kuwa kasancewa a wajen party ba zai hana ya ci ubanka ba idan ta kama!

Yanda tsarin yake sai amarya da angonta sun zauna kafin kowani namiji da ya jero da mace ya rakata har wajen zamanta gefen hagu sannan ya koma gefen dama domin rawar guitar, (sai wanda ya san yanda ake yi zai fahimata🤪🤪🤪🤪🤪),

Amarya da ango na zama suka fara juyawa dan kai yan matan wajen zamansu,

Dan tsai ta yi a lokacin da ta fahimci yanda wajen zaman yake, haka ta juya jiki sabule zata je wajen zaman yan matan ta zauna ita daya,
Bai fi taku biyu da ta yi ba ta ji hannunta cikin nasa, ba zata iya rasa sannin hannunsa bane domin ta gama karantar yanda hannunta ke zama daram cikin nasa,, ta yannayin da jikinta ke nuna mata du idan ya yi irin wannan lamari ya saka ko dubansa bata yi ba ta karantawa zuciyarya shi din ne, a hankali ya kara kusanta kusancinsa da ita ya shiga bin takunta ba tare da ya kaleta ko ya ce da ita ufan ba har suka sauka suka nufi wajen zama,

Suna karasawa ya tsaya wajen kujerar da kanwar Alhinayett ke zaune, wace take facing dinsa , Kallonta kawai ya yi da idannuwansa ta mike a wajen ta koma wata inda ya kali yannayin kujerar kafin da hannunsa na hagu ya yi mata nuni da ta zauna,

Cikin nutsuwa ta dago idannuwanta da sukai mata nauyi , nan ta ga ikon Allah ashe du yawancin hankalin mutanen wajen na kansu, tun daga kan sojojin har yan matan wajen, uwa uba Farid da ta gani zaune shima ya yi zuru yana kallonsu,

Da sauri ta zauna tana dan zaro idannuwanta inda ya dan yi tsai , kafin ya rage tsayinsa wajen kunnenta ya ce" Na haramta maki motsawa a nan har sai an tashi!

Du mai kallon su, zai yi tunanin maganar soyaya ake a wajen nan, zai yi tunanin an gama mutuwa a son juna ne, bai damu da kallon da ake binsa da shi ba, hasalima sai da ya dan kara tsayawa ya mike da kyau ya bi kowa da kallo hakan ya sa mutane suke kawar da dubansu daga kansa kafin yake nufar kujerarsa,

Walyn, Walyn, walyn, wani kakausan kallo take binsa da shi har ya gama du abinda yake ya dawo ya zauna a wajensa wato kusa da ita,

Bata dubi tarin mutanen wajen ba, bata yi la.akari da wajen ba bale ta ari kissa irin tamu ta mata ba, yana zama ta shiga magana kamar haka" Wardugu, wannan wani irin mulakanci ne? Meye hadinka da kaskantaciyar yarinyar da muka dauko daga kasurgumin jeji dan cireta daga kangin talauci? Meye daraja a bakar mace har da zaka dauki hannunka mai daraja ka rike nata? Wardugu menene tsakaninka da tsohuwar bazawarar da amininka ya aura ya saki dan ba zai iya zama da ita ba? Wardugu wacece ita a wajenka? Wardugu!

Ta karashe tana mai dan daga murya da wawatsa hannayenta wanda duka na kusa da su na jin abubuwan da take fada da irin dibar albarkar da take tafkawa inda na nesa da su ke hangen Walyn na yuwa Wardugu fada , domin kuwa geste dinta kamar uwa na yiwa yaronta fada ce, irin zazafan fadan nan ma kuwa,

Dubansa ya dago ya dora saman kanta, hauka? Shirme? Aa Raini! Kai tsaye, ido cikin ido, ba wani gargadar murya, ba wani kawar da fuska, ko tausasa harshe Wardugu ya ce" kina son ki san ko wacece ita? Ita din *ORRONUR* dina ce.......

Dankari,
Kaka kara kaka
Ku samo ma.anar ORRonur sai na baku wani page😕

Walyn? Walyn! Wardugu!
Agaishat

More comment bilahi🙄🙄🙄🙄🙄

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

73

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA*  in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

Laye suke tun daga bakin hall din har ciki suna jiran karasowar amarya da ango, inda mutane ke zauzaune gefe da gefe wato hagu da dama bisan kujerun karfe farare kar da aka dan daudaura masu wani dan kyale pink da fari a jikinsu sai yan table table a gabansu ,
Can gaba kuwa kujeru shida ne masu shige da kujerun falo na alfarma wa.inda aka tanada domin zaman ango da amarya da aminin ango da matarsa da kuma general da matarsa
Guitar kuwa sai tashi yake inda mutanen da suka riga suka zo suka nuna takardar gayatarsu aka barsu suka shiga suke dan rausaya daga zaune abinsu domin an hana kowa shiga rawa tukunnan

Kannen amarya da sukai anko da kawayensu cikin shadarsu bugagiya sai meko take kowace ka kala sai ka kara kala don sun hadu ba wani kwaramniya sun fito ba ta yarwa,

Haka akai motarsu hudu, sai motar amarya wace ke tare da Agaishat ,
Ta sha dinkinta da ta zaba, yau kam bata lulube gashin kanta ba daurin dan kwalin da akai mata daga gaba aka fitar da shi sosai sannan daga tsakiya daure shin da aka yi da dan karamin ribom sai aka fitar da shi gaba dayansa, hakan ya sa ya malalu a bayanta, ga rigar kanta yau mai wuyan Bateau ce wato irin wuyan nan na zamani mai tsayawa a kafada , sai yar siriryar sarka mai wani dan dutsi kwaya daya tal fari kar da yan kunayensa, sai farin takalmi da farar pos mai kyalkyali mai forme din heart, gashin idonta ta saka masa maskara hakan ya sa ya kara tsatsayawa ya kara yin duhu sosai, lebenta ta shafa masa jan baki ja mai dan haske kadan ba dayawa hakan ya kara fitar da kwaliyar tata dan daidai masha Allah wace ko a cikin duhu zaka

iya gannin hasken fuskarta komin karancin hasken waje kuwa,

Kusa take da amarya wace ta sha nadin Lafaya fara kar aka zuba mata sarkar gold dinta da awarwaraye sai takalmi mai dan tudu itama mai ruwa sarkar wato zeba zeba hannunta bata rike da komai dan zai zame mata kaya,
Su biyu ne kawai a cikin katuwar motar da irinta kwaya biyu ce , dayar basu san ko su waye a ciki ba, aman baki daya motocin bakake ne wuluk har madubansu baka gannin na ciki ko daga gaba inda direba daya rak ke jan su cikin ayarin motocin,

A lokacin da suka karaso nan yan matan suka shiga fitowa inda Kanwar Alhinayet ta kara jadada masu tsarin shigar, dan kuwa sai amarya da ango sun fara shiga gaba, sannan General da matarsa, sannan aminin ango da matarsa, sai su kawayen amarya kowace da dan bouquet dinta na flower dan karami sai ta layu da soja daya wa.inda suke cikin yan tafiar makusanta da ango ne sosai manyan mutane ne suma daga colonel sai captain su shida ne wato harda Agaishat nada daya su bi bayan Amaryar da angon a haka su ratsa ta tsakiyar sojojin dake tsaye suka hada kawunnan wukaken nan na hannayensu sukai masu runfa da su, gldaga can gefe kuwa da yan yara biyu yayan buzaye dake watsa wani kyalkyali kyalkyali ga du wanda ya zo shigewa,

Wayarta dake jakar Agaishat ce ta shiga kuka a hankali da kidan celine dion i love u,

Cirota Agaishat ta yi ta mika mata , nan ta daga ta kara a kunnenta tana hangen motar dake kama da tasu mutanen ciki basu fito ba aman ta hangi angon nata ya fito ya karasa wajen motar,

Kallon Agaishat ta yi dake son a bude mata ta je wajen su sajida ta riko hannunta kafin take amsa shi da ohk in sha Allah,

Tana kashewa ta dubi Agaishat ta ce" Agaishana, dan Allah kar ki layu da kowani namiji kin ji? Ki zo mu shiga tare da ke mu saka Colonel tsakiya (wato mijinta)

Agaishat ta zaro ido da mamaki ta ce" wani irin ku saka shi tsakiya ba wani tsari sai kace mai.mata biyu? Allah ya sawaka yo dan me ba zan layu fa wani ba sai kace matar wani?

Alhinayett ta zaro ido ta hada hannayenta ta ce" ki rufa mini asiri dan Allah kar ki yi haka, walahi idan kika yi ina tsoron wajen nan ya hargitse 👏🏻

Agaishat ta yi mata wani kallon mamaki, da tarin tambayar me take nufi? Sai fai kafin take aika mata da tambayar aka bude motar,
Colonel ne, cikin shigarsa ta kakin shima, ya hade ya gama haduwa, hannunsa ya mikowa Alhinayett nan ta saka nata ta sauko,

Idannuwan Agaishat ne suka sauka kansa, shine a cikin motar ashe, ta madubi take hangensu,

shi da matarsa, ta sha doguwar riga baka mai shegen kyau, ko dan ta san ita din fara ce take son saka bakin kaya? Sai dan gyale baki da ta dan yane kanta ta yi irin daurin larabawa da shi ya zagaye kyakyawar fuskarta, sai tanfatsetsiyar jaka baka mai adon fari fari wace ke cike da yayan banki domin yau ranar ta kara kankarowa kanta mutunci ne .

Kanta ta kauda cikin jin zuciyarta wani iri, a hankali ta kara kai dubanta wajensa, kaki ne jikinsa irin na kowa, sai hular kansa da ta dan banbanta, sai bakin takalmi dake walwalwal ko daga nesa ka hanga ka san zai yi kudi,
Fuskarsa a hade take yana duban yanda ake laya mutanen dan shiga wajen diner da yake fatan a yi a gama lafia,
Bai ga adonta ba, bai san a ya ta zo wajennan ba, yana fatan bata yi dinki irin na yan matannan ba , domin doguwar riga ce du suka yi sai dai an yi mata fant har saman kaubri, so yake ta fito a motar aman har yanzu shiru .... shi ne damuwar Wardugu!

Kallonta ta kawar daga dubansa ta mayar kan Alhinayett dake tsaye tana jiranta,

Murmushi ta yi ta saki kafarta ta fito a motar ta tsaya gabansu,

Innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, shi ne abinda Wardugu ya fada a file kafin ya kawar da kansa daga dubanta ya maida wajen gugun mazan wajen,
Ido hudu suka yi da Mu.azam dake tsaye tare da Khadija da kuma daya daga cikin Kanwar Alhinayet tanai masu magiyar su zo su bi layin masu shiga da amarya aman fir ya kiya kan shi da ba soja ba ya zai bi lafi ya bata masu tsari

Kawar da kansa wardugu ya yi ya maida inda suke tsaye, nan ya yi ido hudu da mijin Alhinayett dake masa magana da fuska aman bai gane me yake nufi ba,

A hankali ya maida dubansa wajenta, dinkin shadar doguwar rigar da akai mata da sket , an saba lesh da shada ne cikin juna, leshen kuwa mai manyan tiloli ne, sannan du inda aka saka shi mai yawa ake sakawa, ga tsagun da akai gefe da gefe har saman ciki duda sket din ya hau har saman cikin aman du yanda ta yi wani juyi sai rigar ta dage dan kuwa an rage mata nauyi sosai tana daguwa du yanda aka so ta dagun,

Rintse idannuwansa ya yi lokacin da ta juya tana dafe kanta da alama fafatawa suke kan maganar ba zata jera da wani gardi ba bisa umarninsa, juyawar da ta yi, kamar da gangan ta hargitsa bayin Allah dake biye da ita ba dare ba rana wa.inda Allah ya halitata da su dan ta ringa  zaman kawai (🤣), sai da sukai sama sukai kasa hakan ya saka shi jin kansa ya sara sakamakon tunanin ko ba shi kadai ya ga hakan ba?

Juyowa ta yi tana duban mijin Alhinsyett ta ce" dan me ni kadai za.a hana cikin mu duka? Wani abin na yi? Ni a maida ni wajen Ayyana dan kuwa ba zan zo dan taron ba ace ni ba zan shiga ba
Ta karashe tana yin takwaf takwaf da fuskarta tamkar zata fashe masu da kuka,

Alhinayett ta matso ta kama hannunta zata yi magana kennan sai ga Farid, cikin shigar shada gizner ta sha aiki simple ruwan sararin samaniya ya dan dora wani mayafi fari kar a kansa abin rawaninsa ne sai ya yi yafe da shi, dogon buzu fari, bashi da jiki ko kadan ,
Ya jima a wajen tun kafin motar amarya ta karaso yana ts nemanta,

Gaban Alhinayet ne ya fadi ta yi saurin kara damkar hannun Agaishat tana dan waiwayen Wardugu ta ga kyam a tsaye yake su kawai yake kallo,

Da dan karfi ta janyo Agaishat da ta ga Farid ta sakar masa dan murmushi tana kokarin gaisawa da shi Alhinayet ta janyota,

Alhinayett ta hade fuska sosai ta ce" ki rufa mana asiri, ki rufawa kanki asiri Agaishat,
Kar ki tabo abinda ya fi karfinmu,
Kina wasa da lamarin da ba zaki iya tara ba,
Kar ki kula kowani namiji a wajen nan, idan ba haka ba ina mai tabatar maki zaki janyo rigimar da zamu kwana muna tserere a wajen nan a yau!

Ido ta zaro da yannayin tsoron yanda Alhinayett ke magana, ga mijinta shima sai waige waige yake yannayinsa na nuna bashi da nutsuwa,

Bata kara tsurewa ba sai da ya matso ya ce" Alhi, idan ta ki amincewa mu juya gida mu duka a fasa dinern,

Agaishat ta ce" wai me ke faruwa? Meye aka yi?

Mijin Alhinayett ya dubeta da kyau ya dan karancin yannayin firgicin da ta shiga , dan haka ya ce" wajen ne da hatsari, shi yasa ake kare lafiarki domin ba.a san me dauke da hatsarin ba,

Ai kuwa nan da nan ta shiga kifta ido ta rike hannun Alhinayett ta shiga waiwaye, ganninsa ta yi kyam a tsaye, ba zata iya fadin yannayinsa ba domin dare ne koda kuwa wajen ya kawatu da hasken fitila dare dare ne,
A yanzu muradinta ta kasance kusa da Ya Wardugu, snce waje da hatsari? Dubanta ta maida wajen shigar, an layu su kawai ake jira,
Sai ta maida wajen Farid ta ga yana tsaye da wayarsa a hannunsa, ita yake kallo, hakan ya saka da hannunta ta masa nuni da ya biyo bayansu,

Juyawa suka yi suka je gaban layin inda Wardugu ya cira kafarsa da Walyn da hannunta ke cikin nasa ta gama wayar da take amsawa suka bi bayansu,
Da farko tsakiya suka saka mijin Alhinayett, daga baya ta bar wajen ta koma bayan su Alhinayett ya kasance su Wardugu da Alhinayett sun sakata tsakiya,

Yau Wardugunma bata iya gaisarwa ba, dan a dan rikice take , fama take su yi su shige, aman

ganninta kusa da shi sai ta ji ta samu nutsuwa, ko ba komai ta san idan wani abin ya nufota da yardar Allah zai tare mata, kai ba ita ba, du wanda ke wajen bashi da dar!

A hankali suke takawa, salon kidan ya canza, daga can gefe aka harba bindigar toka ta yi kara sannan aka saki kidan harbin bindiga wanda ya saka du jiki ya kwashi wani tsam,

Idannuwansa a kanta, du wani motsi nata , sannan hankalinsa du a tashe yake, sai dai a fuskarsa ba zaka taba fahimtar hakan ba domin ya hade fuskar tamau ba wani fara.a, hakama yaran nasa ba wani mai isashen sakewa dan kuwa kasancewa a wajen party ba zai hana ya ci ubanka ba idan ta kama!

Yanda tsarin yake sai amarya da angonta sun zauna kafin kowani namiji da ya jero da mace ya rakata har wajen zamanta gefen hagu sannan ya koma gefen dama domin rawar guitar, (sai wanda ya san yanda ake yi zai fahimata🤪🤪🤪🤪🤪),

Amarya da ango na zama suka fara juyawa dan kai yan matan wajen zamansu,

Dan tsai ta yi a lokacin da ta fahimci yanda wajen zaman yake, haka ta juya jiki sabule zata je wajen zaman yan matan ta zauna ita daya,
Bai fi taku biyu da ta yi ba ta ji hannunta cikin nasa, ba zata iya rasa sannin hannunsa bane domin ta gama karantar yanda hannunta ke zama daram cikin nasa,, ta yannayin da jikinta ke nuna mata du idan ya yi irin wannan lamari ya saka ko dubansa bata yi ba ta karantawa zuciyarya shi din ne, a hankali ya kara kusanta kusancinsa da ita ya shiga bin takunta ba tare da ya kaleta ko ya ce da ita ufan ba har suka sauka suka nufi wajen zama,

Suna karasawa ya tsaya wajen kujerar da kanwar Alhinayett ke zaune, wace take facing dinsa , Kallonta kawai ya yi da idannuwansa ta mike a wajen ta koma wata inda ya kali yannayin kujerar kafin da hannunsa na hagu ya yi mata nuni da ta zauna,

Cikin nutsuwa ta dago idannuwanta da sukai mata nauyi , nan ta ga ikon Allah ashe du yawancin hankalin mutanen wajen na kansu, tun daga kan sojojin har yan matan wajen, uwa uba Farid da ta gani zaune shima ya yi zuru yana kallonsu,

Da sauri ta zauna tana dan zaro idannuwanta inda ya dan yi tsai , kafin ya rage tsayinsa wajen kunnenta ya ce" Na haramta maki motsawa a nan har sai an tashi!

Du mai kallon su, zai yi tunanin maganar soyaya ake a wajen nan, zai yi tunanin an gama mutuwa a son juna ne, bai damu da kallon da ake binsa da shi ba, hasalima sai da ya dan kara tsayawa ya mike da kyau ya bi kowa da kallo hakan ya sa mutane suke kawar da dubansu daga kansa kafin yake nufar kujerarsa,

Walyn, Walyn, walyn, wani kakausan kallo take binsa da shi har ya gama du abinda yake ya dawo ya zauna a wajensa wato kusa da ita,

Bata dubi tarin mutanen wajen ba, bata yi la.akari da wajen ba bale ta ari kissa irin tamu ta mata ba, yana zama ta shiga magana kamar haka" Wardugu, wannan wani irin mulakanci ne? Meye hadinka da kaskantaciyar yarinyar da muka dauko daga kasurgumin jeji dan cireta daga kangin talauci? Meye daraja a bakar mace har da zaka dauki hannunka mai daraja ka rike nata? Wardugu menene tsakaninka da tsohuwar bazawarar da amininka ya aura ya saki dan ba zai iya zama da ita ba? Wardugu wacece ita a wajenka? Wardugu!

Ta karashe tana mai dan daga murya da wawatsa hannayenta wanda duka na kusa da su na jin abubuwan da take fada da irin dibar albarkar da take tafkawa inda na nesa da su ke hangen Walyn na yuwa Wardugu fada , domin kuwa geste dinta kamar uwa na yiwa yaronta fada ce, irin zazafan fadan nan ma kuwa,

Dubansa ya dago ya dora saman kanta, hauka? Shirme? Aa Raini! Kai tsaye, ido cikin ido, ba wani gargadar murya, ba wani kawar da fuska, ko tausasa harshe Wardugu ya ce" kina son ki san ko wacece ita? Ita din *ORRONUR* dina ce.......

Dankari,
Kaka kara kaka
Ku samo ma.anar ORRonur sai na baku wani page😕

Walyn? Walyn! Wardugu!
Agaishat

More comment bilahi🙄🙄🙄🙄🙄

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

74

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA*  in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

Wannan kalma ta daki Walyn a lokacin da bata shirya ba,

Zurbat ta mike daga zaunen da take inda wayar dake saman cinyarta da jakarta suka fadi saman fari kal din careau din wajen,
A lokaci daya gaba daya jikinta ya dauki rawa, ba inda baya rawa a jikinta,
Bakinra ta kara budewa da bila adadin dan yin magana sai dai kawai hakoranta suke hadedewa bakin na rawa lebunanta na marmarmar,

Juyawa ta yi da karfi wajen da Agaishat take,
Kafarta ta daga da niyar karasawa wajen Agaishat din idan ya so idan ta isa sai ta aikata mata abinda ya samu koma menene,
Sai dai me, idannuwanta ne suka rufe ruf,
Bata gani sannan a hankali lumfashinta ya yi sama ya dauke dif, inda ta aniya zubewa a wajen,

Du hankalin mutanen wajen ya yo kanta inda du aka mimike hankali tashe, domin bata karasa kasa ba ya tarota jikinsa ta sume a jikinsa,

Tsai ya yi ya kurawa fuskarta ido, a sumen abin sha.awa da ita, ta yi fayau ta nuna fuskar innoscent,

Dan mayafin da ta yiwa wayo ne yake faman sabulewa inda Alhinayett ke tsugune inda suke hankalinta tashe ta shiga magana kamar haka" War, mu je asibiti, ta suma fa, bata motsi, Wardugu mu kaita asibiti,

Dubansa ya dago a hankali inda take ,
Murmushi ya sakar mata yana dubanta , muryarsa ya rage sosai domin ana faman zagaye su du kuwa da irin tsaron da sojawan ke faman bayarwa da tsare du wani wanda zai yi gigin karasawa inda suke sai wa.inda aka tabatar da kusancinsa da wardugu mai girma ne ake bari ya karasa inda suke, hakan bai hana mutanen dake wajen zaman amaren karasawa da sauri suna tambayar wai lafia? A hanzarta kaita asibiti mana?

Wardugu ya ce da Alhinayett, " Alhi, bafa wani abu na yi mata ba, ke ai kin san ina hakuri da ita ko? Gaskiya ce kawai na fada mata fa,

Alhinayett ta ce" menene ma.anar Orronur?

Wardugu ya lunshe idannuwansa ya kai dubansa inda Agaishat ke tsaye tana so a barta ta karasa wajensu aman an hanata dan gurin faman cakulewa yake sai kacaniya ke tashi kowa na faman a barshi ya karasa ya ga kwakwaf,

Ya dawo da dubansa wajen Alhinayett ya lumshe idannuwansa yana dan shafa gaban goshin Walyn dake kan kirjinsa sume kafin ya ce" *ORRONUR* na nufin *RAINA*

idannuwa Alhinayett ta zaro cike da tsoro ta kai dubanta da sauri kan Walyn, Balaki! Shi ne kalmar da ta fito daga bakinta, ai kuwa da sauri ta mike tana fadawa mijinta a saki hanya a kai Walyn asibiti, domin tana adu.ar Allah ya sa lamarin ya tsaya a iya sumar kawai, kar ta samu mutuwar barin jiki na bugawar zuciya,
A yanda Walyn ta baiwa kishi madaukakiyar daraja a rayuwarta, a yanda walyn ta dauki lamarin soyayar mijinta a zuciyarya da son kai mai girman gaske, a yanda Walyn ke taka tafiarta na rayuwa da izgili da fariwa da neman magana? A yanzu, wardugu , ya ce kau bani gu, Wardugu a yau zata iya kiransa da Masifafe, ohk so yayi ta daga bali, ta jawa kanta ya daki banza, tabas suma ta zama wajibi a rayuwar Walyn a yau, domin da wannan lamari bai razanata ta suma ba, zata tafka haukan da Wardugu zai sumar da ita, ya salam, ya salam, haka kai tsaye? Tabas tana hangen Wardugu zai zama jarumi wajen fadawa Walyn wannan lamarin a duk lokacin ta sani ya bayana, aman bata taba tunanin kai tsaye haka ba? Mata? Me ke yawo da kusoshin kanmu ne? Gashi dai, da darajarta , da girmanta, da dan shakunta da yake ji ta bale ta saka lokaci daya ya janye du wani laka na jikinta! Ribar me ta ci? Ana kishi, kishi halal ne, kowace mace na kishin mijinta, aman kishima ai taku ne, 🤦‍♀️,

Da sauri aka bude wajen aka shigo da mota, du wannan tsare tsare haka mijin alhinayet ya take da mota har kusan matatakalar , aka bude motar ,

Mikewa Wardugu ya yi da ita a jikinsa ya samu ya sauka a hankali ya sakata cikin motar,

Bai shiga ba, ya dawo bayan ya cire rigarsa ta saman wato kaki din mai dogon hannu sai bakar body ta ciki ta bayana mai dan gaheran hannu sannan ta tantanke jikinsa baki daya, hakama ya sakata cikin wandonsa ya yi zanzaro da ita a ciki,
Hular kansa ma cirera ya yi, ya koma wajen da Alhinayett ke tsaye ya dubeta ya ce" ki zo mu je,

Da sauri ta juya dan dauko jakar Walyn da wayarta,  har ta bude ta saka cikin motar ta ji muryarsa ya ce" ita fa?

Ba sai ta tambaya ba , ta san wace yake nufi , dan haka ta karasa kusan Agaishat ta damko hannunta kawai ta janyota suka nufi motar inda shi ya shiga gaba su kuwa suka shiga baya suka zazauna,

Gudu yake da motar, baka jin komai sai kuryar Agaishat tana ta tamabayar abinda ya samu Walyn, me ke damunta? Me ya sameta ? Bata da lafia ne? Ko gurdewa ta yi? Alhinayett ki bani amsa mana? Dibi fa ta suma fa,

Uta dai Alhinayett ta yi wani zuru tana kallonta, to me zata ce da ita? Ita bata ma san abinda ke faruwa ba, bata taba kawowa ranta haka ba, hasashenta bai taba hasaso mata haka ba, ita yanzu fatanta a karasa lafia kar ta farka ta ganta kusa da ita ta kashe su a motar nan, kai rana tsoron zafin kishin Walyn, macen da ta salwantar da gudan jinninta dan kar ta haihu da wuri a fara yi mata irgen abinda ya rage a mata kishiya idan hakan ta kama? Ina ga yanzu hakan na kokarin kamawar? Taf

A haka suka karasa clinik, wato asibitin kudi,
Nan da nan aka gungura gadon mararsa lafia aka dora Walyn aka shiga da ita, inda du suka fito suke zazaune a harabar wajen mai cike da shukoki masu fulawa masu kyau sosai,
Mutane na kai kawo masu zaman jinya, sai likitoci, sai motar sojoji biyu fa ra biyo su suka dan rarabu suka zagaye asibitin kowane ka dube shi ba alamar ya san kalmar dariya ,

Agaishat dake zaune kusa da Alhinayett ta yi zaman yan makaranta , ta dafe kuncinta da hannunta na dama ta zubawa gazon din wajen ido tana kallo aman fal tunani ne cikin ranta da sumar da Walyn ta yi, har ga Allah hankalinta a tashe yake, me ya samu Walyn din?

Wayar Walyn ce ta dauki tsuwa , Alhinayett ta mike ta mikawa Wardugu tana kule da yanda mijinta ke binta da wani kallon da ba zata iya gane fasararsa ba, aman kallon na bata tsoro itafa tsoronsa take ji, domin a daren jiya ba abinda ya yi mata bacinsu suka sha sosai ko hannunta mai taba ba, amab a yau sai wani kallon gididiga yake binta da shi!

Mahaifiyarta ce ke kiranta, hakan ya sa ya daga ya fada mata suna likita da sunnan GAZOBI sannan ya kashe

Agaishat dake dan satar kallonsa tana mamakin yanda ya amsawa sarakuwarsa, wani a dakile

kuma kalmomin basu fi a kirga ba,
Taf, hakan na cikin hukunce hukuncen da zata gindayawa wanda zata aura, walahi au ya girmama iyayenta tamkar nasa au a hakura da auren koma waye, yo ita ina zata iya zama da irin halin wardugu? Namiji ne da ya fito mata na faman wawura kansu da kafarsu? Ina sam bata son namiji mai kyau da cika ko mai kudin da zai kasance ita kulun hankalinta a tashe yake, namiji ne da dan isar sa mace ko wacece baya duka mata? Du kuwa da irin son da yake mata? So dai ai bai kai wanda yake yiwa Walyn ba, aman ko ita sai ya dankari banza idan hakan ta kama? Anya wardugu na wasa da matarsa irin yanda annabi ya yi? Anya Wardugu nada lokacin sauraron matarsa? Kai ita zata so ta samu namiji irin wa.inda ba ruwansu, wa.inda zasu baka incinka su baka damarka su baka darajarka,

Ajiyar zuciya ta sauke a lokacin fa ta bude ido ta kale shi ta ga sun yi ido hudu, harare ya watso mata wanda ya bata mamaki da tsoro, me kuma na yi? Shi ne tambayar da ta yiwa kanta.

Dubanta ta maida wajen Alhinayet ta ce" Alhi, bani wayarki na yi kiran Ayyana dan Allah, na fada mata halin da ake ciki na kuma fada mata ta biyo min da hijab dina kin ga dan kwalin ya fadi fa,

Da sauri Alhinayett ta dubi kanta, Lah kanta ba dan kwali, gaba daya kyan gyaran gashin ya fito sosai ta yi wata yar caras da ita,

Ai kuwa wayar ta mika mata tana ayyana Wardugu sai ya hada daga ni da a aurena ne kika fito a haka da ke din ya ci ubanmu

Number Ayya dake kwakwaluwarta ta dora tana satar kallonsa, mamaki take wai kallon nan da ya same shi na meye? Sai ya tsurawa mutun ido tamkar yana kallon tv ko waya, kuma ba abinda ya dame shi dan kun yi ido hudu ya kawar da dubansa? Aa sai dai kai ka kawar, wannan ai musulunci ya hana irin kallon nan tsakani da Allah

Shi kuwa duban da yake mata, yana so ne lale lale ta iya yarensa na kallo, yana so idan ya dubeta ta gane me yake nufi da dubansa ba wai ya tsaya yana ta haikar baki ba, yana so ta gane wannan shigar batai masa ba, baya so, hankalinsa, ransa, nutsuwarsa duka yana nema ya rasa a lokacin da ta fito a haka, ku ji fa hankali kwonce yltana danna waya ta kara tana zubawa mamanta shagwaba ba ruwanta da wa zai kala ko me mutun zai kiyasta a kanta a ransa? Yana kallonta ta kashe wayar ta mikawa Alhinayet ta maida taguminta ,
Sai damun mutane take da tambayar me ya samu Walyn, ko meye damuwarta a ciki? Shi kadai ke fadansa a cikin ransa kafin ya yi kwafa yana tunanin idan ta kai shi bango bai san irin jijigar da zai mata ba,

Ba.a wani jima sosai ba mahaifiyar Walyn ta zo, tsakaninsu da Ayya kuwa bai fi minti biyar ba, sai gata itama an tukota a motarta
Kamar ko yaushe cikin kanshinta da lafayarta har kasa da san saukakun awarwarayenta hannunta dauke da leda kamfanin Butique wace ta sako hijab din yarta,

Salama ta yi masu kafin ta tambayi mai jiki?

Nan suka shaida mata docter ne ciki , yace ya daidaita numfashinta aman cikin ruwan da ya jona mata da na baci wanda zai saka ta farka a hankali,

Ayya ta yi fatan Allah sawake, ta tambayi daman bata da lafia ne?

Su kam basu da wannan amsar, hakan ya sa ta bude hijab din, maimakun ta bata ta saka sai ta budeshi da kyau ruwan shadar jikinta ne, ta juya Agaishat dake tsaye kusanta ta kama gashin kanta gaba dayansa ta hade shi ta yi masa dan tuntun madaidaici sannan ta zira mata hijab din mai hannu da wani dantel a jikinsa sannan zif ne da shi dan karami wajen wuya wanda mutun ke ja ya kama fuskarsa ,
Hijab din ya yi kata kyau das a jikinta sannan tsayinsa har kasa sosai,

Ajiyar zuciya ya sauke sannan ya kawar da dubansa daga wajensu,

Docter ne ya fito da dan sauri yana tambayar ina wardugu?

Daidai nan su Mu.azam suka karaso ,
Wardugu ya nufi wajen docter, Inda Ayya ta je wajen su Alhinayett ta ce" ku kuwa me kuke har yanzu a nan ? Ku zo maza ku tafi gida haba dare ya yi,

Alhinayett zata yi magana wata nurse ta fito da gudu ta ce" Docter tafa tsoge allurar ruwan kuma du wanda ya je kusanta doke shi take,

Da sauri du suka nufi wajen hankali tashe,

Wardugu ya saki wani murmushi yana kallon yanda suke rige rigen shiga dakin,
Kansa ya girgiza ya bi bayansu,

Mahaifiyarta ce ta karasa da sauri kusanta yanda take rusa kuka tana fadin" Walahi, sai na kashe su, daga shi har tsinaniyar bakar fatar nan! Da raina ba.a yi ba, ba za.a yi ba yarinyar da Wardugu zai kira da *ORRONUR* ba, ita ita Wardugu zai ciwa mutunci?

Daneta uwar ke faman yi karta mike, sannan ta tambayeta wai meye? Meye? Me aka yi?

Walyn ta daga jajayen idannuwanta ta sauke saman mahaifiyarta ta ce" a wajen partyn banzan nan da suka tsara ne ya rakata wajen zama bayan ni ya barni nan zaune ni da nake matarshi, shi ne na tambaye shi wacece ita? Wani matsayi ke gareta da har zai lakaba mata wannan sunnan? Yar gidan waye ita?

Shi ne yace da ni wai *RANSA CE!*

dif dakin ya yi Agaishat dake bayan Ayya tana dan lekowa idannuwansu suka hade da na Walyn,

Wani kukan kura ta yi ta ture mahaifiyarta ta taso da gudu da karfin balaki ta nufi wajen Ayya tana furta" Walahi sai na ga ubanda ya tsaya maki, ko wani irin boka ko malan ya ci.......shi! Ya dura ashar mai yaji😋, shegiya bakar fata mai bakar aniya, mijina ya fi karfin buzuwa banza jahila!

Kafin take isawa ta ganshi tsaye, tsaye tsakaninta da Ayya da kuma Agaishat, kikam ya tsaya ya tsura mata ido

Zagaye shi ta so yi ta karasa wajensu, sai dai ya riko hannunta ya yi mata turawa daya da ta saka ta je can ta fadi,

Daga kafarsa ya yi ya tunkareta da wani irin sauri da niyar kasara wata gaba ta jikinta
Sai dai muryar Ayya ce ta dawo da shi daga wannan niya tashi wace du mazan wajen suka yi gagawar tarar shi, rike shi sukai suna faman bashi baki kan kar ya yi, ko ba komai mahaifiyarta a wajen a zaune, idan ita ta saki baki tana abubuwa irin haka shi ya ci girma,

Wani irin huci yake saukewa inda ya bi umarnin Ayya da ta nuna masa hanyar fita,

Shi ya fara fita sannan suka mara masa baya inda ta fashe da kuka da wani ihu ihu tana munana mangangannun kan ba dole ya tafi ba, ita ga mabaukaciya ai dole a bar mata waje, daman ita ta san Ayya bata taba kaunarta ba, gashi ta kawo masa karuwa har gida ana cin amanarta, ita kuwa zata ga yanda za.a yi soyayar nan!

Mahaifiyarya ce ta daka mata wata gigitaciyar tsawa kafin ta ce" dan ubanki ta yaya kikai masa tambaya kan wacece itan??

Kwashe du magangannun rashin da.ar da ta yi masa ta fadawa mamanta, inda ta shiga bata karfin gwuiwar cewa" ya fada maki haka ne dan ya tunzura ki ke kuwa kika hau banza, ko ni kika yiwa rashin kunyar nan ai sai na baki haushi bale Wardugu, me zai yi da wannan mumunar halitar in ba shirmen kishi da ya rufe maki ido ba? Ya fada ne dan ki zubda haukan, kin kuwa zubda hankalinki ya kwonta! .....haka ta yi ta dorata kan yayi haka ne dan ya bata mata itama aman me zai yi da Agaishat?

Tunda suka kama hanyar gidan ayya kansa ke jingine jikin madubin motar yana sauraron ajiyar zuciyarta , domin ta tsorata da gannin kamar ita walyn ke farauta,

Shiru motar ba mai kwakwaran motsi har suka karasa gidan Ayya,

Shi ya fara fita ya nufi falon ayya, kafin ya shiga ya iya sabule takalman kafarsa sannan ya ciro rigar dake cikin zanzaron jikinsa ya yi tsaya yana mai jin kansa tamkar zai rabe gida biyu!

*BAKA KYAUTA MINI BA!*

Ayya ta fada a lokacin da suka shigo da Agaishat, tana kallo Agaishat ta nufi dakinta,

Kanta ta juyi wajensa , ya dafe kai yana jijiga kafarsa, balaki na cinsa, da wanda zasu yi kawai yake nema, ta ce" Baka kyauta min ba, ka san sarai halin matarka dan me zaka sako min yarinya cikin shirmen ku? Me ya hadaka da fadin wannan maganar a kan yarinyata a wajen matarka?

*DAN INA SON TA*

Maganar ta fito daga bakinsa da amo mai karfi karfi,

Da sauri ya juyo wajen Ayya ya taka har zuwa inda take zaune ya duka ya dora kansa saman cinyarta,

Zuciyarsa ce ke wani irin dokawa ya ce" *Ayya, Wayo Allahna Ayya zan mutu, Ayya mutuwa zan yi, Ayya zafi nake ci a nan*

🙁

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

7️⃣5️⃣

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA*  in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

*Walahi ma cherie, Madame dakoro ina jin nauyinki da kunyarki, kin kasance mai mugun alkhairi a gare ni, ki sani aminiya kuma yayata ko sako ne ki turo na wanda kike so a farantawa ta hanyar nvl da dukan abinda Allah ya hore min, in sha Allah ba zan baki kunya ba, na gode na gode*

Ya nuna daidai zuciyarsa still kansa na saman cinyarta,
Jinsa yake bashi da wani karfi, jinsa yake bashi da wata dabara, dan Allah kowama ya ji kuma ya shaida yana kaunar yarinyar Ayya,

Jikin Ayya ne ya mutu, a ranta tana fadin shikenan ya fada, eh lale, aman aurensa fa? Matarsa fa? Aurensu duka duka shekara nawa? Wannan tada ce al.ada ce ta iyaye da kakani, ba.a yiwa macen tubawa kishiya haka gatsal sai idan ta yi haihuwa uku zuwa hudu ko ta samu kwararun shekaru da mijinta a kafan bakwai abinda ya yi sama, daman a dangi a baki suke, an sako su a gaba, komai kanantar abu idan Wardugu ko ita suka yi zaka ji ya yi gagawar zagaya dangi a labe a yi da su aman a gabansu ba.a nunawa sai dai a yi ta masu fadanci, tana cikin rudani......sai dai kuma wannan lamari mai girma ne, ya kasa jurewa, ya kasa kawar da kai, abin na bashi wahalar da ya kasa hadiyewa sai da ya fada! To aman ba a nan gizo ke sakar ba, ita Agaishat din da bata san me yake ciki ba? Bai fada mata ba, bai nemi soyayarta karara ba, shi girma girma, shi bai san ta yaya gododo da shi zai tsaya gaban yarinya ya ce da ita yana sonta ba, gashi ya tada dan karamin yaki a gidansa wanda take fatan Allah ya tsawatarwa abin, aman kuma ya fake a bayan fage,
Ita kam, ba zata taba tirsasawa Agaishat ta so Wardugu ba, aa, ta yaya? Ace da ita me? Dan danta ne? Dan ita ta haife shi? Ita kam tana da kunya!

Yawu ta hadiye kafin ta saka hannunta ta dago da kafadarsa,
Abinda ya cika idonta ta mayar kafin take dan dukansa a kirji ta ce" Wardugu? Dama zaka taba sarewa kan mace? Ka zauna kanai min rigima tamkar wani baby kan yarinyata? To ni me kake so na yi maka bayan ka san lamarin nan ba zai taba yiwuwa ba dan duka duka yaushe ka yi aure?

Wardugu ya bude jajayen idannuwansa ya dora kan mahaifiyarsa , ya jima a haka kafin ya ce" a gabanki, sai na iya yin kuka, tunda kika haife ni, kika sha gwagwarmayar rayuwa wajen rainona da komai nawa ai ba zancen na kai kukana wani wajen,
Ayya ni ba zan bude bakina na dubi yarinya karama kamar Agaishat nace da ita ina sonta gatsal haka kawai salon ta raina ni, sannan Mu.azam dake wani takamar ya aureta ya saketa dan ni kennan ya ji dadin kara fada ko me?
Haka fa yarinyar samari ne da ita fa, kin ga wani shegen buzu wuyansa na lauyewa yana jawo shi kwana ya yi ya wuni yana kiranta yau shi ne har wajen dinern nan, Ayya kinfa san yaren nan na zamani ko wasa kake da su yanzu zasu samu hanyar rainaka!

Ayya ta shiga girgiza kai tana murmushi a kasan zuciyarta ta ayana" da sauranka, zako ka ga halin yarinta!
A fili kuwa ta ce" Wardugu, maganar Walyn fa?

Wardugu ya mike tsaye kafin ya koma saman kujerar ya zauna kusa da Ayya sosai ya ce" Ayya, shin adini ne? Aurena da Walyn kusan shekara hudu fa , Ayya kece shaidar irin rayuwar auren da nake da Walyn duda ba zuwa nake ija baki labari ba, aman du lokacin da kuka hadu sai haukan ya bayana , Ayya, yanda kika san rayuwar tumakai haka muke da Walyn,
Sam bata zauna bama, ta fahimci waye ni, ta fahimci menene ainahin zaman auren bale har ta wani kula da shi,
Takamarta kyau, wayonta yawo, isarta ta je wajen yawon ta yi gadara da kudin da ni ke nema, Kishi....sakaran kishi, in ba dan ina tsaye a gidana ba Ayya da Na rantse maki Walyn ko ke sai ta hana ni yiwa magana bale wata mace a duniya, tarota nake , lalabata nake, kwatanta mata nake, fushina nake nuna mata , ko zata yi hankali ? Ko zata gane ni ne gaba da ita? Ni ya dace ta bi? Aman cikin kwakwaluwarta banda kusoshi ba komai, gashi ina zaman zamana, ta sa na shiga wata rayuwar ta shirme! Shirme mana Ayyana .... wai ka zauna tunanin yaro karami?
Ayya zan koma kauyensu yarinyar cen, na fadawa iyayenta komai abubuwan dake faruwa, na fada masu ina neman aurenta,

Ayya ta mike ta ce " kul, kul, kar ka yarda yarinyata bata aminta da kai ba ka wani je neman aurenta, ba wanda zai mata karfi, kana magana rigima na yawo a harshenka, to ka zauna min ba inda zaka yau, dan na san in dai ka fita a gidannan sai ka tafka wani abin !

Ta karashe tana yafa mayafinta ta nufi hanyar kicin inda wardugu ya bita da kallon mamaki,

Ayya kennan, a duniya ba wace yake zuwa ya sanarwa sirinsa mafi sirri irinta, yana da rike abu

gaban kowa aman ita yana gagawar sanar da ita damuwarsa ko farin cikinsa, tana kuma iya yinta dan gannij ta shige al.amarinsa, bata taba saka wani ya yi masa abu ba, sai dai yau gashi wai wai shi ya fada mata zai mutu ko zata tsorata? Aman wai tace da shi ya nemi soyayar yarinyar? Daga yanzu ya yarda yarinyar nan ba shi kawai ta gama halakawa ba, har Ayyansa ta kwace! Yar Buzuwa ta iya kwace,

Wayarsa ce ta dauki kuka,

Dagawa ya yi domin mijin Alhinayett ne,

Mikewa ya yi da kyar ya fice ya nufi can tsakar gidan,
Tarar da su ya yi cikin mota Alhinayett sai kumbura take tana karawa kan ita su biyo kafin su tafi,

Wardugu ya yi tsaye ya kare mata kallo, kafin ya maida dubansa wajen Colonel ya ce" walahi idan ka yi wasa ta fahimci halin da kake ciki na mugun sonta da kake zata mayar da kai hotiho! Kai yanzu gabjejen kato da kai, ta sakoka gaba ka kawota wai ta ga lafiata lau? Da ni na haifeka yau da sai na baka shegen duka, yo ina anfanin wannan lamari?
Sai da wardugu ya gama yi masa fada tsaf sannan ya taka ya karasa wajen motar,

Kwonkwasawa ya yi ta bude, tana dubansa kafin ta ce" Wardugu lafiarka kalau? Ina Agaishat din?

Ce maki na yi bani da lafia?

Wardugu ya fada yana zazaro mata idannuwansa,

Da sauri ta dube shi da kyau kafin ta ce" gani na yi hankalinka a tashe,

Ohk shi ne kika tiso keyar danki ya kawo ki?
Ya kuma bata amsa yana hararanta,

A ranta ta fadi" To fa,

Wardugu ya nunota da yatsarsa ya ce" walahi na san ciwon kaina, ba zan bari ki wulakanta bawon Allah ba nima Allah ya kama ni ta hanyar saka wani dan rainin wayon ya wulakanta ni, ke yanzu da nine aka tiso keyata zuwa ganninki a lokacin da nake ango me zaki kalen? Alhi, bana son ki kaini wajen da zan rike makogworon wuyanki, walahi a kan aurenki idan baki zama mace mai kyawawan dabi.u abin alfarin mijinta ba, zan tarda ke har inda kike na ya gashinki a kasa ! Ke ni ba nasiha ko rarashinki zan ba, ke kanwata ce, idan kika zubar da mutunci da darajar gidanku , kika aniya wulakanta wannan mutumin ni zan masa aure da kaina sannan na tataka ki idan kina so ki rufe ni,

Kiwit kiwit take da ido bata ce da shi komai ba, dan ta san idan hakuri tace zata bashi yanzu abin zai girmama, yi masa shirun shi ne ya fi sauki, sannan ta yi dan daman bata matsa kan su biyo ba, ita wollah yannayin Agaishat ne ma ya tsaye mata a rai, bata so ko kusa Agaishat ta saka tsoron Walyn a ranta, ta so ta ganta yau ta fada mata abinda ya sa Walyn yi mata haka sannan ta karfafa mata gwuiwa, kanta ta sada har ya gama fadansa wanda tana tunanin taka kaya ne dai suka yi, dan kuwa har colonel din da ya biye mata sai da akai masa ,

Ja ya yi ya goya hannunsa daya a bayansa yana dubansu har suka fice da motarsu,

Agaishat dake tsaye bakin window din dakinta ta sauke ajiyar zuciya kafin wani murmushi ya kubuce mata,

Zama ta yi bakin bed dinta daga ita sai gajeran wandonta da yar riga karama na baci ta ce" Wai wai wai, rigimame yayana, kai aman gaskiya shi ne daidai da matar nan tasa , haba mace kamar wace aka haifa ana dambe? Ita kulun cikin fada da neman a gabzu take?

Gashin kanta ta tatara ta daure kafin take yin bismillah ta bi lafiyar gadon,

Idannuwanta ta lumshe dan neman baci, sai dai me....idannuwansa ta ji sunna yawo a jikinta,

Wani irin tsammmmmmm ne ta ji tun daga kanta har yatsarta,
Da sauri ta mike zaune tana yatsina fuskarta,

Mikewa ta yi ta koma bakin window din ko zata kara ganninsa? Kai wollah ita bata gajiya da kallonsa, tana tsoron rigimarsa , aman kuma tana girmama irin yanda yake girmama mahaifiyarsa, ba mahaifiyarsa kawai ba du wani abinda ya shafeta yana masa mugun girmamawa, zata so komai ya daidaita tsakaninsa da mahaifinsa, zata so gobe kiyama ya samu rabauta, domin aljanarsa tana karkashin kafar mahaifansa, tana so alkhairinsa ya same shi gobe kiyama ,

Yana tsaye dai, da waya a hannunsa yana danawa, ba zata iya gannin me yake dannawa ba,

Bata shirya gannin ya dago da kansa ba sai gani ta yi ya kallo wajen windows dinta, da sauri ta duke kasa domin ba zata so ya kamata tsamo tsamo tanai masa kallon kurulah ba, me zai ce? Ina ai sai ya yi mata wata muguwar fasara,

Ajiyar zuciya ya sauke kafin yake sakin murmushi, ya ji idannunta a jikinsa, ya san ta tsaya a wajen can.....

Juyawa ya yi ya koma fallon yana kara kiran abokinsa kuma direbansa kan a gobe su bi jirgi su jufi timiya, zai daki abin da karfi ya ga mai tsayar da shi daga Walyn, da Ayyar, da uta Agaishat

din! Idan tana so idan ta ji ya aureta ta hadiyi shinkafar bera 😒

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

7️⃣6️⃣

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA* in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

A nan falo ya kwana , ko nace ya yi rabin kwana , domin bai shigo falon ba sai da ya dauro alwallah ya zo ya tayar da sallah ,
Ya jima yana sallah kafin ya zauna ya yi ta adu.a,
Ya roki Allah, ya kaskantar da kansa wajen ubangijinsa, ya roki zabin Allah, ya sani bai isa ya baiwa kansa ba, ya roki Allah ya sa alkhairi ce a gare shi da kowama,

Nan saman salayar dake falon ya jingina da kujera ya dan rintsa,

Asuba na yi ya farka ya fice a falon inda ya je ya sake daura alwallah ya fice a gidan dan zuwa masalaci,

Yana dawowa wajen karfe shida da yan mintuna ya zauna nan saman kujera idannuwansa suka kai kan wayarsa dake ta vibration,
Ikon Allah, shi ne abinda ya fada kafin ya ja dan tsaki kasa kasa yana mai jin haushin masu saukon kiran nan! Ko me zai masu?

Wayar ya janyo yana duba sunnan,

Mamaki ne ya kama shi, aa *GUKUNNI* kuma?,

Da sauri ya mike ya daga kiran, domin abu daya ya fado masa a rai ko wani mai laifi ne ya gudu daga cikin prison?

Salama ya yi masa , suka gaisa da kyau kafin wardugu ya yi shiru yana saurarronsa,

Gukunni ya ce" gani a kofar gidanka Wardugu,

Wardugu ya kara kamuwa da mamaki aman sai ya boye ya ce" ai ina gidan Ayya ne Honorable,.

Gukunni ya shafa sankon kansa ya ce" ka kwatanta min in sha Allah zan karaso, ina tafe da muhimiyar magana ne , wada na jima ina nemanka Allah bai yi ba sai yau na samu wayarsa

Wardugu ya dan tsurawa waje daya ido, anya kuwa zai kwatanta gidan mahaifiyarsa haka kai tsaye?
Sai dai wata zuciyar ke fada masa da ba komai bane sai alkhairi, dan haka ya yi masa kwatance suka katse kiran,

Rigarsa ta saman kakinsa ya nema ya dora saman bakar rigar dake jikinsa,
Kansa ya daga sama ya ga basu fito ba, bai ji motsinsu ba, dan haka ya zauna nan yana jiran karasowar Gukunni Bayan ya baiwa masu gadi damar idan ya zo ya shigo,

Ya kai minti arba.in kafin ya karaso, domin dai ba sannin gidan ya yi ba bale ya kai kansa kai tsaye,
Sai dai a lokacin da ya ga kofar gidan ya gane ko gidan waye, wato Elhaji Marahut, tabas sunnan Wardugu , Wardugu Marahut,
Murmushi ya yi ya lalubo wayarsa ya dannawa Marahut kira , da yannayin barkwonci yake sanar masa komai da fadin ai yana kofar gidansa,

Nan marahut ya yi jim kafin yace da shi baya kasar fa, aman zai shigo da wuri wuri, shima ya yi

murna sosai sosai, sukai salama,

A tsakar gidan aka dakatar da shi, kafin Wardugu ya fito,

Tunda ya fito yake dubansa da yannayin farin ciki, kai shi dai yana son yaron nan ko dan kwazonsa da rashin tsoronsa,

Wardugu na zuwa ya bashi hannu suka gaisa sosai, sannan Marahut ya ce" Wardugu, tafe nake da magana mai mahinmanci, fatan zan samu lokacinka,

Wardugu ya amsa shi tare da yi masa jagora zuwa falon Ayya, domin ko ba komai yana kaunar datijon yana gannin mutuncinsa, dan kuwa su shara.ar da ya je ya gani da idonsa wace ya yanke hukunci na manyan kasa masu laifi, yana gani da idonsa yana yankewa ne da zuciya daya ba tare da wani dar ba, hakan ya sa ake bashi tsaro domin ya kasance yana samun hare haren mutanen da suka ji haushin irin hukuncin da ya yanke masu ko wani nasu!

Suna shiga suka tarar da Ayya na saukowa daga sama, sai naza kanshi take, zuwa lokacin duka duka karfe takwas ce, inda Wardugu ke duba lokaci dan kar karfe tara ta yi lokacin tashin jirginsu zuwa agadez,

Gaisawa suka yi, nan Ayya ta mike zata bar masu wajen aman ya nemi da ta zauna,
Cikin nutsuwa ya shiga warware masu abinda ke tafe dasa shi,  ya dora da fadin" lamarin ne a cakule, lamarin ne a hargitse, kadara ce ta afka mana, sai dai mu ce Alhamdulilah, autata Allatchi ita ce mahaifiyar yarinyar, ta fuskanci rayuwa sai hamdallah, yanzu haka tana Chaina, tana karbar magani, nima nakan zo sati sati dan na kara duba tsohon da muka zo da shi duda akoy masu kula da shi, nakan zo na ga komai na tafia daidai kafin na koma wajensu,

Al.ajabi, tausayi, ne suka kashe Ayya a zaune, inda wardugu ya sada kansa yana jin wani lamarin da bai san menene ba,

Ayya cikin mamaki ta ce" ta yaya? Waye ya daura masu aure? Waye ya yi gigin daura masa macen da bai ga alwalinta ba???

Gukunni ya yi shiru, jikinsa ya kara mutuwa, hankalinsa ya rashi, ransa ya kara baci da lamarin, dubansu yake yana tunanin sun cancanta su ji haka kuwa?
Eh kwarai sun cancanta, idan ya so, idan mijin da ya aureta ya ce ba zai zauna da ita a haka ba ba laifi, Allah ne gatan bawa, dan haka ya dago fuskarsa da ta nuna yannayin da ya shiga lokaci guda ya ce" *BAI AURETA BA, BA AURE YA ZAUNA DA ITA , BA AURE SUKA SAMU ALBARKAR HAIHUWA*

Innalilahi wa.ina ilaihi raj.une,
Shi ne abinda Ayya ta fada tana mai dora hannunta saman kanta,

Wardugu ya dago da kansa da mugun sauri tare da bugawar zuciya,
Bin innalilahin da Ayya ke maimaitawa ya yi,
Tausayi? Mugun tausayin matar ne ya dirar masa, sai tausayin Yaren, ya Allah, kowa da kalar kadarar rayuwarsa, Agaishana....shi ne abinda zuciyarsa ta ambata,

Ayya?
Muryar Agaishat ya katse masu halin da suka shiga,

Da sauri Ayya ta sauke hannunta daga saman kanta, domin hakan da Agaishat ta hango ne ya sakata saukowa da gudu daga sama dan jin ba.asi, sam bata lura da Gukunni ba, sai da ta ji an riko hannunta an juyota,

Tsarki ya tabata ga Allah, sarkin da ya halici bayi, sarkin sarauta rabih,
Ga yarinyar nan, wannan itace mai kama da shi din, ga kamarsa karara a fuskar yar, har irin yanda idonsa keda tsaga da girma,

Tsai ta yi tana dubansa, kwarai ta ga kamar fuskarta a tare da wannan mutun , sai dai tunanin ta ina? Ta yaya? Ita yar asalin timiya fuduk zata hada jini da mutun haka Wanda suturar jikinsa kadai ta isa ta shaida shi din ko waye?

A hankali ta bi hannunta da ya rike da kallo, yatsutsansa irin nata,
Da sauri ta dago zuwa fuskarsa, sai kuma ta juya wajen Ayya gabanta na dokawa ta ce" Ayyana, wanene wannan?

Ayya dake ta kokarin maida kukanta ta ce" Agaishana, kakanki ne, ta karashe tana mai sakin kukan dan ta kasa rikewa,

Agaishat ta janye hannunta tana dubansu su duka, da sauri ta je wajen Ayya ta ce" kukan me kike? Wani ne ya mutu? Kaka kuma? Ni nake da kaka? Me ya saka ki kuka Ayyana?

Wardugu dake duban Ayya kansa kawai yake girgiza mata dan kar ta fadawa Agaishat abinda ya sakata kuka, baya so, abin sai ya yi masa yawa, bai sanba ko zata yi tawakali ta yi hakuri?, dan haka a hankali ya lumshe idannuwansa yana ji Ayya na fada mata gaskiyar waye gukunni a wajenta, wato mahaifin mahaifiyarta,
Cikin nutsuwa ta warware mata yanda suka hadu da Algabit, sai dai sam Ayya bata fada mata dayar maganar ba,

Farin ciki kam ta ji shi, sosai ta yi murna, sannan ta yi adu.ar shiriya ga mahaifinta, domin bata da abin cewa kansa ita kam,

Nan aka kuma shaida mata rashin lafiar Anna dalilin tonuwar asirin ,

Da da uwa, nan ta yi sokoko ta zauna tana sauke ajiyar zuciya, du sai ta ji duniyar ba dadi,

Kanta ta sada dan kar ta nuna mugun damuwarta har abin ya taba Ayya, domin zuwa yanzu ta gama yarda da soyayar Ayya a kanta tamkar ta uwa da d'a ne,

Dubanta ta kai wajen Wardugu idannuwansa a lumshe ko barci ma yake?
Bai ci komai ba , shi ne ya fado mata a rai haka kawai, dan haka ta mike ta nufi kicin ba tare da ta kara bi ta kan wani ba,

Nan Ayya ta fara fada masa maganar auren Agaishat din da ya mutu,

Sosai abin ya dake shi, har ya tambayi ba.asi?

Wardugu dake zaune ya ce" bashi da huja,

Ayya ta kai dubanta kansa, ta girgiza kai ta ce" ya gabatar da hujarsa, wace sam bai dace dan wannan hujar a saki mace ba, batai masa laifin komai ba, shima bai mata ba, hasalima tun kafin a yi masa aikin ya yi sakin, bisa hujarsa na aminin nasa ya fi shi son ta!

Dum gabansa ya fadi, da sauri ya kalli Ayya, la.ila ha ilala , shi ne abinda ya iya cewa, ya ake maganar yana magana kai tsaye bayan ga wada ke yi? Bai taba zaton, bai taba kawowa ransa cewar Ayya zata fadi maganar haka kai tsaye ba ,

Shiru ne wajen ya dauka, kafin Ayya ta ci gaba" na ji ba dadi, na yi fushi, Aure? Sai kace abin wasa? Ya tashi ya guntule igiyar auren yarinyar da bata san me ake ciki ba? Kan wani shirme? , shima Wardugun ya nuna masa ba dadi, maganar da nake maka har yanzu ba wani jituwa tsakaninsu,
Nan ta kwashe du abinda ya faru ta sanarwa Gukunni da da farko ya dauki zafi har ya ga kamar an wulakanta yarinyar ne dan anai mata kallon marar gata, sai dai daga baya da ya ji komai ya yi tsam ya dubi Ayya, ya kuma dubi Wardugu da ya dafe kansa yana tunani, aa, du wannan jawabin na menene? Ya Allah🤦🏻‍♂️

A daidai lokacin da Agaishat ta fito dauke da farantin da ta soyawa Wardugu dankalin turawa da plantain ta nufo falon,
Muryar Gukunni ta karade wajen da tambayar da ya saka ni ranaza har na saki biron hannuna,

Gukunni ya dubi Wardugu ya jefo tambayar da basu tsamaci zai yita ba, Gukunni ya ce" *SHIN DA GASKE KANA SON AGAISHAT NE? ZAKA IYA AURENTA KODA KUWA TABON DA RAYUWARTA KE DA?**************

MEMBERS BAK'A CE GRUP, WOLLAH INA JI DA KU TAMKAR NAMA DAYA A MIYA,
WATO KUNA SAKANI NISHADI DA COMMENT DIN KU,
HAR KUKE SAKAWA NA JI NI YESSSSSS NI DIN TAKU CE😌😌😌😌😌

🐪🐪🐪🐪 *BAK'A CE* 🐪🐪🐪🐪

Na
*SAJIDA*

77

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA* in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

Da sauri Ayya ta ce" Aman ya Gukunni, ba shi ya dace a tambayi wannan abin ba, bana so a kuma yiwa y'ata abinda akai mata sai ta zaba! Kuma da ake maganar nan , bai jima da yin aure ba fa, ko cike shekara hudu bai yi, hasalima matarsa na kwonce asibiti dan ya dankara mata maganar cewa yarinyata *Orronur* dinsa ce! , dan Allah kar a tauye min yarinya,

Dubansa ya kai kan Agaishat da ta ja ta tsaya tana binsu da kallo, wai bata fahimci wa ake shirin hadata da shi kuma? Waye matarsa ba lafia? Wardugu ne, meye kalmar Orronur ke nufi? Ya Allah wani hadin za.a kuma yi mata ko me? Hadinma da Wardugu? Mutumen da ita ce shaidar irin yanda yake kwasa da matar so ma bale ita?, mutumen da ta yi imanin har abada ba macen da zata samu gurbi a zuciyarsa kamar yanda *AISATA* ta gama mamaye ko.ina? Domin a yi yawo da ganga ba zata hadiye cewar ba sonta da yake ne ya saka ya kasa yafewa mahaifinsa dan ya aureta ba! Mijin WALYN? ko ba wannan ba, ita ta yi imanin koda daura masa ita za.a yi a kafa zai ja banza a titi sannan ya take da ranjasss ya bale ya jefawa karnuka su cinye banza, ita a wa? Yar wa? Algabitt? Um, yayan manya, manyan kansu suna farauta ? Ita bata son mai kyau dan kar a ringa rububinsa, ita ita....

Tunaninta ne ya katse a lokacin da Ayya ta ce" kar mu yi haka da kai,

Tsai ta kai dubanta wajen Ayya a ranta tana fadin" ki yi wani abu, ni ban san wani kaka ba, yaushe ma ya zo gidan? Ki yi wani abu kar a kashe maki d'a, sannan a kashe maki y'a!

Wajen sai ya kasance Agaishat na kallon Ayya da wani yannayi, Wardugu kuwa tsai kawai ita yake kallo yana son sannin halin da ta shiga dan kuwa ya san ba kurma bace, kuma ba sakara bace, tabas ta fahimci maganar da ake,

Ayya kuwa Na duban Gukunni, inda Gukunni ya gyara zama yana sakin murmushi yana duban Wardugu da yannayinsa, ya san waye shi, ba zai taba amsa shi a haka ba, ya kuma lura da yannayin Agaishat da irin duban da take yiwa uwar rikonta, wani sanyi ya ji a ransa domin ya ga shakuwa, kauna ta Allah tsakanin Agaishat da mahaifiyar Wardugu,

Mikewa ya yi ya yiwa su Ayya salama, inda Wardugu ya mike ya bi bayansa dan yi masa rakiya yana mai jin ba laka a jikinsa,

Sai da suka dangana da motarsa ya dakatar da shi, inda ya dauki katuwar wayarsa ya danna kira,

Dagawa ya yi tare da kara yin salama sannan ya ce" honorable ka samu ganninsa ne?

Gukunni ya yi murmushi ya ce" wato Alhaji, ka manta ni lauta ne kafin na zama alkali, ? Bayan wannan ka manta numberka na niger ne na kira ya shiga ba cod ba komai? Kana ina ne? Domin ina so in sha Allah mu hadu kafin lokacin sallar azahar, ina tare da Wardugu,

Jim ya yi yana jin ba dadi, ya Allah, kowa dai ya san halin da suke ciki da matarsa uwar dansa, koda yake shekara da shekaru its normal,

Fada masa ya yi su hadu a Wardugu Palas, wajen da ya dawo operation irin na da,

Wardugu kam gum da baki, bai ce komai ba ya bi bayan Gukunni cikin motarsa da bodyguard

dinsa biyu suka daga sai wajen da yake ainahin wajensa,

Murmushi Marahut yake tunda ya gama magana, ya dubi Wardugu ya ce" kana son ta kennan?

Wardugu ya hade fuskarsa ya kawar da kansa irin ba shi ya kawo maganar ba,

Marahut ya girgiza kai yana murmushi ya ce" mai hali, baya daina halinsa!

Honorable, kana nufin, ba zaka juya chaina a gobe ba sai an daura auren nan? Baka gudun rigimar Ayyansu? Ita yarinyar shin tana so?

Gukunni ya ce" ina tunanin su za.aiwa alfarma!

Marahut ya sada kansa,
Agogon hannunsa ya duba, sannan ya mike ya ce" karfe 2 ka zo da sadaki saifa millions arba.in. ka same mu a masalacin Elhaj Murtala ,

Yana gama fada ya mike ya shige ciki inda Gukunni baki bude ya mike ya bi bayansa yana fadan wani irin Millions 40 sai kace wata yar gwal ko wata budurwa?

Wardugu kam wani tsadaden murmushi ne ya saki daga zaunen da yake, yau ranar Asabar, 5 ga watan Jun , rana ta raba tsaka zai malaketa,

Jama.ar da suka halarci sallar azahar suka shaidi daurin auren, Daurin auren *WARDUGU MARAHUT* da *AGAISHAT ALGABITTT* bisa sadaki Millions 40 cefa ladakan, ,

Zamanin whatsup, zamanin android , nan da nan mutane suka fara watsa wannan lamari, inda ake yayatun buzuwa ce, suna yi har fiye da haka, Buzuwa ce General ya santale,

Nan da nan yan jaridu suka fara neman Wardugu cikin birnin Niamey,

Yan mata suka fara doka waya suna neman jin karin bayani,
Gidan redio ta saki labari,

Walyn,
Walyn dake kwonce tana shating ta ga kanwar kawarta ta dora saman status cewa" kaka kara kaka, wai da gaske ne ko da wasa? General ya bada sadakin buzuwa million 40 arma ta zama tasa? General wardugu ya watsa kuraye, abin son jinma ana cewa Black ce!....?

Ta karanta ya fi a girga , kafin kamar hadin baki, kira ne, mesage ne whatsup ne, facebook ne? Abu ya zama a lokaci daya ya shiga shigowa,

Bata gama tantancewa ba mahaifiyarya ta shigo dakin asibitin a fujajan ta ce.............

Ayya hankalinta ne ya gama tashi a lokacin da ta ji wannan bayani ta bakin Marahut da ya yi kiranta da bakuwar number ya yi mata murna da fada mata ya daurawa dansa aure da yarta ga sadakin nan zai zo ya kawo da kansa idan tana so ta saka a hana shi shiga!

Wardugu,
A lokacin da ya ji eh lale Allah ya damka masa igiyoyin jan ragamar rayuwarta ya mike ya shiga motarsa da kayan jikinsa na tun jiya da bai samu ya tsaya bama bale ya canza,

Zama ya yi ya jinginar da kansa, idannuwansa ya lumshe sai kuma Walyn ta fado masa a rai, Wani tausayinta ne ya ji ya dirar masa, dan ya sani ne Allah kawai zai tsayar da ita kan saka kanta a uku,

Motarsa ya tayar da kansa ya harbata bakin titi da gudun balaki......

Bai zame ko.ina ba sai clinik din da Walyn take,

A nitse ya kashe motar ya zare kys din ya fice daga ciki,

Taku yake cikin nutsuwa da ingarma, ba zaka taba fahimtar halin da yake ciki ba har ya tura kofar ya bude,

Ido hudu suka yi shi da ita, tana zaune ta ziro kafafuwanta kasa, ta ja rigar clinik din can saman cinyoyinta, kanta bude gashin kanta ba ribom, ta tsurawa waje daya ido domin jinta da ganninta ne suka fauke na dan lokaci,

A hankali ya karasa kusan gadon da take zaune ya cire takalmin kafarsa ya dan saci duban mahaifiyarta ya ga tanai masa wani kallon da ba zai gane na kyama ne? Na tsana ne? Ko na deception bane!
Hannunta ya kamo yana dubanta,
Murya cinkushe ya ce" Walyn,

Idannuwanta kawai binsa suke da kallo, Namiji? Bata taba sannin kalmar da zata yi ajalinta bane sai yau! Namiji Namijinma wanda ta fi aminta da shi, Kishiya? Kishiya Wardugu ya yi mata? Ita Walyn? Me ta rage shi? Menene? Ita ya wulakanta a idon duniya? Ita ya wulakanta a dangi? Yanzu uban wa zata yiwa daga kai da jiji da kai a gari? An taka dokar al.adunta ma, an tarwatsa takamarta ma, an ci amanarta, dan me? Me ya yi zafi? Me na rasa? Ban taba haihuwa ba....hasalima ban bar kwan ya zama gudaji ba na watsa shi, du domin ka???

Muryarta na rawa ta ce" Wardugu, dandan me? Sex ne ko? Dan wannan ka tozarta ni? Nawa

bai isheka ba???

Wardugu ya dane , ya ki nuna komai ya rikota jikinsa ya ce" aa, ba wulakanta ki na yi ba, kuma ba ramuwae gaya na yi maki ba Walyn, ba dan sex na kara aure ba, ina so ki kwontar da hankalinki, ki kwontar min da nawa, idan har kika yi haka Walyn, ina mai tabatar maki da zan canza, zan dawo maki yanda kike so Walyn, idan har kika yi hakuri da wannan jarabawa...zaki ci ribarta, ki yi hakuri, ina baki hakuri ne ba dan na aikata haramun ba, aa , sai dan kema matata ce, ina son ki, ba cusa min ke aka yi ba, Walyn haka itama ba wanda ya yi min dole, ki sani aure lokaci ne, kuma rai ne da shi, ki dauka lokacin yin ne ya yi na yi, kar ki yarda zugar mutane ko na shedan ya yi tasiri a kanki, dan Allah matata ki jure wannan karon, bana so mu raba hali, ki jure walyna......
Ya karashe yana mai shafa gashin kanta,

Wani irin kuka ne ta fashe da shi mai karfi da rudu,

Gaba daya ta saka hannunta saman kanta tana ihu,

Da sauri ya hade bakinsa da nata dan rufe bali ihun da take ......... aman ina cizo ta gantsara masa kafin take kokarin kwacewa daga rikon da ya yi mata tana jifansa da wani kallo irin na bakon halita mayaudari ko wani azalumi,

Aniya wartar du abinda ya zo hanyarta ta yi tana dokawa da kasa, ihu take wanda ya fara tsoratar da dakunnan kusa da ita sannan likitoci suka fara yowa dakin da gudu dan ko tunanin mutuwa aka yi wani marar imanin yake kuka irin haka!

Hannunsa na dama ya saka ya tokare habarsa yana kallon yanda mamanta ke binta tana kiran sunnanta aman cikin ikon Allah dan karamin frij din dake dakin kansa sai da tajanyo ta kifar tana ihun yau sai dai a yi daya, ko ita ko Agaishat!

Mikewa ya yi ya damki hannunta ya jata,

Kiiiiiiiiiii inda du aka rufa masu baya wasu na tambayar lafia ? Cike da tsoro wasu na kallon ikon Allah da yiwa Walyn kallon wayo Mahaukaciya ce da alama?

Motar ya bude gidan baya ya turata ciki sannan ya koma gaba ya shiga ya rufe ya yiwa motar ky sannan ya tayar ya harba ba tare da ya tsaya daukan mamanta ba, dan ya sani ne, ba zata taba tausarta kan lamarin ba, dan shi kadai ya san abubuwan da ya tsinta uwar na fada a lokacin da ya karaso asibitin,

Hauka fa tuburam, Walyn fa ta zauce, magangannu take saki tare da fadin Warsugu macuci ne,

ya cuceta a haka har suka karasa gidan su,

Wannan karron daukanta ya yi cimak ya nufi falonsa da ita, yana budewa ya direta cikin falon ya rufe fallon ya barta nan ya nufi cikin dakinsa ya shige bayi,

Wasa sabon girki, wato dabi.un wasu tubawan idan akaiwa kishiya , shi Walyn ta aro, inda ta aniya dira tana fasa du wani abin fasawa na falon Wardugu, ciki harda katuwar plasma din dake mamaye da bango, ta tarwatsa table din diner da na tsakiyar falon, ta dauko wuka ta yayaga wannan tanfatsetsiyar kujera ta alfarma, ta kawo ruwa ta makawa moket din ta aniya dira tana yagawa,
Ta kama labulayen bangon du ta yaga shegu, ta dira dakin bakinsa ta aniya yaye jibgegen bargon dake malale saman katifar dake kan bed din, ta saka wukar ta yayaga katifar, ta kama kyarta jikin gadon da sif din da komai na dakin, ta fasa madubin dake kawaye a dakin, ta dauki iphone dinsa kwara uku ta tanfatsa da kasa,
Aiki take na gangan, aiki na motsa mutun domin koda Wardugu mai kudi ne an masa asara ta kirki, gashi bai jima da canza komai na gidan ba,

Fitowa ya yi daga wanka daga shi sai tawul yana mai jinsa yana yawo a sama, sai dai me, turus ya ja ya tsaya yana hangen bayanta yanda ta dukufa take yaga bargon da ta yaye stilll tana ihun kuka,

Habarsa ya dafe da hannunsa yana bin dakin da kallo, kafin ya maida dubansa kanta,
Ikon Allah, shi ne abinda ya fada a ransa,

Zagayeta ya yi ya bude sif din yana bin inda akaiwa sabon zane da kallo , ya janyo boxer dinsa da wasu kayansa na kanfanin Gudd ya ciro yana ajiyewa nan jikin bed din,

Ai kuwa ta ankara da shi ta nufo kayan da ya ciro ta dauka ta saka wukar ta yaga,

Bakinsa ya rike ya ce" Walyn da tsada fa??

Bata bashi amsa ba sai harararsa da ta yi ta ce" walahi sai ka saketa, walahi ni na san dan ka rama abinda na yi maka ne, baka yafe mini zubar da cikin da na yi bane shi ne zaka hukunta ni ta hanyar yi mini kishiya, walahi sai ka saketa ko daga ni har kai mu bakunci lahira,

Murmushi ya yi kawai ya girgiza kansa ya kuma fitar da wasu, aman yanzu yana cirowa yana sakawa ne bai ajiye ba dan kar a maimaita abinda aka yi,

Juyawa ya yi bayan ya kile sif din dan akoy kayansa masu mahinmancin da ba zai so ta wulakanta ba ,

Da gudu ta biyo shi tana faman yi masa tijira inda ta nufe shi da wukar hannunta ta nufi cikinsa da ita ido rufe tana alwashin sai ta halaka shi tunda ya yi mata kishiya,

Da sauri ya goce ya tara hannunsa, nan ta yanki gefen hannunsa wajen kaurin hannun nasa da wukar ta yi masa baban yankan da jini ya bale ,

Idonsa ya rintse yana jin zuciyarsa na fara yaba gayatar balakin da take masa,
Kara nufo shi ta yi tana ta balaki da tubanci wanda zagi ne kawai bata saka ba aman har Ayya sai da ta dorawa laifin da bata ji ba bata gani ba tana fadin daman idan sarakuwa ta tsane ka ai ba ta inda ba za.a biyo maka ba,

Hannun mai wukar ya rike inda ya matse shi da dan karfin da ya saka ta kwala kara ta saki wukar,
Janyota ya yi inda yake tsaye ya fala mata mari ya kara mata,
Bai kuma yi mata magana ba sai janta da ya yi waje  kujerar da ta yiwa ta.asa ya kama rigar asibitin dake jikinta ya yagata , toh daman rigar ba wani kwari ba sannan botira ne jikinta,
Bata gama gane ina ya dosa ba sai da ta ga daga rigar bai zame ko.ina ba sai wajen da baya faduwa ya saka hannunsa shima ya yage shi ya.......
Tumurmusarta yake da dukan karfin da Allah ya bashi ta wannan fannin,
Dukan da ya fi duka zafi ne yake bata ido rufe ko zai samu ta rufe masa bakinta ta daina magana kan mahaifiyarsa tamkar wata tsararta!
Shin wacece ita? A darajar masu daraja da Allah ya halita a duniya musulmai wacece ita da ba za.a yi mata kishiya ta yi hakuri ba?
Wacece ita da zata ringa budar baki tana jifan halitar da Allah ya halita ba tare da ya ce dan ya yi mata kalar fata haka laifi ta yi masa ba?
Wacece ita da zata ringa zagin kadararsa? Domin kuwa shi ya san Allah ne ya kama shi a kan Agaishat, ya ba zata bar shi ya ji da irin rigimar da yake hangowa kansa ba a tare da mahifiyarsa da kuma yarinyar da bai san meye a zuciyarta game da shi ba? Ya ba zata tarbe shi, ta kula shi, ta taya shi a wannan lokacin da yake cikin garari yana sakin magangannun da sai ya yi wata bai yi masu tsayi irin haka ba ? Ya bata lura da ya so su yi masalaha su fahimci juna, ya so ya rarasheta irin na kowace mace mai inci mai fada a wajen miji idan akai mata kishiya ba? Shin Walyn kwakwaluwarta a tabe take ko tsabar iskanci ne da samun guri? Shin ya fara sakin fuskar da har raini mai karfi ya kara yin tasiri tsakaninsa da Walyn da sauran mutanen?
Ya ga Alama ba Walyn ba, harta da ita Agaishat din idan ya yi wasa za.a samu matsala......
Ya Walyn zata manta ainahin Waye Shi a doron kasa? Ya zata manta shi ne asalin batube gaba da baya cikake mai jininsu dake yawo a jikinsa har ta nuna masa wuka?
Shin ta manta yaya suke da wuka ne?
Shi zata tarba da balaki hauka , da tashin hankali batan ta san adireshinsa ne complet??????

Morning

Idona ya fara ciwo, ni kam sai na huta😍😍😍

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

7️⃣8️⃣

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA* in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

Ups sauran kadan dai💃💃💃💃💃💃💃

Dakinta ta tura ta shiga , jiki ba karfi ko kadan,

Wajen salaya ta hangota inda itama ta dago da kanta tana dubanta, salar la.asar ta gabatar kennan, ta zauna tana adu.a,

A hankali ta karasa inda ita kuwa take faman mikewa tana duban Yannayinta, tamkar tana cike da damuwa,

Mayar da ita ta yi saman salayar ta zaunar da ita sannan itama ta zauna ta rakubu da bangon dakin ,

Kanta ta daga sama tana kallon shilling,

A nitse Agaishat ta ce" Ayyana , lafia??

Shiru Ayya ta yi tana tunanin ta inda zata fara, can ta ce" ina jin kinyar Allah, ina jin kunyar amana , ina jin kunyar soyayar da kike min tamkar uwa,

Da sauri Agaishat ta dubeta da kyau kafin ta matsa kusa da ita sosai ta ce" Subahannalah,

Ayya ta dawo da dubanta wajen Agaishat ta ce" na yi wasa da ke sosai, a yanzu ban san wani hali nake ciki ba,

Agaishat ta dora kanta gefen kafadar Ayya tana fan girgiza kanta, dan ita bata san me zata ce ba, a hankali ta ce" Ayyana, baki yi min komai ba, ba abinda kikai min, me ke damun ki?

Ayya ta ce" Agaishat, na farko haka ya zo ya shige tamkar wasan yara, yanzuma gashi an kara maki wani mai hargitsi,
 Agaisha, ni na haife shi da cikina, da aurwn soyaya, aman ni zan fadi dole matarsa ta yi hakurin zama da shi , shi din  mai rigima ne, shi din mai taryan rigima ne,
Tun yana yaro nake fama da hakan, gashi abu guda dai shi din bai iya son abu ba,
Agaishana, basu saurare ni ba, basu ysaya sun ji me nake da shi na cewa ba, ko ke abinda ke cikin ranki mahaifinsa ya yi jagorar daurin aurensa da ke,

Da sauri ta dago ta dubi Ayya, idannuwanta du ta ruko da mamaki da tsoro, aure? Da da Wardugu?

Ayya ta kawar da kanta daga dubanta ta ci gaba da fadin" Marahut, jira yake, hanyar da zamu raba abin kallo yake nema, bai jima da fita a gidannan ba, a gadarance ya kawo min jakarnan ta sadakinki ce, tabas gaskiya ne an daura aurenki da Wardugu bisa sadaki Cefa Millions Arba.in,

Kanta sai da ya sara dan dukan da maganar ta yi mata, a hankali ta silale ta dora kanta saman cinyar Ayya kafin take kawo hannunta na dama ta rukunkume cinyoyin Ayya,
Ji take zuciyarya zata balli gangar jikinta ta fito dan tsoro , shikenan, ta faru ta kare,

A hankali Ayya ke shafa kanta ta ci gaba da magana kamar haka" ba zan maki tilas ba Agaishat, duda a yarena namiji nada cikenken iko da matarsa, domin ko ni mahaifiyarsa ban isa na takura masa da lamarin matarsa ba, kin ga a yau a yanzu idan wardugu ya yi niyar wulakanci sai ya zo ya dauke ki ya tafi da ke tafia ta har abada ba wanda ya isa ya tanka shi, musuluncima ya bashi iko a kanki a yanzu, sai dai na sani ne, yana da dar a kaina, ko a al.adunmu na tubawa yana daga abubuwa da yawa idan dai ya shafe ni, idan kika ce ba zaki zauna da shi, in sha Allah zan ci karfinsa,
Sai dai zan so ki nutsu, ki fara duba na rayuwarki kanta, yarinya ce ke karama, idan ba muguwar kadara ba , ba zan so a ce an kama yi maki saki saki kina shiga hannun maza kina fita tamkar kwalo,
Zan so ki saurare ni, ki dauki dabi.u kyawawa, ki rungumi aurenki, zan so ki zowa rayuwarsa da sauyi, ina da kyakyawan zaton ke din zaki iya tankwasa shi kan wasu lamuran na yau da kulun,

Agaishana , *ina rokar ki da ki tsaya ki yi tunani ki ganni, idan har ba zaki cutu ba, ki amshi auren nan, in sha Allah zaki ji dadinsa*

Agaishat da ta yi lamo tana sauraron Ayya ta dan dago da kanta , jikinta har rawa fa yake ta ce" Ayya, Ayya, matarsa, Ayya shi din kansa, ya ji wannan abin? Ayya zai sumar da ni ne, Ayya ni din me? Ni a wa? Ayya matarsa.....

Ayya ta saki murmushi tana kara shafa kanta ta ce" *MATARSA* bani da wata damuwa da ita, du yanda ta ga zata kwaba tuwonta ta ci , tukunyarta ce, abinda na sani shi ne, Bama hada mata gida guda, komai talaucinka indai ka ce mace biyu zaka yi ko sama , to fa kowace gidanta daban,
Sai abu na gaba matarsa, ba ruwanki da ita, sannan koda wasa, ko da wasa kar na ji, kar na ga tsoronta a tare da ke, na me? Aa, ba zamanta zaki yi ba!
*SHI KUWA* baki da damuwa da hakan,

Daga nan Ayya ta yi shiru, bata kara mata haske a abinda take nufi ba,

Baiwar Allah ajiyar zuciya kawai take saukewa, bata da abin cewa , ta san zata je ne a kara sakota ta dawo, toh a sakota mana, an saketa a auren so ma bale na hadi? Nan baci ya aniya sandarta har ya dauketa, ita fa ta sakwa kanta dangana, abinda ta sani daya ne, bama zata ishe shi kallo ba bare har ya wani zauna da ita, ita fatantama kar ya karya mata kafa ko hannu dan haushin an aura masa ita ko ya jirkice mata kanta,

Jin ta dan kara nauyi ya saka Ayya dubata,
Tausayinta ne ya kama ta, ta san dama da wuya ta yi mata wani diban albarka, aman bata yi tunanin ko kuka ba zata yi ba, yarinyar na da hakuri, sannan da alama zata bata hadin kai su baiwa marada kunya,

Gyara mata kanta ta yi da kyau kafin ta kuna mata ac ta dauki jakar kudin ta fice,

Mai aikinta ta kirawo ta aiketa kasuwa dan karo mata itacen magarya, bata ga ta zama ba, yarinya da kishiya gashi da alama tsoron kishiyar take dan haka dole ta zagine, ga irin yanda Wardugu ya yi kundumbala ya ce yana sonta ai sai ta dagewa yarta!

Walyn ta ga rana, Wardugu ya ware mata dukan karfinsa sai da ya kai bata koda iya daga hannunta kafin ya mike,
Bai koma dakin ba, ky din mita kawai ya dauka sai computern aikinsa ya fita,

Motarsa ya shiga yana mai jin kyankyamin kansa ya dauki hanyar gidan Ayya inda gabansa ke dokawa yana tunanin yanda zasu karke da ita,

A lokacin da hancin motarsa ta shiga gidan ya tatara du wani tunani ya watsar kawai ya nufi falon,

Tsaftsaftsaf kamar koda yaushe,
Bai tsaya neman kowa ba ya shige dakin da mu.azam ke sauka ya cire kayansa ya shige bayin da ya tabata a tsaftace take ,

Tsarkake kansa ya yi kafin ya fito ya nufi wajen da kayan ke cikin dakin,
Tsaye ya yi yana duban kayan, anya kuwa zasu yi masa? Shi kuwa ba zai mayar da wadacen ba, da kyar ya lalubo wata jalabiya fara kar sabuwa ya saka ya caje kansa da kumb, ya dauki turare ya fesa sosai ya tsaya gaban mirror,
Sakayau yake jinsa, ya rage nauyi dan haka ya fito da niyar kira da wayar Ayya kan a kawo masa waya,

Dan dakatawa ya yi sakamakon hango Ayya da ya yi tana kallon wajen dakin, sai bayanta ita kuwa tana tsaye da alama wani abu ne a hannunta,
A ransa ya ayana , ya Allah, tana son saka doguwar rigar da ta dan dara gwuiwarta ko dan ta san tanai mata kyau ne?,

Ayya ce ta ce" Wardugu? Yaushe ka shigo ?

Tea din da ta sirba ne ya so sarketa inda ta samu da kyar ta hadiye shi tana zaro ido tana duban Ayya, ta kasa waiwayawa ta kasa zaune ta kasa tsaye sai rike cofin da ta yi da kyau tana jin zufa na neman karyo mata,

Ayya ta dubeta ta yi murmushi, ta ce" ehem, me ma kika ce? Ke dai ina wayarki ina wayarki?
Mu ci gaba.... ta fada tanai mata murmushi, domin tun da ta farka bayan magariba ta shiga rigimar ita ina wayarta ne wai? Ina aka kai mata wayarta ? Wa ya ga wayarta?

Salama ya yi kafin ya shiga yana duban yannayin Ayya,

Fuska sake ta amsa shi tana fadin" War, baci ba ka yi ?

Shi kam wata kunyarta ce ya ji ta lulube shi, dan haka ya zauna  saman kujera inda yake ta kokowa da idannuwansa kan su yi hakuri kar su dubeta,

Ayya ta kaleta ta ce" Agaishar kawowa yayanki ruwa,

Kamar jira take a kunnata ta juya da dan sauri ta shige kicin,
Sai da ta bacewa ganninsa kafin ya tataro dukan jarumtarsa ya gitse ya hade rai tamkar ba shi bane ya kare mata yaren Wayo Allah zuciyarsa,

Ayya ta dubi yannayinsa kafin take sakin murmushi, wato ita zai rufewa tabarmar kunya da hauka ko? Kunya ta ishe shi shine ya aro jarumtar wawa ya afkawa kansa,

Cikin wayewa ta datijuwar da ta san kanta ta ce" Wardugu zo nan,
Ta nuna kusa da ita sosai,

Wajen ya bi da ido, kafin ya mike ya koma ya zauna yana kakawar da kai,

Ayya ta ce" Wardugu, barkan mu ko?

Kunya ya ji ta kara dirar masa dan haka sai ya sada kansa, kafin ya dago a hankali ya ce" Ayyana, hakuri👏🏻

Ayya ta sakar masa murmushi kafin taa ce" me na ce ni? Ina cikin farin cikin hakan, sai dai me ka tanadarwa zaman y'ata a gidanka? Sannan wani gida zaka kaita? Ka san dai ba.a hada mata ko?

Wardugu ya yi tsai yana dubanta, shi kam yaya zai yi ya raba Ayya da maganar al.adun nan ne? Shi ya so ya hada su, a hankali yau da gobe wata rana zasu yi zumunci, aman yanzu an ce ya raba su,  yaushe Walyn zata yi hankali?

Ajiyar zuciya ya sauke bai ce komai kan lamarin ba, Ayya ta ci gaba" za.a yi biki kamar yanda ake yiwa kowace yar gata, za.a kai amarya kamar yanda ake kai kowace amarya, za.ai mata gyara , zaka yi bajinta irin namu domin da namu da nasun du kusan iri guda ne, Wardugu harta da garar namiji ban cire maka ba , sai ka yiwa y'ata,
Ta karashe tana gimtse fuska , daidai Agaishat ta dawo da ruwa cikin goran Awa da kofi na kwalba , abinda wardugu ya fada ne ya sakata jin ba dadi, duda ta san zata fuskanci hakan, Warsugu yana duban Ayya ya ce" aman Ayya , sai nake gannin kamar ranki a bace kuma kina dariya, Ayyana, Marahut ya daura auren nan, kin ga kuwa tilas na yi masa biyaya,.....

A hankali ta karasa ta ajiye ruwan ba tare da ta tsiyaya ba ta juya zata fice a dakin ta je tsakar gida ko zata ji iskar Allah ta ratsa hancinta yanda ya dace,

*KE*, shi ne abinda ya daki kunnenta da kakausar murya,
Wa zai cewa ke a wajen da daga ita sai Ayya sai shi?
Dakatawa ta yi, a kasan zuciyarya kuwa fadi take, walahi da wani gaulan ne sai na bala masa harara wai wani ke, aman ba komai ba komai😕,

*Ki je dakin ki* , ya fada yana kawar da kansa daga dubanta inda ya ji ransa ya baci a tsakar ransa,

A hankali ta juya ta haye sama ta nufi dakinta,

Dubansa ya maido wajen Ayya ya ce" Ayya, ya zaki bari yarinyar nan tana yawo haka ne tsakani da Allah? Idan da kin ce igiyar wa ke kanta yanzu fa? Ayya, gidannan da maza fa, ga masu gadi, ga sojoji, ga direba, Haba Ayya,

Ayya ta hade fuska ta ce" toh ubanna, nace toh ubanna kawo min duka,

Dan yatsanta ta nuna masa ta ce" Wardugu ka kiyaye ni, bilahilazi na fika ciyayi, kai ku ji kin yaro da rainin hankali, ka je ka gindaya mata dokar mana dan raini ka sakani gaba bayan ka gama raina min wayo da maganar wai ka yiwa Marahut biyaya ka korar min y'a, sannan ka rufe ni da fada? Sauran duka sai na gane ba za.a iya taroka ba!

Habarsa ya dafe kawai yana dubanta, sai da ta gama fadan ya mike ya shiga haurawa saman dakin Agaishat din inda Ayya ta mike da sauri ta bi bayansa,

Gannin tana biye da shi ya saka ya haye da sauri ya shige dakin ya rufe,

Zaune take tana cila yan kafafunta saman kujera, ita bata wani saka abin a ranta ba, sai tsagal ta ga mutun a gabanta,

Fuskarsa ce ta kayar mata da gaba, inda ya nemi waje ya rike a jikin hannunta , kausasa muryarsa ya yi ya ce" ba sai na rantse maki ba, ki yarda ko aa, daga yanzu du wani katon da ya ga fuskarki dukanta wanda ba muharaminki ba , sai na kwakwalo idannuwansa  na soya maki kin ci!
Ya zaki ringa fita da irin wannan shigar kowani gaula na gannin ki? Ke kin san me zai raya a ransa a kanki? Ya yarinya karama da ke tun da kika shigo rayuwana zaki ringa zigani uwa shayi? *KE* ya fada yana nunota da dayan hannun nasa wato da yatsarsa manuniya sannan sai a lokacin ya hada idannuwansa da nata,

Gaba daya ya ji ana janye iskar tashin hankalin da ya zo a yi daga jikinsa, fuskarta ta marairaice ta zama tamkar ta jariri, dan bakinta ta dan bude shi inda hakoranta na gaba kwaya biyu da suke da dan tsayi kadan ruwan na zomo suka dan leko haka kuma ana gannin na kasan jere reras fari kal da su suna dan shekin abin yawun bakinta,
Idannuwanta tar cikin nasa, sun dan canza kala daga fari kar zuwa orang kadan alamun suna

daf da cika da kwala,
Dan girgizatan da ya yi ya saka gashin kanta dan hautsinewa suka bazo gaba kadan,
Kallon cikin idon da take masa, tafe yake da sakon ka ji tausayina, kar ka ilata ni👏🏻,

A hankali ya shiga sasauta mugun rikon da ya yi mata, tsayinsa ya rage kafin yake lumshe idannuwansa,
Abinda ke kara tarwatsa tunaninta ya yi mata, wato janyota ya yi a hankali ya rungumeta tsam a jikinsa inda idannuwansa ke lumshe yana daidaita bugun zuciyarsa tare da neman tayimakon Allah kan kar ta ci karfinsa😒,

A hankali ya ce" *ki daina fita a haka, kin dai san yanzu mijinki ne ni ko? Walahi idan kika ki bin magana na, Allah zai toya ki, ni kuwa in dai kan fita ba lulubi ne ba zan iya yafe maki ba, dan ina iya aikata aikin dana sani ORRONUR*......

TO KU BANI KIDAN COMMENT A SAMA...........

NVL YA KUSA KAREWA, ALLAHU YA NUNA MANA KARSHENSA LAFIA

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

7️⃣9️⃣

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA*  in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

Sowie yau kadan ne😔😔😔😔😔😔😔😔

*Mijinki ne ni ko?* shi ne kalmar da ta fi kara sakata wani yannayi na firgici da shiga wani irin hali,
Kennan ya ji, ya sani, harma ya kirayi kansa da kalmar *MIJI* a gareta, wannan gayen mai tsada?
Idannuwanta ta lumshe ta kara shiga kirjinsa dan walahi kamshinsa daban ne, duda na yau ba irin na kulun bane aman na yau dinma wani silent kanshi ne,
A hankali take kara shigar da hancinta wajen botiran jalabiyar tana shakar kanshin, tana mai jin duniyarta ta kawata,

Shima dake rungume da ita caji kawai yake dauka, a hankali ya dora hancinsa saman gashin kanta, kamshin daban ne, kamshin mai ni.ima ne, mai sanyi ne, a hankali ya dora hannunsa wajen tsatsonta daga baya ya dan rike kadan kafin ya ce" *UM*?

Agaishat da ta hadiyi yawu da kyar , ta dan cire hancinta daga wajen kirjin masa , idannuwanta ta dan dago ta ce" *Um?*

Wardugu ya tsura mata ido shima yana dubanta, a ransa kuwa fadi yake....yanzu haka ya je wajenta? Haka ya ratsa min ita? Haka ya taba min jikinta? Har fadi min yake ni.imarta? Ya Allah😔,
A fili kuwa ya ce" baki ce komai ba, bayan na budi baki na yi ta maki zubar da bana yi!

Agaishat ta mayar da kanta saman kirjinsa dan walahi ita bata so ya janyeta a yanzun kam, a hankali ta ce" ni tsoro nake ji,

Wardugu  ya yi jim tamkar ba zai tankata ba kafin ya ce" tsoro? Na me?

Agaishat ta yatsina fuska kafin ta ce" idan ranka ya bace, idan kana fada, tsoro nake ji, dan Allah idan na bata maka rai kar ka yi min duka ka ji? Ba zan kara fita a haka ba, dan Allah kar ka min mugun duka walahi ba laifina bane,

Ta karashe tana lumshe idannuwanta tana jin yanda zuciyarta ke dokawa,

Bai so ta yi shiru da magana ba, buzancinta na tafia da imaninsa, ta iya karya harshenta da fadin RRRRRRRRRRrrrrrrrr sannan tana magana tana lumshe idannuwanta ne, sannan lebenta na wani marmarmar gashi sam baya rabuwa da man lebe,
Dan haka Wardugu ya ce" *Laifin me kika yi?*

ya tambayeta a hankali ,
Dan haka ta dago da kanta ta kure shi da kallo, yanda fuskarsa ke fitar da wani yannayi mai fuzga, idannuwansa kuwa a limshe suke, dan haka tana duban nasa bata san da shima ita yake kallo ba ta dan yatsina fuska ta ce" na aura maka ni da ya yi,,

Bude idannuwansa ya yi gaba daya bisanta, hakan ya sa ita ta kawar da dubanta a kansa,
Janyeta ya yi kadan daga jikinsa dan lamarin ya fara karkata baya so ko daya ta gane shi,
A hankali ya karasa da ita bakin bed dinta ya zaunar da ita ,
Wani tsadaden murmushi ya yi mata kafin ya daga kafadarsa ya ce" zan yi tunani.......

Tana zaune ya juya ua je ya bude dakin , burum Ayya ta shigo tana dubansa tana duban Agaishat,
Bata ga wani yannayi na firgici ko tsoro a tatare da ita ba, haka shima bata ga wani bacin rai a tatare da shi ba, hasalima rabawa ya yi gefenta ya fice a dakin,

Ayya ta karasa inda take zaune tana dubanta,

Agaishat ta dago da murmushi mai sauti ta dubi Ayya ta ce" Ayyana, bai dakeni ba, Ayya wai menene ma.anar *ORRONUR*

Ayya ta zaro idannuwanta da yanayin mamaki karara a fuskarta,
Kawar da kanta ta yi tana boye murnarta, da fushi ya shigo dakin, aman ya fita wasai....shi ne abinda ya fi tsaye mata a rai, Alhamdulilah... shi ne abinda ta fada, sai ga wayarta na kuka,

Kanta ta dan dafe ta dana ta mikawa Agaishat ta juya bata bata amsar tambayarta ba, yo ita me zata ce mata? Kai gaskiya da nauyi.

Agaishat ta kara wayar a kunnenta, nan Alhinayett t saka ihun murna daga zaune fadi take" Agaishat, ina yake? Yana ina? Tun da na ji labarin nake doka wayoyinsa aman gaba daya a kashe, takima a kashe, wayo Allahna dan Allah bani labari dala dala tawan, fada mini yanda aka yi lamarin, ya furta? Ya fada ne?

Agaishat ta rafka tagumi tana sauraron Alhinayett kafin ta ce" wai an furta me? Waye zai furtan?

Alhinayett ta ce" wahala ne zaki bani dan kin san ba zan iya fitowa yau ba ko? Ki fada min ta yayane ya furta? Wayo ni baku tashi soyewar ba sai da aka shige daka da ni?

Agaishat kam du ta sakata cikin duhu, wai soyewa, wai ya furta? Murmushi kawai ta yi ta mata gum kan itama bata san da auren ba sai dazu Ayya ta shigo ta fada mata,
Alhinayett ta jinjina lamarin, ta fada mata in sha Allah da ta fara zuwa aiki zata roli alfarmar ta zo gidan, tana da magama da ita, sannan ta buda wayarta....

Haka dai suka yi salama , inda Agaishat ta yi tsai da wayar a hannunta, magangannun take kara bita tamkar karatu,
Guguwarsa bai hana shi zama special a wannan fannin ba,

Aa, ita da ba auren soyaya bane tana jin duniyarta sabuwa a cikin kirjinsa to ina ga matarsa?
Ya Allah dole ta yi kishin abinta, dole ta ji ba dadi,
Wani tausayinta ne ya dirar mata da tunanin magangannunta na asibiti,
To ko dai tun a lokacin aka ce za.a yi masu aure? Ko me fushi Walyn ke nufi a lokacin?

Kafadunta ta daga tana fadin" damanfa ba kaunana take ba, ba fadan wannan take ba, me yiwuwa na mata wani abin ne dan ni banma san me take fada a fadan nata ba🤷🏻‍♀️,

Ya jima tsaye kofar gidan nasa,
Ba wata anguwar manyan masu kudi bace , aman anguwar sai ka shigeta zaka ringa cin karo da gidaje na alfahari,
A boye take , gashi a bakin gari take, bai jima da gama gine gine a anguwar ba, inda tuni an fara kama hayar gidajen,

Tankamemiyar vila din da daman can ya ginata ne dominsa ya danna horn inda mai gadi ya bude masa dan ya san shi ne kawai mai zuwa,

Gidan du shukoki ne an yi tsari da su an masu kwaliya waje waje, sai wajen ajiyar motoci can kasan wata runfa,
Kana shiga zaka ga kanka a ciki, ko.ina madubi ne gaka tun daga kanka har kafarka,
A hankali ya sauka inda yaronsa ya dauko jakar da ya zo da ita yana biye da shi har suka sadu da accenseur din gidan ,
Shiga ya yi ya dana number etage hawa na shida wanda yake na karshe inda dakinsa yake,
Su ya ajiye su suka sauka, sai da ya kai masa jakar har kofar dakinsa sannan ya juya ya tafi,

Panneau  solaire ne le aiki a gaba daya gidan, sai katon inji irin na ma.aikata dake boye nesa da dakunnan dan zafinsa ko kara kar ya damu kowa,

A hankali ya shiga da adu.a, dan bai taba zuwa ya kwana gidan ba,

Dakunnan dake bangaren nasa ya leleka, komai ya yi masa kamar yanda tsarin rayiwarsa yake, mutun mai son farin abu, sai dan maroon da aka sirka dan kar farin ya yi yawa,

Dawowa ya yi  dakin da ya fi girma wanda shi ne dakin bacinsa ya shiga ya bude wajen kakinsa, domin a gidan nan abinda babu kawai mutane ne, mutanenma masu gidan, dan kuwa du abin bukatarsa ya saka, sannan gidan a boye yake bayi niyar zama cikinsa kwana kusa ba, kai shi ya yi niyar ya ringa sauke mutanensa idan zasu yi baban meeting da sojoji na harkar aikinsa dai da sauransu, ya so gidan ya zama na sirri, aman baki daya walyn ta fitar masa da wancen gidan a ransa, baya jin zai kuma rayuwa cikinsa domin ta fitine shi a gidan nan,
Ya yi masa tsarin da zasu rayu tamkar soyayar fari, tsaftataciyar soyaya sai dai bata zauna bama bale ta gina hakan ,
Wannan gidan ya yi shi da wani irin gini ne mai dakuna barkatai, sannan du wani bangare akoy hanyar da zata sadaka da bangarensa, inda maduban bangarensa bulet ba zai ratsa su ba,
Kai an fa zuba nema a gidan dake anguwar da ba wanda zai hasaso irin gida tamfatsetse haka a wajen  ba wato *AEROPORT*,

Sai da ya gama uzuririkansa, kafin ya zauna ya hada wayoyin da ya shigo da su da layikansa ya jona ya haye saman bed dinsa domin zuwa lokacin dare ya yi sosai,

*idan kana fada, tsoro nake ji, dan Allah ka daina*, shine abinda ya fado masa, na daina fada?
Ya fada , to ni mafadaci ne ?
(Fans wardugu ya ce wai shi mafadaci ne ?)

Haka ya juya ya kuma juyowa yana duban memory card dinsa, wace a cikinta akoy hotonta da ta juya da niyar zuwa wajen zama a wajen diner Alhinayett,

Alhinayett, sai da ya ambaci sunnan ta fado masa a rai, aminiya, na san kin neme ni,

Kwonciya ya yi da tunanin a gobe gobe ba sai an kai nesa ba zai yiwa Ayya dukan abinda ta bukata a kawo yarinyar nan kowama ya huta, domin duda tace ba zata fita haka ba, shi kam ta dawo kusa ya fi,

Idannuwansa ya lumshe, yanda da ya rungumeta ta kwonta a jikinsa ya fado masa a rai, Mikewa ya yi yana tsaki, a kasan zuciyarsa ya furta ba dole ba ita da ta taba aure! Malama ki bar min rayuwa na huta hakannan!

Haushin kansa yake ji irin yanda ya zauna tunanin wannan yar yarinyar! Dan haka ya mike ya saka kakinsa na aiki, ya dauki karamar wayar da ya saka layinsa na aiki ya yi kiran commisariar da ta fi kusa da gidansa ya tambaya wa.inda suka fito raful da hanyar da suka bi,

Haka ya fito a katon babut dinsa dake gidan ya tarbe su, daya daga cikinsu ya sauka ya dauki babur din dan kai shi ma.aikata su kuwa suka shiga bin anguwa anguwa sunna kama du wani mai laifi, da wanda ya cika dare kuma bashi da takarda, inda su ne har su plastomo, su rond poind 6em, du wani lungu na yan duniyar da basu da damar zama wajen sai da suka durfafa aka riga tserere da sojojin da masu laifi......

Chaina

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

8️⃣0️⃣

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA*  in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

Tunda Gukunni ya fara bata labarin abubuwan da suka faru ita da jikokinsa wato yayan Anna kuma yayun Agaishat daidai lokacin da aka tafi massage din jikin Anna wace yanzu sosai jikin da sauki , suke dubansa da mamaki,
Dama akoy mutane irin haka?
Anmi, wato mahaifiyar Anna ta ce" wai kana nufin , Wardugugu dai general Wardugu ne ya auri Agaishat din,? Kuma ka ganta da idonka?

Gukunni ya yi murmushi ya ce" a irin halin da na ganta, ko mu iya walwalar da zamu iya bata kennan,

Fatimata ta ce" wai wai wai rayuwa, yanzu Agaishanmu ce ta yi aure har ya rabu har ta kara samun wani da gagawa haka? Ku a birni ba ruwanku da kalar fatar mutun kennan?

Gukunni ya ce" wanninma da ta samu ko a cikin mutanen baban mutun ne, ba kun ga sojan da ya je tare da mahaifiyar tasa ba? Uwar rikon Agaishat din?

Gaishat ta zaro ido ta ce" eh eh, wani irin mutun mai cika waje da ido, tunda aka je da shi bai cika magana ba aman idan ya dago ya yiwa mutun duba daya sai ka nemi kallon me ya yi maka ka kimtsa zamanka,

Gukunni ya saki murmushi ya ce" to ko a ma.aikata haka yake, shi dai ne ya biya sadakin auren Agaishat million Arba.in!

Gaba dayansu sun girgiza, sun ji dadin lamarin kuma sun kara yarda Allahn da ya yi bawa, shi ya san me ya kunshe tatare da shi, Wai Agaishat dai Agaishat, itace haka ya sameta, abun alkhairi da kaf timiya ba.a taba kawowa wata y'a haka ba, kai ko a cikin agadez sai yayan sarke ke samun haka,

Anmi ta ce" damuwana daya, ka ce bai jima da aure ba , kuma matarma batuba ce, fatan dai ya isa da gidansa, yana iya sakawa ko hanawa,

Gukunni ya girgiza kansa kafin ya ce" ban ce ba idan baya nan,
Idan kuwa baya nan ita jikar taki idan ta zauna kishiya ta cin mata ita ta gano,
Maganar idan yana nan da nake maki, ni na ga a idon jarumin ba lale ne ya yarda kuda ya taba fatar jikinta ba,
Zai iya da su!

Ai kuwa Mariama ta mike ta aniya kada harshenta ta rangada budar buzaye, inda Anmi ta yi gagawar tarota tana tina mata asibiti suke fa, kar a zo a yi waje da su,
Mariama kuwa dariya kawai take, ta zauna tana duban yan uwanta ta ce" ban taba sannin inada kaka mai kudi ba, da yan timiya sun gayawa yan garinsu! Ban taba sannin Bakar Anna zata yi

kudin aure ba , da na koya mata fito na fito!
Yanzu ko yaya? Ko ta bar rabewar idan an tabata? Ko ta bar lafewa ta dora kanta inda ta samu ta yi hawaye? Ko ta gane Allah kawai zata kaiwa kukanta, du ubanda ya tarota ta taro shi?

Gaishata ta kai hannunta ta buge bakin Mariama kafin ta girgiza kanta ta ce" Allah ya shirye ki, gwarama wannan likitan dake bibiyarki a bashi mu tataraki mu bar masa a nan mu daga abinmu dan har yanzu baki shiryu ba,

Wai wa? Fahad? Baki ga zama cikin yan chaina ba shima tsayinsa da idannuwansa ne kawai basu koma irin nasu ba? Wata shegiyar kunya  dazu fa da muka hadu wajen cin abinci kinga yanda yake hade hannu yana gaishe ni?

Fatimata da haushi ya gama tirniketa ta dubi Gukunni dake kallonsu da sha.awa ta ce" Papou, ka yiwa yarinyar nan magana, idan tana abu kamar itace Agaishat karamarmu, wai kawai dan yace da ita yana sonta abinda ta fara ce masa zai iya soyaya da shegiya? Wai ita bata da uba,

Gaba daya suka kai dubansu kanta, inda itama su take kallo,
Kanta ta girgiza kafin ta ce" menene? Karya na yi? Ni fa ban iya karya ba, kuma ganninsa na yi ya hade karshen haduwa, zan cuci kaina ne? Dan Nigeria ne, wai iyayensa suna zaune a abuja, shima nan ya yi karatun likitanci da ya gama ya yi zamansa nan yake kara koyon aiki tare da kwararu likitoci, gani na yi daga haduwa da shi ya bani cikenken ko waye shi, shine nima na bashi nawa asalin ko?

Anmi da suke kira da Mamou, ta girgiza kai kawai ta mike ta bar dakin, ita kam bata ga ta ibda za.a daidaita halayan Mariama ba, irin halayen Gukunni ne da ita, tamkar itace yar batuben, sam bata da dar ko shayi, magaifiyarta kawai take tsoron kallo cikin ido ta fadiwa magana, itama ta ci karfinta ta hanyar shareta da yi mata wa.azin girman darajar iyaye.

Gukunni kam sai da ya dan shafa habarsa yana dubanta kafin ya girgiza kansa shima ya ce" kin kyauta, kuma sai na hada ki da Annarki! (Ba ka ji ba, ba zai ga wani girman laifinta ba, domin shima halayarsa kennan🤣),

A wannan ranar da likita ya zo ya fada masu zasu iya kowani yama su fitar da ita ta dan rawata kadan kadan,  sannan a ci gaba da kwontar mata da hankali, a yawaita saka mata abinda zai sakawa ranta dangana, idan musulmai ne su yawaita kusantata da wa.azizika, da astaghfari, su nuna mata girman kadara, su nuna mata ba kowa Allah ke jarabta ba👏🏻,
Idan har ta nutsu nan da satima zasu iya salamarsu...

Ai kuwa sun ji dadi sosai, inda Herde sai a lokacin ta tatara ta koma tare da Fatimata da dan gidan Gaishata wato Sultan wanda take jin yaron har bargonta, shima ya wani shaku da ita du motsinsa yana makale da ita.

Soyaya kuwa ta dinke da Mariama da Fahad, inda ya hadata da familynsa a vidio call suka

gaisa da yar hausarta da bata taka kara ta karya ba, dan kuwa french dinma ba wani sosai take ji ba, buzanci ne shi kuwa ba yarensa ba, soyayar dai ana yinta ne karfi da yaji domin wani sa.in sai a rasa ta yanda za.a isar da sakon khalb.

Niger

Da gaske yake, ko nace da gaske suke,
Abu ne ake tamkar ba gobe,
Dukan bukatun Ayya kan lamarin tarewar yarta an cika mata, inda ake shan rigimar shi ba za.a yi wani taron diner ba, kawai a yi saukar alkur.ani, Ayya kuwa tace ai ko walima ne sai ta yi ta gayaci mutanenta an yi taro na kirki itama ta aurar da yarta,
Ido ya kawo ya zuba , yama maida hankalinsa kan aikinsa wanda kulun cikuluftu ke karuwa,

Ayya kam ba kama hannun yaro, wani irin shiri take yiwa yarta wanda siri ne,
Ya kasance  ko masu aiki basa gannin Agaishat a dakin da ta kilaceta, daga ita sai ita,
Du a tunanin Ayya y'artata ta saan aure, hakan ya sa take wani irin shiryata dan ko ba komai ta iya zama a gidanta, kar a rainata ta wannan fannin,
Sosai ta bata magannin infection, kafin ta shiga bata lakaninika ciki harda yusufa da kankanna,
Kwata kwata ta haneta shan ruwan sanyi, inda take dumamata da masu dan dumi ,
Haka indai jikinta ya ji iska tofa wanka ta shiga, tana fitowa take maida lulubinta ta lulube, dalilin haka har yan kurajen zafi ta yi, suka mutu dan kansu jikinta ya saba ya kasance koda yaushe cikin dumi yake,

A kulun zai yi zuwa biyu gidan, yakan bi Ayya da kallo ne, tun lokacin da ta masa iyaka da tambayarta Agaishat, ya kawo ido ya zuba mata, wai tana gyarata, har sai da ya ce"Ayya, ni guaran na menene? Me kike gyarawa ne?
Ta yi masa shiru ta kawar da kanta, dan ba za.a ja maganar da ita ba, idan shi bashi da kunya ita kam tana da ita
Shi kuwa daga shi ya yi shiru ya daina tambayarta ita, kuma abinda ke bashi mamaki ko wulginta da baya gani, ya dai san lokaci ta deba, kuma saura kwana uku, hakan ya saka ya kawo ido ya zuba mata,

Yau sauran kwana daya kacal tarewar Agaishat,
Kowa ya dauka kan tarewa ne, dan ta taba aure,
Jama.a da yawa na mamakin wannan aure , General ya auri bazawara? Ayar tambaya, wa.inda suka san matar da amininsa Mu.azam ya saka ce kuwa suna yayata maganar daidai da mandan bakinsu,

Wardugu, bai san irin halin da zai kwatanta yake ciki ba, ga aiki da ya sako shi gaba domin ana yawan kawo hare hare yankin Diffa, tsaye kan kafafunsa , dan haka ya kara neman alfarmar kar a yi maganar diner, gannin halin da ake ciki ya saka Ayya amincewa , aman hakan ba zai hanata yin nata taron ba,

An kawo garar amarya da akwatuna,
Zama zanowa bata lokaci ne, Wardugu ya kashe kudi sosai, kaya kuwa an zuma na yar gata,

Agaishat kan fashewa da kuka wani lokacin , kukan murna, kukan godiya ga Allah, tana jin Ayya har kasan zuciyarta, girman Ayya daban ne, tana sonta so irin na da da uwa,
Saima idan ta zauna tana tuna hirarsu ta yau bayan salar asuba, yau da ya kasance za.a mikata dakinta, gidan mijinta, wanda take fatan sai dai a fitar da gawarta, Ayya ta dubeta ta ce" zan so biyayarki, tsoron Allahnki, ya kasance bayan zuciyarsa da kika shiga, ki shiga kowani motsi nasa,
Agaishat, ban hore ki da rashin kunya ba, ban hore ki da tsayaya ga miji ba,
Agaishat, shin wanda aljanarki take karkashin kafarsa wani irin motsi zaki yi dan gannin ya dage kafar nan tasa ya baki damar shigewa?
Ki yi masa biyaya,
Ki barshi ya fada,
Idan ya daga murya ki kaskantar da kanki,
Kar ki yarda yana fada kina fada Agaishat, da haka gwara ki yi nesa da shi! Ban ce ki zauna ya wulakanta ki ba fa, ko daya, ina dai doraki kan hanyar da zata kai ki ga ci ne,
Kin ga kar ki yarda daga saman salayarki ki sauka da asuba ba tare da kin furta kwali a kwayar idannuwanki ba, ki adana kwalin ki kusa da abin salar ki!
Kar ki haye gadon da kika gyara dominsa kafin shi ya hau (ina kuke ne mutanenmu , iyayen mu🤣, gafa wajen🤣),
Idan ya yo dare, ki kasance mai jiransa , kar ki je ki jibge saman gado, har ya zo ya gama abinda zai yi kina minshari (😅 kin ji ko maniu🤣🤣),
A duk lokacin da kika ga da hali, akoy robar wankin kafa, akoy dutsi, ki zauna a yar kujera ki saka kafarsa ki wanke, ba dan ta yi dati ba, sai dan kara shakuwa tsakaninku koda kuwa bai saba gani ba, kar ki wani damu ke dai ki koya masa irin zamanki da kike so ku yi,
Akoy wahala fa, domin kuwa ba ke ya fara aura ba, ba ke kika fara rainonsa ba, zaki ga abubuwa da yawa wanda haka matarsa ta hore shi da su, wasun zasu canzu cikin hikima da juriya da hakuri, wasun kuwa Agaishat sai dai ki rayu da shi a haka!

Sai maganar kananun kaya,
Ina mamakin zamani, ina mamakin yayi,
Wai idan za.aiwa yarinya aure da budurwar da bazawarar da datijuwar sai ki ga ta kama kwasar kananun kaya , kananun kaya ita dai,
Uhum, kuskure baba,
Ke Agaishat shin sex din ne kawai ya kai ki gidan auren? Tabas shi ne jigo, shi ne farkon gini, aman shi din an gaya maki zama kusan tsirara a kulun ne zai saka shi armashi?
To albishirinki, walahi ni na fada maki, du abinda ya kasance shi kulun a fili a bude yake komai darajarsa a hankali take raguwa har ya kasance ta bace bat!
Shigar kananun kaya, akoy lokaci, ba ina nufin kowani dare ba, no , aa, lala!
Ki sayi masu tsari, masu ma.ana , masu kai,
Masu taushi!
A cikin gidanki Agaishat, ki kasance cikin shiga ta kamala, ki ringa yawan yi masa rowar

ganninki gaba dayanki arha,
Agaishat, ki ringa saka riga da zani da dan kwalinki, ki yi sasaukar kwaliyarki sannan ki zauna cikin kanshi,
Ki ringa saka sket da rigarki na atamfa, ki ringa saka doguwar rigarki au ta atamfa ko abayoyinki, ki ringa nada saharinki, ki ringa hawan lesh da shadarki kina zamanki, ke wani lokaci ki yi sasaukan shiri abinki,
Ki ringa daukan lokaci kafin ki yi masa shiri na kananun kayan, ya kasance a ranar yana kusa, ki saka abinki , ki juya a gabansa,..... Agaishat zaki baiwa wani labarin mahinmancin hakan, mijinki zai kasance yana mai jin zumudin riskar ranar da zaki hade masa cikin shirin nan, sannan koda lokacin da zai ziyarce ki ne, zaki ga zai warewa wannan lamari mahinmancin da za yana nuna maki, ( iyayen mu, na zaunar da mu ne, su yi mana huduba, fila fila, shin da wada take yarena ta tabatar? )

Sosai Ayya ta yiwa Agaishat nasiha, gargadi, ta ankarar da ita zaman duniya, dama hasashen na auren da take, kafin ta nanata mata maganar cewa *AGAISHAT* ,tabas kyau, fari, mulki, arziki, na jan soyaya,
Sai dai ki sani *ZUCIYA NA SON MAI KYAUTATA MATA* ,
Wannan kalma kuwa , ta tsaye mata a rai kamar yanda sauran suka tsaye mata,

Haka aka wuni shagulgula kamar ba gobe,
Sosai Ayya ta gayaci mata, mata kuwa sun amsa kira, inda aka wuni ana tafiar da taron yan gayu,

Kai amarya, ba.a tashi shirin amarya bama sai wajen karfe goma na dare,
Ayya ce da kanta ke darwaye yarta, kafin ta mulketa da turaren Angel,
Haka ta zaunar da ita ta saka mata kwali kadai a idannuwanta kafin ta damka mata shi a hannunta,
Wata arniyar Lafaya ce ta nada mata saman lafiyayiyar doguwar rigarta ta atamfa mai ruwan ja da fari kar,
Ba.a saka mata dan kune ko awarwaro ba, takalmin kafarta kansa wani plat ne,

Dirar motoci suke ji , tun suna hasashen za.a dakata abin gaba kawai yake,

Labule Alhinayet dake tsaye cikin shigar wata dakakiyar shada ta daga,
Gaba daya sai da tsigar jikinta ta tashi,
Hasbunalahu wani.imal wakim,
Shi ne abinda ta furta a lokacin da ta hango motoci layi biyu, kowace tana kilyoten yan wutocin gaba, kowace da soja tsaye a kusa da ita,
Sun layu gaba dayansu suna ta tafi ana shakiyanci irin na sojoji a cikin yannayin farin ciki,

Ta tsakiyarsu yake ratsowa a lokacin da Alhinayett ta hango shi ta saki wata buda tana kada harshenta ta shiga kwasar shoki,
Wato wani irin shirya daukan amarya ne aka yi wanda sai wanda ya gani,

Haka Ayya ta kamo hannun Agaishat dake ta hawaye tana jin wani irin lamarin a jikinta wanda bata taba ji ba a aurenta na farko,
Ya Allah, ya Allah,
Ayya na fitowa da ita daga dakin nayake ainayin nata aka shiga guda ana zuba mata kudi,
Ayya ta riketa da kyau suka shiga saukowa daga matatakala inda ta shiga neman aminiyarta dan ta mika Agaishat dakin mijinta,

Tsakiya suka saka Agaishat suna tarairayota,
Alhinayet kam har jikinta rawa yake , domin gaba daya wajen fa ba dama, muryar sojoji ne suna fadin"Hei Hei Hei Hei,
Inda Wardugu ke takowa a kafarsa, jikinsa sanye da kakin soja marroon , wandon da kadan ya zarce kaurinsa sannan ya rike shi daga kasa, rigar kuwa baka ce jikinsa aman bai sakata cikin wandon ba , janta ya yi ya dorata saman yar karamar bindigar dake tsatsonsa, sai ranjes maroon waro takalmin sojoji, rigar mai karamin hannu ce , hakan ya sa damatsunansa du a waje,
Du taku da zai yi sai kura hei tun karfinsu murya irin ta garada, sannan su yi wata yar rawa da kafarsu ta dama baki dayansu a haka har ya karaso wajen yan matatakalar da zai taka ya hau kafin ya shige dakin Ayya , aman sai ya ja ya tsaya,

Daidai nan su Ayya aka bude masu suka fito da amarya,

Gaba daya wajen ya kwashi wani busa na sojoji kafin a karashe da fadin *GENERAL HEI GENERAL HEI*

Tsura masu ido ya yi daga inda yake,
A hankali ya dora kafarsa ta hagu saman abin takawar na fari, kafin ya lankwashe kafar ya kasance gwuiwar kafar tasa ta hagun a kasa, sannan ya matso da ta damar saman na gaban ya dorata, ya yi irin taugunon nan da maza suke yi dan tambayar hannun budurwarsu (kasar larabawa da turawa),
Wani irin ihu wajen ya dauka a lokacin da ya mika hannayensa baki daya kan a bashi, ya zo a bashi...........

To fans saura kiris bilahi😔😔😔😔😔

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

81

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA* in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

Dakatawa Ayya ta yi, kafin ta dubi tarin jama.ar,
Dubanta ta kai wajen mutanen da suka wunnin mata sannan ta kara duban yan matan dake wajen wato kannen Alhinayett da aka wuni da su,
A hankali ta yafito Alhinayett, ta karaso inda ta yi mata radar du rintsi a sada Agaishat dakinta da ita,

Ai kuwa Alhinayett ta amsa, kafin Ayya ta kama hannayen Alhinayett ta karasa kusa da Wardugu,
Hannunta na dama mai dauke da jan kunshi dan kadan ba mai yawa ba ta dora saman nasa na dama kafin a hankali ta ce" ka riketa mudin ranka War....,

Wardugu ya rike hannun da kyai inda ya kai dubansa da kyau domin jin wani laushi da hannun ya kara kan nasa na da, dubansa ya kai wajen mahaifiyarsa a hankali ya furta" Allah ya tabatar maki da shiga aljannah,

Aminiyarta da Alhinayett da Agaishat kawai suka ji, dan haka suka amsa kowane daga

bangarensa, inda ya mike a hankali ya karasa hawa ya matsota jikinsa ,
A fakaice ya duba irin daurin lafayar da akai mata, aa yau sun yi abin kansu, an yi mata daurinnan na saman kirji wanda baya nuna surar mutun, dan haka ya sauke ajiyar zuciya ya sakali hannunta da kyau inda ya zame mata jagora yana takawa a hankali tana bin sahunsa ,
Sojojin gaba daya bindigoginsu suka daga sama kafin daya daga cikinsu da ya fi murya ya ce"REPOS!
Gaba daya suka sauke

A hankali suke takawa, inda Alhinayett ke bayansu, sai yan matan suma suka rufa masu baya , sai iyayen da zasu rakata domin fir Ayya ta ki ta saketa haka kawai,,

Motar da zata kaisu ce ta karaso ta tsakiyar sojojin, nan Wardugu ya bude ya sakata gefen dama kafin ya zagaya ya shige gefen hagu,
Mu.azam,
Shi ne abunfa Wardugu ya fada a lokacin da ya ga Mu.azam ne zai tuka su,
Mu.azam ya tsare shi da ido ta jikin madubin hakan ya sa ya yi shiru ya zauna da kyau yana duban yanda kowa ya je ya shiga mota suka dauki hanya,

Shiru ne ya ratsa motar, inda gabanta ke dukan tara tara, me? Mu.azam? Shi ne zai kaita dakin miji? Lale Mu.azam, kai itafa har yanzu bata san komai ba, kuma bata da niyar sani!
Haka dai ta yi shiru har lokacin da Wayar Wardugu ta dauki tsuwa,
Dagawa ya yi ya kara a kunnensa,
Ai kuwa a dake ya ce" ka gane, abu daya za.a yi da su su dan daidaita halayensu, dangina ne na san meye zuciyarsa, du wanda ya kashe ka saka bakin bindiga ka harbe shi a tsakiyar ido! Du wanda ya jigata wani, ka jigata shi, hakan zai sa su daina fadan da zasu jiwa junansu har a kawo su asibiti,
Ku kennan haka zaku kare? Kulun kuna fama da rabiyar fadan cikin kasa bayan ga wanda ya adabi duniya? Ba so suke su kare ba? Zan kuwa karar da su!

Shiru ya yi kafin ya daga murya ya ce" commandan kana da ja ne?,
Amsa aka bashi kafin ya ce" ohk, ni na ce, a zartar!

Kit ya kashe kiran yana kokarin ajiye wayar sukai ido hudu,
Tsakaninsa da Allah sai da gabansa ya fadi, domin wani irin fayau ta yi masa, ga idannuwanta da yake gannin tamkar an kara masu girma, kawar da kansa ya yi, dan kuwa ya tabara fadansa ya sakata bude lulubinta harma ta tsura masa ido,
Haushin kansa ya ji ya kama shi, ya aka yi bai yi hakuri ba har ya fita a inda take kafin ya dauki kiran?
Wata zuciyar ta ce" kai sai me? Hala tsoronta kake?
Harare ya wurga kafin ya ja tsaki, sai kuma ya kai dubansa wajen Mu.azam ya ga bai kula shi ba, baima dubansa tuki kawai yake,
A yansa ya shiga mita, oh ni ga mahaukaci, ina fada ita ta tsareni da ido, kai kuwa ka mini halin ko.in kula ko? Ni ba mahaukaci bane, kuma ni ba mafadaci bane🙄,

Haka ya tamke fuska har suka karaso gidan, wanda du mutane ke fitowa baki wangale, a gaskiya, an tafka gini na zamani...fatan a mora lafia,

Fitowa ya sake yi ya zagaya ya fito da ita bayan ya ja mata rufarta ya mayar mata yanda yake da,

Hannunta ya ja inda mutane ke kallonsu ya nufi ciki da ita,
Sai da suka shige cikin accenseur ya kara kusancinsa da nata ya ce" kukan bai isa haka ba?

Agaishat ta dan dago ta saci kallonsa, danme yake da fada, wai fa a kashe mutane yace, ita tsoro take a je ta yi wani abu ya harbe banza,
Kuma mamaki take shi ya je ya daukota, dama haka ake a birni ko me? Sannan wai ta bar kuka, yo ita idan bata yi kuka ba me zata yi? Allah ya ceceta da fushinsa.

Kira ne ke ta shigowa dan haka ya rike hannunta ya daga,

Kukan da take rusawa ya saka shi yin dan tsam kafin ya duba number, Walyn ce, dan haka ya mayar a kunnensa ya ce" hm,

Walyn ta ce" kar ka mini haka, na tuba ba zan kara ba, na bi Allah na bi ka, ka rufa mani asiri kar ka kadaice da wata macen bayana,

Wardugu ya girgiza kai a hankali ya ce" dan me?

Walyn ta ce" dan ni kadai kake so, dan ni kadai nake da hurumin ganninka ba......, Wardugu kar ka zubda mutuncina a idon yarinyarnan,

Wardugu ya dan fakaici kallon Agaishat dake biye da shi a hankali, murmushi ya saki ya ce" kai, bazan iya ba, canza wani abin Walyn, yarinyar a shekaru take karama, aman a zahiri ke kanki zaki yarda da baba ce, waima dan ban ga ainahin zahirin ba, da na fayace maki ko dan ki yarda,

Idan ka tabata kashe kaina zan yi, na rantse maka,

Wani wawan tsaki ya ja, kafin ya ce" sai me? Dan kin kashe kanki walahi ba zai hana ni zama da ita ba, ke harma na kara wasu su yi ta min go slow a gabana, ke kuwa kin mutu kafira!

Wardugu.....ta fada murya shake,

Walyn ya fada yana mai ja ya tsaya,
Walyn ta ce" bani da lafia, sai da aka yi min dinki, ka zo ka duba ni ka ji? Wardugu ka zo ka min cikin na rantse ba zan zubar ba,

Kansa kawai ya girgiza ya kashe wayar yana tunanin bata dadara ba, shi kuwa zai yi watsi da ita har zuwa lokacin da zata yi hankali!

Dubansa ya kai wajen Agaishat, gani ya yi ta dan ja rufar ta bude fuskarta, ta yi wani shar da ita,
Da hannunsa ya nuna mata inda zasu yi kafin yake dora hannunsa wajen ya bude,
Shi ya fara shiga kafin ta yi adu.a a ranta ta saka kafarta ta dama,
Waouh  shi ne take fada a zuciyarta, masha Allah, a hankali ta taka ta karasa tsakiyar dakin tana bi da kallo,
Ta shagalta da kallon sai da ya kama hannunta ne ta ankara da ita yake jira ,
A hankali ya yi mata jagora dakin baci,
Suna shiga ya ja ya jingina jikin garun dakin yana dubanta,
Kafafuwanta dake dauke da jan lale take takawa cikin nutsuwa , a hankali ta juyo tana dubansa, tsaye ya yi kawai yana kallonta dan haka wata kunya ta darsun mata,
Juyar da kanta ta yi, hakan ya sa bata ga zuwansa ba , sai hannunsa da ta ji kusan fuskarta,
Bayan yatsarsa ta tsakiya ya dora gefen fuskarta tun daga wajen girarta ya shafo har zuwa wajen habarta kafin a hankali ya kai wajen lebenta dake zagaye da dan lips kadan ba dayawa ba yana dan sheki,
Idannuwansa ya lumshe sannan a hankali ya saka hannayen nasa ya janye rufar lafayar,
A hakama an saka mata bakar hula marar ado daga ciki an rufe mata gashinta dake wanke tas ba.ai mata kitso ba, sai gobe!
Hannunsa ya kai wajen kulin da akaiwa lafayar wajen kirjinta, hakan ya sa gabanta dokawa har ta dan daga kanta ta saci kallonsa, sai dai ta ga shi yana yi ne tamkar aikin da zai yi ya gama ne, dan haka ta sada kanta duda ba wani mahalukin namijin da hannunsa ya taba zuwar mata nan, idan ka cire Ayya dake daura mata lafaya ba wanda ya taba samun kusanci haka da ita sai wannan bawan Allah,

Kwoncewa ya yi kafin ya zagaya ta bayanta ya yaye shi ya sake shi nan kasa,
A hankali ya sako hannayensa ta bayan nata ya rungumota jikinsa daga baya ya dora habarsa kan dokin wuyanta,
Muryarsa kasa kasa ya ce" Menene?

Agaishat da jikinta ke rawa rawa ta dan girgiza kai bata iya amsawa ba,
Wardugu ya dan kara goga mata sajen fuskarsa a dokin wuyan nata yana lumshe ido sannan a hankali yana lura da yannayinta yanda du ta firgice da bakon lamarin da bata taba gani ko ji a tare da ita ba, sai ya dauki hakan a wata fasara daban, ganninsa ta saba ne, har ta fara daukan caji... dan haka ya sasauta rikon da ya yi mata ya ja hannunta ya kaita kusan bayin dakin ya nuna mata da hannunsa, sannan ya nuna mata salaya ya juya ya fice,
Wata wawiyar ajiyar zuciya ta sauke kafin take dora hannunta daidai zuciyarta, wai Allahna, shine abinda ta fada....menene wannan? Me yasa idan na ganka nake jin irin wannan faduwar gaba da tsoron ka gusa daga inda nake? Me ya sa ka zama mai zafin taba fatar jikina aman maimakun na hana sai na bige da lafewa a fafadan kirjinka, Sadaukina....bakon mijina, zan kwatanta yi maka biyaya mudin raina, Allah ya bani ikon cin nasara

..

Haka ta shiga bayin da ta so zama yar kauye, du kuwa da irin wajajen gayun da ta rayu,
Da kyar ta samu ta daura alwallah ta fito ta yi sallah,
Ba wani wanka da zata yi, bata zo da wannan rawar kan ba, sannan kafin a kawota sai da Ayyanta ta cika mata ciki dan haka tana gama sallah mikewa ta yi ta nemi wajen kwonciya ta nade saman lalausan lafiyayen bed din da bashi da wani tsayi sosai sai dai fadi,

Bata wani jira gannin ya zo inda take ba, domin kuwa koda Ayya ke mata jawabi ta cika da tambayar kanta daman miji zai tardota inda take ko me? Ita dai a aurenta na fari, bai taba zama saman bed dinta ba, bale a kai ga kwonciya, dan haka bata cire doguwar rigarta ba ta yi kwonciyarta da abinta, (kar ku manta, budurwa take, du wani rawar kai wani a cire kaya a sake wanka , a wani canza kaya sai kace uwar mata ko wata wace ta jima a lamarin , walahi a kiyaye, zaki iya sakawa mijin dar a zuciyarsa, koda kuwa a bazawara ya aureta idan ya tardo cas cas malan ka8 nake jira ba wani aji ba wani dan kunya ina dalili? Dan Allah ku mu dauki al.adunmu na malan bahaushe, amarya amarya ce, ta bari a tardota, kai koda ta san lamarin ta bari ya ja daren farkon nan, aman ba wai daga an tabaki ba kema har kin koya! Yin farin? Zuwan farin? Yan mata yaya dai?🤣🤣🤣🤣😹😹😹😹😹),

Luluba ta yi cikin bargonta dake malale saman bed din, bayan ta yi adu.o.inta cike da kewar ayyanta ta lumshe ido da fatan Allah ya tasheta lafia cike da tunanin ta ina zata ji kiran sallah wannan gida tamkar ma.aikata ko hotel?

Wardugu kam, haka ya je masu shi kadai yana muzurai, domin sun shirya yar karya karya tsakaninsu idan an kawo amarya harda amaryar, sai dai ganninsa suka yi shi daya,
Ba wanda ya takura shi haka suka dan jima ana murnar karin aurwn general kafin suke watsewa , ciki kuwa harda Alhinayett da mijinta da yan uwanta inda suka tafi suna kunshe dariyar lamarin wardugu,

A nitse ya koma bangarensa, lokacin har karfe daya na faman yi, dan haka wanka ya fara nema ya dauro alwallah,
Shafa.i da wuturi ya yi, ya shafa adu.a inda yake jin cikinsa na kuwar yinwa, sannan abin mamaki bata zo inda yake ba, dan kuwa Walyn ita ke tardo shi koda yaushe, shi ba zai irga ranar da ya je mata ba,

Mikewa ya yi ya kai dubansa kan ledar da aka bashi, wai kajin amarci,
Murmushi kawai ya yi ya zauna ya bude,
Bridel ya gani ciki dan haka ya bude da bismillah ya kafa kansa, sai da ya yi kat ya ajiye goran ya rufe ledar ya mike ya zauna bakin bed,
Shiru ya yi yana  tunanin me ya hanata zuwa inda yake?
*DAN BAKA ISA BA, BA KAI TAKE SO BA!* tunaninsa ya bashi haka,
A hankali ya dora kafarsa ta dama saman ta hagu yana kadawa, ya yatsina fuskarsa, wani sashe na zuciyarsa ya tunasar da shi.... Wardugu, amanar Ayya? Idan fa tana cikin wani hali?

Gata bakuwa a wajen?

Agogon dakin ya kaiwa kallo, karfe biyu kennan, dan haka ya ajiye carbin hannunsa na dannawa ya mike ya fice a dakin nasa ba tare sa ya kashe komai ba nufinsa ya lekota ya dawo abinsa....

A hankali ya shiga, gannin tar dakin da haske ba.a kashe ba ya saka shi dan dudubata,
Hango tudu tudu saman bed ya saka shi gane tana sama baci take, aman ta shige gaba dayanta har kanta cikin bargon,

A hankali ya karasa bayan ya rufe dakin ya karasa har wajen gadon,
Hannunsa ya saka da niyar janye bargon, aman ta nadidiyeshi sosai kamarma bata samun isashen numfashi,

Kansa ya girgiza ya samu ya haye saman bed din da kyau, ya samu gefenta ya bude bargon kadan sannan ya saka hannunsa yana dan tapin din wajen da bai san ko menene ba yana kiram sunnanta a hankali,
Tsai ta yi da sauke lumfashi kafin ta bude idonta cike da nanauyan baci,
Shiru ta yi cike da tsoron meye? Waye? Wayo Allahna Ayya!
Ta fada can kasan makoshi kafin ta shiga neman wajen da zata yaye bargon jikinta sai bari yake,
Taimaka mata ya yo ta yaye bargon , inda gaba daya ta ruruko idannuwanta cike da tsoro take dubansa bayan ta dubi agogon bangon dakin fari kal mai adon dawissu fari kalkal da shi, ta ce" me me lafia? Me aka yi?

Wani kallo na kin raina min wayo ko? Ya yi mata kafin ya bi yanda gaba daya jikinta ke bari,
Da yatsarsa ya nunata ya ce" ke meye jikin ki ke rawa haka?

Agaishat ta hade hannayenta dan ta samu karfi karfi a jikinta, ta dube shi da kyau ta ganshi dare dare saman bed din da take tunanin nata ne na cikin dakinta ta ce" to aman me ka zo yi dakina karfe biyu na dare? Ko dai nan dakinka ne na kwonta har na yi baci?

Kan Uba, ido kawai ya zaro yana dubanta, a tunaninsa, salo ne irin na mata zatai masa na rainin wayo, lalalallala shi? Me ya zo yi inda take? Me yasa take son yi masa abinda zai iya mangareta ko ya dauke mata jinta ta hanyar wanka mata mari ne wai? Ko dan ta san baya son kai hannunsa jikinta ne?

Kafafuwansa ya tankwashe yana dubanta ya ce" zo,

Inda ya nuna mata ta kala, kusa da shi, koma tace gabansa, wai ta je?
Ido ta kikifta tana  dubansa ta kasa motsawa daga inda take,

Kansa ya juyar yana tunani, wato shi bai isa ba ko? Bai kai wajen da zata zo gareshi ba ? Aman waninsa har yanai masa ikirarin ni.imarta?

Juyo da dubansa ya yi kanta, ransa ya fara baci ya mika hannunsa ya janyota jikinsa inda ta zo gaba dayanta luu ta shige jikinsa,
A ransa fadi yake kamar mage, aman a fili a hankali ya saka hannunsa ya dan dagota daga kwonciyar da ta yi jikinsa,
Fuskarta ya tsurawa ido yanda ta lumshe ido, a hankali ya kai dubansa kan lebunanta, duda ta yi baci man leben nan, bata side shi ba,
Yana kallon leben yana kara kusancin fuskarsa da tata, har ya hade lebensa da nata,.....
Lokaci guda ta bude idannuwanta tana zaro su,
Janye kanta ta so yi domin har ta yi nasarar raba lebenta da nasa dan kuwa dama ba wani harshensa ya zira bakinta ba, gannin tana neman daukaka rainin hankalinta a kansa ya saka shi rikota ya rike kanta da karfin da ba zata iya koda juyar da kan bane....
Ya yi haka ne dan ya horar da bakinta da fada masa magana gatsal, domin shi a ganninsa tana nan fitina da shi ne,
Sai dai ina , a hankali ya shiga sarafa yannayin kissing din, daga zafi zafi zuwa slowly,
A hankali ya sasauta rikon karfin da ya yi mata, sannan itama jikinta ya mutu ido kawai take zarowa cike da tsoro da mamakin bakinsa cikin nata? Wayo Allah, bata kara firgicewa ba sai da ta ga ya kai hannunsa bayan rigarta ya ja zif din rigar cikin wani yannayin da ba zata fadi lokacin da ya kai nan ba
,idannuwanta ta bude ta zuba cikin nasa kafin ta shiga mutsu mutsu da bakinta da ya mayar tamkar alewa a nasa tana fadin"umumumumumum sannan tana dan girgiza kanta da dan karfin da ya rage mata,
Aman me, gaba dayama sai ya kwontar da ita saman bed din ya yi mata runfa,
Bai tashi idasa rikice mata ba ya kasance idannuwansa sun rufe ba sai da ya ji bayin Allahn nan biyu tawaye fiye da yanda yake hasashe,
A hankali ya zare bakinsa daga nata ya bude idannuwansa da suka canza kala wa.inda ta yi dan daman bata hada ido da shi ba a wannan lokacin ya shiga yin kasa da kansa har wajen da bata tsamani............a takaice, a wannan rana, wajen karfe uku na dare, Wardugu ya yiwa Agaishat wani irin zuwa,
Ya salam bai yi haka dan ya cutar da ita ba, sai irin yanda ya kasa tsayar da kansa,
Wayo Wayo Wayo Allahna.... shi ne abinda ya yawaita fada , haka bayan ya samu nutsuwa zama ya yi ya dafe kansa ya tsurawa yannayin da ya kaita ido, cike da tausayawa, da wani matsanancin kaunarta ya koma gefenta ya rungumeta a jikinsa yana mai fadin.......

Ku yi hakuri, ba zan iya fayace wani lamari ba, 😔😔😔😔 bana iyawa😭

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

82

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA* in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

A hankali yake shafa gashin kanta bayan ya dan luluba mata bargo har wajen kirjinta yana dubanta cike da tausaya ya ce" ki yi hakuri, kin ji? Ban, ban san baki taba ba,
Shiru ya yi yana mai jin yanda yake jin haushin kansa , a hankali take lumshe idannuwanta har wani wahalalen barci ya yi nasarar yin gaba da ita,
Ya dan jima zaune nan kafin ya mike ya je ya tsarkake kansa,
Yana fitowa zaman ya ci gaba da yi yana dana waya,
Dogon rubutu ya yi ya tura kafin ya kashe wayar ya juyo da dubansa wajenta,
Ta yi lamo baiwar Allah har abin tausayi,
Idannuwansa ya lumshe a karo na ba adadi kafin ya kai dubansa wajen agogo, har karfe uku ta gota, dan haka ya haye saman bed din , aman bai shiga bargon nata ba ya dai kwonta gefenta yana facing dinta ya tsare fuskarta da ido,
A ransa ya furta" ko tana baci kyau take, gashin idonta tamkar ta kara masu na kanti, lebunanta sun yi jajir bayin Allah,
Hannunsa ya kai wajen kansa kafin ya saki murmushi,
Ya aka yi haka? Tamkar ya kuna ruwa🙈, komai ya ji zanzan,

Abinda ya kara birgeshi da ita irin yanda ta nuna juriya baiwar Allah, kallonsa kawai take da abin ya ci tura, irin kallon nan na ka ji kaina,
Ya yi mamakin da bata aniya kwana tanai masa kuka ba, abinda har yanzu Walyn indai zai yi mata kwatankwacin zuwan nan to fa ba wanda zai rintsa haka zasu kwana yana jinya ita kuwa tana bali tana botsarewa,
Murmushi ya yi ya girgiza kai tuna a halin da ya tsalaketa ya yi tafiarsa, Allah ya shiryeta shi ne adu.ar da ya yi mata kafin ya kara juyar da kansa wajen windows,
Baya jin baci, baya jin farin cikin da yake ciki zai barshi ya iya rintsawa, so yake ya ga farkawarta a kan idannuwansa , so yake ya ga budewar idannuwanta a cikin nasa,
Du wani motsinta yana hankalilce, inda take baci tamkar jariri tana sauke ajiyar zuciya a kai a kai,
Idan ya tuna wasu abubuwan sai ya ji dariya ta zo masa, yana mai jin matsanancin farin cikin zamanta halalinsa, yana mai jin wani irin girma da darajarta, sai ma idan ya tuna irin firgicewar da ta yi a lokacin da ta ga abinda bata taba gani ba, inda ta nuna masa jikinta na bari dan kuwa cikin mayen inda ya kaita idannuwanta suka bude,
Kansa ya girgiza yana mai jin farin ciki, idannuwanta basu kiririce ba, bata yi kale kalen yan matan zamani ba, shi ya koya mata shi ya nuna mata,

Kiran salar fari ya doki kunnenta, a hankali ta shiga kokarin motsawa  sai dai zafin azabar da ta ji a jikinta ya sakata dakatawa,
A hankali ta karanta adu.ar tashi daga baci kafin ta shiga bude idannuwanta inda take jin jikinta da cikinta tamkar an yi mata sata, sannan take jinta fayau da ita,
Tsuru idannuwanta suka shiga cikin nasa, a hankali tamkar ana tariyo mata abubuwa suka shiga dawo mata ,
Da sauri ta rintse idannuwanta sannan jikinta ya dauki bari,
Bakinta na rawa ta ce" dan Allah na tuba, kar ka min wannan abin , walahi da zafi, ba zan iya ba,

Wani sabon tausayinta ne ya ji ya darsun masa,
Mikewa ya yi ya zauna yana dubanta kafin ya mika hannunsa a hankali ya tayar da ita zaune,
Taki su hada ido, sam sai kawar da kai take tana neman inda zata saka kanta, dan haka a nitse ya ce" ba zan maki komai ba Orronur, zan taimaka maki ne ko zaki ji dadin jikin ki ,

Agaishat ta girgiza kanta a hankali   ta ce" zan iya  dan Allah ka bari zan iya,

Wardugu ya lumshe idannuwansa, da ya sani kawai yake yi,
Mikewa ya yi ya kare mata kallo kafin ya nade hannun rigarsa a hankali ya yaye bargon da ta ruko ido take rikewa kar ya cire mata, aman ya janye shi baki daya daga jikinta ya duka ya dauketa a yanda ta dukunkune jijinta ta nufi bayi da ita,
Yannayin yanda yake bata kulawa ta isa ta nuna irin yanda yake jinta a ransa,
Da doguwar jalabiyar jikinsa ya samu ya sakata cikin ruwa masu dumi sosai, yana yi yana gyara mata gashin kanta inda ita kuwa kanta ke kasa kamar ta je gaishe da sarki,
Sai da ya gamsu da yannayin yanda fuskarya ke nunawa du idan ya canza mata ruwa kafin a

hankali ya ce" kin iya wankan tsarki?

Da sauri ta dago ta yi masa duban da bata shirya ba, irin kallon mamaki mai hade da dan hararen nan, sannan ta dan kada kanta sai kuma ta sada kanta,
Murmushi ya yi ya lakaci hancinta ya darwaye kafafuwansa da hannayensa ya juya ya fice

Bayan fitarsa kam Agaishat kanta ta sada ta shiga tunanin rayuwa,
Wannan shi ne auren, wannan shi ne zaman? Ya rab lale in ba aure ba, me zai hada shinfidarta da ta Wardugu? Ta isa ta kai nan? Ta tabata koda bariki yake take astaghfrullah ba zai dubeta ba,
Aman sai gashi darajar aure ya saka sun taka wani mataki mai girma na duniya,
Bata tunanin a halita a yanzu akoy wanda ya san sirinta irinsa, lale shi din sirinta ne!
A hankali ta kara gasa kanta ta hanyar kara shiga wani ruwan zafin , domin ta lura tunda ya sakata cikin ruwa ta ringa jin jikinta na yin sauki sauki,
Haka ta gama ta tsaftace jikinta ta dubi bayin ba komai ciki, ko tawul.ita bata gani ba dan bata ga inda aka adana su ba,
Dan haka ta kama tsayuwa cikin bayin kankame da jikinta tana mai jin lamarin wani iri, bata saba haka ba ita!

Burum ya shigo hakan ya sa ta kwala dan kara ta juya da niyar boye jikinta,

Murmushi ya yi ya karasa ya bude wajen madubin dake zagaye da bayin ya ciro farin tawul kal baba sosai ya kawo ya rufa mata sannan ya ciro irinsa dan madaidaici ya dora mata saman kanta,

Hannunta ya ja suka fito, nan ya nuna mata wajen kayanta da kuma darduma,
Da hannunsa ya nuna mata zai je masalaci...

Kanta ta daga masa kawai kafin ya juya ya fice a dakin,

Wajen kayan ta karasa cikin nutsuwa ta bude ,
Doguwar riga ja mai duhu ta dauko ta saka kafin ta saka pant ,
Hijab dinta ta zara ta karasa saman salaya,
Cikin nutsuwa ta gabatar da sallarta kafin ta dukufa azkhar ,
Kyar take zaune tana ta adu.a, ba komai take roko ba sai fatan cikawa da duniya lafia, ta yiwa iyayenta adu.a da uwar rikonta, ta roki Allah da ya basu zaman lafia da mijinta ya kade du wata fitina ya sa ya sota fisabililahi👏🏻,
ba ita ta tashi ba sai da ta hangi hasken rana sannan ta hakura ta shafa fatiha,
Kwali ta sakawa idannuwanta sannan ta mike a hankali ta nufi wajen turarukanta ta yiwa jikinta badede (😅🤣),

Gadon take kallo, yanda du ya fita hayacinsa,
A hankali ta yaye rufar gadon ta kai bayi ta ajiye wajen da idan ya zo zata tambaye shi yanda

ake anfani da mashine din wanki,
Wata ta ciro ta shinfida ta bi dakin da kallo,
Kwarai zata so gyare gyare , sai dai zata bari ta ji karfin jikinta sosai, dan haka sai ta haye gadon ta nade abinta.

Ayya na saukowa da sasafe , domin kuwa karfe takwas ce, dirar motoci ya sauko da ita, inda ta hango Alhinayett daga sama, hakan ya daga mata hankali ya sakata saukowa da mugun sauri,

Alhinayett dake jagorar mutanen da suka kawo kyautar Agaishat, bisa kiran mijinta da Wardugu ya yi ya roki alfarmar hakan, dan kuwa shi bashida wata aminiya fa, kuma wannan lamari ya zama dole, du buzuwar da ta kai.mutuncinta dakin miji, mijin ma yin irin kokarin da yake da hali, dan haka ne Wardugu ya tayar da ita da jama.ar da ta gayata aka yiwa Ayya dirar bazata, bisa lamarin da ya sakata yin zuru tana bin su da kallo,
A sanninta ana irin wannan kyautar ne idan yarinya ta kai mutuncinta,
Me hakan ke nufi?
An kawo dankareriyar sarkar zinari, da ky din mota da ambulop din kudi kato wanda ba.a kifaya ko nawa bane ita kuwa bata tsaya dubawa ba, sai rakumi amale jibgege da ake janye da shi da Sa fari kal da sakon cewa a yankawa amarya a yi mata soye ta ci ( ku je ku yi tambaya, tabas haka al.adunmu suke, ana yiwa wace ta kai mutuncinta kyauta ta bajinta da abin yanka a yankawa amarya ta ci, dan dai rawar na zuwa daidai da kidan ne, wato barikinka aljihunka....iya kudinka, iya shagalinka)

Wayarta dake saman kujera ta rarumo ta shiga kiran numbersa,
Dama ya san a rina, cikin yan kaiwa kuwa harda khadija da ya nema da kansa,
Ayya sai da ta yi masa kira uku kafin ya datse ya biyo bayan kiran nata,

Gaisheta ya yi kafin ya yi shiru,
Ayya ta ce" am, Wardugu sai naga sako,

Wardugu ya amsa Ayya a takaice yana mai kunshe dariyarsa inda ya ce" eh,

Ayya ta dubi wayar ta mayar a kunnenta ta ce" sakon kuwa masha Allah, an gode , Allah ya saka da alkhairi,

Wardugu ya kara gimtse dariyarsa ya ce" amen, amen,

Ayya ta dane zuciyarta dai ta ce" harda su amale kai aman kosashe ne,

Wardugu ya ce" eh haka fa,

Ayya ta mike tsaye ta ce" Wardugu dan ubanka ina y'ata? Tana ina? Walahi maza maza a kawo min yarinya a yi mata kitso da kunshi a gabana, lahauli, Wardugu bana jin motsinta, tana ina me ka yi mata?

Ai kuwa wardugu ya saki murmushi kafin ya ce" haba yanzu na gane Ayyana, meye za.ana bin wani layi da ni kuma? Lafiarta kalau,

Ayya ta ce" aman wannan kyautar ai da manufarta ko? Gashi yaran da suka kawo ni basu ce min komai ba, ta yaya hakan zai faru?

Wardugu ya girgiza kai yana murmushi kafin ya ce" eh manufar dai da kike tunani Ayyana haka ne.

Innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, ai Ayya ita ta datse kiran dan walahi kunya ce ta kamata, sintiri take tana zancen zuci, ba mai hanata wankawa Agaishat mari kan shiru da ta yi mata ta yi ta shiryata tamkar wace ta san hanyar,
Ba mai rabata da Wardugu idan ya jiwa yar amanarta ,
Zama ta yi tana duban Alhinayett da ta rage, domin ta salami sauran mutanen, ta ce" kin san ai ba.ai mata kitso ma sai yau ko Alhi?

Alhinayett ta amsa Ayya tana dubanta, kafin Ayya ta ci gaba da fadin" to bara ki ji, zuwa zaki yi ki dauki Melina daga saloon mun gama magana da ita ki kaita gidan Agaishat, idan kin je ki yi min vidio call na ganta, idan wani abu bai gamshe ni ba, zaku ganni a kanku, kun jima baku ce na dauko y'ata ba!

Ai kuwa Alhinayett ta maida hankali, domin yannayin Ayya ba wasa,

Ita kanta sai da ta je ta gane ba kyautar tarin kauna bane ya yi kata, kyautar cika al.adunmu ne, kuma ya yi haka dan a san da eh ruf ta je,

Sosai ta tausaya mata, ita da kanta kunyarsa ta ringa ji dan a gabanta ya tsare Agaishat da abinci sai da ta ci ya shirya ya fice aiki bayan ya jadada a bar waya a kusa, inda ya wuni yana aikin kira ya ji ya take, me take,
Daga nan ma wajen Ayya ya fice inda suka sha daru, ta dage tana fada, aman ta ki fadin asalin fadan, ita dai fadi take du wanda ya takura yarinyarta zata je ta daukota ne!.....

Kwonci tashi, zaman Wardugu da Agaishat zama ne na amana,
A hankali take binsa, shima a hankalin yake binta,
Ya kusanta kansa da ita, ya mayar da ita abokiyarsa, ya saka shakuwa ta kirki tsakaninsu, inda ta sakankance take afkawa cikin kogin soyayarsa aman har yau ba wanda ya fadawa dan uwansa kalmar so.
Sau daya ta yi masa maganar Walyn, maimakun ya fahimceta sai cewa ya yi" Walyn dai matata ce, kika san ko idan na fita daga inda kike wajenta nake tarewa? Ba ruwanki da rashin raba kwanakin ku, ko so kike ki nuna min na isheki dan bakya so na?

Shiru ta yi ta shiga goge masa zufar motsa jikin da ya yi, inda ta mika masa tea mai zafi ta shiga

tatare wajen,

Kamar yau, ya kama wajen sati uku da aurensu, kuma har yau ya ki ya bata wayarta da ta gane tana hannunsa,

Zaune yake yana kallon France 24, ana ta hasko labarun duniya,
A nitse ta zauna kujerar dake facing din inda yake zaune,
Kallon yake aman yana cirewa yana dubanta, sai kuma ya maida dubansa kan tvn,

Kafarta take dan karkadawa a hankali, ta hade cikin doguwar atamfa, rabonta da wardugu ya kai mata hari tun na daren farkonsu,
Ya kasance komai dare idan ta yi baci zai janye ya kwana daban daban da ita, ta sha kama shi yana dibgar lemun tsami, ta sani, ta sha azaba ya ba gobe, qman kuma ta fara shiga damuwa, ta dai san mijinta namiji ne lafiyaye, kuma ta san ba ita daya ne da shi ba, idan wajen matarsa yake zuwa ita hoto ce? Aa fa, ba zata so ta zama hoto a fadar Wardugu ba,

Zaman kafar ta canza tana kadawa, dan haka a hankalce ya ce" menene?

Agaishat ta zumburo bakinta ta ce" wai me sunana ne?

Wardugu ya tsura mata ido, a ransa ya ayanna yau kuma fitina take ji,

Murmushi ya yi ya tashi ya koma kusa da ita ya zauna, habarsa ya dafe yana duban kwayar idannunta,
A hankali ya ce  sunnanki...Orronur,

Agaishat ta zumburo bakinta ta dube shi da kyau ta ce" menene ma.anar Orronur,
Tsareta ya yi da ido, zai bata amsa kira ya shigo wayarsa dan haka ya daga yana dubanta,

Walyn...ya fadi sunnan a sanyaye,

Walyn ta amsa shi da Wardugu, dan Allah ka lamuncen ganninka, ka bani damar ganninka, na tuba, ka tuna fa, hakina dake kanka idan har ka tauye min Allah ba zai barka ba, ba sakar min kudi bane kawai hakina dake kanka,

Wardugu ya lumshe idannuwansa kafin ya bude yana kallon yannayin Agaishat ya ce" kina ina ne?

Walyn ta amsa shi da tana gidansu na da,

Wardugu ya saki murmushi a zuciyarsa dan kuwa zai so ya ga yannayin da Agaishat zata nuna, dan haka ya ce" ki shirya min tarba, zan so shinfidarki ta yi kamshi, gani nan zuwa,
Kamar an doka mata ice a kanta ta ji, a zaunen da take ta lumshe idannuwanta tana kiran

sunnan Allah, domin kuwa juwa ce take ji daga zaune,
Bata tashi jin kamar an gaura mata mari ba sai da ya mana mata kiss, ya mike yana gyara belt din wandonsa ya yi mata wani murmushin shegantaka sannan ya juya ba tare da ya ce da ita zai fita ba , ko zai je wani gurin ba, ya fice a gidan inda ta gane haka ta tvn bangon dake nuna mai shigowa ko mai fita daga gidan dan ba.a jin dirar motoci in dai dakunnan a rufe,

A hankali ta silale saman kujerar ta rushe da kuka dan zuciyarta take ji zata balo kirjinta ta fito,

Dan me ba zan zama mace mai inci irin na kowa ba?
Zaman kwana ashirin da daya da na yi da kai, zaka yi min wasa tamkar wata baby, na san bana yawan neman zama inda kake ba suturar kirki a jikina, aman irin idan ta kama ka shigo na fito a wanka zaka yi gagawar juyawa ka bara min dakin, wari nake? Ko kaima kana kyamar *BAK'A CE?*, ni na san kana zaune da ni ne dan girman kaunar da kake yiwa mahaifiyarka, aman kuma kaunar ba zata sa ka nunan nima mace bace? Ko na zurmi da yawa ta hanyar bin nasihohi ta hanyar kyautata maka? Na san matarka ce, ta fi ni fada a wajenka, aman idan ka yi niyar raba mana kwana ne ka hada mu mana ka yi kamar yanda kowace mace ke samu? Ba ko salama ko? Ni ko? Ba komai Wardugu, nima zan kama kaina, na farka daga yaudarar kaina da nake cewar so ne, aa *Kyautatawa ce*,
Nima zan kyautata maka!

Wardugu kam na fita sai da ya gama shawaginsa a gari kafin ya je gidan,
A bangarensa ya sameta, an gyagyara dakin ba laifi, sannan dai cikin shigarta ta kananun kaya, Ga mamakinsa bai yi wani zumudin shigarta ba kamar kulun, saima zama da ya yi yana son kwadaitawa kansa ita dan fita haki, da kuma samun nutsuwar kansa, dan ba karamin takure yake ba dagawa Agaishat kafa da yake, yana matukar tausaya mata , yana so ta karasa yarda da shi, ta idasa sakewa da shi, kafin a hankali ya kara dirmiyar da ita ruwa ta hanyar da ya dace, so yake ta fada soyayarsa komai kankantarta, yana so ta so shi koda da wasa ne, shi dai ya samu soyayarta kamar yanda yake ciki,
Sai dai yarinyar ya lura tana zaune da shi ne kawai dan biyaya, domin sha nawa zai samu kiran yan mata a gabanta, maimakun ta nuna bacin ranta irin na Walyn, saima ta shiga sabgar gabanta, kennan dai bata son sa bale ra yi kishinsa ko? Dan me? Dan me jarabawarsa ta diro ta nan? Ya Allah......

Walyn dake zaune kanta kasa tana share hawaye cike da tsoronsa, kar ta yi abinda za.a maimaita wanda aka yi kafin ya bar gidan ta budi bakinta na rawa ta ce" War.....
Hararar da ya watsa mata ne ya saka ta hadiye sauran maganar,
A hankali  ta taso ta dawo kusa da shi tana duban yannayinsa ta ce" .......

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

83

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA*  in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

Ta ce" Wardugu, har ka manta da ni? Tun ba.a je ko.ina ba har ka manta da ni? Wardugu ni ce fa matarka, uwar gidanka, danme maza bakwa yiwa kanku adalci bale ku yiwa wani? Wardugu saboda wata can bakar mace zaka yarda ni? Dan an cusa maka mace an baka shi ne ni zaka yi watsi da ni?

Wardugu ya dade kansa da hannayensa bibiyu kafin ya dago da dubansa,
A hankali ya ce" me yasa ba zaki yiwa kanki adalci ba? Waye bai san irin yanda nake daga maki kafa ba? Walyn, kawai dan na yi aure sai karin tijara? Walyn yaushe iyayena zasu yi daraja a idannuwanki? A lokacin da na je wajenki na kasance mai matsanancin girmama iyayenki, a sanu kika koya mani halayen tafka rashin kunya a gabansu,
Walyn nima fa mutun ne, ina so na ga canji a rayuwana,
Mahaifiyata da kika gani, ta fi min kowani halita a nan gidan duniya, da kina da hankali, kina da wayo, koda kin tsaneta ne sai ki boye tsanar nan ki kyautata mata,
Aman ina, a gaban idona sha nawa zaki bita da wani kallo idan ta bada baya? Ina sane, ina gani , ina lure, kawar da kai ne nake dan a zauna lafia!

Da ace rashin hankalin ki iya ni kika tsaya, da zan ci gaba da jan kwababiyar rayuwar nan, Aman walyn bayan ni, kika tsalake kika haura iyayena, sannan kika tashi kika je kika cire kwaina? Mahaukaci ne ni da ba zaki hada zuri.a da ni ba? Meye aibuna? Me na rage ki da shi?

Walyn dake sauraronsa sosai zuciyarta ke kuna, au fadama zai dora daga inda ya tsaya kennan? Du irin yanda ta zubar da ajinta take son su fuskanci juna shi ne zai rufeta da fada? Mahaifiyarsa, mahaifiyarsa,

Walyn ta dube shi, walahi ita tsoron haukansa take da ta fadi magana, dan haka ta ce" aman ai ba.a kyauta min ba ko?

Wardugu ya kausasa murya ya ce" waye bai kyauta makin ba?

Walyn ta so tace Ayya, aman gannin yana cikin yan maganan, kar ta kwabe komai ya sa ta ce" kai mana, ka kyauta min ne?

Da na yi me?,

Walyn ta kifta ido tana du dubansa ta ce" da ka yi aure kafin lokacin ka yin ya yi, da ka yi aure baka sanar mon ba kafin ka yi, da ka auri wannan yar yarinyar har ka juya min baya tsayin sati uku, da ka dauketa ka kaita gidanka na aeroport ni ka barni a nan ana ci min amana,

Wardugu ya sakar mata murmushi, ya kawar da kansa, can ya ce" adinina bai zo min da salon al.adata ba, dan na yi ban yi sabo ba,
Sannan da na yi ban sanar maki ba uwata ce ke? Nan ana daura aurena ban je na ga kowa ba sai ke, aman kika take ni!
Dubanta ya yi cikin ido ya ce" Agaishat kuwa, Wollah sonta nake!

Kyam ta yi tana dubansa,
Kanta ta kawar ta ce" ba zaka huce ba kennan?

Mikewa ya yi ya dauki ky dinsa ya juya da niyar tafiarsa,

Da sauri ta mike ta ce" Wardugu tafia zaka yi?

Juyowa ya yo yana dubanta kafin ya tako zuwa inda take tsaye ya dubeta da kyau ya ce" ban tsara saki wa mace ba, da na jima da rabuwa da ke bisa rashin hankalin da kike tafka min na yau da kulun Walyn,
Ban waiwaye ki yau ba dan isarki, kyanki, ko farin ki kamar yanda kike takama sai dan tsoron Allah da tunanin ko kin nutsu ne ?
Baki nutsu ba, har yanzu baki sauka daga inda kika hau ba,
Allah kawai nake tsoro, ina jin tsoron haduwata da shi da laifin wani a kaina, idan kika cire wannan, ki je du abinda zaki yi ki yi!

Yana gama fadar haka ya juya ya fice tana kugin kiran sunnansa ya yi mata banza,
Tsaki ta ja kafin ta wurgawa hanyar da ya bi harara ta yi kwafa ta ce" in dai rawar kan amarci ne, zaka yi ka kare, ba wani ka waiwaye ni dan wani abin face kana so na, ba zaka iya ba sai da ni! Wannan bakar ba zata girgiza ni ba!

Barci Agaishat take saman kujera a takure, da alama tsoro take ita daya,
Haka ya shigo dakin ya kai dubansa inda take,
Bai tasheta ba, bai yi mata magana ba ya fice ciki ya duba wajen abinci ya ga bata ci ba,
Bai tasheta ba ya fito ya nufi bangarensa ya kwonta domin ransa a bace yake, indai zai tasheta ne dalilin bata ci abinci ta kwonta ba yana iya bata mata rai,

Kamar yanda ta saba kiraye kirayen sallah suka farkar da ita, da kyar ta iya mikewa domin kwoncib da ta yi du jikinta ya yi tsami,
Dakinta ta zarce ta je ta kimtsa dan yin sallah,
Koda ta gama sallah zama ta yi ta tsurawa waje guda ido, zuciyarta ke mata fada, ba na komai ba sai na ta yi sabko, ya zata damu haka da son ganninsa bayan ta san ba ita daya gareshi ba? Ita fa zuwa ta yi ta tarar da wata, idan ta tsiri damuwa da jinsa a kusa bata so kanta da yawa ba kuwa?

To aman ai sai ya min bankwana ko? Wayar da ya yi ita kawai ta shaidan inda zai je, daga shi bai ce min komai ba,

To meye dan wannan a halayan wardugu? Ke dai ki kiyaye,
Wata zuciyar ta bata amsa,
Dan haka a hankali ta mike ta ninke salayar, yau kam sai ta ga masu gyara gidan nan, a kulun kafin ta fito daga sallah an yi komai an gama, har kulun mamaki take, danma ita ke shiga kicin abinta, aman tana kyautata zaton da masu aiki a gidan, dan kuwa har yanzu tunda ta shigo bangaren nan nata kafarta bata fita ba, du sati Ayya ke turo mai kitso ta zo ko ta yi mata kitso ko ta mata gyaran kai, kunshin kafarta da hannayenta kuwa da sun fita ake dora wasu domin wannan lanlan ne na zamani mai saurin fita,

Labule ta dage ta leka sosai,
Ai kuwa sai shige da fice suke kowa da abubuwan aikinsa, hakan ya tabatar mata da har cikin ma da masu gyarawar kennan, ita dai abinda take yi da kanta saka turaran wuta, wanda take yin garwashin a kicin ta saka da toka mai zafi ta saka dan turaranta ya game dakunan da kamshi,

Murmushi ta yi ta je ta salo wankanta,

Tana gama shiryawa cikin doguwar atamparta an yi mata dinki simple, sai hannayen ne kawai akaiwa ado , ta daura dan kwalin atampar ta tsaya gaban madubi tana kallo,

A hankali ta sauke ajiyar zuciya a fili ta ce" Ba sofona, ina yawan mafarkinka, Allah ya sa lafiarka kalau ka ji? Zan so ka ganni Ba, tabas maganarka haka ne, birni ga girma ga abubuwan girma, birni mai dauke da wardugu da Ayya da kuma Walyn,
Birni mai mota mai jirgi,
Birni mai kalolin fata ba biyu kawai ba,

Sai da ta gama kalon kanta kafin ta yafa mayafi saman shigarta ta fito a hankali ta nufi wajen abin turaran wutarta ta dauka ta nufi kicin,
Sai da ta hada shayi ta zuba a dan cofi ta dauko biredi mai beurre sannan ta kuna garwashin ta hado turaran wutar ta fito da su a hannunta ta dorashi wajen da yake gana dakin sannan ta je saman cafet ta zauna ta yaye mayafin ta ajiye ta zauna ta fara karyawa,

Tana tsaka da ci ta ji kanshin turaransa hakan ya sa ta yi dan tsai kafin ta dago da dubanta,
Cikin shirin zuwa aiki yake, yannayin fuskarsa ba fara.a hakan ya sa ya shaida mata da ransa a bace yake,

A hankali ta kawar da dubanta daga fuskar tasa ta ajiye kofin glass dun dake hannunta ta mike daga zaman da ta yi tana goge hannunta da tissu duda ba abinda ya yi, ta kai dubanta wajensa,
Tsaye yake kikam yana dubanta,
A hankali ta mike ta karasa dan kusa da shi kadan kafin ta duka ta gaishe shi,

Mutanen kam a kusa suke yau, domin gaisuwarma da kai aka amsa mata, dan haka ta mike da niyar shiga kicin ta hado masa abin karyawa kafin ya fita,

Hannunta ya riko da hannunsa na dama ya dawo da ita gabansa,
Hannayenta ya kamo baki daya ya kai wajen botiran rigarsa dake bude ba.a bala ba,
A hankali ta shiga bala masa tana duban kasa ,
Sai da ta bala masa har daidai wanda yake tsayarwa sannan ya zauna saman kujera ,
Cikin nutsuwa ta juya ta shiga daki ta dauko kumb,
Dawowa ta yi ta caje masa sumar kansa da kyau ta juya ta mayar ta dawo da niyar shiga kicin din dai,

Rikota ya yi , ya juyo da ita suna kallon juna,
Kansa ya girgiza mata a hankali sannan ya mike ya dauki ky dinsa ya juyo ya mika mata wata dankareriyar samsung bai mata bayanin komai ba ya fice a gidan,

Ta jima tsaye cikin yannayin damuwa, me ke damunsa? Me ya bata masa rai haka?
A hankali ta zauna bakin kujera tana duban hanyar da ya bi ya fita,
Ya Allah, shi ne abinda ta fada a fili, azumi yake ko kuwa cin abincin ne ba zai yi ba? Yaushe ya shigo gidan ma ni ban ji ba?
Idannuwanta ta lumshe tana tuna maganar Ayya cewar wani lokacin zaka rasa gane kansa, zai dulmiyar da kai cikin tunanin waye shi? Dan haka ki yi ta hakuri Agaishat!

Wardugu, ka taimaka, ka bani hanyar da zan fahimce ka, ka taimaka ka ringa fara.a tare da ni ba sai ranar da ka yi niya ba, ka taimaka na zama wace ke gane du wani motsinka!

Wayar da ya ajiye mata ne ta shiga kuka ta hanyar salama da muryar mace zazaka tana karawa,
Sai da ta zabura dan ta zurfafa a tunani, kukan ya ankarar da ita dan haka da sauri ta dauko wayar tana duba sunnan wanda ke kiran, Anmou, waye Anmou????
Dagawa ta yi da salama sannan ta yi shiru,

Daga can kuwa sai da aka daga ta mika mata wayar tana dubanta da murmushi inda ita kuwa ta karba ta dan yi tsai , bata san da me zata fara ba, bata san me zata ce da ita ba, marabinta da ita tun kanta na cikin duhu,
Dan haka a hankali ta ce' Agaishat!

Tsai Agaishat ta yi, lokaci guda zuciyarta ta buga,
Wayar ta cire ta kali numbobin sannan ta mayar a kunnenta,
Muryar matar ta kara cewa " Agaishat, kina ji na kuwa? Da yaren buzanci, da irin yanda take rrrrrrrr dinta sak irin na Agaishat din,

Da sauri Agaishat ta kai zaune muryarta na rawa ta ce" Anna? ANNA ke ce?

Anna ta lumshe idannuwanta ta amsa da " Eh Agaishat,

Ai kuwa Agaishat ta fashe da kuka tana sauraron limfashin mahaifiyarta,
A hankali ta ce" Anna, ina kike? Kun dawo ne? Kin warke Anna? Anna ina yan uwana? Ayya ina Ba Sofona? Annata kin kama sunana sak Annata kin kama sunnana,

Anna ta lumshe idannuwanta tana mai jin nauyin yar da ta haifa da cikinta, tabas ta saki rayuwar Agaishat dandaja, Allah ne kawai ya zama gatanta, ita yanzu haka bata wani hadiye maganar wai dan amininsa na sonta ya saketa, ita fa tsoro take ko bai sameta daidai bane ya saketa? Sakin yaro karami na kutse kutse kofa kofa waje waje dan neman gurin da zai ji sanyin rayuwa , neman abinda zai saka a bakinsa, a haka har ta rago ta kawowa baba sofo da kuma Anna, a haka ta iya tatalin dan kudin da ta samu ta kawo masu, a haka take zuwa ta rabu tana tsoron wani abin ya faru ko mahaifinta ya zo ya karta mata abin wulakanci dan kawai kalar fatarta na da duhu? Tausayin yar ne ya saka Anna kasa yin magana, dan haka Mariama dake tsaye tana ta so a bata wayar ta yi dabara ta karbi wayar ta bushe da dariya ta ce" Agaishat, Agaishat din Ba Sofo, Agaishat an girma?

Kafin ta amsawa Mariama Fatimata ta sabce wayar ta tsere kusa da Gaishata ta ce" Agaishat, Agaishat din Ayya Agaishat kina ina, ina ne gidanki?

Ai kuwa ta kwalalo ido cike da murna ta mike ra budi baki ta ce" Fatimata, Fatimata....
Sai kuma ta ji muryar Gaishata,

Ita kam bata taratsinsu, cikin nutsuwa ta ce" Agaishana,

Agaishat ta zauna tama rasa ina zata saka kanta dan dadi, muryarta nitse ta ce" Gaishata, Gaishata ina kuke ne? Gaishata Anna da sauki jikin nata? Kuna Timiya ne?

Gaishata ta girgiza kai tamkar tana gabanta ta ce" aa, muna garin da kike, mijinki ne ma ya kira jiya, Gukunni ya bashi number Anmou,

Agaishat ta sauke ajiyar zuciya ta ce" Gaishata kin haihu? Me kika samu?

Gaishata ta yi murmushi ta ce" du wannan tambayoyin adana abinki abinda zamu zo? Dama muma zumudin mu ji muryanki ne, aman Anna da sauki sosai alhamdulilah, nima kuma na haihu, Agaishat, lafiarki kalau dai ko? Ba abinda ke damunki gidanki ko? Agaishat amarya, yar Ayyanta aure sai da hakuri kin ji?

Agaishat ta yi murmushi tana ta sauraron muryar yayarsu ta fari, wani dadi take ji na ratsata har suka kashe kiran bayan sun tabatar mata da suna gari da zama , da sun huta zasu zo inda take,

Suna kashewa ta ji wani karfin gwuiwa ya zo mata, hakan ya sa ta zauna ta shiga game d wayar hankalinta kwonce,
Ta so kiran number Ayya, sai dai tunanin kar ta huce gona da iri ya saka ta bari idan ya zo sai ya kira mata kamar yanda ya saba , ta bata albishir,

Fararan hakoranta kawai take yawan washewa,

Ta jima nan kafin ta mike ta nufi kicin dan shi ne kawai aikinta a gidan,

Da yama bayan ta gama salar la.asar ta zauna da wayar da ta wuni game tana jujuya abinda ta rubuta da yarenta, inda ta samu da kyar ta gama message din kamar haka

*Salam*

Ina yini Ya, ya aiki?
Zan kira ayya ne......................na gode

Agaishat

Numbersa da ta shanye tun tana gidan Ayya saboda tarin zero din dake ciki irin number nan mai shige da juna ne ta rubuta ta tura dan ita ta kagauta ta ji muryar Ayya ta fada mata sun yi waya da yan uwanta da Annarta,

Wardugu dake tuki daga justice ya fito ransa a mugun bace sakamakon kiransa da Gukunni ya yi kan case din AISATA  matar Marahut, za.a salameta nan da wata biyu domin a lokacin da ake binciken asalin masu shigo da kwayar Niger ta bada hadin kai wajen fadin sunnayen wa.inda ke siyar mata baki daya, ta bada sunnayen wa.inda ta san suna siya a wajensu, sannan ta yarda bata baiwa sharia wahala ba ta hanyar gardana ko kin hada kai, hakan ya sa ta samu sasauci bayan kason da take yi an dankara mata tara ta millioyin kudi sannan wai za.a salameta!
Hakan ne ya kunno shi, ido rufe ya fito ya dauki hanyar neman Marahut, nemansa yake ido rufe, shi ya san koda da haka, to fa da saka hannun Marahut ta hanyar gannin masu Niger din dan a salamo masa matarsa marar mutunci,

Wayar ce a hannunsa yake dannawa yana neman layin Marahut, aman amsar daya ce, number a kashe, layin ba zai shiga ba,

A haka message ya shigo, da yake orange ne yake kiran da shi sai ya yi tunanin ko zasu shaida masa number ta bude ne?

Yana budewa ya ga message din,
Kallon number ya yi ya ga number wayarta ce da ya saka mata layinta cikin wayar nan,

Wai wardugu gatsal tamkar wani sa.anta? Sannn shi zata turowa message da umarni? Me take tunani? A me ta dauki kanta? Ba damuwarta bane da damuwarsa itama ko? Bata damu ba da halin da yake ciki ko?

Wani kuuuuu ya taka birkin motar kafin ya samu ya yi riboss da matsiyacin gudu ya dauki hanyar Aeroport din, ba zai hadiyi cewar, shi yana hana kansa komai idan ya ga koda yannayin fuskarta ya canza ne aman ita bata damu ba, da damuwarta kawai ta damu, zai warware mata rashin mutunci ne ta san cewa bafa shayinta ko taoronta yake ji ba! Zai je gidan ya.......

Wayo yar muleka😕😕😕😕

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

84

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA*  in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

Yana sake saken tarin mugunta ya karasa gidan,
Bai yiwa kowa magana ba, bai shiga hurumin kowa ba  kamar yanda ya fita ya nufi hanyar sada shi da ciki, inda kowa ya shiga tatara kafafuwansa yana barin wajen dan ba zai so abinda za.a kula da wani laifi nasa ba,

Bata falo, hakan ya sa ya zarce dakinta na barci,
Nanma bata nan, dan haka ya fito ya nufi kicin,

Dago kan da zata yi ta ganshi ya nufota,
Yannayin fuskarsa ya sakata sakin nade naman da take cikin kabeji zata yi name,

Da sauri ta mike daga kan kujerar mai ruwan silba ta daga kafarta,

Kafin ta shige inda zata shige dan ta san wannan zuwan nata je, dan irin kallon zaki ci yan garinkun da ya yi mata ya saka hanjin cikinta motsewa waje guda,

Rikotan da ya yi da karfi sannan ya fincikota baya ya jefar cikin kicin din,

Yau ta ga rana ta ga tashin hankali domin binta ya yi inda take yaden nan ya wanka mata wani

lafiyayen marin da ya dauke jin ta,
Tabas wani dummmm ta ji na lokaci mai dan tsayi domin za.a kai second ashirin hakan ya saka bata ji fadansa na farko farko ba sai da kunnen nata ya dawo ta fara tsintar fadansa kamar haka" *Ba zai yiwu kema ki wulakanta min zuciya kamar yanda ta wulakanta min ba!* ta yayama zan fita daga gidannan raina bace , baki damu da yi min wani abin da zai faranta min ba sai faman ki dura min abinci kafin na fita bayan ina azumi? Ya zan je ma.aikata kin san wani irin aiki nake yi aman ki turon message gatsai gatsai da rashin tauna zance ya zama dadi kamar ke ce gaba da ni ki turo min, oho o na ji abinda zan ji ko? Da wannan dan iskan ne da ya zo wajen diner mai dogon wuyan nan yana launi uwa lagwani da kin zauna kin ware yare kin masa tausasa ko? Da ace tsohon mijinki ne kin iya yi masa kalamai, wanda nima shaidar shi mai daraja ne ana bashi kulawa ne ko? Ni zaki turowa sako da kama sunana kai tsaye tamkar dan gidanki? Sai mutun ya gama mutuwar muku ku wulakanta shi ku zubar da shi ku kara gaba abinku ko? Ku buzayen nan haka halayenku yake? To bari ki ji, a kaina an tsaya, walahil azim Agaishat hanya a bude take, kafarki ke ta taka waje da niyar barina sai na harbe ki! Sai dai a kashe ni! Jarabawata ce soyaya da buzuwa? Na karba, aman kuma rantsuwata ce ke ce buzuwar karshe da zan ringa mafarki ina juyi kanta! Ke ce zan yiwa son karshe a cikin buzaye na wahala dan buzuwa! Ke ce wace zata rayu da ni ko a wani hali, ke rabon haihuwarki da wani namijin sai dai idan ajali ya dauke ni!

Hannunsa ya buga jikin madubin kicin din da aka kafa kato domin ado inda ya fashe dan kuwa mai fashewar ne, ya tako zuwa gaban Agaishat dake zaune, cikin wani irin firgici da bugawar zuciya mai tsanani ya dubeta ido cikin ido ya ce" ke ko mutuwa na yi, Allah ya isanmin idan wani ya shiga gonata (Dankari, ka ji masifa fa, an taba yin haka dama?),

Sai da ya gama tashin hankalin da ya dirmiyar da ita cikin wani yannayi na furgici da tsoro, kara jin shayinsa, tashin hankalin abinda ya ringa maimaitawa a fadansa *ba zata wulakanta masa zuciya kamar yanda Aisata ta wulakanta masa ba,* sannan ya juya ya fita a kicin din,

Kafafuwanta ta hado gaba daya ta hade a jikinta, barin da jikinta yake yi ta samu ta daidaita ta hanyar adu.a,

Mikewa ta yi ta je wajen kayan da take gyarawa ta harhada komai ta kimtsa still jikinta na rawa sannan tana share hawaye ta ajiye komai wajensa ta fito,

Sai da gabanta ya fadi ganninsa a fallon, bai fita ba kennan, yana waya da alama da Ayya yake dan a tubancin da yake tana tsintar yan kalmomi da kuma sunnan Ayyan

So ta yi ta koma kicin din, sai dai wani abin ya hanata dan haka ta taho a hankali ta raba ta nufi dakinta,

Da kallo ya bita ya ci gaba da wayar, sai da ya gama ya taka zuwa dakinta, tun da ya fara fadan nan ko ci kanka bata ce da shi ba, yanzun ma da ya shigo yana ta muzurai ya bala mata harara kafin ya karasa ya tsaya kusa da ita ya ce" wato ga mahaukaci ko Agaishat? Shine kike nufi na

yi na gama ko?

Agaishat ta dago da idannuwanta da suka rine dan tsabar shiga tashin hankali ta dube shi,
A hankali ta ce" ka yi hakuri,

Wardugu ya ce" hakuri? Hakurin me zan yi a ciki? Na rashin bani muhali a rayuwarki ko na raina ni da kika yi?

Agaishat ta kuma dago da kanta, wannan karron bata sada duban nata ba ta kafe shi tsai da kallo,
Fitina kawai yake ji, so yake ta biye masa kamar yanda suka saba da matarsa ya tataka banza ya yi gaba abinsa, tabas ta yi rayuwar rashin sannin ciwon kai, aman bata tunanin zata yi rayuwar duka a gidan miji,
A hankali tana dubansa ta ce" menene laifina? Meye na yi mai girma haka? Ka taba nunan baka son sunnan nan? Ince kulunma da shi nake kiran ka kuma ka amsa ba tare da ka nunan bai yi ba, menene? Ganninka a irin halin nan an taba *AISATA!*

ido ya zaro yana dubanta, kai kai kai,
Agaishat ta ci gaba" dan Allah ka yi hakuri, kar ka saka ni a irin wannan rayuwar, ban iya ba, ban iya wannan rigimar ba, idan na bata maka ne ka yafe min, sannan ka daina tuna baya kana hada ni da wasu gardawa da aurena kuma na san darajar auren nawa,

Tana magana ne gabanta na dokawa, aman dan karfin hali sai da ta gama cikin sanyin hali tana hankalce da yannayinsa, kafin ta juya a dabarance ta yi wajen bayi ta tsaya gannin bai juyo ta tabatar da tunanin abinda zai mata yake dan haka da dan gagawa ta bude bayin ta shige ta rufo kofar sannan ta duka daga kasa ta ce" kuma Aisata dai ko? Zamu kai kukanmu wajen Allah ya raba tsakanin nan dan haramtace ne!

Da sauri Wardugu ya juyo sai dai ganni ya yi wayam, bata nan,
Kafarsa ya daga ya je ya tura bayin , aman a rufe ruf,
Wai waiwai dukan kofar ya shiga yi yana fadin" me kike nufi? Me zan yi da wannan banzar da ta banzatar da kanta? Me zan yi da macen da ta auri ubana dan abin duniya? Ki bude ki fada min abinda kike nufi da wannan maganar,

Haka ya yi ta bambaminsa kafin yake yin sanyi a hankali ya kai kasa ya zauna jikin bayin ,
Muryarsa ta tabatar mata da kamar ya shiga duniyar tunanin maganarta, inda ya ce" Ya zaki saka na mare ki?

Agaishat dake zaune itama tana sauraronsa, ta lumshe idannuwanta, walahi da ita fara ce ta tabata yau da sai ta nemi maganin tashin fata, aman yanzu haka jin idonta take da nauyi, ta maru fa,
A hankali ta shafa wajen , muryarta na rawa ta ce" dan me ba zaka mari matar cushe ba?

Wardugu ya dubi kofar bayin , bai san lokacin da ya saki murmushi ba ya ce" ke ce matar cushen?

Agaishat ta gyada kanta tamkar yana kallonta kafin ta ce" haka ne,

Wardugu ya ce" to fito ki ji,

Agaishat ta yi murmushi sannan ta yi irin na yara kafin ta ce" aa,

Aa? Ya maimaita a hankali yana zaro idannuwansa da mamakinta,

Agaishat ta ce" eh, ina tsoron duka, bana son duka,

Wardugu ya yi shiru, nan ya ji tausayinta ya kama shi, bata son duka, ya zo da bacin ransa ya sauke saman kanta,
Idannuwansa ya lumshe ya ce" kin san menene ma.anar Orronur?

Agaishat dake zaune dandabar cikin bayi daga ita sai yar doguwar riga ta kanti da ta saka take aikinta rigar bata da nauyi , sannan da kadan ta fi gwuiwarta tsayi, kanta ko dan kwali babu
A hankali ta dago dubanta kamar shi ne kofar ta dubi kofar kafin a sanyaye ta ce" Me yake nufi??

Wardugu ya saki murmushi mai dan sauti, ya ce" ki yarda da amon kuryana, ki yarda da yannayina, ki bude min , ki zo gareni, ki sauke min fushina, ki ririta ni, ki bani na tsotsa (😳🙆🏻‍♀️), ki bani na samu nutsuwa, Agaishat , ki karanci menene Orronur a tare da ni, ki bani amsa da kanki,

Wani irin yamyamyam ta ji tun daga yatsar kafarta har tsakiyar kanta, idannuwanta ta lumshe da karfin gaske dan kuwa har jikinta sai da ya amsa sannan ya dauka,
Wayo Allah, shi ne abinda ta fada a kasan makoshinta, domin kuwa a yanda ya yi maganar, ya karashe tamkar yaron dake neman mamansa ido rufe,

Hannunta na dan rawa rawa ta mike ta kai hannunta wajen budewar ta dana inda ta yi kundumbala da tsoron haduwar da shi, ta tataro jarumta ta bude kofar (Agaishat😳, idanfa ya yi haka ne dan ya damke ki? Baki dadara da marin ba ko? Wayo Agaishat😔)

Budewa ta yi baki daya kofar ta bude, sai gata bayane gabansa, gaba dayanta yar ficik a gabansa,

Taku daya ya yi ya karasa gabanta, hannunsa ya mika ya.................

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

8️⃣5️⃣

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA*  in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

*ASALAMU ALAIKUM FANS, BAK'A DAI BA NA SIYARWA BANE, DU WANDA YA KARBI KUDINKU DAN YA SIYAR MAKU YA CUCE KU NE, NI BAN RUBUTA BAK'A CE DAN NA SIYAR DA SHI BA*

A hankali ya mika hannunsa ya janyota jikinsa,
Bata ki ba ta kwonta a jikinsa luf,
Cikin nutsuwa ya lalubi lebenta , bai tsaya dogon turanci ba ya shiga aika mata kis cikin sauri sauri dan kuwa a matukar matse yake da ita,

Kokarin kaita kasa yake nan, ta samu a hankali ta kai bakinta daidai kunnensa ta ce" Dati jikina Yah, ka bari na yi wanka daga kicin na fito, karnin nama nake,

Idannuwansa ya lumshe domin ji yayi tamkar tana yi masa susa a kunnen dan kuwa a hankali

ta yi maganar ga kuma lebunanta dake gugar kunnen nasa,
Tsai ya yi, kafin ya lumshe idannuwansa,
A hankali ya samu ya janyota jikinsa sosai,
Hannunsa yake bi dukan jikinta yana neman hanyar cire rigar kafin ya iya fuzgo maganar bakinsa ta hanyar cewa" kin fi armashi a haka.........
Da gudu na baro dakin, domin kuwa Agaishat ta zagine tana baiwa mijinta goyon baya dan raya sunna ,

Sun jima suna maida numfashi bayan komai ya lafa, a hankali yake shafa gashin kanta, kafin ya ce" kin san me?

Agaishat ta girgiza kanta tana lumshe idannuwanta, dan kuwa ya yi kokarin binta a laluma , sai tarin gajiyar da take ji dai na rashin sabo a jikinta,
Wardugu ya ce" Oroonur, na nufin *RAINA*

Da sauri ta dago da dubanta daga kwoncen da ta yi lamo a jikinsa,
Ido ta tsura masa tana dubansa,
Hakan ya sa ya hade fuska shima yana dubanta,

Murmushi ta saki kafin ta mike ta shige jikinsa gaba dayanta, a hankali ta ce" ni? Ni ce Ranka?

Wardugu ya rungumeta da dan karfi a jikinsa, hakan ya sa ta yi lamo, still ta kuma cewa" *KANA SO NA?*

Wardugu ya yi murmushi bai bata amsa ba,

Can har ta cire rai da jin amsarsa ya ce" me kike so na maki a duniya na kare min mutuncin kanki da kika yi?

Agaishat ta dago da kanta tana dubansa, ita kuwa me ya rageta da shi? In mutunci ne ya siya mata, in kaunar ce ya kilaceta a gidansa, ba yunwa, ba kishirwa, ba rashin mutunci, ba ruwansa da kauyancinta, kuma yanzu ya gama shaida mata ita din Ransa ce, ita kuwa me zata nema bayan shi nashi jin dadin? Kai walahi ta dauki aniyar faranta masa mudin ranta!

A hankali ta dora kanta saman kirjinsa, hannunta dake kusan keyarsa ta dan karawa tsayi ta duko da kansa wajen fuskarta,
Kanta ta daga ta kai lebenta kusan bakinsa,
Yana tsaye tamkar ya kurma ihu dan dadi yana jiran ya ga ikon Allah me zata yi,?

Ba zato ba tsamani ya ga ta ciro harshenta a hankali, kuma idonta cikin nasa ta kawo harshen daidai lebensa, idannuwanta ta lumshe kafin ta lashi lebensa na kasa,
Tana lashewar ta bude idannuwanta sanadiyar kara matseta da ya yi a jikinsa, idannuwansa ta gani a lumshe,

Murmushi ta saki sannan a hankali ta ce" burina shi ne, ka yi hakuri, ka zama mai hakuri, ka zama mai yafiya, Yayana da ciwo, da mugun ciwo, aman a yau idan ka dubi wani abinda ya gani a rayuwa naka mai sauki ne, ka duba ka ga yanda kake cikin rufin asirin Allah,  ALlah ya baka rai kyauta, ya baka lafia kyauta, ya baka iyaye kyauta, ya bata yan uwa kyauta, ya baka mata masu kaunarka domin Allah kyauta, ya baka arziki ta hanyar halal kyauta, ga kyau,
Ta yi tsai ta dago tana duban idannuwansa, ta yi wal da idannuwanta ta ce" Mijina ga jarumta, ga farin jini , ga karfi, duka ba dan karfinka ko dan dabararka ba,

Shiru ta yi ta kuma dagowa tana duban yannayinsa, gani ta yi kawai ya tsura mata ido yana sauraronta,

A hankali ta dan zame kadan tana dubansa ta ce" duka bai tambayeka komai ba sai ka yi masa bauta, ka yiwa iyayenka biyaya, sannan ya ce *ALJANARKA TANA KARKASHIN KAFAR IYAYENKA* ,

Ka san me?

Dubanta yake bai amsata ba, bai kuma nuna bacin ransa ba, kai hasalima ba zaka fahimci wani yannayi yake ciki ba, yana dai kallonta ne,

Ji ta yi ta fara jin tsoron yannayinsa, dan haka a hankali ta yi shiru ta mike dan daukar rigarta zata saka,

Hannunta ya riko, ya kawota bakin bed din,
Maimakun su hau bed sin sai ta ga ya zauna da ita nan kasa ya sakata tsakankannin kafafuwansa ya dora bayanta saman jirginsa sanna ya saka hannayenta cikin nasa, a hankali ya ce" *sai kin fada*

Gabanta sai da ya wulwula ya fadi, anya kuwa zata iya ci gaba da magana a haka ? A hannunsa fa take dumu dumu, idan ta yi garaje daga haka yana iya juyar da kanta zuwa dubansa wato ya karya kan,

Yawu ta hadiye ta ci gaba da fadin" ni ba zan yi wasa da aljanata ba, du rintsi, du wuya, zan bi aljanata da gudu, a kanka sujada ne kawai ba zan maka ba shima dan haramun ne, zan tarbi mai tarbanka, zan banki mai yi maka mugun kallo, zan harbi mai zundenka, somin kai din uban gidana ne, mijina ne, mai take da aljanata ne,

Wani irin gingirigin kansa ya yi, wollah jinsa ya yo ya cika dakin dan girma, wani yuuuu ya ji gaba daya jikinsa, mace bata taba fada masa haka ba, macen ma Orronur, yarinya karama, yarinyar da ta yi girman daji, dama ta iya dadadan zance haka? Yaushe ta koya? Yaushe ta san tace da shi mijinta, yana jin dadi da gannin girman kalmar bale da ta fito daga bakinta, wai wai dadi, a hankali ya lumshe idannuwansa sannan ya kara rike hannayenta, muryarsa kasa kasa ya ce" Orronur,

Kina so na?

Shiru ta yi, tana mai kara tunanin hikinkimun da zata bi da shi,
Sai da ta kwontar da kanta saman kirjinsa ta yi lamo, sannan ta ce" *ARREKI DI IMANINE DU IDINETTE* (U.R TH MAN OF MY LIFE......TU EST LHOMME DE MA VIE),

sannan ta rike hannunsa ta kawo daidai zuciyarta ta dora, a hankali ta ci gaba da fadin" sun ce, daga na fara so, idan na ga abin son zuciyata zata fara bugawa, za.ina son gannin abin, za.ina son kasancewa da shi koda yaushe,
Tabas a kanka na san wannan abubuwan,

Gaba daya ya juyota tana facing dinsa, hannayensa dake rawa rawa ya saka ya dago fuskar tata daidai tasa yana kallonta, A hankali ya ce" fada, fada min , na roke ki,

Agaishat ta lumshe idannuwanta ta bude ta ce" *INA SON KA*

Bai bari ta karasa ba ya shigar da ita jikinsa, ajiyar zuciya kawai yake saukewa tamkar yau ya fara jin kalmar so a bakin mace,

Sai da ya jima sannan ya sasauta mata rikon, aman kuma tana cikin jikinsa tamkar wani zai kwaceta,
A hankali ta ce" zan so gobe kiyama na yi alfahari da kai, zan so yayanmu idan Allah ya nufe mu da samu su yi koyi da halayanka,
Ba zan iya budar ido na ga danka yana gaba da kai ba, zan iya samun arret cardiaque (heart attack) dalilin haka, domin kuwa d'a ko na wace mace ne, in dai naka ne toh bugun zuciyata ne,

Tsai ya yi yana kallonta, zuciyarsa fesss , inda ya  dago inda ta nufa da magangannunta,

Shirun da ta kuma yi tana mai daidaita bugun zuciyarta da tsoronta ya saka shi dan tapping din bayanta ya ce" Uhum?

Dan dago da idannuwanta ta yi ta ga ya tsareta da kallo, irin kallon nan na ya fara kausasa,
Takwaf takwaf ta yi da fuskarya ta samu ta mike tsaye inda ta yayumo abin shinfida tana kare jikinta da shi,

Hannunsa ya saka ya dangwarar da ita gabansa tamkar baby, ya daga girarsa duka biyu ya ce" karasa,

Da sauri ta girgiza kanta ta ce" shikenanma , abinda zan fadi kennan,

Wardugu ya girgiza mata kai shima ya ce" karya ne, fada min karshen maganar

Agaishat ta lumshe idannuwanta, a hankali ta fashe da kuka tana dubansa da yannayin yanda

zai dauki kukan,
Ai kuwa ya nunan domin kansa ya dafe ya ce" meye na kukan kuma ? Me na miki?

Agaishat ta ce" to ai na san idan na fada kana iya dukana, ni kuwa bana son duka,

Wardugu ya sauke ajiyar zuciya ya ce" nima bana son taba lafiayarki, ki yafe min na dazu kin ji?

Agaishat ta gyada kanta ta ce" to, ka sani idan ka dake ni, ba komai, na yafe maka, aman dan Allah kar ka min mai zafi,

Shi dai kallon yannayinshagwabarta yake kafin ta ci gaba da fadin" yaya kake son haduwarka da Allah ta kasance? Ni mahaifina ya tsane ni, baya son ganina, aman ba Sofo yace na yi ta masa biyaya dan na samu rabauta gobe kiyama, ka ga ina son mahaifina komai mumunan halayan da yake aikata mana da mu da Anna,

Da sauri ya dubeta, wani tausayinta ne ya ji, tana son mahaifinta? Koda kuwa ta ji a irin hanyar da ya same su su duka?

Katse shi ta yi ta hanyar fadin" kuma ka ga kaima zaka haihu, idan ka haihu yayanka suka yi maka haka fa? Mace? A kan mace? Ka dora muguwar gaba da mahaifinka haka? Dan Allah ka min rai, ka gyara tsakaninku da Aba, da kuma tsakaninsu da Ayya, na tabata idan yau ka yi niya sun gama shiryawa kennan, idan ya so ka barsu su gani da kansu, zasu koma rayuwa tare ne ko ba zasu koma ba? In dai an samu sulhu, zaka samu ladan hakan, kaima kuma Allah zai yafe maka, zaka ga daukaka sai dai ta yi ta kara zuwa, Allah zai kara kareka daga du wani shari, yayanka zasu mutuntaka su yi maka biyaya, matanka zamu ci gaba da mutuntaka mu yi maka biyaya,

Hannunsa kawai ya saka ya dafe yana dubanta,
Sai da ta gama sannan ta sake mikewa da sauri ta nufi bayi,

Tana shiga ta rufe tana sauke ajiyar zuciya, wai wai wai, bai kara tsinka min marin ba.....shi ne abinda ta fada kafin ta je ta shiga kiciniyar kimtsa kanta tana mai adu.ar Allah ya sa ta ci nasara,

Ya dan jima zaune kafin ya mike ya nufi bangarensa,

Shima wankan ya yi ya fito ya zauna bakin bed,

Shiru yana duban waje guda, wa ya koya mata? Dukan magangannun nan da ta yi, ba wanda ya taba yi masa su haka a dukan masu neman sulhunta shi da mahifinsa, ko kuwa ita dan yana jinta a ransa ne magangannun suka yi tasiri a zuciyarsa haka? To aman ai Walyn ya fara aura, hasalima bata taba tayar masa da maganar ba, tana tsoron ta yi ne ya mara fada ko me ya hanata yin? Ko bata damu da gobensa bane?

Wani abin yace...aaa, ba rashin damuwa da gobenka bane, just ita dai bata da kula a wasu abubuwan ne ai,

Ya jima zaune, kafin yake gannin haske a wayarsa,
Marahut ne ke maido masa da kira,
A hankali ya daga, yana dagawa Marahut ya ce" Wardugu, walahi babu saka hanuna a sakin wannan yarinyar, hasalima ni tun da na gane irin mugun aikin da take yi, da bin maza da urena a kanta na saketa, ban san wa ya shige gaba wajen sakinta ba, yanzu nima Gukunni ke fada min sakinta za.a yi, Wardugu ka fahimc.....

Wata kunya ce ta lulube shi, innalilahi wa.ina ilaihi raj.une, mahaifinsa? Mahaifinsa ne ke rawar murya dan ya wanke kansa a wajensa? Wata irin masifa ce wannan? Dama haka suke rayuwa? Dama haka Marahut ke masa magana ko yau ne haka ta faru?
Muryarsa ya ji tana rawa, a hankali ya ce" ABIH,.
Marahut dake ta faman kare kansa ya yi dif,
Kunnensa ne ke jiyo masa abinda yake son ji daga bakindan nasa ko kuwa gaske ne,?

Dan haka sai ya ci gaba da maganar a darare,

Wardugu cikin yaren tubanci ya ce" Abih, dan Allah ka bari, ya isa haka, ka bar mini rantsuwa,

Da sauri ya dubi wayar, number Wardugu ne, dan haka hankalinsa ya tashi, mikewa ya yo ya ce" me ke damunka? Baka da lafia ne? Me akai maka? Kana ina ne? Wani abu ya sami Ayyanka? Ko wani abu ya samu iyalinka? Menene War?

Wardugu ya ce" ina gidana , dake aeroport, kai kana ina Abih????

Marahut kashe wayar ya yi, daga inda yake sai cikin motarsa ya tayar cikin tashin hankai ya nufi gidan Wardugu,

Wardugu kam kansa ya dora gefen gado yana jin wani irin tausayin mahaifin nasa, yanzu da shi ne haka ke faruwa da shi , da dansa ina zai saka kansa? Ya zai rayu da haka?

Bai san adadin lokacin da ya dauka a haka ba, sai kiran masu tsaron kofar suka shaida masa Marahut ne,

Cikin tsawa tsawa ya bada umarnin a barshi ya shigo ko.ina, babansa ne fa!

Ai kuwa suka bar Marahut shiga ,

Yana parking din motar ya fito yana neman ta inda zai fara dan samun gannin Wardugun,

Sai dai hango shi ya yi tsaye yana kallonsa,

Takawa ya shiga yi yana duban yannayinsa har ya isa gabansa,
Ya budi baki zai yi magana kennan ya ga Wardugu ya duka..... ya duka har kasa, kansa na kallon kasa,
Jijiyoyin jikinsa du sun daga dan yannayin da yake ciki, muryarsa wani irin ya ce" dan Allah ka yafe mini, ka yi hakuri ka yafe mini,

Marahut da ya ji wani iri zuciyarsa ta buga da karfi ya saka hannunsa ya dago wardugu yana dubansa, hannunsa ya saka yana taba lafiar jikinsa sannan ya ce" me ke damunka? Baka da lafia ne?

Wardugu ya girgiza kansa yana mai jin haushin kansa, wai ace dan ka yi dadan magana wa mahaifinka sai ya shiga rudu? Lale ya jima yana tafka barna,
Kansa ya dafe da hannun nasa kafin ya ce" lafiyata kalau, ina neman yafiyar irin abubuwan da na yi maka  Abih, tabas matar mutun kabarinsa, tun ran gini tun ran zane, ka yafe min ,

Ai kuwa Marahut ya saki murmushi ya rungume Wardugu a jikinsa, bai iya cewa komai ba sai jan hannunsa da ya yi suka nufi motarsa suka shiga, Wardugu ke ja, Marahut kuwa sai sakin murmushi hamdallah ga ubangiji yake, baima san me yake ji ba, fatansa ya shawo kan Ayya cikin sauki
(Mace ta gari kennan, masha Allah)

Bayan kwana biyu da faruwar wannan , Walyn ta zo gidan,
Sun sha daru da masu tsaro , inda suka hanata shiga fir,
Ta kusan wuni a kofar kafin Wardugu ya dawo, ganninta a zaune a waje ya saka  ya barta shiga cikin gidan, inda ta ringa bin ginnin da kallo, tana mamakin nan ya kawo bakar mace dan zubar aji?
(Ku gane, shi fa gyaruwar halayan mutun abu ne mai matukar wahala ba kamar yanda muke zano mugayan halayan mutane sannan mu nuna lokaci daya sun gyara a cikin novel ba ko an sake su ba, kowa kuma na zaune da ra.ayinsa ne, shi shiryuwama sai Allah ya nufa, sannan ba lale mutun ya daina dukan halayansa ba, sai dai a rage a samu sasauci, sannan idan ya hadu da daidai kugunsa sai a yi ta buga game din wardugu dai ba zai saki mace ba, domin wani irin mutun ne shi mai kishin balaki, ku gane ba wai wani so ko wani abin ya hana shi sakinta ba, sai kishin ya saki macen da ya malaka wani ya malaketa, shi fa izgili yake yiwa al.adu da canfe canfe inda yace rabon ya jima bai.kashe shi ba! Idan abu ya yi kamari ne sai ya watsar da ke, ranar da kikai hankali kya nemesa ) ,

Tsayuwa ya yi yana dubanta ya ce" me kika zo yi?

Walyn ta yi kalar tausayi ta ce" aman ai gidan mijina ne ko? Na zo a bani part dina na zauna a gidana nima ,

Murmushi ya yi ya girgiza kai ya ce" yau kuma ina maganar al.adu? Yaushe batube ke hada mata gida guda?

Walyn ta ce" aman ai adalci na nema ko?

Wardugu ya yi murmushi ya gyada kansa, ya ce" kin ga, bama son rigima, idan nan din kike so, ita sai ta koma can, ko ta koma wani, idan kuwa wani kike so ki je ki zaba ai kin sansu gidajen sai a kara gyara maki ki koma kin ji Walyn?

Walyn ta gyada kanta, can ta ce" dan Allah ka maida ni gida,

Wardugu ya dubeta da kyau ya ce" ki je zan zo,

Walyn ta ce" to motana ba mai, kuma bam fito da cart dina na banki ba,

Wardugu ya gyada kansa, daman ya san maganar dai ba zata fice hakan ba, dan haka ya mika mata cart dinsa ya bata sabon cod din da ya saka , sukai salama ta tafi da niyar sai ya zo,

Cike da kurna take tuki, zako ta zabi gida, gidan da ya hada haya take so, wanda gwamnati ta dauka ake projet a ciki, shi take so a gyara mata ta koma, dan kuwa ta san zata bada kala,
A haka ta karasa gidan mamanta ta kai mata kudin da ta yi mata alkawar sannan ta juya ta nufi gidanta dan kuwa yanzu du ta watsar da kawaye, dan ta san idanma ta koma cudanya da su zata sha habaici a fakaice ne,

Tana zuwa ta zauna bakin kujerar falonta ta yi jigum, bafa ta da mahaifa! Abinda ko.mahaifiyarya bata sani ba,
An juya mata mahaifa, du dan gudun ta kara samun cikin da wuri, ko kuwa ta haihu du ta lalace dan ta ga daga an haihu ake zama rusheshe ko du a lalace , tana yawan tuna maganar Wardugu da ya ce" me na rage ki da shi da ba zaki haihu da ni ba?
Yana son yara har haka? Yanzu ina zata je a gyara mata mahaifarta? Dan kuwa bata yarda da maganar doctern garinnan ba,
Zata kwontar da hankalinta, ta sada kanta, har ya amince mata ta tafi india a dubata, a yi mata aiki a gyara mata mahaifarya, itama ta dawo ta haihu sai ta ga yanda za.ayi gata ta haifar masa abinda yake so, ta tabata soyayarta zata dawo kamar da a ransa!
(BAK'A CE BA NA SIYARWA BANE, FANS DU WANDA YA BIYA DAN KARANTA BAK'A CE NI DAI MARUBUCIYARSA KYAUTA NA YI SHI, SAJIDA CE)

washe gari ya kama asabar, tana zaune ta gama waya da Ayya kan ta tsife kanta za.a zo a yi mata kitso, tana zaune tana tsifar kan tana mai jin zuciyarta na tashi haka kawai , bata san me ya shiga turaran wutar da ta saka yau ba, du sai take ji kamar an canza mata shi kamshinsa baki daya,

Tana cikin haka ta ga shigowarsa,

Tana kokarin ta hade gashin ta mike ta hango su,
Su duka uku ne da wata datijuwa mai kama da Anna,

Bata san lokacin da ta mike ta kwala karan murna kamar yanda suka yi ai kuwa da gudu suka makalkale juna,
Ihun murma suke kowace na kama sunnanta, itama sai kama sunnayensu take suna latsa jikinta da mamaki itama sai kallonsu take da mamaki inda Wardugu da Anmou ke tsaye shi yana sakin murmushi dan ba a gidan ya kwana ba, zuwansa kennan ya zo ya sanyo su , anmou kuwa na dariya itama gannin yanda Agaishat ta rasa inda zata tsaya ta kalli wannan ta juya ta kalli wancen sai kawai ta saka kuka ta dora kanta saman kafadar Gaishata ta ce......

🐫🐫🐫🐫 *BAK'A CE* 🐫🐫🐫🐫

Na
*SAJIDA*

86

*KUTKALE* (PRISON)

*AURE YAKIN MATA NE*

*KAMARTA, BATA DA NIYAR CUTARWA*

daga alkalamin yar mutan niger *SAJIDA*  in sha Allah,

........kar ku bari a baku labari.....

*ALHAMDULILAH ALHAMDULILAH ALHAMDULILAH*

*ND*

*ND*

*ND*

Wardugu kam juyawa ya yi ya nufi gidan Ayya domin a jiya da ya je gidanta fatatakarsa ta yi kamar kwanakin nan da suka shige,
Yau kuwa da kanta ta yi kiransa tana son ganninsa,

Yana zuwa gidan Ayya ya zarce dakinta,
Kwonce take saman bed sinta idannuwanta lumshe, aman kwonciyar ta mutunci ce domin ko.inanta a rufe ruf,

Da sauri ya karasa ya duka inda take ya ce" Ayya, baki da lafia ne? Me ke damunki Ayyana? Tashi na gani Ayya?

Ayya dake kwonce ta lumshe idannuwanta ta ce" Wardugu, ka zabi mahaifinka yanzu ko? Ka zabe shi a kaina ko?

Wardugu ya kama hannun nata da ta janye ya janyo ya dora gefen fuskarsa ,
Muryarsa ce ta raunana, ya ce" bani da tamkarki du duniya,
Sai dai shima haka,
daga ke sai shi a duniyata,

Ayya ta yi shiru, can ta ce" mutumen da ya zabi mace a kan iyalinsa? Mutumen da ya auri yarinyar da na guji dana ya aura dan ban yarda da tarbiyarta ba, mutumen da mai yiwuwa ya yi zaman aure da macen da dansa ya gama gannin sirinta,  na san baka aikata zina da ita ba Wardugu, aman kuma na san da ba yanda ba zata yi ba dan jan ra.ayinka,
Sai yanzu da ya rasata zai waiwaye mu? Sai yanzu zai san da zaman mu?

Wardugu ya rike hannun Ayya da kyau yana dubanta ya ce" ki yi hakuri,
Gani gabanki, duke saman gwuiyoyina, ina mai neman sulhu,
Sulhu kawai na roka a wajenki mahaifiyata, ba zan roke ki kara zaman aure da shi ba idan hakan bai maki ba,
Aman ina so ku daina gaba, a fitar da fushin nan ,

Ayya ta mike zaune tana dubansa,

Kanta ta girgiza kawai sannan ta ce" ba komai, Allah ya shige mana gaba, ni na yafe masa, ba maganar gaba tsakaninmu, aman kuma bana tunanin zan iya rayuwar waje daya da shi again, A barni na huta,

Wardugu ya amsata yana mai gyada kai, ko ba komai ya ji dadin cirw fushin dake tsakaninsu, Maganar wancen kuwa, ya barwa Allah zabi,

Haka suka jima suna hira da Ayya , nan yake fada mata zuwan yan uwan Agaishat, daman sun zo sun gaisheta Gukunni ya kawo su satin da ya shige, nan ta yi murna kafin ta ce" Allah ya sa dai kar su fada mata wannan lamarin,

Gabansa ya ji ya fadi, Ruwan tea din da ya dauka zai kai bakinsa ya dakata,

Mikewa ya yi ya yiwa Ayya salama ya dauki hanyar gidansa,

Yana zuwa ya shige ciki direct dakinta domin bata falo, kuma da alama bakin sun jima da tafia,

Kwonce ya ganta cikin bargon, sai rawar dari take,

Da sauri ya ajiye kys din hannunsa ya karasa inda take kwonce ya yaye bargon yana dubanta ya ce"Orronur, lafia? Menene?

Hawayen da ta sha ne ta yo gagawar gogewa cikin dabara da hannunta, kafin ta mike a hankali dan ya kamata so yake ta mike din,
Jikinsa ta shige ta yi lamo tana duban gashin dake kwonce saman hannunsa,
A hankali ta dora hannunta tana shafawa , cikin nutsuwa ta ce" kuma du wannan abin da aka yi dan a tara dukiya aka kare ba komai, karshema yanzu mijin Gaishata ke fadin an nemesa an rasa,

Ribar me ya ci? Ko zaman da aka yi idan ya karbi kudin auren yan uwanmu basa jimawa yake batarwa ta hanyoyin da basu da kyau kuma ya dawo ya shiga hangen wasu, uku sun rasa ransu ta haka,
Ashema duka zaman bai gina shi da aure ba? Ashe mu dukanmu ba daya da aka haifa da aur..........

Hannunsa ya saka ya rufe mata bakinta,
Cikin nutsuwa ya ce" wanda ya halice ku, haka yake son ganninku,
Kuma muma bamu da damuwa da hakan,

Kanta ta dora saman kirjinsa tana mai jin wani girmansa, kunyarsa, kaunarsa na kara shiga cikin jinnin jikinta,

A hankali ya karkata ya sauka da ita ya ja hannunta bayan ya dauki yar ledar pharmaci din da

ya shigo da ita ya nufi bayi da ita,
Yar robar dake cikin abin ya mika mata , fuskarsa ya shagwabe kamar wani yaro ya ce"
Orronur, dan bani fitsarinki kadan a nan kin ji??

Da mamaki ta zaro ido, fitsarinta kuma? A wannan yar robar mai shegen kyau? Me za.a yi da fitsarinta?
Tsaye ta yi tana dubansa da iyakacin gaskiyarta, sai dai gannin da gaske yake ya sakata fadin" to ka juya mana

Murmushi ya yi ya juya bayansa inda ta samu da sauri ta yi tana kallonsa dan kar ya juyo ya shanmaceta,

Kallonsa take har ya dauka ko kyankyami baya ji, ya ciro dogon abin dake cikin wata yar farar leda mai kabar kabar ya saka kan abin sannan ya dawo kusa da ita ya janyota jikinsa sukai tsaye su duka sunna kallon abin

Ita kallon da take dan ta ga menene? Me kuma zai yi bada da fitsarinta?
Shi kuwa jiran lokaci yake dan gannin result din test din

Bayan minti biyar ya dauko ya duba,
Radau suka nuna kansu sanda biyu, wanda hakan ke nuna ciki ne jikin Agaishat,

Idannuwansa ya lumshe, can kasan zuciyarsa yake godewa Allah,
Aman kuma wani tsoron ta sani ya darsun masa, yana tsoron kar aje itama bata son haihuwar, dan haka sai ya yi shiru ya kamo hannunta suka fito daga bayin,
Bakin bed ya kwontar da ita, ya rankwafa yana gyara mata gashin kanta, sai wani bibinta da kallo yake fite da da, hakan ya sa du ta tsargu,
A hankali ya mana mata kis a goshinta, sannan ya kai hannunsa kamar cikinta yake shafa , ya shafo wajen mararta ya saki murmushin da bata san ko na meye ba, sannan ya mike ya fice a dakin bayan ya dauke abin test din, yace da ita yana zuwa....

Kwonci tashi kayan Allah,
Agaishat wajen wata biyar da aurenta da Wardugu,
Zuwa yanzu, koda sun yi fitinarsu da matarsa baya nuna mata , yakan nuna ya tafi gidan Walyn din da ta koma itama gida ne na gani na fada, sai ta yi baci ya yi zamansa abinsa,
Cikinta kam na tafia cikin nutsuwa, bai yi wani girma sosai ba, ya tasa dai, wanda Zuwan Gaishata garin da ta je ganninta ita take fada mata ciki ne da ita fa? Ta sha mamaki, ita kai, tana gannin cikinta na dan kara girma, bata jin motsin komai kuma,
Kakarta kam dariya kawai ta yi, tana yiwa Anna tsiyar ta daina jin kunyar nan da take na yayan nata fa, domin su sun jima da sani, Ayya ta fada masu Wardugu ya rangada mata albishir din, a takaive dai ita mai dauke da shi ne bata san da shi ba, kai harta da baba Sofo ashe ya san da maganar, taimakon da yake bata na sha ashe dan cikin ne? (Domin kuwa alhamdulilah, baba

Sofo na samun kulawa ta musaman, yana dan ciwoce ciwocensa na jikin tsufa, aman kuma hakan baya hanashi walwala da jin nutsuwar zama tare da wadinnan bayin Allah, ga Agaishat ba.a kwana biyu bata yi kira an bata shi a waya ba, koda bata zo ba, yana jin wani gurbi da ya rasa ya cike masa, yana jin kaunarsu tamkar ciki daya, Gukunni na zuwa ya taya shi zaman fada idan baya aiki, aukan yi shayi su sha, sannan su yi hirar rayuwa, inda Ba sofo ke bashi sirika na tsari)

Itama kunya ce ta ji kamar ta nitse kasa, ya Salam ciki? Cikin mijinta, bangonta, abin alfaharinta, yanzu Ayya ta san tana dauke da ciki take zuwa gidanta ta bararaje abinta?
Yo ita ba laulayi, dan zazabin dare dai take tabawa shima ba wani mai zafi ba, haba gaske idan ta je take samun kayan kwadayi, kuma wardugu na yawan kawo mata kayan kwadayi ,
Kanta kawai ta sada dan tsabar kunya, gashi ana cikin cuwa cuwar auren Mariama da docternta dan Nigeria, Fatimata kuwa da wani dan kasuwa mai sunna Muhamadu,

Walyn, a yanzu lamarinta, zan iya cewa da sauki, domin kuwa tana kare lamarin Ayya tun karfinta,
Abu daya ne take fama da shi dai kishinta, har yanzu ba zata iya wani kishin kissa ba, gashi wace take haukan dan ita a garin, take zuba kayan, tana zubawa makadan kudin dan sunnanta ya kara dagawa fiye da na kishiyar tata bata ma san tana yi ba, domin kuwa fitar Agaishat fita ce ta idan ta kama, idan ka ganta waje zai kaita gidansu ne, wato gidan kakaninta, ko ya kaita gidansu, wato gidan Ayyanta,

A hankali ta ci gaba da rainon cikinta, sannan ta ci gaba da fuskantar lamarin mijinta, wani lokacin daga waje za.a kuno shi ya zo ya yi ta neman fitina, wai danma ciki ne a jikinta ya yi ta jajensa sai ta yi masa gum, idannuwansa su kade masifa kawai yake nema idan ta ki kula shi sai ya shiga mota ya bi cikin gari ko ya tarda walyn , ita kuwa har yanzu ta kasa gane lamarinsa sai ta biye masa ko ta hanyar korafin ita dan ya tsaneta ne yake mata haka, ko kuwa sakma ta mike ta maida martani, wani lokacin ya tumurmusheta wani lokacin ya mayar da ita tamkar doki ba abinda ya dame shi,
Cikinta na da wata shida aka yi auren su Mu.azam, nanma an sha darga domin cewa ya yi bata yi masa barka ba ko ta ji haushin Mu.azam ya yi aure?
Murmushi kawai ta yi masa sannan ta mike ta bara masa wajen, bafa wani laushi ko a kanta, danma tana cin albarkacin cikin jikinta sam baya gigin taba lafiarta ko ya yi mata fadan da zai sakata kuka

A haka aka yi auren yan matan Anna biyu, inda Ayya ta zama aminiya kuma kirjin biki, domin kuwa ita ta sada Mariama har garin iyayen mijinta kafin su daga ta damka amanarta, inda Agaishat ta yi ta fushin ba.a tafi da ita ba, harda kukanta, aman lokacin sai aka yi ta rarashinta domin kuwa ciki ya tsufa sai fitintinun masu ciki kala kala,

Cikinta nada wata tara da sati daya wani yamacin alhamiss suna tafiya da Wardugu a tsakar tankamemen gidanta ya rike hannunta suna dan takawa dan kafafuwanta su rage kumburi, da kuma yanda docter tace da ita su ringa tafiar kafa idan haihuwar ta kusa zata samu saukin

nakuda,

Sanye take da irin kayan indiyawan nan riga da wando blue, manya ne sosai domin ba daidai da ita bane, tunda cikinta ua taufa suka zama suturarta , ciki take bulmuya ta yi ta yawa abinta, Hannunta rike da kasar da take sha a boye tana so ta sha tana tsoron ya gane abinda take boyewar su casu a wajen nan, ta ji ciwon bayan dake sandarta sai kara yawa yake,

Dan dakatawa take dan yi idan ya lafa sai kuma su ci gaba da tafia, yana mata labarin abin dariyar da yake gannin na dariya ne, wanda ita kuwa binsa dai take ta yi dariyar dan kuwa du abin wani fadansa ne da wani, wani rikici da suka yi dai da sauransu, du ba wani abin dariya saima abin tsoro da mamakin irin yanda fada ke saka shi nishadi da take,

Ji ta yi wani irin das das das tun daga bayanta yake sarawa har ya sauka kafafuwanta sannan lokaci guda cikinta ya wani irin hautsina ya rikide da wani irin ciwo tsakurw tsakure gefe gefe kafin ya garwaye ta rasa takamaiman indama zata ce yanai mata ciwon.

Da sauri ta tsaya, tana son dukawa aman ina, wani yawu ta ji a  bakinta na wuya mai wani taste daban, sannan wata zufa ta karyo mata,

Da sauri ta damko hannunsa da wani irin riko mai karfin gaske, hakan ya saka shi juyowa da dan sauri yana dubanta,

Yanda ya ga tana faman kaiwa gurfane ne ya saka shi tarota jikinsa yana mai tambayarta lafia? Menene??

Da kyar ta iya juyar da kanta ta ce" Wardugu , zan mutu, zan mutu,

Ido ya firfito mata kafin ya ce" ke, ba zaki mutu ba, .....
Yana fada yana dabarar yanda zai dauketa ne kar ya ji mata kuma kar ya jiwa abinda ke cikinta,

Da kyar ya sungumeta ya nufi motar da ta fi kusa inda yake ihun a bashi kys a bude masa gida,

Kanta kawai take juyawa, domin abin wani tashin lokaci guda ne ya yi mata, daga ya dan lafa sai ya kuma tashi, hakan ya sa a fili take fadin *ALLAHUMA LA SAHLA, ILAMA JA.ALTAHU SAHLA, WA ANTA TAJ.ANUL HAZNA, IZA SHI.ITA SAHLA* (ALLAH KA SAUKAR MIN KAWAR KWARAI AMINIYA SAMIRA LAFIYA , AMEN YA RAB),

haka har ya karasa da ita asibiti,
Sai da aka karbeta aka shiga da ita yana ta sintiri kafin ya tuna da Ayya, gashi ya fito ba waya ko daya a jikinsa, gashi mutane sun fara ankara da shi ne a wajen,
Waje ya samu ya zauna ya yi bakam yana kallon waje guda, adu.a kawai yake a zuciyarsa wace bai san bama me da me yake ja,

Yaren gidansa ne suka shaidawa Ayya abinda ke faruwa, dan haka bata tsaya wata wata ba ta je gidan ta dauki abinda zata dauka sannan ta bi bayansu asibitin da take awo dan ta san can za.a kaita haihuwa, asibitinsu ta sojoji

Zaune kawai ta tarar da shi, hakan ya sa ta zauna tana tambayarsa yaya dai??
Dago da kansa ya yi a raunane yana dubanta ya ce" Ayya, wai wai cewa ta yi mutuwa zata yi, Ayya idan ta mutu ni kuwa na yi yaya?

Ayya ta girgiza kanta tana dubansa ta ce" Allah baya barin wani dan wani ya ji dadi Wardugu, aman  kuma zafin ciwo ne ka ji? Mu yi mata adu.a in sha Allah zata sauka lafia,

Shiru ya yi yana gyada kansa, shi kam ko ciwon kai take sai ya jishi bashi da wani anfani, wollah dan ba makoki bane, da ko yatsarta ke ciwo sai ya yi kuka, dan sosai yake jin abin a ransa, bale yanzu,

Agaishat kam ta sha wahala ba laifi, nakudar awa shida ta yi, da kyar Allah ya sauketa lafia ta haifo baby boy dinta, bashi da girma sosai domin cikinta bai yi mugun girma ba,
Zo ka ga murna wajen Wardugu Ayya da duk wani sojan da kafarsa ke cikin asibitin,
Nan da nan wajen ke ta daukan harama duda dare ne sosai, haka aka yi kiran su Gukunni aka fada masu, inda Anna ta shiga murna a cikin ranta tana tausaya yar tata da adu.ar Allah ya raya,

Wardugu kam dariya yake hakoransa waje, mutane sai murna suke taya shi, inda ya yi kiran Walyn dake baci ya sanar mata yana mai farin ciki,

Bai tsaya ya ji amsarta ba ya kashe yana ta doka kira,

Walyn kam daga saman bed din ta doko kasa, idannuwanta du ta zazaro tana kallon dakin, me me ta haihu? Ciki ne da ita daman? Daman ciki ne da ita? Yaushe har cikin ya girma? Yaushema aka yi auren? Ni ina zaune ban yi cikin ba? To walahi sai na je indiar nan nima sai na haihu!
Haka ta yi ta sambatunta wanda sam bata san halin hasadar dake cin zuciyarta ba, a wajenta normal ne, itama muradinta take fada .....

Biki ne aka yi a tsare, bikin da ya hada dangin Tubawa da na Buzaye,
Du girman gidan nan sai da ya cika ya batse,

Walyn ta sha wata danyar shada wace takanas ta tada mutun aka je dubai aka kawo mata kala uku dan ta saka ta uagawa kishiya a bikinta,
Ta sha zinariya tun daga wuyanta, hannayanta, yatsutsanta, harda ta kafa,
An sha gyaran hashi an sha mak up an kawo mahaukatan jaka da takalmi an saka sai baza kamshi ake ana daga kai inda maroka ke ta waketa, sai dai abinda ya tsaye mata a rai gannin

bata ga mai jegon da yaron ba,

Wajen karfe biyu ake walima, dan haka du aka taru ana gabatarwa,
Nan Agaishat ta fito, cikin shirinta na doguwar rigar lesh mai ruwan golden,
Ta sha sarka da yan kunaye da awarwaraye sa agogo da abin hancinta kowane na zinare ,
Kwaliya yar daidai ce a fuskarta wace ta kara fitar da tsararen kuma nitsatsen kwaliyarta wace sai da Wardugu ya duba da kansa cewar babu kowa sannan ya yarda da ta fita a haka domin kuwa ta jima da aka yi mata tana son fita sai jaje yake wai ta yi kyau sai binta yake da kallo,

Ba kwaliyarta ta girgiza walyn ba, domin kwaliyarta nitsatsiya ce duda tsadar leshen da kuma su sarkar, ta san wardugu ne ya siya mata dan haka bata wani damu ba saima hura hanci da ta ringa yi ta biya marokiya na yi mata kirarin uwar gida,

A lokacin da aka fara rabon kyauta wa du wanda ya zo , a lokacin ta haukace da mamaki, kyautar daga kakar Agaishat, bata ifasa sarewa ba sai da ta ga wacece kakar ta agaishat, Matar GUKUNNI? ita ta haifi mahaifiyar Agaishat,
Ambulop ce ake baiwa mutane dauke da kudi, sai ka buda ka ga adadin abi da aka baka, nan da nan wajen ya kara rikicewa da murna da shewa, kamar da wasa aka fasa zuzuta walyn din , kudi ya karbe hasken nata, nan da nan maroka sai suka gane bikin wanda suka zo suka juyar da akalar wasawar zuwa ga amarya shalele,

Basu kara sarewa ba sai da garar amarya ta shigo, wace iyayenta sukaiwa ango,
Ba wai wani abinda ba.a taba gani bane aa, abin ne ba.a yi zaton za.a yi shi haka daga wajen amaryar ba, inda Ayya ta zagime itama ta bada kyauta wa yaron da ya ci sunna *ABDALLAH* Bawon Allah, da kuma mahaifiyarsa,
Haka aka gabatar da kyautar da Wardugu ya dankara mata, aman bai yiwa yaronsa kyautar komai ba, ya dai yi dogon rubutu na saka albarka,
Kai bude bude ne ya cike gidan, inda ba wanda ya san fitar Walyn sai kofa...

Bayan wata bakwai.....

Rarafowa ya yi ya karaso kusan kafarsa,
Ya kama kafar ya mike ya rike kafar da kyau sannan ya washkale da dariya yana duban Wardugu dake zaune yana kada kafa ya gama tashin hankalin ba zata je wajen sunnan matar Mu.azam ba, ita kuwa tace a na me? Ba.a zumunci su ke kai kawo hanya?
Ai kuwa ya hayayako yana fadin" Orronur ni ne sai me? Ni ne sai me? Bara na gwada maki sai me!
Da gudu ta afka dakinta ta dani kofar tana kilkila dariya ta kuga ta ce" Wardugu bana son duka

Shi kuwa daga zaunan da yake ya saki murmushi ya dauki yaronsa dake ta bangalar masa

dariya ji yake wasa ne ake masa ya rungume a jikinsa kafin ya ce" ORRONUR, BA DAI NI NE WARDUGUN BA KO? KUMA NI NE SAI AN JE DIN KO? BA ZAN DAKE KI BA, AMAN WALAHI CIKI ZAN JARA MAKI!

IDO ta zaro kafin ta shiga kiciniyar bude kofarta dan zuwa ta baiwa mijinta, amininta, yayanta, ubanta, masoyinta, abokin wasanta hakuri ta rarashi abinta cikin hikima....

Tamat bi hamdika👏🏻👏🏻👏🏻